[1/25, 5:35 AM] Hafciey Musa😘: *LAYLERH*

(The prettiest emerald)

Dukkan godiya ta tabbata ga Allah subhanahu wata'ala,tsira da amincin shi su tabbataga ga annabin rahama..

Godiya ta tabbata ga Allah daya sake Ara mini lokaci da lafiya Mai tsada da dumbin daraja inda Zan Fara rubuta *LAYLERH* ina kuma rokar sa da ya bani ikon gamawa,ban yarda wani ko Wata su juya mini labari Na ba ta kowace tsiga..

Na sadaukar da littafin nan ga mahaifiya ta😍Alherin Allah ya Kai miki a duk inda kike

Bismillahi Rahmani Raheem

No disappointment in sha Allah

Page 1

"Kiiiiiiiiiiiiiiiiiiiiiiiiii."

Shine Karar take birki da driver yayi,motar dai tsohuwa ce da gani kuma an Dade Ana tafiye-tafiye da ita shiyasa tsufa ya kamata yanzu haka bacin ta Na uku kenan a hanyar tasu Wanda hakan ya tilasta musu tafiyar dare.. Take birkin da aka yi har masu bacci a motar sanda suka farka saboda a bazata suka ji shi wasu ko har buga goshin su suka yi jikin seat Na gaba ciki ko har da yarinya Yar budurwar da ba zata wuce shekara sha bakwai ba

"Wayyo Allah na"

Ta fada idanun ta Na cikowa da kwalla tana yarfa hannu saboda sosai taji zafin buguwa da tayi,matar da ke kusa da ita wacce zata Kai 45yrs ne ta harere ta tana cewa

"Wallahi duk da bana ganin fuskar Ki da kyau saboda dare ne kada Ki sake Ki mini kuka da wanne daya zanji da fargabar tafiyar dare koda shegen kukan banzan Ki kamar karamar yarinya maza Ki hadiye kukan ko naci uban Ki".

Rintse idanun ta tayi da sauri jin Wai ko taci ubanta Amma bata isa tayi magana ba saboda tsananin tsoron matar da take yi kuma a yanzu duk duniya bata da kamar ta tunda tare suke Gashi itama harga Allah tsoron tafiyar Daren take yi haka kawai sai gaban ta yake mugun faduwa wannan dalilin ne ma ya Hana ta bacci a motar duk da dai yau kam Alhamdulillah da alama gab suke da Isa garin da zasu saboda yau kwana 2 kenan tafiyar taki karewa...tsaki taja ganin yarinyar ta hadiye kukan sannan ta dubi driver tana fadin,

" lafiya dai ko malam".

"Wallahi ina ji taya ce ta yoye dole sai Na canza Wata".ya fada lokacin da ya juyo yana kallon ta

" subhanallah cikin Daren nan,Gashi a daji muke Dan Allah Ka hanzarta mu bar nan tsoro nake ji ".murmushi Mai sauti yayi gami da fad'in

" kada Ki damu ba komai in sha Allah Ai Mun Saba irin tafiyar ".

Ya karisa zancen shi da bude kofar motar ya fita, ita ko kallon yarinyar tayi sai ganin ta tayi jingine da jikin kujera ta rintse ido Wanda ta tabbatar ba bacci take ba tsoro ne ya sata yin hakan saboda harga Allah dajin abun tsoro ne Gashi su biyu ne kadai passengers da suka rage..

" Dahiru dauko mana taya a boot da sauri"

Driver ya Kira Karen motar sa nan take ya fice domin cika umarnin uban gidan shi yana Kai masa sai ya tayasa suka sauya tayar motar sai yace Bari ya Dan taba Ruwa nan ya shige daji shi ko driver kuma motar ya kunna inda kafar shi daya Na waje daya kuma Na ciki nan suka zauna zaman jiran dawar Dahiru..

kamar daga sama sai jin karan bindigogi suka yi take jikin su ya hau rawa ko wannen su duk addu'ar da tazo bakin sa yake yi Dahiru kuma jin haka sai ya makale a inda yake domin tseratar da tashi rayuwar.. gani suka yi 'yan fashi sun zagaye su ko wanne fuskar sa rufe da marks sai ido da wajen hanci ne a bude duk da dare ne suna iya gano su Wanda akalla sun Kai mutum bakwai nan suka janyo wuyar driver suka jefa shi waje cikin muryar su Mara dadin sauraro irin ta yan shaye-shaye suka ce

"Duk Ku fito a motar".

Har kokawa wajen fitowa suke yi suna fitowa kuma suka zube a kasa kamar yadda suka ga driver yayi..shiru shiru ba Wanda ya sake bin ta Kansu sai sigarin su da suke busawa a kan su ita dai yarinyar har fitsari sai da tayi a jikin ta duk son kukan ta kuma yau ba baki,ganin sun koma can gefe sun mance da sune ya sa driver kokarin magana

" Oga"

ga mamakin su sai suka ji an sake bindiga suna juyawa kuma suka ga driver kwance ba rai a jikin sa saitin zuciyar sa suka harba hakan yasa suka sake shiga hankalin su kowacce zufa Na fitowa daga jikin ta cikin su ma ya rude gaba daya..sun Kai kusan 40mins Bayan sun gama shaye-shaye da bushe-bushen su sai suka Kama Mata da yarinyar suka hau tafiya da su sun yi tafiya kusan Na minti goma kan suka hango motar su nan aka jefa su a ciki suka hau tafiyar da tsam ba gane hanya suke yi ba gaba daya lamarin ya daure musu Kai shin In da gaske yan fashi ne Ai kudi zasu tambaya in ko yan kidnapping ne Ai gidaje suke zuwa ba tsayawa cikin dare a hanya ba..

Dahiru ko koda yaji sun tafi bai fito ba sai Bayan 20mins don gani yake kamar buya suka yi nan ya haska touch Na wayar sa jikin sa duk rawa yake yi don yana ga kamar zasu dawo sosai yayi kukan kashe uban gidan shi da suka yi yana jinjina rashin imani irin tasu da kuma tausayawa matar nan da Yar ta da suka dauka..

Tafiya dai taki karewa da kyar ta kare kasan wani katon dutsen nan aka fiddo su waje gaba daya baka hango ko alamar daki a wajen don da gani daji ne sosai..

ita yarinyar addu'ar cikawa da imani take yi saboda yau dai ta San dole rai zai yi halin shi ko kuwa....

Da sauri ta cire tunanin a ranta don in har suka ce lalata Mata rayuwa zasu yi to wallahi gwara kawai su kashe ta din..

Dutse suka Fara hawa Wanda da kyar suke iyawa kasancewar su Mata gwara ma ita yarinya ce Amma matar ba karamin wahala take sha ba don girma ya Fara kamata haka suka riga ture su suna jin ciwo su kuma tashi su cigaba da tafiya da kyar Allah ya basu ikon karasa karshen dutsen inda nan suka ga kangon kidnappers din yake don yanzu kam sun tabbatar kidnappers ne ba yan fashi ba dama sun San Nigeria Na fama dasu....

sun zauna sai dai tsam wurin ba haske ko fuskar su baka iya gani Amma dai wurin ya nuna tabbas an Dade Ana zaune wajen har ya dawo tamkar gida suma zubewa a kasa suka yi kowa da abunda ke damun sa...

Bayan Isar su da kamar hour 1 sai suka hura wuta tare da daura kaskon tuya sai da tayi zafi sannan suka yiwa matar alama da hannu tazo jikin ta na rawa ta nufe su sai suka ce ta zauna a kaskon da suka sauke,tabbas ta san gasa duwawun ta zasu yi za kuma ta sha azaba amma saboda tsoron su mata yadda suka yiwa driver sai ta zauna tare da sakin razanenniyar kara tana kuka tsakanin ta da Allah ganin haka yasa yarinyar ma fashewa da kuka aiko mari suka ringa kai mata a fuska take bakin ta ya kumbura dole ta hadiye sauran kukan don azaba, matar ko har yanzu bata daina jin azaba ba duk da kayan da yake jikin ta ganin haka sai suka koma wajen zamar su suna harkar gaban su Na shaye shaye da hira cikin yaren su Wanda ba Hausa bane.. bayan irin 1 hour lokacin kaskon yayi sanyi sai suka ga duk sun baje

sai bacci suke Gashi basu ce da su komai ba kuma basirar daure su bai zo musu ba da yake suna ganin ba iya sauka zasu yi ba kasancewar su Mata..

ganin fa kamar da gaske bacci suke yi yasa matar tura kafar ta gaba ta kuma dawo da shi baya basu farka ba,karfe ta kuma bugawa taga ba Mai motsi cikin su saboda kwaya da suke sha basu ma San tana yi ba Kama hannun yarinyar tayi suka mike a hankali nan suka Fara sauka dutsen Wanda zuwa yanzu cinyoyin su da kafufun su sunyi tsami da kyar suke iya sauka kuma sun tabbata in sun Kama su to mutuwa zasu yi sai dai koma yaya ne ya zama dole su bar wajen kan su farka in har suna son tsira da rayuwar su aikuwa ba karamin azaba suka sha ba kan su gama sauka nan suka Fara jefa kafa duk inda suka samu cikin Daren ba tare da sanin ina suka dosa ba su dai tafiya kawai suke yi haka ko suka kwana tafiya kan gari ya Waye gaba daya sun galabaita Amma ganin tsam ba alamar mutani a kauyen sai suka cigaba da tafiyar har sai wajajen 9 Na safe suka shiga kauyen da akwai mutani nan suka nemi Ruwa suka sha gaba daya sun koma kalar tausayi daga nan suka tambayi inda Tasha yake aka sanar da su Kai tsaye Tasha suka nufa saboda dama ita bata sa kudi a purse a kashe ni Ka dauka take Sawa direct motar Kano suka shiga abinci ma sai a hanya suka ci duk Wanda ya kalli yarinyar ko sai yaji tausayin ta saboda galabaituwa da tayi Gashi idon jazir ya dawo don wahala ga bakin ta har karkashewa yayi ..

Yau din ma dai kusan dare suka yi a hanya Amma sun isa inda suke so da yake an San da zuwan su cikin Daren aka budo musu kofa Ai kuwa sosai aka yi murnar ganin su take aka basu abinci Kala Kala ita dai matar cikin dare taje chemist aka hada Mata magani yarinyar ce dai ba wacce tabi ta kanta nan suka kwanta don ba abunda suke bukatar yi fiye da bacci duk da zuwa yanzu bakin yarinyar ya kumbura sosai..

Koda asuba tayi da kyar suka iya sallah sannan suka koma bacci kan su tashi matar gidan ta fice wajen aikin ta saboda tasan dole suyi hutu sosai..ranar dai yan Gata suka zama don bacci suka wuni yi sallah kawai ke tada su basu wani damu da abinci ba kam duk da bakin ta Na Mata Zafi sosai sai dai tayi ta Zubda kwalla, Bayan baccin ya bar jikin su ne matar ce ta Fara yi wanka kan yarinyar.. Koda ta shiga wanka zama tayi kan dutsen wankan dake bandakin ba tare da ta cire Kayan ta ba, a zahiri bucket Na karfe da Ruwa ke ciki da cup Na wanka ta zubawa ido Amma a badini kuwa tunani take yi

"Ya Rabbi wacece ni daga ina nake gaba daya duniyar ta fice mini a rai komai ma ba son shi nake yi ba,Na rasa dalilin da yasa bana iya tuno komai a rayuwa Na sai suna Na Wanda shi din ma banda tabbacin haka ne,banyi hatsari ba bare ace kwakwalwa ta ta samu matsala Na kamu da ciwon mantau,shin banda iyaye ne ko dai ni din marainiyar ce ?" In ko ina da su meyasa ba Wanda ya taba nema Na, to ko dai shegiya ce ni in ko haka ne ai dole zan tuna baya na..wai ko da uwa ce ta mini baki kamar yadda kowa ke fadi inko haka ne na tabbata tsinenniya shiyasa kullum bala'e da fitina basu da wajen zuwa sai waje na,Gashi yanzu baki Na ciwo yake Amma saboda rashin Gata da asali Na rasa me saya mini magani.

Hawaye ta shareda Bayan hannun ta tana Mai Jan hanci da kuma jinjina wannan lamarin a ranta haka kawai ace mutum bai iya tuna komai sai sunan shi Wanda shima ba tabbas akan ta wannan wace iriyar kaddara ce iya sati biyu da suka wuce a rayuwar ta zata iya tunawa..ganin ba inda tunani zai kaita a hankali ta Fara cire Kayan jikin ta tana makalawa a katangar bandakin sannan ta wanko inner wears nata tare da gasa bakin ta duk da tana jin Zafi haka ta daure daga bisani tayi wanka sanin dama ita din ba kaya ne da ita ba duka duka basu wuce Kala hudu ba Gashi sun Bari a motar inda yan kidnappers suka riske su dole kayan jikin ta ta mayar tana fitowa ne ta karewa gidan kallo madaidaici ne yana nan dai bana masu kudi ba haka zalika bana talakawa ba sai dai da ganin gidan macece ke rike da shi Kai tsaye zata iya cewa gidan ba Na miji..alwala tayi jin an Fara kiraye-kirayen sallah'n magrib nan ta gabatar da sallah'n a brander'n dakin saboda akwai hasken Nepa a wajen sannan ta Nade sallayar tayi ciki saboda gudun kada sauro su gama da ita a waje tunda bata da Mai saya Mata magani.. tana shiga ta takure waje daya ganin matar gidan ta dawo Hala lokacin da take wanka ne kuma ta shigo da alama kuma labarin abunda ya faru da su aka bata saboda taji tana cewa Allah kiyaye gaba

"An wuni lafiya"

Ta fada Wa Mai gidan

"Lafiya kalau"

Ta amsa tana Mai kare Mata kallo sannan ta mayar da kallon ta ga matar da suka zo tare tace,

"Larai ita ce ko?"

"Ehh ita ce ina fatan ta miki?"

Kallon yarinyar ta kuma yi a Karo Na biyu sannan ta sauke numfashi tace

"Eh ba laifi Amma sai nake ganin kamar tayi yarinya".

" ah Haba shekarun ta 17 fa ba wani yarinya baki ga ma tana da halittar girma ba Ki bata nan da shekara biyu cikekkiyar budurwa zata zama".

Ita dai tana jin su Amma ta kasa cewa komai sai da ta tsinci muryar matar tana fadin,

"Meye sunan ki"?"

"Laylerh".

Ta fada kanta a kasa murmushi Mai sauti taji matar tayi Wanda ya sata dago kanta ta kalli matar sai ji tayi tace,

" Larai jira Na dauko miki kudin Ki Na San gobe zaki wuce".

Washe baki tayi kamar gonar auduga tana fadin "Ai kuwa"..

"Ya ilaheee kenan saida ni aka yi innalillah wannan din kuma wace ce Shikenan haka rayuwa ta zata kare Na zama kamar kwallon kafa duk Mai bukata zai buga"

Larai din ma tsintar ta tayi a hanya sati biyu da suka wuce nan ta ringa rokon Larai da ta taimaka Mata da kyar da dauke ta don duniya ba tabbas Ai kuwa ta gwammace yawo a titi da wahalar da Tasha a gidan saboda wanka ne kadai bata yiwa Larai kuma abinci ma sai ya game ta take bata..

Bangaren Larai din kuma ta kan yi safarar Mata a boye Wanda da yaran talakawa kawai take yi Gashi dama tayiwa Kawar ta alkawarin kawo Mata yarinya shiyasa da Allah ya hada ta da Laylerh ta karbe ta ta kawo ta ba tare da sanin ita Kawar tata nan zata ajiye ta ko gaba ita ma zata saida ta ba...

Fitowa tayi da kudi masu yawa ta mika Mata nan tayi godiya ganin matar ta fice a daki yasa ta kallon Laylerh daga sama har kasa tana fadin,

"Saura kada kiyi biyayya wallahi uban Ki zata ci don ta fini Zafi Anya ma ba uwa bace ta miki baki Kika shiga duniya saboda kullum cikin fitina kike nima Gashi yanzu ya Fara shafana Ai gwara Na bar Ki a nan nayi gaba kan rayuwa ta ta hallaka".

Ita dai Laylerh ido ta zuba Mata ta kuma fahimci duk duniya ba zagin da Larai ta iya fiye da cewa zata ci uban ta duk da kusan kullum tana fada Mata Kalmar yafi a Irga Amma duk sanda ta fada sai taji Zafi a ranta..

" kallon fa?mayya kawai wallahi kuruwata daci Gare shi yafi karfin Ki don ni wallahi idanuwan kin nan tsoro suke bani".

Kasa ta sauke idanun ta don Allah ya sani tana tsoron Larai kusan kullum sai ta duke ta tsaki Larai taja gami da diba Mata abinci cikin Wanda aka kawo musu ta tura Mata gaban ta kallon abincin tayi tana jinjina rashin imani irin Na Larai yau ko yaro Dan shekara uku Ai sai ya cinye ya nemi Kari bare ita da tasan da a kauye take

tuni tayi Aure Harda yara..cin abincin tayi don ba yadda ta iya sannan ta fitar da kwano tana kallon yadda Larai ke cin abincin gaban ta Wanda mutum biyu zasu ci har su rage..tana dawa tayi i'sha ta kwanta...

Washe gari da sassafe Larai ta gama shirin tafiya Bayan ta sallami kowa sai ta kalli Laylerh tana fad'in,

"Adai yiwa manya biyayya".

Karon farko kenan a rayuwar ta ta fada jikin Larai ta rungume tana fashewa da kuka saboda ita dai Larai kadai ta Sani a rayuwar ta ture ta Larai tayi tana fad'in,

" munafuka su din ce miki aka yi ba mutani bane?"

Tana gama fadar haka ta Kama hanyar fita cikin kuka Laylerh tace,

"Allah kiyaye hanya".

" Amin"

Tace saboda sanin wannan addu'ar tafi bukata a yanzu sannan ta fice abun ta..

Durkushewa tayi a wajen tana kuka Mai cin rai ko da matar ta dawo daga daka Larai kallo daya ta Mata Wanda ya sata hadiye kukan ta gami da mikewa..cigaba da tafiya matar tayi ba tare da ta juyo ta kalle ta ba tace,

"Ki shirya yau zaki Fara zuwa wajen aiki".

" aiki".

Ta maimaita a ran ta to wani irin aiki ne wannan da ba za'a tausyawa halin da take ciki ba a Bari sai ta warke sanin ba Mai bata amsa ya sata mikewa ta Debi Ruwa a buta ta wanke fuskar ta sannan ta nemi hijab ta saka da Slipper's tana jiran fitowar ta..bata dauki dogon lokaci ba ta fito rike da handbag nata tana Mikawa Laylerh da wuri ta Karba ita ko Key's da suke hannun ta ta rufo kofar da shi tayi gaba ba tare da tace da Laylerh ci kan Ki ba ganin haka ne ya sata bin Bayan ta da wuri suna fita ta rufe k'ofar da kwado hakan ne ya Dada tabbatarwa Laylerh cewa su kadai ne a gidan....

adaidaita ta tare tana fad'in Jan bolo suka shiga sai kallon yanayin garin Laylerh take yi Amma bata cewa komai,tafiya Mai Dan nisa suka yi kan taji tace a nan suna fita ta mika mishi kudi tayi gaba Laylerh na biye da ita suka shiga wani guri..

Ganin yadda kowa ke gaishe ta hakan ya tabbatar Mata da ita ce me wajen kenan a hotel zata yi aiki..hararar ta tayi gami da fisge jakar ta tana fadin,

"Mairo ga sabuwar ma'aikaciya a nuna Mata komai da komai"

Cikin girmamawa da tsoro tace,

"An gama ranki ya Dade".

Sannan ta juya tana kallon Laylerh tana mamakin ina madam nasu ta samo wannan kyakyawar yarinya sai dai hanci ne bata da shi Gata karama sauran ma duk sun kalle ta kowa ya koma bakin aikin sa ita ko bin ko ina take da kallo ganin yadda kowa ke aikin wahala Amma bata ji komai ba saboda ta San ba mummunar hannu ta fada ba duk da bata da tabbacin iya aikin hotel din zata ke yi don tsam madam d'in bata Mata Kama da mutumiyar arziki ba tafi ganin kamar ita ma tana shafarar Mata irin Kawar ta Larai..

In naga comments Na cigaba in kuma naji shiru Shikenan

Comment

Share

©Hafciey

[1/25, 5:35 AM] Hafciey Musa😘: *LAYLERH*

(The prettiest emerald)

Naga comments sosai Na gode sosai Allah bar kauna

Cikin restaurant mairo ta wuce da ita ganin safiya ce ya dace a tsaftace shi kan mutani su Fara zuwa cin abinci

"Kiyi mopping Na nan".ta fada tana nuna Mata wajen da zata yi mopping din da hannu.

Kai tsaye ta amsa da"ban iya ba".

'Daga curtains da su plate and spoon a wajen tayi sannan ta nuna Mata yadda zata yi mopping din gami da barin ta a wajen ta koma bakin aikin ta..Laylerh farawa tayi dai dai yadda aka nuna Mata Amma ba hakan take yi ba,madam din ce tazo

wucewa sai taga shirmen da Laylerh ke yi sai kace karamar yarinya don bata matse ruwan tsumman da take mopping din sosai shiyasa zaka ga ruwa a duk inda ta goge nan ta bude murya tana kiran

"Mairo".

Ba mairo da aka Kira kadai ba hatta da Laylerh sanda ta tsorata nan take jikin ta ya hau rawa don kallo daya zaka mata ka tabbatar da irin yara matsoratan nan ne wadanda basu tashi a gaban iyayen su ba shiyasa komai suke zaka ga ba sakewa a tsorace suke yin shi sai ga mairo ta fito da wuri ta durkusa a kasa

" Mairo kina ganin aikin da yarinyar nan take mini,me yasa baza Ki bata aiki dai dai Wanda ta iya ba?".

"Sorry ma'am jira nake yi ta gama wannan in Na bata breakfast sai Na nuna Mata wani aikin".ta Kai karshen zancen nata murya Na rawa

" break....me?"

Ta tambaya tana rike kwankwason ta tare da nyamusa fuska sannan ta mayar da kallon ta kan Laylerh ta kalle ta daga sama har kasa sannan ta nuna ta da yatsa tana fad'in,

"Dago idanun Ki, Ki kalli cikin ido Na wallahi duk Randa Kika kuskura aka baki abinci bada izini Na ba to Zan gwada miki ni din 'Yar Tasha ce don ni nan da kike gani duk wacce iyaye suka ce Mata je Ki zaki gani to irin mu take gani".

Maida kallon ta kan Mairo tayi sannan taja tsaki tana fad'in,

" ke kuma duk Randa Kika kuskura Kika bata abinci bada izini Na ba to wallahi a bakin aikin Ki kuma kin San I mean what I say".

Rusunar da Kai kasa tayi tana kallon tiles Na wajen tace,

"Sorry ma'am".

Wucewar ta tayi ta barsu a wajen suna bin Bayan ta da kallo sai dai ba wacce ta iya cewa komai a cikin su,Mairo ce ta daga kafar ta tayi kitchen nan Laylerh ta bita..

" kin iya yanka Ganye?"

"Eh"

Ta amsa Mata tana kallon ta don akwai ta da iya kallo kam sannan ta Lura ita ma tabbas tsoron wannan matar take ji..buhu ta jawo nan ta zubo alaiyaho idanu Laylerh ta bude don a zaton ta Dan dai dai za'a bata..

"Ki yi maza Ki yanka kafun ta dawo Kinji".

Kai ta gyada alamar to tana Mai tausayin kanta da kanta sannan ta zauna a hankali ta tankwashe kafar ta gami da cire hijab nata ta ajiye a gefe nan ta Fara gyara alaiyahon duk da yunwa take ji cuxx bata yi breakfast ba..ta jima tana yankawa sannan Mairo ta shigo kallon ta tayi tana fad'in,

" Kai har yanzu baki yanka dayawa ba wallahi in madam ta dawo ranki in yayi dubu sai ya baci".

Kwabe fuska tayi alamar zata Fara kukan ta Na gado tana danne kukar tace,

"Wallahi Aunty akwai wahala kuma Tun dazun nake yi Gashi yunwa nake ji".

Karo Na farko kenan a rayuwar ta da taga tausayin ta a fuskar Wata don yadda mairo tayi tabbas taji tausayin ta to Amma ba zata iya bata abinci ba

" ina zuwa".

Tace nan ta fice Laylerh kuma da ido ta raka Bayan ta ba jimawa sai Gata ta dawo da Wata wacce ita ma a wajen take aiki

"Laure Ki taya yarinyar nan aiki don Allah kuyi da jiki kan madam ta dawo kun gama".

Bata jira amsar su ba ta fice domin Komawa bakin aikin ta saboda ta daura Kayan miya a wuta su ko nan suka cigaba da aikin sai sauri suke yi domin cika umarnin Mairo da ta kasance shugaba a Gare su...Bayan irin 30mins sai ga mairo ta dawo cikin tsoro ta kalli sauran alaiyaho tana fad'in,

" har yanzu Baku gama ba?maza Laure tashi Ki bar Mata je Ki Kama wani aikin madam ta dawo".

Aiko jiki Na rawa Laure ta mike da wuri ta fice a kitchen din haka ma Mairo,a kofar kitchen din suka gamu da madam din kallon Tara saura kwata tayiwa mairo tana kesta chewing gum sannan tace,

"Ina yarinyar nan?"

Murya Na rawa Mairo tace,

"Tana ciki".

Bankade Mairo tayi tana murkuda duwawu irin Na 'yan bariki Tasa Kai cikin kitchen din idanu ta waro waje tana kallon alaiyahun da ya rage a gaban Laylerh

" ke wace irin shegiyar yarinya ce yanzu Tun fita Na har Na dawo baki gama ba?"

Ta karashe zance da bugawa Laylerh key'n hannun ta a goshi Wanda yake hade da key holder Na karfe Ai kuwa azaba sosai taji sai ta fashe da kuka dama gwana ce wajen kukan banza duk da ita ba yarinya bace bare da yanzu ta samu hujjar kukan cikin kuka ta fada cikin alaiyohu da suka yanka ta cigaba da kuka ,ganin kuka take yi yasa madam din Kai Mata dundu a baya Ai ba shiri ta mike waje ta nufa cikin rashin sanin inda zata ta wuce ta restaurant da mutani suka Fara taruwa domin yin breakfast ta nufi waje, customers din duk da ido suka rakata ganin madam din ta fito sai wani cikin su tace,

"Madam lafiya kuwa?Ai yarinya ce a bita a hankali".

Cikin salon son kare kanta da nuna tausayin ta ga Laylerh d'in sannan ta cusa musu tsanar ta a zukatar su tace,

" wallahi yarinyar irin yara masu mugun halin nan ne,me banyi wa yarinyar nan a duniya ba ko uwar da ta haife ta iyakaci Amma don kawai nace tayi sauri sai budan baki tayi zata zage ni".

"Ah wannan ba ta da tarbiya".

Wata ta fada

" tsam fa tarbiya kam babu wannan d'in ma Nike kokarin bata tarbiya".

"Allah kyauta".

" Ameen"

Tace tana jin dadin yadda taga sun yarda da zancen ta sannan ta koma ciki ta debo abinci cikin plate da nama ta nufi waje domin kaiwa Laylerh tana ji Wata Na fad'in,

"Gaskiya tana da zuciya Mai kyau duk da rashin kunyar yarinyar dubi abinci zata Kai Mata".

Murmushi tayi ta karasa ficewa,ita ko Laylerh ta hada Kai da gwiwa kuka sosai take yi jin wurin har ya tashi nan ta ajiye Mata abincin tana shafa kan ta tace,

" yi shiru abun Ki ki ci abinci".

Laylerh irin yara masu zuciyar nan ne shiyasa duk rarrashin duniya tayi Laylerh taki cin abincin daga karshe ta daga ta wuce ciki nan customers suka cigaba da zagin ta da irin mugun halin ta..

Sanda tayi kuka Mai Isar ta sannan ta Fara rabuke-rabuke gudun kada ta shiga madam din taci uwar ta nan dai ta shige suka cigaba da aiki Amma tsam ko lokacin sallah ba'a barin su suyi..

Bayan azahar customers suka Fara zuwa nan ogar tasu ta kalli Laylerh tana fad'in

"Biyo ni".

Binta tayi duk da a tsorace take da ita Amma ba yadda ta iya tsallaken titi suka nufa shagon wani gonjo suka shiga nan taji ance a duba Mata kaya dai dai ita..sosai tayi farin ciki ganin yau dai zata cire Kayan jikin ta da ya Kai kwana hudu nan aka zabo Mata skirt Na gonjo da wani Riga daban ta gwada yayi dai dai ita nan madam din ta tambayi kudin sa aka ce 1500 tace zata biya 1300 nan aka ce ta kawo ta biya

suka fita Laylerh ta bude bakin ta zata yi godiya ta tsinkayo muryar madam Na fad'in

" Ki bar murnar Na saya miki kaya wannan watan ba Zan biya Ki salary ba".

Kamar Tasa hannun a Kai tayi ta ihu haka taji nan suka koma hotel din suka Fara serving mutani Laylerh Na cikin masu serving saboda sun San ba aikin arziki zata iya ba Gashi yunwa duk ya nuna a jikin ta har Bayan asr Ana Abu daya da kyar ta samu ta zame jikin ta taje tayi azahar da la'asar din, karfe biyar Na yamma kuma aka Tara dumbin wanke wanke nan suka nufi backyard Na restaurant din inda a wajen ake girki da itache..su biyar ne suke wanke wanken uku Na wankewa kowa da ruwan kumfan shi da soso, biyu Na lailayewa Wanda Laylerh Na cikin masu daurayewan basu suka gama ba sanda aka Kira magrib.. ciki suka koma kowa ya Fara tattare Kayan sa sauran abincin kuma aka Sawa madam din a kula tare da hada Mata da manyan kuloli nan yan matan suka dubi Laylerh suna fad'in,

"Laylerh sai da safe ke kam Ki jira madam ta fito".

Murmushi tayi tana fad'in

" Allah bamu alkhairi ".

Nan duk suka fice ita ko zama tayi cikin restaurant din tana kallon masu wucewa a waje da yake akan titi yake tafi minti Ashirin sannan madam din ta fito waya a kunnen ta da alama waya take yi kuma ko da Wa take wayar yana da mahimmaci ba tare da ta cire wayar a kunnen ta ba kuma bata kalli Laylerh din ba tace,

" ki je waje Ki tare mana kake sannan Ki Debi coolers nan kisa a ciki".

Tana gama fadin haka ta koma ciki Laylerh kuma ta mike ta fice domin cika umarnin ta..ko yadda zata tare keken ma bata iya ba ta jima a titi sannan ta tare sanda Mai keken ne ya fito domin tayata Sa kulolin a napep suna gamawa madam din Na fitowa ita dai Laylerh ikon Allah take kallo saboda seat din duk ya cika da

tarkashe ita dai bata ga inda zasu zauna ba ga mamakin ta sai taga madam din ta zauna a gaba gefen Mai keke

"Malama Dan Allah shiga boot Ki zauna sauri nake".

Inaa ai bata iya ba sanda Mai keken ne ya tayata taci wahala kam da suna tafiya saboda duk inda aka zo gargada sai ta bugu da haka suka isa gida Mai keke ya sauke musu Kayan su Laylerh kuma tana shigarwa gida da kyar saboda sun fi karfin ta, madam din kuma ta biya shi kudin sa...

Tana gama shigar da Kayan ta zauna bakin dakalin dakin sai taji madam din Na kiran ta daga waje da gudu taje sai jin ta tayi tace biyo ni ba musu ta bita..a kalla gida biyu suka wuce a Na ukun taga ta tsaya nan ta Fara knocking tana fadin,

" oga Emeka nice zo Ka bude mini kofa".

Aiko tana rufe bakin ta ya bude kofar yana fad'in

"Me ne ma zaki zo Ki dami mutum da Daren nan".

Ya fada cikin hausar sa da bai kware ba ita kuma sanin wani Abu take nema a wajen sa sai tayi murmushi tana fad'in,

" yanzu fa karfe takwas ne Ai dare bai yi ba".

Fuskar sa a daure yace,

"To mene ne fadi naji don ke kamar tauraruwa Mai wutsiya ce ganin Ki ba alkhairi ba".

Tsam bata ji zafin Kalmar da ya fada Mata ba don ta San dole ko ba yau ba zata Rama Amma tunda yanzu Abu take so dole tayi shiru.

" oga Emeka wannan yarinyar da take mini aiki ne to kuma yau ina da bako kasan ba inda zata kwana a gidan".

"To ni kuma sai Na miki yaya?"

"Dan Allah ta kwana a dakin Ka kayi hak'uri".

Kallon Laylerh daga sama har kasa yayi sannan yace,

" ba matsala ".

'Na gode sosai oga Emeka".

" sai kace mutumiyar arziki ".

Ita dai bata tanka shi ba ta juya saboda dukkan su 'yan bariki ne..gaba daya kafafun Laylerh Na Neman gagara daukar ta jin Wai wani kato aka kawo mishi ita ta kwana a dakin shi katse Mata tunani yayi da fad'in

" come in".

Da bismillah ta shiga gidan sai ji tayi ya mayar da kofar ya rufe Harda sa sakata nan ya wuce tana kallon sa ba Babba sosai bane don a kalla ba zai wuce shekara talatin ba,karewa gidan kallo tayi inda daki daya ne tak a gidan sai toilet ganin ya nufi daki sai ta bishi don ita a zaton ta akwai Mata a gidan Amma tana shiga dakin taga

karamin katifa ce sai hanger da ya rataye Kayan shi kenan hakan Na nufin shi kadai ke rayuwa a gidan..

"Seat down".ya fadi yana nuna Mata carpet da hannu

Jikin ta har rawa yake yi ta zauna don ba karamin yunwa take ji ba shi ko kallon ta yayi yace,

" are you sick".

Kai ta girgiza mishi sannan tace,

"Ina jin yunwa".

" hungry madam naki bata baki abinci bane?"

Kasa ta sauke kanta bata ce da shi komai ba yana ganin haka ya mike a gefen ta ya dauki karamin pot da yake girki a ciki ya tura Mata ragowar taliya da waken da ya dafa ya bata pure water daya da sauri ta Fara ci kamar ba gobe shi ko fita yayi ya zaga kan ya dawo ta cinye tas sosai ta bashi mamaki nan ya bata guntun biredi shima Karba tayi ta cinye nan ya fice a gidan gaba daya, jin ya fice ne Bayan abincin cikin ta yayi digesting sai ta lallaba ta nufi kofar sakata Tasa sannan ta dawo tiolet ta wuce nan ta wasa Ruwa ganin sabulu a ciki sai ta wanke Kayan ta da ta cire dazun a restaurant ta shanya akan gini sannan ta koma ciki tayi i'sha akan dankwalin ta ta daura da shafa'i da wutiri jin bacci ya Fara fisgan ta Amma tana tsoron yi nan ta koma ta cire sakatar sannan ta dawo dakin bacci barawo bata San sanda ya dauke ta ba..

Cikin bacci taji an buga kofar da karfi a razane ta mike ta fita a dakin sai ganin oga Emeka tayi a buge kallon ta yayi yace,

"Who the hail are you?"

Bakin ta Na rawa tace,

"Nice wacce neighbor'n Ka ta kawo maka dazun".

Tsaki ya buga sannan ya nufi daki yana tangal tangal irin Na bugaggu direct katifa ya fada yana kallon sama ita ko tsoro duk ya rufe ta tsayuwa tayi akan shi tana kallon shi har kafafun ta suka yi tsami can taji ya Fara gwarti alamar bacci yayi nisa nan ta zauna bacci Na fisgar ta tana farkawa da haka har tayi bacci Mai nauyi....

Washe gari karfe 4:30 suka ji an Fara buga kofar gidan ita ce farkon tashi shi ko mikewa yayi yana dafe kanshi da yake mishi ciwo nyamusa fuska yayi sannan ya dube ta yace,

" go and have a look".

Cikin yanayin bacci da bai sake ta ba da kuma sanyin jiki irin nata tayi kalar tausayi tace,

"Ina tsoro".

Tsaki yaja sannan ya mike tabi Bayan shi da wuri yana budewa yaga madam ce wani tsakin ya kuma ja ita kuma cewa tayi

" oga Emeka good morning ".

Ba tare da ya amsa ba yace,

" what do you want?"

"Yarinyar nan"

ta fada tana fisge hannun Laylerh ganin sun fice sai ya maida kofar sa ya rufe Laylerh kuma kallon kofar tayi tana Mai jin oga Emeka ya burge ta saboda a yanzu ina za'a bar mace da Na miji su kwana a daki daya ba abunda ya shiga tsakanin su bare shi da yake ba musulmi ba tabbas yana cikin mutanin da zata Irga sun Mata halacci a rayuwar ta..zungure kanta da aka yi ne ya dawo da ita hayyacin ta nan suka shiga keke suka nufi wajen sana'ar su Amma da alama sauran duk basu zo ba har Mairo.. Backyard ta kaita inda ta nuna Mata tukunya lamba hamsin tace ta hura wuta,tukunyar irin masu kafar nan ne so ba sai an daura a murhu ba itace kawai zata sa Ai tukunyar sai Jan shi tayi don ba zata iya dauka ba da kyar ta tsaida shi da kafar shi ta Fara kiciniyar hura wutar..

Durkusawa tayi ta Fara kesta ashana Bayan ta sa icce da ledoji har da su tarkashen take away da basu da kyau Ai ko sanda ta kusa karar da ashana kan ya Kama kasancewar wurin akwai iskar asuba..tana ganin ya Kama Harda guntun murmushin ta sannan ta mike ta Fara jido Ruwa a fanfo Wanda tuni Bayan ta ya rike don wahala saura bai wuci kafa biyu ta cika ba taji an shiga sallah a masallacin dake kusa da su nan ta ajiye bucket din ta shimfida Dan kwalin ta zata tada sallah kenan madam din ta fito tana fad'in,

"Kin daura?"

"Eh"

Bude tukunyar tayi sai gani tayi ruwar bai cika tukunyar ba

"Ba cewa nayi Ki cika tukunyar in ya tafasa Ki rage Ki bar dai dai shinkafar ba"

"Aunty naji Ana sallah....."

Bata barta ta Kai karshen zancen ba tace

"To sannu wacce ta fini sanin Allah Ai Kinga ni ba musulma bace ko?"

"A'a"

"Rufe mini baki Ki wuce Ki cika mini tukunya".

Da wuri ta dauki bucket ta nufi famfo jin an idar da sallah ta cika tukunyar tazo zata sake tada sallah madam din ta kuma fitowa tana fad'in,

" ikon Allah wallahi in baki maida hankali ba uban Ki zanci Wa zaki nunawa son addini".

Cikin Zubda hawaye tace,

"Wallahi Aunty Na cika".

" da Kika cika sai aka ce miki aikin Ki ya kare?"

Kai ta girgiza

"To Kije ciki Ki auna shinkafa mudu Ashirin sannan Ki wanke in ya tafasa Ki zuba".

" Ayya Aunty sallah..... ".

Kasa karasa maganar tayi saboda robar hannun ta da ta buga Mata a Kai har ya fashe sannan ta fusgo ta tace,

" daga yau in ina magana kada naji kince wani Abu".

Da kyar ta hadiye nyawu saboda shakar ta da tayi sai Kai ta gyada alamar to magana kam ya gagare ta..sake ta tayi nan ta wuce ciki ta debo shinkafar jin yayi nauyi sai ta Fara Jan baf da Tasa shinkafar a ciki Ai dundu ta sha"Wato so kike Ki fasa mini robobi ko,dazun Na fasa daya a kan Ki yanzu kuma Bari Ki fasa wani ko". Allah ma ya so ta ta iso waje nan ta riga diban Ruwa tana wankewa tare da Kara icce a murhu don ya tafasa da wuri tana gamawa ta nufi sallah don har gari ya Fara haske kuma yanzu kam tayi alkawarin koma me zata Mata sai tayi sallah Ai ko tana raka'a Na biyu ta fito taga ta bar Mata shinkafa a ruwa bulala ta wuce nema Wanda Laylerh din bata sani ba,tana idar da rak'atainil fajir ta daura da farillah tana zaman tahiya madam ta fito daidai ta sallame ta karaso inda take Ai nan ta Fara jibgar ta kamar aiko ta aka yi sanda tayi Mai Isar ta don kanta ta barta ita ko a wajen ta kwanta tana kuka Mai cin rai

"Ya Rabbi wannan wace iriyar Mata ce da ba Allah a zuciyar ta ko addini ba zata bar mutum yayi ba,to kodai gaskiyar Aunty Larai ce da tace uwa ce ta Mini baki in ba haka ba azabar tayi yawa Ai".

Kuka sosai take yi ganin ruwan ya Fara tafasa da wuri ta tashi gudun shan wani dukan ta rage ruwar sannan Tasa shinkafa dai dai lokacin su Mairo suka zo gaisuwa suka yi kowa ya Kama aikin sa ita ko tattase da tarugu Mai yawa aka kawo Mata aikin shi tana yi tana kuka kamar yarinya sannan tana azkhar da ta haddace tana Gamawa aka hada ta da yaro ta Kai nika dai dai sun dawo shinkafar ya nuna nan suka debo manyan coolers kuma lokacin hannun ta ya Fara radadi bare da suke kwashe shinkafa yaje gangan wuta har kuka sanda ta yi kowa mamakin saurin kukan ta yake don a ganin su yanzu Ai ta wuce kuka..

Daga nan sauran aikin su mairo ne suka cigaba ita ko 'Yar aika ta dawo don akwai karamin kasuwa kusa dasu kan abun hamsin sai su aike ta kasuwa.. Kafar ta kusan 6 a wajen Ai sai Bayan azahar ta samu kanta sai lokacin kuma suka karya sannan aka Fara kaiwa customers abinci..

Yau ma karfe biyar suka Tara wanke-wanke suka yi Bayan magrib kuma kowa ya gama shiri sai suka ce

"Laylerh sai gobe".

" Allah bamu alkhairi ".

Tace don ita kadai ta San me take ji Bayan ta kamar zai tsage...

Bayan Mai keke ya ajiye su a kofar gidan su sai taga madam din ta nufi gidan oga Emeka da yake yau basu dawo da tarkashe ba bugu uku ta mishi ya bude

" Wai me ne ma?"

"Am oga Emeka yau ma Na kawo ta".

" Ai yau baki da bako don haka Ki tafi da ita haka jiya Kika yi ta buga mini kofa ina bacci ba Zan iya ba".

"Ayya dai oga...."

"Ke Na San Ki ciki da waje fa ke din ba mutumiyar arziki bace".

" buhun uba Emeka har ni zaka ce Ka sanni ciki da waje,to wallahi yau sai Ka fada mini a wani daki Ka sanni".

"Yo ke Ai baki Kai Na San Ki ba don nasan maza kalilan ne baki sani ba".

" kar Ka fada mini zancen banza don kawai Na kawo yarinya kwana a wajen Ka baka ji dadi ba ma Na maka kyautar yarinya ".

" Ehhh bana so".

Yana gama fadar haka ya koma ciki sai Gashi ya fito Mikawa Laylerh Kayan ta da ta shanya yayi sannan ya koma ya rufo kofar da karfi cikin takaici ta rankwashe Laylerh sannan tayi gaba..

Dafe wajen Laylerh tayi tana hawaye tabi Bayan ta suka nufi gida..koda suka shiga tabarma da net ta jefa Mata waje tana fad'in,

"Kuma in baki shiga net din ba ya rage naki don wallahi in sauro ya cije Ki ba jinya Zan miki ba".

Tana gama fad'in haka ta rufo kofar ta Laylerh ko shimfida tabarma tayi ta ajiye Kayan ta sannan ta nufi toilet wanka tayi da alwala sannan tayi shafa'i da wuri tana gamawa ta shiga net tare da yin filo da Kayan ta da ta wanke a gidan oga Emeka duk da a tsorace take da kwanan waje Amma da yake ta gaji sosai ba dadewa bacci ya dauke ta....

Comment

Share

©Hafciey Musa

[1/25, 5:35 AM] Hafciey Musa😘: *□LAYLERH□*

(The prettiest emerald)

Firgita tayi da sauri ta tashi jin an watsa Mata ruwan sanyi a jiki Gashi dama sai kudundunewa take yi a net din don sanyin asuba ya Fara sauka madam ta gani rike da bucket tana fad'in,

"Ah kin samu waje sannu Wato nice Zan zo nayi ta jiran Ki ko?".

Tana Zubda hawaye tace,

" yi hak'uri ".

Sannan ta mike jikin ta tsam ba kuzari Kayan ta ta dauka ta nufi bandaki a hankali take cire Kayan sanyi ko har kashin jikin ta take yi shiyasa ma ta Fara rawan sanyi har hakoran ta rawa suke ta hanyar gogan juna sai Kat Kat Kat zaka ke ji..

" Wayyo Allah Na sanyi nake ji".

Ta fada tana yarfa hannun da wuri ta karisa cire Kayan ta canza sannan ta shanya su a ginin bandakin ta fito da gudu jin ta Fara kwala Mata Kira..kallon ta daga sama har kasa tayi tana fad'in,

"Hijab din kam ba zaki canza bane Abu duk tsami yake yi kullum da shi kike wuni baki cirewa sai kace wani abun arziki ne a kirjin Ki da kike boyewa".

Ita maganar kunya ta bata don haka ta rike bakin hijab d'in tana wasa da shi sai da ta sake daka Mata tsawa tace,

" Wai bada ke nake magana bane?"

"Ba....ni.....da.....shi".

Ta Fara murya Na rawa tsaki kawai taja sannan tayi gaba nan Laylerh ta bita a baya gaba daya rawan sanyi take yi..suna isa ta Fara aikin ta irin Na jiya bata jira ance tayi ba Bayan ta zuba shinkafa sai tayi sallah zuciyar ta fal farin ciki yau dai ba zata sha duka ba..

Yau ma sanda gari ya Fara wayewa kan su mairo suka zo Laure ce ta dube ta tana fad'in,

"Laylerh Ai hijab nan yayi Dotti dayawa Ki canza wani mana".

Kai mairo da ke soya nama ta daga ta kalli Laylerh din tana jiran taji amsar da zata bayar

"Aunty Laure Ai bani da shi".

Shiru duk suka yi inda suka zuba Mata ido Na wasu dakiku kan ko wacce ta koma bakin aikin ta ba tare da sunce da ita komai ba sai azumi ce tace,

" to tunda omo'n da nayi wanke-wanke da shi ya rage Ki cire sai Ki wanke Ki shanya zuwa mu gama aiki zai bushe sai Ki maida jikin Ki".

"Ina tsoron madam zata ce omo'n ta".

" kada Ki damu ta fita".

Mairo da Laure dai da ido suke bin su ba wacce tace Kala nan Laylerh din ta wanke hijab din ta shanya Ai ko Dotti kam yayi don sanda ruwan ya koma baki sannan ta dawo cikin su suna aiki Ana Dan taba hira Rabin hankalin ta ko Na kan hijab nata don gani take kamar tsirara take sai ma hade cinyar ta da kirjin ta tayi da suka fahimci haka sai suka cire idon su a kanta saboda lokacin ta ne ko wacce budurwa tayi nata kuma gaba ko ance tayi ba zata yi ba..

Yau dai komai normal yake tafiya kuma duk sun sake da yake ta fita shiyasa ma yau Laylerh bata sha aika sosai ba kuma taci abinci on time an kuma yi warning nata kan cewa ko an tambaye ta tace bata ci ba...

Serving Na customers suka Fara yi inda take kallon tsanar ta karara a idon wasu da alama jiya suna nan ta gwada bakin halin ta sai bata damu da su ba..sai Bayan sun idar da sallar azahar madam din ta dawo zuwa lokacin kuma hijab Na Laylerh ya bushe har ta saka komai neat ta samu sai tace yau ayi tuwon masara kadan nan suka koma kitchen Laylerh dai nata idanu har aka yi talge don zata iya rantsewa bata taba ganin irin tuwon ba nan madam din tace abawa Laylerh ta tuka har kuka tayiwa su Mairo tana rantse musu da Allah cewa bata iya ba..to daman tuwon masara kam Ka iya ma yaya bare baka iya ba aiko gudaje iya gudaje yayi gaba daya hankalin su ya tashi kowa Na tsoron irin hukuncin da zata yiwa Laylerh din...

 Koda madam ta fitoTana ganin yadda tuwon ya dawo tayi ihu gami da debe Laylerh da wani gigitacce Marin da yasa taga walkiya har kasa ta fadi.

"Shegiya Mai bakin Zuciya ni zaki batawa kasuwa don bakin hali yanzu ya zanyi da customers da zasu zo after asr".

Duk shiru suka yi kowa kan shi a kasa ba Wanda ya isa cewa komai ball tayi da tukunyar din ya zube kasa sannan ta nemo Mara ta Debi tuwon cikin tukunyar

sannan ta nufi Laylerh dake durkushe tana kuka,tafin hannunta ta bude ta zuba Mata wani Kara ta sake sai Gata ta kwanta sumemmiya...

Dukkan su rintse idanu suka yi don tabbas wannan yaci gaban mugunta rashin tsoron Allah ne kuma kamar so take taga Bayan Laylerh din

" Mairo kiyi maza Ki daura mini wani tuwon".

Ta fada lokacin da ta juyawa ta koma ciki tana huci kamar mayunwaciyar zaki mairo ko daura wani ruwan tayi ganin ta shige ciki duk suka yi kan ta suna kiran sunan ta.

"Laylerh! Laylerh".

Inaa bata ma San suna yi ba dole Laure Tasa ta a cinya azumi ko ta debo ruwa aka watsa Mata Mairo ko Zuma ta dubo cikin kitchen nasu tazo ta shafa Mata a hannun da kuka ta farfado nan suka Fara rarrashin ta zuwa lokacin har hannun ya tashi,ko tayi shiru in taga hannun sai ta fashe da kuka...

Ranar dai Mai hannun daya ta zama don alwala ma da kyar take yi...

****

" ohk ma'am in sha Allah ba za'a samu matsala ba".

Mikewa tayi gami da fita backyard nan ta Kira duk masu aiki a karkashin ta yau dai duk sunga sauyi a fuskar ta don sosai take farin ciki

"Mairo Hajiya kaltume ce ta kawo contract Na auren daughter'n ta".

Washe baki Mairo tayi tana fadin,

" ah alhamdulillah gaskiya naji dadi".

"Hmm Ki Bari kawai kin San matan manyan nan Ai wallahi Na tabbata in muka musu abunda ran su ke so ba karamin samu zamu yi ba".

Ita dai Laylerh abunda ta fahimta a nan shine an kawo mudu contract Na girkin gidan biki,to ita din ma dai dadi taji tunda yanzu kam madam din ba zata ke wuni da su ba..Laure ce ta katse Mata tunani da fad'in,

" to yanzu yaushe ne za'a Fara bikin?"

"Hmm gobe ne fa wallahi sunyi booking Na wani ne so sai yayi failing nasu bisa samun contract da yafi nasu shiyasa suke tambaya ko Zan iya".

" kenan yanzu kasuwa zamu wuce ko?"

"Ehh yanzu daga kasuwan ma gidan zamu wuce don gobe da safe snacks za'a musu sannan abincin gidan Aure lunch and dinner mu zamu riga yi".

" to madam ina ji ni,ke,Laure sai muje in yaso sai mu bar Laylerh da azumi da sauran yan shago su cigaba da running business din ko?"

"Wa wallahi kafa ta kafar yarinyar nan,Ai in muka bar ta a nan kan mu dawo customers duk guduwa zasu yi".

" ohk to kuje Ku uku ni kuma Zan tsaya a nan din".Cewar mairo

"Better duk Ku shirya kasuwa zamu shiga".

Alert taji a wayar ta nan suka nufi kasuwa Laylerh sai kallon kasuwar take yi don Babban kasuwa ne Gashi sai uban shopping suke yi da kyar suka kammala Gashi dare yayi shiyasa suka fasa zuwa gidan bikin sai gobe kawai..

Yau ma dai a wajen ta kwana cikin net Washe gari da sassafe driver yazo Daukan su da Kayan su...tafiya sosai suka yi kan su shigo gidan

" wow"

Laylerh ta furta har sanda madam din ta zungure ta..sosai gidan yayi kyau da tsari tsaya zayyana shi ma bata lokaci ne nan driver yayi parking gate man yazo suka fitar da Kayan tare..

Tana sauke kafar ta a motar ta Fara bin gidan da kallo Harda rike kwankwaso wannan shine mafi kyawu da girman gidan da ta taba kallo a rayuwar ta,yanzu mutum daya ke da wannan gidan shi ko wani irin aiki yake yi..jin an Kama hannun ta ne ya dawo da ita daga tunanin da ta fada

"Ban son kauyanci fa".

Hannun ta Laure ta rike suna biye da madam din har main entrance Na gidan nan suka shiga mutuwar tsaye su Kayi ganin tsaruwar falon..ganin madam din ta zauna sai duk suka zauna nan aka kawo musu abun tabawa su dai ganin Hajiyar su bata ci Ai dole su hakura.. Wata kyakyawar budurwa ce ke saukowa daga benen gidan hannun ta dauke da waya duk hankalin ta Na kan wayar Laylerh ko bin ta da kallo take yi tana yaba kyawun ta a zuciyar ta,sanda ta karasa saukowa sannan ta Lura da su nan ta musu sannu sannan ta fice har ta fice din kuma idanun Laylerh a kanta yake..

Can sai ga Wata dottijuwa ta sauko ita ma kyakyawa ce da gani yarinyar 'Yar ta ce don kamanni dake tsakanin su nan ta zauna kan kujera tare da d'an sake fuska

" Barka da fitowa Hajiya ".madam ta fada kan ta a kasa Laylerh ko murmushi tayi a zuciyar ta tace " gaba ma da gaban ta Ai".

" Yauwa Ince kune caters din?"

"Eh mu ne".

Nan Laure da Laylerh suka gaishe ta duk da ido ta bi su tana nazartar ko wacce a cikin su Bayan dogon nazari sannan tace,

" Khadija".

Wata maid ce ta fito nan tace ta nuna musu kitchen su Fara aiki da "to" ta amsa sannan suka nufi wajen Ai ko nan suka tarar da mutani dayawa kowa Na aikin gaban sa nan suka Fara nasu ta hanyar juye fulawan a baf da duk wani Kayan hadin suka kwaba sai wajen yankawa ne haka kawai Laylerh ta tsinci kanta da iya styles Na yankan iri-iri Wanda ya janyo hankalin mutani dayawa Gare ta ita kanta madam din mamaki tayi don ko ita bata iya irin shi ba Ana cikin haka sai ga Hajiyar ta fito ita ma jinjinawa Laylerh tayi madam ko sai cewa tayi,

"Ai horo Mai kyau nake yiwa yaran shago Na shiyasa ba abunda basu iya ba".

" kin kyauta".

Cewar Hajiyar sannan ta juya to koma inda ta fito nan Laylerh taci gaba da yi suna soyawa..ganin aikin da gaske bai da niyar karewa sai Laure da madam din suka cigaba da yin irin Wanda suka iya Laylerh ma Na yi Amma a haka har dare sannan suka gama nan suka nufi bangaren Hajiyar domin sallamar ta..

Kallon Laylerh tayi sannan tace

"Me kike da suna?"

"Laylerh".

" gaskiya Laylerh Na jinjinawa aikin ki sosai shiyasa ma har nayi sha'awar miki kyau ta".

Kala bata ce ba sai ma lumshe idanu da tayi ta bude su kan madam tsantsar bacin rai da bakin ciki ta hango shimfide a fuskar ta,tana kuma Mata kallon yau taki ta kare

"Zo".Hajiyar tace da kyar ta iya Jan kafar ta ta nufe ta,bude hannun ta tayi sannan Tasa Mata kudi Wanda bata San nawa bane gami da cewa

" gobe in za'a zo azo da yarinyar nan".

Sannan ta juya ta koma ciki madam ko Jan hannun Laylerh tayi suka fice Laure Na biye da su a baya ko ta kan driver da aka ce zai maida su bata bi ba suna fita tace,

"Shegiya mayya kawai don uban Ki asirce su Kika yi ko yau ko sai Na kusa hallaka Ki,akan me the whole me Zan Kai Ki waje ace ba za'a yi recognizing Na present Na ba sai ke Bayan nice Na Kai Ki".

Tana kaiwa Aya ta hau jibgar ta a kofar gidan, Laure dai ta tausaya Mata Amma bata da bakin magana karshe ma hada goshin Laylerh da bango tayi Ai take ya fashe nan ta fashe da kuka..napep suka tare suka nufi gida Laylerh sai kuka take yi Laure suka Fara saukewa sannan suka nufi gida suna isa ta kwace kudin ta Irga nan taga dubu biyar ne kuma ko sisi bata bata ba..

Ganin ta shiga ta rufo kofar ta sai ta nufi bandaki ta wasa Ruwa sannan ta wanke jongon ta da hijab don gobe da shi take son Komawa gidan bikin tana gamawa tayi activities da take yi kan ta kwanta bacci sannan ta kwanta..

Saboda ta sa abun a ranta sai Gashi ta Riga madam d'in tashi nan ko ta ji goshin ta sosai ya kumbura bakin kuma ya bare tana jin Zafi a wajen da wuri Tasa gonjon ta kasancewar yanayin hunturu ne ma yasa ya bushe sannan ta ajiye Wanda ta cire Harda wanke slippers nata yau so take taje gidan bikin fes fes..sallah tayi Bayan ta idar madam d'in ta fito tace su tafi nan ko suka fice Amma restaurant suka Fara zuwa sanda suka kusa gama aikin sannan ta Tara su dukka tace,

"Zanje inda aka bani contract sai dai yau ba zanje da yarinyar nan ba duk da sunce aje da ita Amma zance musu bata jin dadi".

" ma'am kina ganin hakan ba zai kawo matsala ba?Kije da ita kawai Amma she should be under your control ".

Shiru tayi tana nazartar maganar sannan ta dubi Laylerh din gami da rike kunnen ta tace,

" wallahi kada Ki kuskura yau kiyi wani Abu bada izini Na ba in ba haka ba wannan goshin naki sai Na miki Wanda yafi shi ".

Tana hawaye tace,

" in sha Allah ba Zan yi ba".

Nan ta sake Mata kunnen ta sannan suka fice irin Na jiya da driver.. Yau dai aikin abinci ne kuma tunda suka Fara ta Fara jin zazzabi Amma take daurewa saboda sanin halin madam din,Hajiyar Na fitowa ta Gan ta nan tace

" subhanallah baki da lafiya ne".

Da kyar ta iya d'aga kanta nan tace tazo a kaita asibiti Ai nan take ran madam ya baci ta ma rasa me take yi...

Hajiyar kuma driver ta bawa kudi tace ya kaita asibiti madaidaici suna isa ya taimaka Mata ta fito

"Ba Zan iya tafiya ba".

Hannun ta ya rike suka nufi emergency suna isa ya zaunar da ita sannan ya nufi wajen yankan Kati Bayan an bude Mata folder ne sai ya dawo ya zauna kusa da ita hankalin sa duk Na kan tv'n dake waiting room din ita ko kwanciya tayi akan dogon kujerun da ake ajiyewa domin masu ganin Likita..

Kasancewar sun samu mutani dayawa a gaban su dole suka jira har layi yazo kan su Ana kiran sunan ta ya tallafa Mata ta mike sannan ya kaita har ciki ya ajiye ta kan chair dake kallon Na doctor sannan ya juya ya fita..

Folder'n ta doctor ya duba sannan ya maida kallon sa kan ta yana fad'in,

" me ke damun ki"

"Zazzabi nake ji".

" Tun yaushe ya Fara kuma akwai amai ne".

"Ya kwana biyu Amma yana yi ya Bari sai dai bana amai".

Rubutu yake yi kan folder'n ta ba tare da ya kalle ta ba yace,

" kinje asibiti ko chemist tunda ya Fara ko kin sha wani magani".

Kai ta girgiza nan ya gama rubuce-rubucen shi sannan yace

"Zamu sa miki Ruwa sannan Na rubuta miki magani sai kuje Ku saya".

Hannu ta Mika ta karbi folder'n da yake mika Mata sai yace,

" in kin fita Ki Kira Fatima Hamza".

To tace don ta fahimci ita ce next person da zai duba tana fita ko taja mishi kofa sannan tace ance Fatima Hamza taje..driver Na ganin ta ya nufe ta yana tambayar ta me aka ce nan ta fada mishi.. Kiran Hajiyar yayi ya sanar Mata abunda aka ce nan tace ba damuwa su sa Mata ruwan..

Maganin yaje ya sayo sannan aka bata gado don ruwan har leda uku ne aka sa Mata Na farko tare da Mata alluran bacci ba jimawa ko bacci ya dauke ta..

A hankali yaga ta Fara motsawa alamar zata tashi nan ya jawo kujerar sa Wanda yake Na zaman masu jinya ne kusa da ita,ita ko nauyi idanun ta suka yi Mata a hankali ta bude su ta zuba kan shi sai jero Mata sannu yake da kyar ta mike don taji sauki sosai Amma kuma jikin ta ba karfi

"Na gode".

Tace da shi tana jingunuwa da jikin gadon asibitin tana kallon dakin da mutani ke ciki akalla gado Ashirin kuma daga yanayin garin ta San yamma yayi.. Daga kanta sama tayi tana kallon ruwan da ake Kara mata ganin saura kadan ya kare sai ta sauke ajiyar Zuciya ko ba komai zata Rama sallolin da ake bin ta..

" tunda kin tashi Bari naje bakin gate Na sayo miki abinci kan ruwan ya kare dama ganin kina bacci ne yasa ban sayo miki ba".

"To"

Tace don tabbas yunwa take ji nan ya fice ita ko bin ko wani gado take yi da ido har ta sauke idanun ta kan Wata yarinya da zasu yi sa'a.

"Umma Nifa ba Zan iya ci da hannu Na ba".

Yarinyar ta fada cikin shagwaba

" to matso kusa Na baki Mama Na".

Matsowa tayi gami da kwanciya jikin Maman tace,

"Shiyasa nake son Ki".

" nima haka".

Ta fada tana Kai Mata peck a goshi..

"Uwa!uwa!shin ni ina tawa uwar ta shige ta bar ni ni daya tunda dai ba daga bishiya Na fado ba kila dai ni din shegiya ce?".

Da wuri ta girgiza kan ta tana fad'in,

" Ai ko shegiya ce uwa kam dole ta so ni duk lalacewa,Yar ilahee what have I done wong da nayi deserving kaddara irin wannan, ba uwa ba uba ba yan uwa sai uwar daki wacce tsam zuciyar ta ba Allah..mutum Na jinya a asibiti ace ba wani nashi a kusa da zai Lura da shi sai wasu mutani Na daban da basu Santa ba,basu San Asalin ta ba suka taimaka Mata in sha Allah har ta koma ga Allah ba zata daina musu addu'a ba..

Tsam tayi nisa a tunani bata San ruwan ta ya kare ba har ya Fara Jan jinin ta sanda taji alamar Ruwa da wuri ta dubi wajen sai ganin jini tayi,kallon matar dake kusa da bed nata tayi wacce take gyara daurin zanin ta Bayan ta gama karkabe bed da Mara lafiyar ta ke kai tace,

"Ayya Aunty Na Ki Kira azo a cire mini ruwan nan".

" ohk"

Tace sannan ta fice nan ta dawo da Wata Yar practical ta cire Mata nan driver ya dawo da take away a hannun sa..

"Ayya ina ne toilet Zan wanke hannuna ya baci da jini".

Da yake dakin ward ne ba toilet a ciki sai a waje nan suka fita ya nuna Mata..shiga tayi ta wanke hannun ta da bakin ta sannan ta fito tana kallon wadanda suke shan Iskan yamma a harabar asibitin kan ta nufi ciki..abincin ya bata nan taci sanda ta koshi sannan ta sha Ruwa sai ta koma toilet d'in tayi alwala tana fita ta roki Wata sallaya tayi azahar da la'asar sannan ta koma cikin dakin ta samu yana zaune nan ta zauna a bakin gadon duk basu cewa komai sai hayaniyar mutanin dakin dake tashi..

Magrib nayi yace Mata Bari yayi sallah a masallacin asibitin ita ma waje ta koma tayi sallah bata dawo ba sanda tayi i'sha sannan ta dawo Amma shi bai dawo ba..kwanciya tayi ba jimawa sai Gashi ya shigo da take away zama yayi yana fad'in,

" tashi kici wannan sai Na Kira a maida miki ruwan da ya saura Ince dai kinyi i'sha?"

"Eh".

Tace tana mikewa kadan taci ta ture tace ta koshi nan ya Kira aka daura Mata ruwan..Kallon sa tayi sannan tace,

" ba zaka je gida ba kada a neme Ka naga dare yayi".

"Kada Ki damu iyalai Na ba a nan suke ba kuma Hajiya tace Na kwana da ke".

" to yanzu a zaune zaka kwana?"

"A'a Kinga dakin Na Mata ne ba yadda za'a yi Na kwana cikin Ku don haka zanje masallaci Na kwana".

" to sai da safe".

"Yauwa Allah tashe mu lafiya,in kuma kina da bukatar wani Abu cikin dare Ki roki yan uwan Ki Na dakin su miki Kinji?"

"To".

" ga Ruwa kuma Na ajiye miki sauran abincin ma in Kinji yunwa kici".

"Na gode".

Daga nan ya fice ita ko TV dake dakin take kallo tunda ita dai bata da Gata bare ace tayi hira da Mai jinyar ta..kallo take yi bata San sanda bacci ya dauke ta ba...

Share

Comment

©Hafciey

[1/25, 5:35 AM] Hafciey Musa😘: □*LAYLERH*□

(The prettiest emerald)

Kasancewar tunda ta shigo kano karfe hudu take tashi yau d'in ma hakan ce ta kasance..tana bude idon ta taga cleaners Na asibitin sun gama share dakin har an Fara mopping nan tabi kan gadajen da kallo duk patients din suna bacci don haka sai bata tashi ba Amma taci gaba da kallon cleaner din har ta gama sannan ta feshe room freshner a dakin ta fice gami da Jan kofar ta waje daga wajen taji ta tana fadin,

"Daga yanzu ba Mai shiga har sai ya bushe haka zalika ba Mai bin corridor'n nan sai Na gama shara da mopping".

Tsaki Wata taja a dakin su tana fad'in,

" kaji mini arniya da karfin hali to wallahi ko zata mutu sai munyi sallah ".

Na gefen ta ne ta karbi maganar tana fad'in,

" kin San cleaners nan da rashin mutunci kuwa wallahi kullum da asuba sai sunyi fada da mutani".

Ita dai mamakin su take saboda in har da gaske suna son sallah kamata yayi su fita kafun ta Fara mopping saboda ba yadda za'a ce tayi mopping waje bai bushe ba su kuma su taka zai zama asara ne.agogon dakin ta kalla ganin hudu da rabi ne sai ta kwanta ko ba komai da sauran lokaci kuma kafun biyar dai zai bushe..

Karfe biyar nayi kowa ya Fara Daukan buta a kasan gado da sallaya yana fita ita ma a hankali ta sauke kafar ta kasa sannan ta janyo slippers nata a kasan bed din ta nufi corridor din inda zai sada ta da wajen Fanfo nan take kallon sauran dakunan rabi an fice sai wadanda ba musulmai bane aka Bari...layi ake yi wajen shiga bandaki saboda karancin su haka ta jira yazo kan ta sannan ta shiga tayi abunda zata yi ta fito ta durkusa a bakin fanfo tayi alwala tunda bata da buta..ganin yanzu dai kowa Na amfani da sallayar shi Gashi bangaren Mata ba'a Gina masallaci ba sai Na maza a gefen ta taga wani taburmar da raba ya kamashi ta karkabe sannan ta tada sallah a Kai..ko da ta idar azkhar tayi sannan ta zauna tana shakar iskar asuba sai da taga kafin gari ya Fara haske sannan ta dawo daki nan ta tarar da driver zaune..

"Ina kwana".

Tace da shi

" lafiya ya jiki?"

"Jiki da sauki alhamdulillah".

" Masha Allah, Allah Kara sauki".

"Amin Amin".

Daga nan duk shiru suka yi sai ya katse shirun da fad'in,

" Zan zauna a waje kan doctors su shigo round don ance shida Na safe suke zuwa sai muji me zasu ce".

"To".

Ficewa yayi yayinda ita kuma ta gyara kwanciyar ta ba jimawa ko tayi bacci tunda an Dade ba'a hadu da katifa ba shiyasa baccin baya Isar ta, ba ita ta farka ba sai bakwai da rabi ganin time sai tayi tunanin kila doctor yazo ita kam ma tana bacci don haka matar dake jinyar Na gefen ta ta duba tana fad'in,

" Aunty Na doctor yazo ina bacci ko?"

"A'a bai zo ba".

" but ance shida Na safe yake zuwa Ai".

"Eh haka ne sai dai yau sun shiga yiwa Wata Mata CS ne shiyasa har yanzu bai zo ba kuma kin San ko sun fito sai sun huta abun Ki da asibiti sai Kayi hak'uri".

" Ayya Allah basu sa'an aiki".

Ba matar kadai ba duk masu sauraron zancen su Amin suka ce sai Wata tace,

"Naga Wanda kuke tare dazun ya shigo kina bacci".

" Allah sarki".

Tace daga nan bata sake cewa komai ba su ma kowa harkar gaban shi ya Kama sai takwas driver ya shigo Mata da breakfast ya ajiye a gefen gado kusa da kafan ta yana fad'in,

"Kin tashi kenan dazun Na shigo kina bacci".

" Ayya sannu da sungulla".

"Ba komai ga wannan kici don doctors din sun shiga theater room ni nayi tunanin war haka kam ma an sallame mu Amma har yanzu shiru".

Shiru tayi bata ce komai ba sai tashiwa zaune da tayi a hankali ta nufi waje domin wanko bakin ta shi ko cire abinci a cikin Leda yayi tana zuwa ya mika Mata spoon Na roba nan ta Karba ta Fara ci sai ruwan tea da ya sayo Mata wajen Mai shayi nan ta Karba ta Fara sha don Allah ya sani tunda ta shigo garin bata sha tea ba..tana gama breakfast ya dauke tarkashen hade da kofin ya fice...

Karfe goma dai dai doctors suka Fara round Amma kuma dakin su ne karshe don haka kusan karfe sha daya suka zo..

" kowa ya fita a bar Mara lafiya kadai doctors zasu shigo round ".

Shine abunda wani security ya fadi nan take aka Fara ficewa a dakin ganin sun gama fita sai ya rufe kofar ta waje bai kuma budewa ba sanda doctors din suka zo..

Doctors biyu ne sai nurses biyu sai kuma yan practical suna biye da su a baya rike da tarkashen su..daga bed one suka Fara inda wasu in doctor ya duba patient sai suyi rubuce-rubuce cikin folder'n Ka da suka ajiye kan bed din in akwai allura kuma a maka in ko magani ne yan practical su baka..

A haka har aka zo bed seven ita ko bed eight take cire kanta daga Gare su tayi duk da kasancewar ta Mai son kallo har suka gama suka iso wajen ta..kujerar da driver yake zama doctor yaja ya zauna sannan ya dauki folder'n ta ya duba gami da kallon ta yace,

" sannu ya jiki?"

"Da sauki"ta fada kanta a kasa fuskar kuma a hade

"Me ke miki ciwo?"

Ya tambaya yana riko hannun ta domin gwada BP'n ta

"Ba komai".

Gwadawa yayi ganin komai dai dai sai yace,

" to sake fuskar mana kiyi dariya yau dai in sha Allah a gida zaki kwana ".

Bata ce da shi komai ba kuma bata sake fuskar ba sai dayan doctor'n ne ya kalle ta yana tabe baki yace,

" ikon Allah, mace Na dariya ma ya aka kare da ita bare wacce bata yi".

Nurse din ce tace,

"A'a Sir tana dariya fa".

" to ni dai ban gani ba".

Dan practical ne yace,

"In iri nane mijin ta Ai da Na shigo gida kallo daya zata mini Na tsorata".

Maganar sa dariya ya bata don haka sai ta juya gefe ta murmusa nan nurse din tace,

" kalli Sir tana smiling ".

" yeah yanzu kam Na kalla ".

Ya fada yana wucewa zuwa next bed doctor dake zaunen yace,

" in wacce kuke tare tazo Kice taje ta biya kudin gado sai ta same ni a office Na Na rubuta muku sallama".

"To"

Tace nan duk suka wuce zuwa next bed din tare da Daukan folder'n ta"..

11:40 suka bar dakin ita ko maganin ta ta sha sannan ta daure a Leda ta zauna jiran shigowan driver Ai suna fita bai wuci da minti biyar ba ya shigo nan ta fada mishi abunda suka ce ya fice...wajen biyan kudin ma ya dau lokaci don layi da yabi sannan ya koma doctor ya rubuta musu sallama dakin ya koma yace,

"Muje ko".

Mikewa tayi shi ko bed Bayan bed yaje yana musu Allah Kara sauki su dai an sallame su ita ma yadda yayi haka tayi nan suka nufi mota shi ya bude Mata ta shiga ya rufe sannan gate Man ya bude musu gate ya jefa hancin motar a titi suka bar anguwar ..

Tafiya Mai nisa suka yi kan su iso gidan Ai kuwa tabbas ta gane gidan nan yayi horn gate man ya leka yana ganin su ne ya wangale musu kofa nan ya sa hancin motar a gidan dai dai gate man ya suke Glass Na motar tare da fitar da hannun shi ya mika mishi suka gaisa yana tambayar mai jiki Laylerh ma gaishe shi tayi ya Mata ya jiki kan suka nufi cikin gidan..

Tabbas yau ko ba'a fada Mata ba tasan biki ake yi a gidan saboda ko ta ina gilmawar mutani kake gani ga yara sai wasa suke a harabar gidan kowa an mishi ado da Na kasan akwati shi a dole sun zo gidan aure..

Sauke ta yayi ya dube ta yana fad'in,

" to Ki karasa ciki Allah Kara lafiya".

"Na gode sosai Allah saka da alkhairi".

" Ameen".

Yace sannan ya juya ya nufi gate wajen Abokin hirar sa..

Kallon yaran dake wasa tayi ga gidan ta ko ina anci abinci an zubar direct apartment Na Hajiyar ta nufa bakin ta dauke da sallama,Ai ba karamin tsinkewa zuciyar ta yayi ba ganin duk girman falon a cike yake makil da mutani kuma da gani matan manya ne, har kasa ta tsunkunya ta rika gaishe su wasu Na amsawa kamar an musu dole wasu ko yi suka yi kamar basu San da ita ba..

"Tabbas masu kudin ma suna suka Tara tunda Hajiyar gidan dai tana da mutunci Amma dubi kawayen ta".

Zama tayi a wajen ganin tsam ba Hajiya ba alamar ta tana so taje wajen kitchen wurin su madam Amma har jiri take ji in ta daga ido taga yawan mutanin Gashi ta San wajen kitchen din zai fi mutani saboda yan gidan biki basu wasa da ci..tana ji sai gulman wasu suke yi Kala bata ce ba kuma ko dagowa bata yi ta kalle su ba sai ga Khadija

" Laylerh dama kun dawo ne?"taho muje dakin mu Ki huta kan Hajiya ta fito don umarnin ta ne".

"To"

Tace gami da mikewa tabi Bayan ta nan suka bar apartment din dukka suka nufi nasu..bedroom ne daya sai toilet sai kuma kananan katifa irin Na gadon asibiti guda uku sai Kayan su a Ghana most go in ta fahimta kenan mutum uku ke kwana a dakin..sosai dakin ya burge ta har taji ina ma su dauke ta Yar aiki a gidan da ta tabbata sai tayi kyau

"Ki zauna a nan Bari Na kawo miki abinci in kin ci sai kiyi wanka".

Bata jira amsar ta ba ta fice ita ko so take ta tambayi ina madam Amma bakin ta yayi nauyi abinci Khadija ta kawo Mata fried rice nan ta zauna a kasan tiles tare da tankwashe kafafun ta ta dibi abincin a spoon tana tare Wanda zai iya zuba kuma da daya hannun ta,ta Kai bakin ta ido ta lumshe jin dandanon abincin ta kuma deban Na biyu nan kam gagara hakura tayi tace,

" Aunty Khadish gaskiya abincin nan yayi dadi ".

Murmushi tayi tana fadin

" da gaske?"

Da Kai ta amsa a zuciyar ta ko cewa tayi

"Su madam Anga gidan manya Harda zagewa ayi abinci Mai dadi irin haka".

Sosai taci Khadija ko Na zaune a gefen ta sai kallon ta take yi tana Mai jin tausayin ta,Ashe itama a rayuwa akwai wacce zata fi..sanda ta koshi ta bar abincin nan Khadija ta riko hannun ta suka nufi toilet Tasa Mata ruwan wanka, toilet d'in dai normal ne shiyasa ma bata yi kauyanci ba nan tayi wanka tare da maida rigar jikin ta ta fito.

" Laaa Kinga Na Ciro miki kaya cikin nawa karbi Kije toilet Ki sa kuma Ki jira ni Zan sayo miki brush yanzu a shagon kofar gidan nan".

"To"

Tace gami da karban Kayan ta juya toilet don ita kanta ta San bakin ta Na wari tunda ba brush take yi ba..sa Kayan tayi duk da ba wani Mai kudi bane kuma ba sabo bane Amma sanda tace,

"Wow nayi kyau sosai".

Sannan tayi alwala ta fito tayi sallah tana idarwa Khadija Na shiga brush ta sayo Mata nan ta Karba ta nufi toilet tayi brush tana ta jin dadi yau dai Yar Gata ta zama ita ma tayi Kama da yaran masu kudi..

" yanzu Ki kwanta Ki huta zuwa sanda Hajiya zata neme Ki Zan zo Na sanar da ke yanzu Bari naje ko za'a aike ni".

"To"

Nan ta fice ita ko murmushi tayi sannan ta koma toilet ta kalli kanta a mirror'n ciki Ashe ita ma tana da ranar yin kyau sanda ta gama haukan ta kan ta fito ta kwanta tana fad'in,

"Bari Na sha bacci kan Na koma gidan madam nasan ba samun ishesshen bacci zanyi ba bare Harda katifa yau dai su Laylerh an zama yan Gata".

Wani farin ciki take ji Wanda ta manta rabon da tayi irin shi fuskar ta dauke da murmushi tayi bacci..

Karfe hudu ta tashi sallah tayi sannan ta zauna jiran Khadija Amma ba ita ta zo ba sai karfe biyar nan tace tazo Inji Hajiya.. A balcony'n gidan suka same ta nan Laylerh ta zube kasa tana fadin,

" an wuni lafiya Hajiya? "

"Lafiya ya jikin?"

"Da sauki Na gode sosai Allah biya miki dukkanin bukatun Ki Na alkhairi".

Amin Amin Hajiya da Khadija suka amsa

" tunda kin samu lafiya sai Ki koma wajen aikin Ki sannan daga gobe ba sai kinzo ba saboda ogar Ki ma Tun jiya Na sallame ta".

Ras zuciyar ta ya tsinke me kuma ya faru aka sallami madam duk da irin dokin aikin da take yi Allah sa dai ba akan ta bane in ba haka ba kashe ta zata yi

"Hawayen me kuma kike yi".

Ita bata San hawayen tausayin kanta da kanta ya zubo bama nan Tasa Bayan hannun ta ta share Amma Inaa sai ga Wasu Na Koran wasu

" Kinga Nifa Na miki abunda Na miki don Allah ne kuma ba Zan boye miki ba,ba Zan iya taimakon Ki ta hanyar Daukan Ki ba don duniya ba tabbas bare ke da a hotel kike aiki".

Ita dai Laylerh kasa cewa komai tayi sai kukan da take yi nan Hajiyar tace

"Amshi nan dubu goma ne shine taimakon da Zan iya miki Allah yaga Zuciya Na"..

Mika hannun tayi ta Karba tana godiya nan Hajiyar ta barsu a wajen Khadija ce tace ta tashi su tafi,daki suka koma nan Khadija Tasa Mata Kayan da ta cire Kala daya a Leda tare da maganin ta da brush sannan ta raka ta wajen dakin

" Kinga Ki daina kuka Kije gida Kinji"

"Dan Allah Ki fada mini akan me aka kori madam?"

"Ba Zan miki karya ba wallahi ban sani ba don bana wajen".

Jin ta rantse yasa ta tafiya Khadija ko ciki ta koma ita ko tana tafiya tana goge hawaye ita kanta tana mamakin saurin kuka irin nata ta girma Amma kuka a bainin jama'a baya bata kunya, ta Isar tsakar gidan kenan gate Man ya wangale kofa nan motoci guda biyu masu tsada suka sa Kai cikin gidan suna gama shiga ya rufe ita ko tsayawa tayi tana kare musu kallo gaba daya tinted ne..

Abokanayen Ango ne da shi kan shi Ango sun zo ganawa da amarya da kawayen ta ko wannen su Na glowing Musamman angon ita kam sokuwa ta koma sai kallon su take yi har suka gama fitowa..angon ne ya Fara sauke ido akan ta nan ya kankance idon shi yana Mata kallon tsab daga sama har kasa sannan ya dafa Abokin sa Wanda ke kusa da shi yace,

" Dude kaga ga Wata Kala can".

"Haba guy gobe fa daurin auren Ka ba zaka daina halin nan ba Ka San fa in in laws naka suka gane Shikenan za'a fasa auren don ba Wanda yasan kana wannan harkar".

" Baba share su Dan Allah wallahi wannan danya ce shakaf".

Lashe baki Abokin yayi kamar sabon maye sannan yace,

"Ai kuwa gwara mu kwashi rabon mu".

" yanzu Ka dawo kan layi gara Na rage Zafi anan kafun gobe ".

Yana gama rufe bakin shi sai yayi kalar mutanin kirki ya Mata alama da hannun tazo ita ko nufar su tayi

" yan Mata lafiya kike kuka ko dai wani abun ne ya same Ki?"

Kai ta girgiza, cikin muryar rarrashi da yaudara yace,

"Look ni ne angon yarinyar gidan wadan nan kuma abokanaye nane so zaki iya fada mana matsalar Ki in kina da bukatar taimako Na miki alkawarin taimaka miki".

Jin haka sai tace shima Na San yana da kirki irin Na mutanin gidan

" dama so nake a raka ni wajen madam Na a taya ni bata hak'uri ".

A ina madam taki take?"

"Tana gida?"

"Shikenan wannan ne matsalar Ki?"

"Ehh".

"Yanzu abunda za'a yi kizo Ki jira ni cikin motar nan zamu shiga ciki mu zanta da amarya da kawayen ta in Mun fito sai Na Kai Ki".

"A'a nikam gida Zan tafi". Kallon juna suka yi shida abokanayen shi sai daya daga cikin su yace

" Ai har gida zamu raka Ki ko baki yarda da mu bane? "Kai ta girgiza

" to Ki dauke mu kamar yayyun Ki wadanda ba zasu cutar da ke ba Kinji".

Shiru tayi kamar Mai nazari sai angon yace

"Ba don ina gudun magana ba ma da tare zamu shiga da Mun gama zantawa sai mu Kai Ki Amma kin San halin Ku Mata da kishi shiyasa ba zamu shiga tare ba".

to tace Allah ya sani bata kawo komai a ranta ba kuma ganin mutanin arziki ta musu shiyasa ta shiga AC ya kunna Mata sannan ya maida kofar ya rufe yana Mai kalle kalle domin tabbatar da ba Wanda ya gan shi,kasancewar yamma ce driver da Mai gadi sun fidda kujera sun zauna ta wajen gidan suna shan iska shiyasa ma basu Gan su ba...ciki suka nufa ita ko tana mota tana shan AC.

Tun tana jiran fitowar su da kauna har ta gaji basu suka fito ba sai gab da magrib daga cikin motar take bin su da kallo daya Bayan daya da yake ta San ba ganin ta zasu yi ba, tabbas angon yana da kyau sosai ga kudi haka ma abokan shi..

Kamar yadda suka zo haka zasu koma don haka mutum hudu ne suka nufi motar da take biyu a gaba biyu a baya sai ya zamana su uku ne a baya Amma cikin su ba Wanda ya maida hankali a kanta sai angon da yake zaune gefen driver ne yace

" Kinga gwara muje dayawa don taji dadin hakura".

Kai kawai ta daga don ji tayi gaba daya tana takure,waje suka nufa suna hawa titi sai Na kusa da ita yace,

"Ouchh kunga d'an Allah muje Na karbi aikan mom Na a nan kusa kan mu wuce gidan su Tun dazun take jira Na".

Juyowa driver'n yayi yace,

" kanwata kin yarda muje".

Da Kai ta amsa nan ya karawa motar gudu basu tsaya ko ina ba sai wani katafaren hotel nan duk suka fece ita kam sai ma gyara zaman ta da tayi don a zaton ta jiran su zata yi a mota suje su fito irin Na dazun duk da wurin yayi kyan da bata gane hotel bane saboda ta San ba zasu kawo ta wajen ba Amma dai kallo daya ta mishi ta San ba gida bane..

"Kanwata fito muje mana".

" a'a yanzu ma Zan jira Ku a mota ".

Kallon juna suka yi sannan angon yace,

" yanzu ke a tunanin Ki zamu cutar da ke ne?yadda ba zamu cutar da kannen mu ba haka ke ma ba zamu cutar da ke ba kuma Ai da muna da niyar cutar da ke ba zamu fada miki mu angwaye bane".

Jin haka sai taga bata musu adalci ba nan ta fito da Kayan ta dayan su kuma tuni ya shiga domin booking daki

"Muje ko".

" Zan biku a baya".

"Ladies first".

Ya fada yana Mai nuna Mata hanya dole ta shiga gaba suka rufa Mata baya shi ko Wanda yayi booking daki text ya turawa angon Na dakin da yayi booking wajen suka nufa knocking daya ya bude

" bismillah".

Shiga tayi su ma suka shiga nan suka maida kofar suka rufe gami da cire key din muryar ta Na rawa tace,

"Ina sakon da zaku Karba".

" relax baby kada Ki wani tada hankalin Ki karatu kadan zamu koya miki kuma Harda kudi zamu biya Ki".

Gane inda suka dosa sai ta Fara kuka tana fad'in,

"A'a Dan Allah Ku bude mini kofa Na tafi kun fa yi alkawarin ba zaku cutar da ni ba".

" Ki nitsu a hankali zamu miki ba zaki ji Zafi ba kuma har gida zamu je mu bawa madam naki Ki hak'uri ".

Ganin fa bata musu rai da gaske zata yi yasa daya buga Mata tsawa yana fad'in,

" Ki nitsu ko Na take ruwan cikin Ki sai hanjin Ki sun fito waje".

Ai ko hadiye kukan tayi jikin ta duk Na rawa nan daya ya nufi toilet sai Gashi ya fito daga shi sai boxers da vest kallo daya ta mishi ta cire idon ta da wuri kan gadon ya fada daya ko sigari ya kunna ya Fara zuga ankon kam ba kunya a gaban ta ya cire Kayan ya bar boxers da vest shima..

Tashin hankali yau ta shiga Wanda tunda take a rayuwar ta bata taba shiga irin shi ba zuciyar ta bugawa yake yi sosai har kaman zai Faso kirjin ta ita wallahi gwara su kashe ta da ace su Mata fyade har su hudu..

"Zo nan".

Angon ya fada yana Mata alama da hannu Amma ko girgiza bata yi ba cikin tsawa yace

" ba kiran Ki nake ba".

Har hanjin cikin ta sanda suka kada nan ta daga kafa a hankali tana nufar shi su ko fashewa da dariyar shakiyanci suka ita ko hawaye sai zuba suke yi ba kakkautawa saura bai wuce taku biyu ta karasa gaban shi ya janyo ta jikin shi

"Innalillah wa'inna ilahee raji'un".

Take ta maimaitawa a zuciyar ta jin ta zaune a cinyar wani kato gaba daya jikin ta rawa yake

" Dude Ka bita a hankali fa kaga yarinya ce ba lallai ta iya daukar ka dukka ba".

Sunsuna ta ya Fara yi tana gocewa tabbas kanta wari yake da yake ba wanke shi ake yi ba da wuri ya cire fuskar ya yana Kawar Wa gefe yace,

"Ke kina wanka kuwa?"

Ita kam jikin ta sai rawa yake kamar mazari juyo da fuskar ta yayi yana fad'in,

"Wallahi ko ma mene ne yau ba barin Ki zanyi ba".

Kokarin manna bakin shi da nata yake yi suka ji Ana knocking Na kofar

" oh my gosh"

Dariyar sa sauran suka yi daya ya mike zai nufi kofar da sauri angon yace,

"Are you out of ur sense kasan wake knocking da zaka je budewa".

What do you mean?kenan mu Bari ayi ta knocking".

" yeah in Mai shi ya gaji zai tafi".

Jin an sake knocking ne sai dayan yace,

"Dude Ka Bari a bude maybe is important".

" to yarinyar nan fa?"

Wanda tunda suka shigo bai yi magana ba sai danne danne a waya yake yi yace,

"Ku sata a wardrobe".

" what a brilliant idea".

Jan hannun ta yayi har gaban wardrobe din nan ya cusa ta gami da maida kofar ya rufe ita ko addu'a take yi Allah yasa kan ya dawo ta mutu...

Jin har yanzu ba'a daina knocking bane yasa angon da kan shi nufar kofar yana gajeren tsaki key yasa sannan ya bude..

He was shocked saboda ganin Wanda bai yi tsammani ba

"Ya Naseer".

Ta gefen shi ya wuce yana fad'in,

" bismillah manager".

Shiga manager'n yayi nan ya biyo su sai gani suka yi kowa ya Kama harkan gaban shi cikin abokanayen, daya Na waya da budurwa daya ko Na chatting while daya game yake yi duk suka nuna kamar basu San da shogowan mutani ba..

Ya Naseer handsome guy ne sosai ga saje shimfide a fuskar sa kallon sa manager yayi yace,

"Kace sun sace kanwar Ka zasu yi raping Ka so Tara mana jama'a a receptionist to ina take".

" believe me Sir akwai mace a dakin nan".

Kallon sa angon yayi sannan yace,

"Enough is enough Ya Naseer just because kana yayan matar da Zan aura doesn't mean zaka ringa acquiescing Na".

" malam stay out of this ba da Kai nake magana ba".ya fada yana nuna shi da yatsa

"Well tunda haka kace you are free to search the entire room".

Ya fada yana batsarwa kamar Mai gaskiya

" Ai ko baka fada ba dama zanyi searching room din".

Nan aka sa securities suka duba ko ina Amma basu Gan ta ba har Bayan labulaye

"For goodness sake what's all this,ina aiki Na Ka taso ni cewa kanwar Ka Na dakin nan but she is no where to be found".

" bar shi manager akwai wani Dan misunderstanding ne between us".

Tsaki manager yaja gami da nufar kofa shi ko Ya Naseer in ranshi yayi dubu to ya baci don ya Dade da sanin angon Dan iska ne kuma ya sanar da iyayen su Amma aka Ki yarda karshe har yaso kawo tsabani tsakanin sa da kanwar shi daga lokacin yayi shiru Amma kuma yayi niyar tona asirin sa ko ba Dade ko ba jima..

Kofa ya nufa idanun sa sun yi ja bai San ma ina yake jefa kafar sa ba sai kawai yaji kamar yayi Ball da Abu yana dubawa yaga ledan kaya ne kamar zai share sai kuma

ya sunkuya ya dauko budewa yayi sai yaga kaya ne da magunguna ciki kuma Harda receipt sannan da sunan mace a rubuce..

Wani murmushi yayi yana juyawa sannan ya dubi angon yana fadin,

"Wannan ma zaka ce mini naka ne ko saboda sunan Ka Laylerh?"

Cak manager da securities suka tsaya tare da Juyowa suna kallon shi,angon ko ji yayi kamar yasa hannu akai yayi ihu haka yaji..

"Ina bakin naka yake zaka fada mini inda take ne ko sai Na nuna maka karfi Na".

" hmmm Naseer kenan me kake tunani? Zaka kure ni ne? Aure dai sai Na auri kanwar Ka yarinya kuma Kai sheda ne a gaban idanun Ka aka duba bata nan".

"Sai Ka Aure ta fa kace,yau Zan nuna maka level da yaya zai iya zuwa don ya ceci rayuwar kanwar sa daga maza irin Ka da kuma yarinyar da kuke da niyar cutarwa har Ku hudu".

" bismillah ".

Duk abunda suke yi tana jin su Amma taki cewa komai don zuwa yanzu numfashin ta Neman daukewa yake yi..

Bude murya Ya Naseer yayi sannan ya kalli receipt din da kyau gudun kada ya Kira sunan ba dai dai ba yace,

" Laylerh kada kiji tsoron kowa a cikin su ni din nan Na miki alkawarin ceton Ki don Allah Ki ceci rayuwar kanwata Ki bani alama Na inda kike".

Sarai taji shi Amma bata ce komai ba su ko duk kasa kunne suka yi jin shiru sai angon yayi wani mugun smile da har San da taji,kamar Naseer din zai yi kuka yace

"Don Allah dai Laylerh Na San kina dakin nan kada Ki yi sanadin bata rayuka biyu,kada Ki bata rayuwar kanwata da kuma taki rayuwar wadannan mutanin ba Allah a zuciyar su cutar da ke zasu yi,so kike su bata miki rayuwa har su hudu".

Tabbas da su Mata fyade gwara ta mutu a ciki Amma kuma tunda ga Mai ceton ta yazo Wanda bata sani ba to gwara ta fito saboda in tana buri a duniya bai wuce ta San Asalin ta ba wannan dalilin yasa ta daga hannu da kyar tayi knocking Na wardrobe din Ai yana jin sound din ya nufi wajen da wuri su ko duk mikewa suka yi cikin Tashin hankali..

Budewa yayi sai gani suka yi gaba daya ta gama hada zufa numfashi ma da kyar take fusga ya bude baki zai yi magana sai Gata zata fadi sumemmiya da wuri ya taro ta ta fada a jikin shi sumemmiya..

" Laylerh! Laylerh! "

Ya Kira yana Marin kumatun ta a hankali Amma inaaa...

Comments

Share

©Hafciey Musa

[1/25, 5:35 AM] Hafciey Musa😘: *□LAYLERH□*

(The prettiest emerald)

korafin Ku ya karbu ga page five din ina zaman jiran ruwan comments😎

Page 5

Security ne ya mika mishi Ruwa dake kan bed side drower nan ya wasa Mata sai Gashi ta kawo dogon numfashi tare da bude idanun ta a hankali duk sannu suka rika jero Mata nan ta Fara kokarin tashi ganin haka ne sai ya taimaka Mata ta mike yana cewa sannu

"Me hakan yake nufi?" Cikin hotel namu zaku sato yarinya kuzo domin biyan bukatar Ku Wato so kuke ku lalata mana sunan waje ko?"

Dukkan su hudun shiru suka yi ba Wanda yace komai sai Naseer din ne ya rike hannun ta yana Jan ta har suka iso gaban su sannan yace,

"Ce maka aka yi dama Zan cire ido akan Ka ne,hanyoyin Allah dayawa yake shiyasa Na Gan Ka time da kake sata a mota daga nan kuma ban ce komai da Kai ba sai ma godiya ga Allah da nayi saboda nasan yau dole asirin Ka zai tonu sannan kuma dole Na ceci yarinyar nan wallahi kunji kunya dube Ku fa ace kun rike zina aikin yi tir da masu hali irin naku sannan Allah ya shirye Ku".

Yana gama fadin haka ya juya ga manager har yanzu kuma hannun shi Na rike da ita yace,

" pls do me a favor Zan baka number'n parents Na da nashi parents din Ka Kira su zo nan su gani da idanun su if not komai zance ba yarda zasu yi ba".

"Well ba damuwa".

Number'n Mom nashi ya bayar sai dai yayi ringing har ya katse ba'a daga ba nan ya bada Na Dad nashi Wanda ringing biyu kawai yayi aka daga

" hello".

"Assalamu Alaikum"

Dad nashi ya fada daga daya bangaren

"Sorry Sir wa'alaikasalam kana magana ne da manager'n hotel in ba damuwa pls muna da bukatar Ka a wajen".Kai tsaye yace

" Sorry wrong number bane"

"Nope son naka Naseer ne ya bamu number'n".

Jin an Kira sunan son nasa bakin sa har rawa yake yi wajen fadin

" I am on my way coming ".

Daga nan manager ya katse kiran shi ko dama da Hajiyar yake zaune ganin duk ya rikice sai ta mike tana fad'in,

" lafiya kuwa".

"Naseer ne".

Bai iya karasa zancen ba saboda bai San ma exactly abunda ke going on ba ita ma jin Naseer ne sai tace,

" I will come with you".

Saboda duk sun San shi ba Mai Neman magana bane sannan baya shiga tsabgar da ba nashi ba..cikin hanzari suka fice Bayan ya sake Kira ya tambayi sunan hotel din nan aka sanar mishi sai suka Kama hanyar hotel din.

A can hotel din kuma still Naseer din ne ya bada number'n Dad Na angon saboda iyayen su abokanai ne shiyasa aka zama kamar family su ma yadda aka yi da iyayen Naseer haka aka yi da Dad nashi da wuri yace Gashi nan zuwa jin ance son nashi ne..

Ruwa ya dauka ya mika Mata tana makale da shi sai hawaye take yi saboda gani take kamar har yanzu bata tsira ba,durkusawa yayi a kan gwiwowin sa sannan ya dafa dukka kafadun ta da hannayen shi biyu yace,

"Relax ba abunda zasu miki Kinji you are save now".

Ita dai Kala bata ce mishi ba Gashi dare sai Kara yi yake yi da alama an kusa sallar i'sha ma..

Ba tare da bata lokaci sosai ba sai ga iyayen kusan a tare suka shigo main entrance Na hotel din sai suka yi musabaha suna tambayar junan su lafiya sai duk suka ce kiran su aka yi nan suka Kira manager ya fada musu room nawa zasu zo nan ne suka fahimci tafiyar nasu daya ne sai suka nufi room din tare da knocking suka shiga..

Kallo daya Hajiya tayiwa Ango ta cire Kai saboda har yanzu bai sa kaya ba kuma surkin ta ne, Ai iyayen su maza kuma duk bin dakin da kallo suka yi har suna hada baki wajen tambayar lafiya.

Nan manager ya musu bayani sai a lokacin kuma Hajiya ta Lura da Laylerh dake makale da hannun Naseer.

" this is rubbish d'a Na ba zai taba aikata haka ba"Cewar Baban Ango

"Yes Dad sharri kawai Naseer ke mini helping nata kawai Zan yi".

" hmmm help?wani irin help kenan?Ka kawo yarinya hotel room da friends naka guda uku sannan ga Ka nan daga Kai sai boxers kace help,in taimakon ta zaka yi Ai zaka iya affording rooms biyu Mai ya Hana Ka Kama Mata daya".

"Naseer you are crossing the line".Cewar Dad Na angon

" what line uncle? Ba sai an maka bayani ba pls Ka yarda da abunda idanun Ka ke gani".

"Alhaji Na gode da cin mutuncin da kuka mini sosai,Ai in kuna son fasa auren ba ta nan zaku bullo ba kawai cewa zaku yi an fasa Amma tunda har kuka mini haka Na janye batun Aure"

"Dad....".angon ya fada cikin rikicewa

" shout up kuma maza kasa Kayan Ka mu tafi".

"Kada muyi haka da Kai Alhaji Haruna".Cewar Baban Naseer

" maganar Aure da yaro Na dai nace Na fasa kuma ba Mai tilasta ni nayi abunda ban yi niya ba".

Zai sake magana sai Hajiya ta rike hannun shi tana Mai girgiza mishi Kai cikin dabara don tabbas ta yarda da abunda Naseer yace da kuma Wanda ta gani saboda Naseer ba zai taba mishi karya ba

"Tunda haka kace nima Na sauke batun auren Allah sa hakan shine mafi alkhairi".

A take angon ya Fara hada gumi don Allah ya sani yana son Yar su ko don kyanta Gashi ya kwallafa rai a kanta Amma yanzu Naseer nan duk ya bata mishi komai

" muje ko".Dad nashi ya fada

"Excuse me uncle Ai ba batun tafiya kamata yayi a mishi hukunci dai dai da abunda suka so aikatawa Wanda Na tabbatar ba wannan bane Na farko, in da ban riga bin su ba da yanzu sun gama da rayuwar ta sannan Na biyu da ace Mun Dad'a bata time muna cecekuce da yarinyar da suka rufe a wardrobe ta mutu".

Manager ne yayi dialing number'n police Alhaji Haruna ji yake kamar ya shake Naseer saboda shi har yanzu bai yarda Dan shi ya aikata ba Bayan irin 20 mins aka zo aka tafi da shi da friends nashi da basu cewa komai..

A hankali ta zare hannun ta daga nashi gami da sunkuyawa ta dauki ledan Kayan ta sannan ta nufi kofa ba tare da kowa ya farga da ita ba nan ta fice a dakin ta nufi waje..

" Allah Mai iko ace d'an Ka ya aikata ba daidai ba Amma kace tsam karya ake mishi,shi kuma Naseer yayi duk abunda zai yi ne don ya kubutar da kanwar sa daga auren Wanda ba mutumin arziki ba gaskiya dangi yayi tsam ni ba Wanda ya Lura da ni a cikin su bare su tausaya mini kowa ta kan shi yake yi".

Wani Zuciya ne yace,

"Su tausaya miki a dadin me?ke ina naki iyayen meyasa suka yarda ke".

Jin har an idar da sallah a masallacai ne ya sata Kara saurin tafiyar ta duk da ba sanin hanya tayi ba kasancewar ta bakuwa a garin yanzu ita ta ina zata Fara Neman hanyar gida Gashi da ta tuna gida sai zuciyar ta ya tsinke tana fargaban abunda zata je ta tarar.. horn taji a Bayan ta Amma tsam taki juyawa Mai horn din ma bai fasa ba sai ma shan gaban ta da yayi ya sauke glass din motar sai ganin Naseer tayi

" Allah ya sani guy nan yana da kyau".

Ta fada a zuciyar ta shi ko cewa yayi

"Shigo Na Kai Ki gida".

Zuwa yanzu kam ta daukarwa kanta alkawarin ba zata sake shiga motar Na miji ba saboda taga illar yarda da maza don haka tace,

" a'a kaje Na gode Zan koma da kaina".

Hararar ta yayi sannan yace,

"Zaki shigo ne ko sai Na fito".

Jin haka sai ta Fara tafiya da sauri, shi ko bude motar yayi ya fita gami da nufar ta,riko hannun ta yayi ya nufi motar da ita sai Neman tirjewa take yi nan ya bude motar ya jefa ta a kujerar gaba sannan ya zagawa ya shiga yana fad'in,

" ance miki nima maye ne me ma za'a samu a jikin Ki".

Tsam taki nitsuwa haka ya tada motar sannan ya dube ta yace,

"Wani anguwa kike?"

Banza tayi da shi tsaki yaja yana fad'in,

"Dama sanda Hajiya tace kada Na kuskura Na taimake Ki don masu aiki a layi sai a hankali".

Juyowa tayi da wuri ta kalle shi sannan tace,

" to Ka ajiye ni tunda ta Hana".

"Kin taimaka mini wajen ceto 'Yar uwa ta nima dole Na taimaka miki Kinga yanzu fada min sunan anguwar saboda ban yi sallah ba".

" Nifa Na manta sunan anguwan saboda ni bakuwa ce Amma in muka koma gidan Ku Zan iya gane hanya".

"Ohk"

Yace sannan ya juya motar suka nufi anguwan su sai gudu yake shararawa suna isa gate Na gidan ta Fara nuna mishi hanya a haka har Allah yasa suka iso kofar gidan tace,

"Yauwa nan ne".

Parking ya gyara zata bude yace,

" baki ji ba".

Juyowa tayi tana kallon sa wallahi ita dai kyau yake Mata

"Ki nitsu Ki Kama mutuncin Ki duniya ya lalace an daina taimako tsakani da Allah don haka duk Wanda yace zai taimake Ki kada Ki yarda Kinji".

Kai ta daga mishi alamar " to"sannan ya dubi gidan yace,

"Nan ne gidan naku?"

"Eh".

" to je Ki sai da safe".

"Na gode"

Tace sannan ta bude motar dai dai lokacin kuma madam din ta Rako wani bakon ta sai ganin Laylerh tayi ta fito daga mota kallon ta tayi daga sama har kasa sannan tace,

"Iyeeh Ashe Kai ya Fara wayewa an Fara bin maza ban sani ba".cikin daga murya ta fada

Rintse idanun sa yayi da karfi jin kazafin da take yiwa yarinya nan ta leko cikin motar tana Washe baki tace,

" sannu fa".

Banza ya Mata ita ko motar ta karewa kallo sai dafa motar take yi tana murmushi sannan ta dubi Laylerh tana fad'in,

"Muje ciki Ki bani rabo Na don uban Ki tunda nice uwar Ki".

Ledan Kayan ta ta dauka duk tsoro ya gama bayyana a fuskar ta murya Na rawa tace,

" sai da safe ya Naseer".

Shi bai ma jita ba saboda yayi nisa a tunani in har kamar Laylerh za'a yiwa kazafin zina sannan a nuna Mata hakan dai dai ne duk sanda ta samu kudi ta kawo to tabbas Tun bata yi har Wata Rana zata Fara kenan rayuwar ta Na cikin hadari..

Tada motar yayi jikin sa duk yayi sanyi yana mamakin ina nata iyayen da suka bar ta haka,da haka ya nufi gida...

Suna shiga ta hau jibgar ta tana fad'in

"Shegiya dama jira nake Ki dawo saboda tabbas Na San baki da inda yafi nan har a kan Ki za'a Kore ni a gidan can".

" wallahi madam bani nace su Kore Ki ba".Ta fada cikin kuka

"Ince bakin cikin an Kai Ki asibiti yasa ni fita hayyaci Na ringa kwaba musu girki Na lafta gishiri har ya gagara ciwuwa nan aka ce kada Na sake zuwa".

" kiyi hak'uri ".

Haka ta ringa jibgar ta sanda tayi me Isar ta sannan ta zauna a bakin baranda laylerh ko na durkushe a gaban ta kamar mai neman gafara nan tace,

" kawo kudin da ya baki".

"Allah bai ban kudi ba".

Fisgo ta tayi ta fara Cajin jikin ta nan taji kudi a bakin skirt nata hannu Tasa ta Ciro tana kallon yan dubu daya daya Wanda ta tabbata ba zasu wuce dubu goma ba

" iyehh Ashe fa kina da farin jini,Hala shine ya Fara sanin Ki 'ya mace shiyasa ya baki kudi Mai yawa haka".

Kuka sosai take yi tana girgiza kanta saboda Allah ya sani ta manta da kudin da Hajiyar ta bata ma

"To Ki saurare ni da kyau,ba Zan Hana Ki ba tunda naga zaki ke kawo mini kudi Amma kuma Ki tabbatar da sai dare zaki rika fita sai Ki kwana a can saboda dole zaki rinka mini aiki a hotel sannan duk abunda Kika samo tare zamu raba Kinji".

Kai kawai ta iya daga Mata

" kawo ledan kuma muga me a ciki".

Kan ta mika Mata ma tuni ta fisge ledan nan ta zazzage abun ciki duk a kasa sai ta dube ta tace,

"Kayan jikin Ki shi ya saya miki ne?"

Kai ta girgiza

"To Ki jini da kyau daga yanzu Zan Fara gyara Ki ciki da waje in kinje kin samo sai mu shiga adashi don naga Yaron masu kudi ne dole yaji Ki yadda ya dace kada mu rasa shi".

Tana gama fadin haka ta mike ta nufi daki ita ko sanda tayi kukan ta Mai Isar ta sannan tayi alwala tayi sallolin da ake Binta sannan tayi shimfidi ta kwanta jikin ta duk yayi tsamin dukan da ta sha...

Yau kwana biyu da haduwar ta da Naseer d'in kuma har yau ba abunda ya canza cikin wahalar da take sha a wajen madam yanzu ma suka dawo daga hotel din tana shigar musu da kaya ciki tana gamawa ta zauna a bakin baranda tayi tagumi abun duniya duk ya ishe ta madam din ce ta fito daga daki tare da mika Mata cup tace,

" kar bi Ki sha wannan don wallahi Na Lura Yaron nan yaji Ki ba taste shiyasa bai sake dawowa ba kuma yau kam dole a waje zaki kwana don ba Zan kashe kudi Na a banza ba".

Yau kwana biyu kenan tana bata abunda ita dai bata gama gane mene ne bane Amma daga zancen madam din ta San Na gyara ne kuma dole ta sha duk da tana jin sauyi a jikin ta in ta sha..Karba tayi ta sha nan tace

"Maza je kiyi wanka Ki zo".

Wanka tayi nan ta dauki gonjon ta ta saka da hijab sai ta fisge hijab din ta Miko Mata wani Vail tace,

" karbi wannan Ki sa ke dai ba zaki taba wayewa ba".

Karba tayi ko yadda ake yafa shi bata iya ba nan ta taimaka Mata wajen yafawa tace,

"Kuma Ki rinka tafiyar da zai ja hankalin mutani ba wai tafiyar da kika saba kamar Na shanu ba".nan ta fesa Mata wani turare sannan tace

" Allah bada kasuwa".

Sannu bata ce ba ta nufi waje a zuciyar ta tana cewa zata roki oga Emeka ta kwana a gidan shi da haka ta fice..

Fitar ta yayi dai dai da parking Na motar Naseer a kofar gidan tana kallon shi bata San sanda ta yi murmushi ba da wuri ta karisa jikin motar, kwanciya kadan yayi inda ya mika hannun sa ya bude Mata gidan gaba ta shiga tare da maida kofar ta rufe fuskar ta dauke da murmushi saboda ta San Allah ne ya turo sa Gare ta domin ya Cece ta tace,

"Ina wuni ya Naseer".

Shi dai gaba daya ta daure mishi Kai ganin murmushin da ta mishi sannan ya tabbata tularen da yake ji a jikin ta Na Jan hankalin maza ne shiyasa ma tsoro ta bashi cikin hade rai yace

" waya baki tularen da Kika sa?"

"Laaa ya maka dadi ne?"ta fada tana kallon sa don haka kawai yake Mata kyau

Tsawa ya Mata yace,

"Nace a ina Kika samu?ko dai dama kina bin maza ne?"Da wuri ta Fara girgiza kan ta nan take hawaye ya Fara bin fuskar ta ganin haka ne sai ya sassauta murya yace

"Fada mini ko dai tularen dadi yake miki ne?"

"A'a madam ne ta fesa mini".

Cikin rashin yarda da zancen ta yace,

" Shikenan haka kawai sai ta fesa miki".

"A'a"

Nan ta fada masa duk yadda suka yi da madam din nan take idon sa yaji jaa saboda shi mutum ne Mai tsaninin tausayi sai yace,

"Yanzu akan kudi ta tura Ki kwana a waje?"

Kai ta gyada mishi alamar ehh zazzafan numfashi ya fusga sannan yace,

"Shikenan Na miki alkawarin Zan ke baki kudin Ki ringa Kai Mata Amma ko da wasa kada Ki kuskura Wata ran Ki aikata abunda take so Ai ke ba yarinya bace kin San zina haramun ne kuma kin San hukuncin Mai aikatawa sannan turaren Kice Inji ni a daina sa miki bana so".

" a'a ba zaka iya ba kudi sosai fa take so".shi maganar tata ma dariya ta bashi shiyasa ya murmusa

"Kada Ki damu zanke bata cikin salary Na but baki da iyaye ne?".

Shiru tayi sai da ya maimaita tambayar tare da fad'in,

" bani tarihin ki mana".

Yaken da yafi kuka ciwo tayi sannan tace,

"Kowa a duniya Na tabbata yana da labari ko tarihin da zai bada in an tambaye shi,tabbas ni din ma ina da Wanda Zan bayar sai dai ya banbanta da Na kowa saboda duk Mai bada labari daga yarinta zai Fara Amma ni ba haka bane a iya sani Na ban taba yin hadari ba bare ace nayi loosing memory Na da ba Zan iya tuna baya Na ba,iya abunda Zan iya tunawa a rayuwa Na Wata 1 da ya wuce ne".

Nan ta bashi labarin Tun haduwar ta da Larai har zuwan ta Kano da irin wahalar da take sha nan yayi shiru har ta gama sannan ya dube ta cike da tausayi tana hawaye tissue ya mika Mata yace,

" karbi Ki share hawayen Ki to ita wacce ta kawo Ki bata fada miki inda ta tsince Ki bane?"

Kuka take yi ta gagara bashi amsa nan motar yayi shiru sai AC da ke tashi,tabbas da yana da hali zai iya ceton ta daga tarkon madam sai dai taimakon ta Na nufin auren ta kuma ya San koda wasa ba Wanda zai yarje mishi da auran wacce bata da asali shi kan shi ba zai fara ba don baya zuciyar ta bare ya San gaskiya ta fada ne ko kirkire ne...

Ruwa ya dauka a seat Na baya ya mika Mata nan ta shanye tana ajiyar Zuciya shi ko time ya duba a hannun shi sanin yana da abun yi sai yace,

"Yanzu kiyi shiru sannan in kin shiga gida Kice Harda abun da ake baki kina sha nace bana so".

Duk da ya fahimci bata San takamemmen abunda ake bata ba ita dai tace Ana bata wani Abu ne

" to"

Tace nan ya bude wajen ajiye kudi a mota ya Irga dubu Ashirin yace,

"Gashi Ki Kai Mata sannan Kice nace a daina cewa Kije wani wajen Zan ke biyan ta yadda take so".

Karban kudin tayi tana mishi godiya ta fice har zata shiga gida yace,

" kar Ki manta fa nace bana son turare da maganin".

To tace tana murmushi sannan ta shige gida lokacin kuma madam din ta fito daga toilet tana ajiye buta ta ganta nan tace,

"Kada Kice mini har kin dawo yau ko zanci uban Ki".

Nufo ta tayi ganin da gaske zata duke ta sai ta Ciro kudin ta mika Mata Washe baki tayi Tasa yatsan ta a baki ta dangwali nyawu sannan ta Fara Irga sabbin kudin da sai kamshi suke tana gamawa tace,

" Masha Allah Kai gaskiya kinyi goshi maganin yayi kyau shiyasa naga Harda kuka kika yi Wa yace miki ni din wasa ce".

Shiru tayi ganin madam din ta cusa kudi a cikin bra din ta sai tace,

"Uhmm uhmm dama...dama...".

" Ki bude baki Ki mini magana hai".

"Dama yace kada Na sake shan wani Abu kuma kada Na sa turaren".

Kwashewa tayi da dariya har tana shewa daga bisani kuma Tasa hannu a hanci tayi guda bata damu da dare bane tace,

" shege dama waya ce mishi borno gabas take Kice kin bashi a jikin shi,to koma yaya ne ba za'a sake ba tunda yana bada kudi yadda ake so Ince Na ranar ne ko?"

Kai ta gyada alamar Ehhh daga nan madam din ta shige daki tana murmushi ita daya ganin cikin kwana uku Laylerh ta sama Mata dubu talatin Ai dole ma ta koya Mata karuwanci tunda maza Na bata kudi..

Shirin kwanciya tayi tana Mai jin Naseer har cikin ranta saboda yanzu shine uwa kuma shine uba a Gare ta..

Comment

Share Fisabillah

©Hafciey Musa[1/25, 5:36 AM] Hafciey Musa😘: *LAYLERH*

(The prettiest emerald)

Page 6

Kasancewar yau weekend kuma abun mamaki sai taga basu fita aiki on time ba..karfe bakwai dai dai yara biyu suka shigo gidan da gudu direct dakin madam din suka nufa ba tare da sun kalle ta ba..

Cigaba da sharan ta tayi tana gamawa madam din ta fito rike da hannayen yaran Wanda ba sai an fada maka irin tsananin son da take musu ba kallon Laylerh tayi sannan tace,

"Mu tafi".

In dai ta fahimta da kyau wadan nan din yaran madam d'in ne saboda sai kiran ta mommy suke yi..direct hotel nasu suka nufa ita dai backyard ta wuce don ta San yanzu dai a can kowa yake Ana girki

" Aunty Mairo ina kwanan Ku".

Wannan girmama su da take yi ne yake Kara sa son ta a zuciyar su,aiki ta Kama nan madam din ta fito tace,

"Laylerh Ki dafa musu indomie sun ce yunwa suke ji".

" to"

Tace gami da mikewa ta nufi store sai bata ga indomie ba instead of ta tambaya sai kawai tace Bari ta dafa musu spaghetti Ai duk daya ne.. Bata wani jima ba wajen dafa musu nan ta kwashe musu sannan ta juye musu a plate ta Kai musu yaro Babban kuma Na mijin ne ya kalli abincin yace,

"Cabb wallahi ba zamu ci spaghetti ba Ai cewa aka yi Ki dafa mana indomie".

Shiru tayi tana kallon shi don ita rashin kunyar sa bai wani bata mamaki ba tunda madam ce uwar sa,tsawa ya daka maka yana fad'in,

" Kije Ki dafa mana indomie dama Mommy tace baki da hankali ".

Unbelievable Yaron da take iya kallon har tsakiyar kan shi ne yake fada Mata wannan maganar in ita ce kuma ta fadawa uwar shi irin haka to tabbas kashe ta zata yi..

Jin hayaniyar yaran yasa madam din fitowa nan ta kalli yaran da tsantsar soyayya tace,

" me ne nake jin hayaniyar Ku".

Babban ne ya kwabe fuska yace,

"Mommy kince ta dafa mana indomie shine ta dafa spaghetti".

" iyehh yaushe Kika Fara iko kan Abu Na ban sani ba?ke har kin isa nace Ki dafa musu indomie Ki Ki naga ba uwar Ki ke mini shefene ba kuma dole yara Na suci abunda suke so tunda hotel din Na uwar su ce ".

Ta karishe maganar tana Kai Mata dundu Yaron ko suna hada ido ya Mata gwalo nan takaici ya sake kamata

" kuma maza Ki koma Ki daura musu indomie yanzu ".

Tana gama fadar haka ta rike hannun yaran ta suka shiga office nata Laylerh ko backyard ta wuce nan ta tambayi Laure inda indomie yake sai ta sanar da ita..

Komawa kitchen din tayi ta daura musu yana nuna ta juye a plate Tasa fork sai ta Kai musu office d'in Na ta tarar da su sai zallan shogwaba suke zubawa madam din ita dai tabe baki tayi ta fice abun ta don taga akan yaran nan ba abunda ba za'a Mata ba..

Bayan sun ci sai aka Kira ta ta musu wanka bata musa ba ta Debi ruwa a bucket ta nufi can da su,yarinya macen ta Fara yiwa wankan kan tazo kan Na mijin

" wallahi ni dai ba zaki mini wanka ba yarinya da ke".

Kallon sa tayi tana nazarin tabbas in har da yadikko yake zaune to tana ganin ikon Allah kam,janyo hannun shi tayi saboda ya gama cika ta da takaici nan ya tirje yana fad'in,

"Ke Ana dole ne nace bana so".

Tsaki taja gami da rike hannun sa zata Fara masa kenan ya Fara wasa Mata ruwan wankan ya jika ta takaici har wuya nan ta daga hannu zata mare shi sai akan idon madam

" kada Ki kuskura wallahi ko mafarki Kika yi to kiyi sadaka saboda duk Randa hannun Ki ya sauka a jikin da Na to kona hannun Zan yi".

Mamaki ne ya kamata Wato ita bata ga abunda Yaron yayi ba sai laifin ta za'a gani kenan d'a yafi d'a, wankin Babban bargo ta Mata sannan ta rike hannun Yaron tace,

"Zo Yaron kirki Bari mommy ta maka wanka".

Da kanta ta mishi wankan...

**

Cikin bacci ta Fara jin kamar motsin maganar mutum shiru tayi ba tare da ta bude idon ta ba,tabbas motsi take ji kuma irin Mai ban tsoron nan ne a hankali kuma cikin tsoro ta bude idanun ta sai ganin wajen duk duhu da wuri ta mayar ta rufe tsoro Na 'Dad'a rufe ta ganin ita kadai ce kwance a waje..jin alamar tabbas maganar ba Mai karewa bane kuma kamar ta saman ta take ji da yake wajen window ne sai tayi tunanin kila yaran madam din ne

" to wadan nan yaran kiriniya ne ya Hana su bacci har war haka sannan suke kokarin Hana ni ".

Mikewa tayi da kwarin gwiwar ta don ta musu magana sai Tasa idon ta a jikin window da yake kuma akwai haske a dakin.

Firgici da tsoron abunda ta gani ya sata Komawa da baya har ta fadi kasa nan zufa ya Fara karyowa a jikin ta gaba daya jikin ya hau rawa ji take yi kan ta Na juyawa kamar dai numfashin ta Na Neman yankewa..

Da kyar ta iya daga kafar ta ta sauka a barandar ta nufin barin gidan cikin dare Amma sai kawai taga mage sun Fara fitowa daga da wani bangare na gidan Gashi ko wanne da kalar su kuma duk ita suka nufo..durkusawa tayu a tsakar gidan addu'a ma kusan gagarar ta yayi don gaba daya ta fice a hayyacin ta da kyar ta iya nemo addu'a ta Fara yi duk da rabi ba dai dai take yi ba..wani mage ne ya nufo ta yana irin tafiyar zaki idanun sa dai normal Na mage ne sai dai shi din abun tsoro ne yana zuwa kusa da ita yayi tsale zai Dane jikin ta da sauri ta buge shi sai Gashi ya

fadi a gefe,sake tasowa yayi wannan Karon yayi nasarar cafke hannun ta nan ya cize ta bai kuma cire bakin shi a wajen ba ita ko har yanzu bata fasa yin addu'ar da wani ba daidai take yi ba..cikin kwarin gwiwar da bata San kan ta da shi ba Tasa hannun ta dayan ta shake wuyar sa nan ya Fara kiciniyar kwace kan sa Amma taki a fili tace,

"In ma mutum ne wallahi kan Ku kashe ni sai Na kashe Ka ko mu mutu tare".

Mage dai idanu yake zarewa abunda ya 'Dad'a tsorata ta shine time da ya cire bakin sa a hannun ta zai yi ihu tana jiran taji kukan mage sai taji Na Dan Adam Gashi bakin shi mouth odour mutum take ji sanda taga yana Neman mutuwa sannan ta sake shi tana fad'in,

" in ma mutum ne wallahi gobe sai Ka tashi kana dingishi".

Sauran kuma ganin haka sai suka Fara wasewa..

Ba komai ta gani a dakin madam ba face madam da yaran ta sanye cikin jajayen kaya sun sanya kaskon wuta a gaban su gaba daya idanun su ya koma irin Na mage Gashi jini sai fita yake yi daga bakin su Wanda hakan ya tabbatar Mata cultism ne..tabbas kamar yanda ta Gan su su ma duk sun ganta wannan dalilin yasa su Sawa a ran su dole ta mutu kan ta tona musu asiri..

Ficewa tayi a gidan da gudu saboda ko me zai faru dole ta bar gidan don ta tabbata Wata ran naman ta zasu ci..

Jin ficewar ta a gidan ba kamarin tada hankalin madam yayi ba dole ta sauya kaya gami da rufa Mata baya don tabbas rayuwar Laylerh hatsari ne ga nata rayuwar..

Tana fita niyar ta gidan oga Emeka zata sai wani Zuciya yace kada taje can don haka sai ta Kara gaba ta gammace ta hadu da duk wani abun cutarwa da ta zauna a gidan can..

Neman duniya ba Wanda madam bata Mata ba cikin Daren inko taga mutani sai ta tambaye su tana describing kamannin ta tare da tabbatar musu ita din mayyace saboda ta Kama ta tana shan jini shiyasa ta gudu ta fita gudun kada a kashe ta..kowa yaji wannan zancen sai ya taya ta Neman Laylerh domin a Kau da mugun iri a cikin su Amma babu ita babu labarin ta zuwa lokacin kuma kusan Rabin anguwar duk madam ta sanar musu cewa ita din mayya ce kada Wanda ya bata mafaka a gidan sa..

Duk sun dau alwashin in sun ga Laylerh kashe ta zasu yi saboda dayawan su sun San ta sakamakon ganin ta da madam din wasu ko a restaurant.. Daren ranar tsam madam bata rintsa ba har da Na sanin sayo Laylerh tayi..

Ita ko tuni ta bar anguwar bata San me ke tafiya ba ma bata taba jin ta tsani rayuwar ta irin ta yau ba sai dai duk tsanar da tayiwa rayuwar ta bai Kai kwatan Wanda tayiwa madam ba a haka taci gaba da tafiya tana tunanin yau dai in sha Allah ta bar hannun madam Amma kuma bata San hannun Waye zata fada ba Gashi ko number'n Naseer bata da shi kuma ya kwana biyu bai zo wajen ta ba Tun last da yazo har ya Mata kyautar dubu biyar nan ta bawa Mairo ta ajiye Mata sanin halin madam din in ta gani..

Har aka yi sallar asuba bata samu tayi ba haka taci gaba da tafiya saboda so take tayi nisa da inda madam take da ace tana da hali ma da Kano zata Bari...

Karfe Tara Na safe dabarar zuwa hotel nasu ya fado Mata domin ta karbi kudin ta wajen Mairo in yaso sai ta bar garin da kudin nan ta nufi restaurant din tana addu'ar Allah sa madam ta fita..tana isa da wuri ta shige ciki Amma kuma sai taga kamar kowa Na wajen kallon tsoro yake Mata ba tare da sanin madam duk tace musu ita mayya ce kuma sun yarda don kamar yadda mugu bai da kamanni haka ma maye..backyard ta wuce wajen mairo dama kuwa a restaurant din ta Mata ajiya yau tsam ba Wanda ya amsa gaisuwar ta bata damu ba ta fadi bukatar ta kan Mairo ta Kai ga bata kudin sai ga madam ta fito

"Alhamdulillah ga mayya kam".

Nan ta janyo ta waje ta Tara jama'a tana cewa su zo ga mayya kam Ai ko kowa da irin makamin da yake fitowa da shi cuxx Tun zuwan ta duk shagunan kusa da su ta sanar musu..

Finciko Laylerh din suka yi nan kowa ya Fara Mari wasu ko dundu suke Kai Mata har ya Kai ga sun fasa Mata baki wani ko sanda ya kwala Mata sai ga goshin ya face ihu take yi da iya karfin ta tana ransuwa kan cewa ita ba mayya bace,wani dottijo ne da yake dinki kusa da su yace,

" ko zaku kwana dukan ta ba jin Zafi zata yi ba wannan kukan da take yi ma so take a ji tausayin ta kawai Ku kawo taya a kona ta".

Aiko duk sun yi Na'am da batun sa nan suka Fara kananan maganganu a tsakanin su tsam ba alamar tausayin ta a idan ko dayan su..durkushewa tayi a kasa cikin zuciyar ta take fad'in,

"Shikenan Laylerh yau za'a rufe babin Ki taki ta kare ke dai ba abunda Kika samu cikin duniyar nan face wahala".

Kwantar da ita a kasa suka yi tare da aza taya a kanta dadi kamar ya kashe madam daidai an zuba kero akan Ana Neman ashana wani mota yazo da gudu dole duk suka ja baya,bude motar yayi ya fito kan su ce me ya dauke ta a kafadar sa ya shige motar da ita ya rufe tare da bawa motar wuta at 360 ya bar wajen,rufa masa baya suka yi Amma Inaa gudun su da mota ba daya bane nan hankalin madam ya tashi tana fad'in,

" wallahi ina ji shine ogar ta".

Su dai cewa suka yi tunda ta tsira Shikenan Amma duk Randa suka Gan ta a anguwar su tabbas kashe ta zasu yi..

Duk da ta gama cire rai da rayuwa ta San mutum daya ne zai iya ceton ta kuma ba kowa bane face Naseer shiyasa bata wani damu ba..sunyi tafiya sosai kan yayi parking a wani lungu sannan ya cire ta a jikin sa ya ture gefe sai ta koma daya kujeran shiru duk suka yi ba Mai cewa komai a cikin su shiko kallon ta yayi sannan yaja numfashi yana fad'in,

"Wannan karon kuma me Kika aikata?"

Banza ta mishi cikin zafin rai da bata taba sanin shi da shi ba ya daka Mata tsawa sanda jijiyoyin kan shi suka tashi yace,

"Wallahi Kika kuskura idanu Na suka rufe duka Zan miki".

Tabbas yana da Zuciya kuma bai iya fushi ba don abun baya kyau

" me yasa duk sanda za'a cutar da ni kake taimako Na?me yasa rancan baka Bari an keta mini haddi ba?meyasa baka Bari nabi umarnin madam Na Fara zina ba?me yasa yau baka Bari sun kashe ni ba?ni din wacece a Gare Ka da Ka damu da ni haka,kada Ka manta uwar da ta haife ni ma ta iya Bari Na bare Kai da ba kowa nawa ba,Na roke Ka enough of the help yanzu duniya ta koya mini hankali kuma a shirye nake Na tsaya on my own ba sai Ka taimake ni ba har yaushe Zan cigaba da rayuwa da hope din duk sanda nake cikin matsala zaka zo Ka taimake ni?"

"Har zuwa ranar da Zan tabbatar rayuwar Ki ta inganta,ni din ba kowa bane a Gare Ki face Dan uwan Ki musulmi sannan ina so Ki sani ba sai mutum Na son Ka bane zai tausaya maka nasan a naki yarintar tunani kike kan cewa son Ki nake yi to Ki cire wannan daga ranki Ki dauke ni jigo Na rayuwar Ki".

Kallon sa tayi da jajayen idanun ta saboda tabbas kamar yadda ya fada ita ta dauka son ta yake yi da tafi kowa murna Ashe duk hauka take yi

" Ki fada mini me ya hada Ki da su suke kokarin kashe Ki?"

Last night

Gidan su Naseer

Hajiyar sa ce zaune a main falo sai Khadija dake zaune kusa da Wata dottijuwa shi ko yana kwance a three seater yana operating wayar sa..

"Hajiya hak'uri zaku yi don yanzu tsufa ya Fara kamani dole ina da bukatar Khadija".

" Dada Ai Khadija ta zama Yar gida wallahi ina jin dadin aikin ta don Allah Ki bar mana ita".

"Ba Wai barin Khadija ne bana so ba a'a tabbas nasan tafi samun Gata anan Amma duba da yadda kafa ta ke ciwo ga tsufa dole ina da bukatar Mai kula da ni".

Dada tsohuwar ma'aikaciyar su Naseer ne sannan kuma ita ce Maman Khadija, Khadija ce aurar ta ta Dade tana aiki a gidan kuma sosai take jin dadin aiki a karkashin su har zuwa lokacin da mijin ta ya rasu nan suka bata mazauni sai ta tattara ta dawo gidan da zama lokacin da suka fahimci tana fama da ciwon sugar yau lafiya gobe kishiyar ta sai suka ce ta ajiye aikin kawai lafiyar ta yafi komai ta yarda da shawaran su Dari bisa Dari shiyasa ma ta bar musu Khadija ita ko ta koma gidan ta da zama Amma ta kan zo lokaci lokaci ta duba Khadija ko yau din ma hakan ce ta kasance Amma a wannan Karon so take ta tafi da Khadija gaba daya don tana da bukatar Mai taimaka mata..

Tunda suke magana yana jin su bai ce komai ba sanda aka zo wannan gaba abun Ka da wasu yaran masu kudi in iyaye Na magana tsoma baki kawai suke yi nan ya mike zaune sannan yace,

" Haba Dada kamar yadda Hajiya tace Khadija ta zama Yar gida kuma in batun Mai kula da ke kike so ina da wacce zata kula da ke".

Kallon tuhuma Hajiyar sa ta masa on a serious note tace,

"Naseer ba nace Ka fita harkar yarinyar nan ba ni wallahi tsam ban yarda da ita ba".

" Mom ba ita bace fa".

"Wace ce in ba ita ba wallahi duk abunda taja maka ni ba ruwa na".

" Mom trust me gaskiya Na fada,kin San mom and Dad Na mansur sun bar kasar nan so maid nasu Na nan kuma shima Ai jiya yazo ya sallame Ki kan cewa zai yi tafiya shiyasa ya bani amanar maid din yace don Allah Na nemi inda Zan ajiye ta kan su dawo bai kamata a bar ta da maza kadai a gidan ba".

Mansur Abokin Naseer ne kuma tabbas yazo ya sallame ta sanin Naseer ba zai Mata karya ba sai ta yarda da zancen shi Amma ta daura da fad'in,

"Ni dai Na fada maka waya San daga ina take haka kawai iyayen ta ba zasu bar ta ba".

Shiru yayi sai Dada ce tace,

" Hajiya kin San baya karya Ai Ki yarda da shi kuma ni Na amince ya kawo mini ita tunda Zan zauna a gida Na,Na kwana biyu kan Na koma Taraba".

"Na gode sosai Dada".

Washe gari Allah Allah yake gari ya Waye yaje ya sanar da ita wannan albishir saboda zama gidan madam kalubale ne ga rayuwar ta..karfe takwas ya nufi gidan su sai ya tarar sun fito hotel da yake ba sanin karfe nawa suke fita yayi ba,kasancewar akwai go slow a hanyar da yabi dole sai Tara da wani Abu ya iso nan ya tarar Ana kokarin kona ta..

Numfashi yaja tuno abunda ya faru last night sannan ya dube ta yace,

" ke nake sauraro".

Tiryan tiryan ta bashi labarin abunda ya faru shiru yayi yana nazari

"Shin abunda ta fada gaskiya ne,cikin ita da madam din wace ce mayyar Gashi sanda Hajiyar sa taja mishi kunne batun ta,to yanzu shi bai ma San ina zai Kai ta ba sannan kada ya kaita wajen Dada ta cutar da tsohuwar da ta kare rayuwar ta a musu hidima wani Zuciya ne yace ya sauke ta kawai har ya bude baki zai ce ta fita sai kuma ya fasa nan ya tada motar ba tare da sanin ina daya zai Kai ta ba..kofar wani karamin asibiti suka tsaya nan ya fito ita ma fita tayi tabi Bayan shi duk warin fetir take yi ganin yadda kowa ke kallon ta ne ya daure masa Kai kar dai su ma sun ji abunda aka ce,bai San ganin yadda ta sha duka ga Kayan ta dake war in fetir yasa suke kallon ta..

Koda suka je gaban nurse tambayar shi tayi me ya same ta shiru yayi sai kawai taga ya mike hannun ta yaja suka fice a asibitin gaba daya don tabbas ya San in yace accident tayi za'a ce ina police in ko yace duka aka Mata nan ma za'a nemi jin ba'asi...gefen titi yayi parking yana kallon gaban sa ba tare da ya kalle ta bayace,

" Laylerh ina son taimaka miki Amma ina tsoro saboda ban San ke din wace ce ba kuma ina gudun kada Na Kai Ki wani waje Ki cutar da su saboda Hajiya ta ma ta gargade ni kan cewa kada Na kuma shiga tsabgar ki".

Numfashi taja sannan ta share hawayen ta da Bayan hannun ta tana Jan magina ita ma ba tare da ta kalle shi ba tace,

"Tabbas Kai din mutum ne da yafi kowa daraja a rayuwa ta saboda banda tamkar Ka sannan har zuwa numfashina Na karshe ba Zan manta da Kai ba kuma ba Zan daina maka addu'a ba,kamar yadda Na fada maka tunda Mom naka ta gargade Ka to kabi umarnin ta saboda ita din ba abar wasa bace tunda ni ban San tawa ba ko yanzu Ka bar ni duniya ta koya mini darasi zanyi zaman kaina".

" Ni kuma Naseer Na miki alkawarin in har ina nan da rai Na to Ki cire a ranki cewa Wata Rana zaki yi zaman kan Ki Zan taimake Ki tsakani da Allah in kuma Kika mini butulci Na bar Ki da Allah ".

Tada motar yayi nan suka nufi wani anguwa Dan dai dai a kofar wani karamin gida yayi parking yace,

" fito".

Nan ta bude motar ta fito sannan suka shiga gidan a tare gidan karami ne Amma ko ina tsab tsab da alama matar gidan Nada safta...

Jin muryar Naseer yasa Dada fitowa sai ganin sa da bakuwa tayi nan ta karewa Laylerh kallo lokacin da take shimfida tabarma tana fad'in,

."sannun Ku da zuwa".

Zama yayi nan ita ma ta zauna nesa da shi kadan Bayan ta gaishe da Dada ta amsa sai yayi gyaran murya nan ya fadawa Dada komai akan ta bai Mata karya ba don ba halin sa bane shiru Dada tayi Na wani lokaci kan tace,

"Gaskiya Naseeru ba Zan boye maka ba in har za'a ce yarinya kamar wannan tana yawo a titi ba iyaye to waya San me ya fiddo ta daga gidan su kila can ma korar ta aka yi akan maitan".

Shiru yayi yana daura kalamanta a mizani tabbas tayi gaskiya Amma sai ya daure yace,

" Dan Allah Dada Ki yarda da ni kuma kin San shi zato zunubi ne koda ya kasance gaskiya ".

" Naseeru maita ba abun wasa bane ba Zan iya karban ta ba".

"Ban taba rokon alfarma a wajen Ki ba yau har durkusawa zanyi a gaban Ki domin neman alfarma".

Da wuri ta girgiza Kai tace,

" Shikenan Allah ya gani Zan rike ta da Zuciya daya in ta cutar Dani Allah zai saka mini".

"Na gode sosai".

Ita ma godiya tayi tana jin wani Abu Na Musamman game da Naseer din

" yanzu Dada ya za'a yi da ciwon ta?"

"Wannan ba matsala bace Ka kwantar da hankalin Ka Zan matse Mata da ruwan Zafi sai kuma kudin da zaka kawo Na saya Mata maganin ciwon jiki a chemist".

Cire kudi yayi ya mika Mata nan taja hijab akan kofar dakin sannan ta fice shi ko Juyowa ga Laylerh yayi yana fad'in,

" Dan Allah ba don ni ba Ki rike ta tsakanin Ki da Allah kuma kada Ki kuskura Ki fita gudun kada wanda ya San Ki ya ganki sai kin kwana biyu,batun kaya kuma Zan bawa Khadija kudi ta sayo miki kiyiwa Dada biyayya tamkar ita ta haife Ki don mahaifiya ce ga Khadija ni kuma Zan ringa shigowa lokaci lokaci kan Ku bar garin nan".

Ba karamin faduwa gaban ta yayi ba jin Wai zasu bar garin har sanda ya gani a fuskar ta murmushi yayi sannan yace,

"Kada Ki damu ba abunda zai same Ki Na yarda da Dada".

" Amma zaka ke zuwa waje Na ko?"

"Kin San yanayin aiki Na,Amma in anyi hutu Zan je kuma kan Ku tafi Zan saya miki waya duk lokacin da kike bukatar wani Abu ko magana da ni sai Ki Kira ni".

To kawai tace Amma jikin ta duk yayi sanyi nan Dada ta dawo shiko sallama ya musu da Kara cewa don Allah kar a Bari ta fita sannan ya roki alfarmar kada ta sanar da Hajiyar sa komai ta kuma yarda..

Bayan tafiyar shi wanka Dada ta sa ta tayi sannan ta bata wani extra fellen zani da wani rigar Khadija nan ta sha magani Dada ta matse Mata goshin tana kuka Amma Bayan wani lokaci sai ya lafa sosai kuma taji dadin wajen...

**

Karfe hudu Na asuba ta tashi kamar koda yaushe a hankali ta bude kofar dakin ta fice ta bar Dada kwance a katifan da suka kwana tare waje ta nufa da touch a hannun ta dama sun cika ruwa a duk butocin su kan su shiga sai ta dauki daya ta nufi toilet Bayan ta gama biyan bukatar ta sai ta dauro alwala ta dawo dakin ta shimfida sallaya da Daukan hijab da Dada ta bata tace ta Rika sallah akai sannan ta Fara nafila..karfe hudu ta rabi Bayan ta sallame sai ta maso kusa da katifar ta Fara bugawa a hankali tana fad'in,

" Dada Ki tashi muyi nafila kan ayi Assalatu".

Numfashi Dada taja tana mika gami da bude ido kamar Mai baccin gaskiya Bayan kuma duk abunda Laylerh din ke yi idon ta Na kanta..waje ta nufa tayi alwala tazo suka yi ta nafila..

Bayan sun idar da sallah sai Dada tace su kwanta ko Na hour daya ne in sun tashi sai suyi dumamen tuwon su Na jiya su ci..

Da yake bata Saba baccin Asuba ba gari Na Fara wayewa taje ta musu sharan Dan tsakar gidan tare da wanke-wanke sannan ta hada wuta ta daura dumamen nan ne Dada ta fito tace,

"Sannu fa da aiki Gashi duk kin gama komai ina bacci".

" to me amfani Na Dada in Zan bar Ki kiyi aiki".

Dumamen nayi ta juye musu a plate nan suka daura ruwan tea..tare suka ci dumamen su sannan suka daura da black tea..

Karfe goma Khadija ta shigo gidan tana ganin Laylerh ta fada a jikin ta sai yanzu ta gane Wato ita ya Naseer ke nufi jiya Ai sosai tayi murna sannan ta mika Mata ledan Kayan tace,

"Wannan ya Naseer ne ya bani kudi Na saya miki".

Zuba Kayan tayi a kasa Kala biyar ne dogayen riguna Na material irin Na 1500 nan guda biyu sai Riga da skirt Na kanti guda biyu sai kuma fallen zani da top daya,da panties guda uku da bra daya sai hula biyu..sosai tayi murna ji take yi yau ta zama 'Yar gatan ya Naseer nan Dada tace su shigar da kayan ciki ranar haka suka wuni

murna Khadija ma sai cewa tayi zata kwana dole Dada ta bar su Washe gari ko ta kori Khadija..

A hankali suka Fara sabawa da juna nan kuma Dada ta Fara fahimtar kyawawan halayyan Laylerh ...

Duba da yadda littafin tsam bai samu karbuwa ba ina ga Zan hutar da Kai Na kawai ta hanyar daina typing

Comment

Share

©Hafciey Musa

[1/25, 5:36 AM] Hafciey Musa😘: *□LAYLERH□*

(The prettiest emerald)

Dada ce zaune kan kujera Laylerh ko Na sugune a gaban ta bucket ne cike da ruwa a gaban su sai gefen su ko shampoo ne irin Na naira darin nan..

"Laylerh ke ko mutuwa Kika yi ne da zaki bar kan Ki da Dotti haka?duba fa omo'n naira hamsin Na juye a kan Ki Amma har yanzu da sauran Dotti".

" wallahi Dada ranar Na wanke to da yake a kitse ne kila shiyasa bai wanku ba".

"Mutum da ran shi da lafiyar shi ace ya bar Kai haka kila ma in nasa shampoo din karewa zai yi".

Tana maganar a lokaci daya kuma tana dirje Mata Kai din Wanda har ita Laylerh din Na jin Zafi Allah ma yasa Dada'n bata da farce..shampoo ta zuba a Kai d'in nan ma sanda yayi rabi ganin Kai din ya fita sai ta dauko conditioner ta zuba ta Fara wanke Kai din kenan wayar ta ya Fara ringing..

Hannu Tasa cikin ruwan wanke Kai din ta dauraye hannun ta sannan ta mike tana goge hannun a jikin zanin ta sannan ta nufi daki domin amsa kirar...

" Laylerh a ina Kika ajiye mini waya Na duba ko ina ban gani ba".

'Daga murya tayi tace,

"Dazun da nake shara Na ajiye a kasan filo".

Dubawa tayi sai ko ta ga wayar nan ta amsa sai tace,

" subhanallah yaushe".

Shiru tayi tana sauraron maganar da ake yi daga can daya bangaren kan ta sake cewa

"In sha Allah zanyi kokari".

Bayan wani lokaci sai ta katse kirar..Laylerh kuma tunda taji tace subhanallah ta dakata da wanke Kai da take yi tayi shiru tana sauraron ta har zuwa yanzu da take fitowa..

" Dada me ya faru?"

"Hmm Ki Bari kawai wallahi Kira ne daga gida Wai Dadda Na ba lafiya".

" Allah bata lafiya Bari kai na ya bushe in yaso sai muje mu duba ta kitso kuma sai Mun dawo".

"Waya ce miki a nan ne?a Taraba fa take".

" Taraban akwai nisa ne?".

"Sosai ma".

Daga nan duk shiru suka yi Laylerh din kuma taci gaba da wanke Kai din tana gamawa ta dauki kujera ta ajiye a Rana sannan ta zauna don Kai din ya bushe da wuri Dada ko daki ta koma..

Bayan azahar Dada tace tazo ta Kama Mata Kai din nan suka zauna zaman kitso

" wallahi kan Ki tsam baya kitsuwa yadda ya dace dubi fa gashin sai hardewa yake yi in nasa cumb kuma sai ya tugu".

Shiru tayi Dada ko Na kitson can taji shiru Dadan tana cikin kitso ta tsaya kuma ga kitso a hannun ta d'aga Kai tayi ta dubi Dadan sai taga tayi nisa a tunani dafa kafar ta tayi tace,

"Dada".

Firgita tayi tare da Jan guntun tsaki

" ina hankalin Ki ya tafi ne?"

"Wallahi tunanin gida nake yi batun jikin mama Na kin San shekaru yaja Gashi kudin mota har dubu biyar da wani Abu gwara da ni kadai ce zanje to ga Ki".

" A'a tunda jikin sosai ne Kije ni Zan zauna a nan".

"Duk abunda ba Zan iya yiwa Khadija ba to ina Mai tabbatar miki ke ma ba Zan miki ba,da hankali Na ta ya Zan tafi Na bar Ki ke daya a gidan nan".

" to yanzu me abun yi?"

"Dole zamu nemi kudin motar Ki sannan matsala ta Na San dole suna tsammanin wani Abu daga Gare ni duba da sana'a nake yi a nan".

" to me zai Hana mu tambayi ya Naseer kudi Na tabbatar zai taimaka mana".

"A'a in Kinga Mai kudi yayi taimako to ba a banza bane yana da tashi manufar sannan in Mun tambaye shi kudin motar Ki in Munje can kuma zai biya kudin jinyar ta ne".

" gaskiya ba zai yuwu ba to yanzu me abun yi?"

"Kin taba sana'a ne?"

"Gaskiya in ba Wanda nayi a hotel ba ban taba ba".

" to Shikenan ina ga yanzu Zan Fara miki masa a kofar gida don kan tsufa ya Kama kafa Na ina yiwa Khadija to yanzu kuma Kinga bata nan".

"Eh to akwai kudin shefe ne?"

"Eh ina da dubu goma sha biyar zamu dauki dubi biyar sai muyi Na sati daya kafun in sha Allah Mun samu Na motar Ki sai mu tafi".

" Shikenan Allah bamu sa'a".

"Amin Amin"

Daga nan suka cigaba da kitso suna gamawa tace,

"Ni yanzu Zan shiga kasuwa sai Ki daura mana abincin dare".

" ba komai yadda kike so haka za'a yi".

Shiryawa tayi ta tafi kasuwa sai Bayan asr ta dawo da shefene sanda almajiri ne ya shigar Mata da wuri Laylerh ta shimfida Mata tabarma sanin ciwon kafar ta sannan ta debo Mata ruwa a Kofi ta kawo..Karba tayi ta Kai baki sanda ta sha ya ishe ta sannan ta cire tana fad'in,

"Na gode"

Kunce bakin zanin ta tayi ta Ciro naira Ashirin ta Mikawa almajirin da ke tsaye sannan ya tafi..

Laylerh din kuma shefenen ta Kai kitchen..

Washe gari!!

A ranar ko suka Fara tuya kwano biyu suka yi da yake dama an San Dada nayin masa sai Gashi tas ya kare dadi kamar ya kashe Laylerh nan suka zauna Irga kudi uwar kudi ya fito Amma ba wani riba Gashi ya kare dukka nan suka tashi hankalin su sai Dada ta Mata uzuri tunda ranar ce Na farko..Washe gari ma hakan ce ta kasance wannan Karon kam har yaso kawo tsabani tsakanin ta da Dada don da kyar aka hada uwar kudi ita kanta abun Na damun ta don gani take Dada zata yi tunanin ita ce ke Daukan kudin..

Ranar Na ukun tuyar yamma suka yi gaba daya yanzu Dada bata fiya sake Mata ba hakan ya Dada tabbatar Mata da cewa Dada Na zargin tana Daukan kudin..ta gama fitar da komai Na tuyar sai Dada ta dube ta tace

"Ni Zan Dan shiga gari Na tambayi bashin da nake bi ko Zan samu don naga wannan sana'ar kam ba komai cikin ta fashe fadiwa".

Addu'ar nasara ta Mata cikin sanyi jiki don tsam matar bata cancanci bacin rai daga Gare ta ba Amma ko ma yaya ne in sha Allah yau zata tabbatar ta fidda riba..

Tana cikin tuya masu saya Na saya motar Naseer yayi parking a kofar gidan gami da fitowa..

Yau sanye yake cikin kananan kaya sai yafi Mata yau fiye da kullum nan take ta Fara blushing kallon ta yayi sai ta tsunkuyar da Kai tace,

" sannu da zuwa".

"Yauwa".

" mu shiga daga ciki ko?"

"A'a dauko mini kujera a nan Zan zauna".

" a nan.....".

Wani murmushi Mai narka zuciya da ya Mata ne ya Hana ta karesa maganar ta wuce cikin gida ta dauko masa kujera ta ajiye nesa da wutan sannan ta koma wajen zaman ta da wuri ganin kamar masar cikin kasko ya Fara konewa..dauko kujerar yayi ya matso kusa da ita Amma akwai Dan tazara kadan tsakanin su sai ya zauna..

Gaba daya yau gani take ya sauya kamar ba shi ba to ko dai ya Fara son ta ne shima..Yaron da yazo tsaya ne ya katse Mata tunani nan ta daga Kai ta kalle shi tace,

"Na nawa kake so?"

"Dari".

Naseer din ne ya maida wayar sa aljihun gaban rigar sa sannan yace,

" nawa nawa ne?"

"Uku hamsin shida Dari".

Hannu yasa cikin masar tare da Daukan Leda nan ya irgawa Yaron sannan ya karbi kudi yaron ko ya tafi..kallon sa take yi cike da mamaki fahimtar haka ya sa cikin batsarwa yawa,

" naga fuskar Ki ya canza yau".

Tsintar kanta tayi da cewa,

"Eh nayi kitso ne".

" Masha Allah ".

Yace yana kuma Sawa Wata yarinya yana mika mata ta mika mishi kudi nan ya dubi Laylerh yace,

" yaushe kuma Kika Fara sana'a? "

"Yau kwana uku naga zaman baida amfani ne".

Tace da shi ba tare da ta sanar da shi Asalin dalilin tallah ba

" kin kyauta kuma".

Ya bata amsa Bayan ya fara zubawa wani nan ya Miko dubu daya duba inda take ajiye kudi yayi sai yaga ba canjin nan ya daga Kai ya dubi saurayin yace,

"Ba chanji fa".

" Laa ba komai ya Naseer Ka bashi Na Saba da shi Anjima zai kawo mini in ya samu".

"A'a gaskiya ina tsoron ya gudu mana da kudin mu,mu rasa riba".

Maganar tashi dariya ta bata don haka tayi murmushi tace,

" Allah Na San shi ba zai gudu ba".

"Kaga saurayi je Ka nemo chanji sai kazo Ka karbi abun Ka".

Juyawa saurayin yayi ya tafi shi ko kallon Laylerh yayi yace,

" Wa ya ce miki haka ake sana'a kada Ki yadda Dan Adam ba abun yarda bane".

Sai yanzu ta gane a irin haka take batar da kudi da kuma in mutum yace ta kyauta sai ta Kara mishi..

Wayar sa ce tayi ringing nan ya dube ta yace,

"Hannu Na da Mai sa left hand naki cikin aljihu Na Ki cire mini sai kiyi receiving Ki sa mini a kunne".

Jikin ta har rawa yake yi Tasa hannun ta tayi receiving shi ko matsowa kusa da ita kadan yayi Tasa mishi a kunne yana sauraron me ake cewa can yace,

" Shikenan gani nan zuwa yanzu ".

Sannan ya kalle ta da ido ya Mata alamar ta cire wayar a kunnen shi nan ta cire ta maida mishi aljihu sai yace,

" ban ruwa a mota Na wanke hannu Na".

"Ka Bari Na kawo maka a buta".

" a'a kada kafun Ki dawo ya kone bude seat Na gaba akwai faro Ki bani".

Motar ta nufa tana budewa wani kamshi Mai sanyi ya ratsa zuciyar ta ruwan ta dauko mishi nan ta zuba mishi sannan ya mike yana karban sauran ruwan ya sha ganin zai tafi tace,

"Ya Naseer ba zaka ci masar bane?"

"Kinga ina sauri jira Na ake yi".

Shawagbe fuska tayi tace,

" to Ka tsaya naga akwai takeaway a kitchen Bari Na dauko sai Na sa ma a ciki".

Kan yace wani Abu tayi gida da sauri sai Gata ta dawo da takeaway Karba yayi ita kuma ta cire Na cikin wuta, guda uku ya sa sai yaji a gefe ba tare da sanin ta ba sai ya ajiye Mata Dari biyar guda biyu a cikin kudin nan yace

"Na tafi sai Na sake zuwa".

So take tace mishi nan da kwana hudu zasu bar garin Amma kuma tana ganin Dada ce ya dace ta fada mishi,to in kuma bai sake dawa ba har suka tafi ba..

"Laylerh ".

Ya fada da Dan karfi nan ta dawo hayyacin ta yake tayi tace,

" Allah tsare".

Ameen yace sannan ya tafi nan taci gaba da tuya har magrib ta gama nan ta Fara tattara Kayan sana'ar nata tana kaiwa cikin gida ta dauki kujera ta shigar don shine karshe sai ga Dada tayi sallama

"Wa'alaiksalam sannu da dawa".

Fuskar nan a hade yake da gani da bacin rai ta shigo sai mita take yi

" wallahi wasu mutanin tsam basu son biyan bashi kamar basu tunanin mutuwa Wai ace naje har gidan su matar nan Na Gan ta fa Amma tace kannen ta su ce bana nan takaici kamar Na mutu ga asarar kudin machine da nayi,Ai naji zata daura Aure kwanan nan Allah taje mutuwa Na nan yana yawo mutani tsam ba Allah a zuciyar su"..

Buta ta dauka ta nufi bandaki tana cigaba da mita irin Na Wanda yaje Neman bashin sa bai samu ba tana fitowa tayi alwala lokacin kuma Laylerh har ta Fara sallah..da yake Laylerh din ta shimfida Mata sallaya akan tabarmar da take sallah sai tayi sallah suna idarwa Bayan sunyi addu'a ta dubi Laylerh tace,

"Ya sana'ar duk da nasan zancen gizo bata wuce ta koki ke ma bacin rai kawai zaki Kara mini ni ina ga gwara mu Bari kawai tunda ba riba ake samu ba".

Mikewa tayi ta nufi daki nan ta daga kasan wani kwalla ta Ciro kudin tana zuwa ta zauna kusa da Dada sannan ta mika Mata kudin bata ce komai ba irgawa tayi sai taga ta wuce uwar kudin sannan ga wasu kudin a takaice dai yau sun samu riba har Na dubu daya da Dari bakwai.

" Masha Allah yau dai an samu riba da alama kin Fara gane kan kasuwanci".

Ta fada tana Daukan ledan kunun zaki da ta shigo da shi ta dauki kulli daya ta bula ta Fara sha

"Ai ba ni Na sayar ba Ya Naseer ne ya tayani".

Da kyar Dada ta hadiye kunun zakin jin sunan da Laylerh din ta Kira sannan ta cire ledan a bakin ta tana zaro ido tace,

" wani Naseer din?"

"Dada wani Naseer kuma Na sani Bayan Wanda ya kawo ni nan".

Kafe ta da idanu Dada tayi tana son gane gaskiyar abunda ta fada Lura da yarinyar bata Mata karya sai ta gyara zama cikin hikima irin ta manya ta Fara buga cikin Laylerh din don taji ko soyayya suke yi

" a titi ya tayaki sayarwa Bayan nan kuma me yace miki".

"Ba abunda yace mini an Kira shi a gida ne ya tafi".

" Laylerh nikam me a tsakanin Ku ne?"

"Wallahi ba komai".

" kin fada masa batun tafiyar mu ne?"

"A'a gani nake ke ce ya dace Ki fada mishi".

" Ai Shikenan ".

*****

Jiya kwana suka yi Neman shi Amma shiru babu shi babu labarin shi anyi nema da shigiya amma shiru yan anguwar duk an tayasu Neman shi shiyasa ma suka kwana ba Wanda ya rinsa tsakanin su biyun yanzu ma duk zaune suke a falo hannun malam rike da carbi yana istigfari ita ko takumi tayi ta zubawa agogo idanu yanzu karfe takwas Na safe Tun jiya kuma ya bace..

Karar fadiwan Abu suka ji ta Bayan dakunan da wuri duk suka mike sai dai kan su isa sai ganin gilmawar mutum yana fita daga gidan suka yi da wuri suka rufa mishi baya Amma ko da suka fita basu ga Mai Kama da mutum ba ma bare shi Wanda ya fitan..Komawa ciki suka yi dube dube suka Fara har corridor sai suga ga kofar dakin shi a bude nan suka kalli juna kamar hadin baki kuma suka nufi dakin..

Sassanyan kamshi ne ya bugi hancin su lokacin da suka sa kai cikin dakimln sannan Ba karamin mamaki suka ji ba ganin shi kwance a kan gado yana bacci da wuri suka karasa cikin dakin dafa kan shi malam yayi yace,

" Allah maka albarka".

Baaba ko hawaye ne wannan Na bin wannan ta shafa sumar sa tana duba jikin sa domin tabbatar da ba abunda ya same shi sha'anin uwa, kasancewar shi farin

mutum abu kadan Na taba shi zaka gane shiyasa taga hannun shi jini ya Dan bushe akan wani jijiya da alama an ja jinin shi ne

"Tunda bacci yake zo muje falo sai ya tashi".

Ficewa suka yi zuwa falo suka zauna kowa da abunda yake tunawa shiyasa falon yayi shiru can Baaba tace,

" yanzu kam Ka yarda cewa akwai Mai shiga gidan nan ya cutar da Umar Farouq?d'a daya da Allah ya bawa mutum Ana Neman ganin Bayan shi wallahi ko Waye ne yayi sanadiyar wannan lalurar ta sa ba Zan yafe ba sai anyi magana sai kace Na kyautata zato Bayan ni da Kai duk Mun San ba haka yake ba yi mishi aka yi,Bayan an cutar da shi din ma bai isa ba nema ake aga Bayan sa".

Ta fada cikin kuka

"Naji Na yarda saboda Na gani da ido Na akwai Mai shiga gidan nan Amma ta ina yake shiga?"

"Wannan ne ban sani ba sai dai tabbas wani lokacin har abinci suke bashi Wanda Na tabbata barazana ce ga rayuwar shi akwai Randa Na shiga dakin sai ganin sa nayi a tsakiyar gado yana cin kaza Na tambaya kuma kace ba Kai Ka saya ba sannan ranar Na lallaba da kyar ya shiga wanka ina gyara dakin sa da Na daga gado wallahi Kayan sanyi ba kalar da babu Gashi ba magana yake yi ba bare Na tambaye shi ina ya samu wadan nan abubuwan sun bala'in tada mini hankali".

"Rayuwa kaddara ce kowa da irin ta sa ga yaro har yaro kyau kwarjini izza komai ya hada sai Allah ya jarabce shi da hauka".

Mikewa Baaba tayi ta zuba mishi ido fuska a hade tace,

"Malam Kai ma kana cikin masu kiran shi da mahaukaci?to wallahi d'a Na ba mahaukaci bane daura masa aka yi kuma in sha Allah zai samu lafiya".

" gaskiya dai kin San daya ce kuma ita ce shi din ba Mai hankali bane,ni din ma Ai uba ne kuma duk sanda Na tuna cewa d'a Na mahaukaci ne ina jin Zafi sosai Amma kuma ba yana nufin Zan karya ta hakan bane".

"Ni dai Ka daina danganta shi da hauka Ehem".

" Shikenan Allah bashi lafiya tunda ya dawo ni Bari Na tafi kasuwa kin San zaman gida kam ba zai yuwu ba".

"A dawo lafiya Allah bada sa'a".

" Ameen" yace sannan ya fita a falon Yana gyara hular sa gate Na gidan ya nufa yana budewa yaga motoci baki guda biyu masu tinted glass sun yi parking da wuri ya maida kofar ya rufe yana numfashi da wuri sai jin karar gudun motoci yayi yana budewa yaga motocin ne suke gudu so yake ya samu sani evidence ko da plate number ne ya rike Amma bai samu ba don kurar da suka tayar gida ya koma..

Baaba ko yana fita ta Fara jin karar fashe fashe daga dakin shi alamar ya tashi kenan kuma haukar tashi yau kuma bana nitsuwa bane da gudu ta nufi dakin ta bude da key don sun rufe shi ta waje..

Tsaye tayi ganin yadda cikin mintuna kadan ya fasa abubuwa dayawa gashi ya daura hannu dukka biyu a Kai idanun shi sun yi jaa sai hawayen da ke fita yana bin fuskar shi ganin kamar yana Neman suma ne da gudu ta karasa dakin ta riko sa a bakin gado ta ajiye shi sannan ta nufi fridge Na dakin ta dauko ruwa budewa tayi Tasa mishi a baki sai Gashi sanda ya kusa shanyewa ya cire Kai

"Sannu Baba Na Allah sa ba abunda suka maka".

Oho shi bai San me take fada ba ma kitchen ta nufa nan ta kawo mishi abinci sai gani tayi ya kwanta ya bawa abincin baya kenan ya koshi Wato sun bashi abinci yaci..

Abu daya yake burge su a haukan nashi don yana Dan nitsuwa in abun bai tashi ba Amma in ya tashi suma ba ragar musu yake yi ba sai sun kulle shi a daki

" Na shiga uku har yaushe zasu daina cutar da Kai don Na tabbata duk maganin da zamu baka a banza ne in har zasu ke samun ganin Ka har su baka abinci. To Waye ne su kuma me suke so a wajen mu Bari Na Kira malam gwara ya turo mana doctor'n Ka yazo ya maka check up Ko dai poison suka baka".

Tana rufe bakin ta yana turo kofar ya shiga a rikice.

"Lafiya kuwa?"

"Wallahi ba lafiya ba wasu Na gani a kofar gidan nan da motoci bakake masu tinted glass suna gani Na suka gudu shiyasa nace Bari nazo Na jaddada miki Ki kula da shi sosai".

" innalillah wannan wace irin masifa ce Wato ba za'a bar shi ba har sai Anga Bayan ran shi".

"Ba komai Allah Na nan".

" Yauwa kaga Na kawo masa abinci yaki ci nace ko zaka Kira doctor yazo ya duba shi don bamu San me aka bashi ba".

Hannu yasa a aljihu ya Ciro waya nan ya Kira doctor Jibril dake aiki a Specialist bugu biyu ya dauka don shine likitan shi nan malam ya sanar da shi bukatar su yace Gashi nan zuwa..

Bayan 40mins doctor yazo time din ma har yayi bacci nan yayi duk wani abunda zai yi sannan ya d'ebi jinin sa ya tafi da shi domin yin test..

Wannan Karon malam bai fita ba jira yake sai an kawo result kan ya fita don hankalin sa ba'a kwance yake ba..

Wayar sa ce ta Fara ringing nan ya duba sai ganin doctor Jibril ne picking yayi Bayan sun sake gaisawa sai yace,

"Malam Ku kwantar da hankalin Ku ba komai wallahi dama yanzu Zan kawo result din to sai aka kawo mini patient don haka kuyi hakuri sai zuwa Anjima Zan kawo".

Ajiyar zuciya malam yayi sannan yace,

" alhamdulillah wallahi ba komai Kayi aikin Na gode".

Sallama suka yi nan ya nufi dakin Umar Farouq don ya sanar da Baaba, sosai tayi murna tare ma suka fito falon yana kokarin ce Mata zai fita suka Fara jin hayaniya a kofar gidan har Ana buga gate din da wuri suka fita..

Tabbas saurayin da Umar Farouq ya taba chakawa wuka ne don har yau hannun bai warke ba kallo daya zaka yiwa hannun kasan yana jin jiki..

A ranar da Umar Farouq ya caka mishi wuka da kyar maganar ta mutu Bayan ya fadi nawa za'a bashi to Bayan ya tafi yayi ta jinya hannu yaki warkewa don kan jijiya Umar Farouq ya yanke shi shiyasa ya debo yan Iskan abokanayen shi har uku domin suzo gidan su kashe Umar Farouq ganin yadda suke buga kofar yasa matasan da

suke kafa majalisa a kofar gidan su Umar Farouq din tambaya ko lafiya nan suka ce sai sun ga Bayan Umar Farouq..

Sanin daraja da martabar malam yasa matasan cewa ba zasu shiga gidan ba don malam ba mutumin banza bane kuma Ai Dan shi mahaukaci ne bai San me yake yi ba akan me zasu kashe shi..

Sun tabbatarwa matasan yau ko me zai faru sai Umar Farouq ya bakonci lahira shiyasa matasan ma suka tsaya tare da tabbatar musu to sai dai ayi jina jina ko me zai faru ya faru wannan hayaniyar ne su malam suka ji

.ganin abunda yake faruwa kuma za'a iya Zubda jini yasa Mai anguwa sa baki Amma suka ce su dai a basu Umar Farouq..

To mutumin da kowa ya San ba hankali bane da shi sun tsaya tada jijiyoyin wuya akan shi Gashi an gagara raba gardama sai kawai aka Kira musu police nan malam yace shi zai bi su police station ita kuma ta koma ciki ta Lura da shi..

Gida ta koma gaba daya ta rasa wani tunani zata yi sai safa da marwa take yi..

A can police station kuma Bayan an shigar da case Na Umar Farouq sai D.P.O ya tambayi malam me ke faruwa

"Wallahi ranka ya Dade ina da yaro mahaukaci Wanda kowa ya shaida har da asibitoci cewa yana da tabon hankali to kuma shi duk Randa haukar ya tashi ba abunda ba zai iya aikatawa ba har kisan Kai in ya Kama shiyasa muke Hana shi fita..Wata Rana ya fita bada sanin mu ba kawai sai ya chakawa wannan bawan Allah wuka in da Allah ya takaita a hannu ne to da kyar muka kashe case din Bayan mu biya shi kudi yadda ya fada daga nan bamu sake ganin shi ba..

To Ashe shi kullum yana bibiyar rayuwar Dan mu bamu sani ba ko jiya ba'a gida ya kwana ba yau Bayan sun dawo da shi kuma suka sake dawa akan sunzo su kashe shi..anyi kokarin ganin batun ya mutu Amma sun Ki sai da ya kawo aka shigo da ku lamarin to ni dai so nake a tambaya mini su wani laifi ya musu da suke Neman ganin Bayan shi har suke shiga mini gida ba tare da sani Na ba su dauke shi"..

Kallon kallo dukka su hudun suke yi nan D.P.O yace,

" kun dai ji abunda yace to sai Ku bashi amsa".

Idi Wanda shine aka yanke a hannu ya kalli Abokin shi Na kusa da shi yace,

"Haka nayi da Ku?nace Ku bibiyi rayuwar shi har Ku shigar musu gida"..

" wallahi oga mu bamu taba shiga gidan su ba hasali ma ko kashe ni za'a yi ni ban San ya kamannin Dan shi yake ba sai dai in uche ne".

"Ya haka zaka daura mini sharri nima yadda Ka fada din haka ne ban San shi guy din ba sai dai ko mayen sallah".Wanda aka Kira da uche ya fada

Mayen sallah Abokin su ne Wanda duk iskancin shi da tantiranci to lokacin sallah baya taba wuce shi shiyasa suke kiran shi da mayen sallah..

" to Wai Ku duk kun manta Tun shekaran jiya muna tare muna aiki har safiyar yau da mahaifin Yaron yace an dawo da shi,ta yaya za'a ce dayan mu ne tunda duk a waje daya muke ".

Tabbas yayi gaskiya don Tun shekaran jiya suke gini a wani gida Wanda an biya su kudi Mai tsoka shiyasa ma suka maida hankali kan ginin don ganin sun gama akan lokaci..

Sun sanar da D.P.O nan yasa aka bincika tabbas gaskiya suka fada..

Shi ko malam duniyar tunani ya tafi don shima ya gamsu kuma ya yarda basu bane tunda dama ba ganin su yayi da idon shi ba kuma ance zato zunubi..

A nan dai aka rufe case tare da Kora musu gargadi kan cewa duk abunda ya samu Umar Farouq din sune tunda dama doka bata aiki akan mahaukaci..

***

Da karfi yake horn din Amma shiru tsaki ya kuma jaa yana horn kamar zai dage kofar gidan da gudu gate man da yanzu fitowar shi a bandaki ya nufi gate din ya leka sai ganin Naseer yayi wangale mishi gate yayi yana addu'ar Allah sa kada ya mishi fadan jinkirin da yayi duk da ba halin shi bane sai gani yayi ya shiga gidan da gudu bai tsaya ko ina ba sai wajen parking yana gama parking ya fito da sauri har yana Dan hadawa da gudu gaba daya baya cikin nitsuwar shi ya nufi bangaren Hajiyar shi yana shiga zai Fara hawa upstairs din cikin muryar Mai kauri da kuma gwauraye da bacin rai aka ce,

"Daka ta".

Tsayawa yayi cak ba tare da ya juyo ba saboda ya San ba muryar kowa bane face Hajiyar sa yana kuma addu'ar Allah sa ba abunda yake tunani bane..

" kafi karfin Ka juyo ko kazo ne?"

Cikin sanyi jiki da kuma takaicin yau shine yayi sanadiyar fushi Mom nasa ya juya ya nufe ta kan shi a kasa yana isa ta mika mishi waya tace,

"Karbi nan".

Cikin confusion ya kalle ta to shi kuma me zai yi da wayar Amma bai yi magana ba ita ce cikin Dan tsawa tace,

" nace karbi".

Hannun shi har rawa yake yi ya karbi wayar ba karamin bugawa zuciyar shi yayi ba ganin abunda take so ya kallan

"Me wannan".

" Mom is not what you are....".

Mari ta Kai mishi tana fadin

"Will you shut up Wato ni ban isa Na fada maka magana kaji ba ko Naseer,nace Ka fita harkar yarinyar nan Amma kaki Tun Randa kacewa Dada kana da Wata nayi zargin ita ne Amma sai Kayi outsmarting Na Ashe yau ni zaka yiwa karya akan Wata banza har zaka bita layi kana sayar Mata da masa".

Ba komai bane a wayar face hoton shi,shi da Laylerh lokacin da Hajiyar Tasa ta Kira sa a waya Laylerh ta masa receiving Tasa mishi a kunne..

" Mom am sorry but Allah ni ba son ta nake yi ba kawai Na taimaka Mata ne".

"What Eva!but ina so Ka saurare ni da kyau wallahi wallahi ko Bayan raina ni Kaltume ban yafe maka Ka auri yarinyar da bata da asali ba".

Da sauri ya daga Kai yana kallon ta cikin yanayin da ba zaka fahimci halin da ya shiga ba

" and you know I mean what I say".

Tana gama fadar haka ta wuce zuwa sama shi kuma Komawa yayi da baya baya ya zauna akan kujerar dake cikin falon ya kurawa waje daya ido..

Daren yau ji take yi tsam ba zata iya bacci ba don farin ciki ba komai take tunawa ba kuma sai dazun da Ya Naseer ya tayata sai da masa ji take yanzu bata da wani sauran damuwa a duniya murmushi tayi ta kuma juyawa ta kwanta a hannun ta Na dama tana fad'in,

"Alhamdulillah Allah Na gode maka Allah Ka Kara mini son Ya Naseer".

Laylerh fan's 1,2,3 hak'uri da ni zaku yi Tun shekaran jiya ntwrk ya Hana ni sakat message basu shigo mini in Na tura ma da kyar yake tafiya shiyasa bani ke muku posting ba

Comment

Share

©Hafciey Musa

[1/25, 5:36 AM] Hafciey Musa😘: *□LAYLERH□*

(The prettiest emerald)

TARABA, Jalingo local gov

Anguwar yandan

Anguwa ce Wanda kusan duk mazaunin taraba jalingo ya San ta kasancewar ta tshohuwar anguwa Wanda Rabin tsoffi ne a anguwar,duk inda kake Neman matasa majiya karfi da kuma 'yan iska tantirai to in sha Allah kana zuwa wannan anguwar zaka samu duk kalar da kake so saboda can shine anguwan yan iska har ma da wadanda ba'a anguwan suke ba can su kan je,duk wani Dan iska da ya amsa sunan shi anguwar ce wajen wunin shi a bakin kogi inda zasu yi ta masha'an su in ta Kama har danne 'yayan mutani suna yi shiyasa ba'a fiya aikan yara Mata lambu dake anguwar ba..duk da kasancewar sa dadedden anguwa har yau tsam ba cigaba a anguwar don gini Tun Na zamanin kakani ne shiyasa har yau fama ake a anguwar tsam taki samun cigaba kalilan ne wadanda yaran su suka maida hankali a kan karatu suka zama wani Abu har sun yi Aure suke yiwa iyayen su renovating Na gidajen su wannan dalilin yasa ba gidaje masu kyau dayawa a yankin..

Wani gida madaidaici ne Wanda wajen sa dai ba za'a Kira sa da Mai kyau ba don bai yi zubin gidajen yanzu ba Mata hudu ne da karamar yarinya suka tura kofar gidan suka shiga..

Flat ne babba a gidan Wanda daga waje ba zaka yi tunanin cikin ya Kai haka kyau ba duk da tsam ba'a yi painting gidan ba..main kofar entrance Na falon suka nufa tare da sallama a bakin su Bayan sun tura kofar falon..kamshin soye-soye da ake yi a ciki ne ya bugi hancin su kallon juna suka yi suna murmushi..

Wata Babbar Mata ce da zata Kai 50yrs ta fito daga kitchen dake cikin falon tana Dan dingisa kafa alamar tana fama da ciwon kafa ta tsaya a dining din tare da siyaya ruwa a cup ta Kai baki Bayan ta shanye sai ta sauke ajiyar zuciya gami da sauka a Dan step da zaka shiga falon..Babban falo ne Wanda yaji Kayan Mure rayuwa ba abunda babu a ciki fuskar ta a sake ta karaso ciki tana fad'in,

"Ashe kuna tafe jikoki Na".

Tabbas zata iya haifan su Amma bata Kai tayi jikoki da su ba kasancewar ta Mai son girma da kuma wasa da dariya da mutani yasa take kiran su jikokin ta Gashi ita din uwar adashin su ne don yanzu ma kudin adashi suka kawo..

" Allah Baaba sai Ki ringa cika mutani da kamshi sai kace gidan amarya me ake dafa mana ne".

Dariya tayi tana fad'in,

"Ai har yau ni amarya ce a wajen malam".

Mika Mata kudin suka yi Bayan ta Irga sai ta mike da alama tsufa ya Fara kamata kitchen din ta koma..Babban tray Mai kyau ta dauko nan ta juye Irish da da koyi da ta soya cikin wani hadedden kula Mai tsada sannan ta dauko wani soup boll ta sa pepper soup Na kaza da tayi sai karamin flaks da ta sa ruwan tea a ciki sai tea spoon da fork ta dauka sannan ta nufi dining ta ajiye..Komawa kitchen din tayi nan ta bude wani pot sai ta juye jollof Na spaghetti ta nufo Palon da shi janyo center table tayi ta ajiye musu tana fad'in

" bismillah kuci abinci ".

Kallon abincin suka yi don sun San tabbas ba kamshin wannan suka ji ba sai dai ba Wanda yace Kala..

Ita ko abincin tray'n ta dauka ta nufi corridor inda a can dakunan baccin su ke jere da ido suka bita har ta bacewa ganin su..kofar wani daki tayi knocking har sau biyu taji shiru sallama ta kuma yi nan ma shiru sai kawai tayi deciding ta shiga a hankali ta tura kofar dakin kamar Mai tsoro..

Babban daki ne guda daya sai toilet dake ciki Amma kuma dakin Nada kyau sai dai ba wani tarkashe..makeken gado ne sai wardrobe Mai guda biyu sai TV dake jikin bangon Dan daidai,wajen tv'n anyi decorating da wallpaper kusan Rabin dakin ma

zance anyi decorating da wallpaper sai madaidaicin fridge ga center table a tsakiyar dakin kallo daya zaka yiwa dakin Ka San dakin Na miji ne..

Ido ta sauke kan gado,Mutum ne zaune akan gadon ya bawa kofar shiga baya sanye yake cikin three quarter da Riga armless kallo daya zaka mishi kasan shi din fari ne tas kasancewar armless ne a jikin sa.. Murmushi tayi saboda tabbas ta San me yake yi in yana zaune a irin wannan lokutan..

" Baba Na kana sana'ar taka ce".

Shiru ba amsa ita dai ta San duk sanda ya bawa kofa baya to yana Irga yatsun hannun sa ne yayi ya sake baya taba gajiya da hakan har ya zamto tamkar dabi'ar sa..kan center table din ta ajiye mishi abinci tana karewa dakin kallo don ko ina a wargaze yake duk da ba Wai Dotti ne ba a'a kaya a can cup a can remote a can da dai sauran su..

Sunkuyawa tayi ta Fara tattare dakin har zuwa yanzu kuma bai juyo ba Nade Kayan ta Fara yi tare da Daukan filon da yake yashe a kasa nan taji yayi wani Kara Mai ban tsoro hannun ta har rawa yake yi ta sake filon ta juyo Gare sa daidai lokacin shi ma ya sanya jajayen idanun sa masu kalar bacci cikin nata..

Masha Allah Kyakyawa ne sosai fari sal da shi gashin kan shi a cike yake da alama bai fiya aski ba saje shimfide a fuskar sa sai manyan idanu da yake da Shi Wanda suka rikide suka koma kalar jaa tsam fuskar sa ba annuri ko kadan..

Ganin kallon da ya Mata nan take jikin ta ya hau rawa ta nufi kofa sai ji tayi ya ture tray'n abincin ya zube cikin rawan jiki ta dawo dakin ta debe abincin tana fad'in,

"Kayi hak'uri don Allah".

Ficewa tayi da sauri gami da rufe masa kofar ta waje nan ta mannu da kofar tana sauke dogon ajiyar zuciya..sanda nitsuwar ta ya dawo jikin ta sannan ta nufi falon aiko suna ganin abinci sai yarinya karamar ta fashe da dariya tana fad'in,

" kullum muka zo gidan nan haka kike mana sai Ki bamu abinci daban Wanda yafi dadi kuma sai Ki dauka Ki kaiwa 'Dan Ki Gashi yanzu ya kunyata Ki yaki ci".

Buge bakin ta Maman ta tayi duk da ko kamar ta San abunda yake ran su ta fada..murmushi Baaba tayi tace,

"Tunda haka Kika ce Bari Na kawo miki kici saboda naga cup Na tea a dakin shi ina ga Bayan sun dawo daga motsa jiki malam ya bashi tea kuma nasan ko Na ajiye abincin Anjima ba ci zai yi ba kin San Dan Gata ne".

" Dan walaha dai".

Kallon corridor'n tayi da sauri dugun kada yaji su sai ta kalli yarinyar ta shafa kanta tace

"Kada Ki ringa fadawa Na gaba da ke haka Kinji".

" to".

Nan ta basu abincin suka ci sai santi suke yi suna gamawa suka Mata sallama suka fice..gyara falon ta sake yi nan ta zauna shiru tana tuna rayuwar 'Dan Na ta..

Umar Farouq,born in Taraba state gossol local government,Hausa by tribe also student of Cambridge university graduate of law like exercise and horse race alot cuxx he is a rider football player but doesn't watch a computer configurer hate meeting new people and making new frnds duk yadda kake da shi karya ne kace Ka gane inda ya dosa rashin magana kuma Ai wannan ta Saba don bata taba jin yace komai ba duk da wani lokacin alamu Na nuna kamar in anyi magana yana fahimta..

Rashin son mutanin shi har tsoro yake bata da alama kuma lalurar sa ce ta sa haka...

Sallamar 'yan Mata biyu a k'ofar falon ne ya dawo da ita hayyacin ta tana kallon su lokacin da suke shigowa tace,

"Yan Mata sannun Ku da zuwa".

" Yauwa mama ina wuni".

Suka hada baki wajen fada

"Lafiya kalau ya iyayen naku".

" suna lafiya sun ce a gaishe Ki".

"Allah sarki ina amsawa Gashi jiya mutumiyar taku ta koma skull".

" shine ko sallama babu".

"Eh da yake an neme su a skull din ne shiyasa".

" Allah sarki".

Wajen Yar ta suka zo wacce take Autar ta sai dai sunyi rashin sa'a ta koma skull da yake a nan FGGC take shiyasa Wata ran sai Bayan la'asar take Komawa..shiru yan matan suka yi suna kallon TV ita ko ganin haka sai tace,

"Wallahi kamar kun shiga raina dama ina Neman Mai shigowa ne so nake Na fita kuma ban son barin gidan ba kowa"

"Ayya anguwa zaki ne?"

"A'a wallahi nan cikin kasuwan yelwa nake son zuwa shefene yaran makotan namu ba son aika ne da su ba".

" kiyi zaman Ki kawai kawo kudin muje".

"A'a Ku Bari zanje da Kai Na ba wani jimawa Zan yi ba Ku Dan Lura mini da gidan saboda ni din Mai jama'a ce kada azo aga gidan a rufe".

" to ba komai ".

Ita ko tana sane taki aikan su ita din ma zuwan sun zai fi Mata Amma ganin su 'yan Mata tana tsoron wani Abu yaje ya faru da su ace ita ta aike su Gashi tsakanin su da kasuwan yelwan akwai Dan nisa gwara da Yar ta ne zata iya aika..ciki ta shiga ta shirya nan ta fito tana fad'in,

" Dan Allah kuyi hak'uri ba jimawa zanyi ba".

"Ba komai fa".

Ficewa tayi ta bar su a gidan su ko ganin haka sai suka baje tare da Fara hiran samari abunka da yan matan yanzu duk inda aka zauna basu da zance sai Na samari suna yi suna shewa dariya suke yi muryar su a sama..

Ji suka yi Ana buga kofa daga corridor'n sai basu damu ba nan dayan tace,

" Bae Kinga tunda Mun samu falo Mai background Bari nayi connecting wufa'n nan da waya ta sai nayi maiming wankar labari Na don wallahi dadi yake mini".

"Hmm Kawa ta Ki Bari kawai Ai wakar ta hadu bana gajiya da shi in kinyi nima zanyi na Fanan don Na haddace falo dai Gashi Masha Allah yaji furniture's".

Connecting suka yi nan cikin falon da dakunan dake corridor ya dauki sauti suko sai maming suke hankali kwance..

Zuwa yanzu hayaniyar ya gama shiga kan shi idanun sa sun rikide sun koma jaa kamar Na Wanda ya bugu ji yake yi kamar brain nashi zai tarwase har dishi-dishi yake ganin Abu don bai iya bude idanun dukka sai dai ya lumshe su ya kuma budewa kamar Mai jin bacci, kofa ya nufa yana fadiwa a hanya ya kuma tashi da kyar har ya isa kofar nan ya daga hannun shi da kyar ya Fara bugawa alamar a kawo mishi agaji Amma ji yake kamar Kara sautin ake yi..

Duk buga kofar da yake yi basu ji ba sanda suka yi stopping music din zasu duba maming da suka yi nan suka ji karar fashe fashe a corridor gaba daya tsorata suka yi jikin su ya hau rawa jin abun da gaske ne sai suka deba da gudu zasu fita cikin rashin sani suka sa wani karamin lock da sai Ka Lura zaka gani nan suka Fara Jan k'ofa Amma ina yaki buduwa..

A bangaren sa kuma zuwa yanzu idanun shi sun rufe duk abunda hannun sa ya kai wajen fasawa kawai yake yi gaba daya ya gama fasa komai Na gaban dressing mirror sai wani irin gurnani Mai ban tsoro da yake yi yana huci kamar mayunwacin zaki..

Knocking Na kofar suka ji anyi da gudu suka buya Baaba ko bata fasa knocking ba jin shiru kuma kofar a rufe sai ta nufi window'n kitchen nan ta Kira sunan su da gudu suka nufi wajen

"Me ya faru Na Gan Ku a firgice haka?"

"Wallahi Baaba akwai mutum a ciki".

Cikin tsoro tace kun ga mutum din ne ko dakin shi kuka je".

" waka kawai muka sa nan muka Fara jin buge-buge".daya ta fada tana Mai waige waige

"Innalillah kuyi sauri Ku fito akwai matsala".

Ganin yadda ta rude sai suka Kara tsorata nan suka Fara kuka ita ko waje ta nufa da gudu domin Neman agajin matasa azo a balla kofar kan wani Abu ya samu yaran mutani..

Da yake har matasan anguwan Na mutunta ta nan suka nufo gidan domin balla kofar sai a lokacin kuma yarinya daya ta Lura da lock din nan ta cire suna ganin kofar ya budu da gudu suka fice matasan kuma kokarin shiga falon suke yi sai tace,

" Shikenan Na gode jikoki Na kuje kawai".

Juyawa suka yi duk suka fice a gidan nan ta shiga falon tana son zuwa ta dubo shi Amma tana tsoro.. Shiru gidan yayi baka jin motsin komai sai Ac don har TV ta kashe, jin haka sai ya mike da kyar har kamar zai fadi fararen fatar kafar shi ya bayyana inda gaba daya Gargasa ne kwance a fatan ya nufo falon duk inda ya wuce sai jinin sa ya diga tana ganin haka taje wajen sa da wuri nan ta riko hannu Mai lafiyar ta ajiye shi a two seater idon ta Na hawaye tace,

"Dan Allah Na roke Ka Ka daina jiwa kan Ka ciwo wannan lalurar ban San ya zanyi da ita ba duk maganin da ya kamata ayi anyi Amma ba nasara Mun karasar da komai namu akan Ka Amma ciwo yaki ci yaki cinyewa".

Mikewa tayi da sauri ganin yadda jini ke fita a hannun shi ta nufi dakin sa first aid box ta dauka nan taga farin tiles na dakin shi duk ya diddiga mishi jini hawaye ta share ta fito nan ta Fara dressing mishi hannun da yake before a asibitin gwamnati take aiki lalurar shi yasa ta ajiye aikin..

Tana gamawa ya fisge hannun sa nan ya nufi kitchen da wuri ta sha gaban sa tace,

" dazun gani nayi kamar ba zaka ci abinci ba shiyasa Na kyautar Amma Kayi hak'uri yanzu Zan girka maka wani".

Oho shi bai ma San me take fada ba Amma ganin ta sha gaban shi sai ya juya ya koma daki ita ko ajiyar Zuciya ta sauke nan ta nufi kitchen cikin minti Arba'in ta dafa rice da yake a gas ne ta nufi dakin da shi".

Ajiye masa tayi nan ta sake karewa dakin kallo da yadda ya zamar sannan ta juya ta koma falo janyo abincin gaban sa yayi yana ci rabi Na zuba kuma hakan ya faru ne saboda rawar da hannun sa ke yi yana gamawa a wajen ya kwanta yayi bacci..

Bayan minti sha biyar ta turo kofar dakin ta shiga nan ta Gan shi kwance a wajen da yaci abinci kyakyawar fuskar shi ta kalla gami da shafa sumar kan shi da yake baki wuluk yana kwance a Kai din har wani dauke ido yake yi sannan ta nufi kitchen ta debo ruwa a wani roba tazo ta wanke mishi hannu sai tayi amfani da privilege Na baccin da yake yi ta gyara dakin sannan ta debe kanukan taja mishi kofa ta fice..

Wannan lalurar tashi ita ke cinye musu kudi Gashi duk da ba lafiya ne da shi ba ya kan zabi abinci kuma sun gane hakan ne ta hanyar in an Kai mishi abunda baya so to fa a nan za'a zo a dauka ba abunda yafi tsana kamar tuwon masara Wanda a da kam yana ci,shi da yake ba Dan kowa ba ya saya zabe Gashi duk Randa ba Nepa in basu sa mai a generator ba to fa ranar gidan ba Wanda zai rintsa shiyasa komai nasu da suka Tara a rayuwa yanzu gab yake da karewa..Babban Tashin hankalin su da addu'ar su shine kada a kawo ranar da zai fita waje don ranar da ya taba fita wuka da dabawa wani inda Allah ya takaita a hannu ya daba mishi kuma lokacin suna da abun hannu sai suka toshe bakin iyayen yaron, saboda komai ma zai iya

aikatawa shiyasa suke yawan kulle shi a daki ko kuma iyakacin shi falo Wanda sai ya shafe fiye da Wata ma bai fito falon ba..

**

Yau tunda suka yi azahar ta fitar da wankin Dada ta fara shiyasa Dada ce ta daura musu abinci ba ita ta gama ba kuma sai goshin la'asar nan ta shige bayi tayi wanka..tana fita tayi la'asar sannan ta saka Riga da skirt Na kantin ta sosai ya Mata kyau ita kanta ta San yanzu ta Fara sauyawa..

Tayi nisa sosai a tunanin lafiya kuwa Tun Randa Naseer ya kawo ta har yau bai kuma sake dawa ba shi yasa ma ta firgita lokacin da Dada ta taba ta tana fad'in,

"Ina kuma Kika Kai hankalin Ki ina magana".

" yi hak'uri ".

Ta fada tana sa hula a kan ta

" nace tunda kin gama kizo muci abinci ".

" to ina zuwa".

Ficewa Dada tayi nan ta shimfida musu tabarma ta jikin gini inda inuwa ya sauka a gidan su da kullum a share yake sannan ta Debi abincin ta ajiye musu..

Laylerh Na fitowa ta deba musu ruwa a kofin silver sannan ta zauna suka Fara cin abinci da yake in suna cin abinci Dada bata taba yarda suyi magana..suna cikin ci kamar daga sama Laylerh taji sallama Wanda kuma tasan ba muryar kowa bane face Naseer..

Dada ce ta amsa don ita ta kasa cewa komai sai zuciyar ta dake bugawa da sauri sauri.. Jin ya karaso inda suke ne sai ta gyara zaman ta nan ya cire takalmin sa ya zauna ta Bayan ta..

Tsam ta gagara daga ido ta kalle shi duk da tafi kowa son ganin sa jin yana cewa,

"Dada ina wuni".

" lafiya kalau Naseer sai yau kake tafe?"

"Ayyuka ne wallahi suka mini yawa shiyasa Tun rancan ban sake shigowa ba".

" Allah sarki Yasu Hajiya ".

" suna lafiya ".

A hankali ta daga idon ta ta kalle shi sanye yake cikin blue jumper'n da ya matukar karbe sa duk da cewa shi din ba fari bane kuma ba za'a ce mishi baki ba sajen sa kwance lub a fuskar sa sai hular sa da yasa kalar Kayan hannun sa rike da wayar sa iPhone 11 pro sai key dake hannun sa yana Dan girgizawa..

" ba zaki gaishe ni bane? "

A bazata taji tambayar tashi sauke kanta kasa tayi don taga ba ita yake kallo ba hankalin sa Na kan wayar hannun shi murya Na rawa tace,

"Ina wuni Ya Naseer".

" ba Zan amsa ba sanda Na roka ".ya fada a gadarance

Shagwabe fuska tayi cikin shagwaban da bata San ta iya ba ta langwabe wuya tace,

" Kayi hakura ba Zan sake ba".

Ba shi kadai ba har Dada sanda ta daga ido ta kalle ta shi kuma cire kan shi yayi yana fad'in,

"Ya jikin nata".

" da sauki fa da dai cewa take hannun ta ke ciwo kuma yanzu ta daina".

Daga Kai yayi ya kalle ta inda ya tankwashe kafar sa yace

"Muga hannun"idanun sa duk a kanta

Daga inda take ta nuna mishi

"Matso mana".ya fada yana hade fuska

Matsowa tayi nan ya Kama hannun ta wani yarr taji a jikin ta don ta gama cika budurwa tunda ta Kai 17 dole in Na miji Wanda take so ya taba ta taji wani Abu a jikin ta da wuri ta dago tana kallon shi Amma shi hankalin sa Na kan hannun matsewa kadan yayi nan tayi karamar Kara sai ya sake hannun ita ko jinjina taushin hannun sa take yi sai kace hannun mace..

" Dada ko za'a kaita asibiti a duba hannun ne kila karaya ce".

"Ba damuwa fa dama mutumi me chemist din yace mini a hankali jikin zai daina ciwo kuma da karaya ne Ai ba zata iya aikin da take yi ba".

" haka ne kam"

Daga nan duk shiru suka yi Dada ta cigaba da cin abinci Amma ta Lura tsam Laylerh ba cin abincin take ba wasa da cokalin kawai take yi..haka kawai taji abincin ya ishe ta ta koshi cikin wasa Dada tace,

" wallahi gwara kici abinci don in ya tafi ba baki wani zanyi ba".

Cikin jin kunyar maganar Dada don ji tayi kamar Dada ta fahimci tana son shi tace,

"Na koshi ne fa".

Yi yayi kamar baya wajen har sanda suka gama cin abinci nan Laylerh ta tattare kwanunkan sannan ta dube shi tace,

" ya Naseer rice and stew ne da beans in sa maka beans din a kan race ko Na kawo rice and stew din kawai?"

"Bar shi kawai naci abinci kan Na fito don yanzu ma tafiya zanyi saboda ina da aikin yi Na leko ne domin Na duba lafiyar Ki".

Shiru tayi nan ta dawo ta zauna shi ko tattaunawa suka Fara yi da Dada Wanda ita bata fahimta tunda ba sanin wadanda ake zance akan su tayi ba ta dai yi shiru ne kawai..

Ledojin da yazo da su Wanda sai yanzu ta Lura da su ya Mikawa Dada daya nan ta bude taga madara da bournvita ne sai kuma five alive guda biyu

" Ahhh Harda sungulla Ka shiga".

"Mara lafiya dai nazo dubawa".ya karishe zancen nashi idon shi a kan Laylerh

" an gode sosai Allah yi albarka".

Amin Amin suka amsa shi da ita sai ya mika Mata daya ledar hijab ne guda uku sai flat shoe guda biyu da abaya guda daya godiya ta mishi nan Dada ma ta tayata mikewa yayi Bayan ya sallami Dada har ya kusa kofa sai ya juyo yace,

"Laylerh zo mana".

Wani salle zuciyar ta yayi nan ta dauki hijab Na Dada a kofa sannan tabi Bayan shi a hankali tana isa ta tsaya d'an nesa da shi nan ya dube ta yace,

" ina fatan ba Wata matsala kuma kina jin dadin zama da ita".

"Eh".

" Masha Allah ".

Shiru duk suka yi kallon sa tayi tana nazarin sa duk da kasancewar sa ba Mai yawan dariya da hayaniya ba sai tausayi yau dai ta gagara gane masa tsam ba sakewa irin ta kullum to ko dai ya gane tana son shi ne..katse Mata tunani yayi da fad'in,

" Ki koma ciki ni Na tafi".

"Allah kiyaye hanya".

" Amin".

Nan ya fice a gidan tana kallon shi a zuciyar ta ko addu'a take yi Allah sa ya juyo ya kalle ta Amma har ya shige mota ya tafi bai kalle ta ba nan ta koma gida cikin sanyin gwiwa...

**

Driving yake yi a hankali gaba daya yau on the other side of bed ya tashi shiyasa shi kan shi bai ganewa kan shi ba bare Laylerh ta gane mishi..tabbas akwai abunda ke damun ran shi Wanda duk sanda ya tuna sai ya zama wani iri Wanda kuma bai son kowa ya fahimci damuwar ta shi yana dai addu'ar Allah yaye mishi ita..

**

Da gudu ta fito daga daki a tsakiyar falon taja birki tana fadin,

"Mallam Mun shiga uku wallahi Umar Farouq baya daki".

Cikin Tashin hankali Wanda aka Kira da suna malam ya mike yana sake carbin hannun shi da yake istigfari a kasa da gani kuma shine Mai gidan, dakin shi suka nufa ba inda basu duba ba har toilet a tare suka fito da gudu suka nufi gate don Tun da ya taba fita kwanaki abun nan ya faru bai kuma fita ba sai yau,to ko dai wani ke fidda shi daga gidan ne basu sani ba saboda in shi kadai ne baya taba nuna yana sha'awar fita iyakacin sa inda yake exercise..

Kallon ta malam yayi yace

" Tabbas akwai Mai fidda Umar Farouq daga gidan nan"..

Ba inda basu duba ba babu shi babu alamar shi..

Uhum nasan dayawa zasu ce yarinyar nan ta fiya korafi,to ba dole nayi Na mutum ya bata lokacin sa yayi typing takarda dai Free book ne Amma ace cikin mutum Dari shida koma fiye da haka kalilan ke comment Wanda adadin su bai wuce Ashirin ba,sannan cikin Ashirin din masu tayaka sharing basu wuce biyu ba...

For Goodness sake kuna mini adalci kenan Yaseen in banga chanji yau ba Na hakura da rubuta littafin tunda ba abunda nake samu fashe rauni,Ku da zaku yi motivating Na ta hanyar comment ni kuma naji karfin gwiwar cigaba da book din Amma shiru kake ji

Comment

Share

©Hafciey Musa

[1/25, 5:36 AM] Hafciey Musa😘: * LAYLERH *

(The prettiest emerald)

Bayan dawar malam daga police station sai ya zauna akan kujera nan Baaba ta dauko mishi ruwa ta ajiye, shanyewa yayi yana ajiyar zuciya.. Bata tambaye shi me ya faru ba sanda taga ya huta nan ya labarta Mata duk abunda ya faru sannan ya mike a kujerar ya rufe fuskar sa da hular sa..

Mikewa tayi zata nufi kitchen sai taji yana cewa,

"Kunna mini Ac Zafi nake ji".

" ikon Allah malam wani AC kuma?"ta fada cikin tsare shi da idanu

"Ac mana Na sama".

" to Ai gani nayi a kunne yake".

Mikewa zaune yayi yana tsaki don pressure ne kawai ya mishi yawa nan yace,

"To kunna mini standing fan nan Ki Ki kawo shi kusa da ni".

" malam kullum fa sai doctor yayi maganar sanyin nan ya Hana Ka fa".

"Cewa nayi Ki kawo mini in kuma ba zaki kawo ba sai Ki fada mini Na tashi Na dauko".

Fankan ta kawo mishi Bayan ta kunna sai ta nufi kitchen tana cewa,

" Bari Na daura maka kunu".

Bai amsa ba ita ko geda ta dama sannan ta daura kan gas yana ci kadan kadan falon ta dawo ta zauna, tana zama ba jimawa kuwa Umar Farouq ya fito daga dakin shi sanye yake cikin bakar jallabiyar da ta matukar amshe shi lumshe idanun yake ys kuma bude su akan iyayen nashi, tsayawa yayi a kan su sai ita ce tace,

"Ya dai Umar Farouq zauna mana".

Oho shi bai ma San tana yi ba kalle-kalle ya Fara kamar Mai Neman wani Abu nan ya nufi kitchen sai malam ne yace,

" kin bashi abinci kuwa?"

"Yanzu fa ya tashi".

Kan tagama bada amsa har ya shiga kitchen malam ne ya Fara ganin shi ya fito rike da tukunya yace,

" me kuma Yaron nan ya dauko".

Juyawa tayi don ganin me ya dauka sai ganin tukunyar kunun ce a hannun sa cikin Tashin hankali tace,

"Ka ajiye Baba Na zaka kone akwai Zafi".

Abunka da Mara hankali ko a jikin shi duk da kuwa tabbas yana jin zafin nan ya nufo su da gedan gaba daya mikewa suka yi sai malam yace,

" Mun shiga uku Ki Karba mana kin fa San ba hankali ne Gare shi ba".

Gab malam ya tsaya nan ya daga tukunyar ya Fara juyewa cikin hanzari malam ya matsa gefe Ai ko a inda ya tashi ya juye Rabin Baaba kam rufe bakin ta tayi da hannu tana kuka Juyowa Gare su yayi Ai duk baya suka riga yi nan ya juye sauran a tsakiyar falo ya kuma nufar kitchen din sai malam yace,

"Kizo mu gudu wannan Karon in nayi rantsuwa kaffara ba zai Kama ni ba cewa wuka zai dauko".

Ai ko a take suka fice a falon kan ya fito sannan suka rufe shi ta waje sun mance da kofar kitchen da akwai hanyar fita..duk ajiyar Zuciya suke saukewa sai kawai ganin shi suka yi a kan su ba shiri malam yasa kafa ya nufi waje ita ko Baaba cewa take yi,

" yanzu malam tafiya zaka yi Ka Bari ya kashe ni".

Tuni ya fice a gidan matasan kofar gidan Na ganin shi suka ce yaya nan yace,

"Dan Allah kuzo Ku taimaka mini mu daure Yaron nan nawa haukar sa ce ta tashi".

Da wuri suka mike gidan suka shiga daidai lokacin shi kuma ya daga wuka zai chakawa Baaba sai ji yayi an rike hannun sa duk yadda yaso kwatar kan sa ya kasa haka suka taru akan shi daga shi suka yi nan suka tambaya ina za'a Kai shi malam ne ya musu jagoranci suka nufi dakin shi a gado suka ajiye shi sannan suka juya da wuri tare da rufe shi ta waje..

Godiya su malam suka musu nan suka fice Baaba ko kuka ta Fara tana fadin,

" yanzu fa Shikenan duk magungunan da muke basa ya tashi a banza kaga yanzu ya sake birkicewa Amma Allah sai ya saka mishi don nasan baida hakkin su".

"Ni wallahi duk lokacin da Na zauna sai Na rasa tunanin me zanyi saboda lamarin sa akwai rikitarwa addu'a zamu cigaba da yi masa a matsayi mu Na iyaye".

Ita dai kuka take yi don ita kadai ta San me take ji in ta Gan shi a wannan halin

" har zuwa yaushe zai warke ya dawo kamar kowa har yaushe zamu cigaba da ganin sa cikin wannan jarabawar ".

Ta fada tana Kara fashewa da kuka

" har zuwa sanda zamu cimma wannan jarabawar Ki daina kuka a matsayin Ki Na uwa addu'a zaki masa".

"Wani irin addu'a ne bana masa kana sane fa komai namu gab yake da karewa a kan shi".

" kada Ki damu Allah Na nan kuma yana sane da mu don shi ba azzalumin bawan sa bane"..

****

Kasancewar yayi dare sosai a wajen shashancin shi kuma polisawa Na kame Gashi yana da nisa da gida sai kawai ya yanke hukuncin zuwa gidan madam tunda yana bakin titi..

Ya ko yi sa'a gidan a bude yake don haka sai ya shige yana wani murmushin da shi kadai ya San manufar shi..ba kowa bane fashe bakon madam da ke zuwa su kwana tare har Wata ran take tura Laylerh gidan oga Emeka in yazo..

Kofar falon a rufe yake don haka sai ya yanke hukuncin ya zagawa ta baya sai ya buga Mata window yace shine ta bude..

Duk da kasancewar sa namji sanda ya firgita ganin abunda take yi cultism take yi irin Wanda Laylerh ta ganta tana yi..ido ya bude ya Kara kallo tabbas hakan ne don haka cikin sanda ya nufi waje oga Emeka ya bugawa kofa

"Wai Waye ne sai mutum Na zaman shi azo Ana takura masa kuma nasan madam nan ne".

Yana budewa yaga ba ita bane sai dai fuskar is familiar tunda ya Saba ganin shi a wajen madam cikin hade girar sama da kasa yace,

" yes how may I help you".

Zufa yake hadawa nan ya riko hannun oga Emeka da duka hannun sa biyu yace,

"Pls kazo akwai abunda Zan nuna maka so nake Ka zama witness".

" me shi kuma meyasa ba zaka Kira wani ba sai ni".

"Pls I beg of you don't refuse words self can't explain what I see in Munje zaka gani".

" a ina ne".

Da hannu ya nuna masa gidan madam sai ya girgiza Kai yace,

"No ba zanje gidan wancan matar ba bata da mutunci kuma bamu shiru".

Hada hannun sa biyu yayi alamar pleading yace,

" pls zaka yi saving lives ne".

Jin haka sai suka wuce gidan Ai oga Emeka Na gani ya zare ido ya bude baki zai ce Jesus da wuri mutumin ya rufe bakin shi sannan yaja hannun sa suka bar gidan suna fita oga Emeka yace,

"I can't believe abunda ido Na suka gani so ita ce mayya Amma tace is that small girl".

" duk ba wannan ba yanzu me zamu yi?"

"Gidan land load namu ba nisa kazo muje mu sanar da shi".

Haka ko aka yi sauri suke tayi har suka isa gidan shima basu ce da shi ga abunda suka gani ba gudun kada kafun su koma ta gama ya zama sun Mata kazafin maita Wanda tana da damar shigar da su kotu sannan a hukunta su, cewa kawai suka yi akwai abunda za'a nuna mishi Wanda bai dace Ana yin shi ba a matsayin shi Na land load nan yace shinkenan zai je da matar shi suka fita basu tsaya ko ina ba sai gidan madam aiko duk hankalin su ya tashi da abunda suka gani a lokacin ne kuma madam din ta farga da Ana kallon ta a take light din dakin yayi switching kan shi nan aka rika buga kofa taki budewa Wanda sanadin hakan ya Fara janyo hankalin mutani zuwa gidan Ai da kowa yaji sai ayi ta mamaki ciki kuwa Harda masu cewa Haba ba banza ba ma mutani ke mutuwar wulakanci Ashe ita ke kashe su..

Ganin fa ba zata bude kofar ba yasa suka balla kofar cikin Daren nan aka fito da ita aka rike kowa Na Allah wadaren halin ta..gidan land load d'in aka wuce da ita aka daure wasu ko cewa suke yi a kona ta a wajen sannan aje a kona gidan ta tunda Kwanaki ita tace yarinyar can mayya ce nan wasu suka ce a barta zuwa gobe da safe za'a San hukuncin da za'a Mata sannan gida kuma ba za'a kona ba tunda ba nata bane haya take yi masu shi zasu yi asara..

Washe gari!!

Daidai kofar restaurant din keke napep ya ajiye ta bata karu ba kuma bata ragu ba ma'ana ba abunda ya sauya a jikin ta kudi ta bawa Mai keke Bayan ya bata chanji sai ta nufi cikin restaurant din tana tauna chewing gum..

Yadda taga su mairo duk sunyi jugum ta San akwai matsala nan tace,

"Madam fa".

" bata fito ba".

"Tana gida ne?"

"Eh".

Suka ce Mata cikin gajiya da bata amsa..

wani Babban mutum ne ya bata kudin da ya ninKa Na madam uku kan cewa ta nemo mishi yarinya karama kuma ba inda bata duba ba ta rasa shiyasa hankalin ta ya karkato kan Laylerh da ta sayarwa madam don ba zata iya Bari kudin ya wuce ta ba shiyasa ma kawai ta yanke hukuncin zata mayarwa madam kudin ta sannan ta dauki Laylerh duk da ta San Abu ne Mai kamar wuya..

Ficewa tayi a hotel din napep ta sake tarewa nan ta nufi gidan madam din..

Su kuma da ido suka raka ta don zuwa yanzu labari ya gama iso su cewa wacce suke aiki a karkashin ta mayya ce sosai suka tausayawa Laylerh mairo ko matsalar ta inda zata ganta ta bata dubu biyar nata don har yau yana nan a ajiye bata taba sisi a ciki ba...duk tattare abunda ya shafe su suka yi sannan suka fice a restaurant din don daga yau ko me ake basu a wajen sun hakura da aikin...

Duk da taga mutani nata shiga gidan bata kawo komai a ranta ba don tasan madam da kwashe-kwshe shiyasa ta shiga gidan da gadara sai gani tayi Ana kokarin kona Kawar ta nan ta tambayi Na kusa da ita sai ya fada Mata abunda ke faruwa da wuri

ta fara cusa Kai cikin mutani tana wucewa har ta samu ta iso gaban su nan ta dubi Kawar tata da duk an sauya Mata kamanni daga jiya zuwa yau da duka..

" ke kuma Wa Cece?"

Wani ya tambaya

"Nice Aunty'n yarinyar da tayiwa sharri ce kuma nazo ne ta fada mini inda yarinyar take in ba haka ba kotu ce zata raba mu".

" Kinga mu batun yarinya bai dame mu ba Ki masa mu cire mugun iri a cikin mu ".

Kukan munafurci ta Fara tana rokon madam Allah annabi da ta fada Mata inda ta Kai Laylerh sai oga Emeka ne yace,

" Ai ance Abokin barawo barawo ne don haka Na tabbatar ita ma Kawar mayya ce don ba yadda za'a yi tace bata San madam maye bane".

Ya fada cikin hausar shi da bai kware ba sai wani ne yace,

"Mayya ake cewa ba maye ba oga Emeka".

Nan fa jama'a suka yi Na'am da zancen oga Emeka aka cigaba da dukan su tare..

Wannan shine Tashin hankalin da ba'a sa mishi Rana don Larai sanda tayi regretting Na abunda ya kawo ta kano karshe police aka Mikawa su ba don ran wasu yaso ba Amma ya suka iya tunda basu isa Daukan doka a hannun su ba koda aka Kai su police station ba karamin wahala aka basu ba da kyar Larai ta samu ta tsere Bayan ya tabbata ita ba mayya bace don dukan da Tasha bata ko iya gane hanya...

Yau tunda ta tashi da fara'a ta tashi Wanda sanda Dada ta Lura don ko sanda take wanke-wanke sai murmushi take yi ita daya Dada ta gama fahimtar Laylerh din son Naseer take yi Amma sai bata ce da ita komai ba...

Bayan azahar da jiki da Fara aikin masa tsabanin Wata Rana da sai Dada tayi magana sau biyu ko uku,kudin nika ta Karba nan ta fice ta Kai nika tana dawa ta kwaba sannan ta ajiye a Rana domin ya tashi..tunda tazo Kano bata taba yin wanka irin Na yau ba don ba karamin dirje jikin ta tayi ba hakan yasa ta jima sosai a bandaki har Dada ta Fara tunanin ko lafiya sai Gata ta fito..alwala tayi sannan ta nufi daki Kayan ta da bata taba Sawa ba ta fitar nan Tasa sannan ta dauki madubi ta kalli fuskar ta tana murmushi kwalli Tasa sai Jan bakin Khadija da powder da ta manta nan ta kalli kanta tana cewa,

"Ai nasan yau sai ya Naseer ya jinjina kyau da nayi tunda jiya har ya iya gane fuska Na ya canza don kitson da nayi".

Sallah'n la'asar tayi sannan ta sa hijab nata shima Wanda bata taba Sawa ba tana fita Dada tace,

" to wannan kwalliyar kam duka Na Naseer ne?"

Rufe fuskar ta tayi Wai ita a dole kunya sannan ta dauki sinsiya tayi waje hatta sharan ma yau Na Musamman tayi shi,Kayan sana'ar ta fitar Harda fitar masa da kujera sannan ta dauki tularen Dada a boye tazo ta fesa ta mayar sannan tazo ta zauna ta Fara tuya tana duba hanyar shi..

Tun tana sa ran zuwan shi har Randa ya soma baci ta ma daina fahimtar abunda take yi gaba daya ji take kamar ta sa hannu akai tayi ta ihu haka take ji..tabbas ta San wani Abu ne ya Hana shi zuwa Amma ta kasa tausasa zuciyar ta gaba daya ta rasa me ke Mata dadi duk fa wannan kwalliyar don shi tayi har ta gama bai so ba tattarawa tayi ta koma ciki kallo daya zaka Mata Ka fahimci ran ta a bace yake Dada ko sannu bata ce da ita ba don tana ganin wautar Laylerh ina ita ina Naseer

duk da bata San ko shima yana son ta ba..Bayan sallar magrib suka Irga kudi ribar Dari biyu kawai aka samu nan Dada tace,

"Ai dama Na son dole za'a yi haka,in fa baki son sana'ar nan Ki fada mini ba Wai ban son kudi nane Na cire Na Fara miki sana'a da shi ba,Shikenan don Naseer bai zo ba ni kuma sai kija mini asara".

Shiru tayi don Dada Nada gaskiya

" Wato ma banza Kika yi da ni ko to wallahi Bari Naseer din yazo ce mishi zanyi Na gaji ya dauke Ki tunda dama don shi Na karbe Ki Amma tunda ke din naga ba yadda nake tunani bane gwara yasan inda zai Kai Ki".

Cikin sanyi tace

"Kiyi hak'uri Dada in sha Allah ba Zan sake ba".

Bata amsa Mata ba nan suka yi i'sha abincin dare ma cewa tayi ta koshi daga nan Dada bata sake bin ta kanta ba har lokacin shigar su yayi..

So take ta sake rai ta cire rashin zuwan shi a ranta Amma ta gagara Daren ranar da kyar ta iya bacci don bacin rai...

Washe gari daidai da Fara sana'ar su kwana biyar yau saura kwana biyu kenan su tafi jalingo Tun safe komai cikin sanyi take yi Bayan sun karya Dada tayi magana yafi a Irga kan cewa ta tashi taje ta sayo shinkafar masa tunda basu da Na yamma Amma komai cikin sanyi take yi ita dai Dada zuwa yanzu Laylerh ta gama kawo ta wuya ta shiga daki zata dauki hijab kenan wayar Dada ya Fara ringing kuma Khadija ce,

" Dada ina kwana".

"Lafiya kalau ya wajen Ku".

" muna lafiya ya Laylerh".

" tana lafiya".

"Tafiyar taku saura kwana biyu ko?"

"In sha Allah".

" to nima gani a hanyar asibiti Zan Kai abinci in ina dawa Zan biya gida sai Randa zaku tafi Na dawo ".

" Asibiti kuma waye ba lafiya?"

"Wallahi ya Naseer ne".

" subhanallah Mai ya samu Naseer din".

Cak Laylerh ta tsaya jin an ambaci sunan Naseer

"Kwantar da hankalin Ki Dada stress ne Yama ji sauki kin San ciwon shi ai".

" to Shikenan in sha Allah mu ma muna tafe zamu zo mu duba shi".

"To sai kunzo Zan jira Ku sai mu dawo gidan tare".

Suna sallama Laylerh ta dubi Dada ido cike da hawaye tace,

" Dada me ya same shi?"

"Ban sani ba".

Rike hannun Dada tayi tace,

" Ayya dai".

"Ince Tun dazun nake miki magana Kika yi banza da ni yanzu kuma daga jin sunan Naseer kike tambaya me ne".

" kiyi hak'uri ".

" Wai baida lafiya ne shine naje Zan zo duba shi".

"Ayya Dada Na tuba ba don hali Na ba mu tafi tare".

" shefenan masar fa".

"Daga wajen Zan nufi kasuwa nayi".

" to".

Tace nan taji dadi don gaba daya hankalin ta sake tashi yayi jin Naseer ba lafiya nan Dada ta shirya don ita kam dama da shirin ta Na tafiya kasuwa suka nufi asibiti...

***

Tun Bayan barin shi falon Hajiyar sa apartment nashi ya shiga ya gama komai sannan ya kwanta Washe gari kuwa sai ya tashi da zazzabi don bai ganewa jikin sa ba jin shiru bai fito ba sai Hajiyar ta nufi apartment Na shi kwance ta same shi nan tace,

"Yanzu Naseer don Na raba Ka da yarinyar can shine kaki zuwa Ka gaishe ni ko".

" Mom wallahi ba haka bane ban jin dadi ne ".

" ba wani Shikenan don yarinyar nan zaka daurawa kan Ka cuta ko to Kai Ka sani".

Ficewa tayi a dakin don tsam ita bata yarda bai da lafiya bane sai da Dad nashi yaga shirun yayi yawa nan shima ya nufi dakin don ba ranar da Naseer baya zuwa gaishe su nan ya tarar baida lafiya

"Subhanallah Tun yaushe kake kwance tashi Bari Na Kira driver ya kai Ka asibiti ko Na Kai Ka da kaina".

" Ehhh Abba if you are less busy Ka kaini da kan Ka".

Sosai yaji tausayin Yaron nashi nan ya zuba masa ido Musamman da yaga da kyar yake shiryawa taimaka mishi yayi daga nan suka nufi asibiti suna zuwa kuwa aka bashi gado sai a lokacin hankalin Hajiyar sa ya tashi nan suka shirya suka nufi asibitin a wajen duk suka kwana da yake a side ward suke ba ruwan su da hayaniyar mutani..

Washe gari da safe kuma yaji sauki sosai don dama stress ke damun shi ya kuma ga Gata wajen dangin da abokanayen arziki don sai shiga da fita ake yi a dakin kuka duk sanda ya kwanta basu gajiya da zuwa nan aka ce yana da bukatar hutu sai suka mishi allurar bacci..

Ko da Khadija ta kawo breakfast su suka ci shikam yana bacci don ya sha tea..

A wajen asibiti Mai keke ya sauke su nan Dada ta biya kudi suka nufi cikin asibitin..duk da son ganin shi da take yi sai zuciyar ta ya Fara bugawa a haka Dada ta Kira Khadija tace gasu a harabar asibitin tazo ta shigar da su don asibitin ya musu girma ba ganewa zasu yi ba..Ai ba jimawa sai ga Khadija nan suka rungume juna da Laylerh sannan suka nufi dakin..

Tura kofar dakin Khadija tayi da sallama su ko suna biye da ita a baya time din Hajiya ce sai kannen sa biyu a dakin shi ko yana kwance kan gadon marasa lafiya yana bacci..

"Ina wuni Hajiya".

Kin amsa gaisuwar Laylerh din tayi nan Dada ta gaishe ta ita ma cikk-ciki ta amsa Mata ta tambayi ya Mai jiki tace da sauki nan kannen sa biyu suka gaishe da Dada daga nan basu sake ce Mata komai ba..

Abun duniya duk ya dame ta ganin ba haka suka Saba yi da yaran ba don tamkar uwa suka dauke ta kasancewar ta Nanny a Gare su Amma sai Gashi yau gaisuwa kawai suka Mata sannan suka maida hankalin su kan waya..

Laylerh ce ta gaishe su ba tare da sun dube ta ba suka amsa..shiru-shiru har suka yi minti goma ganin they are not welcome tunda ba'a basu fuska ba yasa Dada mikewa tace,

" to mu zamu wuce Allah Kara lafiya".

"Ameen"

Sai Tasa hannu a jaka ta fiddo dubu daya ta Mikawa Dada tace,

"Mun gode ga wannan ayi Na machine".

" a'a da kin bar shi kawai".

Sai yanzu yaran suka saka baki suna fad'in

"Dada yau kuma kece zaki Ki karban kudi a hannun Hajiya sai kace Wata bakuwa".

" Ai gani nayi a asibiti kuke".

"Duk da haka Ki Karba Ai Na machine ne".

Nan ta Karba tayi godiya sannan suka fice Bayan Khadija ta sallame su kasuwa suka nufa kowa da kalar tunanin da yake yi..

Yau gaba daya bata da walwala ba don Khadija ba ma da ko uwar kudin ba lallai a samu ba sun dai samu ribar dubu daya ranar haka suka rintsa kowa rai ba dadi...

Washe gari kuma da shiri suka tashi kimsa ko ina suke yi shiyasa ba zasu yi masa ba ma Dada ce ta kuma fita Neman bashin ta ranar dai tayi sa'a ta samu dubu biyar nan ta dawo tana mita..

Daga jiya zuwa yau ba Wanda ya gane Mata don ita kan ta ba ganewa kan ta tayi ba so take ta ce Dada ta Dan Mata waya ta Kira taji ya jikin shi Amma ta gagara..

Bayan asr Dada taje ta musu booking Na motar Taraba turn one kan ta dawo sun gama abincin dare..suna sallar magrib suka shimfida tabarma a tsakar gidan da hasken farin Wata Na haska ko ina abinci suke ci Amma ita Laylerh ji take yi kamar magani take ci yanzu Shikenan haka zasu yi tafiya ba tare da ta Gan shi ba Gashi bata San adadin lokacin da zasu dauka kan su dawo ba..

Sallama yayi a gidan da wuri ta daga ido tana kallon shi ji take yi kamar taje da gudu ta rungume shi sai ta sadda kanta kasa tana goge hawayen da ke zuba a idon ta..Khadija ce ta bashi wajen zama Dada ko cewa tayi,

" Mara lafiya da kan shi yaushe aka sallamo Ka?"

"Jiya da dare wallahi naji sauki ai sosai".

" Masha Allah Ince dai yanzu ba abunda ke maka ciwo?"

"Ba komai shekaran jiyan ma dai rashin hutu ne".

" to Allah kyauta ".

" Ya Naseer ina wuni?"

"Lafiya Khadija kin gudo ko".

Murmushi tayi sannan tace,

" A'a fa ya jiki".

"Da sauki".

" sannu da zuwa ".tace da shi

" Yauwa".

Mikewa tayi nan ta kawo mishi ruwa sannan Dada tace,

"Bari a zuba maka abinci".

" Dada bar shi kawai baki Na ba dadi".

"Ai miyar shuwaka ce in kaci zaka ji dadi kuma kullum in kazo gidan nan baka son cin abinci".

" Dada kin manta ina da diabetes ne kuma ba ko wani irin abinci nake ci ba".

"Kaga wallahi mantuwa nayi".

Mikewa tayi cikin sanyin jiki ta nufi kitchen shi ko da ido ya bita jin Dada Na mishi magana ne sai ya dawo da hankalin shi Gare ta nan ta wanko hannun ta koma ta zauna..

Ta rasa me take ji guda daya,shin tana murnar zuwan shi ne ko bakin ciki..Bayan sun Dan taba hira da Dada sai ya mike yana fad'in,

" Dada ni Zan wuce dama nace Bari Na leko Ki ne, Mai masa kam ta daina ne? "

Ya fada yana kallon fuskar Laylerh daidai lokacin ita ma ta daga ido ta kalle shi sai gani tayi ya kashe Mata ido daya a take fitsari ya cika Mata Mara shin da gaske ne ko idon ta ne..

Ganin yadda ta rikice sai yayi murmushi sannan yace,

"Ni Na tafi, Laylerh zo mana".

" Mun gode Ka gaida gida".Dada ta fada

Ficewa yayi ita ko Dada ta kalla jin bata ce komai ba sai Khadija tace,

" tashi Na raka Ki yana jiran Ki fa".

"A'a bar ta taje Ai ita ya Kira Baku biyu ba".

Da kyar ta iya mikewa sanda taje tayi fitsarin da take ji kamar zai fasa Mata Mara sannan ta nufi waje cikin mota ta same shi jingunuwa tayi jikin motar shi ko cewa yayi,

" ni ma sai anja mini ajin ne?Ki zaga Ki shigo magana zamu yi kuma dare nayi".

Zagayawa tayi ya bude Mata mota ta shiga sannan yayiwa motar lock da wuri ta daga ido ta kalle shi

"Kwantar da hankalin Ki madam you are safe".

Ajiyar zuciya ta sauke daga nan duk shiru yayi can yace,

" me ya hanaki zuwa duba ni a asibiti? "

Kamar zata yi kuka tace,

"Munje fa da Dada kana bacci ko Hajiya a tambaya".

" Shikenan kuma sai ba zaku sake Komawa ba?"

Shiru tayi saboda a ranar taga tsanar alakar ta da Naseer a idon Hajiya a baza ta taji yace,

"Shine kuma har gobe zaku yi tafiya baki sanar da ni ba yanzu kin yiwa kan Ki adalci".

Kai ta girgiza sai ga hawaye shiru tayi sai ji tayi yasa hannu ya share Mata hawayen yace,

" yaushe zaku dawo?"

"Wallahi ban sani ba don alamu sun nuna zamu jima tunda jinya zata je yi".

Shiru yayi har ta cire ran zai ce wani Abu sai yace,

" Laylerh ni a matsayin kanwa Na dauke Ki yadda ba Zan so wani Abu ya cutar da kanne Na ba haka zalika kema don haka ina baki shawara a matsayin Yaya kuma Na Wanda ya girme Ki da Ki Kama kan Ki Ki kuma rike mutuncin Ki duk inda zaki je saboda can bana nan bare kiyi tunanin in kin shiga wani hali zan taimaka miki,ni ban San da tafiyar Ku ba sai dazu da Zan sa Khadija aiki aka ce tazo nan Wai Dada

zata yi tafiya don haka ban cika alkawari Na ba na saya miki waya ba amma zamu ke gaisawa ta wayar Dada".

Hawaye take yi sosai don yanzu duk duniya bata da wani dangin da ya wuce shi,shi daya

"Ki zama Mai musu biyayya har zuwa sanda zaki dawo kan nan Zan nema miki makaranta in rai bai yi halin shi ba".

Da wuri ta rufe masa baki da tafin hannun ta tace,

" in sha Allah ko mutuwa ce zata ji tausayi Na ta bar mini Kai don Kai din komai Na ne".

"Laylerh Ai mutuwa Na kan kowa Wa ya San Wanda zata Fara dauka cikin mu".

Fadawa jikin shi tayi ta rungume shi tana kuka kamar zata hadiye ranta a hankali ya Fara petting Bayan ta yana fad'in,

" to kuma karya ni zaki yi ne sauka a jiki Na kada Dada ta Gan Ki tace ina lalata Mata yarinya ".

Shiru tayi tana jin yadda zuciyar shi ke harbawa da sauri sauri numfashin shi da yake sauka a wuyan ta kuma Zafi jau kenan har yanzu bai warke ba..

" kalli nan".

Yace dago da fuskar ta tayi sai gani tayi ya dauke su Hoto da wuri ta sauka a jikin shi cikin jin kunya da kuma haushin kanta yanzu zai ce bata da kamun Kai ta juya

tana kallon waje har yanzu kuma tana hawaye don bata son tayi nesa da shi taje wani garin da ba Wanda ta sani sai Dada kadai...

Shima dannewa yake yi kasancewar shi Na miji kuma an San maza da jarumta in ba haka ba bai son nisa da ita yana jin ta tamkar kanwar sa shiyasa yake son inganta rayuwar ta..

Kudi ya Ciro dubu Ashirin yace,

"Ga wannan kuyi kudin moto".

Karba tayi tace,

" Mun gode Amma Ai zaka zo wuri Na ko".

Hancin ta ya jaa yace,

"Ba dole Na ba tunda sisi Na zata tafi".

Murmushi tayi ganin dare yayi yace ta shiga gida nan ya musu addu'ar Allah tsare tana kallon shi yana kallon ta har ta shige ciki..

Shi yanzu Babban burin sa yasan inda iyayen ta suke ya maida ta gaban su ko kuma ya sama Mata miji Na gari Wanda ya tabbatar zai rike ta da amana Amma kuma yasan ba namji Mai tarbiya da zai auri wacce bata da asali..

Numfashi ya sauke sannan yaja motar ya nufi gida..

Tana shiga gida ta bawa Dada kudin nan ta Kira shi ta mishi godiya ranar dai su Laylerh an sha bacci..

Washe gari karfe shida ya same su a Tasha kuma lokacin motar su ya tashi nan Khadija ta koma gida dama ita kadai ce ta musu rakiya..

Tun tana kallon hanya har ta Fara gajiya tayi bacci ta tashi har kafar ta suka Fara kumbura tafiya yaki karewa gaba daya ta gaji Naseer ma ya Kira ya tambaya ya hanya suka ce alhamdulillah..

Ana gab da kiran magrib taga sun iso wani gari da aka rubuta *WELCOME TO TARABA*

" alhamdulillah home sweet home there is no where like home"

Taji Wata fasinja ta fada..

Masu comments ina godiya Allah saka da alkhairi

Comment

Share

©Hafciey Musa

[1/25, 5:36 AM] Hafciey Musa😘: *□LAYLERH□*

(The prettiest emerald)

A Tasha aka sauke su nan kowa ya Fara kokarin fitowa drive da conductor duk sun fito Ana cirewa kowa Kayan sa a booth..tashan a cike yake makil da mutani matafiya da suka dawo gida, daga gefen su kuma wani mota ne Wanda shi kuma

daga jigawa ya fito..Bayan an gama sauke musu Kayan su suna kokarin tafiya sai suka ji ance,

"Wannan kamar Laylerh nake gani"..

Cikin sauri suka juyo ta inda suka ji an kira sunan ta Duk ido suka zurawa dottijon da ya fadi haka sai ita ce tace,

" Ayya Ka San ni ne malam".

Girgiza Mata Kai yayi nan suka gaisa da Dada sannan ya wuce shi da Abokin tafiyar shi, tabbas duk yadda aka yi wannan mutumin ya San ta kawai dai yaki fada ne..

"Haruna Ka San ta ne?"Abokin tafiyar sa ya tambaya

"Sosai ma Niko Na San ta".

" to me yasa kace baka San ta ba".

"Daga ni har ita dalili daya yasa muka bar gida Wanda nikam Kai shaida ne sanda nayi jinyar Wata uku kan Na warke kuma har yau Na gagara sayawa da kafafu Na sai kune abokanaye na kuke taimaka mini".

Shi din ya gagara tsayawa da kafafun sa kullum Gashi a karkashin abokanaye yana Neman taimako ya rasa aikin yi shiyasa Abokin Na shi da zai zo taraba wajen minister of power Wato Sale Mamman yace su zo tare ko Allah zai sa a taimaka a bashi aiki".

" ina ji yanzu kam Ai ya dace Ka bani tarihin rayuwar Ka ko don dadewa da muka yi a tare".

Dogon ajiyar zuciya ya sauke sannan yace,

"Mu samu waje mu zauna sai Na fada maka" .

WAIWAYE

Malam kabiru shine kakan ta Wato mahaifin Baban ta yana da yara maza hudu bai da mace ko daya,yaran duk sun tashi kan su a wargaje don kusan ko wanne da uwar sa..kakan ta kawu ne a Gare ni don haka kusan gida d'aya muka tashi da Baban ta kuma duk kan mu daya..

Mahaifiyar Baban ta Wato Hajja laraba ita ce uwar gida shiyasa Dan ta ya d'an girme mu, kowa a gidan da irin kalar hududbar da uwar shi take mishi shiyasa lokaci da dama kowa burin shi ace yafi Dan uwan sa..kakan ta manomi ne shiyasa yaran ma suka taso da son noma a ran su..lokacin da muka Kai Aure kowa Na kokarin yi sai dai shi Musa Wato mahaifin ta baida sana'ar yi shiyasa gidan su yarinyar da yake so suka ce ba zasu bashi auren Yar su ba saboda bai da abunda zai rike ta da shi don haka ya zage yana Neman aikin yi Amma shiru Gashi yana matukar son Hadiza shiyasa mahaifiyar sa ta nema mishi aiki a wani shago..

Sosai yayi murna daga shi har Hadiza Wata ran Hadiza ta Kai mishi ziyara shago, sun sha hira ganin lokacin sallah yayi sai yace ta jira mishi shago Bari yaje yayi sallah yanzu zai dawo.ba musu ta amsa nan ya tafi sallah ita Hadiza ko kan ya dawo ta sata gold sai Tasa a jakar ta koda ya dawo sai suka yi sallama ta tafi gida..

Bayan zuwan ta shago da kwana biyu sai ta Kira shi a waya tace,

"Ince kudi ne ya hanaka tada zancen auren mu".

" ehh".

Yace da ita nan ta aika mishi da kudaden da ta sayar da gold din sosai yayi farin ciki don bai San inda ta same su ba..

Baikon ta yayi nan ya Fara hada Kayan Aure,dama duk karshen shekara Mai gidan sa yake zuwa su Irga su fidda riba da uwar kudi to wannan Karon ma hakan ce ta kasance sai ogar yace mishi ba daidai bane akwai kudi Mai yawa da babu nan yace ogan bai lissafa da kyau ba..sake lissafawa suka yi a tare nan suka tabbatar babu a wajen ogan ya sallame shi ranar dai sosai hankalin shi ya tashi wasu daga cikin 'yan uwan shi sun taya shi jimami wasu ko dadi suka ji nan dai ya cigaba da Tara Kayan Aure..

Ana saura kwana biyar akai kaya ya hadu da wani Abokin shi nan yake cewa,

"Ashe haka kake da zuciya Mai kyau?"

"Me kuma nayi?"

"Hmm wallahi ranar ina zaune a kasuwa sai kawai naga Hadeeza tazo da gold da Ka bata ta nuna mini tana tambaya Na a ina ake saya nan Na nuna Mata".

Shiru yayi tabbas ya yarda da zancen Abokin kenan Hadeeza ce ta dauka sallama suka yi bai sake cewa komai ba..

Gidan su Hadeeza yaje dama tana da kanwa wacce take 'Yar yadikkon ta nan yace Mata yana son ta in ta amince zai Aure ta nan take ta amince don bata San cewa shine saurayin yayar ta ba..

Ranar da ya sanar da Hadeeza za'a kawo kaya ita ma Amina ta sanar da mamar ta nan aka yi ta shirin karban kaya har biyu..

Ana kawo Kayan dakin su Amina aka Kai Wanda hakan ba karamin tada hankalin Hadeeza da mahaifiyar ta yayi ba koda ta tambaye shi sai cewa yayi ya fasa auren ta,tana ji tana gani ya Auri Amina hakan ko sai ya raba kan su..

Bayan Aure da sati daya suka bar garin..

Maiduguri ya koma cikin local gov Na Biu karkashin wani kauye nan suka Fara sabon rayuwa da matar shi Amina..nasan kowa yasan Maiduguri ba zaman lafiya ake yi ba saboda yadda 'yan boko haram suka sa su a gaba..a can din ma noma malam Musa ya Fara inda Allah yayiwa abun albarka..

Sun shafe shekaru biyu tare kan Allah ya azurta ta da ciki ta haifi 'Dan ta namiji wanda yaci sunan shi Muhammad Bayan haihuwar Muhammad da shekara hudu ta sake haifar mace wacce taci suna Laylerh Bayan Laylerh bata sake haihuwa ba..

A gidan haya suke zaune matar gidan ta rasu Mai gidan ne kawai sai yaran shi in ba an fada maka ba ba zaka taba cewa su din haya suke yi ba dauka zaka yi ita din yadikkon yaran ne da yake malam Musa a wani kauye yake noma shiyasa wani lokacin in damina ne sai yayi Wata bai leko gida ba Amma yana barin su da abinci inko babu Wanda suke haya a gidan shi ya kan saya musu..

"Ba za ki tashi ki d'auko mini abinci bane?"

Jin yadda ya daka mata tsawa sanda ta tsorata nan take ta mik'e sai kitchen ta d'auko masa gami da durkusawa ta ajiye masa a gaban sa.

"'Yar iska kawai yaran shegu".

Carab Aunty'n ta ta amsa tana fad'in,

"Ka daina sheganta ta don kawai muna haya a gidan Ku ba shi ke nufin zaku mana duk abunda ranku ke so ba".

Tsaki ya ja gami da cewa,

" don kawai nace a bani abinci sai a tsaya gaya mini magana,dadin abun ma uba na ke cefene kuma na San in nace ba Zan ci ba cinyewa za'a yi".

"Ni kake fad'awa haka Abdul-maleek?"

Tsaki ya kuma ja gamida cewa,

"Wallahi kin ci sa'a ina ragar miki don mijin Ki ne,anje an d'auko mana yarinya karama an ajiye mana a gida".

" Allah shirye ka".

Tana gama fadar haka sai ga mahaifin su Laylerh ya shigo.

"Yauwa Malam kaji abunda Abdul maleek ya fad'a ko".

Banza ya mata ya shige d'aki nan ko ta biyo shi d'aki tana fad'in,

" gaskiya Malam abunda kake yi sam bai dace ba,ka duba abunda yaran nan suke mini amma baka cewa komai sannan su Laylerh kuma basu Isa su raina su ba sai ace rashin kunya Bayan ni kuma ba'a ganin Wanda suke mini".

"sau nawa zance ki cire ido a kan su?"kin San fa ba abunda mahaifin su baya mana a gidan nan".

Ya fad'a cikin daga murya

"Haba malam...."

Ganin ba yi da niyar sauraron ta don littafi ya jawo inda ya bude da alama wani Abu yake nema hakan yasa ta fita ta aiki Laylerh ta siyo kayan miya..

Amina Nada shekara 15 malam Musa ya Aure ta suka zo Maiduguri,tana da shekara 19 kuma ta haifi Muhammad wannan dalilin yasa yaran da suke haya a gidan su raina ta don first born na gidan ma ta girme ta,Kai har shi Abdul-maleek d'in ma ya girme ta shiyasa suke mata rashin kunya iya son ransu don ganin ta yarinya kuma suna jin haushin zaman gidan su da suke yi duk da suna biyan haya sannan ba wani kula su har can take yi ba in kaji ta musu magana to sun sheganta Mata yara ne.. Asma'u ita ce first born na Mai gidan kuma ita kadai ce mace a wajen mahaifiyar su inda tayi Aure amma ta kan zo taci mutuncin Amina duk Randa taso da kuma lokacin da taso shiyasa yanzu Amina ta koma zaman hak'uri don ko ta fadawa malam baya wani Daukan mataki kuma ya gargade ta da kada ta kuskura ta fadawa mahaifin yaran duk da ba zama yake yi ba.

Yanzu Muhammad Nada shekara 15 Laylerh Nada shekara 12 tsangomi iri-iri mahaifiyar su ke sha tsam bata jin d'ad'in gidan amma hak'uri take Gashi Allah ya zuba ma yaran ta tsoron yaran gidan ba na wasa ba kace su ne uban su.

Da yake Laylerh yarinyar tana da ladabi da biyayya ga shiga rai, ko sau dubu zaka aike ta in taje sai ta gaishe da mai shagon hakan yasa kowa sanin tana da son gaisuwa yanzu ma hakan ce ta kasance Gaisar da mai anguwa da kuma cabinet nashi tayi sai ta shige cikin gidan tana rike da kud'in gam a hannun ta,Bayan ta

gaida matar sa sai ta fad'i aikan da aka mata nan ko aka bata sai ta fice da gudu sai gida..

Da gudu ta shigo tana haki har zufa take had'a Wa,yarinya ce Fara sal sai dai Hasken ta Nada duhu kadan hancin ne dai babu sosai, son kowa kin Wanda ya rasa idanun ta manya-manya su ta ware tana fad'in,

"Aunty naji mai anguwa yace za'a kawo farmaki cikin garin nan Wai yan boko haram sun turo sammanci".

" Dallah bana son shiriritar Ku na yara".

Mahaifin ta ya katse ta

"Allah da gaske nake Abbu ko mai anguwan ka tambaya a majalisar kofar gidan shi naji Ana fada".

Ta fada tana Mai rike naman wuyar ta daidai makogoro alamar rantsuwa

" ba nace ban son karya ba".

Nyamutsa fuska tayi kamar zata yi kuka don tabbas taji shi ya fad'a mahaifin ta kuma yace karya ne..

"Amina zanje naji ko gaskiya ne tunda Kinga duk kauyukan da yake kusa da mu an far musu,in gaskiya ne sai mu shirya abubuwan da zamu bukata mu bar kauyen nan Da yake ba'a cikin Biu suke ba a kauyen Biu suke Daga haka ya fita sai kuma ya tarar da maganar Laylerh gaskiya ce da wuri ya dawo gida yace

" Amina ki had'a mana kayan mu ya zama cikin shiri muke ko da yaushe zamu iya tafiya ".

" to malam".

Ana cikin haka Washe gari sai ga Sani yazo Wanda akayi masa baiko da Laylerh,saboda Tun tana yarinya ya kama kasancewar sa d'an bappan ta ne, Yaron irin masu Karyan arziki ne don 'Dan kasuwa ne saya da sayarwan motoci yake hakan yasa duk Randa zai zo kauyen da mota daban daban yake zuwa kuma Tun wajen shiga garin zai yi chanjin kud'i naira hamsin hamsin ya ringa rabawa manya, yara kuma ishirin-ishirin Yana isowa garin zai Fara raba kud'i a cikin garin duk da bai San nawa yake cirewa ba amma yana kiyastawa..Kan ya Isa gidan su Laylerh labari ya Isa gidan su cewa yazo yau d'in ma hakan ce ta kasance..

Zata fita kenan suka ci karo da shi nan ya rike ta yana fad'in,

"Amarya ta ina zuwa?"

Kwace hannun ta tayi abun ka da yaranta tace,

"Ka sake ni na tafi wasa".

Sake ta yayi gami da bin ta da kallo don ya San duk Randa aka ce ya sami Laylerh ya warke..

Shiga ciki yayi da sallama nan Aunty'n ta tace,

" Marhaban lale-lale".

Gami da basa wajen zama aka kawo masa shayi da yake yana so saboda Aunty'n ta ta iya had'a tea sosai don sun yi amanna da tea a gidan Ba kunya ya sha da yake shi na gida ne sai yace,

"Yanzu naci karo da Laylerh zata wasa".

" wannan yarinyar da wasa,kwanan nan duk wasa Tasa a gaba".

Cikin kula yace,

"Makaranta fa?"

"Tana zuwa amma tana wasa don na 20 tazo".

" hmmm Ai gwara ta maida hankali a kan karatun don shine zai amfane ta".

A haka suka yi ta hira mai dad'i sannan ya cire 3k ya bayar Wai a saya ma Laylerh kaya Aunty'n ta kuma 1k ya bata kyauta..Ya tashi zai fita kenan sai ga Abdul maleek inda suka gaisa Sani kuma ya sallami Aunty sannan ya fita Abdul-maleek na raka shi da yake d'an karya ne duk kud'in sa sun Kare sai bai bama Abdul -maleek komai ba..Abdul-maleek na dawa gida yace,

"An bi an mallake shi,da da yake zuwa kullum sai ya bamu wani Abu amma tunda aka basa Laylerh ya daina bamu komai".

Aunty dai cewa tayi duk zai wuce tunda yanzu take da shekara 29 Ai dole ma su raina ta..D'aki ta shige abun ta..

**

Suna cikin bacci da daddare suka Fara jin karar bindiga cikin Tashin hankali kowa ya tashi sai bullet da yake bin ta jikin ginin d'aki ya wuce A Daren iya Tashin hankali sun shiga ga Laylerh da su Muhammad sai kuka suke kamar ransu zai fita..Gaba d'aya kauyen ihu ne kadai zaka rinka ji nan suka fito tsakar gida kowa ihu kamar ran su zai fita Su Abdul-maleek zasu fita Abbu ya Hana su sai Abdurazak ne yaki jin magana ya fice Abbu na,

Da yake dama boko haram sammanci suke turawa ko wani kauye ko garin da zasu shiga in kuna son ran Ku zaku bar garin in ko kun zauna kun musu taurin Kai shiyasa dole su shigo garin domin gamawa da Ku sannan basu shigowa sai tsakiyar dare ko kuma da asuba lokacin kowa Na bacci..

" ka dawo Abdurazak komai zai iya faruwa".

Ina ya Riga da ya fice da yake ya San ba uban shi bane ke mishi magana nan yace da Abdul-maleek da su shiga ceiling nan ya yaga ceiling ya shigar da su gami da rufewa sannan yace,

"Amina in sunzo Kice gidan ba maza nima Zan shiga ceiling amma ta bandaki".

" to"

Tace shima ya wuce ya shiga sai ta koma d'aki tana Neman yaran ta amma shiru bata gansu ba nan ta shiga Tashin hankali sai can ta lek'a kasan gado ta gansu tare da Laylerh sai zare ido suke yi Muhammad ta fitar gami da sa Mi shi kayan mata tunda uban su ya buya amma bai tuna da Muhammad d'in ba sai kace ba d'an sa ba ko kuma ba namji ba.

"Aunty zasu kashe mu?"

"A'ah Laylerh ba abunda zai same Ku".

" Aunty to kizo mu buya mana tunda Abbu ma ya buya".

Yake tayi wanda yafi kuka ciwo gami da cewa,

"Laylerh ki zauna a kasan gado ko anzo kar Ki fita kin ji".

" to Aunty ke ma zaki je ki buya ko?"

"A'ah sallah Zan yi".

Daga haka tayi alwala tana ta jin karar kashe-kashe ta tada sallah a zaune domin mika lamuran ta zuwa ga Allah saboda ita yanzu ba ta rayuwar ta take yi ba,rayuwar yaran ta ne ya dame ta..Tana cikin sallah sai taji Harbin yayi yawa sosai da alama kuma akwai Harbin soldiers saboda Wanda suka far ma garin da AK47 suke amfani soldiers kuma ba shi bane Jin tabbas akwai karar bindigan soldiers sai hankalin ta ya Dan kwanta sai kawai taji Ana buga k'ofar gidan kamar za'a 'balla nan ko jikin ta ya hau rawa idon ta na hawaye don ta San yau kam kashe su za'a yi yaran ta kawai take tausayawa Kamar daga sama sai taji mutum ya shigo gidan ta gini,a wannan lokacin da zaka tsaga jikin ta ba zaka samu jini ko kadan ba nan ta ringa jero addu'o'i sai kuma taji Ana numfashi sama-sama gami da kiran malam Musa..

" tabbas wannan muryar Abdurazak ne ".

Da wuri ta mik'e ta fita sai ganin sa tayi kwance a kasa jini na zuba daga jikin sa don an harbe sa a goshi..K'ok'arin tsaida jinin tayi cikin Tashin hankali amma ta gagara nan ta wuce toilet ta Fara buga ceiling tana fad'in,

" malam ka fito Abdurazak yaji ciwo sosai".

Shiru yayi don a jin sa sune suka shigo gidan sannan suka ce tace da shi ya fito Bugawa ta ringa yi amma ya mata banza nan ta wuce inda su Abdul-maleek suke tace su fito Abdurazak ba lafiya Suma sun dau lokaci kan suka fito nan suka Gan shi kwance rai a hannun Allah sai suka Kira Abbu..

"Wallahi in d'an uwa na ya mutu sai na kashe ki,kila ma ke Kika masa wannan illa muguwa kawai".

" Haba Abdul-maleek Tun yaushe nake kiran Ku amma kuka ki fitowa ".

" makaryaciya me yasa ba za ki Kira mijin ki ba".

"Shima na Kira sa amma yaki zuwa".

Shi kuma Abbu akan yace ta Kira sa sai yayi shiru nan Abdul-azeez ya d'auka

" Ai ba sai kinyi haka zamu San cewa kina son kashe mu ba".

Laylerh dai tana kasan gado sai zare ido take kuma sarai tana jin me ake cewa amma kuma shekarun ta yayi kadan ta fahimci abun gwara ma muhammad don haka sai bata fita ba kamar yadda Aunty'n su tace kada su fita, Suna cikin Cece Kuce rai yayi halin sa nan kowa ya Fara kuka inda Aunty'n kuma salati kawai take Duk da basu ta'ba d'aukar ta da daraja ba amma taji mutuwar matuka har ranta don zaman yau da gobe yafi k'arfin wasa..

Abbu a wurin ya durkushe yana girgiza Abdurazak yana kuka haka ma sauran yan uwan shi..Wanda suka Kai ma garin farmaki kuma sojoji sunyi nasaran watsar dasu gaba d'aya..

A Washe garin aka tsinci gawaki dayawa nan ko gidan su Laylerh zaman makoki a ke a ranar kuma Baban su abdul maleek din ya dawo don shi Kama kifi yake da kuma noma. ..

Sani na jin labarin ya d'auki matar sa suka nufo kauyen domin gaisuwa A k'ofar gida yayi ma kowa ta'aziya inda matar sa kuma ta shige ciki nan Aunty ta bata tabarma amma sai ta'be baki tayi tace,

"Tabarmar tana warin fitsarin Laylerh".

Gwaggonen su Abdul maleek da suke wurin sai murmushi suka yi..

Laylerh ce ta shigo gidan jikin ta duk Dotti amma da yake Fara ce ba zaka ga dottin sosai ba wuyan himar nata a juye yadda yara ke sawa da yake anyi rasuwa a gidan Aunty'n ta bata ce tayi wanka ba ko kuma ta mata,durkusawa tayi a gaban matar sani tace,

" ina wuni".

Don ita dabi'ar ta ce gaisuwa saboda bata ma San wacece bane Hararar ta matar sani tayi don ta tabbata duk Randa Laylerh ta girma ba k'aramin kyau zata yi ba hanci ne kadai bata da shi.

A dai-dai lokacin Sani ya shigo domin gaida 'yan cikin gidan bayan yayi ma Aunty da gwaggonin su Abdul maleek ta'aziya sannan ya Dan zauna a gefe nan Laylerh ta nufe sa tace,

"Ina wuni".

" lafiya ".

Yace gami da shafa kan ta sai ya fitar da Bond d'in naira hamsin ya mika ma gwaggonin su Abdul maleek Aunty kuma Bond d'in naira ishirin Abunka da kauyawa ganin yayi yawa basu San duka-duka kud'in naira dubu biyu bane sai gani suke kamar nata yafi yawa..

Matar sa kuma ganin kyauta da yake tayi tunda suka shigo kauyen ba k'aramin tayar mata da hankali yayi ba Gashi yazo ya bama Aunty don ita baya mata tunda karyar arziki ne da shi Tafiya suka yi nan gwaggonin su Abdul maleek suka Fara magana,

" ya za'a yi a bamu kud'i kadan ke kuma dayawa gaba d'aya kin mallake yaro".

Ita dai ganin gidan mutuwa ce sai bata ce komai ba Amma tana mamakin karfin hali irin nasu sai kace Sani d'an uwan su ne Ana cikin haka sai ga Abdul-maleek ya shigo nan yace,

"Ai wannan ba yau ya Fara faruwa ba kuma Wallahi Ana gama zaman makoki sai ta bar gidan nan".

" ke ba uwar Wanda ya mutu ba an kama an baki kud'i ".

Haka suka ringa zagin ta mahaifin su Abdul maleek na shigowa ta d'auki kud'in ta ba shi sai cewa suka yi,

" gwara kam tunda shine uban Yaron ko cefene zai yi da shi".

Ita dai bata ce da su komai ba sai d'aki da ta shige da ace bata haihu bane sai ya dame ta..

Ana gama zaman makoki Abdul-maleek yace sai ta bar gidan nan ko 'yan uwa suka sa baki kan cewa bai dace ba saboda ko ba komai ta mijin ta Nada kirki kuma yaran ta kanana ne tSam yaki yarda sanda kawun sa yasa baki sannan ya hakura gami da cewa,

"Tunda Abba ya zabe ta akai na to ni Zan bar gidan"..

Haka ko akayi ya bar gidan..

Matar Sani ko ganin an gama zama sai tazo har gidan domin ja ma Aunty kunne Wajen zama aka bata sai tace,

" ba zama nazo yi ba,Wallahi ki tabbata 'Yar ki bata auri Sani ba in ta girma don na lahira sai ya fita jin dad'i ".

" Ai ni da zaki ce ma Sani ya fasa auren ta da na huta".

Jin haka sai ya d'an sanyaya zuciyar ta Sannan ta tafi..

Aunty ko tausayin rayuwar 'Yar ta take don har ga Allah ba son auren take ba kawai dai ba yadda ta iya ne,in ba haka ba me Laylerh zata yi da yaro d'an karya irin sani sannan baya ta'ba kyauta da ya wuce dubu biyu in ba Laylerh d'in yayi ma ba..

Abdul-maleek na barin gidan su kauyen da ke gefen nasu ya nufa ba tare da sanin shine next target na mutanin ba tunda soldiers sun yi nasara akan su a can, Cikin rashin sa'a aka kashe sa nan aka kawo ma Abban shi gawar sa ranar har hawan jini sanda yayi cuxx yana asibiti aka yi sadakan uku....

**

Zaune suke duk a tsakar gida Laylerh ta shigo da gudu tana fad'in,

"Aunty Kinga result na,nazo na d'aya a islamiyya".

" Haba mama na zo na gani".

Cewar mahaifin ta.

Nan ta zauna a cinyar sa tana nuna masa sai ya karba ya gani..

"Ina alfahari da ke Laylerh".

Ita dai murmushi kawai tayi sai Aunty ne tace,

" Ai alhamdulillah Laylerh akwai kokari ba irin Muhammad ba".

"Fad'i duk abunda kike so Zan saya miki".

" Abbu kayan wasa nake so irin na yaran alhaji shamsu".

"To in sha Allah Zan saya miki,yauwa Amina na manta ban fad'a miki ba kanina na Gombe ya mini kyautan gida saboda Tashin hankali da ake a garin nan, yace bai kamata naci gaba da zama a nan ba".

" Masha Allah Abu yayi kyau, Amma malam ya kamata ko sau d'aya ne muje wajen su tunda ya koma gombe fa bai zo ba".

"Haka ne kam Amma Ai bai dace nake bin sa ba kasancewa Na babba tunda shi bai turo iyalan sa ba".

" Abbu zanje wajen sa".

Cewar Laylerh.

"In sha Allah duk zamu je".

" yanzu malam yaushe ne zamu kaura?"

"Ehh to Kinga yanzu mai gari ya tafi umra jiya mu Bari sai ya dawo don sallah a wajen da baka Saba ba ba d'ad'i".

" Ehh Abbu mu ma bamu son muyi sallah a inda bamu San su ba".

Suna zaune sai ga Asma'u ta shigo da kuka ga kuma akwati a hannun ta sai Aunty tace,

"Innalillah Waye kuma ya rasu?"

"Ba rasuwa bane Amadu ne ya sake ni".

" ya sake ki?me Kika masa?"

"Dama Tun ran sadakan ukun Abdul-maleek Hajja'n Niger da tazo sai taji Surkuwa ta tana cewa,

" Wallahi gwara ki tattara ki koma gida don ni ba Zan iya kula da yaran ki ba".

Da ta fad'i haka sai nayi banza da ita, hajja Niger kuma da taji sai tace zata bani maganin mallakar miji Harda uwar sa,shine ta bani naje Zan sa a abinci sai Maamar sa ta ganni tace Wai asiri ne shine Tasa ya dake ni kuma ya sake ni".

"Yanzu Asma'u me amfanin abunda Kika yi?"

Cewar Abbu.

Shiru tayi

Tsaki yaja gami da sauke Laylerh a cinyar sa ya fita waje domin kiran Abban ta a waya ya sanar mishi ita kuma sai kuka take nan Aunty ta ringa rarrashin ta sannan tace,

"Laylerh d'auko mata ruwa ta sha".

To Aunty tace gami da mik'ewa ta debo ta durkusa ta Ajiye mata.

" to yanzu kuma ke da Muhammad Ku d'auki akwatin ta Ku kai d'akin marigayi,dama Abdul-maleek da Abdurazak, d'akin su d'aya tunda yanzu sun mutu sai ta zauna a ciki don bai kamata ta zauna a d'akin su Laylerh ba don yara ne.

"To Ku Kai mata kayan d'aki, ke kuma je ki huta".

To kawai tace gami da mik'ewa da alama saki ya sata yin hankali😁....

Yana kaiwa wannar gabar sai yaja dogon numfashi tare da yin shiru ya kurawa waje daya ido,dafa hannun shi Abokin shi yayi yana fadin

" uhum ina sauraron ka Haruna".

"Zan cigaba da baka labarin amma Shin me Ka fahimta a kadan daga cikin labarin ta da Na baka".

" to a gaskiya ban wani fahimta sosai ba Amma da alama akwai magauta kewaye da ita".

"Da kyau yanzu Wa kake ganin yake da hannu a shigar ta duniya?" Yayi tambayar yana kafe Abokin nasa da ido.

"To kasan dai shi zato zunubi ne Amma mutum Na farko da Na Fara zargi yayar Maman ta ce sai kuma ita matar Sani don suna da dalilin da zai sa su badda ta".

" Shikenan su biyun kake zargi cikin dukka mutanin da Na lissafo?"cike da kwarin gwiwa yace

"Eh".Numfashi ya ja sannan ya cigaba da bashi labarin....

Readers Ku kuma Wa kuke zargi??

nasan duk kuma kun matsu kuji Asalin Laylerh, ba komai lokaci yazo da zaku San wace ce LAYLERH but before then comment pls

yanzu Na koma posting da asuba😁don Na Lura lokacin ne ntwrk Na yake nan guarantee

Comments

Share

©Hafciey Musa[1/25, 5:36 AM] Hafciey Musa😘: *□LAYLERH□*

(The prettiest emerald)

Alhamdulillah, Masha Allah naga comments naku Na kuma gode sosai..wasu Na cewa matar Sani ce wasu ko wasu ko Asma'u Hadeeza Kai wasu ma har shi Sanin da kan shi suke zargi😁but masu zargin matar sani sun fi yawa anyways za dai muji wane ne silar shigar ta duniya

LAYLERH fan's 1,2,3 godiya Mai tarin yawa da rashin comment□

"Oyoyo Daddy"

Zama yayi gami da ajiye manya-manyan ledoji da ya dawo dasu daga tafiya, nan matar sa ta fito gami da bashi ruwa ya sha."Sannu da dawa".tace da shi idanun ta nakan ledojin da ya shigo dasu

"Yauwa na same Ku lafiya?"

"Lafiya kalau".

" Daddy ka saya mana kayan sallah? "Dan shi ya tambaya

"Ehh Ahmad Gashi nan ma".

Nan ya Fara zazzage ledojin kaya ne na gani na fad'a, gown's guda uku ya saya ma 'Yar sa sai atampa guda biyu ya Mikawa matar sa yana fad'in,

" wannan sai a Kai ma Suwaiba dinki".

"Masha Allah Abu yayi kyau Allah Kara bud'i".

Ameen yace gami da,bayar da na Ahmad sai kuma taga ledoji a can sai tace,

" wancan fa?"

Zare kayan yayi yana nuna mata,gown's ne na yara masu kyau guda biyar".

"Abban Ahmad Ai yayi ma Maryam girma".

" ba nata bane,baga can nata na bayar ba".

"To wannan fa?"ta tambaya zuciyar ta Na bugawa ta kuma kosa taji Na wacece

"Na Laylerh ne,d'aya ledan kuma na saya ma Muhammad ne".

" wallahi baka Isa ba,yarinyar da ko irgen dangi yanzu ne ta fara zaka tsaya bauta mata sai ta girma ka gama wahala a bawa wani".cikin jin zafin furucin ta yace

"Laylerh mata tace ba na wani ba kuma duk Wanda yayi kokarin rabarta Zan San yadda zanyi da shi".

" to ni kuma ina nawa kayan sallah'n?"

Cire 5k yayi ya bata nan ta Fara masifa

"Wallahi ba Zan yarda ba,yau dole ka zabi tsakani na da Laylerh yarinya Tun bata shigo ba ka Fara wulakanta ni waya San me kake fada Mata a kaina ni dai wallahi Allah ya Isa tsakani Na da Laylerh".

" na zabi Laylerh".ya fadi yana kallon ta har cikin ido da ta

" haka kace ko?"tayi tambayar idanun ta Na Tara ruwa

"Ehh na fad'a".

Nan ta shige d'aki ta tattara kayan ta tana fad'in,

" wallahi gidan mu Zan tafi".

"To dama kafar ki na rike ne?"

Nan taja akwatin ta ta fice sai gidan su..Tana zuwa ta musu bayanin abunda ke faruwa nan Baban ta ya Kira sa ba mutsu yazo..

"Sani Kai ka tura Sa'adatu gida?"

"A'ah ita tace zata tafi".

" akan me?"

"Wai sai na fasa auren da nake shirin yi".

" Baba kaya fa ya sayawa yarinyar nan masu kyau da tsada ni kuma Wai dubu biyar ya bani na sai kaya".

"Haba sani Tun baka Aure ta ba ka Fara rashin adalci a tsakanin su,to lallai Sa'adatu ba zata koma gidan ka ba har sai ka janye maganar auren nan".

" gaskiya ba Zan iya ba".

Ya fad'a yana mai sa takalmin sa ya fice..

A Washe garin ya D'ebi yaran sa sai gidan Maman sa tana ganin su tace,

"Sani lafiya kuwa?"

"Lafiya mama kawai iyayen Sa'adatu ne Wai in ban janye maganar auren Laylerh ba ba za ta dawo ba".

" kada Allah yasa ta dawo,Yar uwar ka dai sai ka aura ita kanta Sa'adatu tasan Laylerh ta fita nesa ba kusa ba".

"Ki rabu da su mama,yanzu dai ga su Ahmad na kawo".

" ba komai zasu zauna har sai sanda ta dawo ".

" to Mama Bari na fita".

"A dawo lafiya".

Nan ya fita zuwa wajen aiki,yana Isa abokin Baban sa ya Kira sa a waya yace ya same sa a gida nan take ya wuce sai ya masa albishir da cewa ya sama mishi aikin gwamnati da yake nema Sosai yaji farin ciki gami da masa godiya sannan ya fita..Fitar sa da kiran Mamar sa a waya duk d'aya ne nan ya shaida mata ya samu aiki..

" alhamdulillah, kaga daga rabuwa da ita ka samu aiki da alama Laylerh ba mai farar kafa bace Aure ba fashi".

"Haka ne mama sai anjima".

" mu jima dayawa".

***

Aunty ce zaune tana aiki a kitchen Asma'u ta fito da alama kullum kuka take..

"Sannu da aiki".

Cike da mamaki Aunty ta kalle ta sai tace,

" kin fito kenan".

"Ehh wallahi".

Ta fad'a tana kallon wajen wanke-wanke, don tunda ta dawo gida tana d'aki sai dai a dafa abinci a bama Laylerh ta Kai mata ko kuma Muhammad ya shiga wajen ta..Wajen wanke wanken ta nufa sai Aunty tace,

" me zaki yi?"

"Zan wanke su ne".

" A'ah ki Bari aikin Laylerh ne don basu da yawa".

Bata ce komai ba ta d'ebo ruwa a Randa sannan ta dauko kujera ta zauna ta hau wanke-wanke Aunty kam baki ta wangale Tana gamawa ta d'ebi shayi don su ko k'arfe nawa ne zasu sha shayi..

"Asma'u ki cire komai a ranki in sha Allah hakan alkhairi ce".

" don Allah kiyi hak'uri, Tun farko sanda Kika ce mini kada na kar'ba amma na biyewa son Zuciya Gashi yanzu abunda na jawa kaina,nasan ko na koma gidan can ba mai yarda da ni shiyasa ba Zan koma ba ma".

"Kada Kice haka Asma'u Ai yanzu kowa zaman hak'uri yake, yaran ki kuma Wa zaki bar Wa".

" Ai gidan uban su ne yayi duk yadda yaso da su in yaga dama ya dafa su ya cinye ni dai ki yafe mini".

"Ba komai duk ya wuce kuma na godewa Allah da Kika gane hakan Tun lokaci bai kure ba,ni dai abunda zance shine ki sake tunanin batun komawan ki gida".

Laylerh ce ta shigo da gudu abunka da yarinta kullum cikin gudu bata tsaya ko ina ba sai cikin bandaki Wanka tayi ta fito amma tsam jikin ta bai fita ba nan ta shige d'aki can sai Gata ta fito..

Fuskar ta ta labtawa powder'n da Sani ya ta'ba kawo mata ga Jan baki da Tasa kamar zai yi magana kuma powder'n yayi yawa a fuskar ta sai kayan da ta Saka..

" Laylerh yau kuma kece Kika yi wanka ba Wanda ya saki?"Asma'u ta tambaye ta

"Adda akwai inda Zan je ne".

Nan kawar ta Nana ta shigo ita ma tayi wankan Gaishe da su Aunty Nana tayi sannan ta kalli Laylerh tace,

" mu tafi".

A kunnen ta Laylerh ta rad'a mata,

"Ki jira ni a waje in ba haka ba Aunty na zata hanani".

Da gudu Nana ta fita tana fad'in,

" Aunty sai anjima ".

Kai kawai Aunty ta girgiza sai ga Laylerh kam ta deba gudu Aunty na kiran ta amma taki dawa..

" Wai ina zasu je ne?"

"Ai tunda Kika ga Laylerh tayi wanka da kanta to kila biki ake a anguwan nan".

" Laylerh dai akwai son biki".

"Ki Bari kawai yaranta na damun ta".

Suna gama magana sai Gata ta shigo gida tana lek'e sai Aunty tace,

" ki gama leken ki zaki zo ki same ni tunda kince baki ji".

Shiga tayi gami da Neman waje ta zauna fuskar ta ba walwala tsam sai Aunty tace,

"Ina yanzu Kika gama guduwa don kar ki tayani aiki shine har kin dawo".

" Aunty dama biki zamu je 'yan uwan su Nana ne shine ina fita naga wani kullum sai yace nazo".

"Kizo kuma?"

"Ehh".

Aunty dai bata ce komai ba don tasan tabbas akwai abunda ta mishi ne sai tace,

" tunda Allah ya dawo da ke d'auki books naki ki tafi lesson tunda kunyi hutu a islamiyya".

Dole ta shiga d'aki gami da d'aukar books tana fad'in,

"Aunty na tafi".

" a dawo lafiya ".

Tana fita duk Wanda ta gani sai ta gaishe sa a haka har ta Isa gidan su Basheer Wanda yake Mata lesson.

Bayan ta gaishe da 'yan gidan sai ta gaishe shi nan suka Fara lesson amma da suka yi nisa duk sai ya shagala wajen kallon ta Duk da cewa ita yarinya ce amma kuma kowa ya ganta sai yaji yana son ta ba Wai kuma don kyau bane a'a dayawa sun fita kyau a kauyen nasu ita dai jini ne Allah ya bata..Ganin kallon ya mata yawa sai ta tura baki tace,

" ni kam ka Kara mini karatun na".

Bai ma San tana yi ba sai kallon ta yake sai tace,

"Ni na tafi gida kuma Wallahi sai na fadama Aunty sai kallo na kake".

Gida ta wuce Aunty na ganin ta tace,

" me Kika yi ya Kore ki?"

"Babu sai kallo na yake".

" ban yarda ba".

Aunty ta fad'a sannan ta d'auki hijab tana fad'in,

"Asma'u Lura mini da girki kada ya kone Bari naje".

" to".

Daga nan suka fice sai gidan su Basheer suna Isa suka gaisa sai tace,

"Bashir wani laifi Laylerh ta maka ka Kora ta gida".

" babu Aunty Zan zo gida muyi magana ".

" me zai Hana mu yi yanzu?"

"A'ah kije gida Zan zo".

Tafiya suka yi a ranta tana tunanin me kuma Bashir zai ce don ta San halin 'Yar nata ba tsokana take yi ba amma ko ma menene in yazo Ai zata ji.A hanyar su ta komawa Laylerh ta rike yatsun Aunty'n ta biyu sai tsalle take yi a yayinda suke

tafiya..tabbas Aunty'n ta na sonta kasancewar ta mace Yar fari kuma auta tsam bata kunyar ta saboda in bata ja yaranta a jiki ba Wa zai ja su.suna cikin tafiyar Laylerh taga Wanda yake yawan kiran ta sai ta gudu ta buya a Bayan Aunty'n ta tana cewa,

" Aunty Wanda yake cikin motar can ne yake Kira na Wai nazo na karbi sweet ni kuma sai na gudu".

Ta karishe maganar tana Mai nuna shi da 'yar yatsa.

Inda ta nuna Aunty'n ta tabi da ido sai ta kalle sa,Yaron uban sa mai kud'i ne sosai amma a cikin gari suke..

"Duk Randa ya Kira ki in Kika je dai yanka wuyan ki zai yi don mai yankan Kai ne".

Zare manyan idanun ta tayi gami da rike fuska tana bude baki tace,

" Aunty zai yanka ni?"

Cikin gaskiya da gaskiya Aunty'n ta tace,

"Ehh in Kika shiga motar sa ba".

Ta fada tana Mai Jan hannun Laylerh suka cigaba da tafiya Rungume kafafun Aunty tayi tana fad'in,

" Wallahi ba Zan je ba ".

" yauwa 'Yar albarka ".

Aunty ta fad'a mata haka ne don Tasa mata tsoron maza kada ta sake da su..duk inda suka wace sai an ce Aunty'n Laylerh an wuni lfy tsam ba zaka ce Muhammad Dan ta bane don laylerh ta kwace sunan shi,ba zaka taba jin ance Aunty'n Muhammad ba sai dai Aunty'n Laylerh... Suna Isa gida Bayan ta d'an huta sai Aunty tace,

" gaskiya Laylerh zaman ki a gida ba fa'ida koma wajen Bashir kawai tunda yace ba abunda Kika masa".

To tace gami da fita,Ai fitar ta ke da wuya wannan mutumin yace tazo abunka da yaranta sai ta Fara ihu,

"Wayyo mai yankan Kai jama'a kuzo Ku Cece ni".

Nan take aka fito kowa da abunda yake rike da shi a hannun sa Ana fad'in

" ina yake? "

"Gashi can a mota".

Sai an Isa wajen motar sai aga d'an alhaji Habibu ne haka ta tara masa jama'a da ihu sai aka ce,

" yanka ki yace zai yi ne?"

"A'ah Aunty nane tace mini shi d'an yankan Kai ne kuma in na shiga motar sa sai ya yanka ni".

Kallon juna mutanin wajen suka Fara don sun fahimci tsoratar da ita ake sai Mansur d'a ga Alhaji Habibu yace,

" Wallahi koma wace ce Aunty'n naki yau sai na kulle ta,har ni zata duba tace d'an yankan Kai".

Ransa in yayi dubu ya baci,yarinya karama taci zarafin sa a gaban jama'a lallai yau kauyen ba zaman lafiya don duk sai ya kulle 'yan gidan su".

Hak'uri aka soma bashi amma tsam yaki hakura can sai ga mahaifin ta nan aka fad'a masa abunda ke tafiya nan yayi ta bada hak'uri da kyar mansur ya tafi .

Suna shiga gida yace,

"Laylerh me yasa Kika yi haka?"

"Abbu asirin sa nake son tonawa".

Nan ya shiga yi ma Aunty'n ta holo akan me yasa zata fada mata haka Gashi saura kadan yau ta jefa su a matsala bai yafe ta sake sa mata irin tsoratarwa nan ba,ya yarda yana da kyau a tsoratar da ita don maza ba abun yarda bane amma kada ta yi mata da mutum Hak'uri ta ringa basa ita da Asma'u Laylerh kuma sai zare ido take ita ta kasa fahimtar abunda suke ma..

Mansur ne yayi parking motar sa gami da shiga cikin gida rai a bace a falo ya tarar da alhaji Habibu..

" son lafiya na Gan ka cikin Tashin hankali? "

"Dad the whole me Wata yarinya ta Tara mini jama'a Wai ni d'an yankan Kai ne kadan ya Hana su kashe ni".

" what?"

Alhaji Habibu ya tambaya yana mik'ewa sannan yace,

"A cikin kauyen can har akwai Wanda ya Isa ya Tara maka jama'a,to kwantar da hankalin ka yau d'in nan Zan sa a kawo mini yarinyar ita da uban ta har gidan nan na kulle su".

Juice ya d'auka gami da sipping don ya San tabbas Dad nasa zai daukar masa fansa..

Turawa yayi aje a kamo malam Musa da Laylerh..

**

Wuri yayi kyau iya kyau anyi decorating na ko ina da gani ba sai ka tambaya ba an kashe kud'i..

Mansur ne da friends nasa a falo suna hira hade da wasa da dariya don yawancin su ba yan garin bane wasu yan gombe ne wasu kuma kano wasu ko wani wajen na daban, Alhaji Habibu ma yana tare da abokanayen sa cuxx business tycoon ne shi Wanda lokaci guda ribar sa yayi multiplying na friends nasa..

Kasancewar yau birthday'n Mansur sai yayi inviting har da abokanayen hamaiyyar sa..Duk zaune suke a main falo sai hura hanci yake yana fad'a musu riban da yake samu Abokin hamayyar sa ya gama kuluwa sauran friends nasa ma duk haushin sa suke ji bai sani ba..Suna cikin haka aka Fara jin hayaniya sai yace a masa

connecting CCTV,nan aka yi connecting..Laylerh ne da mahaifin ta aka kama amma suna shiga first gate ta zare ido, Ana zuwa second gate ta Fara ihu tana kuka sai cewa take,

" wallahi gidan yankan Kai ne ba Zan shiga ba za'a yanka ni,nikam Abbu mu tafi wajen Aunty ".

Ba yadda mahaifin ta bai yi ba wajen ganin ya rufe mata baki amma abun ya gagara don sai an rike ta sai ta fisge jikin ta zata gudu a kamo ta..

Ganin haka sai yasa Alhaji Habibu fita da wuri enemy'n sa kuma sai ya rufa masa baya don wannan ne opportunity nasa cuxx sun dad'e suna zargin sa da hakan..Yana Isa wajen ya debe ta da Mari har sanda ta fad'i a kasa nan ran mahaifin ta ya baci don shi zai jure duk wani wulakancin da za'a masa amma akan yaran sa zai iya yin komai Shake Alhaji Habibu yayi niyar yi amma securities suka rike sa ita kuma sai kuka take tana fad'in,

" nikam Ku bar mu kada Ku yanka mu Ku sake mini Abbu na".

Durkusawa Alhaji Isa yayi wato enemy'n Alhaji Habibu, nan su Mansur da friends nasa suka fito..

D'aga Laylerh yayi gami da karka'be mata jiki sannan yace,

"Baki ji ciwo ba kam?"

"Ehh banji ba,don Allah kace su barni mu tafi gida kada a yanka mu".

Kun San shi yaro in ka fad'a masa Abu sau d'aya shikenan ya rike shiyasa Laylerh take ta cewa za'a yanka su..

" akwai Wanda ya ta'ba ce miki Ana yankan Kai a gidan nan ne?"

Kai ta girgiza.

"Kin ta'ba ganin an yanka wani a gidan nan?"

Kai ta kuma girgizawa sai tace,

"Amma na San Ana yankan Kai".

" Good kunji abunda tace kuma yaro baya karya so a bincike gidan".

"What rubbish cewar Alhaji Habibu".

" me yasa zaka tada hankalin ka tunda ka San karya take ka Bari a bincika kawai".

"Before a bincika Ai kuna da bukatar takardar search warrant".

" kada ka damu zamu nema".

Nan aka ajiye su Laylerh a gidan sauran yan birthday kuma suka watse aka bar masu kwalli a ido..

 cikin gari aka je domin Neman Wanda zai buga search warrant don ayi sueing nashi a court

Sanda aka je wani gari inda suka fara tun 5 na yamma sai 7:30na dare before aka dawo da search warrant aka ce ayi searching gidan.

Searching na gidan aka Fara lungu da sako amma ba'a ga komai ba Laylerh kam nata ido uban ta kuma ya San tabbas bala'i ta shigar da su..

Har bedrooms sanda aka duba Harda na matar sa nan aka dawo apartment na Maman sa don gidan apartment apartment ne sai aka bude Suna shiga bedroom d'in wani security ne a gaba nan aka ga ya burme aka neme sa aka rasa

Nan ne aka ce securities 2 su shiga, sai aka daure musu chain a jikin su suka shiga ramin Ana binsu da haske sai suka ga underground building suka Kara shiga cikin building d'in, sai suka ga kan securities d'in da ya burme a kasa jini na fita da sauri suka fito da gudu suka ce Ai Wanda ya fad'i yanzu sun ga kan shi a kasa nan ne aka ce Wa zai shiga amma kowa na tsoro sai suka ce wasu su shiga sannan aka had'a da shi kan shi alhaji habibu, ko magana Kayi sai kud'i yayi ta zuba a bakin Wanda ya mutun,sai skeleton kala-kala sai aka yi ta bincike aka ga kud'ad'e sai aka yi arresting nashi aka tafi da shi..

Yaron sa har gaban Laylerh yazo cikin tsananin bacin rai da tsanar ta ya nuna ta da yatsa yace sai ya kawo karshen su, saboda kidimewa da akayi ba Wanda ya kula da su..

Alhaji Isa dai ya San yarinyar is Lucky for him Nan yasa aka maida su kauyen su, cikin Daren Abbu sai masifa da holo yake ya kuma ce in sha Allah Ana sallah zasu bar garin su koma gombe...

***

Har ila yau idon boko haram Na kan su don yanzu dauki daya daya ake musu sosai hankalin mutani ya sake tashi Amma da an dauka sai ya Dade zasu sake daukewa..

Zuwa yanzu sosai gonar Abbu yayi kyau da shi da Abban su Asma'u don basu taba yin goma irin Na wannan lokacin ba..

Dama can boko haram basu fiya damun mutani ba sai lokacin harvesting Wato sanda abinci ya nuna nan zasu saku a gaba don Ku bar garin su ko su kwashe abincin.. Duk wani manomin da ya amsa sunan shi to dole fa duk shekara zai ke cire musu zakkar abunda ya noma to dai wannan shekarar har da su Abbu a ciki Abban su Asma'u dai ya bayar Abbu ne bai bayar ba sai basu ce da shi komai ba..

**

Aunty ce zaune a k'ofar d'akin ta ita da Asma'u suna hira sama-sama don ma gyaran zogalen miya suke sai ga Wata 'Yar gwaggon su ta shigo da kayan ta a Leda nan aka mata tarba mai kyau tare da bata shayi ta sha..

"Lafiya kuwa kuka shiga garin mu don ba'a ganin Ku a banza?"

Cewar Asma'u

"Kada Kice mini baki San abunda ke faruwa ba".

" kamar ya kenan?

"Aure muka kawo".

" alhamdulillah na zata wani Tashin hankali ne".

"A'ah auren 'Yar Hajjan Niger muka kawo".

" Allah sarki Ashe dai ta samu miji a nan Wa zata Aura? "

"Nifa mannin hauka ne bana so,ko da na Gan ki a gida ma na zata shi ya kawo ki gida".

" ban gane ba".

"Ai uban yaran ki ne mijin shiyasa ma nayi tunanin ko yaji Kika yi".

" me kike fad'i? "

"Wallahi amma dai ba'a d'aura auren ba Jere muka yi don lokacin rasuwar Abdul-maleek ne ya bata sadaki".

Ai nan take Asma'u ta mik'e don ta fahimci sharri aka had'a mata tunda Hajjan ce ta bata magani yanzu kuma ace 'Yar ta zata auri mijin ta..

Hijab ta d'auka tana fad'in wallahi gaban mai gari zanje a Kira shi naji dalilin da ya sa shi saki na.

" Asma'u ki tsaya mahaifin su Laylerh ya dawo kuma Ai Mai gari baya nan ya tafi umra".

"Ina! a Bari ya huce shi ke bada rabon wani batun Mai gari kuma Ai akwai Mai wakilta mishi in baya nan don haka na tafi".

" Adda Zan bi ki ".

" to zo mu tafi Laylerh ".

Da gudu ta tashi Nan suka fita basu tsaya ko ina ba sai gidan mai gari mataimakin shi suka samu nan ta fad'a masa abunda ke tafe da ita shi kuma ya sa aka masa kiran mijin ta..

" Asma'u maimaita abunda Kika ce ".

" Allah gafarta malam ina cikin zama na da miji na lafiya sai Wata 'Yar uwar mu tana Niger taga yadda Surkuwa ta ta mini sai tace kada na damu zata bani maganin mallakar miji kuma mamar sa ba zata ke tsangomata ba shine na kar'ba Zan yi amfani da shi kenan aka kama ni miji na ya sake ni yanzu kuma 'Yar ta miji na zai aura".

"To kaji abunda ta fad'a gaskiya ne?"

"Ehh ni dai na sake ta saboda abunda mahaifiya ta tace tayi,'Yar uwar ta kuma Mun fi shekara muna soyayya kuma auren ta nake son yi".

Kiran mahaifiyar sa aka yi mataimakin mai gari ya tambaye ta ya aka yi ta San cewa zata zuba Abu.

" Allah gafarta malam ina zaune aka Kira ni a waya aka ce Asma'u na shirin kashe mini yaro na sa ido a kan ta,abun ya d'aure mini kai don ban yarda Asma'u zata yi haka ba don tana da biyayya amma don na cire shakku a Kai sai na sa mata ido nan ko na gani shine na sanar da d'a na".

Numfashi yaja sannan yace,

"Lallai wannan abun an kulla sa ne,kuma tunda Aure saura kwana hudu na bawa mahaifiyar yarinyar kwana biyu tazo Maiduguri kuma har cikin kauyen nan in ba haka ba a fasa auren".

Gida suka koma inda suka mayar ma Aunty yadda suka yi sai tace,

" amma gaskiya matar nan bata yi adalci ba,ashe so take 'Yar ta ta shiga shiyasa tayi waje da ke".

"Ai ki barni da ita duk Randa muka yi ido biyu zata yi bayani".

A haka har kwana uku ya shude amma Hajjan Niger ta kasa zuwa sai mai anguwa yace an fasa auren ya mai da matar sa da yake shi mai fad'a a ji ne kuma a gaban sa mijin Asma'u ya tashi sai aka ce Asma'u zata koma gidan ta..

***

Laylerh ce kwance a cinyar Aunty'n ta tana mata kitso sai Asma'u da ke d'aki Laylerh tace,

" Aunty yanzu ya Abdul-maleek da ya mutu ba zamu sake ganin su ba?"

"Laylerh Ai in mutum ya mutu ba'a sake ganin sa".

" Aunty ko na girma nayi Babba kamar Adda Asma'u ba Zan sake ganin su ba".

"Ehh Mama na".

" har Abadan Abadan".

"Sosai ma".

" Aunty nima Zan mutu? "

"Ehh kowa ma zai mutu".

" Harda ke da ya Muhammad da Abbu?"

"Duk zamu mutu mama na".

" Aunty nikam bana son mutuwar nan".

"Mutuwa dole ce Laylerh amma in sha Allah ba zaki mutu ba sai kin girma kinyi Aure har ki haihu".

" Aunty in na girma Sani Zan aura? Don yana ce mini matar sa".

"A'ah in sha Allah ba zaki Aure sa ba,mijin ki a birni yake kuma mai kud'i".

" yehh miji na a birni yake kuma mai kud'i naji d'ad'i ".

" Kinga in Kika Aure sa mu ma Mun huta,amma in kina son d'an birni kuma mai kud'i sai kina da nitsuwa kamun Kai da kuma hak'uri".

" zanyi dukka in sha Allah "

" yauwa kuma ki ringa yin ibadah Allah zai taimake ki,sannan ki ke mana addu'a ni da yan uwan ki"..

"Aunty ko don na auri mai kud'i a birni zanyi,amma Aunty kashe ki za'a yi!"

"Ban sani ba don kowa da kalar Tasa mutuwar".

Murmushi kawai tayi don bata San inda ke mata ciwo ba sai cewa take zata auri d'an birni duk da bata San me auren bama..

" su Laylerh za'a auri d'an birni".

Cewar Asma'u.

"Ko dai bakin ciki kike yi ne?"Aunty ta tambaya cikin zolaya

"Na Isa na mata bakin ciki Aunty'n Laylerh, Ai auren Laylerh mune kirjin biki don Tun Aure na ba'a sake Aure a gidan nan ba fa".

Tana gama fad'ar haka sai ga Sani ya shigo can kasa-kasa Asma'u tace,

" ga d'an birnin Ku yazo ".

Ta fad'a tana dariya Aunty kuma ta had'a hannu alamar pleading kan cewa tayi shiru kada yaji..

Wajen zama aka basa da shayi sai suka gaisa da Aunty..

" Laylerh tashi ki tafi wasa".

"A'ah Aunty Ai wajen ta nazo kullum fa in nazo tana wajen wasa".

" to banda abun ka Sani me kuma zaka ce da Laylerh tunda yarinya ce".

"Laylerh na zo".

" nikam ba Laylerh'n ka bane,miji na d'an birni ne".

Zare ido Aunty tayi ganin Laylerh zata tona mata asiri da wuri tace,

"Je ki gidan su Nana kuyi wasa".

" A'ah tazo na gwada mata kayan da na saya mata Na sallah".

"Nifa nace maka miji na mai kud'i ne kuma a birni yake".

" Ai nima in kina so zamu koma birni da zama,zo na gwada miki".

"A'ah Sani ka Bari za'a gwada mata"

"Ai Laylerh kanwa tace Zan gwada mata".

" A'ah bai dace ba".

Nan Aunty ta gwada mata kayan da ya kawo gasu takalmi ribbons da kuma kayan kwalliya abun dai Masha Allah nan suka masa godiya don Harda na Muhammad..

"Me kuma ya kawo Asma'u gida?".

Sun d'an samu matsala ne da mijin ta amma zata koma in sha Allah..

Nan ya bata dubu biyu yace a Kara akan na shirye-shirye, Laylerh kuma dubu uku..

" Yauwa dama nazo na fada miki munyi magana da Abbu kan Laylerh Zan cire ta a makarantar da take Zan maida ta private a cikin Biu Zan sama Mata Mai machine da zai ke kaita ya dawo da ita".

"Shikenan in mahaifin ta ya yarda Ai ni bani da ta cewa".

" da farko yaki yarda don cewa yayi Zan daurawa kaina nauyi Bayan Na iyali Na shine nace mishi Na samu aiki sai ya yarda"

"To Shikenan Allah sanya alkhairi".

" Ameen gani nayi inda take din ba'a karatu sosai kuma in sha Allah daga nan makarantar Zan wuce Na saya form nayi duk abunda ya dace".

"Mun ko gode sosai"

Daga nan sallama ya musu ya tafi

Yana tafiya Aunty tace,

" wallahi Laylerh sai na yanka bakin ki,ba komai nace sai kin mayarwa mutani ba".

Da idon ta manya-manya take bin Aunty sai ta cigaba

"Wallahi ki sake Kiga abunda Zan miki".

Asma'u ce ta kar'ba

" Ai Laylerh in bata d'aure mu a gidan nan ba zata daure ki".

"Ki barni da ita tayi manya-manya idanun ta a wajen".

"Dakata Haruna".

" lafiya Ka tsaida ni Kai da Ka matsu kaji karshen labarin".

"Ehhh Amma akwai wasu abunda Na Dan fahimta ne".

" kamar me fa?"

"A yanzu ba iya Hadeeza da matar Sani nake zargi ba,Mansur Dan Alhaji Habibu Wanda yayi alwashin cewa sai yaga Bayan ta shima abun zargi ne sai kuma boko haram kaga kenan mutum hudu nake zargi". Murmushi Haruna yayi yace

" to lallai kam Ka kyauta Amma koma Waye ne zaka ji Bari ja cigaba da baka labarin".dukkan hankalin shi ya tattaro ya maida kan Haruna, shi ko nan ya cigaba da bashi labari..

Comment

Share

©Hafciey Musa

[1/25, 5:36 AM] Hafciey Musa😘: *LAYLERH*

(The prettiest emerald)

Felicitations

A journey of thousands miles begins with step,your finals steps calls for jubilations,it's obvious da efforts, sacrifices mades leads to your success.girlie you made us proud, congratulations now nd Alway,more blessings to your life and success.may Allah bless the knowledge acquired and the certificate.the sky is your starting point Mrs Naseer.more congratulations awaits you in future

Page 12

A Washe garin sani ya kammala Mata komai Na Fara zuwa makaranta kuma ba karamin kudi ya kashe ba, shi dai burin shi ace ehh yana da kudin shiyasa yake kashe Mata..ranar da aka kawo Mata uniform Asma'u ce ta goge Mata ita ma a ranar ta koma gidan mijin ta..

Laylerh gani take kamar gari ba zai Waye ba baccin ma ta gagara yi da kyau har Aunty Na Mata dariya da yake muhammad kam yana zuwa government skull kuma shi ma ya maida Hankali akan noma..

A Washe garin sani yazo daukar ta tsab ta fito students nan tayi Wa Anty ta tafi ita ko Allah bada sa'a ta Mata suna fita taga Harda lunch box ya saya Mata cikin zumudi tace,

"Wannan abincin nawa ne?"

"Eh mana Harda indomie Na saya miki a wajen Mai shayi Ince kina so".

" sosai ma Ai indomie akwai dadi".

suna isa makaranta Sani ya rike hannun Laylerh sai office na principal inda yara ko sai wucewa suke suna shiga classes nasu ita ko da ido take bin su...

Gabatar da Laylerh yayi sannan principal d'in ya Kira form mistress nasu yace ga sabuwar student a Kai ta class.

"Laylerh d'auki lunch box naki ki bi Aunt din ku".

D'auka tayi inda tabi bayan ta Sani kuma ya sallami principal ya tafi..

A saman class d'in taga an rubuta primary four nan ko suka shiga,gaba d'aya yaran mik'ewa suka yi suna gaishar da malamar su sai tace ga new comer an kawo musu.

" she is by name Laylerh Musa".

Abunka da skull kowa kallon ta yake Harda masu lek'a sandals nata.

"Laylerh a gaba zaki zauna ko baya?"

Ta tambaye ta da harshen turanci,da yake Laylerh na jin turanci kadqn-kadan Amma kuma in tayi magana da English kam akwai kurakurai don bullet's yafi yawa.

"A gaba Zan zauna don ko a skull namu a gaba nake zama".

Ta mayar mata da turanci duk da English d'in is not correct.

Dama class d'in kowa shi daya yake zama kuma na gaban duk sun cika sai taga Bayan akwai space nan Tasa yaran suka ringa komawa baya har aka iso gaba inda bench ya rage sai aka ce Laylerh ta zauna..

Locker ta bude tare da sa bag nata 'yan klass d'in ko sai kallon ta suke ita kuma gaba d'aya tana takure saboda bata Saba da environment d'in ba.

Malamar na gamawa ta fita sai Wata tazo wajen Laylerh ta mik'a mata hannun tana fad'in

" Assalamu alaikum ".

Da yake su a can Laylerh bata Saba da haka ba abun Ka da government skull,ba tare da ta bata hannu ba tace,

" Ina ce maza ke gaisuwa da hannu ".

" A'ah mata ma nayi kuma shine al'adar makarantar ".

Duk maganar nan da take mata da turanci suke don makarantar ba'a Hausa.

" sunana Fatima ".

" ni kuma Laylerh".

Kan su Kara magana teacher ya shigo nan shima yayi lesson nasa ya gama sai ya fita..

Yana fita kuma break ne nan Fatima ta dawo wajen Laylerh ta kalle ta sannan tace,

"Laylerh ina head tie naki?"

Ita Laylerh da yake jiya Aunty ta mata kiso ya tamke sosai da aka d'aura mata d'an kwali shiyasa suna shiga mota ta cire.

"Yana bag na".

" to kisa don makarantar nan in aka Gan ki ba Dan kwali duka prefect suke yi".

"To".

" me yasa ba zaki ci abincin ki ba?"

Laylerh kam don taga new environment ne ko abinci bata son ci Allah Allah take a tashi taje gida ta shafa musu labarin makarantar Gashi yaran duk a nitse suke ba kamar makarantar da ta Bari ba sai tace,

"Bana jin ci ne".

" to ki kawo sai mu had'a da nawa muci".

Kallon Fateema Laylerh tayi a zuciyar ta tana fad'in,

"Kaji yarinya zata zo ta cinye mini abinci don kwad'ayi shegen kwadayi".

Katse mata tunani Fateema tayi da fad'in,

"Me aka dafa miki?"

D'ago basket d'in Laylerh tayi ckin isa take fadin,

"Indomie da egg".don a San ita ma Yar Gata ce Nan Fateema ta mik'e sai ta d'auko basket nata irin Wanda yake kama da bag d'in nan Laylerh na gani ta turo baki tace,

" kaji yarinya ta d'auko skull bag nata zata cinye mini abinci ".

Ajiye basket d'in tayi sai ta bude ta Ciro food flask nata mai shegen kyau..

Bud'ewa tayi ciki shawarma ne sai na saman kuma soyeyyen Irish ne basket d'in kuma swan water ne gora biyu da kuma faro juice shi ma guda biyu sai tea a cikin flask da ka gani kasan Yar masu kud'i ne..

Tana fama fitarwa sai tace,

" Laylerh mu Fara cin nawa ko?"

"A'ah Aunty na tace in indomie yayi sanyi ba d'ad'i muci nawa".

" to muci naki anjima in munyi sallah kafun muje halqa sai muci nawa".

Zare ido tayi tana fad'in,

"Har azahar ina makarantar nan".

" Ehh primary 1-3 k'arfe 1 suke tashi mu kuma sai 3".

"Har three?"

"Ehh".

Nan suka Fara cin abincin har suka gama,gamawar su yayi dai-dai da ringing bell sai Laylerh Tasa lunch box nata a basket sannan ta Ciro tea'n ta ta mika ma Fateema tace,

" Gashi ".

" A'ah yanzu teacher zai shiga ki Bari sai second break ".

Mayarwa tayi sannan ta d'auki swan water'n ta ta sha.

" Laylerh ki d'aura head tie naki".

To tace nan ta Fara Neman dankwalin ta ba tare da sanin cikin books nata Tasa a bag nata.

Mik'ewa Fateema tayi ta zauna a bench nata don yana Bayan na Laylerh.

Prefect's ne suka shigo class d'in sun Kai 6 Amma yaran ko a jikin su sai tsalle suke,Laylerh kuma ganin kowa ya na harkan gaban sai sai ta juya ta kalli Fateema tace,

"D'azun Aunty tace na copying note don an kusa Fara test tunda nayi one month a gida".

" ohk Bari na baki note na".

"Keep quiet".

Wani prefect ya fad'a Amma ko a jikin su sai ma masu hawa bench yaran maza suna wasan banza, matan kuma kowa na harkan gaban ta yadda kasan ba mutum a class d'in.

Zarga wani yaro prefect d'in yayi Amma duk da haka basu fasa abunda suke yi ba...

" ga head boy ".

Wani student ya fad'a, sit kake jin klass d'in kamar ba halitta hatta prefect's d'in sun shiga hankalin su,Kai numfashi mai kyau ba Wanda ke yi Laylerh kam mamaki ne ya kamata jin yadda suke hayaniya Tun d'azun.

Kan ya shigo kamshin tularen sa ne ya Fara shiga duk da kasancewar sa student, nan ya shigo cikin tafiyar kasaita da Isa hannun sa d'aya a aljihu d'aya kuma rike da dorina,uniform nasa ya sha guga har kamar zai yi magana..

Yaro ne da ba zai wuce 20yrs ba kuma a jss 3 yake don makarantar ba senior secondary school iya junior ya tsaya shi yasa ya zama head boy.

sai kallon class d'in yake.

Gaba d'aya yaran jikin su rawa yake.

" duk Wanda suka San sunyi wasan banza a class din nan su fito".

Kan ya rufe bakin sa ma yaran da suka fito sun Kai 8..

Dama da yake private skull ne kuma a cikin class students basu wuce 30-35 haka nasu Laylerh d'in ma su 35 ne..

Yana had'e da rai ya sake cewa,

"Duk Wanda ya San yayi surutu ya tashi".

Kamar tsafi duk suka tashi ciki kuma Harda Fateema nan ma Wanda suka tashi sun Kai 8 don akwai wad'an da basu magana a class..

Fateema ce ta ta'ba Laylerh da kafa ta kasan bench a kan ta tashi sai Laylerh ta harare ta carab a idon sa hakan ya tabbatar masa masu surutun sun fi haka sai yace,

" iyakacin Ku?"

"Ehh".

" Wallahi wallahi gwara Ku tashi if not in na tada Ku ba dad'i zaku ji ba kuma kun sani sarai".

Ya fad'a da turanci amma ba Wanda ya sake tashi sai ya Fara da group A sai yayi pointing na wad'an da suka tashi yace da Wa Kayi surutu nan zaka nuna a haka har

ya fitar da guda biyar a group A kawai sai ya dawo group B nan ma ya cire su,yana zuwa group C group nasu Laylerh don yaci uban su da kyau sai ya Fara daga last bench a haka har yazo kan Fateema.

"Wace ce partner'n ki?"

Shiru tayi sai ya d'aga bulala ya zarga mata Laylerh na ganin haka cikin hawaye tace,

"Nice".

" how dare you speak vernacular ".

" Dan Allah Kayi hak'uri ".

Ta fad'a da Hausa,Haba ta Kara worsting situation cikin bacin rai yace,

" ina Hana ki kina yi?"

Ya fad'a cikin tsawa Fateema ko tausayin Laylerh taji don shi in yana magana shiru ake yi kuma ba'a ta'ba yin Hausa..

Kallon ta daga sama har kasa yayi sai yace,

"Where is your head tie".

Tana kuka tace,

" ban gani ba".

Locker'n ta ya bud'e sai yaga bag nata nan ya cire ya Fara duba head tie sai Gashi ya gani girgiza Kai yayi wato ma ta raina masa hankali da tace bata gani ba nan ya Fara dukan ta kuma in akwai abunda ta tsana shine duka a baya haka ta ringa kama kafar sa da yaji haushi sai yayi ball da ita cikin jin haushi ya fita a klass d'in nan sauran prefects d'in suka rufa mishi baya .

"Sorry Laylerh".

" Fateema Kiga yadda ya duke ni fa kuma Teacher'n nan yana kallon sa bai ce komai ba ".

" kiyi hak'uri ke kam".

"Allah ni dai daga yau ba Zan sake zuwa makarantar nan ba duk zaluncin prefect Na gov skull basu Kai shi ba".

Da yake yana da Zafi teacher's d'in duk ba mai hanasa mugunta saboda Wata Rana ko teachers basu iya controlling yara sai shi..

Yana fita Laylerh ta cigaba da kuka daga haka sai bacci Ana teaching.

Teacher'n na ganin haka ya zarga mata bulala akan Wanda head boy ya mata da wuri ta farka ji take kamar ta mutu kawai ta huta sai teacher'n ya Fara tambaya d'aya Bayan d'aya har aka iso kan Laylerh hankalin ta ma baya kan sa nan yace ta karanta hadith da ya rubuta a board nan ta karanta tas da yake she is good in Arabic don islamiyyar da take zuwa mamaki ya kamasa don duk students d'in ba Wanda ya karanta dai-dai kamar nata..

Ita ko tuni aka karantar da su a islamiyya

Tana gamawa ya Fara mata tambaya da Arabic nan ta Fara bashi amsa yadda harafin ke fita a bakin ta zaka ce yaren ta ne,yadda take Arabic d'in zaka ce da

rigima take kowa sai kallon ta yake nan yaji ta shiga ran sa dama in ya gama lesson yana bada chocolate nan ya bata yace ta zama best students nashi..

Kanta kamar zai fashe ganin ya yaba ta har wani jin kanta a sama take yi kamar tafi sauran..

Yana fita mathematics teacher ya shigo nan ma ba'a bar ta a baya ba don Harda kanzagi teacher na cewa 1+1 zata ce 2 kan ya gama magana zata bashi amsa ko ta tambayi questions nan wasu suka Fara jin haushin ta..

Yana gama lesson ya fita sai students suka Fara mata godiya Wai ta Cece su daga dukan head boy..

"Laylerh muje muyi sallah".

To tace nan Fateema ta rike hannun ta suka je wajen alwala wasu 'yan jss2 suka ce suna son ta da daughter ita dai bata ce komai ba.

Ana cikin haka sai ga assistant head girl kuma ita ce girl friend na head boy d'in tana jin kanta a skull d'in kuma kowa baya tsallake dokar ta don tsoron head boy duk da ita tafi son shi.

Tana kallon Laylerh tace,

" wow yarinyar nan ta mini kyau ta zama daughter na".

Budan bakin yaran dake wurin sai suka ce ai wane-wane ma tace tana son ta da daughter nan tace sai taga wacce ta Isa haka kuma ya wuce..

Rike hannun Laylerh tayi tace,

"Ya sunan ki".

Da larabci Laylerh ta amsa mata nan ta Fara mata magana da larabci Haba ji take kamar ta hadiye ta nan ta rungume ta a mosque tace wannan daughter nane kada wacce tace zata neme ta da daughter nan kowa yace noted sai suka yi sallah.

Suna idar da sallah Fateema ta kawo musu abincin ta suka Fara ci Ana cikin haka sai ga Muneerat wacce ita ce assistant head girl Amma Neerat frnds nata ke kiran ta.

A wurin su ta zauna sai tace,

" abincin zai ishe Ku".

"Ehh".

Suka amsa a tare sai tace,

" Gashi yau na manta kud'i na a gida da na saya muku ice cream ".

Murmushi kawai suka yi sai ga head boy kam yazo wucewa sai tace,

" baby".

Tsayawa yayi nan tace,

"Baby kud'i nake so ka bani Zan sayawa daughter na ice cream".

Sa hannun sa yayi a aljihu sai ya cire 2k sai kuma yace,

" wacece daughter ki?"

Laylerh ce k'asa k'asa tace,

"Fateema d'azun fa yace ba'a Hausa yanzu kuma yana yi".

Kallon Fateema yayi yace,

." me tace?"

Kan tayi magana Laylerh ta cabke,

"Senior kace ba'a Hausa".

Da yake da Hausa ya tambaye ta wace ce daughter'n ta.

Cikin takaici ya daga hannun zai mare ta sai Neerat ta rike hannun shi tace,

" Wallahi akan ta kowa zai iya jin mu a skull nan don da ka taba ta gwara ka ta'ba ni".

"Kema fa kin San Zan iya Marin ki".

" na fad'a maka Wallahi kada ka sake ta'ba ta muguntar ka ya tsaya a kan sauran students na skull d'in banda Laylerh".

Tsaki yaja sannan ya jefa mata kud'in sai tace,

"Zo ka d'auki kud'in ka don nafi k'arfin sa Wallahi, a kan 2k zaka raina mini wayo".

Laylerh da kanzagi sai ta d'auki kud'in ta mika ma Neerat

" Yar mishi da kud'in sa".

Dama bai yi nisa ba sai ya juya yace,

"Wallahi in Kika Yar da kud'in nan sai na miki dukan mutuwa ".

Bulala Neerat ta kar'ba gami da zare ma Laylerh ido tace,

" Wallahi in baki Yar ba sai na duke ki".

Laylerh dai kuka ta Saka ta rasa umarnin Wa zata bi duk da tasan Head boy d'in ya girmi Neerat kuma ita ma akwai tsoron sa a idon ta kawai don saurayin ta ne.

"Laylerh nace ki jefa masa kud'in sa".

Ta fad'a cikin daka mata tsawa sanda ta tsorata shima cewa yayi,

" Wallahi kina ajiye kud'in nan sai na miki abunda har Abada ba zaki manta da ni ba".

Suna cikin haka sai ga wani teacher irin masu zafin nama yaga Laylerh na kuka sai ya tambayi mai ya same ta nan Fateema ta fad'a masa sai yace,

"Dama garin yaya kud'in shi ya shiga hannun ta?"

Shiru suka yi sai zare ido da suke sai yace ma head boy d'in

"Kar'bi kud'in ka".

Nan ya kar'ba ya wuce yana hararan Laylerh.

Shi head boy d'in duk makarantar ba Wanda ya Kai sa shekaru indai students ne cuxx yanzu da yake jss 3 ma yana da 20yrs kenan kan ya gama secondary school ma yana da 23.

Hakan ya faru ne na rashin shigar sa makaranta da wuri don yana da 13yrs ya shiga primary 1 a haka ma bai yi primary six ba shiyasa..

Tun randa mahaifiyar sa ta haife sa baya gani makaho ne shi,Gashi dai idon a bud'e yake fari tas Amma baya iya ganin komai..

A haka kuma Mom nasa ke son sa kamar zata mutu sai suka kaisa hospital domin duba matsalar idon tunda a bud'e suke nan doctors suka tabbatar mata jijiyoyin idon sa are functioning normal ba wani matsala..

A haka har ya shekara biyar baya gani nan kuma aka tabbatar mata ba zata sake haihuwa ba,ba k'aramin Tashin hankali ta shiga ba nan ta mayar da hankali a kan sa domin sama mishi lafiya..

Yana da shekara 6 ta shigar da shi makarantar makafi kuma Alhamdulillah ya iya karatun Amma matsalar baya gani bare ya San ya A yake ya B yake.

Bata fasa nema masa magani ba har ya shekara goma sha daya a duniya bata karaya ba.

Gashi dai kallo d'aya zaka yi mishi ya shiga ranka in ka ganshi kuma zaka ce yana gani saboda idon fari tas yake..

Yana da shekara 12 da Wata goma Mahaifiyar sa taji akwai wani doctor a kano kuma ya iya aikin ido,don tsam basu ta'ba yin gargajiya ba nan ta nufi kano ko Allah zai sa a dace..

A cikin mota wani mutum ke masa wasa yana waving nashi Amma sai yaga baya responding ko inda yake baya kallo,gudun kar yaji ba d'ad'i sai mahaifiyar sa tace,

"Ai idon sa baya gani".

" subhanallah garin yaya,ga idon a bud'e Ai".

"Tunda aka haife sa yake fama da makanta kuma an tabbatar mana jijiyoyin basu da matsala yanzu haka asibiti zamu je a kano".

" kun gwada gargajiya ne?"

"A'ah".

" wannan sharrin jinnu ne,Zan taimake ki don Yaron ya shiga rai na".

Suna Isa kano ya Kai su gidan sa Ashe Babban malami ne bata sani ba nan ya ringa masa jinya har Allah yasa idon sa ya budu sai yace mata lokacin da take da cikin sa akwai Randa tayi hurgi da daddare Ashe a kan jaririn d'an aljani ne shiyasa suka rike ganin sa..

Sosai tayi farin ciki gami da masa kyauta Amma yaki yace don Yaron ya shiga zuciyar sa ne ya sa shi taimakon ta kuma ta kula da gaba".

Godiya kam ya sha sai suka dawo garin su wato Abuja nan ne Tasa shi a skull kuma daga primary one ya Fara don bai yi nursery ba,ganin Ana ganin sa Babba a klass sai yara suka Fara raina shi wannan dalilin ya sa shi zama mugu don baya son raini.... A haka har aka yi ma mahaifiyar sa transfer suka dawo Maiduguri inda yanzu suke makaranta d'aya da Laylerh.

wannan shine dalilin da ya hanasa shiga makaranta da wuri.

Ana tashi skull Sani yazo nan ta sallami Fateema don ita ma Fateema anzo d'aukar ta.

A gida kuma sosai Aunty tayi kewar ta dawar ta kawai take jira don ta San zata sha labarai

Bayan ta dawo daga skull Ana zaune a tsakar gida tana cin abinci tana bawa Aunty labarin duk abunda ya faru a skull din ba Wanda ta tsallake sai Aunty tace,

"In kina da assignment ki gama sai Ki kawo Na tayaki".

Mik'ewa tayi Bayan ta gama ci ta Kai kwanukan kitchen sannan ta dauki buta ta wanke hannun ta daki ta wuce nan ta dauko skull bag nata

Bayan an gama mata sai Muhammad da yanzu shigowar shi gidan yace,

" Aunty Laylerh ina assignment naki?"

"Kai wani irin wawa ne?ka girmi Laylerh fa Amma sai ka ringa ce mata Aunty".

" ni na zata duk mace Aunty ne Ai".

Shi fa haka kawai yake jin dadin kiran Yar uwar ta shi guda daya tilo da Aunty Laylerh

" Laylerh how was your first day at skull?"

Nan ta fad'a masa duk abunda ya faru Harda nuna mishi Bayanta tayi sai ya Fara hawaye ya hau holo

"Nifa bana son mugunta, yana yaro har zai iya wannan dukan,dole ma gobe naje ni da ya Sani wajen principal".

" A'ah in Kayi haka zaka sa yara tsanar ta ita Laylerh ma tana da laifi kana gani a nan da kaina na daurawa Laylerh head tie, sannan da aka ce wad'an da suka yi surutu su tashi kamata yayi ta tashi tunda ta San tayi,Abu na karshe kuma ina ruwan ta da kud'in sa".

Jin haka sai ya gamsu nan suka mata fad'a kan tabi dokokin skull d'in kuma ta fita harkan Yaron..

"In kuma ya sake miki irin dukan nan sai naje har skull d'in".

Daga haka kowa ya je ya kwanta sai Laylerh tace zata yi note don an kusa Fara C.A sai Aunty tace to taje d'akin ta..

K'arfe 11Aunty ta fito domin d'eban ruwa a Randa saboda na d'akin su ya kare sai taga wutan d'akin Laylerh a kunne nan taje d'akin sai taga tayi bacci a kan books nata sai ta gyara mata kwanciya gami da ajiye mata books d'in a cikin jaka sannan ta kashe mata wutan ta fita tana mamakin yau Laylerh ne ta maida hankalin ta akan karatu lallai taji jiki.

Washe gari aka shirya ta yau ma Sani ne da kan shi yazo Kai ta skull din.

Yau Laylerh tayi niyar ba zata yi laifi ba don haka ba Wanda tayi Wa magana Fateema na mika mata hannu ta ki magana..

Sai da aka fita break tace ma Fateema,

" Salamu alaikum ".

Tana mika mata hannu

" sai yanzu zaki mini magana? "

"Yi hak'uri yau nayi niyar ba Zan yi laifi ba".

Nan suka bud'e lunch box nasu sai Fateema tace,

" nace Wa Mom na nayi New frnd shine ta sa mini komai biyu nida ke,dama biyu ake sa mini na safe da rana yau kuma dukkan mu an sa mana na safe da rana".

"Eyyah nikam ban fad'a a gida ba".

" ba komai wannan abincin ma zai ishe mu".

Haka suka ci abincin su suka gama komai normal sai aka yin ringing bell nan Aji ya nitsu don jiya ma sunga head boy ya kwana biyu bai zaga ba shiyasa suka yi rashin ji..

Prefects na jiya ne suka dawo sai suka duki Yaron da baya ji a class sai yaro kam ya Fara fad'a da su nan hayaniya ya tashi head boy kuma jin haka sai yazo ajin badon prefect d'in ya masa ba da Harda shi zai hada a dukan..

Haka yayi ma Yaron duka sai yace duk Wanda ya San yayi laifi jiya ya fito kuka Laylerh ta Fara. Nan yasa su layi sai ya kusa kan Laylerh sai ta koma baya a haka har ta zama karshe zai duke ta sai tace,

" yaya na yace in an duke ni sai ya fad'a ma principal ".

Cikin jin haushi ya Kira d'aya daga cikin class mate nata yace,

" nuna mata yadda zata yi ".

Nan Yaron yasa kanshi a kasa kafa a sama,tana ganin haka tace,

" gwara wannan da duka ".

Sai tayi,tana kaiwa 2mins ta Fara kukan azaba shi kuma yayi banza da ita a haka har teacher ya shigo nan yace,

" mace ce kada ya sake sa ta wannan punishment "

Nan ya fita Laylerh kuma aka ce ta zauna ji tayi kafar ta kamar ba nata ba sai kuka.

Bayan anyi azahar taga Neerat ta nufo ta sai ta buya don harga Allah ta gaji da zaluntar ta da head boy ke yi..

"Laylerh gudu na kake yi?"

"A'ah ina duba Abu nane".

" ohk zo ga ice cream na kawo miki".

Nan ta ajiye Laylerh a cinyar ta ta Fara bata a baki Fateema ko Na kallon su tana murmushi

Sanda ta tabbatar Laylerh ta koshi sannan tace,

"Ga sauran ki bawa frnds naki sai ta tafi"

Ajiye ma Fateema sauran tayi tana Komawa gida tace,

"Aunty Kinga punishment da head boy yasa ni,, can kawai Neerat ta saya ice cream da su chocolates ta bani duba har da hijab Na ya baci".

Tana gama fad'ar haka Abbu ya shigo

" Laylerh me ya bata miki uniform? "

"Ice cream".

Ta fad'a Kai tsaye

" ina Kika samu?"

"Abbu assistant head girl ne tace ni daughter ta shine ta saya mini mistakenly na zubar a jiki na".

" kada kike karban Abu a hannun students don secrets cult".

"To Abbu".

" tunda ice cream ne duk Ku shirya zamu je sha".

Nan duk suka yi tsalle sai dad'i suke ji ita da muhammad sai suka je shiryawa don yau kam Harda Aunty..

Gown da sani ya saya Mata ta sa Muhammad kuma Kayan sa Na sallah'n da ya wuci ya sa

**

Parking motar driver ke k'ok'arin yi while Wata mota tayi over taking nasu a bakin plaza'n sai driver'n shi ya buga motar ba da sanin sa ba,nan yaro karami ya sauke glass na Bayan yana dakuwa ma driver'n tare da fad'in,

"Durun uwar ka".

Jin wannan ashar ya sa shi sauke glass na motar da yake hakimkance yace,

" Kai baka ganin girman na gaba da Kai ne da zaka zage sa?"

"An zaga Kai in fact Kai ma durun uwar ka".

Astagfurullah

Jin zagin da akayi ma mahaifiyar sa kuma duk duniya ba wacce yake so fiye da ita ya sa shi bud'e motar ba shiri ya fito yana fad'in,

" uwata ka zaga?"

"An kuma, uwar ka".

Haba ba sai ya kama shi da fad'a ba sai punch yake Kai ma yaro har ya fasa masa baki ba yadda driver bai yi da shi kan ya Bari ba yaki..

Da yake duk wrong parking suka yi hakan yasa suka had'a go slow mutani sai fitowa suke yi domin ganin meke faruwa ciki kuma Harda keke napep na su Laylerh..

Bai bar shi ba har sanda ya sumar da shi ganin zai iya aika Yaron lahira sai driver ya Kira mahaifiyar sa cikin 20mins sai ga ta,motoci da suke biye da ita ba adadi tana ganin maroon venza ta tabbata a wajen d'an ta yake saboda da shi ya fita..

Securities na biye da ita ta Isa wajen shi kuma ya d'aga hannu zai Kai punch sai tace,

" dakata".

Cak ya tsayar da hannun sa gami da juyawa ya kalle ta sai ta nuna masa mota da ido..

Yarfa hannun sa yayi Ba musu ya shiga mazaunin driver inda ya tayar da motar gami da buga motar su Yaron saura kadan ya debe Yaron yadda ya fige motar zaka ce kashe kan sa zai yi..

"Wannan wani irin yaro ne?"

Cewar Aunty don suna nesa da su kadan basu iya ganin su Mai kyau daga shi har mahaifiyar ta shi

"Aunty shine Sulaiman head boy da yake duka na".

" Kai Laylerh ki kula don banga tabon imani a zuciyar sa ba".

"Na Lura yana da Zuciya, kuma Ai uwa ba wasa bace".

Cewar Abbu..

" ni dai Laylerh ta kula".

Comment

Share

©Hafciey Musa

[1/25, 5:36 AM] Hafciey Musa😘: *LAYLERH*

(The prettiest emerald)

A yau ne su Laylerh za su yi hutun first term kuma Aunty tayi mata alkawari in bata wuce 10 ba tana da kyauta..

Tunda ta je makaranta zuciyar ta ke bugawa don ta San karya ce tace tayi abun arziki..

Ana basu result suka kama hanyar gida da Sani suna Isa ta bama Aunty result nata don ko Sani taki bawa...

Muhammad da su ma a yau suka karbi hutu ya dawo cikin murna don Na biyar yazo Laylerh kuma 20..

Sosai Aunty taji dad'i ganin Laylerh daga kauye ta fito kuma tazo number mai kyau ba tare da sanin basu da wani yawa a class din ba nan Abbu yace dole suje shopping nan suka shirya suka yi kyau..

Suna Isa kowa ya d'auki abunda yake so sai suka wuce wajen wasan yara a wajen kuma suka had'u da head boy nasu yana basketball da gani kuma yana so don yau kam waje Mai kyau sosai Abbu ya Kai su don ya faranta musu..

Yana ganin ta ya tambaye ta position nata nan suka fad'a mishi sai yace

"Ai dama da gani doluwa ce".

" A'ah fa fist term nan ta shiga skull d'in kuma sanda aka yi one month sannan ta Fara zuwa Aunty tace tayi kokari ".

Cewar Muhammad kamar karamin yaro

"In dai haka ne tayi kokari Bari na saya mata ice cream matsayin gift, nan ko ya saya Mata godiya ta mashi..

Komawa gida suka yi kowa na farin ciki.

***

Yau an wayi gari su head boy sun Fara junior wace..

Wata 'Yar jss 3 ne ta Kira Laylerh kan cewa ta Kaima head boy letter sai ta kar'ba ba don ranta yaso ba,da yake duk sanda suka had'u sai ya zalunce ta sai ta hangi Fateema, sai ta fara gudu saboda ta Kai mashi da kanta don ita ba zata iya fuskantar shi ba..

Mommy'n ta ne ta riko gifts iri-iri zata bata tunda yanzu sun kusa rabuwa sai kiran ta take Amma Laylerh gudu ta Kara nan Neerat ma ta Kara sauri,dai-dai lokacin da ta Isa wajen Fateema tana k'ok'arin mika mata gami da cewa,

" ayya ki Kai ma head boy ".

Sai Neerat ta Isa wajen, da yake tana da saurin hannu sai ta Mari Laylerh tana fad'in,

" ina kiran ki kina gudu".dafe wajen tayi tare da kurawa Neerat ido hawaye Na bin fuskar ta, Allah yau din nan da ace tana da girman jiki ba abunda zai hanata ramawa sai dai abunda zai faru ya faru, a zahiri kuma sai tace

"A'ah fa Wata ce ta bani letter na Kaima head boy ni kuma na San in Mun had'u duka na zai yi shine nake bama Fateema ta Kai mishi".

"Letter?"ganin yadda Neerat ta maimaita Kalmar wasika din ta tabbatar ya daki zuciyar ta shiyasa cike da kwarin gwiwa tace

"Ehh".

"Waya baki?"ta tambaya kan Laylerh ta gama rufe bakj

Nan ta fad'i sunan ta sai Neerat tace,

"Don munafurci kina matsayin daughter na za'a had'a baki da ke?"ganin fa yadda ta birkice Hala dukan ta zata yi sai tace

"A'ah.."

Mari ta Kai mata tana fad'in,

"Rufe mini baki munafuka kawai".

Ana cikin haka sai ga head boy d'in Wanda daga can nesa yake kallon su ganin ta Kai Mata Mari ne kuma ya sa shi tashiwa yazo wajen su sai yace,

" what's wrong? "

"Sulaiman Ashe Kai munafuki ne har mata na tura maka wasika ban sani ba?"

"Ni kuma?"

"Ehh mana,Gashi daughter na aka bama".

Nan ya kar'ba daga Bayan ma anyi zanin heart sai ya Fara karantawa yana fad'in,

" Ai Tun ba yau ba nace miki ita munafuka ce Amma kin ki yarda".haka kawai tsam baya jin Laylerh a jiki asalima ya rasa dalilin da yasa shi tsanar ta, Nan haushi ya d'ebe ta ta zubar da gifts d'in sannan ta cire bulala tace Laylerh ta kawo hannun ta magiya da hak'uri ta Fara bata Amma duk a banza dole ta mika hannun ta sai ya kuma fad'in,

"Amma gaskiya ta iya kalaman soyayya".

Yana fad'a ta Kara dukan Laylerh kuma ya fad'i hakan ne Don taci uban Laylerh d'in asalima ba wasikar soyayya bane ta godiya ce saboda cikin hutun da suka yi akwai Randa yake tafiya shi da Mom nasa zasu je Aure a jigawa sai suka wuce yarinyar

motar su ya baci sai yace ma Mom nasa wancan fa class mate nashi ce sai suka koma baya ita da iyayen ta ne..

Nam suka tambaye su lafiya suke kan titi da Daren nan sai Baban ta yace Wallahi motar ce ta baci kuma ya Kira mechanic sai Mom nashi tace ina zasu sai suka ce jigawa sai tace su kulle motar su tafi..

Nan ko suka d'auke su ashe ma Aure d'aya zasu a dawa ma tare suka dawo shine Baban ta yace ta gode masa shiyasa yanzu ta rubuta Letter d'in Amma Sulaiman ya nuna cewa ta soyayya ce aka ci uban ta..

Tana gama jibgar Laylerh ta wuce wajen yarinyar nan yarinyar ta fad'a mata abunda ke rubuce kuma Laylerh taji, nan take sai taji tsanar sa ya shige ta sosai nan mommy'n ta ta bata hak'uri Amma ko uffan bata ce ba..

A haka har suka gama junior waec inda Neerat ta bama Laylerh phone number kan ta ringa kiran ta don yanzu zasu rabu tunda makarantar a JSS3 ya tsaya a wajen Laylerh ta yarda number'n..

Kwana a tashi ba wuya wajen Allah yanzu Laylerh na primary 6 kuma yanzu tana da 11yrsda Muhammad ko yana jss2 sai dai shi boarding yake yanzu yazo hutun meet time ne inda yake da 16yrs...

Tunda ta shiga primary 5 bata wuce 5-10 hakan yasa aka bata Ameerah na primary, yanzu kam ba wani discipline da takura a skull d'in tunda su head boy suka tafi...

A cikin wannan shekaran ma boko haram sun sake turawa Abbu batun fitar da zakka Amma sai yayi banza da su Gashi zuwa yanzu kam alhamdulillah komai ya zauna mishi har ma yayi gidan kan shi ya bar gidan su Asma'u sai dai suna zumunci sosai da su Aunty ya kanje ganin gida in yaran sunyi hutu sai dai baya tafiya dasu don zuri'ar shi akwai karancin zumunci kowa daga shi sai yaran shi ba Mai zuwa wajen ka..

Tunda arziki ya Fara zama mishi duk yan uwan shi sai suka Fara son shi yana kuma kyautata musu sosai Musamman mahaifiyar shi sai dai ya kan dau dogon lokaci bai je ya duba ta ba duk da kasancewar shi d'a daya a Gare ta..

Har ila yau dai Sani Na nan kan bakan shi sai dai ya mayar da matan shi..

Shara ta kammala tana kokarin yin wanke-wanke taji Ana buga kofar gidan,dama da hijab a jikin ta nan ta nufi kofar gidan ga mamakin ta sai taga ba kowa

"To wane ne".

Gida ta koma bata idda karasawa tsakar gidan ba ta kuma jin Ana sallama

" Wai wane ne?Na fita banga kowa ba".

Ta tambaya cikin daga murya

"Malam Musa yana nan ne?"

"Kai din Waye ne?"

Jin shiru ne sai ta nufi kofar gidan tana fita taga mutum ya juya sai sauri yake yi nan ta Fara cewa,

"Me kake so a wajen sa".tana Mai rufa mishi baya Farare takarda ya Yada daga nan ya shiga mota ya bar wajen ita ko daukar takardar tayi ta nufi gida direct dakin malam Musa ta shige

" malam!malam!"

Cikin bacci yaji yadda take kiran sunan shi da wuri ya mike yana fad'in,

"Lafiya kuwa ina bacci zaki zo Ki tashe ni?"

"Malam kaga abunda aka kawo".

" waya kawo".

Nan ta fada mishi yadda suka yi da mutumin sai yace,

"Amina Ashe dama baki da hankali ban sani ba,meyasa Ku kam Mata Baku da tunani ne yanzu da ace ya miki wani Abu lokacin da kike bin shi me zaki ce".

Shiru tayi nan yayi ta masifa ya gama sannan ya bude takardar ya karanta wannan Karon last warning suke mishi kan fitar musu da zakka

" malam Dan Allah ko gonan suke so Ka basu mu rabu da su kafa San hukuncin Wanda yaki cire musu zaka".

"Sai me in sun kashe ni Ai don mutani nayi musu yadda suke so shiyasa suke jin dadi".

" sai me fa kace don Allah ba don ni ba ko don yaran ka, Ka basu abunda suke so".

"Kinga nace ba Zan bayar ba ko zaki mini dole ne ehh uwa ta".

" Allah huci zuciyar Ka".

Fita tayi a dakin a ranta tana tuna dole ta San yadda zata yi don wallahi ba zata bar shi ya sabawa umarnin su ba tunda Asalin yan garin ma biyayya suke musu bare shi da yaje cin Rani a karshe dai ta yanke hukuncin sanar da kanin sa Wanda yake bin shi..

A waya ta Kira ta sanar mishi sai yace ta bashi kwana biyu in sha Allah zai zo har garin ya mishi magana .

Kamar yadda yayi alkawari kuma sai Gashi yazo sai dai ba yadda take tsammani ba saboda influencing nashi ya Ringa yi kan cewa kada ya basu akwai wani malami da zai Kai shi wajen sa yana irin aikin in boko haram sun saka a gaba to da kaje wajen shi zasu cire ido akan ka nan ko malam Musa ya yarda don ya San Dan uwan shi ba zai cutar da shi ba..

Yana da wani gida a kauyen sai yace Dalha ya sauka a wajen aiko hakan ce ta kasance..

"Malam wallahi batun wani malami duk ba wannan Nifa ban ma yarda da Dalha ba".

" Amina a gaba Na kike cewa baki yarda da Dan uwa Na ba don cin fuska to Ki saurare ni da kyau zancen nan dai an gama ba Zan bayar ba".

"Malam wallahi Ka canza ra'ayi Tun wuri ina jiye mana abunda zai je ya dawo".

" ba abunda zai faru sai alkhairi in sha Allah, shi fa malamin da ya baka magani to ko sunzo sai dai suka gidan naka ya zama kogi Ko fili".

"Kenan yanzu Ka yarda da malami?"

"Gafara can d'an Allah malami fa ba boka bane".

Duk yadda taso fahimtar da shi yaki yarda Dalha kuma wani malami yaje suka hada baki da shi nan yace Ai kudin dubu Dari ne haka ya Irga ba basu..

Wannan maganin da Dalha ya kawo shine ya tabbatarwa da Amina mijin nata yayi nisa baya jin Kira don har tsabani suka samu kan wannan zancen..

Yanzu Laylerh tana jss2 karatu Na tafiya normal kuma yanzu Baban ta ke biya Mata kudin makaranta tunda Allah ya buda mishi don yanzu ita da muhammad duk makaranta daya suke suna sane da rikicin da iyayen su ke yi..

Fitowa tayi daga kasuwa da ledodin da tayi shefene tana jiran Dan adaidai ta nan taga wani makocin su

" Laaa Abubakar Kai ne?"

"Eh wallahi Ince gida zaki".

" ehh ".

" to shiga mu tafi Nima can Zan koma".

Shiga keke napep din tayi suna tafiya suna taba hira..

A can gidan su kuma Tun fitar ta ba jimawa Sani yazo falo ya isa suna Dan taba hira sama-sama da Aunty don zaman jiran Laylerh din yake yi saboda yanzu ta Kai ta Fara tsayawa hira tunda tana jss2 abun Ka da kauye..

Ganin ya dau lokaci bata dawo ba sai yayi deciding ya koma gida kawai nan ya sallami Aunty..

Daidai lokacin da suka tsaya kofar gidan ita da Abubakar nan sani ko ya fito ganin yadda suke hira tana mishi dariya ba karamin tafasa zuciyar shi yayi ba don shi har yau bata sakewa da shi..

Cikin gida ya koma yana fad'in,

"Wallahi Baba Musa ya dawo kawai ayi abunda za'a yi,taya Tun tana yarinya nake dawainiya da ita yanzu da ta girma kuma zata Fara tsayawa da samari ni wannan ne ba Zan dauka ba".

Kallon sa ta tsaya yi don tunda ya Fara zancen tana Bayan shi Aunty ce ta kalle ta tace,

" Laylerh ke da Wa kike hira a waje".

"Aunty Abubakar ne fa ya rage mini hanya don cewa yayi gida zai dawo Shikenan kuma yaya Sani yazo yana hada gaskiya da karya a Kai Na".

" Sani Kayi hak'uri makocin mu ne kuma bikin shi ma ya kusa".

"Ke kuma Ki bashi hak'uri".

Ta kare zancen ta Na kallon Laylerh tare da Mata alama da ido

" Aunty ni fa wallahi ya takurawa rayuwa Na Shikenan kuma daga cewa shi zai Aure ni sai ya hanani sakewa".

Duk mamakin zancen ta suka yi Abbu ne da ba Wanda ya San da shi cikin gidan ya fito daga daki debe ta da Mari yayi yana fad'in,

"Yanzu don rashin hankali har Sani zaki duba Kice yana takurawa rayuwar Ki".

Ta bude baki zata yi magana ya kuma debe ta da Mari sai da bakin ta ya fashe karshe dai Sani ne ya bawa Abbu hak'uri nan shi kuma ya tafi cikin sanyin jiki..

Ranar kwana kuka tayi Aunty ko bata ce da ita komai ba saboda ita ma bata ji dadin zancen da tayi ba..A Washe garin ya sayo waya ya kawo Mata domin ya shawo kanta Amma sai taki nan ta wurga masa waya tana fad'in,

" wallahi tunda har kasa aka Mare ni, samari yanzu Na Fara".

Wannan Kalmar ba karamin tayar mishi da hankali yayi ba don maganar matar shi na neman tabbata da tace sai ya gama wahala a kanta a nemi wani a bashi shiyasa ya nufi wajen Dalha

"Gaskiya Baba Dalha lamarin Laylerh ya Fara bani tsoro don yanzu har rashin kunya take mini sannan Wai ni zata dubi ido Na tace mini samari yanzu ta Fara".

" to Kai sani yanzu me kake so ayi?"

"So nake a tada zancen Aure Na da ita ayi kawai kowa ya huta".

" to kwantar da hankalin Ka kamar anyi an gama".

A Washe garin Dalha yaje gidan da niyar yiwa malam Musa magana sai ya tarar baya nan Aunty ce ta tambaye shi ko lafiya

"Dama zuwa nayi batun auren Laylerh ya kamata a tada zancen".

" to banda abun Ka Laylerh a nawa take?"

"Ban gane a nawa take ba Wato ke kike daure Mata gindi take duk abunda take so ko don Na Lura dama ba wani son sani kike ba,Ince don ta Kai auren ne kanta yake rawa har take mishi rashin kunya".

" Hmm Ai Na San ta Kai Aure kamar yadda Sadiya ta Kai Aure me zai Hana a musu tare".

Sadiya Yar shi ce ta biyu kuma sa'ar Laylerh ne

"Sadiya karatu zata yi".

" to Nima 'ya ta karatu zata yi ba Wanda ya isa ya aurar da ita har sai ta gama Junior secondary school haka kawai ita da har kishiya take da".

"To ni kuma Dalha Zan nuna miki ni Zan bada auren Laylerh kafin ta gama Jss1 a matsayi Na Na bappan ta".

" wallahi ba kai ba ko Baban ta bai isa ya aurar da ita yanzu ba sai lokacin da naso haka kawai".

"Ke da aka aurar da ke din Ai da kadan Kika fita ba son duniya Kika bi ba har da cin amanar Yar uwar Ki".

" ya ishe Ka haka don kana kanin miji Na ba yana nufin zaka ci mini mutunci ba".

"Karya aka miki baki ci amanar Yar uwar Ki ba ko shi Musa ba Hadeeza yaso da farko ba ke da jatumar Ki kuka shiga malamai".

" Dalha ya ishe Ka haka kuma daga yau in har cin mutunci zaka zo yiwa iyali Na to Na haramta maka shiga gida Na".

Duk juyawa suka yi suna kallon Abbu nan ya daura da fadin,

"Sannan batun Laylerh ni Zan yi yadda nake so da 'ya ta ba wani a cikin Ku ba wani shekara Zan aurar da ita ga Sani in muna da rai".

Yana gama fadar haka ya wuce daki Dalha kuma kallon tsana yayiwa Amina sannan ya fice nan ya sanar da Sani wani shekara za'a aura mishi Laylerh..

Ba karamin tashi hankalin Aunty yayi ba don Laylerh Yar ta guda daya ace zata yi Aure a 13yrs sannan ta zauna da kishiya hakan ya sata yiwa malam Musa magana Amma sai yaki bata fuska...

Ita ma Laylerh sosai hankalin ta ya tashi don tafi son makaranta da Aure,auren ma Wai Sani nan ta samu Kawar ta Nana ta fada Mata sai cewa tayi,

" wallahi Laylerh nima fa Sani ba wani burge ni yake ba mutum ne tsam ba farin jini".

"Ki bar wannan Bappan mu mana shi meyasa bai bada Yar shi Sadiya ba".

" ke dai kici gaba da addu'a in sha Allah shi ba mijin Ki bane".

An tsaida auren ta karshen wani shekara an kuma fadawa dangi da abokan arziki Harda su Asma'u..maganar boko haram ma ya lafa a tunanin su kuma maganin malamin ne.

A hankali rayuwa yaci gaba da tafiya Inda yanzu Dalha ya lallaba ya dawo da iyalin shi inda su Laylerh suke sannan Abbu yace su zauna a gidan shi da Dalha din ke sauka..

Yanzu Laylerh tana jss3 kullum Sani Na zuwa hira Amma ba zancen arziki dake hada su shi ko bai damu ba tunda ya San yanzu kam auren ya kusa..

Zuwa yanzu sosai Abbu ya habaka ta hanyar noma shiyasa yake sayan access yana ajiyewa ya kuma bawa Dalha shawarar ya Fara noma Amma yaki dole shi ke ciyar masa da gida Gashi Yar shi Sadiya makaranta daya suke da Laylerh Aji daya kuma duk Abbu ke biyan kudin..

Har ila yau tsam babu jituwa tsakanin Amina da Dalha saboda ita ta gama fahimtar ba son Allah da annabi yakewa Dan uwan nashi ba..shima fahimtar ta gano shi yasa shi tsanar ta..

A makaranta in kaga yadda Sadiya ke ji da Kai zaka ce ita ce biological Yar Abbu ba Laylerh ba..

"Mama Kinga fa yanzu Mun shiga jss3 Kinga sai junior waec zamu yi".

Dalha dake kwance da wuri ya mike ya dubi Sadiya yace,

" kina nufin Harda Laylerh a jss3 take".

"Eh mana Baba ajin mu daya ai".

" Wato Musa ya rainawa mutani hankali da yace zai aurar da yarinya Tun ba yau ba Amma Gashi har ta shiga Aji uku shiru kuma nasan wannan shegiyar matar tashi ce".

"Haba Mai gida ina ruwan Ka da rayuwar gidan su".

" ke Dallah sahashasha rufewa mutani baki kullum baki wayewa".

"Wallahi baba Nima nafi son tayi Aure don a makaranta malamai in ance ni kanwar ta ne sai suke mamaki Wai ya aka yi ni doluwa kuma fa ko Ana fada da ni bata shiga kawayen ta duk ba so Na suke ba".

" Ai ko Aure dole tayi".

Ficewa yayi a gidan ya tafi shagon da Abbu ya bude babba a cikin kasuwan garin Na provisions don ya San a nan ne zai same shi..

Koda ya Fara mishi zancen auren Laylerh sai yaki bashi fuska ta hanyar Fara lissafi da wani d'an uwan shi Dan kasuwa..

Muhammad dai alhamdulillah yanzu ya gama secondary school ya dawo gida murna wajen Laylerh ba'a fadi don ko abinci tare suke ci kullum shine Abokin rakiyar ta in an aike ta ko in Sani yazo zance..

Aunty dai dadi taji ganin ko zancen auren Laylerh baya yi...

Sani ma sosai hankalin shi ya tashi jin bappan nashi yayi shiru..

Ba Wanda ya sake maganar auren ta har suka Fara junior waec Muhammad ko tuni ya jona jami'a saboda Abbu yayi niyar suyi karatu Mai zurfi tunda shi Allah bai nufe shi da yi ba kuma sun san zafin hakan..

Tunda suka Fara junior waec ta maida hankalin ta kan karatu shiyasa ma ta Hana sani zuwa zance..

A ranar da ta gama junior waec suna shagalin su a makaranta da kawayen ta saboda wasu ba lallai suyi senior secondary school a wajen ba sani yazo daukar ta kallon shi tayi

"Nifa ba yanzu Zan koma ba".

Jan hannun ta yayi a cikin kawayen ta ya jefa ta a mota sannan suka nufi gida..ganin yadda idanun shi suka yi ja alamar kuka yayi sai jikin ta ya bata ba lafiya nan zuciyar ta ya Fara bugawa..

Tun kan su isa taga jama'a a kofar gidan su da alama rasuwa aka yi nan ta dube shi tace,

" ya Sani waya rasu a gidan mu".

Shiru ya Mata har suka iso nan ta fita da gudu sai ganin Muhammad tayi yana kuka kamar ran shi zai fita nan ta tabbatar ba shi bane ya rasu..cikin kuka ta karasa gidan sai taga Aunty'n ta ma kuka take da iya karfin ta nan tace,

"Abbu".

Sai kawai ta yanke jiki ta fadi,tunda take a rayuwar ta ba taba suma ba sai yau nan mutani suka yi kan ta aka bata taimako..

Tana farfadowa ta fada jikin Aunty tana kukan da yasa mutani tausayin ta..lokacin da aka gama mishi sutura za'a tafi da shi har waje tabi mutani motar gawar ta shiga kan shi ta fada sai ganin likkafanin duk jini kenan accident yayi..da kyar Sani ya daga ta gaba dayan ta zasu shiga gida taji wani Na cewa,

" Allah sarki malam Musa Allah jikan Ka,Ashe boko haram ne ajalin shi shiyasa yaki fidda Musu zakka Gashi karshe kisa mafi muni suka mishi ta hanyar yankan rago suka raba kan shi da jikin shi".

Allah jikan ta yaa Salisu yasa Ka huta ya Kai haske kabarin ka irin wannan kisan ta yankan rago yan boko haram suka yiwa yaya Na cousin na😭

Haba nan take ta hau ihu kamar mahaukaciya don yanzu ta fahimci su Waye suka kashe shi..

A ranar duk Wanda ya shiga kauyen sai ya San anyi mutuwa a Washe gari kuma yan garin su suka zo Harda yan uwan Aunty kuka sosai aka ringa yi Musamman Adda wacce take mahaifiyar shi kuma shi kadai take da a duniya..

A ranar da aka yi sadakan uku mutani suka Fara Komawa ciki kuma Harda yan Bauchi don zasu koma su karbi gaisuwa a can don akwai mutanin da kudin mota da tsufa ya Hana su zuwa..

Har aka yi bakwai cikin su ukun ba Wanda ya koma daidai gaba daya sun koma kalar tausayi gidan ma ya musu fadi dayawa da kyar Abba mahaifin su Asma'u yasa Muhammad Komawa makaranta don exams..

Tun daga lokacin aka tattara dukiyar Abbu gaba daya aka Mikawa Dalha nan ya Fara abunda ran shi ke so don har gida ya saya..

Bayan anyi arba'in sai aka mishi maganar makarantar Laylerh nan ya Mata registration Na Ss1 taci gaba da zuwa a makarantar da take Sadiya kuma canza Mata makaranta yayi..

Abu wasa gaske sai ga Dalha da kyar yake yarda ya biyawa Laylerh da muhammad kudin makaranta har ya Kai ga wani lokacin sai Aunty ta roki yan uwan ta take biya musu..

Laylerh Na SS2 yace ba zai sake biya Mata kudin makaranta ba Muhammad kuma two hundred level nan Aunty tace Ai bai isa ba sai cewa yayi Laylerh Aure zai Mata..

Sani shi ya cigaba da biyawa Laylerh kudin makaranta Muhammad kuma yana Dan buga-buga ya samu wani lokacin kuma Abban su Asma'u Na biya mishi..

Daga karshe abincin da zasu ci sai ya Fara gagarar su karshe haka wata Rana suke kwana ba zasu ci komai ba kuma duk inda Aunty ta Kai karar shi ba Mai cewa komai sai dai ace kar ta sake kawo maganar daga karshe Muhammad saida wayar sa yayi ya musu chefene suna ci a hankali yana kuma fita nema..

Kayan abincin Na karewa suka koma gidan jiya Gashi wannan Karon har korin Laylerh school fees aka yi Randa aka Fara exams Na third time zasu je Ss3 don Sani ma wannan Karon sungula sun mishi yawa saboda matar shi ta haihu ga kuma makarantar yaran shi uku..

Duk zaune suke a tabarma Aunty ta kurawa waje daya ido don haka kawai zuciyar ta ke yawan bugawa Wanda ta tabbatar dole akwai mummunan abu dake tunkaro rayuwar su,Laylerh ce kwance a cinyar ta a hankali kuma take shafa kan Laylerh kamar Na jaririya

"Aunty wallahi gwara mu yiwa baba Dalha magana ya bamu kudin mu ko ni Zan iya rikewa Ai yanzu ni ba yaro bane tunda Laylerh ma yanzu tana sha bakwai".

" a'a Muhammad Ku bar shi duniya ce".

"Akan me zaki ce haka Aunty Kiga fa yadda muke fama da rayuwa?"Cewar Laylerh

"Har yanzu ke yarinya ce Laylerh ba zaku gane ba,Wai ce muku aka yi haka kawai kowa ya gagara yiwa Dalha magana akan dukiyar Ku ne?to wallahi bai bar su banza ba don haka Ku rabu da shi".

" Amma....".

"Nace Ku bar shi duniya ce yaje.."

Ana gobe Muhammad zai gama weekend ya koma don duk weekend yake zuwa yana raka Laylerh makaranta zai je nema Mata alfarma yace,

"Aunty Laylerh Nifa ba makaranta Zan raka Ki ba gidan Baba Dalha zamu je mu mishi maganar kudin mu".

" wallahi kam Yaya banga me yasa za'a ji tsoron Wanda baya tsoron Allah ba ".

Gidan suka wuce da kyar Mai gadi ya Bari suka shiga sun sha zama a falon kan Sadiya ta fito da yake tana son Muhammad sai wani rawan jiki take yi da ta Gan shi, nan yace Mata ta Kira mishi Baban ta jiki Na rawa ta wuce dakin shi..

Matar shi Na fitowa Harda abinci ta basu suka ce sun gode ba yadda bata yi da su ba suka Ki ci..

Yana fitowa ya zauna tare da Nade kafa daya kan daya yace,

" ba dai maganar rashin abinci bane ya kawo Ku".

"Ko daya baba dama zuwa muka yi batun gadon mu da ke hannun Ka don Zan iya juya su ko a musulunci Na Kai shekarun da za'a bani".

Kallon su yake yi fuskar shi da tsan tsan bacin rai yace,

" uban Ku gado ya jira kan yayi arziki ne?Ince har yau Baban mu Nada rai bai mutu ba don haka Tun wuri gwara kaje Ka nemi Na kan ka yafi maka don ba dukiyar da Zan bayar yan iska kawai in ma uwar Ku ce ta turo Ku kuce ni Dalha nace bazan bayar ba".duk dagowa suka yi suna kallon shi nan ya cigaba

"Sannan ke kuma Kice da uwar Ki ta shirya auren Ki saura sati biyu".

Kallon shi ido cikin ido tayi don dama can haushin shi take ji don yadda baya son Aunty'n ta tace,

" baba duk abunda Ka fada in sha Allah zamu sanar da ita sannan batun kudi da kace ba zaka bamu ba Shikenan Mun ji Amma Ka saurare mu don wallahi court zamu shigar da Kai".

Mari ya debe ta da shi yana fadin,

"Fitsarerriya irin uwar Ki kin isa Ki fadawa uban Ki haka".

Hannun ta Muhammad ya Kama suka mike da zasu fita tace,

" Mun Barka lafiya Baba Dalha sai kaji daga Gare mu".

Ficewa suka yi gida suka nufa ko da Aunty ta tambaya ya suka dawo sai suka ce Anki barin ta tayi exams din ne basu ce da ita komai batun Dalha ba..

A Washe gari da safe sai ga police suka zo Kama Laylerh tambayar duniyar Allah ba Wanda Aunty bata musu ba sai cewa suka yi su hadu a police station..

Daga daukar Laylerh da suka yi Shikenan ba ita ba labarin ta Neman duniya anyi ba'a ganta ba haka ma Dan uwan ta daga cewa Bari yaje ya fadawa Abban Asma'u ko zai taimaka musu ba'a sake ganin shi ba Abban Asma'u kuma yace bai je wajen shi ba...

Daga wannan lokacin Aunty ta koma kamar karamar mahaukaciya bata komai sai kiran sunan Laylerh da Muhammad kullum tambayar ta yaushe zasu dawo...

Farmakin da yan boko haram suka Kai kauyen Na karshe inda suka yi nasarar tada kauyen Wanda a lokacin tuni Dalha ya bar kauyen ya dawo gida Bauchi da zama nan ne Allah ya tseratar da ita ta shiga kauyen makobta Amma kowa yaki taimakon ta saboda in Ka taimake su wasu Na Kira su fadawa boko haram din daga nan su aika Ka lahira ko kuma camp da ake Kai internally displaced people shima Wata ran akwai yaran boko haram din a cikin yan gudun hijira shiyasa kowa ke gudun taimaka musu..

Daga wannan lokacin ita ma ba Wanda ya sake jin batun ta nine dai Na taba tambayar shi Wai ya yayi dasu shine kaga Nima Na bar gida har yau ba inda Na tsana fiye da gida Gashi sanda ya sani jinyar Wata uku..

wannan shine cikekken tarihin Laylerh

Hawaye Abokin Haruna ya share sannan yace,

"Amma bawan Allah'n nan ya cika azzalumi Allah ba zai bar shi ba".

" Ai Ka Bari gaba daya ahalin ta ya wargaza su".

"Allah Toni asirin shi kaga i'sha yayi muje muyi sallah".

Mikewa suka yi nan suka yi tafiyar su..

A bangaren Laylerh da Dada kuma napep suka tare inda Dada tace,

" Mai keke anguwan Baraya zaka Kai mu ciki ba junction ba".

"To Hajiya nawa zaku biya".

" zamu baka Dari biyu".

"Dari biyu yayi kadan Hajiya ciki fa Kika ce kuma kin San yanzu Mai ya Kara kudi Ki Kara wani Abu sai muje".

"Zamu baka biyu da hamsin".

" Ku kawo Dari uku in bai muku ba Na tafi".

"Shiga Laylerh".

Shiga tayi shiko Kayan su ya shigar bayan keken nan suka tafi...

Aunty ko ba zaki yi comment ba Dan Allah kiyi sharing□

Comment

Share

©Hafciey Musa

[1/25, 5:36 AM] Hafciey Musa😘: *□LAYLERH□*

(The prettiest emerald)

Har cikin anguwan baraya suka shiga inda suka tsaya kofar wani gida nan ya sauke musu Kayan su Dada ko touch Na wayar ta ta kunna ta bashi kudi tare da cewa"Mun gode".

Karba yayi inda ya gyara parking Na machine din sannan yayi reverse ya juya ita ko cewa tayi"Laylerh dauki akwatin Kayan Mun shiga".dauka tayi nan suka nufi cikin gidan ido Laylerh ta ware tana ganin ikon Allah..

Tabbas ko ba'a fada ba wannan family house ne saboda gidan Babban ne sosai Gashi tsohun gida ne sosai don yawancin part din da kyaure aka zagaye..kowa Na cikin part nashi sai hasken Nepa dake haska ko ina Bayan Dada tabi can wani shashi a karshe suka nufa can kam ba'a kewaye yake ba saboda shine karshe yana jikin ginin katangan gidan..

"Oyoyo Dada".

Wata karamar yarinya da ba zata wuce 10yrs ba ta fada da gudu ta zo ta rungume Dada.. Me zai faru kowa sai fitowa yake daga bangaren su Masha Allah gidan kam akwai yan Mata ba adadi kuma duk kusan age mate nata ne sai wadanda suka fi ta da kuma wadanda basu Kai ta ba yaran maza ne dai babu sosai kuma dukka yara ne..

Matan gidan ne suka Fara fitowa ko wacce daga bangaren ta a kalla zasu Kai 5 da gani matan kannen Dada ne duk sannu da zuwa suka Mata sannan suka juya kowa ta nufi sashin ta haka ma yan matan gidan kowa sashin su ta nufa..

Cikin daki suka karasa gado ne irin ta rumfa babba sai karamar katifa a kasa dakin Leda ne a shimfide sai irin jeren daki da 'yan da ke yi..tsohuwa ce kwance a gadon rumfa Fara sal da ita sai dai fa tsufa kam sosai ta tsufa don har fatan jikin ta sun nannade..

Wata Mai tsananin Kama da Dada ce zaune gefen ta tana bata kunun da suka dama Mata, zama Dada tayi a tabarmar dake shimfide a dakin haka ma Laylerh.

" Dada kun iso sannu da hanya".

"Lafiya ya jikin Dadda"

"Jiki da sauki sosai"

"Alhamdulillah" Dadda jin an Kira sunan Yar ta mafi soyuwa a Gare ta sai tace"da gaske Dada Na ce tazo? "Mikewa Dada tayi nan ta rike hannun Dadda tana fad'in" nice Dadda ya jikin Ki "

"Da sauki" ta fada tana Kara matse hannun Dada..sosai take jin jiki kasancewar tsufa ya kamata yau lafiya gobe ba lafiya kuma duk rashin lafiyar da zata yi Dada Na zuwa da ita za'a yi ta jinya har sai taji sauki sannan ta koma..abinci kanwar Dada ta gabatar musu sai yanzu ta Lura da Laylerh"Dada bakuwa muka yi".

"Eh Yar daki nace". "Masha Allah"

Abinci suka ci nan suka yi sallar i'sha zasu kwanta Dadda tace ita dai dole da Dada zata kwana haka ta haye gadon ta kwanta kusa da mahaifiyar ta kanwar Dada kuma suka kwanta katifa daya da Laylerh.. ita har Allah Allah take gari ya Waye ta kalli 'yan matan gidan daya Bayan daya..

**

Horn Driver yayi nan security dake gate din ya leka sai ganin motocin da bai yi tsammani ba da wuri ya fito jikin shi har rawa yake ya wangale gate din nan motoci ukun suka sa Kai cikin katafaren company..

NATURES PRIDE FARM

Shine sunan dake rubuce da manyan harufa jikin katon building din..

From the farm gate security ya Kira wani Dan uwan shi security dake fishery department yana fad'in,

"Yau fa boss ya shigo so bamu San da wani department zai Fara ba don haka ayi informing sauran department din da zuwan shi".

Yana gama fadar haka ya katse kiran gaba daya a rude yake ya kuma yi mamakin ziyarar da boss din ya kawo musu..

Farm din Babba ne sosai saboda 500 hectares ne kuma suna da department har hudu..

Na farko akwai agronomy department Wato wajen noman rake

Sai livestock farm wajen kiwon shanun da suke yoghurt da shi

Fishery department shi kuma suna kiwon kifi a wajen

Sai Engineering department a nan masu gyara musu abubuwan company'n suke don ba zai yi wu ace duk girman comlany'n sai sun fita waje domin Neman masu gyara ba..

Akwai sections under the departments

A livestock farm akwai section nayin yogurt

Agronomy akwai section da ake processing sugarcane into sugar..

Sai last admin department Wato a nan head of the farm da sauran staff suke..

Wannan dalilin yasa security dake farm gate din cewa basu San ina daya boss zai Fara shiga ba..bai fiya zuwa company ba saboda in a month da kyar yazo sau uku kuma duk sanda ya tashi zuwa zuwan bazata yake musu..

Direct motoci ukun Admin department suka nufa inda zuwa yanzu Rabin company'n sun San da zuwan shi..bude mishi kofa aka yi sanda ya dau time sannan ya sauke kafar shi daya a waje nan ma sai Bayan wasu seconds ya fito..

komai nashi Masha Allah ne..

Lumshe idanun shi yayi sannan ya bude su yana Mai shakan iskar company

" boss shall we".

Wani a Bayan shi ya fada yana nuna mishi hanya da hannu nan ko ya Fara tafiya cike da izza suka nufi ciki..

Da yake admin department din upstairs ne a downstairs din akwai fili kadan kan Ka Fara hawa upstairs din a wajen ya tsaya cikin isa yace,

"Ina son ganin duk staff Na department nan yanzu".

Na Bayan shi ne ya bude murya tare da maimaita abun da boss din ya fada nan take staffs din kowa ya Fara fitowa da sauri har manager'n department din..

Mutani sun Kai 30 suka sauko kowa kan shi a kasa kallon manager yayi yace,

" ya aka yi farm na rake duk weed?"

"Sorry sir inda Ka gani ba main farm din bane ta gaban ne kuma wajen su jatutu ne ke shuka sugarcane in yayi suna sayarwa".

Jatutu messenger ne

" how dare you?har ace worker's suna da damar shuki a nan".

Kowa kasa ya Kara yi nan yace,

"All of you mu tafi agronomy department din".

Convoy suka hada saboda Bayan motar shi manager ma ya shiga nashi da manyan department din sai sauran staffs din kuma peacock suka shige nan aka wuce farm din..

Staffs Na agronomy ma suna ganin shi duk suka shiga hankalin su nan wani yace,

" Barka da zuwa ranka shi Dade".

Shiru yayi yana karewa farm din da baya ganin karshen shi kallo

Manager yayi gaskiya saboda cikin farm din ba weed Gashi sugarcane din sunyi yadda ya dace nan yace su jatutu su cire nasu gaba daya da yake Allah yaso su duk sunyi nan suka cire..

Engines Na extracting sugar syrup ya taba yana fad'in,

"Yau sugar buhu nawa kuka yi?"

"Dari uku" manager'n department din ya bashi amsa daga nan bai sake cewa komai ba suka wuce livestock department inda ake ajiye shanaye Wanda Tun kan su iso yana hangan kashin shanu nan yace a tsaya don ya hango exotic breed Wato shanun da ba Na kasar nan ba ta haihu wajen dai ba kazanta sai dai mahaifan bai gama fita ba yana yawo a jikin ta.

"Wato duk Baku San kudin ta bane shiyasa kuka yi banza da ita har Wai ta haihu ba Wanda ya sani,Hajiya Na can abuja ta bar muku amanar company Amma kuke yadda ranku yaso ina manager'n department nan".

" sorry sir bai San kazo ba yana ciki Bari a Kira shi".

"Hurry up".

Staffs Na department din uku suka nufi ciki da gudu sai Karo suka yi da shi a main entrance din yana gudu tumbin shi Na bin shi gaba daya a rikice yake nan ya dube shi yace,

" Emanuel what's happening in your section".

"Sorry sir".ya fadi murya Na rawa,cikin tsawa da rashin duba girman Emanuel din yace

" will you shut up".

Veterinary Doctor aka Kira nan suka kawowa cattle din agaji,Yaron da ta haifa yayi wani rago girma..

Suna shiga ciki ya samu workers din nata zubar da yoghurt da yayi expire..

Asalin wajen processing din kam is very clean nan ya tsaya yana kallon extracting milk daga shanaye chamber'n processing yana bin pipe ya wuce da shi..

Wajen processing din suka je komai clean workers din suna sanye da fararen kaya suna busy daga nan wajen packaging suka wuce shi ma komai well arranged, yoghurt daya ya dauka ya bude yana seeping tare da tambayar reason da yake sa yoghurt din expire.

"Sa gaskiya Zan fada maka wannan ba laifin mu bane daga farm gate ne in an fidda sabo ba zasu tabbatar sun tsaida tsohu ba sai su hada tsohon da sabon har yayi expire ba'a gama sayarwa ba don kullum Ana tura musu sannan Nima Randa naje inspection ne Na gani".

Dam suka wuce kogi ne ya wuce ta gonan sai akayi using intelligence aka tare ruwan aka Hana shi wucewa sai waje kadan da aka Bari..ruwan is clean hatta workers d'in suna amfani da shi..

Agogon hannun shi ya duba sannan yace,

" accountant ina da case da Kai but I have some commitment ahead so send me a mail Na budget da kuma profit Na wannan month da expenses ".

"Ohk sir".

Daga nan ya shige mota ya tafi su ko duk ajiyar zuciya suka sauke..

Sulaiman kenan!

**

Tun jiya yake fama da zazzabi saboda yau kuma rashin lafiyar tashi ta Dan motsa gefen shi Hajiyar shi ce zaune a bakin gadon shi tana fad'in,

" Naseer Ka dauki kunun acca Ka sha don ba dadin jikin Ka kake ji ba".cikin jin jiki yace

"Mom Zan sha fa but ni wallahi alale ma nake son ci".

" in dai alale ne kada Ka damu da Kai Na Zan maka Na gujjiya".ta kare zancen nata tana Mai tausayawa halin da yake ciki

"Mom Na gujjiya kuma Ai ba dadi zai yi ba".ya fadi yana Jan dogon numfashi

" Ka taba ganin me diabetes yaci alalen wake?ko so kake mu karya dokan Likita ne, yanzu Ka tashi Ka sha kunun".

"Mom Zan sha but ba yanzu ba".ya fadi yana sake ajiyar zuciya don shi kadai ya San abunda yake ji

" wallahi Naseer these days kana wasa da lafiyar Ka".

Mikewa tayi ta fice a falo taga Nusaiba sai cewa tayi,

"Ba zaki je Ki duba jikin yayan Ki bane?"

"Mom ban San baya jin dadi ba da yake at times ciwon ya tashi har ya lafa ba Mai sani".

" to Kije Ki duba shi".wucewa apartment nashi tayi knocking tayi jin bai ce komai ba sai ta shige ciki tare da zama kan bed din tace,"so Bros baka ji dadi ba Ashe sannu fa"Yauwa yace da ita yana kokarin yin matashi da jikin gado ita ko taci gaba da pressing wayar ta sai da yayi matashin ta dube shi cikin zolaya tace,

"Nifa wallahi kada Ka mutu mana yanzu baka kawo mana masu kiran mu da Gwaggo mu duke su ba"cikin lumshe ido da dariyar karfin hali yace

"Au dama ce miki akayi don Ku duke su zai haifo su".

Juyowa gaba dayan ta tayi tana fuskantar shi tare da tankwashe kafa tace," let's be serious yaci yanzu ace kana zancen Aure"

"To ko zaki bani Mata ne".murmushi tayi tace

" ni dai banda wacce Zan baka ina wancan Wanda naji mom Na cewa bata da asali".murmushi yayi Wanda bai San lokacin da ya tsubuce mishi ba tare da lumshe idanun shi ya kuma bude su ceiling yake kallo sannan yace"Laylerh "kwabe fuska tayi tana kallon Dan uwan nata yadda ya fadada murmushi a fuskar shi sanda yake ambaton sunan Laylerh

"Nifa ban San sunan ta ba"ta fada tana mishi kallon ido cikin ido don so take ta karanto abunda ke rubuce a cikin idanun nashi

"Ita ce Wanda tayi saving yayar Ki daga auran wancan Dan iska".ya kuma fadi yana murmushi Mai sauti don haka kawai yake jin nishadi a duk sanda ya tuno ta

" ohh you mean yarinyar can by the way tana da kirki Ai".

"Sosai ma".

Matsowa kusa da shi sosai tayi tare da daura hannun ta a kafadar shi ta daga masa gira daya tace" so yaya Na yarinyar can yake so ko?"

Buge hannun ta yayi ya hade girar sama da kasa tare da fad'in "you are not serious".

" Dan Allah mana tell me if you guys are in relationship wallahi ina iya karanta yadda kake ji game da ita a fuskar Ka,dubi daga ambaton sunan ta gaba daya sai annuri ya bayyana a fuskar ka".

"Yadda kike a waje Na haka ita ma".ya fada cikin son kauda zancen da Nusaiba ke yi, Kan tayi magana an bude kofa Saudat ce ta shigo Wato wacce aka fasa auren ta rike kwankwason ta tayi ta tsaya a bakin kofar tace,

" so what are you guys discussing about ina zuwa sai kuka yi shiru".

"Sis yayan Ki zai yi baiko".

Da gudu ta karaso dakin ta rungume shi tace," wow congratulations bro am happy for you".tabbas yaji zafin fadawa a jikin sa da tayi kasancewar dauriya kawai yake yi bai da wani karfi Amma sai bai nuna ba Kunnen Nusaiba ya rike yana girgiza Kai nan Saudat ta hade rai tace,

"Wato ni zaki yiwa karya?"ita ma kunnen Nusaiba ta rike sai kara ta sake tace,

"Shikenan Ku tsinka mini kunne Ku huta".

Sake ta suka yi sai Saudat tace," Bro ya jikin ka?"

"Da sauki this Nusaiba is naughty". Wallahi fa ta bashi amsa lokacin da Hajiyar su ta shigo dakin

" Naseer Kayi kokari Ka wasa ruwa tunda naga jikin da sauki don har waje ina jin muryar Ku".

Kokarin mikewa ya Fara yi sai jiri ya debe shi nan ya koma da baya ya fada bakin bed din, duk hankalin su ne ya tashi suka nufe shi sai ya dafe Kai da daya hannun shi yana fadin "relax dizziness ne kawai".

" to ba dole Ka ringa feeling dizzy ba tunda kaki cin abinci, akwai wani doctor da mijin Kawa ta ya taba kwanciya a wajen shi ya iya aiki sosai so Zan nema maka ganin shi tunda Na Lura tsam Kai lafiyar Ka ba damun Ka yayi ba".

Mikewa yayi yana dafa bango har ya shige bandaki nan suka fice a dakin Bayan ya fito jallabiya da three quarter kawai yasa ya koma ya kwanta so yake ya Kira Dada ya tambaya sun isa lafiya Amma kuma ya San dole mutumiyar shi zata dago cewa baida lafiya nan ya hakura..

Hajiya kaltume Na fita side Na mijin ta ta nufa nan take cewa ciwon Naseer fa gaba yake yi ba baya ba Gashi doctor'n shi yayi tafiya ya kamata a fidda shi waje ko kuma akwai wani Doctor da Kawar ta tace Mata ya kware a aikin shi...

"Kinga Nifa Na manta ne wallahi ya turo mini da sunan medicines Na Naseer ta WhatsApp Bari yanzu Na tura driver ya saya mishi".

Haka ko aka yi driver yaje ya sayo mishi ciki kuma Harda na bacci yana sha sai bacci nan duk suka fita don sun San yana tashi zai ji sauki in sha Allah..

**

Yau Tun kan su shigo yayi wanka inda ya sanya three quarter da T-shirt sosai yayi kyau, ya zauna a bakin gadon shiru waje daya ya kurawa ido, Baaba ce ta tura kofar ta shiga da sallama ganin shi fes sai tayi murmushi tace," Masha Allah Baba Na yayi kyau sosai yau dai anji sauki kenan tunda har Ka iya wanka".Kala bai ce Mata ba sai ma Irga yasun hannun shi da yake yi ganin sai Hamma yake yi hakan ya tabbatar

Mata da yunwa yake ji kitchen ta wuce ta jera mishi abincin shi a tray kamar ko yaushe sannan ta shigo da shi..tea ta hada mishi nan ta tura mishi abincin sai ya Fara ci tas ya cinye wanke mishi hannu tayi tana fita malam Na shigowa da Doctor'n shi saboda dole doctor ya duba shi don yadda ya Riga reacting jiya..

"Wallahi doctor Jibril jikin shi gaba yake ba baya ba jiya fa har bin mu da wuka yayi sanda muka Kira samari suka Kama mana shi".malam ya fada lokacin da suke sa Kai a dakin..

Check up ya mishi sai yace" ni dai banga wani matsala ba kuma condition nashi Ana samun improvement ".

" a'a Doctor gwara dai Ka fada mana gaskiya saboda Ku likitoci haka kuke ko kun tabbatar mutuwa mutum zai yi sai kuce da sauki".

"Da gaske fa nake malam Bari dai mu gwada shi".

Kallon Umar farouq yayi Wanda harga Allah kyau yake mishi yana kuma iya kokarin shi wajen ganin ya samu lafiya sannan yace" yau Kayi brush ne?"shiru yayi ba respond Amma ya kurawa Doctor ido sai Baaba tace"Ai Mun fada maka ba wani ci gaba".

"Nuna mini teeth's naka mu gani". Nan ya bude bakin sa kadan yana lumshe ido ya kuma bude su akan doctor ya nuna mishi teeth's nashi, da ido Doctor ya musu alamar ba kun gani ba sannan yace," Irga mini nan mu gani nawa ne?"

Ya fada yana ware yatsun hannun sa guda biyar ido ya tsurawa yatsun doctor sai kuma ya kankance ido kamar Mai irgawa da wuri ya hade yatsun hannun daman sa waje daya ya nuna mishi Wato biyar kenan.

."Alhamdulillah "Malam da Baaba suka fada a tare ganin Ehhh tabbas da sauki magana ne dai babu..

" Ku kwantar da hankalin Ku jikin shi Na sauki dama ciwo ke shiga lokaci daya sauki kuma sai a hankali batun abunda ya faru jiya kuma Abu aka shayar da shi that's why yayi ta hauka kamar ba gobe sannan hannun shi kuma jinin shi suka deba Allah ne kadai ya san me za'a yi da shi kuma don Allah a sanya ido akan shi sosai don ba'a San karshe wani irin Abu zasu mishi ba".

"In sha Allah Mun gode sosai Doctor".

" ba komai a dai Lura don kwanan nan ina yawan zama busy ba lallai duk lokacin da kuke bukata Na Ku same ni ba".

Ya karishe zancen da mikewa tsaye ya dauki brief case nashi nan malam yace,

"Lemme walk you out".raka shi yayi a gate suka gamu da autar su nan malam yace" yau kuma kin zo weekend ne".

"Ehh Baba Na same Ku lafiya"" lafiya kalau "daga nan Doctor'n yayan ta ta kalla tace " an wuni lafiya""lafiya kalau ya makaranta"

"Alhamdulillah" tace daga nan ta shige gida malam ko ya raka shi har mota suna Dada tattauna batun rashin lafiyar Umar Farouq..

A falo taga Baaba da gudu ta fada jikin ta tare da rungume ta"ke lafiya Na Gan Ki a gida ko waya babu?"

"Baaba gani nayi week nan ba Wanda ya Kai mini visit kowa iyayen shi sun je shine nace Bari dai nazo Na duba ko lafiya".

Zama suka yi Baaba Na fad'in, "ina ko lafiya 'Yar nan jikin yayan Ki dai bana kam tsam yaki yarda don har dauke sa aka yi ya kwana daya to fa tunda aka dawo da shi sai sabon hauka".

" innalillah ya Allah Ka bawa yaya Na lafiya wallahi Baaba kullum buri Na bai wuce ya samu lafiya Nima nayi alfahari da shi kamar yadda ko wacce kanwa ke alfahari da yayan ta sannan ya Riga Kai mini visit makaranta".cikin jimami Baaba tace,

"Lamarin ne tsam ni ban ganin wani cigaba duk da kuwa Doctor cewa yake lafiya yake samu to ina lafiya tunda baya magana kuma har ila yau in yaji hayaniya kadan Shikenan har illata kan shi yake yi".

Hawaye ta share tace" Allah yana sane kuma zai saka mishi sannan zai Toni asirin magautan shi a duk inda suke mutum ba wani Mai kudi ba sannan ba 'Dan kowa ba Amma ace an sa rayuwar shi a gaba basu da burin da ya wuce suga Bayan shi".

"Kinga bar zancen nan Kije Ki ajiye hand bag naki".

Da yake tana da kaya a gida indai weekend zata zo to daga ita sai hand bag nata Wata ran kuma da purse ma take zuwa musu

"Baaba ni sai naga yaya Na tukun"ta fada tana shiga corridor'n knocking Na dakin shi tayi taji shiru sai ta bude tare da cusa Kai tana fad'in "suprise"a hankali sanin bai son hayaniya, mikewa yayi daga kwancen da yake sai tayi murmushi tace"nasan yaya Na love suprised shiyasa Na maka".

Fuskar sa dai ba zaka gane yana farin cikin zuwan ta ba ko a'a Amma yadda ya kura Mata ido Ka San lallai akwai shakuwa tsakanin su karasawa tayi ta zauna bakin gadon tana kallon shi tace, "so yaya Na kallon TV yake yi" yanzu ya ciro idon shi a kanta remote ta dauka tare da Fara scrolling nan ta sauya channel inda Tasa karatun qur'ani volume dan kadan sannan ta mike dakin ta Fara gyarawa sanda ta gyara ko ina tsab ta wanke bandaki ta fesa room freshener karatun Qur'ani Na tashi a hankali zuwa lokacin bacci ya Fara fisgar sa ita ko zama tayi a bed side drower tana karanta novel a wayar ta..

In har tana gidan to ko bacci yake yi ita gadin shi take yi basu rabuwa sai lokacin bacci shiyasa duk wani abunda zai faru da shi to a Bayan ta ne..tana Wa yayan nata son da bata yiwa kanta kasancewar shi mahaukaci Wanda ko magana baya yi..bacci

yayi ita ko kallon shi tayi tana murmushi don yayan nata kyakyawa ne duk wanda ta same shi matsayin miji kuka taji dadi ci gaba da karatun ta tayi nan malam ya shigo da Kayan shi da aka dawar daga wanki jera masa tayi a wardrobe nashi..

**

Washe gari da safe suna zaune sai kawai taga an Fara shigo da abinci iri-iri ko wanne da bangaren da yake fitowa..abincin da aka Fara shigowa da shi kanwar Dada ta bude doya da Mai da yaji ne sai Na biyun jollof Na Rice ne Amma bai ji manja ba wani gefen fari wani gefen kuma ja.surkuwar Dadda kuma dumame tayiwa Dadda saboda ta San tsohuwar ba iya cin komai take ba sai tuwo ko maltina sai tayi dankalin hausawa da Mai da yaji ta kawo Wa su Dada..duk kwanukan abincin sanda suka bude sai tsoffin gidan su ma sun shigo da safen su duba jikin Dadda da yiwa Dada sannu da zuwa..

"Dada Ki kawo kudi a saya mana kosai a kofar gida don ni duk abincin nan ba Wanda ya mini ko Mai bai ji ba kusan kullum shi mutum yake ci" kudi ta bayar aka saya musu kosai da biredi sai koko da tace tayi kewan Na jalingo breakfast suka yi Bayan sun gama sai kanwar Dada tace"Dada tunda har Allah yasa kunzo ni Zan koma gida Na don Na bar yara kawai kullum Zainab ke musu abinci kafun su tafi sannan sai ta dawo take musu Na dare".

"Wato dai har yau ke da wannan kishiyar taki zaman doya da manja kuke yi".

" hmmm Ki Bari fa Dada wallahi yanzu kam kowa girkin sa yake yi koda nazo nan mijin mu yace take Sawa yara Na breakfast ba sai Zainab ta tashi ta musu ba tace Ai lokacin da muka yi fada ni Na Fara cewa a raba mana girki don haka ba zata sa ba".

"Ni fa nafi ganin laifin mijin Ku saboda shine Mai fada Aji Amma ace kuna abunda ran Ku yake so".taji haushin abunda Dada ta fada don ita tsam bata son laifin mijin ta shiyasa tace

" Dada wallahi ina hak'uri da ita ba tada mutunci fa".

"Ai Kinga matsalar Ki duk inda Kika zauna sai kin aibata ta ita ko ba haka take yi ba shiyasa tafi Ki ta wannan bangaren"

Shiru tayi saboda tasan tabbas kishiyar ta tafi ta iya siyasa don ita auren dole aka Mata da mijin nasu kuma ita ce uwar gida tana haifan 'Dan ta Na fari ya auro kishiyar ta wayeyiya iya shege iri iri take Mata kullum gasu a dambe yanzu da yaran su suka girma ne suka daina..

Karfe sha daya Zainab tazo tayata kimsawa da yake yau weekend ne ba school nan taga Laylerh sai tace"Dada bakuwa Kika kawo mana ne?""Eh Zainab kin ga ba zata wuce sa'ar Ki ba ko Ki girme ta da kadan".

Ehh fa ya sunan ta".hararar ta Dada tayi tace

"Ki tambaye ta zata fada miki" kan ta tambaya Laylerh tace"suna Na Laylerh ".

Murmushi tayi tace" Ashe tana da fara'a"..

"Kinga Zainab zo maza Ki Kira mini yarinya daya cikin yan matan gidan nan Na aike su kasuwa su mana shefenan dare don nasan dole yau nice Zan karbi girki".

"Wato dai har yau mijin Ki baya barin yaran shi su shiga kasuwa".

" ina yake Bari su fita ma bare shiga kasuwa ".

" Laylerh zo muje"kallon Dada tayi sai Dada ta Mata alama da taje, sai yanzu ta samu damar karewa gidan kallo tabbas gidan talakawa ne sashin da suka Fara shiga a baranda suka tarar da budurwar da zani a kirji tana zaune tana kwalkiya

"Zainab yau ke ce a gidan namu"

" Eh wallahi dama mama Na ne tace nazo nace Kije Mata kasuwa"

"Cabb dubi can Kinga geda Na ya dahu yanzu Zan tafi talla"

" to Shikenan sai Anjima" ta fada tana Kama hannun Laylerh suka fita.. sashi Na biyun kuma a jikin kyaure suka tarar da yarinyar daga ciki suka ji Maman ta Na cewa

" tunda kince baki ji wallahi yau Zan ga abunda zai hanani cin uban Ki a gidan nan har ni zance ba zaki yi anko ba Ki nuna mini Ai ba kudi Na bane".suna jin haka ko karasawa ciki basu yi ba suka juya zuwa wani sashin nan suka tarar da yarinyar ta gama wanke wanke Maman ta Na zaune a baranda gaishe ta suka yi sai Zainab tace

"Dama mama nane tace Dan Allah maryam tazo taje Mata kasuwa".kan Maman tayi magana maryam ta Riga tace,"Ayya Kice akwai inda...."bata karasa ba Maman ta tace

"Kinga bana son abun magana yanzu ace ni Na hanaki wuce Kije Mata"

"to kuce ina zuwa Bari Na wanke kafa Na ".

Ficewa suka yi inda suka koma bangaren Dadda nan suka ce tana zuwa ba bata lokaci kuma sai Gata tazo gaishe su tayi da tambayar jikin Dada sannan tace a bata kudin nan Dada tace

" Maryam kuje da Laylerh don in kun tafi makaranta sai take zuwa mana aika ".

Haka ko aka yi napep suka tare sai kallon hanya Laylerh ke yi sun zo kofar sarki kenen ganin gate din a bude ga dogareye da jajayen kaya sai tace

" Maryam nan ne gidan sarkin garin Ku?"

"Ehh Ai Na manta ke bakuwa ce ban nuna miki wuri ba".

Tafiya su Ka yi sai gasu a bakin kasuwa inda cinkoson ababen hawa yayi yawa a layin yan nono suka sauka Laylerh sai kallon su take ganin su dayawa ko wacce da kwallan Nonon ta a gaban ta tana fadin"Nono ne zo ga Mai kyau".shagala tayi da kallon su sanda Maryam taja hannun ta, ta karamin gate suka shiga kasuwan..

Comment

Share

©Hafciey Musa

[1/25, 5:36 AM] Hafciey Musa😘: *□LAYLERH□*

(The prettiest emerald)

Page 15

Shefene suke yi ita ko duk layin da suka wuce sai tayi ta kallo ba Wai kuma don kasuwar yafi inda ta baro kyau da girma bane a'a tsarin su ne daban daban suna fita Maryam tace"yanzu ba gida zamu wuce ba dama Inna ta ta ce Na biya gidan addana Na karbo Mata kulan ta".

"To Amma kin fadawa su Dada ne?" Ta tambayi maryam din tana kallon ta

"kada Ki damu Inna ta tace zata fada musu"

daga nan keke napep suka tare da fad'in "Nana Aisha zamu je Mai keke"

"Ku shiga". Shiga suka yi nan suka nufi Nana Aisha suna zuwa ya tsaya a junction sai Maryam tace" Ayya yaya Na ciki zaka shigar da mu".

"Nawa zaku bada?"

"Muna da Dari da hamsin"

"Ba zai yiwu ba Ku bada Dari biyu Na shigar da Ku".

" shine abunda yake hannun mu".cikin masifa yace

"To Ku biya ni kudi Na Zan wuce".

Naira Dari suka bashi nan suka Fara shiga ciki da kafa Laylerh sai kallon gidajen wajen take yi sunzo dai dai wani gida tace

" Masha Allah ai in mutum ya samu wannan gidan ya more".

ita dai maryam bata ji me Laylerh din tace ba kuma inda sabo ta Saba wucewa ta gidan don haka ba sabon Abu bane a wajen ta..har suka yi nisa Laylerh bata daina waiwayar gidan ba karshe ma juyawa tayi gaba dayan ta tana kallon gidan cikin zafin nama Maryam tace

"ke masa mota Na zuwa".kan ta rufe bakin ta motar ta take birki da karfi sai ji kake kiiiii har tayar ta ta cize gwiwowin Laylerh Na manne da gaban motar.. Sosai zuciyar ta ke bugawa a take ta hada gumi don ba don yadda driver ya take birki ba da tata ta kare yau.. driver'n shi ne ya fito yana fad'in

"Yar kauye kawai tana tafiya bata kallon gaban ta yanzu in mutum ya buge Ku ace an zakunce ku".cikin takaici ta dago idanun ta da kwalla ya gama cika su kiris kawai take jira su zubo tace

" dakata malam Kai da Ka kusa buge ni baka ce mini sannu ba sai wani holo kake mini ".

Bude kofar motar yayi ya fito driver ko cewa yayi

" taki ta kare yarinya".sanye yake cikin kananan kaya yayi kyau sosai maida marfin kofar yayi ya rufe cikin kasaita ya karaso gaban ta saboda tsarai yaji me tace kuma Ai ita din ba yarinya bace bare ace yaranta Na damun ta, budurwa da ita ta tsaya yiwa mutani rashin kunya to ko zai saita Mata hankali daga hannu yayi ya mare ta sannan ya juya ba tare da ya kare Mata kallo ba

"Allah ya isa Na mugu kawai wallahi gaba Allah zai hadaka da Mai rama mini don kawai kun ganni yarinya shine zaku yi ta zalunta Na".ta karishe zancen tana fashewa da kuka Cak ya tsaya ba tare da ya juyo ba this is the first time da mace tayi embracing nashi sannan kuma yarinya, dunkule hannun shi yayi ya naushi iska sannan ya furzar da Iska a bakin shi cikin zafin nama ya juyo Gare ta ya daga hannu kenan sai ya tsaya cak saboda sauke idon shi da yayi akan ta yana kare Mata kallo..

Tabbas duk da ya dau shekaru bai Gan ta ba kuma ta sauya dayawa ta koma local Amma fuskar ta Na nan yadda yake kamanni bai canza ba

"me yasa Ka tsaya mare ni mana".

Idanun shi ya lumshe ya sake bude su akan ta sannan ya girgiza Kai yana fad'in,

"Driver let's go".

tsam ba haka driver yayi tunani ba don wallahi a ganin shi yau me raba oga'n shi da yarinyar sai Allah shiyasa yana shiga mota ya watsa Mata ruwan wajen da yake a damuna hanyar bai fiya kyau ba ruwa Na taruwa sai yace

"Ranka shi dade meyasa Ka barta Bayan zagin Ka da tayi".

"Hmm abunda yafi haka ma zata iya aikatawa".

" Ka San ta ne?"

"Yeah Tun tana yarinya munyi school daya da ita".daga nan ba Wanda ya sake cewa komai suka cigaba da tafiyar da suke yi...

A bangaren su Laylerh ko maryam tsayawa tayi tana kallon Laylerh wannan rashin kunya haka sai kace 'Yar Bayan kasuwa ita ko hawaye take sharewa tana karkabe jikin ta da driver ya watsa Mata ruwa, dago jajayen idanun ta tayi ta dubi Maryam tace

" haka mazan garin Ku suke ba imani bare tausayi ".

" yanzu ke me nayiwa babba rashin kunya ".tana hawaye tace" to baki ga da nayi shiru wani Marin zai sake mini ba".

Jan hannun ta tayi suka cigaba da tafiya tsam Laylerh bata gane shi ba da yake ya canza sosai kuma bata tsaya kare mishi kallo ba,suna isa gidan Addan maryam ta dube ta tace"me kuma ya samu Kawar taki da girman ta take kuka a hanya".

"Diddi wallahi wasu ne suka kusa buge ta don sun mare ta sai ta hau musu rashin kunya".

" ke Amma bakuwa ce ko?"wacce aka Kira da Diddi ta tambaya

"Ehh Diddi Dada ce tazo da ita".

" to Ki bi mazan jalingo a hankali saboda ba Daukan raini suke yi ba sannan in wani ya bar Ki,ki sani wani ba barin Ki zai yi ba rashin kunya kuma ba inda zai Kai Ki".

"To Na gode".tace cikin jin haushin maryam

" Maryam me ne ya kawo Ku naga da ledar shefene a hannun Ku".

"Daga kasuwa fa muke Inna ce tace Na biya Na Karba Mata kulan da ta Kai muku abinci a asibiti lokacin da Yar Ki ta kwanta tunda kin Ki maida Mata cooler'n ta".

" Kai Inna abunda kulan ma ya tsufa shine Harda Baku Na machine kuzo Ku Karba".hutawa suka yi nan ta basu cooler'n tare da naira Dari tace su cika Na machine a hanya suka gamu da kawun maryam yake tambayar su ina suka fito nan suka fada mishi sai ya basu Dari Wai su hau machine kallon Maryam tayi tace"Ayya in Mun Kai gida kada Ki fadawa kowa abunda ya faru".

"Baki son kowa ya San rashin kunyar da Kika yi ne?" Kai ta gyada alamar Ehhh sai Maryam tace"to Shikenan Na miki alkawarin ba Zan fadawa kowa ba in zaki bar mini darin Ki".

"Dari Na kuma?"

"Eh mana Kinga Diddi Na ta bamu Dari kawu Na ma ya bamu Dari Kinga ya tashi Dari biyu kenan zamu dauki Dari Dari in kin yafe mini rabon Ki ba Zan fadawa kowa ba".

Ba don ranta yaso ba tace" Shikenan Na bar miki"a zuciyar ta ko cewa take ko zata yi kawance da yaran gidan to ba zata yi da Maryam ba don ta fiya son duniya haka kawai ma ta Fara jin haushin Maryam din...

**

Tray'n breakfast nashi ta gama shiryawa nan tace "Baaba Bari Na kaiwa Yaya breakfast"

"To kanwar yaya". Murmushi tayi gami da Daukan breakfast din ta nufi dakin shi da shi nan tayi knocking sai taji shiru tura kofar dakin tayi tana fad'in" breakfast ".

Ido ta ware ganin ba kowa a kan bed don haka ta karasa dakin ta ajiye abincin akan center table tana murmushi tare da fad'in"nasan yana toilet" zama tayi a bakin gadon tana kallon TV dake aiki shi kadai an bar shi a channel Na cartoon Kai ta girgiza tare da mikewa ta nufi wajen TV'n remote ta dauka tana fad'in "yan gidan nan da ban haushi suke,su ke maida yaya mahaukaci wani lokacin banda haka ina za'a Sawa Babban mutum kamar shi cartoon".

Channel Na Saudi ta Kama ta dawo ta zauna tana Dan pressing wayar ta jin shiru har yanzu bai fito ba sai ta nufi kofar toilet din tayi knocking ga mamakin ta sai taga kofar a bude yake nan Tasa hannun a Kai da gudu ta fice zuwa tsakiyar falon tace," Baaba wallahi yaya baya daki".Baaba dake yanka albasa sanda wuka ya yanke ta bata damu ba ta mike tana fad'in "baki duba dakin da kyau ba".

Dakin suka nufa dukkan su sai suka ga ba kowa nan tace" yi maza Ki Kira Baban Ku ya dawo gida mu San nayi to Ince kina tare da shi".

"A'a kin San bana shiga dakin shi da sassafe yanzu ma wanka nayi shine nazo daukar breakfast nashi" ta karashe zancen tana hawaye nan tayi dialing numbern malam Baaba ko sai safa da marwa take yi a falon ringing biyu Ana uku ya dauka nan yace"lafiya kuwa naga ban Dade da fita ba".

Fusge wayar Baaba tayi tana fad'in "Kayi sauri Ka dawo bamu ga Umar Farouq ba". Tana gama fadin haka bata jira amsar shi ba ta cire wayar a kunnen ta tare da Mikawa Auta ita ce ma ta katse kiran..cikin minti talatin sai Gashi a gidan hankalin shi a tashe nan suka fece waje Neman shi kowa ya Gan su ya San basu tare da nitsuwa ita kanwar shi kam ma kuka take yi nan fa jama'ar anguwa suka shiga tayasu Neman shi kamar ko da yaushe Amma babu shi babu alamar shi gida suka dawo zuwa yanzu Baaba ma hawaye take yi" koma Wa yake aikin nan ya ishe shi haka saboda wannan shine Karo Na karshe da za'a shigo har gida Na a dauka mini d'a".

"Baba wallahi don Baku Daukan mataki ne shiyasa". Cewar Auta ficewa malam yayi a gidan ya nufi fadan Mai anguwa yako yi sa'a yana nan da cabinet nashi da yake

safiya ne hannu ya mika musu dukka suka gaisa sannan ya koma ya zauna yana fad'in" ranka shi Dade wallahi matsala ce ke tafiye da ni".

"Allah sarki batun Yaron wajen Ka ko don Tun dazun labari ya iso ni".

" Ehhh wallahi abun ya ishe ni haka Rainin wayon yayi yawa don Ana son ganin Bayan shi har gida fa ake shiga a dauke shi Gashi da an dawo da shi haukan sai ya ninka Na da Na rasa me suke mishi ni wallahi gwara su gama da shi a take akan wahalar da rayuwar shi da ake yi saboda suna killing nashi slowly ne".

Duk girgiza Kai suka yi alamar tausaya mishi sai wani yace"yanzu me kake ganin ya dace ayi?"

"So nake a sa ido akan masu shiga da fitan anguwar nan".malam ya fada Kai tsaye

" wannan shawara ce Mai kyau dole samarin anguwar nan su sa ido don baki Na yawan shigowa da yake Rabin yaran namu yan shaye-shaye ne su ke kawo abokanayen su".

Cewar Mai anguwa nan ya bukaci a Tara mishi duk matasan anguwan haka ko aka yi kowa ya hallara a wajen sai aka bude taro da addu'a nan yace"ba komai bane yasa Na Tara Ku a nan sai don mu magancewa Dan uwan mu damuwar shi nasan duk kun San dan shi Mara lafiya sannan kun San akan zo har gida a dauke shi don haka nake so duk Ku sa hankalin Ku akan baki dake shiga da fita a wannan anguwar don tabbas Wanda ya San shine ya kuma San anguwar yake wannan aikin".

Yana gama jawabi Wata bakar mota ta wuce da gudu duk da ido suka bi motar sai malam yace

"wallahi ban yarda da motar nan ba dube ta fa baka Mai bakin glass".

"To maza kuje Ku duba" aka ce da samarin anguwar nan suka mike cikin hanzari ko da suka isa k'ofar gidan shi basu ga motar ba da yake akwai Dan nisa tsakanin

gidan shi da Na Mai anguwa sai dai tabbas alama ta nuna mota tayi parking a kofar gidan da yake yashi ne kana kallon tayar motar yadda yayi reserve nan suka shiga kiran waya ma anguwar dake kusa da su kan cewa su sa ido in Wata bakar mota Na wucewa ko plate number'n ne a samu a dauka musu Amma kowa cewa yake Ai ta wuce wasu ko suce basu gani ba..

Cikin gidan suka wuce sai ya tarar da Baaba da Auta a falon zaune duk sunyi tagumi sai malam yace"basu shigo da shi bane?"

"Wa kenan" Baaba ta tambaya tana mikewa tsaye nan yace"kun duba dakin shine?"

"A'a". Duk dakin shi suka wuce da samarai din sun duba ko ina baya ciki sun juya zasu fita sai suka ji karan fashewan abu a toilet da wuri suka nufi toilet sai akaga shine ya tarwatsa mirror da hannunshi blood Na dripping, Bayan in the first place Auta da Baaba sun duba basu Gan shi a toilet din ba..

Koda suka tunkaro shi sai ya nufo su suna Komawa da baya har suka shiga daki,karfe ya dauka a toilet din ya Fara dukan duk Wanda ya samu a kuma inda ya samu har fasawa wani Kai yayi ba yadda basu yi ba wajen ganin sun danne shi Amma suka gagara ganin yayiwa mutum uku illa yasa su fita a gidan da gudu shi ko rufa musu baya yayi daidai sun gama fita malam yasa Wa kofar sakata shiko da yake ba hankali Gare shi ba da ya karaso wajen sai ya Fara buga kofar har kamar zai balla da gudu kanwar shi taje ta jingunu da kofar tana kuka tace

" yaya so kake Ka tabbatarwa duniya Kai din mahaukaci ne kamar yadda kowa ke fadi Dan Allah Ka bar su haka kazo mu tafi Na tsani ganin Ka a wannan yanayin sannan ba Zan daina jawa Wanda ya jefa Ka a wannan halin Allah ya isa ba"kuka take sosai har ta durkushe a kasa nan ya yarda abun hannun shi ya juya da wuri ta mike tabi Bayan shi daki ya shige su malam duk da ido suka raka shi a bakin gado ta tarar da shi zaune nan ta wuce toilet ta hada mishi ruwan wanka sannan ta mishi nuni da bandaki sanda ya jima kan ya nufi bandakin yana shiga Baaba Na shigowa nan tace"Allah miki albarka wallahi da mu ne ko zamu kwana ba tashi zai yi ba"

"Baaba wallahi wani lokacin sai naji kamar kada Na koma makaranta saboda yaya rayuwar shi Na cikin hatsari".shiru duk suka yi suna jiran fitowar shi..ba yadda ba'a yi da shi ya tsaya a tsaida jinin da ke zuba a hannun shi ba yaki haka jinin yaita

zuba har ya tsaya da kan shi,duk da yayi loosing blood sosai Amma ba ko alamar dizziness a tare da Shi..

A waje ko malam ne ke bawa matasan hak'uri tare da Kai su chemist a musu jinya nan suka ce su dai ba zasu sake shiga gidan shi ba Amma sunyi alkawarin gano masu Daukan Dan shi..

Wasa gaske sai Gashi yayi har hour a bandaki bai fito ba nan hankalin su ya tashi za'a Kira malam kenan sai Gashi ya shigo nan Baaba tace

" Dan Allah shiga bandakin Ka duba mana ko lafiya Tun dazun fa yake ciki".

bandakin ya nufa ya tura zai shiga sai Gashi ya fito sanye da bath robe idanun shi jajazir ficewa suka yi a dakin suka bar shi da malam ya taya shi shiryawa nan kanwar shi ta sake kawo mishi breakfast yau kam dai yaci kila basu bashi abinci ba Amma kalar idon shi yafi Na kullum har tsoro abun ya basu Gashi sun Kira Doctor line nashi baya shiga..

Gado ya hau ya kwanta yana lumshe idanu alamar bacci ita ko tattare wajen tayi ta dawo dakin yau ma a bed side drower ta zauna tana karanta book nata Na jiya..

Doctor ne yazo cikin sauri da alama yana aiki suka tashe shi nan ya duba shi sai cewa yayi yana lafiya and even ready to donate blood sosai abun ya basu mamaki upon all jinin da ya zubda ace ba abunda ya same shi nan ya musu sallama ya tafi..

**

A junction Mai keke ya ajiye su nan suka shiga ciki da kafa yanzu dai ba ta ce da Maryam komai ba don haushi take ba ta a haka har suka isa gida nan maryam ta ajiye musu chefenan su sannan ta nufi bangaren su, Dada ko kallon Laylerh tayi tace"me ne kika wani bata rai".

"Babu" tace Amma Allah ne kadai yasan haushin darin ta da take ji nan dai Maman Zainab ta dauki chefenan ta don dama ta gama shiri su take jira ta sallame su Zainab Na tambayar Dada yaushe Laylerh zata je gidan su tace Ai suna nan har sai sun gaji da Laylerh din nan suka tafi..

Kunu Dada ta deba a flakes ta Mikawa Laylerh tana fad'in "bawa Dadda Bari Na shiga wanka Tun dazun nake son shiga in Na fito Zan baki kudi Ki saya mini carty a shagon kofar gidan nan Na Kira can wajen su Naseer".

" to"tace sannan ta karba kofin jin an Kira Naseer kuma sai ta nemi nitsuwar ta ta rasa gaba daya hankalin ta ya koma kan shi ganin kunun yayi sanyi sai ta shiga bawa Dadda nan Dadda ta Fara bata labarin lokacin da take yarinya dariya Laylerh ke yi suna cikin hirar taji wayar Dada Na ringing mikewa tayi nan taga "Naseeru" rubuce a screen Na wayar kuma tabbas tasan Naseer nata ne don Naseeru Dada ke kiran shi har wayar ta kusa tsinkewa sai ta zauna kan katifar dakin tayi receiving tare da fad'in "Salamu alaikum".

" Jan Aji ko ba damuwa Wa'alaikisalam".ya fada yana lumshe idanun sa,da sauri tace,

"A'a fa ya Naseer ba Jan Aji bane?"

"To mene ne shi".

Cikin yin kasa da murya tace" Babu".

"Dubi bakin ta a wajen kamar babu in Na Kama bakin cizewa Zan yi".

Yarr haka taji a jikin ta duk tsikar jikin ta tashi yayi shiko Allah ya sani bada Wata manufa ya fada ba nan ya kuma cewa

" ya jalingo ina fatan ba Wata matsala ko".cikin kasalar da ya saukar Mata tace,

"Babu komai in fact ina jin dadin zaman wajen ba don wani Abu bama da ba Zan dawo garin Ku ba".

" iyehh fada mini mene ne wannan abun da zaki dawo domin shi".

"Babu fa".

" Ayya dai Ki fada mini mana".ya fada yana marairaicewa nan tace

"da gaske nake babu".

"To Shikenan tunda ba zaki fada mini ba dama wani Abu Na ajiye miki kuma Na fasa baki".

" rowa ba kyau fa".

"To ba ke Kika Fara ba".

Kan tace wani Abu Dada ta shigo dakin nan tace

" ga Dada ".

Kai Dada ta daga Mata alamar Waye ne sai tayi murmushi kawai tana Mikawa Dada waya nan taga Naseer ne gaisuwa suka yi nan yake ce Mata bai ji dadi bane shiyasa bai Kira su ba "ayya ba komai wallahi Mun gode ya jikin".

" Da sauki".

Daga haka suka yi sallama..

A bangaren shi kuma gaba daya daurewa yake yi don sosai yake jin jiki saboda yanzu haka shiri yayi hospital za'a Kai shi..Hajiyar sa ce ta shigo dakin tana fad'in" Ka gama ne?"

"Ehh mu tafi".tafiyar ma da kyar yake yi nan suka nufi hospital da Mom nashi take insisting akan su je da yake sun nemi ganin Doctor sai basu wani sha wahala ba duba Naseer din yayi sannan ya bashi gado..

Cikin sauri aka sa mishi drip har guda ukuWanda bana masu diabetes ba Bayan wani lokaci numfashin shi ya Fara sama-sama he is fighting for his life ganin haka sai Dad nashi yace" Anya ba wani abun kuka yi mishi ba kasan fa yana da diabetes ".

Instead of su karbi laifin su sai doctor'n yace" Sir we know our work don haka Ku bamu waje zamu yi aiki".cikin mutuwar jiki duk suka fice a dakin nan jikin doctor's din ya Fara rawa oxygen aka dauko za'a sa mishi sai kuma numfashin ya Fara seizing nan wani doctor yace"me zaku yi ne? "

"Oxygen muke son sa mishi".

" wannan Ai ba zai tashi ba da alama rai zai yi halin shi fa".

Tsam Baku comments😟

Comment

Share

©Hafciey Musa[1/25, 5:37 AM] Hafciey Musa😘: *LAYLERH*

(The prettiest emerald)

Dubawa suka yi da kyau sai aka ga yana da rai nan aka bashi duk wani taimako da ya kamata har yayi gaining consciousness sannan aka mishi alluran bacci tare da cewa a bar shi ya huta...

**

Da dare zaune suke a dakin Dadda su hudu inda Dan Dadda Auwalu ya shigo domin gaisawa da Dadda da kuma yiwa 'Yar uwar shi sannu da zuwa Bayan sun Dan taba hira sai Dadda ta tambayi Dada inda ta samo Laylerh nan ta bata labari yadda Naseer ya bata sai Auwalu yace"Allah sarki kenan in kin tashi Komawa tare zaku koma?"

"Gaskiya ni so nake Na bar Laylerh a nan saboda ita kan ta shaida ne yadda yan gidan Alhaji suka juya mini baya akan ta saboda a tunanin su Naseer son ta yake yi sannan Nike goyon Bayan alakar su don haka ta zauna a nan din kawai ta nemi sana'a don Gata nan Masan da muke yi a can din kullum ba wani riba sai fadiwa".

kallon Laylerh Auwalu yayi sannan yace"kina son zama a nan din ne?"

Tabbas tafi son zaman jalingo don ta Lura gidan akwai sakewa ba'a takurawa yaro sannan kuma ga yan Mata sa'o'in ta a gidan Amma can kuma Naseer take so shiyasa tayi shiru sai Dadda ne cikin muryar su Na tsoffi tace"to in ta zauna a nan din wani sana'a zata yi?"

"Ina ga ko doya da kwai ne sai a ringa daura Mata tallan shi".

" tayi karatu ne?"Auwalu ya tambaya

"Eh ba laifi ta taba kadan".

"In ko haka ne akwai wani aboki Na da yake aiki a gidan gona yace mini in akwai yaran Mata da suke bukatar aiki a gidan mu to Na mishi magana don suna Neman ma'aikata shiyasa Na bada sunan Nabeela da yake ita naga tayi karatu".

Nabeela jikar Dada ce mahaifin ta ya rasu mahaifiyar ta kuma tayi Aure a gombe shiyasa ta barta a gidan Dadda to yanzu dai bata nan tana gidan wani Bappan ta

" to alhamdulillah Ai gwara ita ma taje can din da zaman banzan da zata Riga yi".

"Wai gani nayi Kunce ko tallah ne Ai".

" banda abunka Auwalu ga aikin da zata Dan samu Wa yake batun talla kaga ko Na koma zata iya daukar nauyin bukatar ta da kan ta ba sai wani ya taimaka Mata ba".

"Haka ne Zan mishi magana in sha Allah dama gani nayi 'yan matan gidan nan kam kowa sana'a Tasa a gaba kuma ba wani karatun kirki suka yi ba shiyasa".

" to Dan Allah Ka taimaka Ka mishi magana a gobe mu San square root namu".

"In sha Allah" yace sannan ya musu sai da safe ita dai shiru tayi tana tunanin mace kuma wani aiki zata yi a gidan gona Gashi bata da bakin magana saboda Naseer yace tayi biyayya ga Dada shiyasa tayi shiru..

Washe gari kamar yadda Auwalu yayi alkawari sai Gashi yayiwa Abokin shi magana akan ta da yake already an gama na Nabeela zuwa ne kadai bata fara ba nan aka ce Monday ya kawo ta interview murna wajen Dada ba'a magana ita kan ta taji dadi ko ba komai she will stand on her own..

Time da suka je interview din ba laifi Anga she can read and write sannan ta iya turanci wannan reason yasa aka ajiye ta a admin block under accounting ita zata ke

musu typing list Na shiga da fitar kudin su da sauran abubuwa ma'ana ita din typists ce..

Bata taba jin farin ciki irin ranar ba don gidan gonan ba karamin kyau ya Mata ba Gashi komai is well arranged har ma ta raina kan ta don tana jin bata Kai matsayin da zata yi aiki a wajen ba..

Sun bar wajen Bayan ance Mata Wednesday zata Fara aiki aiko har suka fita a farm gate din bata daina bin wajen da kallo ba Bayan fitar su sai ta dubi Auwalu tace"Na gode sosai Allah saka da Alkhairi".

"Ba komai ke ma Ai 'ya ce a Gare mu kamar maryam".

Nyamusa fuska tayi a zuciyar ta ko cewa tayi" Wato shine Baban yarinyar nan me shegen son kudi".nan suka nufi gida suna dawa ta Fara bawa Dadda labarin yadda gidan gonar yayi kyau haka ma Dada yau dai tsam taki gajiya da yaba wajen, kuma kowa ya tambaya zata sake fada mishi har dariya suka Fara Mata ganin haka ne sai ta nitsu Amma ji take yi har Wednesday ya Mata nisa Ai ina ma ace gobe ne zata Fara aikin da sai tafi kowa farin ciki..

Ran Tuesday ta tattara Kayan ta dukka ta Fara guga da yake Tun jiya tayi wanki sosai ta goge su ta jera gobe kawai take jira a ranar kuma Nabeela ta dawo ganin kamar yarinyar bata da matsala nan dai suka Dan Saba tunda dakin su daya..ran Wednesday da sassafe suka tashi kowa ya hau shiri da yake a sashin Dada ba girki ake yi ba bare suce zasu yi aiki..

Riga da skirt ta saka sai well ironed hijab nata nan ta fice a gidan ta nufi dakin wani saurayi Wanda shima jikan Dada ne knocking tayi sai yace"Waye ne"

"Nice Laylerh".

" uhum me kike so?"

"Ayya dama zuwa nayi Ka Dan mini turaren Ka Na fesa kaga yau Zan Fara zuwa wajen aiki".

" iyehh sannu kin San nawa turaren nan? "

"Aikin banza Arabian oud ne fa ce maka aka yi ban sani bane?"

"Ashe dai a kauyen Ku kun San har Arabian oud".

" Wai ni waya ce muku daga kauye nake kaga in zaka bani Ka bani in kuma ba zaka bayar ba nayi tafiya ta".duk maganar da suke yi ita tana waje shiko yana ciki kaya yake Sawa shiyasa bai fito ba yana gamawa ya fito da turaren nan ya mika Mata fesawa ta Fara yi ganin zata karasar mishi sai ya fisge abun shi yana fad'in "ina ruwan an samu Na banza".

" kaga kwantar da hankalin Ka in sha Allah ina karban salary Na Na farko Zan saya".tana gama fadin haka ta juya gaba daya she is eager taga sun tafi koda ta koma side Na Dadda sai ta tarar Nabeela ma ta gama shiri nan Dada tace Laylerh taje ta dubo musu Auwalu..

Bangaren shi ta nufa matar sa ta tarar zaune a kan kujera a tsakar gidan da alama mutumiyar ta maryam bata gidan nan ta dubi ta tace"ina kwana innar maryam".

"Lafiya Laylerh an aike Ki ne?"

"Ehh dama Dada ce tace nazo Na duba ko ya gama sai mu tafi".

" Ayya yana wanka Ai Ki zauna Ki jira shi"

Daga hijab nata sama kadan tayi sannan ta zauna a bakin barandar nan innar maryam taci gaba da jin novel nata tana aiki sai Laylerh tace"Allah ni sai nake ganin kamar abunda ba Zan taba iyawa ba kenan jin novel ko karantawa ".

" hmm baki Saba bane shiyasa ".

" to malama Laylerh har an shirya?"Auwalu ya fada lokacin da yq fito daga bandaki hannun shi rike da kwandon Soso

"Eh ina kwana"

Ta fada tana Dan durkusawa daga zaunen"lafiya kalau kinzo Kira Na ko?"

"Eh"" to Ki bani minti goma ina zuwa".mikewa tayi ta fice nan ta koma sai ta fadawa Dada abunda yace"to Ku jira shi yanzu zai fito".

kamar yadda yace bai fi minti goma ba sai Gashi ya fito sallamar yayar shi da Mamar shi yayi nan suka nufi fita a zauren gidan ya dube su yace"kun karbi kudin machine kam?"

"Eh nikam Bappa Na ya bani Na sati" Cewar Nabeela kallon Laylerh yayi yace"ke fa?"Kai ta girgiza mishi sai yace"to je Kice uwar dakin Ki ta baki".

da sauri ta juya ta nufi gida Nabeela ko waje ta fita shi kuma jiran ta yayi a zauren..

"Dada Wai Inji Baban Maryam Ki bani kudin machine".

Sha'anin Ka da 'yan uwa masu bin juna dama ba shiri suke yi ba sai cewa tayi" Kije Kice in ba zai biya miki ba ya Bari kin hakura da zuwa ".

cikin sanyin jiki ta juya nan ta sanar da shi ga mamakin ta sai yace" to sai Ki koma gidan Ai".yana gama fadar haka ya fice nan take idanun ta ya cika da hawaye don ita a zaton ta zai biya Mata da wuri ta koma cikin gidan har bata San ta shiga dakin da takalmi ba tace"Ayya dai Dada Ki bani wallahi zasu tafi".ta Fada idon ta Na Tara ruwa

"Amma Allah shirye Auwalu tunda yaki biya miki ba Zan bayar ba Ki hakura da aikin". Dada ta fada cikin bacin rai don sosai ranta ya baci nan ta dauki hijab nata tana fadin" Dadda Na tafi".

Haba Ai hannu Laylerh Tasa a Kai duk yadda take marmarin yau Amma dubi yadda suka ruguza Mata komai kuka ta Fara Dadda ko kallon ta take yi ganin Ehhh da gaske kuka take yi sai tace"Miko mini filon can".

banza tayi da Dadda sanda ta sake maimaitawa nan ta mike ba don ranta ya so ba ta dauki filon baya ta juya lokacin da take mika mata Dadda ko Kai kawai ta girgiza..

Zama tayi tana fuskantar Dadda sai gani tayi Tasa hannu cikin filo ta Fara Ciro kudade abunka da ajiyar tsohuwa Ai bata San sanda murmushi ya subuce Mata ba Dadda ko cire kudin ta take yi cikin sanyin jiki tana warwarewa da hadawa waje daya kamar bata San Laylerh Na wajen ba..

Ita Laylerh ta San ita za'a bawa kudin a zuciyar ta sai cewa take Dan Allah Dadda kiyi sauri kada su tafi ganin fa da gaske cikin sanyi Dadda ke hada kudin sai tace"Dadda nace su jira ni kan Ki gama hadawa".

banza tayi da ita taci gaba da hada kudin ta ganin haka sai ta fashe da kukan karya duk Dadda taki kula ta sanda ta gama hada kudin sannan ta Ciro hamsin ta mika Mata"Amma tsohuwar nan ta San kan tsiya duk jiran ta da nayi Ashe hamsin zata bani"ta fada a zuciyar ta nan Tasa hannu ta Karba da gudu ta fita a zaure suka hadu da Baban Maryam sai yace"Ki zo mu tafi".

"Dama Dadda ta bani hamsin Na machine".

"Ki mayar Mata kizo mu tafi". Aiko da gudu ta koma nan ta bawa Dadda kudin tana fad'in" sai Na dawo"daga haka ta fice keke napep suka shiga sai gidan gonar a gate aka sauke su su ukun biyan Mai keke kudi yayi sannan suka shiga a gate suka tsaya..

Da yake tsakanin farm gate din da ciki akwai nisa sosai shiyasa ko yaushe jira ake a gate in kun Kai kamar biyar haka akwai motar dake Daukan staffs yana shigar da su ciki to yau din ma jira suka yi suna cika shida mota tazo ta dauke su..

A admin block suka sauka a wajen suka hadu da Wanda ya musu hanya sai yace"kace staffs namu sunzo kenan".

"Ehh wallahi".

" to Allah bada sa'a Ince kowa ta San department da take aiki"

"Eh"

"To kowa ta tafi department nata".

Nabeela a livestock take aiki under section Na wajen da ake yoghurt a wajen packaging take nan suka sallami Baban Maryam Nabeela ta juya Laylerh kuma tare da shi mutumin suka shiga don shima a admin department yake..

Office Na Accounter aka kai ta da yake under him zata yi aiki sai aka ce mishi ga new student nan ya Fara holo yana fadin" wallahi ni fa ba son new student nake yi ba tsam ba maida hankali suke akan aikin su ba".

"Ji mini katon Arne". Ta fada a zuciyar ta nan ya dube ta yace" can you read and write "

"Yes Sir".

" Asabe".Wata Yar bautan kasa ce tazo wajen ita ma ba musulma bane nan yace"ga New student Ki gwada ta Ki gani may be in kin tafi zata mana amfani"

"OK sir". Nan ta dubi Laylerh tace" let's go".Bayan ta Laylerh tabi zuwa wani karamin office nan tace"what's your name? "

"Laylerh".

" okay nasan dai you can read and write so can you operate system "

"Yeah".

Logo'n company'n Asabe ta dauko ta bata tare da cewa tayi designing nan ko tayi da yake a school nasu suna shiga ICT practical" wow Ashe kin iya".wani pepper ta mika Mata tace tayi typing abunda ke ciki don taga how fast can she type sai ta saita stop watch ta dai yi typing din average ba slow ba kuma ba fast ba nan dai ta yaba da kokarin ta..

Bangaren Nabeela ma komai Na tafiya Mata yadda take so da yake a company kowa da abincin shi yake zuwa in kuma a restaurant dake cikin company'n zaka ci abinci to karfe daya suke tashi break daga nan sai kowa yayi sallah ga musulmai din kenan..

Sallah kawai Nabeela tayi a cikin masallacin tunda ta San bata zo da abinci ba sannan kuma kudin hannun ta naira Dari ne bai Kai ya saya Mata abincin da take ganin Ana ci ba don ba abincin talakawa bane..

A bangaren Laylerh ko Asabe ce ta Mata tayin abinci nan taci kadan sannan tace ta koshi sai taje tayi sallah ganin ta dawo sai Asabe tace ta karasa typing din haka ko aka yi..

Karfe 5 daidai aka tashi aiki tare da Asabe suka fito a harabar department nasu suka tsaya jiran mota nan yazo ya dauke su har gate ya ajiye su sannan ya juya."ya Kika tsaya a nan Laylerh let's go".

"No akwai sister Na a ciki ita nake jira".

" a wani department take?"

"Livestock"

" Ai kusan sune last na fita da yake kin San a ta karshe suke komai nasu special ba'a son Dotti bangaren yoghurt ".

" eyyah".sun Kai 10mins tsaye a wajen kan mota ya kawo su Nabeela nan ta dubi Laylerh tace"kun sha jira ko".

"Ba komai Ai".gate suka fita nan ko wacce ta Kama gaban ta keke suka shiga sai Laylerh tace

" Nabeela wallahi baki ji yadda nake jin yunwa ba".

"Ai Ki Bari kawai ni banda ruwa ba abunda Na sha".

" Allah sarki Ashe gwara ni naci abinci kadan".suna isa junction Na anguwar su suka sallami Mai keke sannan suka Fara shiga cikin anguwar nan Nabeela tace"Laylerh kin San wani Abu?"

Kai Laylerh ta girgiza ita ko cewa tayi"Hmm ance fa oga kwata kwata'n company baida mutunci he is an arrogant and a monster, bai ragarwa kowa a company kuma duk tsoron shi ake ji don zafin shi".

"Aikin banza duk zafin shi ya Kai wuta ne wallahi ni in mutum ya mini ba Bari zanyi ba".

" uhm uhm fa Laylerh alfarma muke ci".

a haka har suka Kai gida kowa oyoyo yake musu abunka da sabon shiga tunda a gidan ba masu aiki..kan katifa duk suka fada sai Dada ce tace"lafiya kuwa?"

"Wallahi Dada yunwa muke ji ba abunda muka ci".

Nabeela ta fada nan Dada tace"ga abincin da aka kawo Na Rana Ku dauka kuci".Haba aiko ci suka Fara kamar ba gobe sanda suka koshi sannan ko wacce ta Fara sauke ajiyar zuciya nan ne fa suka Fara fada musu yadda their first day at work ya kasance..

Bayan sallar i'sha duk 'yan matan gidan Na zaune a harabar gidan ko wacce ta fito da abincin shashin su don dama haka su hudun suke to yanzu kuma sun zama su biyar da Laylerh Hasken fari Wata ya haska sararin samaniya.."Nabeela ya wajen aikin Ku?"

"Hmm Ai aiki kam alhamdulillah" nan Laylerh ta Karba taci gaba da basu labari sai Maryam tace"Ashe dai wajen aikin naku Nada kyau".jin mutumiyar ta ce tayi magana sai tayi banza da ita da Nabeela ta fahimci haka sai ta bata amsa haka suka cigaba da hirar in maryam Tasa baki sai Laylerh tayi shiru taki bata amsa..

Yarinya karama ce tazo da waya tana Mikawa Laylerh nan ta Karba tare da Komawa gefe don tasan Naseer ne"Assalamu alaikum".

"Wa'alaikisalam ya kike yan Mata".

" lafiya kalau ya aiki".

"Alhamdulillah Wato ke dai in ban Kira Ki ba baza Ki Kira ni ba".

" a'a fa ina tsoron tambayar Dada waya ne".

"To Shikenan Na yarda ya Taraba".

" Taraba Na lafiya albishirin Ka".

"Goro".

" Na Fara aiki a wani company ".

" wow finally Lil Sis Na ta girma"murmushi tayi Mai sauti Wanda sanda ya jita nan dai suka taba hira kadan sannan yace ta nemi wayar wacce take WhatsApp ta tura mishi number'n ta shi kuma zai tura Mata hoton su,ita dai a sanin ta cikin yan matan gidan maryam ce kadai ke da Babban waya to kuma ba shiri suke yi ba nan tace zata tura mishi suka yi sallama mayarwa Dada waya tayi ta dawo wajen su sai Nabeela tace"iyehh Ai ni tuni Na dago jirgin Ki Laylerh ".

" a'a fa yaya nane".

"Ehh Ai Mun gane irin yayan".murmushi tayi haka kawai ta tsinci kanta da basu labarin shi duk tagumi suka yi tare da zuba Mata idanu suna sauraron ta har ta gama sai Jamila kuma tace

" hmm wallahi Nima nayi sabon saurayi ina cikin soya kosai na yazo yace sai dai nayi Wa yara sadaka ni kuma nace sai ya kawo kudi sai yace Ai dama da kudin ne to daga nan fa kullum sai yazo yanzu har Mun Fara soyayya". Dariya suka Mata sai fa'i tace Nikam Ai duk kun San anyi baiko Na to ranar a bakin kasuwa sai Na Gan shi a shagon Kayan Mata naje Na Fara mishi bala'i Ashe ni yake sayawa.

"kishi"Laylerh ta fada tana dariya tare da nuna ta da yatsa sai tace"Ehem saura ke Nabeela muna sauraron Ki".

"Cab Ai Nabeela ustaziya ce ba zaki taba jin tace ga saurayin ta ba gwara ma kada Ki bata lokacin Ki". Cewar Jamila

" a'a Laylerh kada Ki yarda da zancen su sharri ne Umma Na tace ban girma ba tukun".

"Ba wani Ku ustazai nan haka kuke naku ciki ciki ne in yayi tsami zamu ji".

Cewar Laylerh Jin Maryam ce ke hira sai Laylerh tace

"Kinga Nabeela tashi mu shiga kada mu makara gobe Kinga dare yayi".sarai Nabeela ta fahimci Laylerh ba son maganar maryam take ba sai tace

"kuma fa gaskiyar Ki Kinga tada ni mu tafi".ta karishe zancen tana Mikawa Laylerh hannu nan taja ta ta mike suka yiwa sauran yan matan sai da safe suka nufi bangaren su..

Tsam cikin su ba Wanda ya Lura da Laylerh ba son maganar Maryam take yi ba Amma ita Maryam ta gane duk sanda take magana Laylerh bata sa baki..

Dada da Dadda tuni sun kwanta don haka suna shiga suka rufe kofar sannan suka kwanta a katifa daya..

Washe gari sun makara kadan Bayan sunyi sallah sai suka Fara kimsawa nan ta Ciro abaya'n da Naseer ya saya Mata da simple shoe ta saka sosai tayi kyau Nabeela ma gown ta saka Amma lace sai karamin Vail da ta yafa a Kai Laylerh ma Vail din abayan ta yafa sai tace"Nabeela ina zuwa Dan jira ni kan Ki gama Bari naje wajen Adam".

"Ohk".kyauren dakin shi ta kwankwasa nan yace Waye sai tace" Laylerh ce".

"Wallahi yarinyar nan kin sa rayuwa Na a gaba da shegen fitina to in turare ne ba Zan bayar ba".

" a'a ba turare bane Ayya nace Ka Dan bani Aron wayar Ka akwai number'n da Zan sa za'a turo mini Hoto ta WhatsApp".

tsaki yayi ita ko cewa tayi"oho dai".tump print yasa sannan ya mika Mata nan Tasa number'n Naseer sannan ta mayar mishi da wayar Data ya bude inda yayi searching Na number'n Bayan ya tambaye ta sunan da Tasa sai ya gani"to ni yaya nane da zaki wani saving da ya Naseer ".

Murkuda mishi baki tayi shi bai ma Gan ta ba sai mika Mata yayi yace," Ki Danna nan sai kiyi magana don ya gane kece kada yaro ya raina ni".

"Badai yaro bane wallahi Babba ne" sallama tayi sannan tace ita ce Bayan message din ya tafi sai ta marairaice tace"Dan Allah Ka bani turaren kadan in sha Allah daga yanzu ba Zan Kara rokon Ka ba"tsaki yayi sannan ya shige daki yana fitowa yace"matso"matsawa tayi da kan shi ya fesa Mata nan ta mishi godiya sannan ta juya ta tafi,sallama suka yi sannan suka fece..

Before gate din company'n Mai keke ya sauke su sai ganin wani mahaukaci suka yi Nabeela tace"Kinga Laylerh mu gudu sunan shi kolo kuma wallahi sliver yake tufawa mutani ".

" York dubi jikin shi fa duk Dotti Kayan shi ma kamar Kayi amai duk tsami yake yi".

"Banga". Yace yana musu dakuwa da hannu Wato uban su ganin ya nufo su sai Nabeela taja hannun ta tace" mu gudu wallahi taba nonon 'yan Mata yake yi".

Haba kafa suka sa nan shima ya Fara bin su gudu suke sosai.

Yanzu a Karo Na uku kenan driver Na horn Amma security bai zo ya bude mishi gate ba kasancewar yana tiolet..body guards nashi duk fita suka yi a motar su domin duba ko lafiya karamin gate din ma a rufe nan driver ya Fara horn ba kakkautawa dole security ya fito ba don ya gama biyar bukatar shi ba yana fad'in "ko wane ne ke horn nan most be stupid".Ai jikin shine ya Fara rawa ganin motocin da tsam basu yi tsammanin shi ba duba da gaba daya bai fi week da zuwa ba sai Gashi yau ya dawo shi da in a month ma sau uku yake zuwa wangale gate din yayi jikin shi Na rawa Bayan sun gama parking sai ya fito cikin bacin rai yana fadin

" Na Lura duk masu aiki a company'n nan basu San aikin su ba kana security zaka shige ciki Kayi shiru ".

" sorry Sir ".ya bude baki zai yi magana kenan su Laylerh suka shigo da gudu ita kam ma Harda bangaje shi Sulaiman, suka shige dakin security suka rufe nan ran shi ya Kara bashi sai ganin kolo suka yi yana biye da su nan security din ya Kora shi waje tare da rufe gate din" Oya Ku biyun Ku fito yanzun nan".ya fada cikin bacin rai

a hankali Nabeela ta bude kofar ta fito waje kadan Laylerh Na daga Bayan ta

"what nonsense ce muku aka yi nan din kowa ne zai iya shigowa".

"Mahaukaci ne fa ya bimu" Inji Nabeela

"You guys should get out" ya fada yana nuna musu hanyar waje so suke suce mishi a nan suke aiki duk tsoron shi ya kama su Laylerh kam ko daga Kai bata yi ba security ne ya musu alama da ido kan cewa su fita nan Nabeela ta rike hannun Laylerh suka nufi kofa shi ko cikin motar ya shiga Bayan ya rufe sai ya sauke glass yana fadin"saura yau ma Ka sanar da su zuwa Na"

daga haka driver ya tashi mota suka tafi sai security yace"Ku dawo Ku jira mota".dawa suka yi suka zauna nan ne Nabeela ta dubi Laylerh tace"nikam me yasa baki son maganar Maryam ne".

"Ki bar yarinyar can kin San me ta mini kuwa?"

Kai ta girgiza nan ta sanar da ita abunda ya faru tsakanin su sai Nabeela tace" riko dai ba kyau sannan in Maryam ce kadan Kika gani in dai akan kudi ne ba mutunci ne da ita ba Amma Bayan wannan bata da wani matsala ".

a wajen suka cigaba da tsayawa har mota yazo daukar su..

Bangaren Sulaiman kuma direct admin block ya wuce kofa aka bude mishi yana fita guards nashi suka rufa mishi baya Allah yaso yan department din yau komai normal office Na Accounter ya wuce dama last zuwan shi yace yana da issue da shi, duk jikin su rawa yake ji nan yace" ina copy'n list da nace Ka tura mini ta mail".

"Asabe go and bring it".

Da yake ta San basu yi ba sai kawai ta mishi printing Wanda Laylerh tayi typing jiki Na rawa ta Mikawa Accounter shi kuma Karba yayi ya Mikawa Oga kwata-kwata..

" What rubbish yanzu da girman Ki Kika yi typing nan".

Kai ta Fara girgizawa nan dai tace"sir I am not the one".

"Then who did it". Daidai lokacin Laylerh ta shigo sai Asabe tayi pointing nata juyawa yayi to their greatest suprise sai suka ga sun San juna" not again"ya fada a fili a zuciyar shi ko cewa yayi tabbas wannan ita ce ta buge sa a farm gate din daga Kayan ta ya gane ta..

Ita ko ganin shi nan take jikin ta ya Fara rawa tunawa da Marin da ya Mata Gashi bata San hawa ba bare sauka.

"so wannan yarinyar da last year or this year ya kamata ta gama secondary school kuka bawa typing you guys most be stupid in fact Waye ya yi employing nata ce muku aka yi akwai abunda ta iya ne dubi fa yadda ta lalata mini komai ".

" Sir.....".

"Shut up" yace da ita cikin tsawa sanda taja da baya har yanzu kuma ta Gaza gane wani laifi tayi

"how dare you ce miki aka yi wasa Kika zo yi a nan".karfin hali tayi tace

"Sir Nifa ban San laifin da ake tuhuma Na akai ba in fact jiya Na Fara aiki a nan".

"Tell her" yace yana kallon Asabe nan Asabe ta fada Mata da yake ita ba waiwiya bace sai tace

"wallahi Sir ba haka bane ni fa an bani nayi typing nashi ne don aga how fast can I type so Bayan munyi azahar da ba aikin yi shine Na cigaba da typing din har Na gama".

Kan Accountant ya koma yana fadin

" dama kullum Kai kam sai an samu case a wajen Ka but ba komai Na San yadda Zan yi da Kai".

"I am sorry Sir".

Tuni Laylerh ta sulale ta fita waje ganin ta tsira mike kafafu tayi tare da cire simple shoe nata tana share gumin da bakin Vail nata tare da fadin" wannan mutumin bala'i ne".

tana cikin hutawa ya fito da staffs na wajen dukka da yake protocol nashi ne all staffs should follow him files manager'n department nasu Laylerh ke Mikawa PA'n shi a bazata suka sinkayi muryar shi yana fadin

"Laylerh karbi files din"

kowa jira yake yaga wace ce Laylerh a wajen har ita kanta da bata iya tuna sunan ta a lokacin juyawa tayi tana Neman Laylerh cikin tsawa yace"Laylerh Musa am talking to you".

mamaki ne sosai ya kamata wannan shine Karo Na biyu a rayuwar ta da taga Wanda ya San ta tabbas shi din ya San ta tunda har da wani Laylerh Musa mika hannu tayi ta Karba nan yayi gaba da guards nashi su kuma suna baya bus Na company'n suka shiga sai livestock department inda Nabeela ke aiki..

Shima komai tsab a wajen Nabeela ko mamakin kyau Na oga'n su take yi duk da shi din ba fari bane Bayan ya gama dube-duben da zai yi sai suka wuce engineering department inda wancan zuwan shi bai shiga ba a wajen har korin staff yayi saboda dama an rubuta list Na abunda za'a saya so sai shi staff din yayi doubling da yazo ya fahimci haka sai yace"tunda akwai irin Ku a cikin company'n Bari Na bada misali da Kai".

kowa shiga hankalin shi yayi ganin ba wasa tattare da boss din shiyasa suna fita ya nufi car's nashi Laylerh ko bin shi tayi Ana cewa ta dawo cikin rada take cewa"files nashi Zan bashi ".

ya rike kofar motar sai jikin shi ya bashi da mutum a Bayan shi ba tare da ya juya ba yace" Ehem ".

" Sir file naka".da ido ya kalli PA nan ya Karba suka yi gaba sannan kowa ya koma department nasu..

Ko da aka tashi Bayan keke ya sauke su a junction sai suka Fara shiga ciki nan Nabeela tace "me ya hada Ki da Sir naga kin rike masa files Amma fa guy d'in ya hadu".

" Nabeela shine fa Wanda ya mare ni Randa muka fita da Maryam ".

" Kai Haba dai Ashe mugu ne".

"Ba ruwa Na" Inji Laylerh don yanzu ta San halin shi sai suka fashe da dariya a haka suka shiga gida Dada ce tace"jiya kun dawo a hade da fuska yau kuma kuna dariya".

"Wallahi Dada oga'n namu ne sai a slow".

Nan Laylerh ta bata labari sai Dada tace" kila fa ya San Ki ne".

"A'a ni Tun da can ba Wanda Na sani a Taraba".

Auwalu dake zaune a gefe yace

" Hmm ina ruwan Yaron Maman shi,company'n Na mamar shi ce kuma da ba a nan suke da zama ba suna Maiduguri ne so abubuwa sai suka Dan rikice Mata har ya Kai ga kamar kamfanin ta Na can zai mutu shiyasa da aka Mata transfer ta dawo nan sai ta bude wannan company'n Yaron Na kula da shi ita ko tana handling Na can".

"Ohh" kawai suka iya fadi..

**

A bangaren Naseer ko har yau jiki yaki sauki don drip din ba karamin rikita shi yayi ba shiyasa hankalin ahalin shi duk a tashe yake shi ko Randa ya Dan ji sauki ne ya Kira Laylerh da daddare to daga ranar fa komai yi mishi ake Gashi ya ramewa gaba daya kamar ba shi ba kallo daya zaka mishi ya baka tausayi..

Asibiti ya koma musu tamkar gida kullum a wajen suke wuni su kwana sannan wajen aiki ba Mai zuwa duk sun koma kalar tausayi..

Mummunar mafarki tayi akan Naseer haka ta farka gaba daya ta fice a hayyacin ta da yake baccin safe ta maida sai ta tashi da sauri cikin gidan ta nufa dakin Adam taje sai ta tarar a rufe da kwado tana hawaye ta nufi sashin su Jamila nan ko ta tarar da ita tana wanke wanke"Jamila don Allah bani Aron wayar Ki Zan yi Kira".

"Lafiya kuwa Laylerh kike hawaye gaba daya kin fice a hayyacin Ki". Hada hannu biyu tayi alamar pleading tace" Dan Allah Ki bani Zan miki duk wani bayani daga baya".

"Kinga wallahi wayar ba carty". Bayan hannun ta Tasa ta share hawayen ta da gudu ta fice zuwa shashin su Maryam ita ko shara ta tarar tana yi

" Maryam Dan Allah bani Aron wayar Ki nayi Kira".

duk da Maryam din ta Lura a rikice take sai tace

"yau kam kin San amfani Na kenan Ince kullum ja mini Aji kike yi".

Durkusawa tayi a kasa ta Kama kafar Maryam tana fadin

"Dan Allah Ki bani daga baya duk hukuncin da zaki yanke mini sai kiyi

"sosai jikin Maryam yayi sanyi ganin yadda take hawaye sai ta mikar da ita tace

"Kinga Laylerh wallahi wayar jiya da Na Kai chaji ko da naje Karba sai Na tarar Bappayo ya rufe waya kam".ficewa tayi tana jin kamar Tasa hannu akai tayi ta ihu don in har bata ji ya Naseer yake ba tasan ita din ma kila hauka zata yi hawaye take yi ta nufi bangaren su a baranda ta zauna jin an dafa ta sai ta dago da sauri Nabeela ta gani

"ke Laylerh lafiyar Ki kike kuka".rungume Nabeela tayi da karfi tana fad'in

"mafarkin ya Naseer nayi to duk wacce Na tambaya waya ban samu ba".

Pitting Bayan ta Nabeela ke yi tace" banda abun Ki baga waya Na ba"ita gaba daya ta mance da batun wayar Nabeela shiyasa ma bata Fara tambayar ta ba,mika Mata tayi nan Tasa number'n shi tayi dialing Amma har ta katse ba'a daga ba.daga Mata Kai Nabeela tayi alamar me ya faru"Nabeela ba'a daga ba".

"Ki sake Kira" Kira tayi a Karo Na biyu har ya kusa tsinkewa Nusaiba ta daga

"Assalamu alaikum "jin muryar mace ce Gashi bakuwa number ne sai Nusaiba ta cire wayar a kunnen ta ta kalli screen din wayar sannan ta mayar kunnen ta tana amsa sallamar" Dan Allah ko me wayar yana kusa ina son magana da shi".

"Sorry yana bacci Ki sake Kira Anjima"

"Ohk Na gode" tace gami da katse kirar Nabeela ko kallon ta tayi tace"Happy? "

"Nabeela in har ba muryar shi naji ba ba Zan samu nitsuwa ba".

" Kinga tashi mu Fara shirin tafiya wajen aiki in yaso da Munje can sai mu sake Kira".

to tace nan suka shiga shiri Amma gaba daya ita bata tattare da nitsuwar ta sunzo fita kenan Dada tace

"ga Naseer akan waya".wani yalwataccen murmushi ta sake da gudu ta amshi wayar har hannun ta Na rawa hannun Nabeela taja suka koma gefe nan Tasa wayar a kunnen tana fadin

"Assalamu Alaikum ".

Rintse idanu yayi hawaye Na gangara ta gefen fuskar shi nan ya daure yace

" Wa'alaikisalam yau dai ba'a ja mini Aji ba".

"Wallahi dazun I was scared to death don mafarkin da nayi shiyasa ma Na Kira da wani line aka ce kana bacci".

" silly girl do you love me that much ".

" words alone can't express my feelings for you".sauya zancen yayi saboda raunin da karayar da zuciyar shi yayi da fad'in

"So ya kike?"

"Lafiya ya jikin Ka?"

"Alhamdulillah jiki ya kusa sauki".

" but yadda nake jin muryar Ka kana jin jiki".

"Laa da sauki fa kin San me?"

"A'a sai Ka fada".

" akwai abunda nake son fada miki".

"Ina jin Ka".

Shiru yayi ita ko Allah Allah take yi yayi expressing Mata feelings nashi sai yayi shiru" ina jin Ka".

"Nafi son sai face to face ido Na cikin naki Zan fada miki".

" a'a Ka fada mini yanzu ".

" banda enough carty".

"To ni bara Na Kira Ka da number'n Kawa ta Nabeela".

" a'a Ki Bari in yaso da Anjima Zan Kira Ki sai Na fada miki".

"To Shikenan Allah Kara lafiya".

" Ameen Ameen ".

" kaga ga Kawa ta Ku gaisa"Mikawa Nabeela waya tayi suka gaisa daga nan ta mayarwa Dada waya suka Kama hanya Nabeela sai zolayar ta take tana fadin"Ashe duk yadda kike mutuwa akan shi bai taba cewa yana son Ki ba".

"A aikace yake nuna mini kuma Ai Kinji yace Anjima zai fada". Haka ta wuni cike da farin ciki a ranar..

Bangaren shi kam Abu sai gaba yake yi ganin haka yasa doctors din cewa za'a Musu transfer zuwa wani asibiti gobe da safe nan hankalin iyayen shi ya sake tashi sai shirin barin asibitin suke yi..

Washe gari da safe before su tafi aiki Dada ta Kira Hajiyar sa domin jin ya jikin cikin kuka Hajiyar sa tace" Naseer kam fa bana jiki yaki yanzu haka abuja zamu wuce da shi".

"Innalillah Allah bashi lafiya".

Kalmar Dada Na karshe ne ya daga Mata hankali nan ta Fara tambayar ko lafiya sai aka ce jikin Naseer ne kuka ta Fara kamar wacce aka ce da ita ya mutu sanda Dada ta nuna bacin rai kan tayi shiru suka nufi wajen aiki..

So silent ta zama komai ma ba daidai take yi ba..

Bangaren su ko suna isa airport rai yayi halin shi Wayyo zo kaga Tashin hankali cikin kuka Khadija ta Kira Dada ta sanar Mata nan take ta shirya sai Tasha da yake safiya ce ta wuce Kano..

Tun a wajen aiki bugun zuciyar ta ya sanan ta haka har suka dawo gida ganin ba Dada sai tace" Dadda ina Dada ne?"

"Ai ta tafi kano anyi rasuwa".

Duuu haka taji kunnen ta yayi idanun ta basu gani da kyau baki Na rawa tace" Waye ya rasu?"

"Naji kamar Naseeru ne ko Waye".

Haba ihu ta saka tana Komawa da baya baya idanun ta na yawo a sama alamar suma take son yi da sauri Nabeela ta taro ta nan ta fadi a jikin ta sumemmiya".

kullu nafseen za'ikatul maut Na sani dayawa ba zasu so mutuwar Naseer ba sai dai Ku sani ko wani Mai rai zai dandani mutuwa

Yau banda chargi shiyasa banyi update on time ba kuma naga ba wani comment juke yi ba

Comment

Share

©Hafciey Musa

[1/25, 5:37 AM] Hafciey Musa😘: □ *LAYLERH*□

(The prettiest emerald)

Page 17

Da baya baya ta Fara Komawa tana fadin"No ba zai yiwu ba wallahi Naseer bai mutu ba".rike ta Baban Naseer yayi yana fad'in "Addu'a zaki mishi ba kuka ba".

" addu'a fa kace,Wai yanzu Ka yarda Naseer ya mutu wallahi ban yarda ba kuma ba Zan taba yarda ba".

da yake ambulance din akwai nurses nan suka sake dubawa tare da tabbatar Mata Naseer fa is no more..ba yadda ba'a yi da ita ba haka ta bushe tace sai dai aje asibiti a duba dole suka nufi asibiti..

Doctor ne ya fito cikin ambulance din ya duba sai yace"sai dai fa kuyi hak'uri meyasa har yanzu

ba'a Kai shi matuary ba".

rufe bakin ta tayi da tafin hannun ta tana girgiza Kai hawaye Na bin fuskar ta tana fadin" wallahi shi kadai Gare ni Na miji innalillah ".

duk dauriya da Baban shi keyi shima sai da yayi hawaye sa babbar yatsar shi yayi yana share hawaye tare da rike ta kuka take da iya karfin ta, ya sata a mota sannan ya koma wajen doctor'n yace gida za'a Kai musu gawar haka ko aka yi..ko da suka isa gidan cike yake makil da jama'a da yake shi din mutumin arziki ne bai da Abokin fada direct apartment Na Hajiyar sa aka nufa da shi daga nan aka ajiye sa a tsakiyar falon..kukan da Nusaiba da Saudat suke yi ko uban su ne ya mutu albarka Hajiyar ma zuwa yanzu kuka take da iya karfin ta don tsam duk da jinyar da yayi basu taba tuna mishi mutuwa nan kusa ba..

penfon ta ce ta rungume ta tana fad'in" Ku daina kukan nan baida amfani addu'a ya kamata Ku mishi ke da ya kamata Ki rarraahi yara sai Ki sa su a gaba Ku yi ta kuka".

Inaa ita fa ba jin ta take ba kuka suke yi sanda Wata Kawar ta malama tazo nan ta Fara addu'o'i sannan suka rage kukan suna amsawa da Ameen Ana kawo likkafani kuma suka sake barkewa da kuka nan aka dauke shi aka tafi domin yi mishi wanka.. Bayan an mishi sutura sai aka Kira ta domin tazo ta mishi addu'a Haba fadawa tayi a jikin shi tana kuka tana addu'a sanda mijin ta ya daga ta shima kukan yake yi yace"ba kyau fa taba gawa Ki Bari zai kumbura".

da kyar ya janye ta sannan aka fice da gawar a wajen ya bar ta suka tafi kai shi gidan shi Na gaskiya.. "Naseer Allah jikan Ka ya Kai haske kabarin Ka yasa Ka huta we loves you but Allah loves you more hakika nayi rashin d'a sannan mahaifin Ka yayi rashi haka yan uwan Ka,Allah gafar ta maka in sha Allah har Na koma ga Allah ba Zan daina maka addu'a ba". Kuka ta sake fashewa da shi tana ficewa zuwa bangaren ta a falo ta zauna domin karban gaisuwa hannun ta rike da carbi tana istigfari da kuma kuka a lokaci guda, Nusaiba kam zazzabi ne ma ya rufe ta,Saudat ko rufe kan ta tayi a daki tare da fadawa gado tana fad'in" Shikenan kuma Na rasa yaya da yake tamkar uba Wanda yayi mini abunda ko uba ya kasa tunda Gashi ya hanani auren bata gari,ya Allah Mun San Ka fi mu son shi yasa Ka dauke shi a lokacin da muka fi bukatar shi Allah Ka karbi bakoncin sa Kai Kai haske kabarin sa".kuka sosai take yi don ita ta San Waye Naseer mutum ne da ko su kannen sa bai daga hannu ya duke su shiyasa Nusaiba ta raina shi bare wasu Na waje in kuma yaga za'a yi rashin adalci to sai inda karfin shi ya kare..

Girki aka daura wasu Na kuka wasu Na girki, wadan da suka Kai shi ma sun dawo duk juriya irin Na Babban da yaga an sa shi a kabari kuka ya Fara kamar karamin yaro dole sai da aka daga shi har yanzu da suka dawo kuma bai daina kuka ba..Dada kam bata samu isa a ranar ba sai Washe gari da safe nan Khadija tazo da gudu ta rungume ta tana kuka kamar ranta zai fita..

Hakika wannan ahalin sun matukar bata tausayi ita ma tunawa da Naseer Tun yana yaro sai da tayi kuka..

**

Ruwa Nabeela ta wasa Mata nan ta kawo dogon numfashi tare da bude idon ta a hankali tana hawaye

"Dan Allah Nabeela Kice da su bai mutu ba ba'a duba da kyau bane ya Naseer shine Gata Na ba don shi ba da yanzu ba'a zance Na".

Ta fada tana fashewa da kuka Mai cin rai" Laylerh kiyi hak'uri Wanda yafi mu son shi ne ya dauke shi kuma Allah shine gatan kowa nasan iyayen shi zasu fi Ki jin mutuwar Amma a haka zasu hakura".

"Ba zasu taba Kai ni ba Nabeela Naseer shine uwa uba sannan Dan uwa a Gare ni,kin San Tun yaushe nake yawo a titi ba Wanda ya mini kallon mutum,Naseer shine Wanda ya nuna mini ni din ma kamar ko Wa ce,ba don shi ba da wasu azzalumai sun mini fyade,sannan ba don shi ba da yanzu zina nake yi and shi ne Wanda ya taimake ni lokacin da nafi bukatar taimako don da yanzu an kona ni".

Tunda Na bar gidan mu ban ga Wanda ya Kai mini shi ba mutumin da ya zama mini uwa uba kike cewa zasu fi ni jin mutuwar shi ta ina?suna da wasu yara suna da kudi ga yan uwa mutuwar shi Na lokaci kalilan ne ni kuma Ki fada mini Waye nake da shi".

Ita ma Nabeela kuka ta Kama Dadda ko tana jin su shiru tayi bata ce komai ba har Nabeela ta sake cigaba da rarrashin Laylerh Abu kamar wasa zuwa magrib jin kanta take kamar zai rabe gida biyu don ciwon da yake saboda kukan da tayi har zuwa

yanzu kuma kukan take yi duk da ta kan ji jiri in ta mike..tana idar da sallah i'sha ta kwanta a wajen shiru tayi tana Mai tuno Tun ranar haduwar su da kuma Randa suka rabu har zuwa wayar su ta karshe kuka ta Kara fashewa da shi Nabeela dai duk tausayin ta take Dadda kam ma ta rasa me zata ce..

Ba yadda ba'a yi da ita taci abinci ba taki sai da kyar ta iya cewa a sayo Mata maganin ciwon Kai nan aka sayo Mata Tasha taci gaba da hawaye tana tuno shi..ranar yadda taga dare haka taga Rana Washe gari ma kin cin abinci tayi da safe nan hankalin su ya Fara tashi ganin in ta Fara kukan har amai take yi Gashi ba komai a cikin sai dai tayi ta kokarin amai Amma ba abunda ke fitowa..ganin haka yasa Nabeela nufar wajen aiki don tasan yau dai ko me ake bawa Laylerh a wajen aikin ta hakura da shi...

zuwa azahar sai ga zazzabi Mai karfi ya rufe ta sai rawan sanyi take yi nan Auwalu ya Kira Baba Ali Mai chemist yazo ya sa Mata ruwa tare da alluran bacci nan ne kunnen Dadda ya Dan huta da kukan ta cikin barcin sai ajiyar zuciya take saukewa..drip din Na karewa aka cire duk bacci take yi sai Bayan asr ta farka da wani mugun yunwa dole ta jawo abinci gaban ta tana ci ba don ta San test Na abincin ba bare ace yana Mata dadi sai goge hawaye take da Bayan hannun ta tana Jan hanci.. Ganin abinci ya Ki samun wajen zama sai ta ture kwanon gefe ta jingina da jikin bango"sai yaushe Zan yi farin ciki a rayuwa Na,ban San ni wacece ba sannan ban San daga ina nake ba,banda yan uwa haka nayi ta wahala a karshe Allah ya turo mini Naseer Ashe shi din ma tafiya zai yi ya bar ni..yanzu Na fahimci ni din Allah bai yi zanji dadin rayuwa ba har Na koma Gare sa".dafa ta da Maryam tayi ne ya firgita ta daga jajayen idanun ta tayi ta kalli maryam"Laylerh kiyi hak'uri Allah jikan shi da rahama".Ameen tace don wannan addu'ar kadai take amsawa ko da kwana magana zaka yi ba zata amsa ba don jin su kawai take yi basu San actual yadda take ji a ranta ba da ace sune aka yiwa rashi da tuni sun fahimce ta..

Wasa gaske ta daina magana haka zata zauna ta kurawa waje daya ido har yayi kwana uku da rasuwa..tabbas ko iyayen shi basu Kai ta nuna zafin rashin shi ba ko su danne nasu suke yi ne sai Allah..

A ranar Na ukun ne kuma aka bugawa Auwalu waya tare da tambayar ko lafiya ta daina zuwa office sai yace in sha Allah gobe zata zo..yadda Ka San ita ce iyayen shi haka yan gidan duk suka shiga suka Mata gaisuwa Dadda dai kallon ikon Allah take wajen Laylerh duk da taji ance son shi take Ai yaci ace ta Fara sabawa da rashin shi Amma tsam taki wannan da ace gida daya suke kam kila mutuwa zata yi ta bi shi..

Dadda Na kwance a gado Nabeela ko waya take da Maman ta sai ita Laylerh da ta kurawa waje daya ido Auwalu yayi sallama nan Dadda da Nabeela suka amsa sai ya shigo dakin

"Dadda kun wuni lafiya ".ya tambaya yana kallon Laylerh

" alhmdll ".Masha Allah yace sannan yace" Laylerh ya Karin hak'uri ".can ciki ciki tace" Alhamdulillah ".

" Masha Allah dama wajen Ki nazo Kinga shi duniya dama haka yake in yau Kai ne gobe ba Kai bane shi wannan ya Riga ya tafi addu'ar Ki yake bukata ba kuka ba don haka Ki cire komai a ran Ki and move on with your life ba Wai kuma cewa nayi Ki manta shi ba a'a kowa da kike gani Ana mishi mutuwa daga baya kuma yaci gaba da rayuwa kamar yadda yake saboda ba Wanda ya isa yayi fushi da Allah, wannan damuwar da kike nunawa yana nufin baki so yadda Allah yayi ba fushi kike yi da shi ko".da sauri ta girgiza Kai

"to ke da baki San kowa naki ba baki San ke wacece ba bai hanaki cigaba da rayuwa a cikin mu ba sai don kin rasa wani".

Shiru tayi tana sauraron shi" don haka Ki shirya gobe Ki koma wajen aiki don an Kira ni Kinga Baku Dade da Fara aikin nan ba bai kamata ace an Fara samu matsala ba".

"Yauwa Auwalu fada Mata kam yarinya sai kace uwar shi wallahi da dare ina jin ta in Mun kwanta sai ta tashi tayi ta kuka Wanda Na tabbata ko uwar Yaron bata yi,ni da kike kallo Na duka duka ban wuce shekara goma ba baba na ya rasu mama Na kuma ina goyon Dada ta rasu daga baya kuma miji Na hakan bai sa Na daina rayuwa ba sai ke". Duk jin su take idon ta a kasa tana hawaye don ita a ganin ta har yanzu basu San me take ji bane nan Auwalu yace" nace musu gobe zaki koma bakin aiki don haka Ki kwana da shiri ".

yana gama fadin haka ya mike yace" Dadda sai da safe".ficewa yayi Dadda taci gaba da fad'in "yarinya kin daurawa kan Ki wahala ko abincin kirki kin daina ci dubi yadda gaba daya Kika rame mutuwa ba a kan Ki aka Fara ba kuma ba a kan Ki za'a gama ba duniyar da kike gani tana jiran Wanda ba'a Haifa bama bare haifaffe".

" Haba mana Dadda ya isa haka da wanne daya zata ji,da rashin da aka Mata ko da holon Ku".Cewar Nabeela "ke bar ni Ai gaskiya nake fada Mata tunda ke kin kasa".

" to taji ta kuma gode ".

daga nan ba Wanda ya sake magana ita ko mikewa tayi a wajen ta kwanta tana Dad'a cewa duniya ba a bakin komai take ba..

A Washe gari Nabeela ta gama shiri tana jiran ta sai ce Mata tayi taje kawai ba zata iya zuwa ba,ta so Mata magana Amma ganin in ta tsaya zata bata ma kan ta lokaci dole ta tafi..

Ai ko a Daren ranar Auwalu ya shigo yana fad'in" tunda duk kin raina mu bamu isa fada miki Abu kiyi ba ga uwar goyon Ki"ya karishe zancen yana mika Mata waya Karba tayi Tasa a kunne

"Laylerh Ashe yan uwa Na basu isa da ke ba?" Kai ta girgiza kamar tana gaban Dada nan Dada taci gaba"Naseer kam ba ya Riga ya tafi ba iya soyayyar da zaki mishi shine Ki masa addu'a Amma haka kawai zaki daurawa kan Ki damuwa ance abinci ma kin daina ci sannan Dadda da Auwalu sun miki magana kin Ki ji kina ganin aikin nan Allah yayi rabon Ki ne in ba haka ba Wa zai baki aiki a can sannan kin tsaya wasa".

"Yi hak'uri".

" to wallahi Tun wuri gwara Ki sake Ki Kama aikin Ki don ni da Kika gani bani da ranar dawa jalingo tunda naga jikin Dadda taji sauki kuma Ai Kinga yadda gidan mu yake duk Randa aka ce baki da kudi to fa kina cikin matsala shiyasa gwara ma kin

rike aikin Ki Na fada miki,Tun dama nayi niyar in Na dawo Zan sanarwa Naseer Na bar Ki a can to Kinga Allah bai sada haduwar mu ba".rintse idanun ta tayi hawaye Na zuba jin an ambaci sunan sa Wai shin ita kam haka zata cigaba da rayuwa Gashi yau Allah ya kawo ta ranar da zata tsaya da kafafun ta ta tallafi rayuwar ta abunda Naseer ya Mata alkawarin in har yana da rai ba zata yi ba tabbas tafi kowa rashin sa Dada da take takama da ita ma tayi tafiyar ta Wayyo Allah rayuwar ta..

har Dada ta katse kiran bata sani ba sai da taji Auwalu ya fisge wayar sa ya juya yana fadin"aikin banza yarinya Ana tausayin Ki baki tausayawa kan Ki waya San Asalin Ki ma".

duk sun ji abunda yace Nabeela kuma haushin kawun nata taji in ba zai fadi alkhairi ba kam yayi shiru mana..ita ko Laylerh cewa tayi"Nima zuwa yanzu Na Fara tunanin Abu biyu ko ni din shegiya ce ko uwa ce ta mini baki".duk tausayin ta ne ya kamasu Amma basu ce da ita komai ba haka suka kwanta..

Washe gari da safe ta tashi da shirin zuwa wajen aiki kallo daya zaka Mata ta baka tausayi Gashi komai cikin sanyi take yi nan dai Dadda ta basu kudin machine tana fadin"duk Randa kuka karbi salary zaku biya ni don ba Mai bani kudi Ehem ".

basu tanka ta ba suka yi tafiyar su sai dai tafiyar tsam ba kamar ta kullum bane saboda ba armashi a farm gate suka jira mota daga nan ko wacce ta wuce department nata..

Holo sosai ta sha wajen Accountant har yake cewa jira yake dama in yau bata zo ba zai sallame ta tunda ta cika kwana biyar hak'uri ta bashi sannan tace rasuwa aka musu da ya tambayi waya rasu sai tace yayan ta nan staffs din suka Mata ta'aziyya..

Aiki dai tana yin shi ba tare da kuzari ba..

**

Da yake weekend Auta tazo tuni ta koma school yanzu gidan saura su uku kamar ko yaushe yanzu ma malam ne zaune da Baaba a falo suna hira

" Kinga don Allah in kinje interview nan kada Ki Dade saboda so nake Na leka kasuwa".

"Ba Zan Dade ba malam".

" Ai Ku Mata ba'a shaidan Ku don in kun fita sai an Gan Ku kawai Kinga yau kasuwa ma ban fita ba sai kin dawo".

"Kada kaji komai Zan dawo Ana gamawa in sha Allah yo ni da wannan ciwon kafar tawa ina zani".

" to Allah kiyaye hanya".

"Yauwa Ka Lura mini da mutumin Ka".

" Amma wallahi ba don kin nace ba da ni ba Zan bar Ki ba saboda in kin Fara aikin nan ni kuma ina zuwa kasuwa Yaron nan da Wa za'a ke barin shi?"

"Nima dai abunda nake tunani kenan wannan dalilin yasa naki offer da suke bani sau da dama Amma kuma yanzu anzo gabar da dole Na Karba tunda komai Neman fin karfin mu yake sannan batun shi kuma dole wannan Karon zai yi hak'uri me nemi Yar aiki".

" Ai ba kawo Yar aikin bane matsala kin fa San baya son hayaniya da jama'a kada yazo ya illa ta Yar mutani ko Mata".

"In sha Allah haka ba zai faru ba kaga tuni muka gama da zancen nan Amma kake maida mu baya da tuni yanzu Na tafi".

" to Shikenan je Ki sai kin dawo "

Yauwa tace tana daukar hand bag nata ta Fara tafiya tana dingisa kafar ta Mai ciwo..ta ko yi sa'a a kofar gidan ta samu machine nan tace" jika Na peacock college of education zaka Kai ni".

shi dariya ma ta bashi Wai jika shiyasa yayi murmushi yana fad'in "to nawa zaki biya Hajiya Hala drop zaki dauka ko?"

"Nawa ne drop din?"

"Dari biyu ne".

" kaga yi hak'uri Zan baka Dari da hamshin tunda a gaba ma zaka dauki passenger ".

" to shiga mu tafi".shiga tayi nan suka Fara tafiya basu dai cewa komai har suka fito titi nan ne ya samu passenger barde way ya dauka sun zo daidai round about Na forest wani politician kuma ya fito da convoy nashi daga PDP secretarial zasu yi malam joda gudu motocin suke.

Mai keken kuma ganin motocin Na da yawa sai yace Bari yayi sauri ya mike kawai Haba ba sai accident suka yi ba nan keken su ya fada lambatu a take mutanin wajen suka nufi wajen su da kyar aka Ciro su a napep din,shi Mai keken duk ya fisu jin ciwo don jini yake zubarwa sosai Gashi kan shi ya fashe a sume ma yake,daya passenger ma yaji ciwo ita ko keken fadiwa yayi akan ta Wanda sai kukan kirjin ta take nan driver'n politician din ya debe su sai police clinic sai cewa suka yi abun yafi karfin su a tafi FMC a wajen suka dauki police sannan suka nufi FMC a wajen ma sanda aka musu wulakanci kan a karbe su da yake dama asibitin kowa ya San su yan wulakanci ne..

Nan ne aka Debi wayar su aka shiga call log nasu tare da kiran last call din ko da aka zo kanta lokacin da suka Kira last call da tayi sai suka fahimci kamar makaranta ne nan suka Kira number'n da aka rubuta Alhaji Na..

A bangaren shi kuma yanzu ya fito daga dakin Umar Farouq Bayan ya tabbatar bacci yake falo yazo zamar shi ke da wuya wayar shi ya Fara ringing yana dagawa kuwa Bayan sun gaisa sai suka ce"ko Ka San me wayar nan".

"Eh Mata ta ce ina take".

" to kazo FMC muna wajen tayi accident ".

mikewa yayi yana fadin innalillah sannan ya koma dakin Umar Farouq duk da bacci yake sai yace" Ka gafarce ni Zan Barka Kai daya a gida zanje asibiti don Baabar Ku tayi accident"

daga nan ya fice tare da rufe shi ta waje sannan ya rufe ko ina Na gidan kan ya isa asibiti ma ya Kira yan uwa Na kusa ya fada musu..

Bayan ya isa sai ya Kira line nata nan aka ce mishi suna emergency direct wajen ya nufa sai ya tarar da ita kwance.. An dai duba Anga ta samu kariya a hannu dukka biyu sai kuma kukan kirjin ta da take a wajen aka yi hoton kirjin tare da dubawa sai aka ga ba matsala nan yace to shi baya son jinyar asibiti tunda karaya ce zasu je gida suyi jinya don raunuka da ta samu an Riga anyi treating nashi da kyar doctor's din duka basu sallama..

Sallamar su ke da wuya sai ga kanwar Baaba tazo nan ma wasu yan uwa suka zo a keken Mara lafiya aka tura ta har bakin motar mijin kanwar nan aka sata a ciki shi kuma da Wasu suka shiga keke napep ganin motar ya cika daga haka suka wuce gida..da yake motar su Baaba ya wuce daukar Mai gyaran karaya shiyasa su malam suka Riga su isowa katifan Autar shi ya fitar da bedsheet aka shimfida Mata a tsakiyar falon tare da maso da standing fan kusa da katifar daga nan ya wuce dakin Umar Farouq domin duba lafiyar shi aiko ya tarar ya tashi

"yi hak'uri Baabar Ku ce tayi accident naje ".da ido kawai yake kallon malam ganin ya juya ya fita sai ya bi Bayan shi a falon sai leke leke yake kamar Mai Neman wani Abu ba dadewa kuma su Baaba suka iso nan ma sai lekawa yake yi yanzu ne malam ya fahimci Baaba yake nema kwantar da ita aka yi nan aka Fara daure Mata karayar ganin haka sai malam ya ja shi daki tunda akwai baki a gidan kada ya musu abun kunya..

**

Haka taci gaba da zuwa wajen aiki ba walwala fara'a kuma an mance rabon da aga tayi..da yake ko staffs din su kan kawo customers su saya kaya a wajen su Wata ce a department nasu Laylerh ta kawo customer..

Kasancewar in abu dayawa zaka saya to ciki zaka shiga in ko kadan ne a farm gate za'a maka packaging ka tafi wannan ita ce dokar company'n.ciki customer'n ya shiga department of fishery yaje don kifi yake so Na dubu Dari uku Bayan an mishi packaging sai aka ce yaje ya biya directly to cashier, Bayan ya biya sai aka Baiwa Penna kudin tunda ita ce tayi link kuma ita ma a accounting take ta kaiwa Accounter kudin..so ta fadawa Accounter an saya kaya a fishery department Na three hundred thousand sai yace su shigar da weekly report da kudin Na ranar ba tare da ya karbi kudin ba..Laylerh ce ta shigar da report din ba tare da sanin Penna bata sa three hundred thousand din a cikin list din ba ta shigar..

Horn ake a gate nan gate Man ya bude yau dai tsam bai yi mamakin ganin oga'n nasu ba tunda ya fahimci satin shi daya da wasu Kwanaki ya dawo..yau dai motocin ba kamar Na kullum bane tunda shi da motoci uku yake yawo yau kuma motoci shida ne suka zo to ko madam ce tazo a'a da ita ne da sunji labari..

Direct gonar rake suka wuce don yau da turawa yazo sun kawo mishi iri ne Na rake Wanda zai yi sugar Mai kyau tunda dama asali company'n sugar suke yi nan suka duba mishi inda ya dace a dasa da kuma lokacin da ya dace daga nan suka yi sallama ya nufi admin block wajen Accountant..

Tun a downstairs din ake ta risinawa Ana gaishe shi guards nashi ke amsawa a haka suka nufi upstairs din wajen zama aka bashi da cool water Bayan yayi seeping Na ruwan sai yace

"kawo mini weekly report Na transactions da aka yi".kallon Penna yayi da yake ita ce sama da Laylerh yace"show him".

gefen shi ta tsaya nan ta Fara operating system din can sai tace"here is it sir"tana mikewa ta bawa pA'n shi kujerar ya zauna a Kai yana duba report din Accountant kuma Na tsaye ta kan shi suna dubawa tare crossing yake yi da yake abun serially ne sai Accounter yace

"this fishery department where is the cashier was it not yesterday ake ce mini an saya kifin three hundred thousand kuma ban Gan shi a list ba".

cashier ce tace"yes Sir an saya mana har Na bawa Penna kudin ta baka sannan nace ta shigar a weekly report, Gashi Nima Na shigar".

"Ohk lemme see". Operating Na system nata tayi ta nuna musu kuma tabbas ta shigar shi dai oga yana zaune shiru sai ma wayar da yake pressing kamar baya wajen..

Bayan an Kira Penna sai Accounter yace" ya Kika yi da kudin jiya?"

"Ehmm Sir typing error ne".

" then where is the money?"

"Na shigar account".

" ina evidence? " nan ta Fara kame-kame da aka ce dole ta kawo sai ta tsorata don ita ta rike kudin ne a ganin ta tunda kullum kudi Na shiga ba zasu gane babu ba nan ta kawo Na sauran transactions da tayi babu three hundred thousand din,nan PA yace"Accountant check your account now".

duba balance din yayi sai aka ga is the same iya transactions Na yau ne babu three hundred thousand Na jiya..

Zuwa yanzu ran boss in ya Kai dubu to ya baci ba tare da ya juya daga basu Bayan da yayi ba ya buga desk dake kusa da shi duk firgita suka yi nan yace

"zaki fada mini inda kudin suke ko sai Na sauya miki halitta".

"Sorry sir....".

" shut up you idiots Wato Shikenan kun samu Na banza Bari kuyi yadda kuke so kun manta promise da duk kuke daukawa kan Ku Fara aiki cewa zaku rike amana so yau Zan bada example da ke ga duk 'yan department Nan da ma Wanda yake shirin aikata irin abunda Kika aikata".

hak'uri aka shiga bashi sai PA'n shi yace"Sir wannan ba aikin mutum daya bane dole su biyu ne".

"Yes Sir Na San ita da wacce tayi typing ne cuxx ba yadda za'a yi taki shigar da transaction Na three hundred thousand din in bakin su ba daya ba".

Tabbas ya gamsu da wannan bayanin sai yace" Na baki just 2 hours duk inda kudin nan suke ki dawar sannan daga yau Na Kore Ki daga aiki".

kuka ta Fara tana fadin"pls Sir ".

" out of my side kan Ki fita tell me waya taimaka miki don duk sai Na Kore Ku yau din nan".

daidai yayi shiru Laylerh ta shigo don daga masallaci take don yanzu bata da walwala ko kallon inda motocin shi suke bata yi ba bare ta san da zuwan shi nuna ta Penna tayi tace"ita ce wannan "duk juyawa aka yi Ana kallon Laylerh so take ta tambaya ko lafiya sai bakin ta ya gagara nan taji muryar shi a bazata yace

"Na Kore Ki daga aiki and from now hence forth ban son ganin ki anywhere near my company tunda sata kuke yi".

Da sauri ta rintse idon ta don sawon rayuwar ta ba Wanda ya taba jefan ta da Kalmar sata sai shi ko lokacin da aka ce ita mayya ce bai Mata Zafi ba kamar wannan Kalmar tana hawaye ta nufi gaban shi yana zaune ta durkusa a kasa ta rike kafafun shi tana kuka tace

" I beg of you kada Ka mini haka this is the first time a rayuwa Na aka tuhume ni da sata"

sake kafafun shi tayi ta hada hannun ta biyu alamar pleading tace

"Dan Allah Kayi hak'uri Ka kuma yi investigating kada Ka Kore ni don da wannan aikin Na dogara".

Mikewa yayi ya bangaje ta tafadi a gefe ya nufi kofa yana fadin" a tabbatar basu sake dawa ba" sannan ya fice...

Comment

Share

©Hafciey Musa

[1/25, 5:37 AM] Hafciey Musa😘: □ *LAYLERH*□

(The prettiest emerald)

Page 18

Kowa Kama gaban sa yayi a wajen ganin boss din ya fice ita ko tana nan durkushe a wajen jin ba alamar motsin kowa sai ta goge fuskar ta ta mike sannan ta nufi office Na Accountant, knocking tayi

"yes come in"a hankali ta tura kofar ta shigo kallo daya ya Mata ya cire Kai yana fadin

"what do you want?"

"Sir an Kore ni daga aiki ba tare da reason ba".

" what nonsense "ya fada yana Mata kallon Tara saura kwata

" trust me Sir I did nothing wrong ".juya system Na gaban shi yayi Bayan ya gama danne-danne yace" you mean bake Kika shigar da report nan ba?"

matsowa kusa da system din tayi tana kallon ciki tace"yes nice".

"And don Rainin wayo zaki ce baki San laifin da Kika yi ba".

" Sir Penna ce ta bani report din ni ko sai Na shigar I can prove my self".tana gama fadin haka bata jira amsar shi ba ta juya ta fice a office d'in,desk Na system da take aiki a Kai taja nan ta Ciro wani pepper sannan ta nufi office nashi knocking ta sake yi nan ya bata damar shiga sai ta shiga"Sir wannan shine list da Penna ta bani you

can have a look"ta karishe zancen tana Mai mika mishi hannu yasa ya Karba nan ya karewa list din kallo ya daga ido ya kalle ta sai kuma yayi danne danne a wayar landline da ke office din ringing daya aka daga

"meet me in my office right now cashier "yana gama fadin haka ya cire wayar a kunnen sa ita ko tana tsaye minti biyu zuwa uku cashier ta shigo mika Mata list din yayi yace" wannan list ne Kika bawa Penna?"

"No Sir this is not my handwriting it's Penna's handwriting"

"Uhum" Inji Laylerh "call Penna" ya fada yana kallon Laylerh ita ko juyawa tayi don fa yau ko me zai faru sai ta wanke kanta daga zargin sata da suke Mata a downstairs ta ganta tana kokarin fita a department din, da sauri sauri take sauka downstairs din har tana hada hanya tana sauka tace"Penna wait".tsayawa tayi nan ta karaso sai tace

"Sir Na kiran Ki"banza tayi da ita taci gaba da tafiya cikin zafin nama ta rike hannun ta tana fadin

"wallahi ko me zaki yi yau sai Mun je"nan staffs da suke downstairs din suka sa Mata baki dole tabi Bayan Laylerh suna zuwa knocking Laylerh tayi suka shiga cashier Na zaune a kujerar dake kallon Na Accountant. Mika Mata list din yayi yana fad'in

"whose handwriting is this". Ba tare da bata lokaci ba tace" it's mine".

"How comes tunda cashier ce ta baki list din".

" Sir nayi re copying ne Bayan ta bani sai Na yaga nata Na bawa Laylerh nawa ta shigar".girgiza Kai yayi bai ce da ita komai ba yace "you can all go "duk ficewa suka yi Laylerh kuma Na tsaye bayan sun fita sai ta hada hannun ta biyu alamar Neman alfarma tace

" sir tunda yanzu komai a bude yake Ka tabbatar ban da hannu implicating Na aka yi pls a maida ni bakin aiki Na".numfashi yaja sannan yace"I wish so amma yanzu is too late cuxx bani da wannan damar da ace nine Na Kore ku to da Zan iya dawo da ke but Boss ne banda wannan hurumin".

shiru tayi can tace"thank you"sannan ta juya ta fita,yaso ace zai iya Mata hanya ta dawo Amma kuma tunkarar Boss din ba Abu ne Mai sauki ba sannan zai ce maybe akwai wani relationship tsakanin su..

Zata Fara sauka downstairs ta hadu da Asabe"sorry Laylerh ".

" khairan in sha Allah"

tace sannan ta fice tana hawaye ba tare da ta sallami kowa ba" for how long haka zai cigaba da faruwa a rayuwar ta Shikenan ita kullum cikin rashin nasarar rayuwa take ba Naseer ba Dada sannan yanzu aikin da shine last hope nata shima babu.napep ta tare ta shiga yana sauke ta ta nufi gida kowa sai tambayar ta ko lafiya ake ganin bata Saba dawa a irin wannan lokacin ba Gashi ba tare da Nabeela ta dawo ba duk banza tayi da su abun bai dame su ba don Tun rasuwar Naseer ta daina walwala bangaren su ta nufa ta ko tarar da ummie kanwar Dada don dama zuwan Dada ne yasa ta daina zuwa dubo Dadda sai dai tayi musu waya yanzu kuma Dada ta tafi dole take zuwa duba lafiyar Maman su sallama tayi ta shiga dakin duk kallon mamaki suke Mata sai ummie tace"lafiya kuwa Kika dawo yanzu "

zama tayi tace" Mun wuni lafiya ummi"

ita dai ummi dalilin dawar ta take son ji shiyasa ma bata amsa gaisuwar ta ba wannan dalilin yasa Laylerh bata fiya son maganar matar ba don tana da shishigi kuma komai ta gani sai tayi magana,nan ta labarta musu abunda ya faru duk shiru suka yi jin basu ce komai ba sai ta fice tare da Daukan buta ta nufi bandaki leka ta Dadda tayi ganin ehh bandaki ta shiga sai tace

"wallahi ni Na gaji da yarinyar nan ya take so nayi da ita,sata fa Babban Abu ne kuma Ai 'Dan yau ko Ka haife shi ba zaka yi shaidan shi ba bare Wanda baka San Asalin shi ba,ba tabbacin ta dauka ko bata dauka ba".

"Haba Dadda Ki kyautata Mata zato mana".

" wani irin kyautata Mata zato kina ganin gidan nan in Dada bata nan sashi daya ne suke sa mini abinci Nabeela kuma naci da yaran gidan to jiya kam koda suka dawo basu tarar da abinci ba so kike Na koma ciyar da ita ne dama dubu goma ne salary'n ta dubu biyar za'a ke bata a rike biyar a San abun yi da shi to yanzu kuma Kinga aikin ma babu ni gaskiya Zan Kira Dada tazo ta San yadda zata yi da ita banda kwashe-kwashe irin nata ma ina zaka kwaso mutum a dandi".

"Yanzu matsalar Ki zama a nan ne?"

"Ba zaman bane daukar nauyin ta ne".

" Ki kwantar da hankalin Ki in wannan ne to ni Zan dauke ta dama Kinga yaran mu sai biyar suke tashi makaranta ba Dan aike ko kasuwa zata ke zuwa mini".

"Ban isa ba yadda Baku jituwa da kishiyar Ki Kice zaki dauki yarinyar da ba'a San Asalin ta ba Ki tafi da ita inko ta kashe miki Aure fa".

" ba abunda zai faru in sha Allah ".

" a'a nasan mijin Ki ba yarda zai yi ba Ki Bari Zan Kira Dada tazo ta dauki abun ta ".

" Kinga kada Ki daga Mata hankali bata Dade da Komawa ba batun yarinya nace Zan dauka Bari ma Kiga yanzu Zan Kira shi a waya Na tambaya ".

kiran shi tayi jin ya Fara ringing sai Dadda tace" kisa a volume yadda Zan ji"a hands free ta sa wayar nan tayi informing nashi sai yace ba damuwa daga haka ta katse kirar

"kuma duk Randa Kika ga alamar zata ja miki damuwa a gidan Ki Ki dawo da ita".to kawai tace don taga fitinar tsohuwar nada yawa.. ita ko Laylerh Tun dazun take jin su ajiye butar tayi ta shigo suna ganin ta duk suka yi shiru sai Dadda ke Mata kallon kasa kasa don tunda tace an tuhume ta da sata taji yarinyar bata kwanta Mata a rai ba

"Ki hada Kayan Ki Laylerh zamu tafi tare".

ita fa har ga Allah ba son maganar Ummi take yi ba Amma kuma ba yadda ta iya dole ta hada Kayan ta,komai da komai nata ta hada nan ta zauna saboda ta San Ummi in tazo gidan sai dare take Komawa shiyasa ta fice a bangaren domin basu dama su Zan ta..a kofar dakin Adam ta zauna bata Lura da kofar ba kwado ba kenan akwai mutum a ciki sai ji tayi an bude kofar har ta tsorata ta mike

"matsoraciya kawai kamar kuma kin San Neman Ki nake".

" to ni kuma me ya faru?"

"Sakon Ki Zan baki Tun Kwanaki sai kuma bana zama daga baya kuma Kika yi wuyar gani".

" wani sako kenan? "Sa hannun shi yayi a aljihu ya Ciro wayar sa sannan ya shiga WhatsApp kan number'n Naseer ya mika Mata..ganin ya Naseer sai taji hawaye ya Fara bin fuskar ta daga nan taga hoton su tare tana kwance a jikin shi sai kace wani mijin ta ko muharramin ta,danne kukan da ke kokarin taso Mata tayi ta dube shi da idanun ta cike da hawaye tace" Dan Allah ko za'a iya wanke mini hoton ya zama Cati".

"Me zai Hana Ai naga hoton yayi haske da gani cameran iPhone ne".

" to Dan Allah Ka biya a wanke mini in sha Allah daga baya Zan biya Ka".

"To me kuma naga hawaye nata bin fuskar Ki". Cikin kukar da ya kufce Mata tace" shine Wanda ya rasu ".

ta fashe da kuka shi ko tausayin ta ne ya Kama shi yace" in sha Allah Zan wanke miki ba sai kin biya kudi ba"

Na gode tace tana cigaba da kuka don yau mutuwar shi sabo ya dawo Mata shiko rufe kofar dakin shi yayi ya tafi..ita ji take har ta koma ga Allah son wani da namji ba zai sake shiga zuciyar ta ba tunda first love nata ya tafi..

Karfi biyar Nabeela ta dawo aiki a hanyar waje ta tarar da ita sai tace"Haba Laylerh Ai in zaki dawo gida kamata yayi Ki sanar da ni ba Wai kiyi tafiyar Ki ba kin San Tun yaushe nake jiran Ki ba don wannan copper Asabe tace mini kin dawo ba da kila har yanzu ina can to ma me ya dawo da ke?"

rike hannun ta tayi suka zauna a wani gefe tace"Nabeela Tun Randa aka yi employing Na a company'n can nake cike da farin ciki da kuma burin a can Zan inganta rayuwa ta Amma Rana tsaka wannan mugun mutumin ya ruguza mini komai".daga haka ta labarta Mata abunda ya faru sosai Nabeela taji tsanar Penna nan ta shiga bata hak'uri a karshe Laylerh ta sanar da ita cewa zata koma gidan Ummi da zama sosai taji wani iri sai tace"Laylerh wallahi ni wajen aikin gaba daya ya fita a raina tsoro ma nake ji".

"Tsoron me kuma?"

"Tsoron shi Boss din mana in har haka yake yanke hukunci ba tare da yayi bincike ba Kinga Nima Ai mistake kadan Zan yi ya Kora ni".

" in sha Allah hakan ba zai faru ba ni din ma don jinin mu bai zo daya bane".

daga haka cikin gida suka koma Bayan magrib su Laylerh suka tafi tana Mai jin zata yi kewar gidan da Nabeela don ta Saba da ita sosai..

Duk da dare ne ras ta karewa gidan kallo Babban gida ne sosai sai dai ba wani ginin kirki bane a gidan flat ne sai daya bangaren da yake kewaye Harda karamin gate aka sa da alama shine Na kishiyar Ummi ne, Na Ummi kuma ba'a kewaye ba..karasawa suka yi shashin dauke yake da Babban baranda sai kofofin dakuna uku da ta gani a gere a barandar..daya dakin ummi ne ciki da falo sai Na tsakiyar dakin yaran ta Mata Na karshen kuma dakin mazan ne..dama dakin ta da kishiyar ta ne ko wacce ciki da falo da bandaki kitchen nasu kuma Na can gefe Bayan wani fadan da suka taba yi sai kishiyar ta tafi gidan su taki dawa dole aka Mata bangaren ta daban Mai kyau..

"Zainab" ta kwala Kira sai ga Zainab din ta fito don kallo suke yi"Wa nake gani kamar Laylerh ".

" nice "nan Zainab ta rungume ta Ummi ko cewa tayi" Kai ta dakin Ku ga Kayan ta".dakin babba ne Wanda dama shine dakin kishiyar ummi sai aka raba biyu aka bawa matan daya mazan daya bandaki kuma a Na mazan yake sannan anyi kofa tsakanin falon Ummi da yaran matan..

Gado ne babba Amma ba Na zamani bane don Na katako ne sai wani karamin kafita sai TV dake makale a bango da kuma dressing mirror sai tarkashen Kayan su"zauna "Zainab ta fada tana nuna Mata katifar ta nan ta zauna sauran yara Mata uku da ke kallo suka gaishe ta ta amsa daga nan abinci Zainab ta kawo musu da kyar taci kadan suka kwanta bacci..

Washe gari Tun hudu da rabi suka tashi ita da Zainab abincin makarantar su suka daura da alama Zainab ke abincin safe, dama tayi miya Tun jiya da dare don haka shinkafa suka daura Bayan ya nuna sai suka raba nan aka daura ruwan wanka.. Sallah suka yi sannan suka Fara yiwa yaran wanka har zuwa lokacin kuma bata ga Ummi ta fito ba..

tsab suka shirya yaran tare da basu breakfast nan Zainab ma ta shiga wanka ita ko sai ta share gidan iya inda zata iya don ta tabbatar in ta share duka Bayan ta ciwo zai yi..Zainab Na fita suka yi breakfast tare abinci kam alhamdulillah a wadace yake a gidan nan ne Ummi ta fito kudin machine ta basu sannan ta koma dakin tafiya suka yi suka bar ta ita daya tattare inda suka yi breakfast tayi sannan ta shiga daki a katifar Zainab ta zauna tana kallo..

Sai karfe goma Ummi ta fito ita dai Laylerh sai mamakin ta take yi sai kace Wata gimbiya durkusawa tayi ta gaishe ta tana Hamma tace

" kawo mini abinci ".da yake Zainab ta nuna Mata komai nan ta kawo Mata sai ta kuma cewa hada mini tea hada Mata tayi ta Fara breakfast ita ko tana takure a waje daya tana gamawa tace

" Ki shigar mini da breakfast Na Alhaji Palo"mikewa tayi tana fadin to daga nan kitchen ta nufa abincin Alhaji ta dauka ta nufi palon,palon ba laifi yana da kyau a center table da ta gani ta ajiye sannan ta fice ummi ko dakin ta koma...

Yau dai tana ganin sarautar Allah shi Alhaji din wani irin Na miji ne da har sha daya yana gida bai fice zuwa wajen aiki ba ..sha daya da rabi taji sun fito nan tazo ta gaishe shi sannan ta koma ciki ummi ko har mota ta raka shi sannan ta dawo daki ta sake Komawa..

"Yau dai tabbas Na yarda nazo gidan yan boko in ba haka ba mutum yayi ta bacci kamar ba lafiya ba". Ita ma baccin tayi sai azahar suka tashi da yake dama ba girkin Rana suke yi ba tunda ummi ce kadai rage Na safe suke yi to ummi debawa tayi ta rage Mata nan taci..tana gama ci ummi tace ta daura tuwon dare sosai mamaki ya kamata tuwon dare ne za'a daura da azahar wannan wani irin bahagon gida ne dole ta daura..

Karfe biyar dai ta gama komai har wanka ummi ce ta fito cikin shirin fita tace" dauko hijab naki mu tafi"da farko ummi bata yi niyar tafiya da ita ba Amma tunawa da tayi akan sata aka Kore ta a wajen aiki sai tace gwara ta tafi da ita kada tazo ta Mata barna a Bayan ta ko taja Mata magana wajen kishiya.. Hijab Tasa suka rufe kofa suka fice ba tare da sun sallami kowa ba..

**

Baaba dai har yau jinya take yi jiki tsam ba dadi dole kanwar ta daya ce ta zauna domin Lura da ita baki kuma kullum akan zuwa suke dole rufe Umar Farouq ake yi a daki hakan yasa bai fiya jin hayaniyar su ba..

Yau din ma kwance take a tsakiyar falon da ya zame Mata bedroom kanwar ta ko Na kitchen tana hada dinner Ummi tayi sallama a kofar falon"Wa'alaikisalam shigo "shiga tayi Laylerh ko zuciyar ta sai bugawa yake tamkar zai fito waje dafa saitin zuciyar tayi Tasa kafar ta daya a falon bakin ta dauke da sallama Ummi ce ta amsa Mata nan ta karasa shiga falon gaban ta Na mugun fadiwa can gefe ta takure waje daya" Baaba Ashe haka ya faru da ke".

"Ehh wallahi tsautsayi fa".

" Allah sarki sai hak'uri da irin mu fa bamu samu zuwa ba sai yau don a islamiyya naji"

"Ba komai wallahi haka ma Mun gode".

" to ya jikin dai?"

"Jiki dai Gashi nan da alama mutumin bai iya dauri ba wani zamu nema".

" aiko akwai Wanda Na sani in sha Allah Zan mishi magana ".

" Amma da kin kyauta mini ya islamiyya kina zuwa kuwa?"

"Ehh"

su biyun a islamiyyar matan Aure suka San junan su Wanda Baaba ta kwana biyu da daina zuwa saboda ciwon kafa da kuma jinyar Umar Farouq..kanwar tace ta fito falon tana fadin"a'a sannun Ku da zuwa ".

" Yauwa sannu ".

zama tayi suka gaisa sannan ta nufi fridge ta dauko musu ruwa ta ajiye gami da zama a bakin katifar da Baaba ke kwance tana kallon Laylerh dake takure a can gaban ta sai fadiwa yake yi" Baaba da alama fa surkuwa Kika samu Kinga can ta takure waje daya".

ba karamin bugawa zuciyar ta yayi ba jin Kalmar surkuwa da kyar ta iya hade yawu idon ta a kasa magana Na fita daya daya tace"Mun wuni lafiya ya Mai jiki".

kallon ta Baaba take yi tana nazarin ta sai kanwar tace ta amsa gaisuwar Baaba ko cewa tayi

"Hauwa wannan Yar Ki ce?"abun Ka da mutum Mai baki sai cewa tayi"a'a ba 'ya ta bace Yar riko ne Adda nace ta kawo ta daga kano to ganin zaman banza take yi sai Na dauke ta ko aika zata ke zuwa mini kafun Na Fara Mata abun talla".

Laylerh ji tayi kamar ta shake Ummi har sai ta daina numfashi,mikewa kanwar tayi ta nufi kitchen domin duba abincin da ta daura daidai lokacin malam da Umar Farouq suka fito a corridor zai Kai shi evening exercise zasu bi ta kofar kitchen Ummi ta gansu.

" Laaa Baaba wannan shine Dan naki ko yaro kam Masha Allah ".

takaici ne ya da haushi ya Kama Laylerh Baaba din ma bata ce da ita komai ba ganin malam zai fice da shi sai ta kuma cewa

" Haba malam kawo shi mu gaisa mana kaga ko a hanya ya Gan mu ya gane mu".

idanun shi ne suka Fara sauya Kala don cikin daga murya take magana jijiyoyin kan shi duk tashi yayi malam din ko a zuciyar shi cewa yayi

"banda Mai daki Na da kwashe kwashe ina ta kwaso wannan ni da zai dake ta ma ido Zan zuba musu"a zahiri kuma sai ya Kama hannun Umar Farouq suka nufo falon har yanzu kan Laylerh a kasa yake a tsakiyar falon suka tsaya Ummi Na gaisawa da malam Laylerh ko daga inda take ta kurawa kafafun shi ido gaban Na fadiwa tabbas wannan kafan da za'a matse ta tabbar jini zai fita kuma ko rantsuwa tayi ba zata yi kaffara ba cewa baya fita.. Kafafun har wani dauke ido suka abun Ka da farin mutum haka kawai ta tsinci kanta da son ganin fuskar shi..

sanye yake cikin dogon wando don tunda Baaba tayi accident ya daina zama da three quarter saboda mutani Na zuwa gidan sai Riga Mara nauyi kofar fita ya kurawa ido,dago kanta tayi kallo daya ta mishi ta sauke Kai kasa zuciyar ta Na bugawa da sauri sauri tsikar jikin ta ko duk mikewa yayi so take ta sake kallon shi a Karo Na biyu ko zata tabbatar da abunda idanun ta suka gane Mata sai ta kasa don ta tabbatar wannan balarabe ne juyawa suka yi malam rike da hannun shi bin shi da ido tayi har suka kusan fita..

Tabbas Tun tsayuwar su a falo jikin shi ya bashi kallon shi ake shiyasa numfashin shi ya Fara fita da sauri sauri don ya tsani kallo da hayaniya gudun kada yayi something stupid yasa malam Jan hannun shi,juyawa yayi yana kallon falon carab idon shi cikin nata da sauri ta sauke Kai kasa shi ko har suka fice bai cire ido daga kan ta ba..

Abinci aka basu ita dai taki ci Amma Ummi ba kunya bare tsoron Allah ta zauna taci abunta har da fadin"Kai Amma miyar yayi dadi sai dai yayi borkono".

"Ikon Allah,Allah kada Ka nuna mini ranar da Zan bi matar nan anguwa don kunyatar da mutum zata yi". Tana gamawa Laylerh ta tattare kwanukan ta Kai musu kitchen sai ta dawo ta zauna jin Baaba Na cewa a bata ruwa ta sha zuwa tayi ta durkusa a gaban ta tare da daga kan ta kadan Tasa Mata ruwan a baki daidai nan

kanwar Baaba ta fito daga corridor'n tana kallon Laylerh tace" ni ko sai nake ganin da kin bar mana Yar goyon Ki ko aika zata ke zuwa mana ko kuma Lura da Baaba in Na shiga wanka ko Na fita".

"Ayya Allah ba don Nima aiki take tayani da zuwa aika ba da Na bar muku ita".

" Ai Ku a cikin gari kuke ko yaran makota zasu je miki Amma Kinga mu nan sai nice Zan bar Baaba a gida naje Na dawo".

"Mu bar zancen nan kawai ba don Nima aikan take zuwa mini ba da Na bar muku ita ko don Baaba".

" Shikenan in sha Allah zamu nemi Yar aiki sai muke biyan ta".hira suka taba suna sallah magrib suka koma gida time din yaran duk sun dawo daga makaranta har sun yi wanka sun sa kaya..Abinci suka ci Bayan sunyi sallah i'sha kuma suka kwanta...

Kamar yadda suka yi jiya da safe yau ma hakan ce ta kasance zuwa yanzu ta fahimci haka al'adar gidan take sai dai yau ko da Alhaji ya fito Ummi ma cikin shirin fita take Bayan ta gaishe su sai Ummi tace"ni Zan fita zanje duba Dadda Na don haka Ki kula mini da gida sosai Bayan azahar kiyi tuwo daidai Na jiya in Na tashi dawa Zan dawo da chefenan miya don yau ba Zan yi dare ba".

"A dawo lafiya" tace nan suka fice ita ko daki ta koma tsoro ne ma ya Fara kamata ganin gidan yayi shiru kishiyar Ummi Na shashin ta ita tunda tazo bata taba ganin ta ko yaran ta ba wannan wace irin tsana ce da har yara uban su daya Amma a raba kan su Wai duk ba Mai zuwa shashin Dan uwan shi..

Azahar nayi tayi tuwo Bayan ta kwashe sai ta shiga wanka ta bar kofofin dakunan a bude koda ta fito sai ta hangi Mata ta fita daga dakin Ummi ta nufi kofa"Ummi har kin dawo ne?"don ita duk zaton ta Ummi ce ganin jikin su daya dukkan su katti ne jin shiru sai ta sake cewa"Ummi sannu da dawa".banza matar ta Mata taki juyawa cikin jin haushi tace"iskancin banza Ana yiwa mutum magana yana tafiya".tsam bata yi don Aji ba sannan bata yi tunanin za'a ji ba kuma bata san lokacin da ta fada

ba sai gani tayi Mata ta juya tace"Dan uban Ki iskanci akan Ki zai kare shegiya Yar tsintuwa waya San irin iskancin da uwar Ki tayi kan ta haifo Ki kuma wallahi Kika yi tsiya yau din nan gawar Ki za'a dauka, kina Yar tsintuwa zaki shigo gida Na har Kice mini iskanci to ni nafi Ki iya barikanci kuma duk iskancin Ki a baya Na kike".Wato wannan ita ce kishiyar Ummi duk da tasan ita ce Mai laifi Amma zagin da ta Mata yayi Mata Zafi sosai daurewa tayi tace"Allah huci zuciyar Ki kiyi hak'uri ".

" an Ki ayi hakurin shegiya kawai ni da kike ganin kinyi kadan nayi dake sai dai nayi da wacce ta kawo Ki".tana gama fadin haka Ummi ta shigo hararar kishiyar ta tayi sannan ta tsaya gefen Laylerh tace"me ya hada Ku?"

"Kawai fa Na shiga wanka ko da Na fito sai naga ta fito daga dakin Ki duk zato Na kece nayi Mata magana har sau biyu bata amsa ba shine nace iskanci kawai Ana yiwa mutum magana yana manna hauka daga nan ta Fara zagi Na".

" an zaga din ko zata Rama miki ne?"

"Kinga Larai Ki fita a ido Na don wallahi zamu yi ba dadi uban me ya kawo Ki shashin Na har daki Na".

" muyi ba dadin mana ce miki aka yi tsoron Ki nake ji ne"daga nan fa suka hau chachan baki ganin da gaske larai so take ta duki Laylerh sai Ummi ta dauke ta sai gidan Dadda bata boyewa Dadda komai ba sai Dadda tace"Ai Tun dama sanda nace kada Ki dauke ta don ita da kishiyar taki kusan duk halin su daya"zuwa yanzu fa Laylerh ta Fara jin Dadda ta fice a ranta akan me daga cewa an Kore ta akan laifin Satan da bata yi ba sai Dadda ta Riga nuna Mata wani hali..

Komawa gida Ummi tayi bata ce da Dadda komai ba don zata je ta daura miya koda Nabeela ta dawo taga Laylerh sosai tayi murna..

Larai fa zuciyar ta sai tafasa yake yi gani take in ta bar Laylerh to taci banza har ita yarinya karama zata cewa iskanci ta barta hijab ta dauka a Daren ta fita sai gidan Dadda..

har bangaren Dadda taje a tunanin Dadda karan Laylerh ta kawo shiyasa take jira in ta gama bayani ta bata hak'uri Amma tana ganin Laylerh ta shigo sai ta mike ta cabko ta sai duka ba yadda Dadda bata yi da ita kan cewa ta bar ta ba taki nan aka Kira Auwalu shima yayi ta magana taki Nabeela ko ganin da gaske matar hallaka Laylerh zata yi sai ta Kai Mata naushi a ciki,a bazata taji naushin don bata yi tunanin Nabeela zata shigarma Laylerh ba nan ta zube a kasa ta rike cikin ta tana ihu ganin haka Nabeela ko hawa ruwan cikin ta tayi ta Mata duka don dama har yanzu haushin zagin da tayima Laylerh take ji sanda Auwalu ne ya daga Nabeela a Daren aka Kira Ummi da mijin su ita Larai kam dama tana gidan har yanzu bata tafi ba..

A bangaren Dadda suka zauna Bayan an gama gaishe gaishe sai Dadda tace"Bello Ka tambayi matar Ka me ya kawo ta gida Na,ko kuma Kai ne Ka bata izinin zuwa ta kashe Yar mutani da duka".kan shi a kasa yace"Dadda a gafarce ni wallahi bada sliver Na Larai tazo gidan nan ba batun abunda tayi kuma ayi hak'uri ".

" Wai har ni larai zata raina irin ta nawa Na Haifa da ina magana zata Ki ji har Auwalu ya Mata magana taki sauraro ni Na gode Allah da Nabeela din ta Mata duka ban son Auwalu ya hanata ba Ai".

hak'uri yayi ta bayarwa nan yasa ta ita ma ta bada hak'uri Ummi ko dadi taji tunda Nabeela ta Mata duka nan ya tattara su suka koma gida aka bar Laylerh a gidan,pain reliever aka saya Mata ta sha sai cewa take

" Nabeela Ashe kin iya dambe shine ranar Kika bar Boss da ya Kore ni,Ai da cire masa hakoran sa Na gaba Kika yi"

dariya suka sanya dukkan su biyu haka suka kwana a katifar su kamar ko yaushe..

Washe gari Ummi tazo gida nan Dadda ta tambaye ta ba wani matsala ko tace ba komai tazo ne ma ta dauki Laylerh "Hauwa wallahi taurin kan Ki ke hada ni dake yarinyar nan ko asirce Ki tayi yaci Ki barta a nan ko so kike auren Ki ya mutu Ki dawo nan mu zama mu hudu a dakin".

" Dadda Nifa banga laifin Laylerh ba ita Larai akan me zata shiga mini daki ba za'a yi magana ba kuma waya San me ta dauka ko me tayi Kinga Laylerh dauki hijab naki mu tafi so nake Na biya gidan Baaba Na dubo ko Mai gyaran Kashi da Na tura musu yayi abunda ya dace".

har ga Allah bata son sake zuwa gidan Baaba Amma ba yadda ta iya dole ta dauki hijab nata suka tafi ba don ranta da Dadda yaso ba..

a kofar gidan Mai keke ya ajiye su nan suka shiga ciki cikin fara'a kanwar Baaba tace

"Au yau ma tafe kike da surkuwar tawa".

ita dai Laylerh kan ta a kasa ta gaishe su sai Baaba ce tace"Ki fita harkar yarinya kin sata a gaba da cewa surkuwa kina da Dan da zaki bata ne tunda Wanda ya Kai auren kin San ba hali yayi".

cikin son jin gulma Ummi tace

"Waye ya Kai Aure kuma meyasa ba zai yi ba"

Kai Laylerh ta girgiza don ta Gaza fahimtar Ummi wani lokacin halin ta Mai kyau wani lokacin kuma kishiyar haka

"Babu fa manta da zancen Baaba ke da Kika Hana mu ita".

"Na isa Gata Ai yanzu ma ita Na kawo muku".

ta fada a tunanin ta zasu ji dadin basu Laylerh da tayi ba niyya su fada Mata sai Baaba tace

"da gaske kike yi?"

"Ehh"

"Amma fa Mun gode sosai Allah bar zumunci". Ameen tace jin basu ce komai ba takaici ya kamata don ita tsam bata zo da niyar bar musu Laylerh ba son jin gulma ne kawai ya sata..

Malam ne ya fitar da shi domin ya duba Baaba da jiki don kullum ya kan fito ya duba ta in ba mutani Laylerh ta daga ido zata kalle shi shima ita din ya sauke idon shi a kanta carab idon su Na shiga Na juna a bazata aka ga ya lumshe idanun shi ya kuma bude su a kanta yana sakar Mata lallausan murmushi..

tsoro da girgici gami da mamaki ne ya Kama su saboda bai taba yin abu makamancin haka ba kenan me hakan yake nufi..

Comment

Share

©Hafciey Musa

[1/25, 5:39 AM] Hafciey Musa😘: *□LAYLERH□*

(The prettiest emerald)

"Wa'alaikisalam shigo mana Gwaggo". Wata 'Yar tsohuwa ce ke sallama a kofar falon Hajiya kaltume shiga tayi "Wayyo tsufa labari mutuwa karar kwana"ta fadi lokacin da take kokarin zama a kasa"a'a Gwaggo zauna a sama mana".

"Kinga duk a gajiye nake gwara dai Na zauna a kasa na mike kafafu na zai fi" Nusaiba dake operating phone nata ne ta dube ta tana fadin"mutum ya tsufa Amma yaki mutuwa".

"Ke yarinyar nan Ki raba ni da mutuwa" murmushi kawai Hajiya tayi nan Khadija ta shigo da sallama ta ajiye Mata ruwa a gaban ta tana fadin"sannu da zuwa Gwaggo "

"Yauwa 'Yar albarka Ai duk kin fi su hankali"

mikewa tayi ta koma ciki domin basu waje su zanta Bayan ta sha ruwa sai tace"Naseer kuma lokaci yayi wallahi Kinga bana gari ne shiyasa ban zo gaisuwa ba sai yau"

"Eh wallahi ya Riga mu gidan gaskiya"

"To Allah jikan shi ya Kai haske kabarin sa,nasan Allah sai ya saka masa kan abunda aka yi mishi".

Ita dai Hajiyar sa Ameen kawai tace don ta San tsegumin tsoffi sai Nusaiba ce ta dakata da Danna waya tace" me aka yi mishi?"

"Ince wannan yarinyar da yake nema har yake sayar Mata da masa a titi mayya ce" .

da sauri Hajiyar shi ta dago Kai ta dubi Gwaggo tace

"wace yarinya yake nema?"

"Ai kaltume Na fada miki akwai Wata yarinya da take gaban Dada tsohuwar 'Yar aikin Ku to fa kullum sai yaje wajen ta kin San anguwa daya muke,ranar kawata tazo ina Mata rakiya sai Na Gan shi yana saida masa sai nake ce Mata ta duba Yaron masu kudi soyayya ta maida shi haka..budan bakin ta sai tace mini Na San da wace yarinya yake tare nace a'a sai ce mini tayi Ai mayya ce anguwar su daya Kwanaki har za'a kona ta wani yazo ceton ta kila Naseer din ne".

Duk shiru suka yi tare da maida hankalin su gaba daya kan zancen ta ganin ehh fa sun maida hankali sai ta Kara da fadin" Ai a anguwar mutani sai mutuwa suke yi daga baya ne aka gane ita ke cinye su"..

"To tabbas wannan Karon taci abunda yafi karfin ta tunda d'a Na daya tilo ta cinye wallahi ita ma sai ta bishi inda yaje" gaba daya idanun ta ya rufe ta mance cewa Dan ta diabetes yake da shi kuma kuskuren likitoci ne yasa shi rasa ran shi duk da kwana ne ya kare

"gaskiya kaltume ya kamata Ki dau mataki "

"Allah tsarki ya Naseer taimakon sa ne yaja mishi Gashi wannan Karon ajalin sa ya taimakawa wallahi mom kada Ki bar ta".

" Ai ko ina ta shiga a duniyar nan sai Na nemo ta ta dandana radadin mutuwa sannan iyayen ta ma su dandana rashi".

"In tana da su kenan".

 fadin Gwaggo,number'n Dada tayi dialing sai taji baya shiga Upstairs ta nufa can sai Gata ta fito da Vail tana fad'in

"Gwaggo Bari naje gidan Dada naji ina yarinyar take Ki zauna a nan Ki huta Khadija zata kaso miki abinci".

" to Allah bada sa'a".

Nusaiba ce ta mike tare suka fice duk maganar da suke yi a kunnen Khadija sosai hankalin ta ya tashi nan ita ma ta gwada kiran Dada number'n baya shiga Nusaiba ke driving don ta fahimci ran Hajiyar su a bace yake sosai, koda suka isa gidan sai gani suka yi kofar a rufe neighbors suka shiga nan ake sanar musu Ai Dada ta tafi Sudan tunda aka yi bakwai Na Naseer kila kuma don mutuwar ce bata sanar da su ba.

"yarinyar da take saida Mata masa fa?"

"Gaskiya yarinya kam ko da ta dawo ita daya muka gani bamu San inda ta barta ba kila a Taraba ta bar ta".

" yanzu ba Wanda ya San ta ina take a Taraba?"

"Hajiya kenan Ku da take muku aiki shekara da shekaru Baku sani ba sai mu makota".

Nan tayi godiya tare da musu Sallama ta kuma yi niyya duk inda Laylerh ta shiga sai ta nemo ta gida suka koma Gwaggo Na ganin su tace" an dace kuwa?"

"Wallahi Dada bata kasar".

Alhamdulillah Khadija ta furta a zuciyar ta saboda ta kawo musu ruwa ne

" Ehhh lallai Nima Na kwana biyu banga Dada ba kenan yanzu zama zaki yi Ki jira dawar ta?"

"Zan San abun yi".

**

Duk mamaki ne ya cika su me hakan ke nufi shin yarinyar yayiwa murmushi har kasan ran shi ko kuma lafiya ya Fara samu hannun shi malam ya rike suka nufi corridor ita dai sauke Kai kasa tayi ta rasa dalilin da yasa duk lokacin da suka hada ido sai zuciyar ta yake harbawa da karfi ..Ummi dai da ido ta raka su tana mamakin Meya sa kullum ba shi kadai ke fitowa ba dole da wani a gefen shi..

kanwar Baaba ce ta katse musu tunani dukkan su biyu da fad'in" Laylerh kin San kasuwar yelwa ne?so nake Ki mini shefene tunda Allah ya kawo Ku ba don haka ba ni da Kai Na zanje ".

Karab ummi ta amshi zancen" Allah sarki wallahi bakuwa ce bata San kasuwar yelwa ba don ba lallai ta gane ba".

"Ayya Wai dama so nake kan ta dawo Na gama shinkafar tana dawa kuma sai nayi miya".

" ba komai Ki je zata yi miki shinkafar me aikin ta Ince Na kawo muku ita don ta taya Ku ne".

kallon Baaba tayi sai ta gyada Mata Kai alamar Ehhh taje saboda su ba masu saurin yarda da mutani bane da har zasu bar Laylerh ta musu girki."ina fatan dai kin iya?"

"Ehh" tace sai ummi ce tace"mutum da yayi aiki a hotel me ba zai iya ba"

"Hotel?" Suka hada baki wajen tambaya.

"kwarai kuwa hotel Amma fa ba Wai ita din yadda kuke tunani bane".

Shiru duk suka yi Amma maganar bai gamsar da su ba aikin hotel kuma Ai sai yan iska nan dai kanwar Dada tace" zo Na nuna miki daidai yadda zaki yi".

mikewa tayi ta bita kitchen sai ta nuna Mata komai yadda take bukata daga nan ta wuce ciki domin shiri Laylerh kuma ta daura girkin...

Dawar ta yayi daidai da sauke shinkafar nan ta raba sai ta fidda kajin da ta saya aka gyara Mata Tun a kasuwan yelwa Ummi Na ganin haka a ranta tace"wallahi Ai dole ma Na bar yarinyar nan a gidan nan don mu kwashi rabon mu tunda yanzu nice uwar dakin ta komai ta samu ni zata kawo Wa sannan ba Zan tafi ba sai naci abincin nan don Na fahimci dadi suke ci".

tare suke aiki a kitchen din Ummi kuma da Baaba suna Dan taba hira Amma Rabin hankalin Ummi Na kan kitchen da abunda ake dafawa

"Ai Saratu naji dadi da Kika kawo mini Mai gyaran nan Kinga yanzu na ji sauki sosai".

"Ayya" tace tana Dan daga wuya da leken kitchen din can kuma tace

"Alhaji kam ba zai je kasuwa bane naga Rana yayi sosai kuma d'an naki baya da aikin yi ne?"

shiru Baaba tayi don Tun da can ta San Saratu da son jin gulma sai cewa tayi"akwai aikin da suke yi a ciki ne"daga nan bata sake cewa komai ba..

Bayan sun gama hada komai sai suka fito falon suka zauna Ummi Na fadin"sannun Ku da aiki".

"Ai Laylerh zaki yi Wa sannu don ita tayi Rabin aikin".

" Ai zaku ji dadin ta tsam bata da kiwuya".

ta fada don su Dad'a jin dadin Laylerh din ita kuma ta samu abunda take so..

Abinci Na nuna aka Sawa Umar Farouq a tray kamar yadda aka Saba nan tasawa Ummi tana gani ta Fara Washe baki da fadin

"Ayya Ai nikam a koshe nake"ta maida hankalin ta kan TV kamar da gaske..

Na Umar Farouq ta fitar ta ajiye a dining in malam ya fito sai ya Kai mishi sai tayi feeding Baaba tunda hannun ta duk a karye suke, ba yadda bata yi da Laylerh a sa Mata abinci ba tace kada asa Mata ta koshi a karshe tace to in taji yunwa tazo ta deba tace to..

Malam ne ya fito zai Kai ma Umar Farouq yana Daukan tray Ummi tace"kina zaune manya Na aiki maza je Ki karbi tray din Ki Kai masa".mikewa tayi malam ko cewa yayi

"a'a yi zaman Ki kawai Na hutar da ke"a'a Alhaji bar ta zata Kai ina da'a ga d'an da babba Na aiki yana zaune ".

shi fa halin matar bata mishi ba kuma yaga in yaci gaba da biye Mata musu zasu yi Gashi ita matar Aure ce..tray din ta dauka sai yace" in kinje daki Na karshe zaki ajiye a kofar "

to tace nan ta nufi corridor tana sake yaba haduwar gidan ta ciki gaban ta kuma sai fadiwa yake a yayin da take nufar dakin, tana isa tayi sallama taji shiru ta sake yi

nan ma shiru sai ganin malam tayi yana zuwa nan ya bude kofar dakin sai ta shiga da sallama..

Kwance yake ya maida duk hankalin sa kan yatsun hannun shi Yana irgawa ita dai ko kallon inda yake bata yi ba kamar yadda shi ma bai kalle ta ba malam ne ya nuna Mata inda zata ajiye abincin a hankali ta karasa cikin dakin kamshi sai tashi yake ta ajiye a center table nan malam yace" Yauwa Na gode kina iya tafiya Zan bashi abincin ".

juyawa tayi a zuciyar ta tana tunani a bashi abinci kuma wannan kam sakalci ne ko rashin lafiya don ta San wannan ya Kai ace Yana da yara dayawa Amma shima bashi abinci ake nan dai ta dawo falon ta zauna lokacin har Ummi ta kusa cinyewa sai faman yaga Kashi take yi..

Tana gama ci tayi musu sallama tare da fadin" duk Randa Kika samu fita sai Ki biya gida Na Ki dauki Kayan Ki tunda zaki ke zuwa muku aika in kuma baki zo ba sai Na sake zuwa Zan kawo miki".

"To" tace a zuciyar ta kuma cewa tayi"Ai kun shiga uku da ita don kullum sai tazo ".daga nan tayi tafiyar ta..

**

Babban malami ne zaune cikin dakin da yake aiki gaban shi tray ne da yashi a ciki shafa yashin yayi da tafin hannun shi sannan ya Debi duwasu ya rufe a tafin hannun shi ya girgiza sannan ya wasa su a tsakiyar yashin nan suka wawwase daya yayi gabas daya yayi Arewa daya kuma yayi kudu da yayi yamma,debe duwasun yayi yace

" tana Arewa masu gabancin Nigeria ".sai ya sake wasa duwasun yace da bakon shi

" dauki daya"hannu bakon nashi yasa ya dauki dutse daya sai mamalmin yayi murmushi yace

"Tana Taraba".nan ya sake debe duwasun tare da wasa su yace ya dauka wani dauka yayi sai malamin yace

"a Taraban tana cikin jalingo ".

Alhamdulillah bakon yace sannan ya Kara da" Allah taimaki malam yanzu ba za'a iya binciko mini anguwa da gidan da take bane?"

"Gaskiya wannan ne kuma ba Zan iya ba don banda ilimi a Kai iya abunda Zan iya yi shi Na maka". Godiya yayi yasa hannu a aljihu nan ya Ciro dubu goma ya ajiye sannan ya Ciro dubi biyar yace

"Na gode sosai ga wannan ayi sadaka da shi sannan gobe goben nan zan tafi Taraba da yardan Allah".

" Shikenan mu ko zamu tayaka da addu'a Amma fa yadda Na ganin nan bata cikin Tashin hankali ".

" ba wannan bane damuwa na malam Na Barka lafiya".

nan yasa takalmin shi ya fice sai motar sa hanyar gida ya Kama..

Yau dai matar shi taga sauyi a fuskar sa ba kamar kullum da yake hade da rai ba"Abban Ahmad me muka samu naga yau sai murna kake yi?"

"Abunda ya sani farin ciki in Na fada miki bakin ciki zai saki".

" to ni kuma Ai abu daya ne zai sani bakin ciki in Ka fada mini kuma Na San yanzu kam ya maka nisa ba samu zaka yi ba".

murmushi yayi sai yace"Ai kuwa in dai batun Laylerh ce to ita ce Na gano".mikewa tayi daga zaunen da take tace

"wallahi baka isa ba yarinyar da Tun yaushe ta shiga duniya yanzu zaka ce Ka San inda take"

banza yayi da ita yaci gaba da Danna wayar shi ganin Wanda yake Kira ya dauka sai yace" Dan Allah so nake a mini booking Na motar Taraba gobe kuma turn one nake so".

Bayan ya gama sauraron jawabin da aka fada daga daya bangaren sai ya kashe wayar ya nufi bedroom yana kuma kiran wani number baya ta rufa mishi Ana dagawa yace

"Dan Allah ba Wanda Ka sani a taraba don gobe a can Zan kwana so nake Na samu masauki". Shiru yayi yana jin amsar da ake bashi can yace" to Dan Allah Ka kokarta".

daga nan ya kashe wayar tare da jefa ta tsakiyar gado akwati ya dauka a saman wardrobe ya Fara jera Kayan sa a ciki,ita ko cikin bala'e tace

"wallahi sai Na fadawa iyayen Ka kana shirin shiga duniya nemar Wata Yar iska Ka barni da yara".

wanka Mata Mari yayi ya nuna ta da yatsa yana fad'in "in baki da hankali Ki kuma kiran ta da Yar iska ke Allah sa yara dubu ta haifa sai na aure ta kuma iyaye Na in sun ji alfahari da ni zasu yi".

Dafe inda ya mare ta tayi tana kallon shi yana cigaba da shirin sa har ya gama nan ya rufo akwatin ya fice a gidan...

Bashi ya dawo ba sai dare lokacin ma tayi bacci ko a jikin ta..da yake ranar laraba ne kuma alhamis da litinin yana azumi karfe hudu ya tashi kitchen ya nufa ga mamakin sa sai yaga ba ta mishi abincin sahur ba flaks ya taba nan ma yaji ba ruwa sai ya dawo bedroom din yana fadin

" sai kiyi Ai auren Laylerh kamar nayi na gama".

"Haka zaka cigaba da bauta don nasan ita ba kalar Ka bace".

" dama Ai nasan idon Ki biyu kina ji Na ba bacci Kika yi ba Niko Zan tabbatar miki ita din Kala tace don ba Zan dawo gidan nan ba sai Randa aka daura mana Aure da ita".

"Aikin banza" ta fada tana Mai bashi baya shi ko shirin shi ya cigaba da yi har aka Kira assalatu nan ya ajiye Mata kudi a kan gado yana fadin"sai Na dawo" da yake ya San ba amsa Mai dadi zata bashi ba shiyasa ma bai jira amsar tata ba yayi tafiyar sa kuka ta fashe da shi tana fadin"wannan wace iriyar rayuwa ce da zai je inda bai sani ba akan yarinyar nan".

Shi fa yayi niya ko sama da kasa zasu hadu to sai ya Aure ta don bai ga dalilin da zai yi ta Mata bauta Tun tana yarinya kuma ya kwallafa rai akan ta ace wani daban zata aura ba shiyasa ma bai damu da batan uwar ta da yayan ta ba don tuni ya fahimci ba wani son shi suke ba Mai son shi Abbu ne kuma ya tafi gwara dai ya nemo ta ita daya don in ta tabbata bata da kowa sai shi dole ta Aure shi..

Tasha ya wuce nan ko ya samu su biyu kawai ake jira ko da ya iso kuma saura mutum daya zama yayi a seat nashi inda aka shigar da Kayan shi boot kamar Na ko wani passenger.. Agogon hannun shi ya kalla ganin zaman minti biyar yayi daya passenger'n bai zo ba sai ya Fara masifa"shiyasa ni wallahi ban taba tafiya da motar haya ba,motoci nawa nake da shi da shiga mota Na nayi kawai nayi tafiya ta kun zo kuna batawa mutum lokaci ni din kun San wanene"..

Hak'uri suka yi ta bashi ba tare da sanin Dan karya bane nan ya amsa wayar da ake kiran shi"to banda abun Ka taya za'a yi Na sauka a gidan matawalle baya gari Ai gwara Ka Kira shi Ka sanar da shi wani Dan uwan Ka zai zo kaga daga nan sai ya sanar da Mai gadin shi zuwa Na zai fi kuma Ka tura musu number Na".suna gama waya dayan passenger'n yazo nan motar su ta tashi...

**

"Baaba ina ganin yau dai tunda ga Laylerh ba ke kadai bane Zan leka gida naga halin da yara suke ciki".

" Ehhh gaskiya ya kamata kam"daga haka mikewa tayi ta Fara shiri tana gamawa ta sallame su nan Laylerh ta zauna tana kallon TV Baaba ko Na kwance karar Ac da kuma Na TV ke tashi a hankali..

Bayan asr irin karfe biyar Baaba tace

"Kinga tunda har yanzu bata dawo ba daura mana abincin dare".

"To me za'a dafa?"

"Normally da dare bamu iya cin abinci Mai nauyi ba don haka Ki daura cuscus kawai".

To tace nan ta nufi kitchen ta Fara hadawa Ai to Masha Allah saboda ta samu komai da ake bukata ita mamaki ma suka bata don fridge dake kitchen din ba abunda babu.. yaji vegetables (carrots,green beans)da koyi sai ice fish ganin komai yayi yadda take so sai ta fito falon tace

" Na gama ban San yadda Zan raba ba".

"Ki duba saman cabinet d'in zaki ga set Na kulolin Umar Farouq sannan kulan malam kuma zaki Gan shi kife a kondo Ki hada ma Umar Farouq smoothy da kuma ruwan Zafi a flakes nashi".

to tace nan ta nufi kitchen din mamaki sosai ya kamata ganin kulan Umar Farouq da Na malam akwai banbanci nesa ba kusa ba

"wannan wani irin so suke mishi da har cooler'n shi yafi Na Baban shi".

tsaki taja gami da buga keyar ta da kan ta tana fadin

"Ai normally maza in basu so ake taba musu abun su suna sayan kula da kudin su kila shi ya sayawa kan shi"a haka ta bar zancen ta kwashe abincin ta ajiye a dinning daidai nan malam ya dawo daga masallaci sai ya dauki Na Umar Farouq ya Kai mishi daki ita ko taimaka ma Baaba tayi wajen yin alwala daga haka suka yi sallah sannan suka ci abinci.. Sai Bayan i'sha kanwar Baaba ta dawo nan aka ce ta kwana a dakin Auta kafun gobe ta gyara dakin baki, Baaba da kanwar ta kuma dama tare suke kwana..

**

"Har tafiyar ya taso to jira ni Bari Na duba maka kaya cikin Na marigayi Abokin Ka". Dan bappan Naseer ne da yazo Tun rasuwa sai yau zai koma da yake su a kauye suke kuma kusan age mate ne da Naseer din abun Ka da family sai suka zama abokanaye don shi Naseer bai dauki duniya a bakin komai ba..

mikewa tayi ta nufi dakin Nusaiba da Saudat Na biye da ita a baya don tunda aka yi rasuwar ta rufe dakin..ya Dan yi kura Amma ba sosai ba da yake ko ina a rufe nan taji hawaye Na bin fuskar ta tare da jin tsanar Laylerh Mai tsanani..wordrobe suka bude nan suka Fara sorting Kayan shi sai Nusaiba tace

" Mom kin fa San 'yan kauyen nan kada Ki bashi kananan kaya don ba Sawa zai yi ba gwara dai a bashi jumper".

"Yeah Mom kuma kada Ki bashi Mai tsada sosai don ba maintaining kaya suke yi ba" fadin Saudat

"Nikam ina wayar shi ne ma?"

"Ai ko ina yake ma yanzu kam zai mutu cuxx nasan za'a yi ta Neman shi Amma fa a ranar da za'a Kai shi asibiti da hannu Na nasa mishi waya a aljihu".

" banda abun Ki Saudat Ai wancan karamar ne Babban nake magana a Kai".

"Ki duba bag Na laptop nashi". Duk maganar da suke yi Hajiyar su Na jin su bata ce komai ba sai sorting Kayan da take yi nan Nusaiba ta duba wayar sai taga a kashe

" Laa kin ganta nan a kashe Bari nasa ta charging ".

nan ta Ciro charger Tasa sai suka cigaba da sorting Kayan suna gama cire mishi toilet aka nufa su brush da soso da dai abubuwan zubarwa aka tattara sannan pics nashi da suke dakin kuma duk an jujjuya shi..

Sun Dade sosai a dakin abun Ka da Mai kudi sai hak'uri bawan Allah Na can yana jira Nusaiba ce tace" Mom ba zai ji dare ba kuwa?"

"Ai ba kauye zai wuce direct ba zai biya gidan kawun shi ya kwana sai gobe zai wuce".

Cigaba da aikin suka yi suna gamawa Nusaiba ta cire wayar tare da kunnawa nan Saudat tace" Ki bar wayar mana".

"Cire chajan Zan yi Na tafi da shi daki Na".

" gadon Wayan zaki yi ne".

Cikin bacin rai Hajiyar su tace"yan Iskan yara yaushe ya mutu har kuke batun gado ko dai farin ciki kuke da wancan shegiya ta cinye mini d'a".

duk shiru suka yi wayar Na Kawa Nusaiba ta kunna screen din nan take ta zaro ido hannun ta har rawa yake yi a zuciyar ta tace

"mace kuma a jikin ya Naseer shi ma yana irin rayuwar can ne?"

ganin yadda tayi poster yasa Saudat cewa lafiya bata iya bata amsa ba sai wayar da ta mika Mata ita ma sosai tayi mamaki Hajiyar su Na tambaya lafiya suka yi banza da ita cikin zafin nama ta fisge wayar sosai gaban ta ya fadi ganin abunda ko wuka za'a sa Mata a wuya cewa zata yi Naseer ba zai aikata ba

"wallahi wallahi shine rantsuwar duk wani musulmi ni Hajiya kaltume nayi rantsuwa cewa sai naga Bayan yarinyar nan kuma cikin kankanin lokaci bata San da Wa take zance bane...

Hmmm Laylerh kina ruwa har wuya"

kun sha errors kam yau ban samu tym Na editing ba Afwan

Comment

Share

©Hafciey Musa

[1/25, 5:40 AM] Hafciey Musa😘: *□LAYLREH□*

(The prettiest emeral)

Na sadaukar da page nan ga duk wani ko Wata Mai tayani sharing alkhairan Allah ya Isa Gare Ku a duk inda kuke

Page 20

A Tasha motar ya sauke shi nan yayi Kira a waya ba jimawa kuwa aka tura mishi number'n Mai gadin gidan da zai sauka dialing number'n yayi Ana picking yace"Assalamu Alaikum nine bakon da aka tura Mimi number'n Ka yanzu haka ina Tasha".

"Ohk to bawa Mai keke wayar". Tsaida keke yayi tare da mika mishi wayar sai yace" Ka kawo shi Nana Aisha ciki kusa da masallacin in kunzo Ku tambaya ina ne gidan Alhaji Musa fari za'a nuna muku don kusan kowa ya San gidan".to Mai keke yace gami da mika masa wayar shi nan suka hau titi sai kallon garin yake aiko sun sha tafiya kam daga Tasha zuwa anguwar suna Fara shiga anguwan ya Fara karewa anguwar kallo a fili yace

"gaskiya hanyar anguwar nan bata da kyau Amma Na Lura duk da lungu ne masu kudi Na boye a anguwar nan".

"Akwai su kam Amma yawancin su ba mazauna gari bane". Mai keken ya bashi amsa suna isa daidai wani shago Mai keke yayi parking yace

" Dan Allah muna tambayar gidan Alhaji Musa ne"kallon tsab mai shagon ya musu ganin su da daddare sannan suce suna tambayar gidan Babban mutum haka sai ya girgiza Kai yace"Nima bako ne gaskiya ban San gidan ba kuje gaba Ku tambaya ".

Mai keken ya dago jirgin Mai shagon don yadda ake kidnapping Na mutani a jalingo abun sai Wanda ya gani kuma Ai shima ba sanin passenger'n da ya dauka yayi ba shiyasa ya juya ga Sani yace" Ka Kira mutumin dazun sai Na fada masa inda muke daga nan sai ya kwatanta mana gidan".

ba musu yayi dialing number'n Mai gadi bai jima yana ringing ba ya daga"ranka shi Dade gamu a bakin wani shago kusa da masallacin Amma mutumin yace bai San gidan ba".

"Ku mike a hannun Ku Na dama gida Na karshen shine".

Katse kirar suka yi nan suka bi kwatancen da ya musu Ai gidan ba wani nisa da shagon sauka sani yayi a napep din yana fadin" nawa ne kudin Ka?"

"Ka bada dubu daya Mai gida". Zaro ido Sani yayi yace" malam haska ido Na Ka gani".

"Me kuma Zan gani a ciki?"

"Nace Ka haska Ka gani to Bari kaji ni din Dan jalingo ne dawa gida nayi anguwar ce ban sani ba don haka kudin Ka Dari biyu ne".

" yafi haka Mai gida "jin shiru shiru bakon bai shigo ba sai Mai gadi ya leka nan ya tarar da su sai yace" kudin shi Dari uku ne".cirewa Sani yayi ya bashi suka nufi ciki Sani Na fad'in "Ai bai San Na gama jin labarin jalingo gaba daya ba ance masu keke in sun dauko Ka daga Tasha da sun Lura Kai bako ne sai su zuga maka kudi kuma dole haka zaka biya".

" lamuran sai a hankali "

fadin Mai gadi yana mika masa hannun suka yi musabaha a lokacin da suka shiga second Gate Na gidan" Masha Allah "Sani ya furta ganin ga gida har gida ina ma ace shi ke da gidan nan wallahi da ko yan uwan matan shi ne sai sunyi waya kan su zo in ba haka ba ba za'a bude gate ba..

BQ Mai gadi ya Kai shi da yake an share mishi nan ya kawo mishi abinci tare da mishi sai da safe ya koma bakin aikin shi..

Alhaji Musa Babban mutumi ne Amma ba sosai ba don sa'an su Sani ne kudi ne kawai ya zauna mishi asalima shi din garin su daya da sani to yanayin aikin shi a abuja yake zama sai in yazo da matar shi da yaran shi ne suke sauka a gidan yanzu ma gobe suna tafe shiyasa yan uwan matan shi suka zo suka share ko ina har suka yi girki Wanda suka Sawa Mai gadi ne ya bawa Sani da yake matar Yar nan ce..

Daki fa sosai yayi Wa Sani a fili yace" ohh duniya Allah Na azurta Wanda yaso a kuma lokacin da yaso yanzu Wa zai dubi gidan nan ace before da Mai gidan muke zuwa roron geda".

karewa dakin kallo yayi nan yayi wanka yaci abinci sannan ya kwanta yana Mai addu'ar Allah sa a anguwan Laylerh take yana ganin ta zai Kira gida ya sanar musu sai a daura Aure a can shi ko ya dauke ta su koma ko kuma su Kama hotel don ya San in sun koma wannan fitinenniyar matar tashi ba barin shi zata ji ya kwashi bonanza a jikin karamar yarinyar nan yadda yake so ba da wannan tunanin bacci ya dauke shi...

Washe gari da safe Bayan ya gama duk wani abunda zai yi nan Mai gadi ya kawo mishi breakfast da ya sayo musu yaci yana mamakin Mai gadin shin baya tsoro ne yake zaune a gidan nan shi daya Bayan yayi breakfast ne sai ya Dan fita domin ganin anguwa sai kallon gidajen wajen yake yi..

Karfe goma Na safe jirgin Alhaji Musa yayi landing nan driver yaje airport ya dauko su lokacin Sani Na daki yana waya da malamin sa kan cewa a sake dubawa ko za'a ga location nata..

Kamar yadda Na fada ba Babban mutum bane don ba zai wuce 35 fa sai matar sa wacce ita ma bata wuce 25 ba da yaran su guda biyu dukka Mata,shigar musu da Kayan su driver yayi already an musu oder'n abinci a Babban falon ya ajiye musu sannan yayi musu a huta gajiya ya fita..daki ya shige ruwa ya wasa matar ma daki ta wuce da yaran domin musu wanka..

"Naji ya iso ko zaka nema mini iso a wajen shi".

" Ai yanzu wanka zai yi ".fadin driver da yanzu fitowar shi kenan shiru Sani yayi nan ya zauna a kujerar da ke kusa da Na Mai gadi suna sauraron radio tare Bayan irin awa daya yace" Yanzu kam Na San ya huta Ka nema mini ganin shi".Mikewa Mai gadi yayi ya nufi cikin gidan can sai Gashi ya dawo yace"ance yanzu lokacin cin abincin shi ne"da yake Sani is a proud person nan take ran shi ya baci don ba kowa akewa irin wannan wulakanci ba fashe Wanda yazo maula to in Musa Na tunanin maula yazo yayi kuskure shi da ya sani ma da bai sauka a gidan ba hotel ya Kama...

Sai 12:30 aka ce Wai ya shigo lokacin kuma bucket ya dauka ya nufi Dam domin deban ruwa Mai gadi ya sanar da shi sakon ya juya ya nufi falon kenan yaji Ana horn a gate din juyawa yayi sai gani yayi Mai gadi ya nufi kofa da gudu ya wangale motoci uku masu tsada suka danno hanci cikin gidan"wannan kuma wane ne?"parking aka yi da wuri daya daga cikin guards nashi yazo ya bude mishi kofa,kasancewar yau Babban Rana ce ga ko wani musulmi Amma a wajen bakon Alhaji Musa ba haka bace don kananan kaya yasa wuyar shi Harda sarkar cross kenan shi din ba musulmi bane, ya shiga gaba biyu kuma Na baya sun sashi a tsakiya "tsarki ya tabbata ga Allah'n da ya halicci wannan mutumin Ashe ba namu bane" fadin Sani yana kuma kallon shi ganin ehh sun zo kusa da shi sai ya basu hanya tsam ba Wanda ya Lura da shi cikin su falon suka karasa suna shiga Alhaji Musa ya mike tsaye yana fad'in "Barka da zuwa Sir" zama yayi sannan ya nunawa Alhaji Musa wajen zama nan shima ya zauna guards nashi ko suna Dan nesa da su mikewa Alhaji Musa yayi ya bashi hannu suka gaisa sannan yace "Mun same Ku lafiya sir ya aikin dai?"

"Lafiya" yace ba tare da ya sake fuska ba duk da Alhaji Musa aboki ne a Gare sa sai dai kasancewar shine babba a wajen aiki yake girmama shi matar sa ce ta shigo falon dauke da sallama tana fad'in "Mun same Ku lafiya ranka shi Dade"." Lafiya kalau".

" bismillah ga ruwa ".ta fada sannan ta juya ta basu wuri" Sir ga ruwa".

"No thanks ina sako Na?"

Envelope ya mika mishi nan ya Karba ba tare da ya bude ba,Sani ne yayi sallama ya karasa cikin falon idon shi akan bakon waje ya samu ya zauna yana kallon bakon yace"Barka da war haka Mai gida".

"Uhmum" bakon ya fadi, yace naga jiji da kai a tare dashi ya Kara burge ni fadin Sani kenan Alhaji Musa ne ya katse mishi tunani da fadin"Kai ne bakon nawa ko?"don shima a tunanin shi Sani yazo ne don ya nemi wani abu a wajen shi

"Ehh nine baka gane ni bane Sani ne fa Dan gidan malam Audu".

"Allah tsarki lafiya Na Gan Ka a taraba?"

"Kasan Bappa Na Mai sunan Ka Ai to Allah ya mishi rasuwa kuma kafun ya rasu ya bar iyalai".

" anzo wajen"Cewar Alhaji Musa a zuciyar shi

"to yaran shi biyu ne mace da Na miji Tun macen Na karama aka bani ita to Bayan rasuwar shi duk sai suka wase ba Wanda ya San inda suke sai jiya naji labarin ita yarinyar a garin nan take shiyasa nazo ".

" Ayya ya sunan ta?"

"Laylerh".

" me yasa baka nemi sauran yan uwan ta ba sai ita kadai".duk juyawa suka yi suna kallon bakon Alhaji Musa da yayi maganar Amma sai gani suka yi yana Danna waya kamar bashi yayi magana ba"tambayar Ka yake yi answer him"

Cewar Alhaji Musa.. Da farko fa guy din ya burge shi Amma yanzu haushi ya bashi da wannan tambayar don gani yayi kamar yasan me a zuciyar shi to ko dai ya San Laylerh din ne

"Ai iyayen ta ma Na neme su Na rasa ita din ma har Na cire rai a kan ta".

"Hmm" ya fada kuma dukkan su sun ji to guy nan lafiyar shi, Alhaji Musa ko kallon Mai gidan nashi yayi don ya karanta psychology haka kawai ba zai sa baki a maganar da ba tashi ba ruwa baya tsami banza

"to ni dai kaga gobe ma Zan juya abuja wannan oga nane sako Na kawo mishi Mata Na da yara Zan Bari a nan ban San taya Zan taimaka maka ba".

Cikin jin takaicin su dukkan su biyu don gani yake saboda sun fi shi kudi ne suke wani sha mishi kamshi yace" ba komai a haka ma Na Gode da aka bani masauki ".

kallon agogon dake daure a sinsiyar hannun shi yayi yace" mu zamu tafi time Na juma'a yayi"ya karishe zancen yana kallon guards nashi wannan dalilin yasa suke jin dadi aiki a karkashin shi ya kan basu lokacin ibada duk da shi ba musulmi bane nan dukka falon suka mike Harda sani shine farkon fita ma sannan bakon an bude mishi mota ya shiga an rufe har sun tada motar sai ya sauke glass Na motar yace"Sani ko?"gane abunda yake nufi da wuri Alhaji Musa ya daga Kai yana fad'in "yes Sir sunan shi Sani" daga haka ya rufe glass din suka bar gidan...

**

Girkin Rana take kokarin hadawa a kitchen sai taga kamar gilmawar mutum ta Bayan ta ya fita, ko da ta juya da wuri sai bata ga kowa ba fita ta kofar kitchen din tayi zuwa waje ta dudduba nan ma ba kowa sai ta dawo tana tsaki gami da cewa kila imagination nake yi banda haka taya mutum zai wuce a baya Na ban gani ba..ci gaba da aiki tayi sai ta sake ganin wulgawa wannan Karon kamar mutani biyu ne

kuma Na karshen kamar da Riga orange ne Wanda in ba karya tayi ba kamar Randa tazo gidan shine a jikin Umar Farouq barin aikin tayi ta nufi corridor domin ta duba duk da an Mata iyaka da dakin shi tana gab da isa taji muryar malam a Bayan ta yana fad'in "lafiya kuwa" cikin hade rai yayi tambayar don shi fa he don't trust anyone when it comes to his son waya sani kila Wanda suke illata shi suna da connection da ita shiyasa suka turo ta gidan, zuciyar ta Na bugawa da sauri sauri sai kuma ta daura murmushi akan fuskar ta lokacin da ta juyo gaba daya tana fuskantar shi tace"abu nane ya fadi shiyasa nake dubawa ".

" to banda abun Ki me zai kawo Ki nan har Ki Yada wani abu"murmushin ta sake yi tana fad'in "wannan tsohon in ya gano ni Na shiga uku" a zuciyar ta a zahiri kuma sai tace"a zato Na dazun da nake shara da safe ne ya fadi".yi tayi kamar tana dubawa ganin yana tayata sai tace"Ka Bari kawai kila ya fita rabo".da yake shi ba Mai bincike bane sai bai tambaye ta mene ne bane ganin ta juya sai ya raka ta da ido ita ma taji a jikin ta ita din yake kallo shiyasa ta Dan daga kafa ta bacewa ganin shi tana tunanin ko meye dalilin da yasa basu son ganin wani a gangan shi sai su iyayen shi sannan ita dai bata taba ganin shi shi daya ba duk yadda aka yi something is wrong da wannan tunanin ta koma kitchen ta cigaba da aikin ta malam ko baya ya koma ya shige dakin shi don dama wankan juma'a ya dawo yi Bayan ya gama shiryawa ganin da sauran lokaci sai yace Bari ya leka Umar Farouq yana bude dakin yaga ba kowa toilet ya leka nan ma ba kowa sai ya cire hular sa yana fifita da shi ya fito falo yace"Yaron nan fa baya ciki"Baaba dake kwance da karyayyen hannu kokarin zama tayi ta kasa nan ya taimaka Mata ta mike dakin suka koma sun duba ko ina baya nan cikin Tashin hankali suka nufi kitchen kallon Baaba dake hawaye Laylerh tayi tace"lafiya kike kuka Baaba".

"Kinga Yaron nan ne bamu gani ba?"

"Wa ke nan". Ta tambaya don ita ta San ba yara a gidan nan malam yace

" Umar Farouq mana".

"Wallahi dazun naga gilmawar mutum ta baya Na koda Na juya sai banga kowa ba a Karo Na biyu Na sake gani kamar Harda shi shiyasa Na nufi dakin sa domin Na duba sai Ka tare ni a hanya".

" banda abun Ki Yar nan Ai da Tun a lokacin Kika fadi sai mu San Na yi".yana gama fadin haka ya nufi waje direct gidan Mai anguwa yaje ya sanar masa sai Mai anguwa ya Kira sarkin matasa ya sanar da shi a take aka Fara kiraye kirayen waya Wa matan San anguwan Harda wadanda suke wajen sa'a aka ce su dawo nan duk suka Fara nufo gida don anguwan akwai hadin Kai..

meeting aka hada na matasa nan sarkin matasa yace"yanzu wani dabara kuke ganin zamu yi domin Kama su dumu dumu in sun dawo da shi".

wani Dan kwaya ne yace"Eh oga ni fa gani nake kawai a Bari in motar ta shigo anguwar nan sai a rufe hanyar din, ta hanyar ajiye durum a hanyar da taya sannan wasun mu sai su tsaya a wajen karshen fita anguwar kuma kusa za'a bubbuga, nan ma wasu sai su tsaya a wajen kasan in tire motar tayi fashi dole su tsaya sannan ba zamu basu clue Na yadda zasu gane an Dara musu tarko ba duk watsewa zamu yi kowa ya zauna a kofar gidan Baban shi ko kofar gidan shi sannan kada mutani su wuce biyu a waje daya, majalisar kofar gidan malam din ma mutum biyu za'a Bari ta haka ne kawai zamu Kama su".ya kare zancen cikin zallar maye da kuma karkatar da bakin shi gefe

tafa mishi suka Fara don tabbas shawarar shi tayi yan Iskan anguwan yan shaye-shaye aka ajiye a farkon shiga da kuma karshen layin anguwar saboda sun San kan tsiya, sannan cikin anguwar kuma sun rabu biyu biyu wasu ko in Ka gani zaka ce harkar gaban su suke yi don wasu busa sigari suke yi sosai Mai anguwa da malam suka yaba da basirar tasu don tabbas ko Wa yake wannan aikin yau sai dubun shi ya cika tunda dole mota zata shiga anguwar ta kuma fita..

Tun suna jira da kauna shiru har lokacin juma'a yayi nan rabi suka yi sallar juma'a a anguwan Bayan sun idar rabi suka sake yi har zuwa karfe uku shiru nan masu gaggawan cikin su suka Fara fad'in "kila sai dare zasu dawar da shi..

" karfe biyar daidai Wata bakar mota Mai tinted glass ta shigo anguwar da gudu tana shiga aka rufe hanyar shigar tare da Fara kiraye kirayen waya kan cewa motar ta shigo kowa ya kasance cikin shiri Ai kuwa nan kowa ya maida hankali ba jimawa motar ta wuce kofar Mai anguwa murmushi yayi yace"ko ma wane ne Kai yau taka ta kare?"a haka motar ta riga wuce matasan Ana jira aga ta tsaya a kofar gidan malam matasan da suka buya a wajen su fito ga mamakin su sai gani suka yi an Kara gudun motar ta wuce kofar gidan ta nufi barin anguwar, matasan dake karshen layin anguwar kuma suna jiran isowar ta don yanzu sune last hope Na yan anguwan Ai ko daga nesa suka hango ta a guje ta nufi fita anguwar tsam basu tashi

ba sai ma sigari da suke sha motar Na zuwa daidai wajen da suka buga kusa dayawa ta take birki suko dariyar shakiyanci suka yi tare da mikewa wadanda suka buya ma duk suka fito zagaye motar suka yi ganin shiru ba'a fito ba sai wani ya daga sanda ya fasa glass Na motar kasss kake ji nan take aka bude gidan driver aka fiddo shi, Wanda suka ganin ne ya matukar basu mamaki ba kowa bane face wani politician da duk jalingo sun San da zaman shi shake wuyar shi yan kwayan suka yi nan fa duk matasan suka nufi karshen layin anguwar don hukunta duk Mai aikata haka ciki kuma Harda su malam da Mai anguwa da sauran dottaban anguwan masu jini a jiki"Honorable "Mai anguwa ya furta shi ko cewa yayi" me haka ne Wai daga shigowa Na anguwa za'a taru a Kai Na haka".

"Ai ba Honorable kake ba wallahi ko gomna kake mu ba ruwan mu in Kayi laifi hukunta Ka zamu yi ba sai Mun jira hukuma ba bare a bada cin hanci a sake Ku Ai kasan halin mu yan anguwan nan".Cewar sarkin matasa

" Dan Allah Mai anguwa ko zaka fada mini me ke faruwa? "Ince dazun Na Kira Ka batun filin nan" ya nuna wani fili dake gefen su"nace maka Zan zo Na duba yaushe kake da lokaci kace kana wani abu nazo da yamma yanzu kuma nazo da yamma duk yan anguwa kun hadu a Kai Na".tabbas ya Kira Mai anguwa lokacin kuma suna jiran dawar Umar Farouq shiyasa yace yana wani Abu yazo da yamma to Amma duk da haka zargi ba zai tsallake kan shi ba nan Mai anguwa yace a bincika motar shi..

A yayin da duk yan anguwa suke karshen layi cikin anguwar ya zama saura Mata kawai keke napep ya ratsa cikin anguwar Wanda da gani kuma ta kogi suka fito daidai kofar gidan malam keke napep din tayi parking wani mutum ne ya fito sanye da mask hannun Umar Farouq ya rike ya fiddo shi a hankali ya tura kofar gidan sannan ya tura shi ciki gami da Jan kofar suka bar wajen koda suka je fita anguwar ta inda suka shigo ta nan din suka fita Maida musu taya da durum din da suka rufe hanya da shi suka yi sannan suka yi tafiyar su..a kasan bishiyar gwava ya zauna shiru da gani he is very weak fiye da kullum gyangyadi ma yake a wajen, Laylerh ko ruwan tattasai da ta gyara ta fito domin ta zubar a lambatun gidan sai ganin mutum tayi a zaune ihu ta saka gami da Komawa ciki da gudu..kasancewar shi Mara son hayaniya ne ihun da tayi ne yasa shi farkawa idanun shi jazir kan shi sai sarawa yake kamar zai rabe gida biyu..

Ihun da tayi ne yasa Baaba da kanwar ta mikewa a kofa suka hadu da ita"lafiya kuwa "Kanwar Baaba ta tambaya

" wallahi Na Gan shi yana kasan bishiyar gwava".da wuri suka fice ita ko harga Allah tsoron shi take ji don gani take kamar shi din ba mutum bane aljani ne,su Baaba ko suna fita suka yi arba da shi daga nesa kana iya ganin yadda idanun shi suka rine zuwa ja..

A can karshen layin kuma Bayan an gama bincika motar ba abunda aka samu sai honorable yace "ni fa nazo duba filin nan ne sannan duba da yadda garin ya koma Na dauke masu kudi shiyasa Na badda Sahu a haka Amma kuma Na kasa fahimtar meke faruwa".

Su fa har yanzu basu wani yarda da shi ba wayar malam ce yayi ringing yana dagawa duk suka zuba mishi ido sai ji suka yi yace

" Alhamdulillah gani nan zuwa"yana cire wayar yace"malam kaji Wai Gashi can a gida".hak'uri suka bawa Honorable sai sarkin matasa yace

"tabbas a cikin mu akwai munafuki don dama sai da Dan gari ake cin gari,duk wani motsin da muke akwai Mai sanar musu shiyasa da suka ga hankalin mu ya dawo nan aka maida shi gida wannan meeting din ma gaba ba haka za'a yi ba kuma ba Zan fadi yadda za'a yi ba kalilan ne da Na aminta da su zasu sani".

duk sun yarda da zancen shi nan kowa ya Kama gaban shi honorable kuma yaje ganin fili..

Malam Na shiga hannun shi ya Kama suka nufi dakin shi Isar su da fadawan shi kan gado duk daya ne don sun Lura he is very weak

"wannan Karon kuma da kasala ya dawo "Baaba dai shiru tayi nan duk suka fice aka bar shi yayi bacci, Laylerh kam tsoron gidan ne gaba daya ya kamata tsoro yake bata Gashi ta zaga fahimta shi din mutum ne ko aljani..

**

"Masha Allah komai yayi yadda nake so".ta fada tana karewa hoton Laylerh din kallo saboda Sawa tayi ayi editing aka cire Naseer ya rage Laylerh kadai..

" Nusaiba ke da Saudat Ku Yada hoton nan a kafafen sada zumunci sannan kuce bata tayi Ana Neman ta Ku sa number Na a kasan hoton kan cewa duk Wanda ya ganta ya Kira number'n za'a kuma bashi kudi masu yawa".

To suka ce nan take ko wacce tayi posting Na hoton a duk social media da take yi..kiran wani number tayi Ana picking tace"akwai hoton da Zan tura maka yanzu Kai da team naka kuyi sharing nashi a kafafen sada zumunta don nasan shine aikin Ku kada Ka damu da kudin".shiru tayi tana sauraron me yake fadi sannan tace"ita din Yar uwa ta ce bata tayi muna Neman ta".nan suka yi sallama ta tura mishi hoton..

Cikin abunda bai zaga hour biyu ba sai ga hoton Laylerh yana yawo a duniya cewa ta bata yan uwan ta Na Neman ta kuma duk Wanda ya gani sai yayi reposting Ana kuma addu'ar Allah bayyanar da ita...

Comment

Share

©Hafciey[1/25, 5:40 AM] Hafciey Musa😘: *□LAYLERH□*

(The prettiest emerald)

Washe gari ya Kama ranar asabar kwance take akan sallaya don tunda tayi sallah Asuba bata tashi ba,ba bacci take ba gaba daya tunanin ta ya karkata izuwa yadda za'a yi a samo Laylerh sai jin wayar ta ya Fara ringing tayi, daga kwancen ta mika

hannun ta domin daukar wayar tana tsaki.. ganin sunan da yayi appearing a fuskar wayar yasa da wuri tayi picking "Wa'alaikisalam".daga can daya bangaren aka ce" Hajiya an samu labarin inda yarinyar take saboda wani ya yi rubuta a kasan page na a kasan hoton ta yace tabbas mota daya suka shiga sannan tare take da Wata babbar Mata take ".

" Wai a ina ta sauka?"

"Yace har cikin jalingo suka shigo tare to shi dai a Tasha ya bar su bai San inda suka yi ba".

" baka da connection a jalingo ne?"

"Gaskiya babu".

" to taya Zan isa ga security officers Na garin ko police station? "

"Za'a duba miki Hajiya" daga nan sallama suka yi tana maimaita jalingo a ranta tabbas journey'n Ummul khair yazo karshe..

Ido ya Kara zarewa yana mai kallon hoton Laylerh da yayi appearing a facebook da yake yi

"to wane ne ke Neman Laylerh kuma Bayan ni?"

zama yayi akan katifar yana karanta comment Na mutani inda ake addu'ar Allah bayyanar da ita gaba daya ya zama confused wadanda ya dace su neme ta su ma ba'a San inda suke ba Bappan ta kuma ba dalili ko hujjar da zai sa shi Neman ta Amma koma wane ne sai ya gane, number'n da aka rubuta a kasan hoton ta ya dauka nan ya shiga dialing...

A bangaren Hajiya kaltume kuma zaune suke a dining suna breakfast da yaran ta biyu wayar ta ya Fara ringing kallon number'n take yi ganin bakuwar number ce"Mom Ana kiran Ki kiyi picking mana".

"Bar shi kawai number sabo ne"

"Mom kin manta number'n Kika sa aka rubuta a kasan hoton yarinyar can" Saudat ta kare zancen tana dafe goshin ta, hannun Hajiya kaltume har rawa yake yi ta yi picking..

Bangaren Sani ko shiru yayi yana jiran ace wani abu sai yaji shiru sai cewa yayi"Assalamu Alaikum ".amsa mishi sallamar tayi shi ko murmushi yayi jin muryar mace ce aikin ba zai mishi wahala ba

" Hajiya naga kina shigiyar yarinya ko?"

"Eh Ka Gan ta ne" murmushi yayi yana mikewa tsaye yace"tabbas Na Gan ta in takaita miki yanzu haka Na San inda take".ajiye spoon Na hannun ta tayi ta mike tsaye su Nusaiba ma ido suka zuba Mata"a ina take fada mini yanzu Zan tura a dauko mini ita ".

" kwantar da hankalin Ki Hajiya Ai ba haka kawai Zan mika ta Gare Ki ba".

"Me kake so?"tayi tambayar da sauri

"Wani dalili ne yasa kike Neman ta sannan ke wacece a Gare ta". Tsaki taja cikin bacin rai tace

" and who the hail are you da zaka yi interfering a family matters".

"Tunda haka Kika ce bye" da wuri tace "wait me kake son sani?

" Ke din wacece a Gare ta kuma meyasa kike Neman ta".

"Ni pendon ta ne mahaifiyar ta ta rasu shiyasa nake Neman ta".

" mahaifin ta fa?"ya jefa Mata tambayar da bata yi zato ba

"yanzu ya fita a nan"murmushi Mai sauti yayi har taji shi sai yace"a halin yanzu tana kwance a asibiti".

"Me ya faru?"

"Bata da lafiya" shiru duk suka yi can sai tace"to ya za'a yi?"

"Zan sake kiran Ki" daga haka ya katse kirar bai jira Cewar ta ba.safa da marwa ya Fara cikin dakin yana fadin

"tabbas wannan matar karya take yi tana da nata manufa Na Neman Laylerh to wace ce ita? koma wacece kan ta isa ga Laylerh Zan Riga ta".wanka ya shiga Bayan ya fito ya sauya kaya sai yace Bari ya shiga suyi sallama da Alhaji Musa tunda yau zai wuce.. wajen Mai gadi yaje nan suka gaisa kan yayi magana sai Mai gadi yace

"Ai kamar kasan Alhaji Na Neman Ka don ya gama shiri kila wani abu yake jira da ya wuce "mikewa yayi ya nufi falon duk da Tun abunda suka mishi jiya ran shi a bace yake har yanzu Sallama yayi Alhaji Musa Na zaune yana karanta magazine shiga yayi ya mika masa hannu suka gaisa sannan yace" kaga ni yau Zan wuce shiyasa nace a mini magana da Kai muyi sallama ".

" Allah sarki zaka wuce kenan"ya tambaya fuskar shi a hade"ehh ya batun yarinyar Ka samu wani information ne?"

"Hmm naga Wata Tasa an Yada hotunan ta a duk kafafen sada zumunta Wai....." Dakatawa yayi da zancen sa saboda knocking da aka yi ko bai waiga ba yasan kamshin turaren da yaji Na mutumin jiya Dan Rainin wayon nan ne Ai ko shi din ne yau ma sanye yake cikin kana nan kaya da gani ma daga wajen exercise yake..ganin Alhaji Musa ya mike dole shi ma ya mike hannu duk suka mika mishi Bayan ya zauna duk sai suka zauna ganin hankalin shi gaba daya yana kan wayar hannun shi sai Alhaji Musa yace"Ehem ina jin Ka"ya karishe zancen kasa kasa yana kallon Sani "Ai Na fada maka sai Na dauki number'n matar Na Kira ta tare da tambayar ta dalilin da yasa take Neman yarinyar sai tace mini ita pendon ta ce".

" yeah maybe ita din pendon tace".

"A'a pendon Laylerh daya ce sannan Tun kafun a haifi Laylerh ta bar garin su in fact bata ma San Laylerh ba,matar daga yadda take magana ba gaskiya a ciki saboda Baban Laylerh ya rasu ita ko cewa tayi yanzu ya fita kaga kenan tana da nata manufar Neman ta". Dogon numfashi Alhaji Musa yaja yace" to Kai yanzu wani mataki zaka dauka?"

"Ni addu'a nake yi kuma so nake Ku tayani da addu'a Na isa Gare ta kan su Riga ni"

" in sha Allah" Sani zai yi magana sai Michael Sunday yayi gyaran murya kallon Sani Alhaji Musa yayi yace "alright kaje kawai Bari zamu yi magana". Mikewa yayi yana hararar Michael Sunday kasa kasa ba tare da sanin sarai ya Gan shi ba ya fice..hankalin shi a kan wayar shi yace

" I went through it"Wato sakon da aka kawo mishi jiya kenan nan suka cigaba da tattaunawa cikin sirri suna gamawa ya mike fuskar shi kamar kullum guards nashi suka rufa mishi baya har mota Alhaji Musa ya raka shi sannan ya juya gida ya sallami iyalan shi ya wuce..

**

Yau din ma girki take a kitchen saboda ta zama Mai aikin gidan dama kanwar Baaba ba son aiki ne da ita ba Gashi Allah ya kawo Mai taimakon ta shiyasa ta daina komai sai dai tayiwa Baaba mopping Na jikin ta,kofa suka ji an taba sai kuma shiru ya biyo baya ba'a shigo ba tsorata duk suka yi har Laylerh dake kitchen don ta gama fahimtar gidan gaba daya abun tsoro ne..tsalle tayi ta shigo falon tana fadin"suprise "duk ajiyar zuciya suka sauke ganin Auta ce hannu pendon ta ta bude Mata da gudu

ta fada jikin ta suka rungume juna suna farin ciki" yapendo nayi fushi ace Baaba tayi accident Amma ba Wanda ya fada mini sai dazun baba ya Kira ya sanar mini ta wayar Wata Yar dakin mu da take boyewa".

"Yi hak'uri Auta"

Baaba ko cikin fada ta Fara fad'in" ke sai yaushe zaki yi hankali ne kina ganin yanayin gidan nan kike irin haka daga yau kada Ki Kara".

"Yi hak'uri ba Zan Kara ba ya jikin Ki" ta tambaya lokacin da take masowa kusa da Baaba "da sauki" Laylerh ko cigaba da aikin ta tayi don ta fahimci Yar gida ce Bayan ta gama hada komai sai ta fito falo daga sama har kasa Auta ta kalle ta tana tabe baki tace"Baaba wannan kuma wace ce?"

"Yar aiki muka samu"tsaki taja dole Laylerh ta daga ido ta kalle ta

" zaki Fara halin Ki ko na rashin son mutani dake da yayan Ki ko"

fadin Baaba Laylerh ko waje ta nema ta zauna tare da maida hankalin ta kan TV, hira suke su ukun can ta mike ta nufi kitchen sai ta tarar abincin ta yayi rabawa tayi Tasa ma Baaba ta kawo don ciyar da ita ake yi ita ko tare suke ci da kanwar Baaba, ganin yau ga bakuwa sai ta hada musu su uku Bayan an gama bawa Baaba sai ta fito ta ajiye musu,kallon kyama Auta ta Mata tace

"ni gaskiya ba Zan iya cin abinci da ita ba Ki sa mini a plate".Wato kyama Na take yi to wallahi bata sanni bane banza Laylerh ta Mata taci gaba da cin abincin ta ita ko jingina Bayan ta tayi da jikin kujera tana Danna wayar yapendon ta har suka gama cin abincin, Laylerh taso tayi banza da ita sai taga rashin dacewar haka yarinya da gidan su sannan Ai ita ma alfarmar su take ci nan ta nufi kitchen ta debo Mata tare da ajiye Mata a hannun kujera tace"ga abincin Ki".

"Don iskanci kina Yar aiki zaki ja mini Aji sanda Kika gama duk wani abunda zaki yi sannan zaki kawo mini". Har cikin zuciyar ta take jin tsanar Laylerh don ta tsani taga wani a gidan su Musamman mace gani take kamar zata kwace Mata iyaye da yayan ta,haka Laylerh din ma jinin ta bai zo daya da yarinyar ba,Kallon Auta Baaba tayi tace

" wallahi Ki Kama kan Ki bar ganin ina kwance Zan ci mutuncin Ki"tura baki tayi tana mikewa tace"kan Ki ake ji"

su fa sun Gaza gane dalilin da yasa yaran basu son wani ya shigo gidan su,direct kitchen ta nufa abincin shi ta dauka dakin Umar Farouq ta nufa knocking tayi jin shiru sai ta tura a hankali ta shiga tsurawa Bayan ta ido yayi Wato kofar shiga hakan ne ya sata juyawa taga me yake kallo

"are you expecting someone else "ta tambaya duk da ta San ba jin ta yake yi ba karasawa ciki tayi ta zauna... gyaran dakin da take mishi kullum yau kam ya gagare ta don ba son Laylerh take yi ba ganin ya Fara bacci sai ta fice a dakin... nata dakin ta nufa ba ita ta fito ba sai Bayan asr..

Da yake ranar da yapendo ta fita ta biya ta gidan Ummi ta dauko Mata Kayan ta shiyasa Tasa doguwar Riga sannan ta daura wani gyale a kanta..

Ganin time Na daura abinci yayi yasa ta fita a dakin ta ta nufi kitchen yau duk jin ta a takure take abinci ta daura Auta Na fitowa ta Mata kallon sama da kasa tana kallon gyalen da ta Daura a kan ta Wanda yake Na Autar ce ranar da tayi sanitation Na dakin ta ne ta gani nan ta tambayi Baaba wannan fa sai ce Mata tayi Na Auta ne in tana so ta dauka Ai haka take da careless kuma ta daina sa shi shine fa yanzu ta daura, Mai abu da abun shi kuma kallo daya tayi tace" Dan uban Ki waya baki damar sa mini gyale Na ke har kina da kimar sa kaya Na a matsayin Ki Na Yar aiki" duk da zagin ya doki kahor zuciyar ta musamman in aka yi duba da shekarun Auta wanda ta tabbatar dole ta girmi yarinyar amma sai bata ce da ita komai ba zare Vail din tayi a kanta ta mika Mata sai cewa tayi

"abu duk tsamin jikin Ki yake Allah sauwaka nasa abunda ya fito daga wajen Ki dirty girl kawai".

in ran Laylerh yayi dubu to ya baci wannan cin fuska har yaushe yarinya karama ta tsaya zagin uban ta kuka har wuyar ta yazo da gudu ta nufi kitchen sai ta tarar da Kanwar Baaba a ciki fita tayi ta nufi corridor tana jin Baaba nayi Wa yarinyar holo duhu kawai take gani can a karshen dakunan gidan dake Jere akwai wani lungu inda suke sa takarkace Wanda kuma manne yake da dakin Umar Farouq wajen ta shige tare da sake kuka Mai cin rai ita Shikenan kullum haka zata tabbata yanzu ba don gadara da gidan su da yarinyar ke yi ba,da ba abunda zai Hana ta fasa Mata baki tunda ta zagi uban ta..

Cikin baccin da yake yi ya Fara jin hayaniyar kukan ta kasancewar saitin window dakin sa take kuma jikin gadon sa, nyamusa fuska ya Fara yi jin kukan ya Fara yawa sai idanun shi suka Fara rikidewa zuwa jawur gashi nauyi suka mishi dafe kan shi yayi da kyar ya mike ji kawai tayi an bude kofar dakin tayi zaton kuma wani ne ya shiga shi ko lungun ya nufa sai ganin mutum tayi a kan ta,daga kafar shi ta fahimci wane ne Amma kuma tsoron kallon fuskar shi take yi jin kamar idon shi na yawo a kan ta ya sata daga Kai aiko ita yake kallo ganin yadda idanun shi suke a take tsoro ya shige ta don in bata manta ba jiya taji kamar ance har wuka ya taba chakawa wani jikin ta Na rawa ta mike da gudu zata bar wajen,tsayawa tayi cak tare da juyawa jin ya rike hannun ta, hannun shi tabi da kallo tana kuma mamakin gargasa dake kwance a hannun sai dai ta Gaza kallon shi gaban ta sai fadiwa yake don namiji bai taba rike ta haka ba banda Naseer da ta taba fadawa jikin sa..

Jin shiru har yanzu bata fito ba sai yapendo tace"Auta dubo Laylerh tayi shiru a ciki ruwa Na tafasa tazo ta juye a flaks".

banza tayi kamar bata ji ta ba sanda ta sake maimaitawa nan ta mike tana fadin

"banda Rainin wayon yarinya tasan aikin ta Ai ta shige ciki"

cigaba da mita tayi ta nufi corridor birki taja tare da zare idanun ta ganin fa yayan ta ne rike da hannun Wata mace,macen ma Laylerh ihu ta sake da wuri Laylerh ta juya ta kalle ta tana kokarin kwace hannun ta ta gagara duk da a ganin ta ba wani riko Mai karfi ya Mata ba, kuka Mai karfi ta sake Wanda ita kan ta bata San dalilin shi ba, da wuri kanwar Baaba tazo corridor tana tambayar ko lafiya poster tayi tana ganin ikon Allah ita tsoron abunda zai yiwa Laylerh din ne ma ya Kama ta nan ta Fara magana kasa kasa

"Kinga tunda yana jin maganar ki Kice ya bar ta kada ya illa ta musu yarinya a samu a jarida".Bakin ta Tasa kan hannun shi duk da taji kamshin turaren shi da kuma laushin fatar bai hanata yin abunda tayi niya ba cizo ta ta Kai mishi a hannu don taji me yapendo tace kuma ita ma tsoron abunda zai Mata din ne ya sata cizon shi don ya sake ta,sake ta yayi ya nufi daki sai ji suka yi ya rufo k'ofa da gudu Auta ta koma falo tana fadin"Baaba wallahi Ku sallami yarinyar nan don kokarin cusa kanta take yi wajen yaya na har fa rike hannun shi tayi waya San nan gaba me zata yi mishi ".shiru Baaba tayi tana nazarin maganar ta ita ko sai ta ringa implicating Laylerh a wajen su kasancewar yapendo bata ga abunda ya faru Tun farko ba sai bata ce komai ba..

Laylerh Na jin duk abunda take fadi a zuciyar ta tace lallai wannan yarinyar munafuka ce sai faman goge bakin da da hannun rigar ta take don har yanzu kamshin hannun take ji a bakin ta,duk ba wannan bane matsalar ta ji take kamar har yanzu hannun shi Na bakin ta Wanda in ta tuna da yadda gargasa ke kwance a hannun Tasa bakin ta sai taji kamar tayi amai shiyasa take ta goge bakin don gani take kamar gargasan ta ci..

**

Tun Bayan tafiyar Alhaji Musa ya shiga gari ko Allah zai sa a dace ya samu Laylerh kudin machine dai kam alhamdulillah ya kashe..

Tunda ta gama abincin dare ta wuce daki don bata son zama inda Auta take gudun kada suyi abun kunya, wanka tayi a toilet tayi sallah sai ta kwanta a zuciyar ta take tunanin "har yaushe Zan cigaba da zama ba dangi don su ma Na San karshe dole Na bar Musu gida daga nan kuma ko ina Zan koma sai Allah" tunani taci gaba da yi har i'sha yayi tayi sallah sannan ta kwanta yunwa take ji sai dai ba zata iya fita falon ba kada ta gamu da Auta...

Washe gari jin har lokacin mutum bai sake kiran ta ba Gashi she is desperate sai ta Kira layin Sani har sau uku bai daga ba zuwa yanzu kuma ranta ya Fara baci don da farko murna take yi ta same ta yanzu kuma murnar Na shirin Komawa ciki Kira ta sake yi sai taji an daga

"Haba malam ya Tun jiya zaka ajiye ni".

"Yanzu me kike so?"

"Ka fini sanin abunda nake bukata a wajen Ka". Murmushi yayi yace

" nawa zaki biya Na baki yarinya? "

"Ce maka aka yi bani da hankali ne da Zan baka kudi Bayan ban tabbatar tana hannun Ka ba".

" hujja kike so kenan?"

"Ehh"katse kirar yayi ya shiga gallery sannan yayi marking hoton Laylerh ita daya har guda biyu kasancewar yana da hotunan ta sai Na ukun kuma su biyu ne WhatsApp ya shiga ya tura Mata ganin ya shiga sai ya Kira ta yace" Ki duba WhatsApp naki Na turo miki da sako "da sauri ta katse kiran nan ta duba kiran shi tayi kan tayi magana ya Fara dariya yana fadin" ko ba ita bace?"

"Ita ce wallahi yanzu Zan turo maka da kudin mota dubu talatin nasan zai ishe Ku har Ku iso Ka tura mini account numbern ka".

" Amma an Dade ba'a raina mini wayo ba irin ta yau ce miki aka yi ni din shashasha ne yarinyar nan fa sato miki ita Zan yi sannan Kice Na mota zaki bani".

"Nawa kake so?"

"Ki bada dubu Dari biyar a kawo miki ita har inda kike".

dubu Dari biyar ta maimaita " ehh ko yayi kadan ne in ba zaki biya ba sai Anjima ".

" Ehh mana Kai da baka kawo yarinya ba".

"Amma ke ba iyayen ta bane ko?"

"Meyasa kace haka?"

"Gani nayi in iyayen ta ne murna zasu yi har a bani tukwuicin da yafi wannan tunda an tabbatar tana waje Na"

"To Ka bani lokaci zanyi tunani

murmushi yayi lokacin da ya katse Kira yace" Ashe dai tana da kudi tana turowa Zan Adana su naci gaba da Neman Laylerh ina samun ta har honeymoon zamu je da kudin"..

A bangaren Hajiya kuwa apartment Na mijin ta ta nufa bata boye mishi komai ba ta sanar da shi yadda suka yi nan ya hau holo

"Ashe baki yarda da kaddara ba mutum ya mutu kin biyewa zancen mutanin duniya cewa cinye shi aka yi".

"Haba Alhaji in an bar ta fa haka zata ci gaba da cinye yaran mutani ni dai Kayi hak'uri Ka bani kudin nan".

"To ni da kike gani duk abunda ya biyo baya Ki kuka da kan Ki sannan batun kudi kuma Ki samu Accountant zai baki".

" Na gode "tace nan ta fice kiran Accountant tayi ta sanar mishi ba jimawa taji alert jikin ta har rawa yake yi ta Fara dialing numbern Sani don tace ya turo asusun bankin shi.....

Na kusa koma yin read more 1 don karancin comment

comment

Share

© Hafciey Musa

[1/25, 5:40 AM] Hafciey Musa😘: *LAYLERH*

(The prettiest emerald)

Picking call din yayi da sallama"wa'alaikasalam nace Ka turo asusun bankin Ka".

"Yanzu kuwa Zan turo miki".

" Ka sani fa duk maganar da muke yi ina recording kuma kaga ina da hoton Ka so kada Kayi tunanin zaka damfare ni".a tunanin shi ko an Kama shi Ai ya San ita ba Yar uwar Laylerh bace sai yace"Ehh kada kiji komai".katse kirar tayi nan ta tura mishi sai ta sake kiran shi"kaga alert ko?"

"A'a bai shigo ba ina ji network ne but yana shiga Zan sanar da ke". To tace nan suka yi sallama Bayan irin minti biyar haka yaga alert dariya ya fashe da shi yana fadin" yanzu Na tabbatar Mata basu da tunani in ba haka ba mace baki sanni ba Ki zauna Ki tura mini dubu Dari biyar akan Laylerh "kulan abincin da aka ajiye mishi ya bude nan yaga rice and stew ne tsaki yaja sannan ya mike yana fad'in" Ai ko yau kaji Zan ci tunda kudin banza ya samu"ficewa yayi a gidan gaba daya ya tare keke yace a Kai shi inda ake gasa kaji haka ko aka yi biyan Mai keke yayi yau fa jin kan shi a sama yake nan ya saya a wajen ya zauna yaci abun shi....

Bayan azahar ya nufi gida wanka ya shiga kan ya fito ya tarar ta mishi missed call bakwai nan ya Kira ta"ya zanyi ta kiran Ka baka dagawa ne? "

"Ki yi mini a hankali tunda ke ba uwa ta bace yanzu fadi damuwar Ki".

" so nake a gobe Ku taso sannan Ka hada ni da driver'n motar"an gama yace gami da kashe wayar yaci gaba da abunda yake yi can kuma sai yaga tabbas fa yayi implicating Na kan shi yanzu in ta mishi wani abu fa gaba daya sai yaji ya tsani kan shi nan yayi deciding ya Kira ta ya fada Mata gaskiya kawai yana Kira ta daga sai yace"gaskiyar magana Hajiya ni ban San inda yarinyar nan take ba kuma ban San ta ba".

mikewa tayi tana fad'in "zancen banza zancen hofi Ince Kai Ka tura mini hoton Ku Tare".

" Nifa da Na gani a social media sai Na yanke hukuncin naci kudin Ki batun Hoto kuma hadawa nayi".

"Wallahi wallahi zuwa gobe Ka tabbatar duk inda yarinyar nan take Ka nemo ta Ka kawo ta Gare ni in ba haka ba zaka San da Wa kake zance a tunanin Ka ni jahila ce ko to try me". Tana gama fadin haka ta kashe wayar shi ko cire wayar yayi a kunnen shi yana kallon screen din wayar a zahiri yace" to me Kika isa mini Wanda Allah bai yi zai same ni ba"can kasan zuciyar shi kuma a tsorace yake shiyasa ma ya cire Sim din a wayar gaba daya don ya fahimci matar Yar bala'e ce..

Sai Bayan magrib ya mayar da Sim din wayar don ya San za'a Kira shi a Daren kuma ya yanke hukuncin Komawa Maiduguri gobe in yaso sai ya nemi wani Babban malami da yafi wancan iya aiki ya nemo mishi inda Laylerh din take...

A bangaren Hajiya kaltume kuma suna gama waya Tasa aka yi yadda aka yiwa laylerh da hoton sani Ai nan take ko ina ya amsa da ya bace Ana Neman shi,security officer Na garin ta bawa aiki don ta tura musu voice da tayi recording da kuma screenshot da tayi Na kudin da ta tura masa shiyasa nashi Neman yayi karfi saboda ta sako hukuma a ciki sannan tace ya damfare ta ne..

Washe gari ko da ya kunna wayar shi bai shiga kafafen sada zumunta ba shiyasa bai San Ana Neman shi ba kammala shirin shi yayi tsab ya nufi Tasha ya shiga motar Maiduguri..

A safiyar ranar aka Kira ta da yake tana da influence nan ake ce mata Asalin shi Dan Maiduguri ne don wani yace yana zuwa wajen saida motocin su nan tace asa jami'an Maiduguri su sananta bincike akan shi duk lokacin da aka Gan shi a kulle shi kawai...

Cikin dare ya iso Maiduguri da yake an gama samun bayanai a kan shi ya iso kofar gidan shi kenan polisawa suka yi arresting nashi suka tafi da shi...

**

Convoy Na motoci guda biyar ne ke tsaye a bakin farm gate din suna horn da gudu gate man ya bude nan suka Fara shiga da gudu direct admin block suka yi parking,guards din ne duk suka fito daga motocin su sai aka budewa motar da ta rage kofar..kyakyawar mace ce ta fito daga motar gefen ta kuma Sulaiman ne da gani kuma ita ce Mom nashi..shiga ciki suka Fara kowa ya maida hankalin shi don sosai take da Zafi halin ta boss ya dauka office Na Accounter suka wuce kujera boss ya ajiye Mata nan ta zauna duk a tsaye suke har shi Sulaiman din"ina son naga record book Na company'n nan"ta kare zancen tana kallon Accounter jikin shi har rawa yake yi don ita din ta kasance mace Mai zafin nama.

"Cashier kawo Mata"ita ma cashier jikin ta Na rawa ta kawo kallon record din take yi

"within two years nayi establishing Na company'n nan Na kashe 3 billion, akan kudi ya haura a samu Riba sai kasa yayi kuna nufin company'n bai samu popularity bane ko customers ne babu".duk shiru suka yi kowa kan shi a kasa Harda boss din"sugar kadai har South Eastern part of Nigeria ina jin yadda ake yaba shi".

waya ta daga nan ta Kira branch nasu dake can abuja tace a tura Mata soft copy Na transaction nasu Na two years, nan aka tura Mata calculating aka yi sai aka ga da Na can da nan din dukka 2 billion ne kenan company'n yana operating at lost dama kuma shi ne reason da ya kawo ta jalingo don taji meke faruwa..

Duba kudin da ya shiga da Wanda ya fita harma da Wanda aka kashe suka shiga yi nan aka ga wasu kudin sun shiga kuma basu fita ba sannan basu account Na company'n.. Accounter kuma ganin za'a Kama shi red handed Gashi tafi boss Zafi sai ya wayance da fad'in "dama ina son nayi surprising naki ne nayi saving kudin

daban" ita dai da yake wayeyyeya ce ta gane karya yake yi fahimtar haka sai yace"Ai da son cin kudin nake yi a account Na Zan sa".

"Company Na operating at lost sannan kace kana saving wani kudi,da gaining ake yi nan ne zaka ce you want to suprise me muga kudin".

Kudin da ake cewa anyi luting nashi bai wuce 10 million ba sai ga 1 billion a account nashi. Dama so yake yayi using smartness ne in bata tambaya ba Shikenan

" that shows an jima Ana haka boyewa Kayi in ba'a tambaya ba sai Kayi amfani da shi Meya sa mutani suke sakaci da Amana ne".nan ta shiga yi musu wa'azi da nuna musu illar cin amana a karshe tace

"asirin Accounter ya tonu saura Ku kuma a sannu duk Zan gane masu cin amanar company'n ".shiru dai suka yi mikewa tayi ta Fara tafiya guards Na biye da ita boss ko yana gefen ta" Accounter Na Kore Ka daga aiki muhammad Sanusi take over Na baka rikon kwarya kan Na samu Wanda yafi cancanta"ta kare zancen lokacin da suka fita daga office din kallon boss tayi

"Sulaiman duk laifin Ka ne if not ta ya wadan nan mutanin suna cin amanar mu ace kana Taraba baka sani ba ina sane fa in a month bai wuci Ka shigo sau uku ba"

"Sorry Mom" hararar sa tayi tare da rike kunnen shi"ouchh Mom stop this yanzu fa ni ba yaro bane Kiga guards Na zasu raina ni".

"To me har gobe Kai yaro ne" ta fadi tana smiling shima murmushin yayi suka shiga mota guards suka rufe musu kofa.

"pls Sulaiman Ka maida hankali akan business nan kaga company'n Na Neman durkushewa tunda staffs d'in duk maciya amana ne"

"In sha Allah mom" ya fadi lokacin da ya kwanta a kafadar ta shafa gashin kan shi tayi tana fadin"Allah maka albarka ".

son da take mishi ko kanta bata yiwa haka shima duk duniya bai da kamar ta kuma zai iya yin komai domin ta..suna isa gidan ta da ke jalingo Wanda kuma a wajen yake zama gate man ya bude kofa nan motocin suka shiga sa Kai" Waye kuma yacewa mutanin nan ina gari"ta fada cikin tabe baki ganin yan maula sun cika kofar dakin Mai gadi"wallahi mutanin are annoying ace mutum da karfin shi da lafiyar shi ba zai fita nema ba sai dai yazo gidan wasu maula"fad'in Sulaiman "kasan wasu zuciyar su a mace take" ta karishe zancen tana fitowa a mota don tuni an bude Mata tafiya ta Fara da fad'in "Sulaiman sallame su" takaici ne ya Kama shi don shi ba bai son abunda zai hada shi da wannan mutanin P.A'n shi ya kalla,biyo shi yayi don ya fahimci abunda yake nufi part nashi suka nufa..

Part ne da yaji komai Na more rayuwa ba abun fadi sai Masha Allah a falo P.A ya tsaya shi ko ciki ya shiga wardrobe Na Kayan shi da bai San adadin su ba ya bude cikin wani locker ya Ciro kudi masu yawa sannan ya koma falo ya Mikawa P.A'n shi..

A bangaren Mom nashi kuma a falon ma ta tarar da wani Dan uwan ta zama tayi a kujera tana amsa sannu da zuwan da yake Mata "Kai dai ba'a ganin idon Ka sai in kana da bukatar kudi". Kan shi a kasa yace" wallahi Mai daki nane bata jin dadi"

"Naseeru baka ji ba" murmushi Wanda aka Kira da Naseeru yayi don P.A'n ta ne"Ka sallame shi Naseeru ni Bari Na shiga ciki Zan Fara shirin Komawa gobe".

"An gama Hajiya Yauwa batun Yar aiki da Kika ce sa samo miki fa an kawo yarinya".

" ina fatan a hannun iyayen ta aka karbe ta don ni ban yarda da yan aikin mu Na can abuja ba yaro bai da asali Wata ma Yar iska ce kazo kana sponsoring nata".

"Ehh iyayen ta ne suka bada ta".

**

Da safe ko da ta fito sharan kitchen ta Fara kamar kullum saboda sai kanwar Baaba ta fito suke daura breakfast, Auta ce ta shigo kitchen din kamar mutumiyar arziki tace" me ake dafa mana ne?"duk da tayi mamaki sai ta shanye fuskar ta bai nuna ba tace"ruwan tea kadai Na daura".

"Meyasa baki daura abinci ba?"

"Saboda sai Pendo ta fito".

" Ki daura yanzu ".ta fada cikin gadara

" Ai ba haka muke yi ba".

"Ina fada miki yadda zaki yi kina cewa ba haka kuke yi ba". Cikin daga murya ta karishe zancen Wanda ya jawo hankalin kanwar Baaba da yanzu fitowar ta kenan "ni haka Na Saba bana tada su a bacci sannan da kike daga mini murya Ki sani Na girme Ki ai".

"Wai meke faruwa a nan" Pendo dubi wannan low class yarinya ina fada Mata abunda zata yi tana ce mini ba haka ta Saba ba sai kace gidan Na uban ta ne".

"Auta kin fiya daukar Zafi a matsayin ta Na Yar aiki Ai sai abunda yan gida suka ce tayi zata yi".

" Ince ni din Yar gida ce sannan ina fada Mata taki yi.."

"Kinga Laylerh yi hak'uri zo mu daura"fadin kanwar Baaba ta fita harkar Auta ita ko ganin haka sai tayi fushi ta koma daki..breakfast suka yi kamar ko yaushe sai an bawa Baaba tukun zasu ci nasu Na Auta kuma an rufe Mata a kitchen.. Kallo take yi kanwar Baaba ko cewa tayi "je Kice da Auta ina kiran ta" duk da bata so hakan ba

dole ta mike dakin ta nufa Bayan tayi knocking cikin isa da gadara Auta tace"Waye ne?"

"Ance kizo" tsaki ta ja tana fad'in "wuce mini a kofar dakin".

Jan kafar ta tayi ta koma falo" ina take?"

"Bata ce komai ba". Ai wannan yarinyar da bakin hali sai dai Ince Allah yaye Mata".

Shiri kanwar Baaba tayi don gida zata je dubo yara saboda kishiyar ta suna biki a satin nan almajiri ne yayi bara sai Baaba tace"Kinga dauki abincin Auta Ki bashi haka take in tayi fushi bata cin abinci ".

" to" tace gami da tashi ta dauki abincin ta Kai mishi nan kanwar Baaba ta sallame su ta tafi Baaba ko bacci tayi a wajen ganin haka sai Laylerh ta koma dakin ta,ta gyara can ta fito falon daidai lokacin Auta ta fito daga kitchen hararar Laylerh tayi tana fad'in "ina abinci Na?"Kai tsaye ta amsa Mata" an bawa almajiri".

"Kan buro uban nan wannan ma ai zancen banza ne uban Wa ya bashi kuma waya ce a bashi" nuna Mata Baaba da take bacci tayi ta yatsa sannan Tasa kafa ta nufi kitchen gaban ta Auta ta sha tana fad'in "ke har kin isa ina magana Ki wuce ba tare da Na baki izini ba kada Ki manta fa ke din Yar aiki ce".

banza tayi da ita cikin jin haushi ta shake wuyar rigar ta ganin haka sai Laylerh tace

" Wallahi in giyar hauka kike sha Ki mare ni,Na rantse da Wanda yayi ni ya kuma busa mini numfashi duka Zan miki".

ta Kai karshen zancen nata tana Mata kallon ido cikin ido tare ta ture hannun ta sannan ta cigaba

"kina yarinya karama za Ki raina mini wayo"ta fadi lokacin da ta nufi wajen TV tana zuwa USB dake jikin receiver ta Ciro gaban ta ta dawo tana nuna Mata bulalan tace

"Kinga wannan da shi Zan miki duka sai dai duk abunda zai faru ya faru in ya Kama a Kore ni a gidan Ku ne ma a shirye nake".hayaniyar su ne yasa Baaba farkawa kallon hannun Laylerh dake rike da cable tayi tace"me haka?"da gudu Auta taje ta fada jikin ta tana fad'in

"Baaba daga tambayar ta ina abincin na kawai ta Ciro bulala zata dake ni" mayar Mata da yadda suka yi Laylerh tayi sai Baaba tace"Auta Ki daina zata ga don ba gidan su bane".

mikewa tayi da gudu ta nufi daki Baaba ko cewa tayi"Laylerh Ki tsaya a matsayin Ki Na Yar aiki bana son kike shiga tsabgar 'ya ta".

"In sha Allah tace tana Mai jin ba dadi a ranta..

Da daddare duk suna zaune a falo Harda Pendo ta dawo Umar Farouq ne kadai baya nan malam yace" waya share dakin Umar Farouq ne?"

"Da safe Auta ta share mishi".Baaba ta bashi amsa

" to ko Ku fa Amma ace an bar shi cikin Dotti Ai abun zai mishi yawa ga hauka ga Dotti Wai a lallai kuna tsoron shi".

"Hauka" ta furta don tsam bata taba tunanin shi din mahaukaci bane ta dai San baida lafiya kam ba tare da sanin zancen ya fito fili ba duk kallon ta suka yi sai ta sauke idon ta kasa.

"kaga malam nace maka shi ba mahaukaci bane".

"Yo naji yanzu Wa zai ke share mishi daki don bai dace yake zama a Dotti ba tunda Auta tafiya zata yi ke kuma ba lafiya Pendo kuma tsoron shiga dakin d'an nata take yi".

" Laylerh take sharewa"Cewar Pendo da wuri ta dago Kai tana kallon ta yanzu fa suka gama cewa mahaukaci ne sannan tsoron shi ake ji ita don bata da Gata sai taje inda yake

"Mama Na daga gobe da safe Ki ringa share mishi daki don naga kamar yana son maganar Ki".malam ya katse Mata tunani bata da option face ta amsa da to nan ta wuce daki don yau bata jin ko hirar ma zata yi,akan me za'a ce taje wajen wanda duk abunda yazo hannun shi cakawa mutum yake yi,gobe dai zata je Amma in ya gwada Mata hauka ba zata sake ba sai dai su Kore ta a gidan da wannan tunanin tayi bacci..

Washe gari ko da ta tashi sallah tayi sai tayi azkhar tana Mai fargaban zuwa dakin shi,kwanciya tayi tana tunanin rayuwa har karfe shida yayi..mikewa tayi tare da sa hijab Na sallah'n ta jikin ta duk ba kuzari ta fice a dakin ta tare da Jan kofar ta rufe dakin shi a nufa zuciyar ta ko sai bugawa yake yi ga gaban ta da yake fadiwa ko da ta isa kofar dakin tsayawa tayi tana karanto duk addu'ar da yazo bakin ta sannan Tasa hannu jikin kofar tayi knocking sau daya saboda ta fahimci shi din ba jin magana yake yi ba jin shiru sai ta sake knocking nan ma shiru murda handle Na kofar tayi tare da cuza Kai cikin dakin bakin ta dauke da sallama idanun ta kuma a rufe suke,a hankali ta maida kofar ta rufe yadda ba zai ji ba daga bakin kofar take karewa dakin kallo lumshe idanu ta yi ta sake bude su akan dakin tana Mai shakan kamshin dake fitowa daga dakin..kwayar idanun ta juyar zuwa ga makeken bed Na dakin sai ganin shi tayi kwance a tsakiyar gado sanye da three quarter sai Riga armless kallo daya ta mishi ta cire ido tana Mai jinjina kwayu irin nashi da mamakin shi kuma su Waye suka maida shi haka Wato rayuwa kaddara ce kowa da irin Tasa shi ga kyau ga arziki daidai gwargwado sannan ga iyayen shi Amma kuma bai yanayin da za'a ce Na jin dadin rayuwa tunda baya ji kuma baya magana ga Karin hauka a kai,ita ko da hankalin ta tana ji tana magana Amma ba iyaye bata San Asalin ta ba ganin ya juya ya bawa inda take kallo baya sai ta girgiza Kai ganin yana baccin shi peacefully,fahimtar ba inda tunani zai Kai ta gwara tayi amfani da wannan damar baccin da yake ta gama aikin ta..

Sine dakin ta Fara ko ina yayi neat banda gadon da yake kwance a Kai nan ta share dakin sannan ta Fara mopping Na tiles din duk yana bacci tazo wajen TV kenan remote ya fadi a kasa nan take ya bude idanun shi da suke jawur kamar wuta kadan ya rake ta fadi kasa da wuri taja baya tare da jingunuwa da bangon dakin don idon ya bata tsoro kallo daya ya Mata ya cire Kai yana kokarin sauka a gadon jikin ta duk rawa yake yi yana sauke kafafun shi ya mike tsaye sai kuma ya fada kan gadon mikewa ya sake yi yana rike da kanshi da hannun dukka biyu ga dukkan alamu yana cikin mawuyancin hali don tafiyar ma ba direct yake yi ba yana abu kamar wani Dan kwaya ikon Allah take gani jin an bude dakin da wuri ta juya tana kallon kofa sai ganin malam tayi"Mama Na har yanzu baki gama sharar bane?"cire idanun ta tayi a kan shi ba tare da ta bashi amsa ba ta mayar da duban ta ga Umar Farouq shima direction Na idon ta yabi ganin yadda Yaron ya birkice cikin Tashin hankali yace

"Ki gudu shake Ki zai yi"Ai kan ya rufe bakin shi ta fito a guje shima fita yayi suka rufe shi a daki suna jin yadda yake ta fashe fashe Baaba kuka take yi daga kwancen da take tana Allah ya isa ga duk Wanda ya jefa Yaron a halin nan ita dai Laylerh kanta ya daure ta rasa gane tausayin shi take ji ne ko kuma tausayin iyayen shi..

Cigaba da fashe fashen yayi sanda yayi Mai Isar shi sannan ya zauna bakin gado hawaye Na gangarowa a idon shi daga karshe ma kwanciya yayi a kasa sai bacci..

Koda suka ji shiru sun San abun ya lafa malam da kan shi ya tattare dakin sannan yaja mishi kofa breakfast da Laylerh ta gama ya dauka ya Kai mishi daki sannan ya dawo yayi nashi breakfast din ya wuce kasuwa..

Bangaren Sani kuma a can Maiduguri anyi bailing nashi yanzu ya shigo gida kenan matar shi kallon shi tayi tana hawaye tace"wallahi alhakin mu ne ya Kama Ka ace zaka yi tafiya dubu biyar kawai Ka ajiye mana har yaushe zaka cire Laylerh a zuciyar Ka Ka gane ta maka nisa yanzu dubi abunda ya faru da Kai a sanadin ta".wannan Karon banza ya Mata don shi kadai ya San me yake ji Bayan gida ya nufa inda yayi wanka abinci ta kawo mishi yana Fara ci sai ga takardar sammaci an kawo mishi Na cewa zasu shiga court a Kano da Hajiya kaltume Na damfar ta kudi da yayi don cewa tayi Dan 419 ne..

Ba karamin tashi hankalin su yayi dukka ba"Laylerh! Laylerh har yaushe? ta fita a rayuwar mu ma bata bar mu ba"Cewar matar tana kuka.....

Comment

Share

©Hafciey Musa

[1/25, 5:41 AM] Hafciey Musa😘: *LAYLERH*

24

Prosciutto ne ya mike inda yake karanta case din"a yau 17 ga watan nan zamu saurari Shari'a da za'a gabatar tsakanin Hajiya kaltume da Sani Wanda ya yaudare ta dubu Dari biyar".yana kaiwa nan ya zauna"suna Na barrister Sauban nine lawyer'n Mai Kara"ya fadi lokacin da ya mike tsaye Kai alkali ya daga sai dayan yace"Suna Na Barrister Isa ni nake kare Wanda ake Kara"shima Kai alkali ya daga mishi Wato yana sauraron su,rubutu yayi a takardar dake gaban shi sai yace"ko lawyer'n Mai Kara Nada hujjar da zata nuna Sani ya damfare Hajiya kaltume? "

"Sosai kuwa ina rokon wannan court Mai albarka da ta bani dama Na gabatar da sani a gaban kowa"

"An baka" fitowa Sani yayi ya tsaya inda suke tsayawa sai lawyer'n Hajiya kaltume ya dube shi yace "shin malam sani Ka San wancan baiwar Allah?" Ya kare zancen yana nuna mishi Hajiya kaltume dake zaune"kwarai Na San ta".

"Alhamdulillah,Ka kuma yaudare ta ta hanyar karban kudi a hannun ta?"

"Ni ban yaudare.....".

" malam Sani amsa daya zaka bani eh ko a'a shin Ka karbi kudin ta?"cike da tsana Sani ke kallon lawyer'n Hajiya kaltume yace"ehh".lawyer'n shi ne ya mike yana fad'in "objection my lord,lawyer'n Mai Kara yana kokarin sa mishi magana a bakin shi ne ta ya zai ce ya amsa da ehh ko a'a sannan bai koro jawabi ba".

" barrister Sauban Ka kiyaye".fadin alkali

"Na gode Sir" ya fadi yana saukar da kan shi a kasa sai kuma yace"malam Sani yanzu Zan gabatar da shaida ta Na farko".

playing record da Hajiya kaltume tayi yace"shin wannan muryar Ka ce?"shiru yayi sai lawyer'n shi ne ya mike yace"batun murya Ai za'a iya daurawa ko ba nashi bane".

"Murya nane" Sani ya katse su dukkan su biyu"Masha Allah Ka damfari Hajiya kaltume ta hanyar karban kudi a hannun ta kace zaka kawo Mata 'Yar ta da ta bata Bayan baka San inda yarinyar take ba".

"Nifa da wasa nake Mata" ya fadi don bai San abunda zai ce ba,murmushi barrister Sauban yayi yace"wasa fa to a nan bamu wasa shin ina yarinyar ".

" yarinya dai ban San inda take ba hasalima Na fito Neman ta ne shine silar zuwa Na Taraba sannan kudin wancan matar yana ajiye ban taba ba,kuma da take cewa 'Yar ta ce karya take yi ni ne nan Dan uwan ta".

"To Kai wani irin Dan uwa ne,kace Neman ta ne ya Kai Ka har Taraba sannan kaga Wata Na Neman ta baza Ka bincika dalilin ta Na Neman ta ba kila ta zauna a wajen su kan tayi gaba sai kawai Ka damfare ta da yake sana'ar Ka ce".

" ya mai girma Mai Shari'a Wanda nake karewa ba Dan yaudara bane".

"Ko kana da hujja".

" ehh Amma ina rokon wannan kotu Mai albarka da tayi mini alfarma a daga wannan case zuwa wani lokaci in sha Allah zuwa nan Zan hada duk wani hujjojin da ake bukata"shiru alkali yayi yana rubutu a takardar gaban shi can yace"wannan Court mai albarka ta daga wannan zama zuwa 22 ga watan".yana gama fadin haka ya buga abun gaban shi nan duk suka mike shi ko ya fice...

**

A yau Pendo take shirin Komawa yanzu haka ma zaune suke a backyard suna wanki ita da Laylerh inda laylerh ke wanke Na Baaba da nata, Pendo ma Na wanke nata"Wai ke Laylerh baki da yan uwa ne?"murmushin da yafi kuka ciwo tayi Amma bata ce komai ba sai ma cigaba da dirje bakin zanin dake hannun ta tayi"magana fa nake miki"

"To irin wannan ance miki suna bada tarihin rayuwar su ne waya sani ko....." da sauri Pendo ta juya tana kallon Baaba tare da girgiza Mata Kai alamar kada ta karisa, murmushi Laylerh tayi sai ta ajiye zanin hannun ta tare da goge hannu a zanin jikin ta ta dauki bucket ta nufi fanfo domin diban ruwa don Tun Kwanaki ta gane yanzu fa Baaba ba kaunar ta take yi ba shiyasa take taka tsantsan da komai Na gidan."Haba Baaba bai kamata Ki fadi haka a kan ta ba".

"To uwa ta zainabu sai Ki hanani karya Na Mata ne yarinya kamar wannan ace ta shiga duniya Ai kin San ba ta hanyar halal aka samo ta ba".

" ke fa kike yawan cewa Auta ta kyautata zato sannan duk haukan nan akan Auta kike yi ita da bata nan".

"Yo wani irin zato Zan kyautata ga yarinyar da ta mallakewa yarinya Na kowa nata wallahi ba don malam yace Allah ya isa in Na Kore ta ko a Bayan shi ba da tuni Na kora Mara asali".

" dole Kice haka tunda yanzu Kinji sauki".

"Sauki Allah ne mai bayarwa kuma ya bani". Ganin Laylerh Na dawa sai Pendo tace" to ya isa Dan Allah Gata nan"cikin daga murya Baaba tace"to tsoron Yar aikin Zan ji wannan ne bata isa ba"sarai Laylerh taji me tace sai bata kula ta ba Pendo ko ganin Baaba ba shiru zata yi ba sai ta dauki bucket Na Kayan ta ta nufi wajen shanya, hararar Laylerh Baaba tayi sannan ta shige ciki, rage tsahon ta tayi ta Fara dauraye Kayan tana gamawa ta nufi igiya domin shanya ta Fara kenan malam yazo inda take yace"Mama Na baki gama bane".dakatawa tayi da shanyar tare da dagowa ta dube shi

"Saura kadan kana bukatar wani abu ne?"

"Ehh so nake Kije wajen Mai gasa kaji Na Bayan layin Mun nan Ki saya mini".

" to Ai saura Na gama shanya wadan nan ne kawai"ta fadi tana nuna mishi Kayan cikin bucket din da hannu, aljihu yasa hannun shi ya Ciro dubu uku yace"kaji zaki saya mini guda biyu".hannu biyu Tasa ta karbi kudin da fadin "to" sai kuma ya sake Ciro Dari biyar yace"wannan kuma Ki saya drinks ko wani Kala guda biyar"shima Karba tayi daidai nan yaro ya shigo yace Ana sallama da malam"kila har Ki dawo ina tare da bako don haka kuci daya a ajiye mini daya Nida Umar Farouq "gaban ta ne ya fadi jin an ambaci sunan shi tsab haukar da ya Mata ya dawo brain nata don yau sawon kwana sha uku kenan bata sa shi a ido ba wasan buya take da shi" ina hankalin Ki yaje"da wuri ta dawo hayyacin ta tana daura murmushi kan fuskar ta tace "Babu" Kai ya girgiza sannan ya nufi waje don shi tausayin ta yake yarinya karama kamar ta ace ta bar gidan su dole akwai lauje cikin nadi..

Tana gama shanya ruwan wankin ta zubar tare da hada buckets din waje daya ta shigar kitchen dakin ta ta nufa hijab ta dauko ko da ta dawo falon durkusawa tayi a gaban Baaba tace"Baaba Bari naje aikan malam".yadda kasan ba mutum a wajen haka Baaba tayi nan ta mike ko ba komai Ai ta sallame ta inda ya fadi ta nufa Bayan an sa Mata a Leda sai taje shago ta sayo drinks Tun a shagon wani ke Mata sallama tayi banza da shi a Cewar ta ko da Naseer baya nan zuciyar ta Na can tare da shi,ganin da gaske sai bin ta yake yi nan ta Kara saurin tafiyar ta tana kallon Bayan ta da gefen ido ji take yi kamar Tasa gudu kawai..

Har suka kusa gida bai daina bin ta ba sun zo daidai gidan wani gida kusa da nasu sai ga malam yana Rako bakon sa kallon ta yayi ganin yadda take sauri yace"lafiya kuwa".

"Shine fa Tun a shago yake bina". Yaron Dan anguwar ne kuma sun shaida juna shi da malam shiyasa ya mika musu hannu suka gaisa sai malam yace" laifi ta maka ne?"keyar shi ya sosa "a'a yarinyar ne ta mini". Gefen da take malam ya kalla yace" jeki gida"yana kallon ta har ta shige gida sai ya juyo ga saurayin "yanzu banda abun Ka Ana tare yarinya a waje ne Ai gida ya kamata kazo don yin sallama da ita".

" ayi hak'uri malam in sha Allah ba za'a sake ba".

"Yauwa kuma Ai bata Kai ta Fara tsayuwa da samari ba". Yana kaiwa nan yaci gaba da raka bakon shi...

A can gida kuma tana shiga a dining ta ajiye da wuri ta wuce kitchen don ta bar girki Ai ko ya Dan kone nan ta raba don yau tuwon masara suka yi ba Umar Farouq a ciki dole ta dafa mishi rice and stew,raba abincin tayi nan ta kawo ma su Baaba don yanzu da kanta take ci sai ta koma ta kawo ledan aikan" Baaba ga wannan Inji malam yace aci daya a ajiye mishi daya".ta karishe zancen tana ajiye ledar kusa da Baaba "dauki Ki Kai muku ke da shi kuci tunda ke din ta gaban goshi ne har za'a ce Auta ta koma da fushi Amma shi sai wani Jan Ki a jiki yake" tana kaiwa karshen zancen ta,ta jefe ta da ledan"Kinga Laylerh in ba zata ci ba bani nan zanci nikam"fadin Pendo"ba zaki ci ba,nace ba zaki ci ba"Cewar Baaba ita dai Laylerh mikewa tayi bata ce komai ba kuma bata dauki ledan ba ta nufi daki...

Har Bayan asr malam ya dawo a falo ya zauna a one seater ya mike kafafun shi tare da cire hula sannu da zuwa duk suka mishi nan ne Pendo taje kitchen ta dauko mishi abinci.. Hannu ya wanke ya Fara ci sai hankalin shi ya Kai ga Leda yace"yanzu yarinyar nan bata ce kuci Ku ajiye mini ba".kamar jira Pendo take yi tace"ta fada Baaba ce tace ba zamu ci ba".

"Kinga Ki daina nuna tsanar yarinyar nan ita ma fa da iyayen ta kuma naga muna amfanuwa da ita ko so kike ta Fara rainaki ne,Ki bar ta suyi duk Abunda zasu yi

wancan tsakanin ta da Auta ne Amma ki rike girman Ki". Nan ya shiga rarrashin ta har ta sauko tare ma suka ci kazar aka ajiyewa Laylerh da Umar Farouq nasu...

Bayan ya gama sai ya dauki abincin Umar Farouq tare da daura naman shi a gefen tray din ya nufi daki yana budewa yaga ba kowa da wuri ya ajiye abincin ya fito falo yana Mai sanar da su cewa bai ga Umar Farouq ba take hankalin su ya tashi..

Laylerh ko yanzu ta gama tsefe kan ta hannun ta don Pendo ta Kai mata naman ta har daki, rike take da cumb ta fito don taje waje ta taaje kanta sai ta ga duk a rude suke da rashin ganin Umar Farouq ta tausaya musu a hankali ta fita ta kofar kitchen ta nufi backyard Na gidan ta cire Dan kwalin ta sai ta kange shi ya bata baya yana facing Na gini da gudu ta koma ciki tace Gashi nan Ai duk fitowa suka yi nan malam ya maida shi daki aka bashi abinci yaci sai bacci...

Da yamma ta raka Pendo shiga keke tana Mai tausayin kan ta da kan ta don zaman gidan ba dadi zai Mata ba in ya rage su uku Baaba ba kaunar ta take ba sannan wannan mahaukacin Bayan mutuwar ta ba abunda take tsoro kamar shi..

Da yake ta Bayan gidan ta samu keke sai ta juya tafe take tana tunani iri-iri daga nesa taga kamar Farouq take gani ido ta zare ganin ehh shi ne kuma ga dukkan alamu kamar Jan hankalin shi ake yi, da gudu ta koma gida ta sanarwa Baaba so ba shiri suka fito don malam baya nan matasa aka roka su maida shi gida..idanun shi jawur kamar zai yi amai wuta ga jijiyoyin kan shi duk sun mike ganin Kama shi za'a yi sai yayi ready fada sai kaiwa iska naushi yake in ko tsautsayi akan Ka ya fada to Kai zaka sha naushi..dama ance sarkin yawa yafi sarkin karfi da kyar suka iya Kama shi suka Kai shi gida nan aka rufe shi a daki a take kuma ya Fara fashe fashe wannan Karon tsantsan yadda ran shi ya baci Harda TV ya fasa sai wani gurnani yake kamar mayunwacin zaki...

**

Parking driver yayi nan ta fito rike da handbag nata ta shiga gida daidai lokacin kuma Baban Naseer ke saukowa daga upstairs direct dinning table ya nufa nan ya Fara bude cooler's da ke wajen yana Neman abincin breakfast sai yaga wayam"where is my breakfast? "Ya tambaye ta lokacin da ta karaso cikin falon

"Khadeeja bata maka bane?"

"Beside daga ina kike da yanzun nan?"ya jefa Mata tambaya ba tare da ya amsa tambayar ta ba

"Ince jiya da dare Na sanar da Kai cewa yau zanje court to dugun kada alkali ya riga mu zuwa Nida lawyer Na a kori case din yasa ni ficewa da sassafe ba tare da Na sallame Ka ba".

" yanzu don Allah me amfanin wannan case?"

"Alhaji Dan 419 ne fa ya damfare ni?"

"To yanzu shi me yace?"

"Cewa yayi kudi Na suna kasa in Ana so zai dawar".

" meyasa baki karbi kudin kawai aka rufe case din ba,ina problem naki kudin ne?"

"Amma....".

" this is rubbish maza next zama da za'a yi Ki tabbatar kin karbi kudin Ki an rufe case din".

"Shikenan kuma yarinyar taci banza,Yaron nawa daya tilo fa ta cinye".

" kaltume Wai ba kiyi imani da kaddara bane ko kin taba ganin inda mutum ya mutu kwanan shi bai kare ba?"

"Ni dai gaskiya sai Na daukar Wa d'a Na fansa".

" ni kuma ina Mai tabbatar miki in Kika yi haka zai iya taba auren Ki".yana gama fadin haka ya fice bai bi ta kan breakfast din bama don ta bata mishi rai sosai..ita ma daki ta wuce ko a jikin ta don fa ko me zai faru sai ta hallaka Laylerh...

**

ADAMAWA

Keke napep din Na cikin tafiya sai ya tsaya sakamakon Mai da ya kare a ciki,"mtsww Mai ya kare mini Gashi gidan Mai Nada nisa da nan Dan Allah malam sauka Ka tura ni zuwa black market da nake ganin can".passengers biyu ne a cikin keken namji da mace,macen ba kowa bace face Aunty'n Laylerh"gaskiya sai matar nan ta fita in ba haka ba keken nauyi zai yi ".

" Hajiya Dan Allah fito a tura keken".

"Haba malam kudi fa zan biya sannan yace Na fito".

" Dan Allah fa aka ce".sauka tayi nan suka Fara tura keken tana bin su a baya har suka iso wajen black market din"ina Me Mai din ne?"da gudu ya taso daga tsallaken titi karkashin Wata bishiya Mai bada inuwa da iska ya nufe su yana fad'in "gani nan". Rintse idanun ta tayi ta da karfi don muryar tamkar Na Wanda har ta koma ga Allah ba zata manta bane Wato Dan ta..Mai ya Fara juye musu a keke napep din zuciyar ta sai bugawa yake yi.. da kyar ta iya lekowa don ganin wane ne illa kuwa Muhammad ta gani da kyar ta iya bude baki tace" Muhammad ".daidai ya gama juye Mai din, kallon ta yayi ganin nan take idanun ta sun kawo ruwa yace" malama ya dai".

"Malama" ta maimaita Kalmar akan labban ta"Hajiya shiga muje ko".nuna Muhammad tayi da yatsa tana fad'in "Muhammad yanzu so kake kace mini baka gane ni ba,Kai fa d'a Na ne".

" ya haka malama taya Na zama d'an Ki,to in ni d'an Ki ne meyasa bana tare da ke mutani da Rainin wayo Wai Dan Ki".

"Dan samari baka fahimce ta bane kila tana nufin Kai din yaro ne ga wani Dan uwan ta".Cewar Mai keken Da sauri ta girgiza Kai tace" wallahi nice nan Na haife shi".

"Zancen banza zance wofi kenan kin taba ganin inda d'a bai San uwar shi ba Dallah in zaki shiga Ki shiga mu tafi in kuma cigaba da tsayawa a nan zaki yi to bani kudi Na nayi tafiya ta". Kala bata ce mishi ba sai hawayen da taci gaba dayi yau ace Gata ga d'an ta Amma ya Gaza gane ta,magiyar duniyar Allah'n nan ba Wanda Mai keke bai yi ba ita hankalin ta ma baya kan shi" dama can bata da kudin keke ne ta shiga yanzu in Ka tafi wani zata sake tarewa".fadin dayan passenger.. "Wallahi mutani tsam ba Allah a zuciyar su". Cewar Mai keke..

Muhammad da tuni ya koma inuwa ya zauna ganin har yanzu Mai keken bai tafi ba sai ya dawo" malam keken ne yaki tashi Na tura maka? "

"Wani keke wannan baiwar Allah ce taki shiga mu tafi kuma taki bani kudi Na". Kallon Aunty yayi yace" tunda kince ke Mama nace shiga Ku tafi"a take ta shiga keken nan ya cire naira Dari ya bawa Mai keke kudin keken ta suka tafi...tsam bai gane mahaifiyar ta shi ba...

A kofar wani gida Mai kyau ta sauka nan ta shiga ciki wani bangare daban ta nufa sai sannu da zuwa ake Mata..

Tun Randa boko haram suka yi galaba akan su ta gudu zuwa wani camp ta dau lokaci sosai a wajen kuma ta kan tuna da Laylerh da Muhammad sai dai ba taba yunkurin nemo su ba da yake aikin asiri ne, nan ne Allah ya hada ta da yan hijira yan uwan ta ganin Dan zaman da suka yi da ita sun fahimci bata da matsala shiyasa

da suka tashi dawa ga yan uwan su daya ta dauke ta suka dawo tare don ita ma ta manta hanyar garin iyayen ta..

wannan kenan!!!

"Na gode" yace da Mai keke Bayan ya mika mishi kudi cikin gidan shi ya nufa a tsakar gidan ya tarar da matar shi dariya ta fashe da shi tana fad'in "ina ruwan angon Laylerh".ganin ba fuska don bai yi niyar biye Mata ba sai ta dauko center carpet ta shimfida mishi tare da kawo mishi ruwa zama yayi ya sha ruwan ita ko tana mishi fifita da yake ba Nepa" ya case din dai angon Laylerh? "

"Ke mutum Na cikin bakin ciki kina sako wasa,wallahi damuwa Na nace da su kudin ta Na zaune Bayan a cikin shi Na hayo lawyer dubu talatin sannan ko wani zama Zan bashi dubu goma".

" yanzu kana son kace mini baka da wani kudi a kasa?"

"Ina fa kudi kina gani Na saya motoci biyu daya miliyan daya da rabi daya kuma miliyan biyu a haka ma akwai kudin mutani a ciki".

" yanzu Abban Ahmad in nace wani abu sai kace kishi ne,Laylerh ko ita ce autar Mata yaci ace Ka hakura da ita don wahalar da Ka sha a sanadin ta baka sha a kaina ba,kana sane watsewar su ba Na Allah da annabi bane kuma duk Wanda yace zai neme su da masifa iri iri yake haduwa ".

" Ai wannan Karon kam Na yarda da zancen Ki kuma in sha Allah Ana kare case nan lafiya Na fita harkar ta kenan abunda Na kashe akan ta kuma sai Allah ya saka mini".

"Maza anji jiki a tunanin Ka zan yarda da wannan dadin bakin ne sai dai in baka Gan ta ba da gudu zaka koma".

"Ko ta dawo ba Zan saurare ta ba sai dai in naga zasu bawa wani ita nan kam dole Na tashi tsaye".

" zancen kenan Ai"....

**

Kwance yake akan makeken Italian bed nashi ya cusa duk hannayen shi a Bayan wuyar shi yana kallon ceiling "gaskiya ba Zan iya bijirewa Mom ba cuxx ban son bacin ran ta but maganar Aure ta ina Zan samo Mata kalar wacce nake so Within Wata biyu". Numfashin ya fesar gami da mikewa zaune ya Fara safa da marwa a dakin" sai dai tayi mishi arrange marriage kamar yadda ta fada..tsaki yaja nan ya nufi jikin window ya tsaya yana kallon waje "ya ilahee kasa duk macen da zata zaba mini kalar wacce nake so ce..

Need your prayer's cux ina fama da mura

Comment

Share

©Hafciey Musa

[1/25, 5:41 AM] Hafciey Musa: *LAYLERH*

23

A yau laraba aka shigar da case Na Hajiya kaltume da Sani court yanzu haka a wajen suke sai dai sun tarar Ana wani case dole suka zauna zaman jira..

Kowa harkar gaban shi yake a court din mutani sai Kai kawo suke daga can gefe kuwa Hajiya kaltume ce da yaran ta biyu sai lawyer'n su,bangaren Sani ma yazo da lawyer'n shi sai dai fa ya razana da ganin Hajiya kaltume don tabbas matar Babban mutum ne..

Bayan an gama wancan case dn sai court clerk ya Mike

"ayau ranar laraba uku ga watan 11hajiya kaltume Mahmud tashigar da karar sani Tanko cewar ya damfareta tsabar kudi dubu Dari biyar (500000)a cewar sa zai kawo mata yarta data bata....ahalin yanzu dai be kawo yarinyar ba Kuma be maida mata da kudintaba".

Yana kaiwa nan yayi bowing alamar girmamawa ya miqa file din kan desk na alkali

Naxartar file din alkali yayi sannan ya dago ya dubi sani yace

"sani kaji abnda hajiya kaltume take karanka a kai,shin ka aikata?"

Da a'a sani ya amsa sannan alkali ya dubi four angles na court din yace,

"shin Wanda ake Kara na da lawyer?"

Lawyer din sani ne ya miqe cikin girmamawa yayi bowing sannn yace

"my Lord,I'm barrister Sauban lawyer me kare Wanda ake tuhuma sannan ya koma yayi zamanshi..

Nan prosecutor ya gyara zaman glasses nashi yace,

"wacce ke qara,shin tanada lawyer?"

Nan itama lawyer dinta ya tashi ya gabatar da kanshi sannan yazauna.

Shiru court din yadauka na wani lokaci yayinda prosecutor keta naxartar file din sai can yadago yace...

"mun daga saurarar wannan qara zuwa sha bakwai ga watan nan in Allah ya nuna mana".

nan ya buga gravel Wanda ke signifying karewar zaman.Atake duk mutanin suka miqe don girmama alkali yayinda ya fice security dinshi na biye dashi...

**

Shimfida Mata sallaya aka yi nan ta fito falon hannun ta daya rike da casbi daya kuma gidan glasses nata sanye take da hijab, salla tayi Bayan ta gama azkhar sai tayi kiran Rabi da gudu ta fito "Barka da safiya Hajiya gani"

"Dauko mini laptop Na a gefen shi kuma zaki ga wani file duk Ki kawo mini" to tace gami da juyawa nan ta dauko Mata ta ajiye, wayar ta ta dauka tare da Fara dialing number'n da aka rubuta other half da tambarin love a gaban number'n picking yayi yana fad'in

 "sorry Mom ina masallaci but yanzu Zan fito"

"Ohk Ka same ni a bangare Na" tana gama fadin haka ta katse kirar tare da bude laptop nata ta Fara operating. Ba jimawa yayi Sallama a kofar falon ta amsa sanye yake cikin jallabiya sosai yayi kyau karasawa ciki yayi ya zauna "Barka da safiya Hajiya".

" Ka tashi lafiya?"alhmdll yace sanin aiki zasu yi nan ya maso kusa da ita suka Fara aiki duk sun maida hankalin su ga aikin har basu San sunci hour daya da rabi ba Rabi ce ta katse su ta hanyar fad'in "Hajiya ga coffee Na kawo" tsaki taja tana fad'in "what rubbish kin taba ganin na yi breakfast by 8 Ince sai Tara nake breakfast sannan daya cup din kuma Ai kin San Sulaiman sai tara yake Breakfast".

" Hajiya naga jiya kince a kawo miki ne".

"That's because jiya Na kwanta ban ci komai ba will you get lost now".

jikin ta Na rawa ta bar wajen duban ta ta Kai ga Sulaiman "I guess we should be rounding up yanzu cuxx da mota zanje yola pls Ka maida hankali akan aiki".

" in sha Allah"

"Tell the driver to get the car ready" ta fadi tana mikewa ta Kara da fad'in

"Rabi kisa mini tea a karamin tea flaks Na sannan pepper soup nan Ki mini take away'n shi yanzu Zan fito" ta Kai karshen zancen ta tana shigewa daki cigaba da sauran aikin yayi yana gamawa ya hada Mata komai da komai..

Koda ta fito zama tayi a kujera tare da kura mishi idanu "lafiya kuwa Mom".

" Sulaiman is high time ace kana da Mata".

"Pls Mom to me marriage is a distance thought a yanzu".

sassauta murya tayi tace"pls duk duniya Kai kadai nake da fa kuma Kai din ma Ka San da irin lalurar da Na haife Ka so kake zuri'a ta ya kare a haka pls Ka nemo Mata Kayi Aure Nima Na samu jikoki kaga duk wadanda kuke uba daya sun kai Aure".

"But....."

"Shush" tace tana daura yatsar ta akan labban ta"yadda Na San Sulaiman baya yi mini gardama so Na baka two months Ka fidda Mata ko Na nemo maka ".

" a nemo mini sai kace mace ".

" a waje Na Kai mace ce kuma Na miji tunda banda ya mace kaga time Na tafiya ".

mikewa duk suka yi tare inda Rabi ta fito da tea flaks ta mika Mata hannun Tasa ta Karba tana fad'in" tomatoes da tattase dake cikin fridge kuyi amfani da shi but kaji goma da turkey biyar da Na saya jiya kada a taba mini nan da two months Zan dawo".

"To Hajiya godiya muke".

" and su Irish nan duk Ku dauka a tabbatar kuma Fridge Na kullum a kunne yake".

"In sha Allah" nan suka jera da Dan ta daya tilo gwanin ban sha'awa mota ya bude Mata yana fadin"Allah kiyaye hanya sai nazo"

"Kullum haka kake fada kace Mom sai kin sake zuwa kawai" murmushi suka yi a tare nan ya rufe Mata kofar motar yana waving nata guards nata duk shiga mota suka yi don ba karamin tsoron ta suke ji ba kasancewar ta mace mai principles ba shi ya koma bangaren shi ba sanda yaga fitar dukka motocin a gidan...

**

Malam ne ya fidda Umar Farouq backyard Na gidan don ya sha iskar waje kuma so yake ya shiga wanka sai ya Kira Laylerh

"Maama Na Ki zauna da shi anan ki sa ido akan shi don Allah Bari Na watsa ruwa".

Allah ya sani tana matukar tsoron shi Amma ta daure tace to" Allah miki albarka ".Ameen tace nan ya shige ciki ita kuma Umar Farouq ta kalla sanye yake cikin three quarter fatar jikin shi fari tas ya bayyana ga gashin da ke kafafun shi sun kwanta a jikin shi baki kirin sai fuskar sa da ba zaka taba gane me yake ciki ba" Sarki ya Tabbata ga Allah'n da ya halicci wannan bawan"ta fada a zuciyar ta tare da zama nesa da shi sosai don in abun gudu ne ma zata San yadda zata yi..

Waje daya ya kurawa ido Allah ne kadai ya San me a zuciyar shi bai ma San da ita a wajen ba sai can yaji a jikin shi kamar ana kallon shi juyawan da zai yi sai ganin ta yayi zaune can nesa da shi murmushi ya sakar mata cikin rashin sanin abunda zata yi sai ta mayar mishi da murmushin don ta tabbata ba haka banza bane dole murmushin Nada ma'anar sa carab a kan idon Auta, lumshe idanu yayi ya sake bude su akan ta sai ganin Auta yayi ta tana zuwa ta Bayan ta nan take ya nemi murmushin fuskar sa ya rasa Wanda hakan ba karamin kona zuciyar Auta yayi ba harara ta watsawa Laylerh sannan ta nufi wajen shi

"yaya baka farin cikin gani nane kenan wancan kazamar tafi maka ni?"

oho bai San me tace ba sai gani suka yi ta fashe da kuka da fuskar confusion yake kallon ta juyawa tayi da gudu ta shige falo jikin Pendo ta fada.

"wallahi Baaba Na tsane ta kamar yadda Na tsani ranar mutuwa Na ta raba ni da kowa Na gidan nan sannan yanzu tana kokarin kwace mini yaya Na".

"Ai ba wacce ta isa ta kwace miki yaya shi din naki ne ke daya" cikin kuka tana Zubda hawaye tace"A'a wallahi shi ma naga kamar yana da interest akan ta".

"Auta zato fa zunubi shi yayan naki ce miki aka yi ya San me yake yi bare har Kice yana da interest akan ta Na fada miki fa Ki daina wannan halin". Mikewa tayi da gudu ta nufi corridor tana fad'in" Ai dama Na San duk kun fi kaunar ta a Kai Na".ta karishe zancen tana Mai bacewa ganin su.

"Baaba wallahi batun yaran nan ya Fara daure mini Kai ba zai yu ko yaushe ace Auta ce Mara gaskiya ba sannan ita yarinyar bamu San me manufar ta ba".

"Ai Ki Bari ni duk sanda suka samu tsabani Na kan rasa Mai gaskiya a tsakanin su danne zuciya ta kawai nake yi nake baiwa Auta laifi don naga yarinyar bata fiya hayaniya ba Auta kuma akwai ta da gadara"..numfashi taja tana fad'in" Allah dai ya kyauta"Ameen Baaba tace..

Tana shiga daki ta fada kan katifar ta tana Mai fashewa da kuka Mai cin rai ta rasa wani irin tsana tayiwa Laylerh da kuma dalilin tsanar Allah ya sani tana kaunar yayan ta like die Amma kuma Ai ba auren ta zai yi ba tunda ita din kanwar shi ce dole Wata Rana ya auri Wata,ita fa ko duk duniya zai Aura ba zai Mata Zafi ba kamar taga Laylerh kusa da shi gani take tazo gidan ne don ta kwace Mata yaya..

Jin kamshin turaren Baban ta sai ta share hawayen ta fito har ya kusa shiga falo"Baba fita zaka yi?"

"Ehh".tana murmushi kamar ba ita ce ta gama kuka ba tace" to in sha Allah kan Ka dawo Zan girka maka miyar da kafi so".

"Allah miki albarka" ya fada yana dafa kanta lokacin da ta karaso wajen shi..mahaifin ta shine komai nata don tafi jin shi a rai fiye da mahaifiyar ta shiyasa ko shawara ma da shi take yi murmushi tayi lokacin da ya shiga falo ita ma falon ta fito Amma kitchen ta shige domin Fara hada mishi miyar kubewa..sallamar su yayi nan ya tarar Laylerh Na zaune can nesa da shi murmushi yayi a zuciyar shi ko yana tunanin ko yaushe Umar Farouq zai koma mutum kowa ya daina tsoron shi ne sai Allah "Allah miki albarka". da yake bata San da zuwan shi ba shiyasa ta tsorata sai kuma tayi murmushi da fad'in "Ameen Ameen" don shi kadai ke sa Mata albarka hannun Umar Farouq ya Kama suka shige ciki,Waigawa Umar Farouq yayi yana kallon ta har suka bacewa ganin ta..

Auta har la'asar ta gama miyar malam nan ta dauko karamin kula ta juye sai ta rufe a drower'n kitchen ta bawa Laylerh kitchen d'in.. Ita mamakin ganin Auta a kitchen tayi don a tunanin ta kila indomie ta dafa nan ta shiga girkin ta ita kuma shuwaka ta dafa tana sauke miyan ta daura tuwo Bayan yayi sai ta kwashe..

Sallar magrib kowa yayi a gidan sai ta fito ta jera abincin Umar Farouq a tray'n shi haka ma Na malam sai Na Baaba da ta Kai da Na Pendo don ita cewa tayi ta koshi daki ta koma..

Dama malam a tsakar gida yake cin abincin shi shi daya shiyasa Auta ko da ta shigo kitchen din sai ta cire miyar Laylerh ta ajiye sannan ta dauki nata ta daura a tray ta nufi tsakar gida cikin murmushi yace"kaman kin San jira nake a kawo mini don yanzu Na gama bawa yayan Ki".

"Allah sarki yau dai miya Na zaka ci Baba".

" to wanke hannun Ki muci tare".

"A'a nawa Na ciki". Bude mishi abincin tayi nan ya wanke hannun shi a ruwan wanke hannu da Laylerh ta jera a tray'n ya Fara ci...

Falo ta fito direct kitchen ta nufa domin daukar cup ta sha ruwan Lipton sai taga miyar malam a zaune da wuri ta fito falon tana fad'in

" Pendo abincin Baba fa"

idon ta akan TV tace Auta ta Kai".Kai ta girgiza a zuciyar ta tace"wannan wace irin tsana ce ta mini da har ya Kai ta dauki abincin Baban ta ta bar miya".don har ga Allah bata San tayi miya ba,daukar miyar tayi ta nufi tsakar gida daga nesa ta hange su suna hira gwanin sha'awa irin Na uba da 'ya karasawa tayi da sallama"malam an manta miyar Ka ta fada tana ajiye mishi miyar".ganin a gaban malam ne sai Auta bata ce komai ba shi ko a tunanin sa so take ita ma yaci miyar ta sai ya Karba yana sa Mata albarka ta juya..

ganin miyar shuwaka ce sai ya Fara ci dama hak'uri yake da miyar Auta yanzu ya samu wani wasa gaske sai ya cinye tuwon da miyar Laylerh Tun a wajen ta Fara

hawaye sai kuma ta danne ta kwashi kwanukan tayi ciki da su shi ko ta bar shi yasa iska. Da kuka ta shiga falon kitchen ta Fara Kai kwanukan sannan ta dawo falon"Baaba Na gaji wallahi ya ishe ni kina ganin yarinyar nan nayima Baba Na miya yana cikin ci ta dauki nata ta Kai mishi sai ya cinye tuwon da nata".

wannan Karon ran Baaba ya baci sai tace"yi hak'uri Auta Zan Mata fada"mikewa tayi ta nufi daki nan Baaba ta kwala kiran Laylerh sai Gata nan durkusawa tayi a gaban su.

"Wato don kullum kuka yi fada da Auta ita nake daurawa laifi shiyasa kike Mata duk iskancin da ran Ki yaso ko,to Ki tsaya a matsayin Ki Na Yar aiki Ki fita harkar Yar masu gida don ba Zan dauki wannan ba banda halacci irin nawa ma waya San inda kike yanzu ".Cewar Baaba

" Tun wuri Ki shiga hankalin Ki,Ki bar Yar masu gida ta sake dama Ku yan aiki Baku iya samun waje ba Wato kin dauki miyar Ki kin Kai mishi don Ki tabbatar mishi da cewa kin fi ta iya girki ko,to 'ya 'yace baki isa maye gurbin ta ba".

Cewar Pendo ita ko hawaye take yi jin sunyi shiru sai ta mike ta nufi corridor zuwa dakin ta..

daga nesa tana kallon Auta Na rufe dakin ta ta waje tana gama rufewa ta cire key ta daga sama tana girgiza Mata Wato ta gani sai taga inda zata kwana yau..cikin Zubda hawaye ta juya ta fita waje ta gefen kitchen sai kule take ta gani tuna abunda ya faru da ita a gidan madam da gudu ta tashi a wurin ta nufi ciki sai kuma ta rasa inda zata zauna don haka ta nufi lungun Umar Farouq zama tayi tare da fashewa da kuka Wato gidan uban Ka duk lalacewa yafi gidan uban wani tana cikin kuka taji sautin buga abu shiru tayi sai taji tabbas karan daga dakin Umar Farouq yake fitowa a hankali ta mike kofar dakin tazo ganin ba Mai zuwa sai ta tura a hankali ta shiga zuciyar ta kuma Na tsinkewa waige-waige ta Fara tana Neman jin inda sautin ke fita sai idon ta ya sauka kasan gado to ko shine ya makale a wajen..

Cikin tsoro da fargaba Tasa gwiwan ta a kasa a hankali kuma ta kwantar da gefen fuskar ta a tiles din tana leka kasan gadon..

Wawan bugawa zuciyar ta yayi a take taji fitsari Na Neman fasa Mata Mara don tsoron abunda ta gani nan take jikin ta ya Fara rawa zufa Na fitowa ta ko wani bangaren Na jikin ta da kyar take iya addu'a Amma kuma ta San karya ne ta iya sake leka kasan gadon,tabbas taji an bude kofar dakin Amma da yake duk ta fice hayyacin ta sai ta daga ido tana kallon kofar sai dai idanun ta basu gani da kyau inuwar mutum kawai take iya gani da kyar ta iya mikewa ta juyo ga kofar don gani take kamar ba mutum bane a wajen..

Tsaye yake idanun shi duk sun yi jawur ganin ta a dakin shi juyawa yayi ji kawai tayi yayiwa kofar key innalillah ta shiga ambatawa saboda gani take kamar halittanshi sauyawa yake yi sai ji tayi ya hada da ita da katifar gadon ya buga da gini azaba ya sata ihu nan ya Fara hurgin ta da duk abunda ya samu tana kaucewa hannu yasa a saman wardrobe sai gani tayi ya dauko wuka fitsari ta sake a wajen don ta San yau kam yankan rago zai Mata ba tare da ya cire wukar a gidan sa ba ya jefe ta da shi Ai kuwa ya same ta ihu Mai Kara ta saka tana Neman ceto nan hankalin mutanin gidan ya juyo Gare su da gudu suka nufi dakin shi har Auta sai aka ji a rufe hankalin su tashi yayi da gudu malam ya nufi store domin Neman abunda zai balla kofa Baaba ko cikin kuka take addu'ar Allah sa kada ya kashe Yar mutani..

A can dakin kuma cigaba da wurgin ta yayi da duk abunda ya samu ganin haka bai mishi ba sai ya Fara nufo inda take ihu take yi don mutuwar ta take gani nan ta Fara gudu a dakin in yayi nan tayi can zata tsallaka gadon taji ya damke hannun ta tana Juyowa ya bata Mari a take guda uku sai ji tayi kunnen ta sun daina aiki don azabar hannun shi nan ya finciko ta ya manna da gini tare da shake ta a take idanun ta duk suka fito waje ran ta Na kokarin barin jikin ta a daidai lokacin kuma malam yayi nasarar bude kofa tare da ture sa da duk wani karfin shi ganin haka sai Tasa kafa ba tare da sanin inda ta dosa ba ganin fa kamar ita ma haukacewar tayi da wuri Pendo ta kamo ta danne ta aka yi don sai fisge fisge take zata gudu..

Shi kuma a wajen malam ya dura mishi maganin bacci cikin minti goma ya mirgina ya Fara bacci kan ta aka koma Ana Mata addu'o'i Amma duk ta kasa nitsuwa ruwa aka bata ta sha sannan aka shafa Mata a fuska nan ne ta nitsu kadan ganin ba zata nitsu dukka ba sai aka dura Mata maganin bacci ita ma...daki Pendo ta Kai ta nan ta dawo falon duk suka zauna jugum kowa da tunanin da yake yi cikin bacin rai malam yace "Wai a ina Kika samo yarinyar nan ne ma banda kwashe kwashen Ki Gashi yanzu nema take ta tada haukan Umar Farouq".

" malam wajen Yar islamiyya mu Na karbe ta ganin ba Dan aika Gashi bani da lafiya Auta kuma Na makaranta dole in pendon su zata je shefene mu biyu ake Bari a gida Wanda hakan barazana ce ga rayuwar Umar Farouq Amma wallahi Nima nayi nadamar kawo ta gidan nan".

"Kun ji Ai tsam Mata Baku da tunani baki San Asalin yarinya ba kila magauta ne suka kawo ta gidan domin ganin Bayan shi,waya San me ta mishi don haka kawai ba zai yi yunkurin kashe ta ba".

" malam Ka manta shi ne? mu ma fa in ya samu dama kashe mu zai yi batun yarinya kuma in sha Allah gobe Zan sallame ta".

"Wallahi Baba ni shiyasa tin Randa Na ganta naji Na tsane ta don I don't trust anyone when it comes to my brother kuma wallahi in wani abu ya same shi gobe ni da kaina Zan dau mataki a kan ta".

" batun sallamar ta yanzu bai taso ba tunda Auta makaranta zata koma Nima gida Zan koma malam kuma a kasuwa yake wuni kunga Ai tana da amfani tunda tana zuwa kasuwa kuma tana girki yanzu fa ni bana aiki a gidan nan"Cewar Pendo.. Duk sun yarda da zancen ta banda Auta nan dai suka Riga tattauna abun Amma sun fi yin da Na sanin kawo ta gidan karshe aka tada ta su shiga sai ta Fara hauka dole a dakin Baaba suka kwana su uku cikin Daren ma in ta farka sai ta ringa fisge fisge...

Washe gari sanda aka yi da gaske kan ta Fara dawa hankalin ta magani aka sayo Mata tare da gasa Mata duk jikin ta da ruwan Zafi...

Daga wannan ranar ko inda Umar Farouq yake bata sake kallo ba gyaran dakin ma sai an Kai shi exercise take zuwa yi kan su dawo ta gama bata kuma gigin leka kasan gadon ba..

Bayan kwana goma sha uku

Abubuwa dayawa sun faru a kwanakin ciki kuma Harda komawar Auta makaranta hakan yasa Laylerh sakewa amma ba sosai ba don yadda take tsoron mutuwar ta haka take tsoron Umar Farouq kuma Tun ran can bata sake yarda sun yi ido hudu ba..

A yau sha bakwai ga Wata ne kuma su sani da Hajiya kaltume suka koma court....

Comment

Share

©Hafciey Musa

[1/25, 5:41 AM] Hafciey Musa😘: *□LAYLERH□*

(The prettiest emerald)

Alhamdulillah it's Friday again😍ina yiwa kowa da kowa Barka da juma'a da kuma fatan Alkhairi, ina kuma cikin farin ciki Mara misaltuwa don haka Ku nishadantu da wannan page

25

Jin gaba d'aya ta kasa samun sukuni yasa ta dawa wajen sana'ar Muhammad, daga can inuwar da yake zama ta kura mishi ido tana kallon shi,shi ko sanye yake da earpiece yana jin waka yana Dan kada kafafun shi sai can jikin sa ya bashi Ana kallon shi ko da ya dago Kai sai ganin matar jiya yayi"wannan kuma yau ta sake dawa kenan"haka kawai ya tsinci kan shi da mikewa ya nufi wajen ta"Hajiya lafiya kuwa?"yanzu Muhammad da gaske kake baka gane ni ba,nice fa mahaifiyar Ka sannan kana da kanwa Laylerh "fuskar ta ya kurawa ido tabbas fuskar is familiar Amma a ina kuma ta yaya" sai nake ganin fuskar Ki kamar ta wacce Na sani".

"Wallahi Ka San ni ni mahaifiyar Ka ce".

" Wai da kike cewa mahaifiya tace ke ya aka yi ban San Ki ba?"

"Ina ne gidan Ku?"ta jefa mishi tambayar

"Cab ni Zan nuna miki gidan mu kalen Ki fitini rayuwa ta".

" Allah ba fitinar rayuwar Ka Zan yi ba so nake naga iyayen Ka".

"To Ai ni ina zaune da aboki nane".

" shi Abokin naka bai da iyaye da dangi ne?"

"Yana da su mana".ya amsa Mata cikin gajiya da tambayoyin da take jera mishi sai kace Wata Yar jarida

" to Kai baka taba tunanin inda iyayen Ka da dangin Ka suke bane".Karo Na farko kenan da ya tuna ina iyaye da dangin don shi bai taba kawo shin bai da iyaye ko dangi ran shi ba ganin yana tunani sai tace"ni ce dangin Ka sannan kana da kanwa Baban Ka kuma ya rasu in Ka bani dama Zan baka labarin komai saboda Nima Na shiga irin halin da kake ciki da farko saboda anyi ta mini tambaya kan dangi Amma ban iya tunawa shiyasa wasu yan gudun hijira suka dauke ni to da taimakon wani malami a makotan su Allah ya bani lafiya saboda kullum Ana bani addu'a ina sha a jiya da Na cika Wata daya da Fara shan maganin Na iya tuno cewa ina da iyaye da kuma iyali Allah cikin ikon sa kuma ya hada mu a jiyan ".kan shi ne ya Fara juyawa ba tare da yace da ita komai ba ya juya yana maimaita Kalmar dangi da iyaye a zuciyar shi sai gani kawai aka yi ya fadi sume...

Da gudu tayo kan shi da sauran mutani dake wajen nan aka wasa mishi ruwa Amma bai farfado ba sai aka Kai shi asibiti a take aka nufi emergency da shi nan makotan shi Na wajen aiki suka ce ita mayya ce daga mishi magana kawai ya suma..ba irin

rantsuwar da bata musu ba cewa ita mahaifiyar shi ce Amma suka Ki yarda Harda police aka Kira Mata..ankwa aka sa Mata a hannu suka nufi fita a asibitin..

A hankali ya Fara bude idanun shi yana bin dakin da yake da kallo nan ya sauke idon shi akan Abokin shi da suke tare" Sirajo ina matar dazun nan?"

"Mayya ce Ai yanzu police suka dauke ta za'a Kai ta police station".

" Dan Allah Kayi gudu Ka dakatar da su yanzu ina da bukatar ganin ta".da wuri ya mike tare da fita a asibitin Ai ko an bude musu gate ne suna kokarin fita Allah yasa ya tsaida su yace muhammad yace a bar ta dole aka kyale ta cikin asibitin suka koma tare sai yanzu Sirajo yake ganin kamar akwai Kama tsakanin matar da Abokin shi..kujerar zaman Mai jinya ta zauna hannun ta ya rike yace"Dan Allah yanzu ya za'a yi Na iya tuno rayuwa ta Na baya har Na tabbatar ke din mahaifiya tace".

"Wannan ba matsala bane yanzu Zan Kai Ka wajen malamin da ya mini jinya sai Ka zauna a wajen shi har Allah yasa Ka warke".

" a'a ina da sana'a ta ba zai yuwu naje Na zauna a wani wajen ba sai dai nake zuwa ina Karba".

"Ehh haka ma yayi in zaka ke zuwa kullum". A haka suka ajiye zancen Amma iyayen Sirajo suna zuwa suka ce basu San da zancen ba akan me Mata ba'a San daga ina ta fito ba zata ce ita ce mahaifiyar shi sannan ba tabbacin abunda take fada gaskiya ne tunda bata da hujja." Allah kadai ne shaida Na Amma yanzu kuzo muje wajen malamin shi zai Baku labari in har Baku gamsu ba sai muje ayi DNA test".akan wannan zancen suka zauna shiyasa suka matsa aka sallame shi a ranar nan suka nufi gidan malamin wajen zama ya basu don ya San baki ne kuma Ai baki sun Saba zuwa wajen shi don shima ba Dan gari bane zuwa yayi yana taimako a nan Adamawa.."sannun Ku da zuwa bayin Allah ".

" Yauwa malam ko Ka shaida wannan matar"Baban Sirajo ya kare zancen yana nuna mishi Aunty "tabbas Na San ta anan makotan mu take da zama Yar gudun hijira ce to kallo daya zaka Mata Ka San tana cikin matsala shiyasa yan gidan suka kawo ta

waje Na ni kuma Na tambaye ta game da dangin ta Amma bata iya tuna komai kenan aikin asiri ne shiyasa daga wancan ranar take zuwa karban ruwan addu'a safe da yamma sannan har yau tana zuwa".

" to Masha Allah dama wannan bawan ta gani tace d'an ta ne shi kuma yace bai San ta ba don bai iya tuna komai nashi".

"Wannan ba matsala bace Ai ko wani cuta Yana da maganin shi sannan ba Wanda ya isa yace asiri ba zai kamashi ba don haka shi ma za'a mishi yadda aka Mata ko Allah zai sa a dace".

" alhamdulillah to malam ko za'a Fara bamu daga yanzu? "

"Eh ba matsala" cikin daki ya shiga nan ya fito da ruwan addu'ar a galon ya basu godiya suka mishi tare da ajiye mishi kudin sadaka suka fito waje "Dan Allah Muhammad kake sha Nima Zan ke tayaka da addu'a har zuwa ranar da zaka gane ni". Cikin sanyin jiki yace to sannan suka yi sallama da ita ko ba komai yanzu ta San inda yake Aiki..

Wasa gaske daga ranar da ya karbi ruwan maganin ba Wanda ya sake ganin shi har wajen sana'ar shi taje bata Gan shi ba Gashi bata San gidan su Sirajo ba har yau kwana uku ba karamin tashiwa hankalin ta yayi ba kullum cikin kuka take don a tunanin ta Shikenan ta gane Muhammad saura Laylerh Ashe abun ba haka bane..

A yau ne kuma su Sani suka sake Komawa kotu inda duk suke addu'ar yau ta zama Rana ta karshe prosciutto ne ya karanta case din lawyers suka gabatar da kan su sai lawyer'n Sani ya Fara bayani" ya Mai girma Mai Shari'a kamar yadda nace yau ina tare da hujjojin da zasu tabbatar da cewa Sani ba Dan damfara bane yana da aikin yi"mika takardun hannun shi yayi nan aka Mikawa alkali gyara glass Na idon shi yayi yana bin takardun da kallo Bayan ya gama sai ya gyada Kai alamar lawyer Mai kare Sani ya cigaba "sannan shaida ta Na biyu shine Wanda zai tabbatar da Sani Dan uwan yarinyar da ake nema ne kuma an mishi alkawarin auren ta". Bayan an bashi dama sai ya kira wani bappan Sani gaban court nan yazo" shin Ka San sani wane ne?"

"Shi din Yaron Dan uwa Na ne".

" yarinyar da matar can tace Yar ta fa?"

"Ita ma Yar Dan uwa Na ne".

" zaka iya Komawa wajen zaman Ka".

"Ya Mai girma Mai Shari'a matar can tace ita din Yar ta ce alhali ba Yar ta bace kenan tana da mugun nufi akan yarinyar".

" objection my lord barrister Isa yana crossing line saboda mu a nan ba batun wane ne Dan uwan yarinya a cikin su biyun muke ba,muna zance ne akan kudin da Sani ya damfare ta".Kai alkali ya gyada tare da fad'in "barrister Sauban Ka kula".shiru yayi ganin haka sai barrister Isa ya mike yace" duba da yadda wannan case ke tafiya Gashi lawyer Mai Kare Wanda ake Kara ya gagara gabatar da kwararan jujja a gaban kotu Na cewa Sani ya yaudari Hajiya kaltume kudi har naira dubu Dari biyar cewa zai kawo Mata yarinya kuma ga Gaza,to mu kaddara yarinyar Yar uwar shi ce kamar yadda shaidu suka nuna Ai kamata yayi ya hada hannu da Hajiya kaltume su nemo ta ko kuma ya samu kusanci da ita Hajiya kaltume don ya gane dalilin nemar yarinyar ba ya yaudare ta ba..sannan Hajiya kaltume tana Neman yarinyar ne don ta maida ta ga iyayen ta don taji labarin ta ta kuma bata tausayi sosai,da wadan nan hujjojin nake Neman wannan kotu Mai albarka ta yankewa Sani hukuncin da ya dace da shi Na gode"yana gama jawabin shi ya zauna sai alkali yayi gyran murya yana fad'in "duba da yadda komai ya wakana sannan Sani ya amsa laifin da ake tuhumar shi da shi to wannan kotu Mai adalci tana Umartar shi da ya maidawa Hajiya kaltume kudin ta sannan zai yi zaman gidan yari na shekara daya ko ya biya tarar miliyan biyu". Daga haka ya buga abun gaban shi nan kowa ya mike security'n shi suka mishi rakiya mutani ko sai tofa albarkacin bakin su suke yi nan police suka dauki sani zuwa prison yan uwan shi sai jimami suke yi..

**

Kasancewar ba karamin hauka yayi jiya ba yasa Tun a jiyan malam ya Kira Doctor sai yace in sha Allah yau da safe kan ya fita wajen aiki zai leko su hakan ne kuma ya kasance don yanzu zuwan shi kenan yana zaune a falo malam ko ya fito da Farouq..

Kallo daya zaka mishi Ka tsorata da yanayin shi don tunda suke da shi basu taba ganin abun yayi worst irin wannan Karon ba idanun shi ma a lumshe suke bai yarda ya bude su don sun rine sun koma kamar garwashen wuta kuma kana gani dole ta tsorata.. Jin muryar malam a falo sai Laylerh ta fito domin gaishe su Amma tana ganin Umar Farouq taci birki tana Neman hanyar Komawa fahimtar hakan ne yasa malam fadin" Laylerh Kinga karaso abun Ki ba abunda zai miki"Baaba ko tabe baki tayi Laylerh ko a hankali ta Fara shiga falon zuciyar ta Na bugawa can nesa da su ta nema jikin kujera ta rabuke"malam ina kwana?"lafiya ya amsa Mata"an tashi lafiya Baaba"ganin idon malam sai ta amsa ba yabo ba fallasa daga nan sai tace"sannu da zuwa Doctor "shima da Yauwa ya amsa shiru wajen yayi Doctor Na mishi check up ta dago ido kenan sai taga ya bude idanun shi da suke jawur kamar zai yi amai wuta ya zuba su akan ta nan take ta nemi nitsuwar ta ta rasa sai ga hawaye don wallahi tana ina karanto bala'in dake cikin idanun shi Wanda kuma tantama bata yi so yake ya sauke a kan ta shiyasa da wuri ta mike har tana hada sawu ta bar falon,tana fita ya maida idanun da suka mishi nauyi suke kuma Zafi ya lumshe har Doctor ya gama duba shi sai yace" maganin Zan rubutu Ku saya mishi don yayi ta buga jikin shi".da to suka amsa nan ya rubutu musu magani tare da musu sallama ya fice.. Malam ne ya dauki Umar Farouq ya maida shi daki sai ya fito ya zauna a falo

"baki ganin yanayin Farouq daga jiya zuwa yau yafi muni duk da ba Wai haukan tukuru yake yi ba Amma kallo daya zaki mishi Ki fahimci ya canza gaba daya".

"Wallahi Nima tunanin da nake yi kenan yanzu kuma Nifa tsoro Na daya kada a bar shi shi daya a daki in abun ya tashi mishi ya rasa Wanda zai sauke akan shi ya hallaka kan shi".

" wallahi Nima wani lokacin nakan tuna haka tunda ba hankali ne da shi ba Amma fa in kin Lura da kyau kamar yana jin zafin yarinyar nan".

"Eh mana Ka duba ya kan Mata kallon tsana da kuma gargadi duk da ba hankali ne da shi ba ina ji fa ko akwai abunda take mishi ne".

" me kuma zata mishi yarinyar da ke kan Ki shaida ce in ta Gan shi yadda jikin ta ke rawa ta rasa sukuni Ki kyautata Mata zato".shiru tayi don bata son suke samun matsala akan Laylerh "Kinga Bari naje Na sayo mishi magani" rufe bakin shi ke da wuya wayar shi ya Fara ringing nan ya cire a aljihu"to fa"ya fada a fili"lafiya kuwa malam?"

"Alhaji Muhammad wakili ke Kira".

" Ka daga mana kada ya tsinke".zama yayi tare da receiving Bayan yasa a hands free

"Wa'alaikasalam".ya fadi cikin tsananin girmamawa tamkar yana gaban Wanda suke wayar

" malam ya gida da iyali"muryar dottijo ya fadi daga daya bangaren"Alhamdulillah ya kokari?"

"Mun gode Allah Na shigo Nigeria fa yanzu haka ina airport Na taraba Amma hotel Zan Fara biyawa sai yamma Zan shigo wajen Ku".

" zuwan bazata haka Alhaji ".

" Ehh kuma gobe nake son komawa".

"To Masha Allah a huta gajiyar hanya sai Ka shigo". Daga haka suka yi sallama kan yayi magana Baaba ta Riga shi" kaga tunda kasan yana da diabetes Ka sayo acca sai a mishi tuwo da miyan kubewa tunda zuwan shin can ma ya tambaya ".

" Ai ko haka za'a yi Amma kin San ya dace a gyara dakin Umar Farouq kan yazo tunda ya kan leka ga kuma girkin Rana da nashi".

"Daki sai Laylerh ta gyara Amma gyaran yau tayi shi Na Musamman sannan tunda naji sauki kitchen din zan lallaba".

" to bara naje".

"A dawo lafiya kuma kada Ka manta da maganin Umar Farouq".

" in sha Allah don nasa takardar a aljihu "daga haka ya fice cikin sauri...

Bayan fitar shi ba jimawa Baaba Na zaune a falon taji sallama daga kofar falon ba'a shigo ba kuma" wa'alaikisalam "shiga Nabeela tayi gami da zama a kasa tana fad'in" ina kwana ".

" lafiya kalau yan Mata Amma ban gane Ki ba".murmushi tayi tace"Ince nan ne gidan da Laylerh take aiki? "

"Eh nan ne yan Mata".

" to Ai ni Kawar tace wajen ta nazo "nan take Baaba ta hada fuska sai kuma ta kwala kiran Laylerh da gudu ta fito sai ta durkusa tana fadin Baaba gani don hankalin ta bai Kai ga Nabeela ba" ga wacce take Neman Ki"Baaba ta nuna Mata Nabeela, da gudu ta fada jikin Nabeela tana"sannu da zuwa"ita ma Nabeela tayi farin cikin ganin Laylerh sai murmushi taji yi"Kinga tashi mu shiga ciki "ta fada tana Jan hannun Nabeela nan suka nufi ciki" saura Kije Ki zauna kada Ki daura abincin Rana ba sannan kiyi da wuri don za'a yi bako kuma zaki yi Na dare ga gyaran dakin Umar Farouq "duk cikin maganar ba Wanda ya bata tsoro kamar gyaran dakin Umar Farouq to ita wani gyara zata sake yi tunda hauka ya gwada mata" lafiya "Nabeela ta tambaye ta" Kinga muje kawai ba komai "dakin ta suka nufa akan Yar katifar ta suka zauna falo ta koma ta kawo ma Nabeela ruwa" ya aka yi Kika gane gidan mu".

"Hmm zuwa gidan ummie nayi ta mini kwatance banda mijin ta Na gida ma da ta biyo ni kuma Ai gidan ba'a boye yake ba".

" to ya mutanin gida?"

"Gida kowa lafiya sun ce Na gaishe Ki Adam kuma ya bani sako Na kawo miki".

" to yau kuma wani irin sako".bude bag nata tayi sai ta Ciro karamin enlargement ta mika Mata, Karba tayi a zuciyar ta tana mamakin me ne Ai ko tana juya fuskar taga enlargement Na hoton ta da Naseer aka yi da wuri ta kifa hoton tana dafe kahon zuciyar ta sai kuma ta Fara hawaye"Kinga in kuka zaki yi tafiya Zan yi"da sauri ta share hawayen da Bayan hannun ta sannan ta girgiza Kai"a'a Na daina Ai ni duk jalingo ba Mai so Na sai ke tunda har Kika iya Neman inda nake,ya wajen aiki kuma?"

"Ba dadi fa wallahi boss yafi da tsanani Nima ranar Harda Mari Na yayi".

" mugu kawai Allah ya isa miki".Baaba ce ta Fara kwala Mata Kira"Kinga Nabeela zo muje kitchen in ba haka ba matar nan ba zata bar ni ba".ajiye enlargement din tayi suka nufi falo tare suka shiga kitchen suna hira Laylerh Na aiki Nabeela Na taya ta"Laylerh har Accounter an Kore shi don an Kama shi da cin amanar company ".

" shi ne ni kuma ya agaza aka Kore mu Ashe shi ma halin shi daya da Penna kenan sabon Accounter aka kawo muku?"

"A'a madam din da kan ta ta bawa wani rikon kwarya baki ga matar ba Laylerh akwai zafin nama in baki fahimce ta ba zaki ce muguwa ce".

" duk zafin ta ta Kai boss ne? Laylerh ta tambaya tana daura pot akan gasa"wallahi tafi shi ke shima tsoron ta yake ji".

"Kice like mother like son".

" Ai kuwa dai".nan suka cigaba da aiki har malam ya dawo nan yayiwa Nabeela sannu da zuwa ya wuce dakin Umar Farouq magani ya bashi ba jimawa yayi bacci sai ya fito don yau dai da alama ba zuwa kasuwa tunda suna da Babban bako..

Suna gama abincin Rana ta fidda set Na kulan Umar Farouq "wow Laylerh cooler's din sun mini kyau". Cikin yin kasa kasa da murya yadda ba za'a ji ta ba tace" a haka kuma Na mahaukaci ne".

"Mahaukaci kuma" da sauri ta rufewa Nabeela baki da fad'in "rufa mini asiri su basu son a Kira shi da mahaukaci" da yake Nabeela ba irin mutanin da suke dipping into people's lives bane sai bata sake magana ba har aka gama raba abincin nan suka dauki nasu zuwa dakin Laylerh suka ci sai suka fito miyar dare tayi sannan ta daura Na Alhaji Muhammad wakili Ai ko girki kam Masha Allah..

Ana kiran la'asar Nabeela ta tafi Laylerh ji tayi kamar kada ta tafi dawa tayi gida Bayan ta raka ta"Allah sa dai jakar tan ba abun gidan mu aka sa Mata ba"murmushin da yafi kuka ciwo tayi tace"a'a Baaba "daga nan ta wuce ciki tana jin zafin abunda Baaba ta fada a kan ta daki ta wuce sallah la'asar tayi sai ta fito falon" Kije yanzu su malam zasu fita wajen training Ki duba daki Na akwai sabon TV da aka saya Ki tafi dakin shi da shi,sannan a store akwai carton Ki dauka sai Ki zuba tarkashen Wanda ya fasa jiya a ciki,Ki bude wardrobe nashi a gefen hagu akwai bedsheets Ki dauki blue Ki shimfida mishi".to tace don ita bata ji da kyau ba ji tayi kamar Baaba cewa tayi sun fita shiyasa ta nufi kitchen kunun gujjiya ta juye a flaks sai ta nufi corridor Baaba ko bata Lura da ita ba hankalin ta Na ga TV..

Dakin Baaba ta nufa nan ta dauko TV duk nauyin shi ta tura kofar da kafar ta a hankali sai ta shiga ta ajiye, store ta koma ta dauko kwali da aka fada.. west nata ta rike lokacin da ta shiga ciki tana karewa dakin kallo"lallai jiya bawan Allah'n nan ya harzuka dubi yadda yayi da daki"a hankali ta sunguna ta tsine TV'n da ya fasa dukka sannan ta ajiye a corridor gefen kofar shi, dakin ta dawo cire tv'n tayi a kwalin shi ta ajiye a TV stand Na dakin sai ta Fara da gado.. bedsheet ta cire tare da karkabewa sai kuma ta nade shi sannan ta jefa shi kan tiles a cewar ta in ta gama sai ta ajiye a inda ya dace,nan ta nufi wardrobe nashi hannun ta dukka biyu ta daura kan hannun wardrobe din Wanda dalilin haka ya tilasta murfin wardrobe din budewa dukka a lokaci guda,ido ta zaro a fili tace"duk Kayan nan Na mutum daya"sai kuma ta tsaya tana karewa bedsheets dake Jere a goge kallo domin blue din take nema kamar yadda Baaba ta fada nan idon ta ya sauka kan blue sai ta zaro shi a hankali gudun kada ta wargaza sauran..rufewa tayi sannan ta juya a bakin gadon ta tsaya,hannu ta mika domin daukar pillow Wanda dole ta Dan kwanto gadon don a can tsakiyar gado yake..Jan dayan tayi tare da cilla shi a kasa sannan ta koma domin daukar dayan,yadda tayi da Na farkon haka taso tayi da Na biyun sai dai kuma taji da banbanci domin wannan kamar akwai abu a ciki, pillow case ta daga zata cire sai taji kamar abu Na rawa a ciki karkabe shi tayi a kan gadon sai ga waya iPhone 12 pro ya fada kan katifar sabuwa fal don da alamar ba'a jima da Fara

amfani da ita ba ido ta tsurawa wayar hannun ta Na rawa ta daga sai taga an Fara kirar wayar kenan yana silent shiyasa bata jin ringing har wayar ta katse bata daina bin wayar da kallo ba,kasancewar ta Mai karambani sai ta tura screen din sama a tunanin ta akwai pattern ko password sai taga ba komai illa hoton handsome guy da ya bayyana a fuskar wayar da gani kuma balarabe ne fari ne tas da shi ga saje shimfide a fuskar sa gashin girar shi a ciccike ga lashes nasa a tsaye iya haduwa guy d'in ya hadu saboda zallar kyau ce Gare shi Wanda ba algus a cikin sa

"wannan duk yadda aka yi Dan uwan mahaukacin nan ne don resembles yayi yawa"maganar zuci da take yi kenan don ita ba wannan mahaukacin bane take gani a hoton..

Tana cikin kallon hoton message ya shigo zata Danna read ya bace sai ta Danna view nan ta shiga message body

"Dear Mr Umar Farouq M wakili Na Kira Ka sau biyu baka daga ba ina son fada maka gaskiya abun ba yadda muke expecting bane ta ko ina abun yana son tashima Na,kuma abun takaicin shine Mun Riga Mun gama hada komai Amma Kuma all effort namu is in vain in har baka Karba abun nan zuwa gobe ba akwai Babban matsala don an Fara suspecting Na ta ko ina kuma in an Kama ni kasan a bakin rai Na ne shiyasa a gobe Zan koma abuja don haka Zan ajiye maka sakon a bakin kogi,steps biyar kan inda masu ruwa ke deba,a filin akwai ciyawa to a tsakiyar ciyayin zaka ga an ajiye blocks biyu kamar mutum ne ya zauna a Kai,Ka daga block daya da ya tsage a gefen sai Ka tona kasa a ciki zaka ga sakon...thank you from Michael Sunday".

 Shine message da aka turo mishi a take jikin ta ya Fara rawa in ta fahimta kenan zargin da ta Dade tana mishi gaskiya ne Na cewa shi kidnapper ne tunda kasan gadon shi makamai ne ba irin Wanda babu..

A hankali ta daga kafar ta da nufin zata je ta sanarwa Baaba sai ganin shi tayi tsaye bata kuma San daga ina ya diro ba don yadda ta tsorata sai kawai ta yanke jiki ta fadi a kasa tana jin ina ma ta mutu kan wannan ranar don ta tabbatar kashe ta zai yi wannan Karon Amma kuma kash ba mutuwar Allah da annabi zata yi ba..

Bata gama fita a firgicin da ta shiga Na ganin shi ba ya dago ta sama ta hanyar shake wuyar ta sai ji tayi ya wanka Mata Marin da yasa taga wuta, bata gama dawa hayyacin ta ba ya kuma debe ta da Wanda yafi Na farko kan ta fita a firgicin Marin da ya Mata ya hada kan ta da gini... zuwa yanzu idanun ta kokarin rufewa suke don azaba Gashi bala'in da take kallo a idanun shi yafi komai bata tsoro lallai ta yarda in kaga mutum yayi kuka to abu bai yi abu bane lumshe idanun take ta kuma bude su a kan shi inda biyu-biyu take kallon shi alamar tana gab da sumewa masa..

Hannu ya mika a inda take kallon gini ne sai gani tayi drawer ne, bude drower'n yayi sai ya fiddo bindiga an hankali ya Dan rage sahon sa tare da janyo ta ya jefa ta kan gado idanun shi nan zaka ce in yayi hawaye jini ne zai fito a kanta ya saita bindigar cikin murya Mai Amo da kuma nuna shi din Na miji ne yace

"Wa kike yiwa aiki". Saukan zazzakar sautin muryar sa da kuma Amo yafi komai daga Mata hankali shiyasa har fitsari tayi a tsaye kenan yana magana ba kamar yadda ta dauka ba, bata gama tunani ba ya shake ta cikin tafasa da kuma bacin rai yace

"nace Wa ya aiko Ki".

Idanu ta lumshe tare da zuba su akan shi,tabbas hannun shi da zafi amma zuwa yanzu wajen ya daina zafi sai goshin ta da ya buga ne ke zugi lokaci zuwa lokaci maganar da taji yanayi shine ya jefa ta cikin mawuyacin hali da har ta gagara magana sai Kai ta shiga girgiza mishi don yau kam mutuwa zata yi"kina yarinya karama kin bata rayuwar Ki don ko wane ne ya turo Ki ina Mai tabbatar miki yau din nan ba sai gobe ba sannan yanzu ba sai Anjima ba Zan kashe Ki".yana gama fadin haka ya jefa ta can karshen gadon ita fa sama-sama take jin shi don ranta a wuya yake ina ma ace ta mutu kan wannan ranar

"nayi shekara da shekaru ina aikin nan sanda nazo last stage of completing my mission zaki lalata mini komai,Zan kashe Ki kuma Na kashe banza don kallon mahaukaci duniya zata mini sannan kowa tunanin kinzo kashe ni ne Na kare kaina za'a yi don haka good bye". So take ta bude baki tayi magana amma ta kasa don ji tayi yawun bakin ta ya kare" waye kai?wani mugun abu kake aikatawa wanda ko iyayen Ka basu sani ba?shine tambayar da take maimaitawa cikin ranta a daidai lokacin kuma ya shako wuyar ta ya manna bindigar da gefen fuskar ta sannan ya tsaita kunamar binhidan ji kake yi ta!!!!!".

in Baku manta ba Michael Sunday shine bakon Alhaji Musa Wanda suka hadu da Sani,me alakar shi da Umar Farouq?

Wallahi dauriya ce ya sani typing don mura da nake fama da shi

This time around Na gaji da cewa ba'a comment in naga ba'a yi comment sosai ba Zan tafi hutu😁a page nan

masoya Na masoyan LAYLERH show some love by commenting nasan zaku so jin cigaban labarin

Comment

Share

©Hafciey Musa[1/25, 5:41 AM] Hafciey Musa😘: *□LAYLERH□*

(The prettiest emerald)

Ah swear naji dadin yadda kuka yi comment a last page□thank you all I love you sosai□..Umar Farouq ma Na gaishe ku□

26

Tsaki yaja gami da sauke bindigar a kan ta zuwa lokacin kuma tuni ta suma,mikewa yayi ya nufi toilet ruwa ya debo ya juye Mata a fuska yana daga tsaye cikin firgita ta farfado zama yayi a kan bed side drower yana wasa da bindigar a hannun shi da gefen ido ya kalle ta yace "mutum Na farko!ke ce mutum Na farko tsahon wannan

shekarun a rayuwa ta da wani ya San sirri Na,ba zan kashe ki ba saboda ni ba makashi bane..Amma Ki sani ko a hukunce kinci kisa!yanzu the choice is yours,your life is in your palms if you are the parrot-kike then go and make lots of noises,I won't waste my time telling you abunda zai faru..

Lumshe idanu tayi murya Na rawa tace" wallahi ba Wanda nakewa aiki asalima an turo ni ne don Na gyara maka daki to ina daga pillow case sai naga waya ya fadi mistakenly Na karanta sakon Ka".duk zancen da take yi baya kallon ta wallpaper'n dakin ya taba sai ga drower ya budu bindigar ya mayar sai yace"fice mini a daki ya rage naki ko Ki rufa mini asiri ko Ki tona".

jikin ta har rawa yake yi ta fice a dakin nan shi kuma ya shiga tunani..

Umar Farouq M wakili d'a ga Alhaji Muhammad wakili mamallakin M wakil petroleum Nigerian limited.matan Alhaji M wakili biyu ne inda Hajja Maryam ta kasance uwar gida a Gare shi,Hajja maryam shuwa Arab ce Baban ta Dan chad ne Amma a Maiduguri suke da zama a can ne kuma ta hadu da Alhaji M wakili suka yi Aure.. d'an ta Na fari da ta Haifa Umar Farouq ne sai Mai bi mishi Hafsat suna kiran ta da Nana,Bayan haihuwar Nana ya Kara Aure to daga nan sai suka cigaba da haihuwa a tare da amaryar shi Hauwa..yaran Hajja Maryam hudu kuma dukka uku Mata ne Umar ne kadai Na miji haka bangaren Amarya Hauwa ma yaran ta duk Mata ne sai autan ta ne Na miji duka duka yaran shi takwas ne..Umar Farouq Nada shekara 11yrs Allah yayiwa Hajja maryam rasuwa nan ne rikon su ya koma hannun Aunty Hauwa..

Umar Farouq matashi ne Mai kimanin shekara 34yrs,Fari tas da shi da Ka Gan shi kaga balarabe don Asalin Maman shi,Law ya karanta a Cambridge university, yayi jss class nashi a nan Nigeria daga Ss class ya tafi dubai wannan ya sa shi rashin sakewa da mutani don shi daya yake rayuwa. Bayan dawowar shi sai Baban shi ya nema mishi aiki da NIA daga nan ya Fara training..

NIA(National intelligence agencies) suna nan kamar reshe ne Na DSS,duka suna kasan office Na national security ne

DSS for domestic intelligence

NIA for foreign intelligence

DIA for military intelligence

Function nasu is similar to that of American course da ake reading before a zama NIA kuma shine International relations sociology in all,social science courses basu da uniform kamar DSS kuma basu rike bindiga sai dai for self defense, it's headed by bichi kuma suna employing secondaries, diploma da degree.. Aikin su shine to source information akan duk wani abunda zai kawo rashin zaman lafiya suna amfani da biro,waya sauran abubuwan duk a headquarters ko special operations with collaboration with DSS suke amfani da shi..aikin su sirri ne don haka bai kamata a San su ba koda Dan uwan Ka Na jini ne wannan dalilin yasa ba zaka taba jin sunce maka ga aikin su ba saboda aikin su kare jami'an Nigeria akan yan wasu kasa sannan su binciko wadanda suke kokarin shigar da makamai da dai sauran mugayen abubuwa Nigeria..basu fita waje don aiki saboda yawancin aikin su a kasan waje ne irin su Cameron, Niger, Us,london basu fiya zama a gida Nigeria ba don su binciko ko daya daga cikin kasashen duniya Na kokarin kawo hari sai military ta shirya..suna aiki da internet da computer Google don su San ko Cameron Na Gina machine guns da zasu kawo Wa Nigeria hari shiyasa ake kiran su da national intelligence agency to source and gather information intelligently sai suyi supplying zuwa ga DSS ko police and Army..

Suna karban salary da ya ninka Na DSS sau uku wannan dalilin yasa in Ka shiga aikin in sha Allah Kai da talauci kam sai wani kaddara sannan basu zama a ko wani gari sai Abuja..yayi shekara bakwai a aikin kuma yawancin aikin shi baya samun long service don bai fiya wuce irin su Singapore ba..

Wata Rana yana zaune a headquarter nasu dake Abuja cikin katafaren office nashi ya kurawa laptop Na gaban shi manyan idanun shi tamkar zai hade system din sai wani Abokin aikin shi Hashim yayi knocking "yes come in" shiga yayi ya zauna har zuwa lokacin kuma Umar Farouq bai dago ya kalle shi ba,hakan tsam bai damu Hashim ba don ya San yadda Umar Farouq ya dauki aikin shi da mahimmanci shiyasa yace"Na sama mana wani quick money a abroad kuma yana kawo kudi sosai"har yanzu bai dubi Hashim ba sai hannun shi dake ta danna key board Na laptop din zaka ce bai gajiya "me shi?" Shine tambayar da ya jefawa Hashim yana cigaba da aikin shi"wani business ne a marlin yana kawo kudi sosai in Mun Fara zaka sani but for now ina bukatar miliyan Dari biyu a wajen Ka".

"Ce maka aka yi buga kudi nake?"

"Kana matsayin da ga Alhaji M wakili kace miliyan Dari biyu zai gagara a account naka". Sai yanzu ya dakata da abunda yake yi ya dago ya dube shi lokacin da yake cewa" don bai da abun yi da kudin shi sai ya Tara mini?".

"Pls dude mu bar wasa da gaske nake yi tunda har kaga Na bar office Na nazo wajen Ka,kuma Tun jiya nake kiran wayar Ka baka daga ba".

" look Zan iya baka kudin but sai naji wani irin business ne kuma naga nawa profit Na a ciki".

"Wallahi akwai riba cikin Wata biyu Zan maida maka miliyan Dari biyun Ka"nan ya ture laptop Na gaban shi yace" Haba Umar Farouq a kan miliyan Dari biyu kake mini haka abunda kafi karfin su kuma banje wajen kowa ba sai Kai"fushi yayi nan ya mike ya nufi fita"zo ba zamu yi haka ba"

"Haba wallahi duk agency'n mu Kai ne nasan Zan nema Ka bani".

" fine Zan baka Amma da condition cewa zaka dawo mini da kudi Na nan da Wata biyu".

"Yeah bare ma riba Zan dawar maka mu cigaba da juya uwar kudin in ya sake ninkuwa Na sake baka miliyan Dari biyu".

" ohk mu rubuta agreement "

ba tare da ya kawo komai a ran shi ba ya amince don yana kyautatawa Hashim din zato bai San kan ya shigo he manage to disconnect CCTv dake office Na Umar Farouq din ba

nan suka rubutu agreement sai suka Kira wani cikin agent nasu ya zama shaida tare da yin photocopy suka rike daya daya sannan shi shaida ma aka bashi guda daya sai ya mishi transfer'n kudin daga nan Hashim yayi godiya ya fita... Wanda ya

musu shaida kuma yace"me Hashim zai yi da kudi masu yawa haka?"baki Umar Farouq ya tabe alamar shi dai ya sani..

Bayan Wata biyu

Kwance yake a office yana aiki a laptop nashi da ya zama Abokin hirar shi baya taba yin minti goma ba tare da yayi aiki a laptop din ba, alert ne ya shigo wayar shi yana dubawa yaga miliyan Dari biyu ne Hashim ya turo mishi"hmm Hashim yayi kokari ya kuma cika alkawari cikin Wata biyu ya dawo mini da kudi Na".ya fada a saman labban shi yana cigaba da aikin shi

"Ko kuma ya dawar don yace Ka Kara mishi miliyan Dari hudu ba".

 fadin kyakyawar budurwa Sadiya Mahmud Ardo wacce kallo daya zaka Mata kasan kudi ya zauna Fara ce Tass da ita sai dai ba yarinya bace don ko Umar Farouq zai girme ta bai wuce ya bata shekara uku ba.Asalin ta Yar Adamawa ce ta taba Aure tana da daughter daya mijin ta ya rasu kuma ita ma NIA ce kamar Umar Farouq suna nan a thesame rank,Baban dan Nigeria ne maman ta kuma Yar sadaka yalla ce.. murmushin dake karawa fuskar ta kyau tayi sannan ta cigaba

"Ka shiga tarkon Hashim fa uncle Umar Farouq" haka Yar ta ke kiran yan agencies nasu

"Ai duk danger'n Hashim kin fi shi hatsari wallahi ".ya fadi ba tare da ya kalle ta ba kuma bai sake Mata fuska ba kace bai San ta ba

" Amma Ai ni duk abunda nake yi kana sane da shi ba kamar Hashim ba".

dakatawa yayi da aikin shi yace"wallahi Nima so nake Na bincika Na gane business da yake yi Amma ban son yace ban yarda da shi ba".ya kare zancen yana danne danne a wayar shi

"Ka bar shi dani kasan I am a very smart investigator Zan bincika maka abunda yake yi da kudin".

" kin kyauta "yace da ita yana cigaba da aikin shi..

Sadiya Mahmoud Ardo mace ce Mai hatsarin gaske don zuciyar mutum ne kadai bata iya karantawa sannan yawancin yan agency'n su haushin ta suke ji don ita nunawa take tafi kowa sannan a kullum bata da burin da ya wuce matsayin ta yafi Na Umar Farouq kuma shi kadai ke kallon idon ta ya fada Mata maganar da yaso shiyasa ko kadan basu shiri da Hashim..

Bayan sati biyu

Fitowar su kenan daga meeting hall kowa ya nufi hanyar office nashi Sadiya ce a Bayan shi" muje office Ka gani"juyawa Sadiya tayi banda Umar Farouq saboda bai bukatar ganin wane ne muryar ya tabbatar mishi da cewa Hashim ne"ohk Sadiya muje".yace don ya yana da aikin da zai sata..

matsowa kusa da shi Hashim yayi cikin kunnen shi yace

"kasan duk maganar da nace muje office sirri ne meyasa zaka ce Sadiya ta bi mu".

"You are not welcome anymore" duk sun gane da Sadiya yake yi sai tayi wani killer smile tana kesta chewing gum da kuma Danna iPad da ke hannun ta tayi gaba,hada rai Hashim yayi yana fad'in "meyasa zaka mini haka ka san ta da bin....." Sai kuma yayi shiru kallon tuhuma Umar Farouq ya mishi yace"Ehem ina jin Ka Na San ta da me?"sai cewa yayi babu a nan kuma Farouq ya fahimci ma'anar shi zata bincika kuma subutan baki ne ya sa shi fadin haka a take Umar Farouq ya tabbatar da akwai abunda yake boyewa kuma yana tsoron kar fa yayi implicating nashi cux shi da Sadiya bai taba yarda da su ba kuma ba zai taba ba gwara Na rike Wanda ya tura mini a madadin riba ya zama uwar kudi Na nayi stopping wannan abun..

Yana tunani ne a yayinda suke tafiya a haka har suka shigo office zama yayi a kujerar shi sai yaga alert Na miliyan Dari biyu daga Kai yayi yana kallon Hashim cike da tuhuma"ba Na fada maka ba business nan Na kawo kudi kana tunanin karya ne Ka San ribar da Na samu cikin sati shida kuwa".

"To ni dai tunda Ka samu Ka tsaya da kafafun Ka ni miliyan Dari hudun ma ya ishe ni ba sai Ka sake Kara mini komai ba". Dariya Hashim yana fadin" nikam Ka Fara zargi Na ne".

"A'a ni irin business nan ne ban so kuma kaki fada mini abunda kake yi" abunka da Mara gaskiya a take ranshi ya baci sai yace"kana tunanin legal business nake yi ne,ni fa security agent ne ya za'a yi nayi legal business "ya fadi cikin haurawa Umar Farouq da masifa

" Kai Hashim nace ba Zan yi ba Ana dole ne"shima Umar Farouq ya fada cikin bacin rai don bai ga dalilin da zai sa Hashim ya Riga daga mishi murya ba..nuna shi da yatsa Hashim yayi yace"be very careful baka San me Zan maka ba bar ganin iyayen Ka Nada kudi kana da influence wallahi sai Na hallaka Ka".

"Kai Hashim who the hail are you a tunanin Ka ban San sirrin Ka bane wallahi nafi Ka danger sannan kan kaga baya Na sai naga Bayan ka".

" to mu zuba mu gani".shi Umar Farouq din yayi haka ne don ya tabbatarwa Hashim ba tsoron shi yake ji ba, sannan Hashim din yaji tsoron shi ko da zai yi wani abunda zai yi implicating nashi yaji tsoro Amma Bayan wannan bai da Wata manufa a zuciyar shi,shiyasa yace"ehh mu zuba mu gani".ko da Hashim zai fita sai ya juya yana nuna shi da yatsa cikin tsananin bacin rai yace"take note".

"No you take note"Umar Farouq ya fadi nan ya fice cikin tsananin bacin rai fitar shi ke da wuya Sadiya ta shigo tana yiwa UmarFarouq dariya "ya naga mutumin Ka ran shi a bace ne ko dai ka hanashi kudi ne ko da yake nasan yanzu yana da kudin da yafi Wanda zaka bashi". Cikin bacin rai da tafasar zuciya yace

" Wai ya kuke mini magana a dunkule ne?"

"Kunyi fada ne?" Ta tambaya,cikin jin haushin Hashim din yace

"can you imagine Wai ni Yaron nan yake warning Na shiga hankali Na if not zai ga baya Na".

" calm down my dear and you should be very careful don zai iya maka abunda baka taba zato ba he is dangerous ".

" kin gano business da yake yi ne?"

"Yeah Na gane but before Na fada maka sai Ka kashe CCTV dake office naka".

da yake yana son sanin business da Hashim ke yi sai ya kashe nan ne tace

" safaran makamai da saida cocaine yake yi".

a take Umar Farouq ya shiga rudani don yanayin aikin sa ba abunda yafi tada mishi hankali sai agreement da suka rubuta Amma da yake Na mijin duniya ne sai bai Bari hakan ya bayyana a fuskar shi ba"Hashim Ka cuce ni".Bai San maganar ya fito fili ba saida yaji Sadiya Na fadin

"Baka ga komai ba ma" ta bashi amsa tana juyawa ta nufi kofa

"Sadiya"ya Kira sunan ta,tsayawa tayi tare da Juyowa "je Ki kawai".ya fada yana nuna Mata kofa

" kana da bukatar taimako Na ne?"

"Ai bana Neman taimako a wajen mace don haka Kije kawai".

A Daren ranar yadda yaga Rana haka yaga dare yana tunanin yadda zai yi sunan shi ya fita a abun ganin an dame shi da Kira sai ya kashe wayar gaba daya... har Dana sanin Fara aikin yayi kasancewar harkar Babban abu ne a wajen aikin shi, tsam Sadiya da Hashim ba Allah a zuciyar su shiyasa bai taba dagawa ko dayan su kafa ba.. Nafila ya Riga yi tunda bacci ya gagara Ana kiran asuba ya fice zuwa masallaci sai da liman bai zo ba wayar shi ya cire a aljihu ya kunna tare da kunna data ya shiga WhatsApp abunda ya Fara cin Karo da shi ne ya matukar tada hankalin shi ba komai bane face mutuwar Hashim a Daren jiya Wanda an tabbatar cewa kashe shi aka yi daga nan messages Na manyan su ya Fara shigo mishi kowa kuma cewa yake karfe biyar da rabi Na Asuba ya tabbatar yana headquarter..

Sallah yayi nan ya shirya zuwa office Ai ko zaka ce Rana ne don headquarter a cike yake da agencies direct meeting hall ya nufa don yasan kowa Na wajen yana tura glass door din ya Fara kokarin saluting oga'n su sai yace

" no need Wato Ka kashe shi hankalin Ka ya kwanta".

"Sir ban kashe kowa ba" ya fadi fuskar shi ba ko digon Tashin hankali don ya San bai yi kisan Kai ba..

karar takalmi hill Na mace ne ya Fara alerting nasu cewa mace ce ke tafe ko da aka tura kofar sadiya ce ta shigo

"Sadiya kince shi ya kashe shi ko zaki bada hujja".

" yes Sir ko rantsuwa nayi ina Mai tabbatar maka ba Zan yi kaffara ba don a jiya sun yi fada koda Na tambayi Umar Farouq sai bai sanar da ni ba shiyasa Na bi diddigin CCTV dake office nashi naji komai inda ya tabbatarwa Hashim cewa zai ga Bayan shi sannan a Daren jiyan Bayan ya tura a kashe Hashim sai ya kashe wayoyin shi sannan dukkan mu nan Mun Riga shi zuwa headquarter da muka ji labarin mutuwar shi ko yana can yana bacci cikin kwanciyar hankali".

tabbas ya San Sadiya zata yi abunda yafi haka don matsayin shi take so shiyasa bai yi mamaki ba,in charge Na camera room aka Kira nan ko aka yi connecting inda

Umar Farouq ke cewa sai yaga Bayan Hashim bai San kuma ya aka yi ba iya wajen ne aka yi playing..

Nan take aka Kama shi da laifin kisa sai aka Kai shi waiting room Na headquarter kafun a San inda za'a Kai shi..yana zaune yaji an fincike shi da yake under ground building ne sai tafiya da shi ake yi gane kashe shi ake son yi sai ya Fara kokarin kare kan shi ya illata Mai Jan shi nan ya Fara Neman hanyar fita Amma babu da kyar ya samu hanya yana fita kuma gida ya nufa nan ya sanar da Dad nashi abunda ke faruwa a take ya shirya mishi barin garin don ba zai Bari a kashe d'an shi akan abunda bai aikata ba..zuwa yanzu ya gama fahimtar yana da makiya dayawa a headquarter Wanda cikin su wani ya kashe Hashim sannan yayi amfani da rashin jituwar da suka samu ya daura mishi laifi kuma shi yafi ganin Sadiya ce don ba Wanda ya San sunyi fada sai ita..

A take aka baza securities ta ko ina a Abuja suna Neman shi da yake Baban shi Babban mutum ne sai ya samu hanyar fita a Abuja suka nufo Taraba don so yake yayi nisa da gida sosai..a wrist watch nashi akwai abunda aka saka a ciki Wanda duk staffs Na headquarter su da shi suke amfani yana nuna location Na inda mutum yake cux su basu siyan watch agencies nasu ne suke bayarwa kuma duk sanda akayi kokarin locating naka ba'a samu ba to zai yi implicating naka shiyasa ya Saba da agogon har yazo taraba bai tuna ba..

A dayan bangaren kuma anyi amfani da location Na agogon da ke hannun shi ake bin shi inda kuma duk sun tabbatar ya shigo taraba, team biyu ke bin shi daya DSS wadanda suke son shi a Raye sai daya kuma yan daba da aka tura su kashe shi.. a daidai mutum biyu ne aka Fara musayar wuta tsakanin bangare biyun don securities din sun hankala da yan Daba, kokarin kare shi suke yi sai a sannan ya Lura da agagon sai ya cire ya jefa a daji sannan ya fice a motar ya shiga wani gona nan take suka neme shi suka rasa Amma kuma tabbas an San yana cikin taraba..dama already ya zubar da duk wani abunda zai yi implicating nashi irin su waya da dai sauran su motar haya ya shiga har zuwa cikin jalingo don ya San in ya tsaya a kauye kowa zai fahimci akwai bako to fa asirin shi zai iya tonuwa..

Yana shiga jalingo ya nemi wani local hotel ya sauka don bai da komai a jikin shi sai ATM Bayan ya Dan huta sai ya fito zuwa wani shagon saida waya.. baby Nokia ya siya sai yace ya za'a yi ya samu Sim nan wani yace Ai suna saida Sim da aka yi register sosai yaji sanyi a ran shi tunda Sim din bada sunan shi aka yi register ba kudi suka cire ta POS sannan ya juya ya nufi masaukin sa.. number'n Baban shi yayi

dialing da yake shima security ne kuma ya iya bincike to ya San dole in an neme shi an rasa za'a yi tracing line Na Baban don dole ya Kira shi shiyasa Ana picking sai yayi shiru can sai ya ja dogon numfashi nan take Baban ya gane shi ne sai ya katse kiran sai Bayan wasu awanni ya Kira

"Umar kada Ka sake kiran line Na yanzu haka Nima ba don influence da nake da shi ba da sun tsare ni yanzu ina kake?"

"Abba ina taraba cikin jalingo kuma daga yanzu ba zan sake Kiran ka ba don hatsari ne a Gare Ka, so nake ka nema mini gidan da zan zauna sai dai ya zama dole na koma mahaukaci in ba haka ba duk gidan da zan je zasu yi suspecting nawa sannan zan nuna musu bana magana haka zalika bana ji don maybe wasu zasu biya su kudi fiye da mu sai su tona mini asiri kaga zan ji daga nan sai na bar garin and naji ance an basa DSS a taraba gaba daya dole anguwan yan iska zan zauna don sune ba'a musu wargi su Bari and zan Riga tada haukan lokaci zuwa lokaci har Randa Allah zai sa na gama binciken na a boye Na gode Abba ".

"Wannan line din ba nawa bane ina gamawa Zan karya Ka tura mini address Na inda kake Zan tura maka mota yanzu". To yace, kasancewar mahaifin shi Babban mutum ne sai ko ya samu Wanda ya sani a taraba nan aka nemi gidan da za'a ajiye shi ta bakin kogi sai aka ga gidan Baaba yafi cancanta don suna da mutunci nan ne fa aka kashe su da kudi tare da musu renovating ta ciki aka canza komai Na gidan dakin shi kuma lokacin da za'a sa wallpaper ne aka mishi drower a sirrance..

Randa aka kawo shi gidan su Baaba sun yi mamakin Wai mahaukaci ne sai rufe musu baki aka yi da cewa baida uwa yadikko ce ta haukatar da shi sannan yanzu ma nema take taga Bayan shi shiyasa suka kawo shi nan sannan da kan su zasu ke kawo mishi magani Amma kada su taba sanarwa duniya cewa shi ba Dan su bane..

Aiko iya tausayin shi sunji nan ne suka ce zasu rike shi tsakani da Allah har makaranta suka sa Auta ita ko ganin kudi sai ta Fara kiran shi yaya sai wani ji da shi take..

Tun daga ranar bai sake ji daga Abban shi ba Amma kuma yana binciken shi ba tare da kowa ya sani ba don duk batun Daukan shi da su Baaba ke yi da kan shi yake fita yana karban evidence da masu mishi aiki cikin sirri ke kawo mishi..

Ko Randa ya yanka wani da wuka yana sane don mutumin ya Kama shi yana waya ne Amma kuma bai tabbatar ko shi din bane don yaji Ana magana ne da ya leka lungun kuma Umar Farouq kadai ya gani zuwa lokacin kuma Umar Farouq ya yanke wayar har ya sa a aljihu ganin mutumin Na mishi kallon tuhuma Anya wannan ba shi bane mahaukacin nan sai ya dauki wuka wajen Mai rake ya yanke shi a hannu don ya tabbatar eh mahaukaci ne zai yi haka..

Sannan ranar da ya kwana a waje kuma kasancewar shi CEO Na company'n Abban shi Ana da bukatar sa hannun shi shiyasa Abban shi ya turo amintaccen shi ya kawo documents d'in yayi signing sannan ya bashi wasu prove da yazo da su daga abuja..

Drinks da Baaba ta gani a kasan gadon shi kuma shiyasa aka kawo mishi,batun rashin iya bacci ba tare da Nepa da kuma cin dadi ya Saba ne..

Idanun shi dake ja kuma magani yake sha sannan jiwa kan shi ciwo da yake kam da gaske ne,duk lokacin da ya dawo idon shi biyu pretending kawai yake kamar me bacci..

Ranar da su Baaba suka ga gilmawar mutum kuma ya manta ID card nashi ne aka biyo shi da shi..mutanin da yake kori a gidan da sunan bai son hayaniya yana haka ne gudun kada Wata Rana wani ya gane inda yake.

Motar da malam ya gani a kofar gidan kuma shi ake jira ya fito yayi signing and ranar da ya fita har aka hada tarko akwai me bashi information Na anguwar duk sanda ya fita duk da cewa Mai mishi aikin bai San shi ba shiyasa amintaccen Abban shi yayi yadda zai yi aka tura honorable wajen sannan ya dawo a keke napep..

Magani kuma Ai dama Abban shi ke turowa Wanda ba Na asali bane shiyasa su Baaba ke tunanin baya aiki..

Doctor kuma Ai biyan shi kudi suka yi shiyasa zai zo ya kare sa shirmen shi yayi gaba..

Akwai ranar da aka dawo da shi Auta Na gida har ya jima a toilet text yake yi Na cewa su bi a hankali yan gidan su Fara sa mishi ido..

Duk wani plan da yake yi Na tafiya yadda ya dace sannan Michael Sunday Na Tara mishi evidence Wanda ba Wanda ya San yana mishi aiki sai a jiya..

Shigowar Laylerh gidan sai ta Fara fahimtar shi don ya kan karanta kwayar idon ta kuma ya tabbata tana zargin shi shiyasa yake Dan sake Mata don ya fahimci takun ta hakan yasa ranar da taga ya fice da orange Riga da ya tashi dawa sai ya Yada rigar ya sai sabuwa..

Ranar da ta fito taaje Kai ta ganshi lokacin ma kokarin hawa gini yake, sai kuma jiya da ta ganshi a waje zai je su tattauna da Michael Sunday ta tona mishi asiri..

Tun shigowar ta gidan duk wani nasara tashi ta tsaya Gashi har bindiga ta kalla a kasan gadon shi da makamai Babban Tashin hankalin shi kuma shine text da ta karanta dole ya kusa kashe ta don shekara da shekaru yayi yana hada evidence da zai wanke kan shi a idon duniya ita kuma ta gama sanin inda duk wani evidence da zai kare shi yake shiyasa ma yau Abban shi yazo don su koma tare wannan dalilin yasa yayi tunanin ko wani take Wa aiki sai dai kuma zallar gaskiya ya gani a idon ta Tun Randa ta leka kasan gadon shi ya mare ta nan ma so yake tayi confessing ta fadi Wanda ya turo ta...

Numfashi yaja Bayan ya gama tunani a daidai lokacin kuma Abban shi ya shigo gidan..

Ko da ta fita daga dakin shi duk a rude take don bata yi tunanin zai bar ta da ran ta ba,to shi wani sirri ne yake magana akai Wanda iyayen shi ma basu sani ba,taya mutum zai ajiye bindiga a tare da shi, tana tunanin yayinda ta nufi dakin ta, toilet

ta fada nan ta wanke fuskar ta goshin ta kuma ya Dan tashi inda ya buga ta da gini..

A can falo kuma Alhaji M wakili ne yazo da amintaccen Dan gidan shi inda ba karamin mamaki su Baaba suka yi ba don duk zaton su Dan gidan shine Alhaji wakili ruwa kadai yasha yana fad'in "ina ne dakin shi?" Amintaccen Dan gidan shi ne ya raka shi har kofar dakin sannan ya juya ya koma falo wajen su Baaba, knocking Alhaji M wakili yayi jin shiru sai ya shiga.. A take idon shi ya kawo ruwa ganin yadda d'an nashi ya koma shima Umar Farouq mikewa yayi ya rungume Abban shi yana jin wani Zafi a ran shi..

A bangaren Laylerh ko jin muryar baki a kofar dakin Umar Farouq sai ta leka ganin amintaccen Dan gidan Alhaji M wakili ya juya sannan taga an rufe dakin sai ta nufi lungun dakin shi da sauri sannan ta tsaya don tana son tabbatar da abunda ya fada Mata gaskiya ne

"Umar Farouq kana lafiya". Cikin danne bakin cikin shi yace" lafiya Abba ya Ka baro yan gidan".

"Duk sun yi kewar Ka sannan sun shirya tarbar ka don Na tabbatar musu Ka gama aikin Ka evidence duk suna hannun Ka". Baya ya bawa Abban shi don bai son yaga rauni a idon shi yace

" Abba duk wannan kokarin da kuma nisa da gida da dangi da nayi ya tashi a banza"da sauri Abban shi ya karasa Gare shi yana juyo da shi suka fuskanci juna yace

"ban gane ba duk shekarun da Na dauka ina jiran wannan ranar kace ya tashi a banza".

"Abba Ana suspecting Michael Sunday shiyasa yace nazo Na karbi evidence din shiyasa ma Na sanar da amintaccen Dan gidan Ka ya fada maka Na gama hada komai, to a ranar da Na fita sai yan gidan suka dago bana nan kan Na Karba sun

gano ni,sannan dazun ya tura mini sakon inda ya ajiye sai aka Riga ni karantawa Wanda zuwa yanzu Na San an dauke evidence din".

" fada mini Umar Farouq a ina yake Zan je Na dauko".

"Abba Ka manta Kai ma Ana biye da duk wani motsi naka".

" to Zan tura a dauko".

"Hmm Dan Adam fa ba abun yarda bane don kila Wanda zaka tura da kan shi zai yi destroying evidence Na cewa ban yi kisa ba sannan banda hannu a wancan harkar Ka Bari kawai Zan bayyana Kai Na in yaso a mini duk hukuncin da ya dace".

" ba Zan iya ba Umar Farouq saboda duk Randa bani Kai zaka rike gida Na me kake son nace da kanne Ka da suke tambayar yaushe zaka dawo".

"Dan Allah Abba kaje don komai zai iya faruwa, da kace da ni zaka zo tuni Zan hanaka don Na tabbatar yanzu an San inda nake kaje kawai Ka nema mini wani waje Zan bar nan cikin dare".

" alright "daga haka suka yi hugging Na junan su Abban shi ya fice da wuri suka bar gidan don su badda Sahu gidaje biyar suka shiga a layin..

Sosai taji tausayin Shi sai ta bar wajen..karfe biyar daidai ta fice a gidan ba tare da sanin kowa ba bata tsaya ko ina ba sai bakin kogi nan taga yan iska iri iri wasu Na shan sigari wasu ko Na latsa yaran mutani ga yan talla birjik a wajen yan garuwa Na deban ruwa, duk da hankalin ta ya tashi sai ta yi ta maza ta Fara bin kwatancen da ta karanta a text message din" ke yarinya me zaki yi a can?"

Wani ya tambaye ta lokacin da ta nufi wajen Allah ma ya so ta a Bayan bishiya ne sai tace"fitsari Zan yi".

"To in kinyi kizo" to tace nan ta nufa gami ta tone wajen tana leke leke gudun kada wani yaga fitowar ta daga gidan ta zama suspect Babban envelope ne brown ta cire anyi ta manna shi da gam da Ka gani kasan abu ne Mai mahimmanci nan Tasa a hijab mazan wajen nata Mata iya shege don tsoron kada a Kama ta da kyar kafar ta ke tafiya tana kuma ji a jikin ta Ana bin ta a baya Amma tsoro ya hanata juyawa sai tafiyar dake Neman gagarar ta don jikin ta duk rawa ya dauka tabbas masu Neman ganin Bayan shi ke bin ta..

Gare su reader's shin Laylerh zata Kai wannan evidence kuwa?ko za'a kamata?

Comment

Share

©Hafciey Musa

[1/25, 5:41 AM] Hafciey Musa😘: *□LAYLERH□*

(The prettiest emerald)

27

Tabbas bin ta ake yi shiyasa rawan jikin ta ya sanan ta har fitsari take ji, kafa ta sa gudu take yi tsakanin ta da Allah ta kuma tabbatar da masu bi Mata ma gudun suke yi shiyasa tana shiga gida ta rufe k'ofar da karfi,jikin kofar ta mannu tana Mai sauke ajiyar zuciya, cikin falon ta shiga hankalin ta duk a tashe sai dai ba kowa don haka ta nufi dakin ta tana shirya yadda za'a yi sakon ya shiga hannun shi.. Kira Baaba ta kwala Mata dole ta nufi falo Bayan ta boye a inda ta san ba Mai gani"Wai ina Kika shiga ne Tun dazun ko jira kike Na daura miki girki"Kai ta girgiza don a tsorace take ko tace zata yi magana muryar ta ba zai fito ba jiki Na rawa ta nufi kitchen da yake already tayi miya tuwo ta daura Ana kiran magrib ta sauke ta kwashe, so take ta samu damar kaiwa Umar Farouq nashi ko don ta bashi sakon shi Amma kuma ta San dole za'a dasa ayar tambaya a kan ta wannan dalilin yasa ta bar malam ya Kai mishi..

Bayan tayi magrib bata cire ko hijab din ba ta dauki envelope din Tasa a hijab nata ta nufi hanyar lungun dakin shi..taga wuta a kunne hakan bai dame ta ba don a zaton ta ko yana bacci..

A bangaren shi kuma dole ya zauna cikin shiri tunda har yau Abban shi yazo Gare shi to dole an gane inda yake yanzu ma kwance yake akan gado abun duniya duk sun taru sun mishi yawa wannan shi ake Kira ga koshi ga kwanar yunwa ya gama hada komai a karshe Laylerh ta ruguza rayuwar shi,ceiling yake kallo yana wannan tunanin sannan yayi filo da hannun shi ji yayi Ana Jan glass na window'n shi shiru yayi yana kallon wane ne ta cikin madubin dake facing Na window gefen shi kuma bindiga ne..

A hankali ta tura window da yake ba Mai Kara bane ba Wanda yaji ta shi kuma hannun ta da ya kalla ne ya tabbatar mishi mace ce sannan Ai a gidan su biyu ne Mata daga ita sai Baaba wannan hannun kuma Na yarinya ne.. cigaba da kallon ta yayi yaga me take kokarin yi.. Envelope din ta Fara turawa dakin sai ya fado kan gado gefen shi zata rufe window yace"tsaya"cak ta tsaya jikin ta Na rawa kan yace wani abu ta Riga shi"wallahi ban bude ba kamar yadda Na karanta a text din haka naje Na dauko but akwai matsala saboda an bi ni"da sauri ya tashi daga kwancen da yake yace"an bi Ki fa Kika ce da kin fada mini zaki dauko Zan baki plan Na yadda zaki dauka but yanzu kin jefa rayuwar Ki a hatsari ".jin alamar malam sai tace" ga malam ya nufi dakin Ka".

"Ki bar nan kan ya Gan Ki daki Na a kulle yake ba yadda zai yi ya shiga". Jin kamar lungun malam ya dosa sai zuciyar ta ya Fara bugawa me zata ce mishi take yi a wajen, shima Umar Farouq ya fahimci lungun malam zai je don haka sai yayi jefi da wayar hannun shi a tiles hakan ya janyo hankalin malam nan ya koma tare da tsayawa a kofar Umar Farouq yana knocking ita ko da wuri ta fece a lungun sai ganin ta malam yayi from no where tsaye a kusa da shi" malam lafiya? "

"Naji sauti daga dakin shi ne kila ya Fara haukan shi".

" ba fa shi bane nice a store muje kawai"tafiya suka yi a tare tana waiwayan kofar dakin Umar Farouq har suka fito falo..

A bangaren shi kuma jin sun tafi sai ya rufe window nan ya bude envelope din ba abunda babu Na prove din cewa bashi yayi kisan ba shiyasa da wuri ya Kira Dad nashi "Abba abunda nake gani ba zai yuwu ba ya yuwu Wata yarinya ta dauko mini but an bi ta".

" subhanallah nasan yanzu haka suna kewaye da gidan jira suke yi waje yayi shiru sai abka muku".

"Wallahi Abba Nima abunda Na tuna kenan".

" listen yanzu Ka zama cikin shiri gobe da asuba zaka bar Taraba".

"But Abba batun kewaye gidan da aka yi fa".

" yanzu Zan tura mutani Na su kewaye gidan yadda ba Wanda ya isa shiga"

"Na gode Abba you mean a world to me" katse kiran suka yi kamar yadda suka yi zato kuma gidan kewaye yake da masu Kai mishi hari Amma sai Mai wayo ne zai lura..a take Abban shi yasa mutanin shi suka nufi gidan nan suka kewaye hankalin yan anguwa kuma ba karamin tashi yayi ba don sun tabbatar ba lafiya tunda har da motar police uku..

"Baaba ba ashana fa kuma Kinga ba'a bude shago da safe". Kudi Baaba ta bata tace taje sayo ashana tana fita taga wajen gidan fa ba lafiya ganin mutanin da ba adadi cikin bakin suit ga kuma polisawa sanda ta saki fitsari don a tunanin ta ita aka zo kashewa shiyasa ta juya da gudu wani Na cewa" zo kiyi tafiyar Ki"ina bata ji ba rufe kofar tayi gami da sa sakata a falo ta zube tana haki malam ne ya dube ta yace"lafiya? "

"Malam wallahi gidan nan a kewaye yake da polisawa".

" innalillah ya fadi yana mikewa take duk tsoro ya shige su, wayar shi ce ta Fara ringing yana dubawa yaga M wakili ne"Malam zuwa safiyar gobe Zan dauke yaro Na daga gidan Ku sannan an Kira ni ance yarinya ta fita tana ganin su ta koma da gudu kada kuji komai mutani nane sai dai akwai wasu ma kewaye da gidan Na Ku masu son ganin Bayan Umar Farouq "kan malam yayi magana ya katse kirar kiran shi ya sake yi Amma bai daga ba" wannan shine Tashin hankalin da ba'a sa mishi Rana to ko dai yadikkon shi gano inda yake ne".fadin malam"wallahi wasu ba Allah a zuciyar su"Baaba ta bashi amsa..a Daren ranar dukka yan gidan yadda suka ga rana haka suka ga dare Harda shi Umar Farouq d'in da asuba aka Fara kiran malam yana picking aka ce"Ka bude gate Na gidan Ka yanzu"katse kirar aka yi shi ko Alhaji M wakili ya Kira yana dagawa yace"an Kira ni yanzu ance Na bude gate Na fa".

"Kada Ka damu mutani nane kana budewa Ka matsa a hanya da hanzari don cikin sauri zasu shigo" to yace nan ya nufi gate din Ai yana budewa kadan ya rage su dage shi yadda motoci biyu suka shigo gidan zaka ce tsafi ne from no where yaga wannan Wanda sukewa kallon mahaukaci ya shige mota a take motocin suka juya sai kuma guda daya ya shigo "maza kuzo Ku shiga mu tafi". Da sauri Baaba da Laylerh suka fito nan aka sa su a mota ba tare da an rufe ko gidan ba aka Fara gudu ganin Ehh tabbas an dauke Umar Farouq sai masu Neman ganin Bayan shi suka Fara musayar wuta da mutanin Baban shi nan take ko ina ya rude..basu tsaya ko ina ba sai Adamawa cikin jimeta motar su Na shiga chairman Na local government din ya bada sanarwa cewa kada a bar wata motar ta sake shiga garin sai nan da awa daya a take aka rufe hanya don dama Abban shi ya Kira gomna to gomna ne ya bada wannan sanarwar....

Umar Farouq ko baya cikin convoy da aka dauki su Laylerh har masu Neman ganin Bayan shi suke bi don ya badda Kama ne yana shiga motar ya fita ta dayan kofar nan ya makale a wani wajen har suka Fara musayar wuta sai ya shiga wani mota daban direct airport Na jalingo ya wuce already an tanadar mishi da jet daga nan Abuja ya wuce..sanin a Abuja ma Neman shi ake sai bai tsaya ko ina ba sai headquarter din su Bayan yayi copying Na ko wani evidence zuwa Kashi uku..daya copy ya ajiye wajen Wata aunt din shi a nan Abuja daya ko yana wajen Abban shi Wanda ya rage din ne yanzu ya kawo headquarter knocking yayi aka bashi damar shiga, ba karamin mamaki oga'n su yaji ba ganin shi har sadiya dake zaune gefen oga mikewa tayi ganin yadda gaba daya ya sauya nan taji tausayin shi,shi ko banzan kallo ya bita da shi sannan ya dubi oga'n su yace"Sir ga evidence Na kawo Na cewa bani Na kashe Hashim ba".

"Ai Ka makara Umar Farouq".

" makara kuma"ya tambaya da fuskar confusion "yeah duk wani prove da zaka gabatar da cewa baka da hannu a kisan Sadiya ta Riga Ka" da sauri ya juya yana kallon gefen da Sadiya ke zaune "but Sir..."

"As I told you Sadiya ta wanke Ka daga zargin da duniya ke maka yanzu haka zance muke Na yadda za'a nemo Ka Ka dawo bakin aikin Ka". Kan shi fa ya daure sosai shiyasa yace" but Sir ita ce fa tayi implicating Na".sai yanzu ta bude baki"yeah nice nayi implicating naka uncle Farouq but Ka yarda da ni manufa ta Mai kyau ce,Tun a farko Na San ba Kai Ka kashe Hashim ba abokanayen kasuwanci shi ne inda ya take dukka ribar da suka samu ya Hana su ko sisi shine su kuma suka gwada mishi abunda zasu iya ta hanyar zuwa har gidan shi suka Kashe shi,to dama ya sanar da su cewa tare kuke aiki shiyasa Bayan sun kashe shi sai suka Fara Neman Ka,a Washe garin ranar da aka yi kisa ko da kazo da asuba Na Gan su biye da Kai kenan hakan Na nufin kana fita daga nan zasu kashe Ka shiyasa nayi implicating naka don nasan dole a headquarter za'a ajiye Ka ba zaka fita ba..ganin ba zaka fito ba sai suka bar wajen ni ko sai nayi amfani da wannan damar Na Fara binciko su wane ne suka kashe shi a lokacin Kai kuma Abban Ka ya tura Ka can jalingo cikin anguwar kasuwan yelwa gidan wani malami da yake da yarinya daya da Mata sai Yar aiki..a hankali nake hada hujjoji akan Ka kamar yadda Kai ma kake kokarin hadawa to a jiya Na gabatar da hujjan a court an kuma wanke Ka daga zargin kisan Kai da ake tunanin Kayi yanzu ma zuwa nayi don Na fada mishi address Na gidan da kake a dauko Ka"..tabbas ya San zata iya don a bangaren bincike kam zasu iya zama daya Amma Bayan shi ba Wanda ya Kai ta iya bincike..."Umar Farouq for now anyi declaring cewa baka da laifi but ba zaka dawo bakin aiki ba har sai Mun Kama wadanda suke da hannun a kisa kuma zamu hada Ka da securities da zasu ke kare Ka".

"Thank you Sir" yace yana saluting nashi nan ya fice bai ko kalli inda Sadiya take ba ita ma ta San halin shi Na share mutani shiyasa bata damu ba..a waje ya tarar da securities da aka hada mishi nan suka mishi rakiya zuwa gida..katafaren gida ne Wanda zai ci anguwa biyu suka yi horn dama already Abban shi ya sanar da security zuwan shi shiyasa yana ganin motocin ya wangale gate..daga gate din yake jin sautin wa'azi Na tashi ga yara Na safa amsa marwa shi dai a sanin shi gidan su ba yara sai Na kannen shi,har bakin bangaren shi aka yi parking nan ya fito shigewa ciki yayi ba tare da yace da su komai ba..

A can cikin gidan su kuma waliman dawar shi Anty Hauwa da su Nana suka hada inda mutani dayawa sun halarci waliman..yana cikin cire kaya yaji Ana knocking kofa kuma ya San mutum daya ce don haka sai ya maida rigar shi ya fito falo ya bude Ai ko ita ce"yaya"ta fada tana smiling "Nana ya kuke?" Ya tambaya yana juyawa cikin falon, kowa ya San masu bin juna akwai raini sosai tsakanin su to shi

kam a nasu bangaren ba haka bane don shakuwar dake tsakanin su ko uwa da d'a albarka shiyasa yaran ta ma sun fi jin shi fiye da Baban su dukka rashin hayaniyar shi"ina wajen walima naji ance kun iso shiyasa nazo ".

" yau kuma ina Kika baro yaran naki?"

"Suna cikin gida Na San yanzu kana da bukatar hutu Bari naje" fita tayi ya rufe kofar don in kaga yayi dogon zance to da Abba ne ko ita Allah ne kuma shaida ba Wai ji da Kai ne ke Hana shi magana ba a'a halittan shi ne he is man of few words shiyasa in kun zauna tare sai Ka tsane shi..a hankali ya fara zare kayan dake jikin shi wanka yayi nan ya fito daure da towel a kugun shi,dogon numfashi yaja yana mai shakan daddadan kamshin dake tashi a dakin wanda ya mance when last yaji shi..wordrobe na kayan shi ya bude boxers da jallabiya kawai ya ciro nan ya sanya ya kwanta don yana da bukatar bacci ko ba komai yau ya sauke nauyin dake kan shi.. Bayan ya huta sauran yan uwan shi duk suka shigo mishi sannu da zuwa nan aka Fara jera mishi abinci a dining ko jaki iyakaci don karya ne ya cinye. Suna kaunar shi sosai don gidan basu yan ubanci duk daya suke ganin kan su..

Bayan kwana biyu aka Kama wadanda suka kashe Hashim nan ne aka ce zai iya dawa bakin aikin shi Amma an bashi hutun sati daya...

Bangaren su Laylerh kuma wani gidan Alhaji M wakili aka Kai su inda aka badda Sahu ta hanyar tafiya airport don masu bin su suyi tunanin sun bar garin..gida ne madaidaici kuma yamallaka musu halaq malaq nan ya tura aka musu shefene ba abunda babu yace in har suna da bukatar Komawa jalingo zasu koma Amma sai an Kama mutanin..

Sannu a hankali suka Fara sabawa da zaman gidan inda yanzu kullum malam Na gida tunda bai da aikin yi,da yake in an kauro sabon gida makota kan shigo su muku sannu kuma a San juna to hakan ce ta kasance a bangaren su Baaba makota Na shigowa yanzu ma wata budurwa ce tayi sallama"wa'alaikisalam shigo ".shiga tayi yarinyar ba zata wuce sa'ar Laylerh ba Amma da yake Baaba Mai son jama'a ce wannan ne zuwan ta Na biyu gidan" yan Mata Kice yau ma kin shigo ".

" Ehh Allah yayi".

"To sannu da zuwa ya mutani gidan Ku?"

"Suna lafiya duk sunce a gaishe Ku". Daga nan shiru ne ya biyo baya sai TV da suka kurawa idanu ganin haka sai Baaba tace" Ai akwai sa'ar Ki ma a gidan"nan ta kwala kiran Laylerh a take tazo"ga bakuwa anyi ".

" sannu da zuwa"Laylerh tace da ita cikin fara'a ta amsa daga nan sai suka Fara taba hira sama-sama..ta jima kan tace zata tafi nan ne Laylerh ta dubi Baaba tace"Bari Na raka ta"da Kai ta amsa mata nan suka fice a gidan "Kinga ga nan gidan mu kizo mu shiga sai Ki gaisa da yan gidan". To tace nan suka nufi gidan tana karewa gidan kallo gaban ta kuma Na fadiwa zuciyar ta Na bugawa so take ta koma don ta tabbatar akwai abunda zai faru da ita a gidan Amma kuma ta gagara a haka har suka karasa cikin falon" zauna "zama suka yi tare nan yarinyar ta kawo Mata ruwa tana kuma Mata hira sama-sama Amma ita Laylerh hankalin ta baya wajen don ji take yi kamar zuciyar ta zai fito" Wato ke Zulai kullum in kinyi wanki sai dai a tattara miki Amma ba zaki iya tattarawa ba"Wata babbar mace ta fada duk ido suka daga suna kallon ta nan ne matar ma ta kalli bakuwar da ke tare da wacce aka Kira da zulai baki Na rawa tace"Laylerh "mikewa Laylerh tayi jin yadda matar ta Kira sunan ta tana kuma Mata kallon Sani sai zulai ce wacce ta San yadda suka yi da Muhammad a kwanakin baya tace" Anty Amina ita ma Yar Ki ce?"ga mamakin su sai ta daga musu Kai a nan wajen kuma ta fadi sumemmiya.. Laylerh ko kafa Tasa sai gida inda zulai bata Lura da ita ba yan gidan su taje Kira suzo su ga Anty Amina ta suma..

Tana shiga gida direct falo ta nufa don ita tsam bata gane mahaifiyar ta ta ba a zaton ta kila masu Neman su ne suka hada baki da ita shiyasa tace"Baaba wallahi a gidan su yarinyar da tazo yanzu Wata tace ni Yar ta ce har da suma tayi".

"Shegiya dama ce miki nayi Kije gidan su?yarinya muna zaman mu zaki jaza mana bala'e" rufe bakin Baaba ke da wuya aka Fara buga gate din da karfi ba kowa bane kuma face su Aunty don ta farfado ta kuma tabbatar musu da cewa Laylerh Yar ta ce to ganin yadda Muhammad ya bace Bayan tace ita ce mahaifiyar shi shiyasa suka biyo Laylerh da wuri gudun kada tayi irin nashi..

Malam da ke daki ne ya fito nan Baaba ta fada mishi abunda ke faruwa shima ya rude sai ya Kira Alhaji M wakili ya sanar da shi nan take ya tura mutanin sa sai suka tarar rigimar ta anguwa ce kiran malam yayi yace ya bude kofar Ai makotan su ne kuma sunce Yar da ke gidan shi Na Wata ce a cikin su nan ya bude kofar dukkan su suka shigo har zulai duk a falo suka zauna Aunty sai kallon Laylerh take yi wannan wace irin jarabawa ce ace Dan cikin Ka bai gane Ka ba.gyaran murya malamin dake bawa Aunty magani yayi yace"Alhaji zaka ga Mun zo muna buga maka gida ba kakkautawa Ka gafarce mu bamu yi da Wata manufa ba wannan baiwar Allah ce taga Yar wajen Ka tace Yar ta ce shiyasa muka zo har gida don mu tattauna saboda akwai abunda ya faru cikin rayuwar su Wanda yake nan kamar sihiri gaba daya

ahalin su sun watse Kwanaki taga d'an ta tunda ya karbi magani sau daya bai sake zuwa ba muna dai addu'a".numfashi malam yaja sannan yace"to Ai malam abun ne da daure Kai taya za'a yi daga kallon mutum tace ta San ta".

"Malam wallahi 'ya ta ce labarin mu Nada saho Amma ita yarinyar a tambaye ta ina iyayen ta mana".

" Laylerh ina iyayen Ki?"

"Malam ban San su ba bana iya tuna komai Na rayuwa Na in Na zauna nakan tuna ni din banda iyaye ne?"duk shiru suka yi don maganar Aunty akwai alamar gaskiya tunda ita yarinyar ma bata San Asalin ta ba" ni ba Zan takura sai Na dauke ta ba tunda mu makota ne don Allah Ku mini alfarmar take karban magani kullum ko Allah zai sa a dace tunda Dan uwan ta kam shiru".

"Ba komai Allah shige mana gaba Amma batun gaskiya ban son yawan fita tana karban maganin zata juyo har ranar da Allah zai sa ta gane Ki daga nan sai kiyi iko da Yar ki". Godiya suka mishi nan suka fice Laylerh Na bin Aunty da ido kamar yadda ita ma Aunty'n take bin Laylerh da ido" Ashe dama yarinyar bata da asali muka zauna tare da ita"banza malam yayi Mata Laylerh ko mikewa tayi zuwa daki a ranta take addu'ar Allah sa Aunty mahaifiyar ta ce ko zata huta da halin Baaba..

Daga ranar take zuwa karban magani safe da yamma tana kuma leka Aunty don matar ta shiga ran ta sosai..sati kawai tayi ta iya gane Aunty ranar kam an sha murna don kallon Aunty tayi tace "Aunty" wannan yasa kowa fahimtar ehh ta San ta tunda bata taba kiran ta da wani suna ba sai gidan su zulai ya koma wajen wunin ta a jikin Aunty'n ta...

Abba ne kwance Aunty Hauwa Na mishi massage yace"wallahi Hauwa Na rasa da me Zan sakawa yarinyar can Wanda Tasa rayuwar ta a hatsari wajen ceton Umar Farouq ".

" Ai my dear ban Gan ta ba Amma naji son yarinyar har raina a zamanin yanzu ina zaka samu irin su".

"Shiyasa nake tuna da me Zan saka Mata Ai don kin San Yaron naki kam ko in kula ne".

" Alhaji kaga dai Umar Farouq ba kula Mata yake yi ba asalima bai da lokacin kan shi sai Na aiki bare yace zai nemi Mata kuma kamata yayi ace macen da zai aura Mai hak'uri ce da aikin shi,a nawa shawarar Mai zai Hana a nema mishi auren yarinyar tunda har ta iya sa rayuwar ta a hatsari don dauko abunda zai Cece rayuwar shi kaga zata iya hak'uri da bahagon halin shi".tashi zaune yayi yana kallon ta da mamaki a fuskar shi yace"wallahi ban kawo haka a raina ba gaskiya shawarar Ki tayi Amma kina ganin zai yarda?"

"Ka bar ni da shi Ai ba auren ne baya so ba lokaci ne baida shi kuma Ka San ba zai maka musu ba".

" wallahi ba Zan boye miki ba naji dadin shawarar taki sai dai fa ance yarinyar bata da asali ".

" ance fa kace Ka San maganar yan duniya kada Ka yarda kawai kasa a bincika maka Amma kafun nan Ka Fara nema mishi auren yarinyar ".waya ya dauka a side drower yana fadin" Bari ma Kiga Na Kira malam din nan ya Fara dialing number'n malam,

Wayar malam ke ringing yana ganin M wakili ne ya daga da sauri "Na San zaka yi mamakin ganin Kira Na ko?"

"Aiko kamar Ka sani Alhaji don Mun Fara shirin Komawa Taraba don Auta Na"

"Malam a gaskiya Na yaba da yadda Ka rike mini d'a kwarai da gaske sannan zance nake so muyi akan yarinyar dake wajen Ka in ba matsala so nake Umar Farouq ya shiga tsahun maneman auren ta".

shiru malam yayi sai Alhaji yace"baka ji nane"numfashi yaja

"naji duk abunda Ka fada Alhaji Amma a halin yanzu banda hakkin bada ita don ba ya ta bace mamar tace zata bada ta tunda ba maza sai dai Alhaji Farouq da ba hankali ne da shi ba kake son mishi Aure".

"Malam Umar Farouq Nada cikekken hankali" nan ya bashi labarin komai tare da bashi hakurin boye musu gaskiya da aka yi sai yace"to ba komai in sha Allah Zan samu Maman ta muyi magana duk yadda ake ciki zaka ji".

"To don Allah kada ya dau lokaci".

" in sha Allah kace da shi Na jinjina mishi ya iya acting "dariya kawai Alhaji yayi sai kuma suka yi jugum suna jiran amsar shi..

A ranar kuma ya fada ma Aunty komai nan tace ba matsala tunda har sun rike Laylerh tsakani da Allah yana iya aurar da ita tunda bata da Dan uwa Na miji..a take ya Kira Alhaji ya sanar mishi zo kaga murna wajen bayin Allah Wato Alhaji da Aunty Hauwa..

Zaune yake a falon shi agencies Na headquarters nasu ne suka zo mishi murnar mayar mishi da aiki ciki kuma Harda Sadiya an cike musu gaba da Kayan dadi shi ko sanye yake cikin kananan kaya ya daura kafa daya kan daya laptop a cinyar shi sannan yana supping coffee.. Dama sun sa ayi musu iso da Alhaji don shima suyi congratulating nashi yanzu haka ma zaman jiran shi suke don Umar Farouq ganin Sadiya a wajen sai ya murtuke fuska" dude Wai ya aka yi haka ne?"

"Is a girl....." Shigowar Abban shi ya katse shi duk zubewa kasa suka yi suna gaishe shi Bayan sun gama sai ya dubi Umar Farouq yace"congratulations Na nema maka auren yarinyar da kake zancen ta yanzu kuma iyayen ta sun amince so aiki ya rage naka Ka samu shiga zuciyar ta".idanu ya lumshe ya kuma bude su akan Abban shi so yake yayi magana amma kuma ba zai iya mishi musu ba shi sai yake ganin da an nemi shawarar shi kan a nema mishi auren ta wannan yarinya Mai rawar Kai tsam ba nitsuwa a tare da ita ina zai Kai ta Gata yarinya karama me zai samu a jikin ta"idon shi ya sauke kan Sadiya wacce dama Danna iPad nata take yi bata bi ta kan ko wannen su ba jin zancen Alhaji kamar saukar aradu ne shiyasa a take ta sake iPad nata a kasa sannan ta mike jikin ta duk ya dau rawa murmushi take son yi Amma har naman fuskar ta rawa yake yi dukkan su wannan abun ya basu mamaki don ba Wanda ya taba ganin raunin ta Umar Farouq ko karantar ta yake yi a zuciyar shi yace"I knew it dama Ai ba yadda za'a yi ace Sadiya ta taimake ni don Allah ".

Comment

Share

©Hafciey Musa

[1/25, 5:41 AM] Hafciey Musa😘: *LAYLERH*

(The prettiest emerald)

28

Fahimtar duk hankalin su akan ta yake sun zuba Mata ido sai tace"excuse me"sannan tayi gyaran murya ta fice da gudu.. securities nata suka rufa Mata baya"Ku shiga dayan motar ina son kasancewa ni daya"wannan dabi'ar ta ce in tana cikin bacin rai da kanta take tuki shiyasa basu Mata musu ba shiga motar tayi ta fige shi at 360 kace kashe kan ta zata yi,driving take yi zuciyar ta Na tafasa a haka ta isa gida horn tayi gate man ya bude ko gama parking bata yi ba ta fito.. power bike(machine) ta dauka nan ta Fara zaga duk wani street dake cikin Abuja don hakan Na rage Mata bacin rai,tafi awa daya tana abu daya jin ta Dan samu nitsuwa sai ta nufo gida yan aikin ta ne kadai a falo direct bedroom ta nufa toilet ta shige wanka tayi sai Tasa gown Mara nauyi da yake kyakyawa ce ajin karshe ko rough dress tayi to sai tayi kyau. Dakin daughter'n ta ta leka taga tana bacci sai ta nufo falo tana taku cikin kasaita hannun ta rike da cup of coffee tana sipping a hankali daya kuma wayar ta take dannawa..

So take ta karyata hancin ta Amma ta Gaza don tabbas kamshin Umar Farouq take ji a gidan shiyasa ta daga idon ta illa kuwa Ganin shi tayi zaune akan hujera ya daura kafar shi daya kan daya sosai tayi mamakin ganin shi a gidan ta abunda bai taba yi ba kenan

"me ya kawo Ka gida Na sannan waya baka izinin shiga ?"

hankalin shi akan wayar shi yace" me ya kawo ni gidan Ki ko waya bani izini duk ban da lokacin amsa miki tambaya ce ta kawo ni".

"Ehem ina jin Ka". Banza ya Mata har ta cire ran zai amsa yace" kin Hana securities bin Ki sannan kin dauki power bike kina zaga street Na Abuja Wanda hakan Na nuna kina cikin damuwa shin me ne ne matsalar Ki?"zama tayi a kujerar dake kallon na shi"har yaushe Ka Fara damuwa da damuwar wasu?"

"Look ba Wai forcing naki nake yi ba gani nayi kinyi saving Na ko ba komai ya kamata naji damuwar Ki".

" bata shafe Ka ba".

"Really?" Ya tambaya yana kallon ta da mayatattuun idanun shi"ko Na fada maka Na San ba abunda zaka iya".

"Feel free Ki fada mini in har bai fi karfi Na ba Zan miki"

"Umar Farouq so nake Ka Aure ni don ina son ka".

" what? "Ya tambaya yana tabe fuska kamar yaga abun kyama" yeah ina matukar son Ka Tun ba yau ba".mikewa yayi sannan yayi taku biyu tare da juya Mata baya yace"Hashim Nada hatsari haka ma mutanin da yake aiki da su suna da hatsari Amma ko kadan basu Kai ki ba Sadiya so I can't marry you ".mikewa ita ma tayi tana fad'in" wallahi ba haka bane kace dai don ni bazawara ce ina da yarinya shiyasa Amma ba don haka ba Kai ma kasan ni test Na macen da kake so ne Ka kalle ni daga sama har kasa ba abunda zaka ce bai yi ba don wallahi yarinyar da zaka aura din ma kasan karya ne kace tafi ni kyau,sannan in don halaccin da ta maka ne kaji kana son ta har Ka tura a nema maka auren ta nawa halaccin yafi nata tunda kan Ka kawo abunda ta dauko maka Na Riga Na wanke Ka a idon duniya meyasa ni ba zaka mini halaccin ba".

"Matsalar Ki kenan ba kyau fahimta" ya fadi yana nuna ta da yatsa sannan ya cigaba "Sadiya ni nasan dole bakin Ki daya da mutanin da suka kashe Hashim ko kuma ke ma kina irin business din".

" Haba Umar Farouq Ka kyautata mini zato Kai shaida ne komai Zan yi a duniyar nan ina sanar da Kai hatta kisan Kai da nayi Na sanar maka mind you ni NIA ce ba Zan taba cin amanar kasa ta ba".

"Ai nasan ba zaki taba yin abu tsakani da Allah ba kin taimake ni don son zuciyar Ki ita kuma wancan da kike kushewa don Allah tayi". Kamar zata yi kuka cike da mamakin abunda bai taba yi ba tace"Umar Farouq a gaba Na kake yaba Wata mace,macen ma wacce zaka iya haifan ta".ta sani wajen aikin su akwai Mata dayawa kuma yana aiki da su Amma bai taba nuna su din Mata bane don duk kallon maza yake musu Bayan aiki ba ruwan shi da kowa,wani lokacin ta kan yi tunanin ko baida lafiya ne ma

"Kinga so nake Ki binne wannan maganar da muka yi a nan ya zama kamar ba'a taba irin shi ba". Shiru tayi na wani lokaci sai kuma tace" Shikenan Dan Allah Ka manta da maganar Kai ma"tsarai yasan Sadiya yanzu zata canza salon takun ta ne Amma tunda ta Fara wannan maganar to fa ba zata Bari ba shiyasa ya Mata kallon gargadi sannan ya fice a gidan..

Laylerh ce zaune a gaban malam bisa kiran da ya Mata gefe kuma Baaba ce"Laylerh naji dadin abunda Kika yi kwarai da gaske, wannan bawan Allah Umar Farouq Na zaune da mu Na wasu shekaru Amma bamu taba kawo cewa shi ba mahaukaci bane sai ke da baki dad'e da zuwa bane Kika Fara zargin shi har Kika gano da hankalin shi to Na yaba miki sosai,taimakon shi da Kika yi ta hanyar sadaukar da rayuwar Ki ya tusa son Ki a ran ahalin shi har ma suka yi kwadayin Ki zama daya daga cikin su..a halin yanzu dai Na gama magana da su inda suka nemi Umar Farouq ya shiga tsahun maneman Ki Na kuma bashi dama "

tunda taji batun Aure zuciyar ta ya tsinke sannan auren ma da wannan mahaukaci gaskiya ba zai yuwu ba zuciya ne da shi kamar kuturu Wata Rana in ta bata mishi rai kashe ta zai yi, sannan duk ba wannan ba ita zuciyar ta Na Naseer ne kadai yaushe ma ya rasu da suke kokarin cusa Mata wani Na mijin ita fa har ta koma ga Allah bata jin zata iya son wani Bayan Naseer

" Laylerh kin yi shiru shin kina so ne?"ita fa Allah ya sani ba ko digon son shi a zuciyar ta taimako kuma don Allah tayi don haka ba zata ce Ehh ba,yo kuma taya

zata Fara cewa a'a tunda malam ya bashi dama, mutumin da ya gama Mata komai a rayuwa in tayi haka bata mishi adalci ba shiyasa tayi shiru bata ce Ehh ba kuma bata ce A'a ba

"to alhamdulillah mu a al'adar malam bahaushe in yarinya tayi shiru tana so ne tashi Kije Allah miki albarka ".da kyar ta iya mikewa dakin ta ta nufa a katifa ta fada tare da Daukan hoton Naseer ta fashe da kuka Mai cin rai" ba Zan iya ba Allah ma ya sani"ta fadi tana kukan rashin Naseer ita tsoro ma Umar Farouq ke bata in har zai iya pretending cewa shi mahaukaci ne waya San gaba me zai iya yi jin zuciyar ta yayi nauyi kamar dutse aka sa Mata a ciki sai ta dauki hijab nata a falo ta tarar da su"malam Bari Na shiga wajen Aunty Na"a dawo lafiya ya Mata nan ta fice a daki ta tarar da Aunty'n ta tana Nade kaya da gudu ta fada jikin ta ta fashe da kuka"wallahi aunty bana son shi tsoro yake bani ni duk duniya Naseer kadai nake so".petting Bayan ta Aunty'n ta ke yi jin ta tsagaita da kukan sai ta dube ta tace"Laylerh Aure shine mutuncin 'ya mace sannan ke kan Ki shaida ce bamu da Gata dukkan mu a karkashin wasu muke so kike Ki kare rayuwar Ki a bautan gidan wasu? bawan Allah'n nan su suka ce suna so kuma Nima Na amince musu don haka Ki roki Allah abunda yafi alkhairi ko so kike duk lokacin da muka iya tuna gida mu koma Sani ya Aure Ki nan kuma Ki kare rayuwar Ki a bautan yaran shi?"da sauri ta girgiza Kai"to Naseer dai kince mini ya rasu kuma ina mishi addu'a don shine mutum Na farko da ya Cece Ki har yaushe zaki zauna da son shi ko dai ba zaki yi Aure bane?"nan ma Kai ta girgiza "kin tuna lokacin da kike yarinya in nace miki a birni zaki yi Aure sai kiyi ta jin dadi to ga lokacin yazo" yanzu kam dariya tayi tana rufe fuska don kalaman Maman ta sun faranta Mata kuma Ai tayi gaskiya da tace basu da komai basu da kowa sai Allah Amma a haka suka ce zasu aura Mata d'an su to a shirye take da ta Aure shi duk da ta San zaman ba zai musu dadi ba don ya Riga yasa tsoron shi a ranta kuma ba zata taba son shi ba".ringing Na wayar Aunty ne ya katse Mata tunani dole ta mike tare da dauko Mata wayar sai tace"Kinga surkin Ki ke Kira".

"Allah Aunty hausawa basu da kunya Wai uba ke nemawa Dan shi Aure" dakuwa Aunty ta Mata lokacin da tayi receiving wayar Laylerh ko cigaba da Nade Kayan tayi"Assalamu Alaikum "Aunty ta fadi cike da kunya" wa'alaikisalam Hajiya an wuni lafiya ".

" lafiya kalau".

"Na San zaki yi mamakin ganin Kira Na to ba komai yasa Na Kira Ki ba sai don malam ya sanar da ni shi fa zai koma Taraba ko don kasuwanci shine nace ita

yarinyar ya za'a yi da ita tunda naga ke ma a karkashin wasu kike ba zai yuwu Ki kara musu nauyi ba"

"Wallahi Nima tunanin da nake kenan".

" to alhamdulillah yanzu so nake Ki barta ta koma da su tunda yanzu an gane juna zata kuma ke kawo miki ziyara,a gaskiya ba Zan boye miki ba ni a zuri'a Na banda bukatar mace tayi ilimi Mai zurfi shiyasa yara Na Mata iya diploma nake aurar da su to haka ita ma Laylerh diploma kadai zata yi sannan ko ta shigo ba batun aiki Zan ke biyan ta salary da duk Wata mace mai aiki take Karba tunda dama don kudi ake sana'ar in tayi diploma kuma tafi karfin a Kira ta da jahila so nake ta zama complete house wife yadda zata kula da mijin ta sosai ".

" to ba komai Zan yi shawara Na gani".

"Sannan batun makarantar in ta koma can zanyi sponsoring nata har sai ta gama diploma zasu yi Aure don auren ba yanzu bane sannan batun yayan ta kuma nasa an Fara Neman shi da kuma addu'a in sha Allah ba jimawa za'a gane shi".

" Alhaji godiya muke ".

" ba komai malam yace nan da kwana uku zasu koma don haka Zan turawa yarinyar sako".

"Godiya muke Allah Kara girma" Ameen yace nan suka yi sallama..

"My dear baka kyauta mana fa akan me zaka yi ta shirin mana Aure ba'a tambayi yadda muke so ba" Aunty Hauwa dake zaune a gefen shi ta fada"d'an naki ne ba Wanda ya isa gane halin shi ba gwara ni uban shi nayi yadda ya dace ba".

"A'a yanzu fa zamani ya Waye Ka bar shi ya nemi so a wajen yarinya sai su tsara yadda komai zai kasance tunda in anyi auren ba Kai zaka zauna da ita ba".

" to Kinga yana da lokaci ne ni tausayin ta ma nake ji don yanayin aikin shi ba zama yake yi ba kuma ba kullum zai ke tafiya da ita ba".

"In auren yazo duk lokacin da ba zai tafi da ita ba sai ya kawo ta nan gidan ta zauna in ya dawo sai ta koma gidan ta".

" gaskiya shawarar tayi Allah dai ya nuna mana rai da lafiya baka ga yadda kannen shi ke shiri ba zaka ce auren wani sati ne ".

" ba dole ba yaya babba zai yi Aure naso ace Maryam Na Raye taga Umar Farouq nata da Mata".duk yanayin su ne ya sauya tuno ta sai Aunty Hauwa tace"Allah jikan ta ya Kai haske kabarin ta"Ameen suka ce a tare..

A bangaren Laylerh ko taji duk abunda yace sai dai bata jin zata iya yarda ita da take burin yin karatu ace iya diploma zata tsaya sannan ba zata yi aiki ba wannan wani irin gida ne sai kace ta sarauta"Aunty wallahi sun fiya zagewa dayawa bafa sadaqa aka basu ba da zasu juya rayuwa ta yadda suke so in ya Hana yaran shi Mata karatu Mai zurfi a gidan shi a gidan mazajen su kam Ai suna yi ni kuma Shikenan sai Na tashi a tutar babu Allah ya bayyanar da Ya Muhammad Na,Na San ba zai taba yarda ba".

"Nima dai abun bai mini ba shiyasa nace sai nayi shawara Amma kuma yana da gaskiya wani lokacin in mace tayi ilimi Mai zurfi sai Kiga ta raina kowa tana jin kan ta kamar Na miji".

" Amma Aunty rashin gaskiyar shi tafi gaskiyar shi yawa".

"Kinga daina fad'in haka tashi Kije Ki daura musu girki kada ace Na rike Ki sannan batun Komawa Ki shirya tare zaku koma Kinga Nima a nan karkashin wasu nake".

" to Shikenan "daga haka ta mike tace sai ta shigo gobe gida ta koma ita fa tunda Umar Farouq ya koma ta rasa ganewa Baaba don yanzu ta daina Mata wasu halin ko fada da take Mata ta daina ko don ta gane ita din me asali ce oho...

Girki take Amma gaba daya tunanin rayuwar ta Na baya da Naseer take yi Musamman inda ya tayata saida masa bata taba kawo mishi mutuwa nan kusa ba tayi burin ta kare rayuwar ta da shi shiyasa cikin sanyi take girkin har ta gama..

shirye-shiryen Komawa Taraba suka Fara inda yanzu da Aunty take wuni tayi ta Mata shagwaba" Laylerh Ki rake shagwaba fa ba ko wani Na miji bane yake so".

"Aunty ni dai kizo mu tafi tare".

" a'a Kinga ina rufawa kaina asiri a nan da kudin covid 19 da Na samu kuje kawai kuma Ai ke Kika ce mini suna da kirki in sha Allah Zan zo".

"Amma Dan Allah duk Randa aka gane ya Muhammad Ki fada mini in sha Allah Zan nemi kudin mota nazo".

" kada Ki ji komai ".

Bayan kwana biyu

Iyalan Alhaji M wakili ne zaune a falon da Aunty Hauwa Umar Farouq ne da Abba sai Salman sune basu wajen Amma Mata shida din duk suna nan da Aunty Hauwa bakwai,Nana ce rike da pen and pepper da alama list suke yi hajara ce Yar Aunty Hauwa tace" Aunty Nana Ki Kara Mata gowns din sunyi kadan".

"Eh kisa Mata goma" Cewar Yasmeen wacce uwar su daya da Umar Farouq

"kunga naga alama duk shirme kuke yi Ku bani Na Mata list din da Kai Na jibi fa zasu koma don a tura Mata Kayan da wuri" Cewar Aunty Hauwa wacce ke rike da last born Na Nana tana Mata wasa"Kinga Aunty ke fa bai kamata Ki ke shiga tsabgar nan ba ke surkuwa ce Ki bar mu muyi yadda muke so da amaryar mu".ba komai suke yi ba face list Na Kayan da za'a turawa Laylerh tunda zata Fara zuwa school Babban akwati suka saya sai wayar da aka saya Mata Samsung yanzu sun gama sa komai Na bukata gowns ne ya rage ko da suka zo inner wears sun sa ne kawai don Umar Farouq kam baida lokacin su bare lokacin hada Mata kaya shiyasa suke abun su ba Wanda ke mishi magana.. Allah ya sani basu San Laylerh ba Amma suna jin ta a jinin su don taimakon yayan su da tayi nan dai suka Mata order'n gowns guda goma dama sun yiwa driver magana shiyasa aka Kai Tasha daga nan aka wuce da shi Adamawa..

A ranar da su Aunty suka ga Kayan sunyi murna sosai har Baaba nan Aunty da malam suka yi godiya ita ko Laylerh mamaki take Wai yau ita ce da wannan Kayan dukka to ina zata Kai su tunda sun fi set Ashirin ba abunda ya Mata dadi irin wayar Gashi har Sim sun sa Mata sannan kuma ko wacce tayi saving line nata cikin wayar..

Ranar da suka tafi da kyar Laylerh ta rabu da Aunty don gani take kamar zasu sake rabuwa ne da yake Taraba da Adamawa ba nisa kan azahar sun iso nan suka hadu suka tattare ko ina tare...

A can Adamawa kuma yau da tafiyar su Laylerh kwana biyu kenan kuma kullum sai ta kira Aunty,a ranar da suka tafi a ranar Alhaji M wakili ya mallakawa Aunty gidan da suka tashi a ciki don malam yace zai sa haya sai yace to zai saya nan ya mishi transfer'n kudin gidan sannan ya bawa Aunty godiya kam tayi nan ta dauki zulai suka koma gidan da zama..

Yanzu haka zaune take a falo zulai ta tafi makaranta taji Ana buga gate mikewa tayi tana budewa taga Wanda bata yi zato ba Wato Muhammad,murmushi ya Mata nan ta bashi hanya shi da Abokin shi Sirajo suka shigo a falo suka zauna ruwa ta gabatar musu sai Sirajo yace"Aunty Ki gafarce mu Na bace miki da muka yi Mun yi hakan ne ba don komai ba sai don bamu yarda da abunda Kika ce ba shiyasa bamu sake zuwa karban magani ba Amma kuma yana shan Na wajen shi,to yanzu haka ya tuna komai nashi muna shirin dawa Gare Ki kenan muka ji wani bawan Allah yana Neman mu Ashe so yake ya hada mu"

"Alhamdulillah yanzu Muhammad Ka gane ni?"

"Kwarai Aunty ina Laylerh?"Dan Jim tayi sai tace" tana Taraba Ku sha ruwa mana".ruwa suka sha suka huta nan ne ta bashi labarin inda Laylerh ta tsinci kanta sosai suka ji tausayin su sai yace"Aunty Na gama shirin komai Na tafiya Maiduguri zanje Na dauko takardun mu Nida Laylerh da naso Na wuce sai naga ya dace Na nemi sa albarkar Ki".

"Muhammad ba Zan taba Bari kaje garin can ba don nasan hallaka Ka Bappan Ku zai yi".

" kwantar da hankalin Ki Aunty Na bincika baya Maiduguri zanje har Na dawo ba tare da sanin shi ba yanzu in Na zauna ya zamu yi muci gaba da karatu tunda ba takardun mu"ita bata taba kawo haka ran ta ba da kyar suka shawo kanta ta yarda Bayan Sirajo ya sa mishi baki..bayan dawar shi da kwana biyu ya nufi Maiduguri har cikin kauyen su da yake basu jima da barin gida sosai ba sai kauyen bai wani canza mishi ba Amma ya badda Kama don bai son kowa ya gane shi gidan su ya nufa da gani kuma an sayar, sallama yayi ya ko yi sa'a maigidan ne ya fito hannu ya mika mishi yana fad'in "Assalamu Alaikum".

" wa'alaikasalam ".

" Dan Allah ko Kaine Mai gidan nan?"

"Eh nine".

" alhamdulillah dama alfarma nazo nema Ka mini uziri na shiga gidan Ka akwai abunda Zan dauka".

"Haba malam ban San daga ina kake ba haka kawai Zan bar Ka Ka shiga gida Na".

" gidan namu ne sai muka kaura".

"Amma Ai ba a hannun Ka Na saya ba". Ba yadda Muhammad bai yi da shi ba Amma yaki barin shi Dole ya tafi ya kwana a masallaci Washe gari ya sake dawa nan ma Mai gidan yaki yarda a ranar Na ukun ne yace" Dan Allah malam Ka mini rai wallahi daga wani gari Na tashi nazo har nan sannan in kana tunanin wani abu Zan dauka ko Na ajiye a idon Ka zanyi komai kuma in nayi abunda bai dace ba Ka mini duk hukuncin da kaga dama"da wannan batun ya bar shi ya shiga gidan direct store suka wuce akwai wani safe da ya tsufa zaka ce baida amfani ba yadda basu yi ba don su bude suka gagara shi ko kasan ya Danna sai ya budu nan ne suka tabbatar ehh ya San gidan..

Takardun su shi da Laylerh ya dauka da kuma takardun wasu fili Wanda su kan su basu San da shi ba don Abbu ne ke ajiya a wajen ciki kuma Harda takardan gidan nan Mai gidan ya dauki takardar gidan saboda ya saya sai Muhammad yace"Dan darajar Allah da manzon shi ko Wanda ya sayar maka da gidan nan yazo Wata Rana kada kuce mishi wani yazo ya dauki wani abu".

"Ko meyasa?"

"Da Allah da manzon shi fa Na hada Ku kuma Ai tunda kuka ga suna Na a jikin takardun kun San nawa ne".

" Shikenan in sha Allah ba zamu fada ba ko don takardar gidan da Ka bamu"daga nan godiya ya musu ya tafi..

Tun daga ranar da ya tafi Aunty bata sake bacci ba don fargaban abunda zai je ya biyo shiyasa kullum cikin addu'a take Gashi bata fadawa Laylerh ba har ta fahimci akwai matsala ko da ta tambaya sai tace Mata bata jin dadi nan ta tada hankalin ta tace zata zo sai tace taji sauki ba don ta yarda ba ta hakura Amma kullum cikin Kira take yi..

Sai ranar da ya dawo hankalin ta ya kwanta murna iya murna tayi a take kuma ya Fara cuku cukun neman makaranta da kudin da ya Dan Tara ita ma ta tallafa mishi sai takardun Laylerh da za'a tura Mata..

A bangaren su Laylerh ko tunda suka koma gidan sai ya zama kamar farkon zuwan ta Baaba Na sake Mata har su zauna hira yanzu ma ta gama shiri saf zata gidan Dadda don yau Sunday ta San Nabeela Na gida a dawo lafiya Baaba ta Mata duk da ta Gan ta da Leda sai bata tambayi mene ne a ciki ba...

Sosai fa Laylerh ta canza cikin abunda bai fi sati ba har kofar gidan Dadda keke ya ajiye ta nan ta biya shi ta nufi zauren gidan,koda ta shiga gidan yara ne suke wasa a tsakar gidan suna ganin ta suka Fara fadin "ga Laylerh tazo Ku zo Ku Gan ta". Ita dai murmushi tayi sai Nabeela ce ta fito da gudu tana ganin Laylerh taja birki tana Kallon ta daga sama har kasa" sweetheart ke ce?"murmushi Laylerh tayi tare da bude Mata hannun nan suka rungume juna hannun ta Nabeela ta Kama suka nufi bangaren Dadda "Dadda Kinga Laylerh tazo" kallon ta Dadda tayi lokacin da take zama tace"ita ce ta canza haka?"

"Eh" daidai nan Ummi da ta fito daga bayi taga Laylerh "Wa nake gani kamar Laylerh?" Murmushi tayi tace"Ummi nice"nan Ummi ta zauna tana Washe baki kun San ta da gulma tace"duk wannan dawainiyar Baaba ce ke miki".a'a tace nan ta basu labarin komai cikin tsananin farin ciki Nabeela tace"Amma Na miki murna Mrs Farouq "Ummi ko matsowa tayi tana gyara zama tace" duk wannan hidimar uban Yaron ke yi da ke?"Kai ta daga nan ta turawa Nabeela ledar gaban ta tace ga tsaraba, gowns uku da ta sa da under wear's sai turare sauran yan matan gidan kuma Harda mutumiyar ta Maryam Dan kunne ta kawo musu godiya sosai Nabeela tayi nan Ummi ta kwace daya Wai zata kaiwa Yar ta Zainab ta kawo ma Dadda ma sabulu da omo don saya tayi da kudin da Aunty ta bata nan ta Kira Aunty ta hada su a waya suka gaisa sai godiya take musu..ranar wuni tayi a gidan sai yamma Nabeela ta raka ta ta hau machine..

Ai a ranar ko da Ummi ta koma gidan ta sai ta ringa sanar da makotan ta Ai Laylerh Mai kudi zata aura kuma dole suci arziki tare a Washe gari taje gidan Baaba Wai tazo daukar Laylerh ai amanar ta ce ita Dada ta bawa kuma dama Ai ba kyauta ta basu ba jinya tazo yi nan Baaba tace bata San da zance ba sosai ran Ummi ya baci Wato Baaba ma taga arziki ta Hana yarinya ko da zata fita a gidan sai tace"Ki jira sammanci kotu Zan Kai Ki".tana gama fadin haka ta fice

Ita Laylerh abun mamaki ma ya bata Wai yau akan ta ake fada ita da bata da Gata har wani kotu za'a shiga..

We no dey carry last ai😂ga update nayi

Comment

Share

©Hafciey Musa

[1/25, 5:41 AM] Hafciey Musa😘: *□LAYLERH□*

(The prettiest emerald)

29

Ummi fa ta dage kan batun ta Na Kai su Baaba kotu don bata ga dalilin da zai sa su rike Laylerh ba tunda ita ta basu sannan yanzu suce basu mayar Mata ba,yanzu haka zaune take kusa da mijin ta yana cin abinci tana mishi fifita

"Alhaji wallahi ba Zan bar mutanin nan ba daga basu Aron yarinya Shikenan sai suce ba zasu bani ita ba kasan fa Kayan amana ko Kuda ba'a so ya taba ya Dada zata ji in nace Na bar Laylerh hannun wasu?"

"Gaskiya basu kyauta ba Amma yanzu ke ya kike so ayi?"

"Yauwa Alhaji kotu kawai zamu Kai su".

" a'a kin San zancen Ku Na Mata ba tabbas Ki Bari ni Zan sami Mai gidan nata sai mu tattauna nasan zai fahimce ni".

"To Ai Shikenan tunda haka kace". A bangaren Baaba ma hakan ce ta kasance Bayan malam ya gama cin abincin shi a waje ya shigo gida sai tace" malam Nifa abun magana ne ban fiya so ba,tunda har Hauwa tace a bata yarinya Mai zai Hana Ka bata kawai kowa ya huta".

"Yarinyar nan Ince a hannun uwar ta Na dauko ta ban fa son kananan zancen Ku Na Mata".

" cewa fa tayi zasu Kai mu kotu".tsaki yayi sannan yace"Bari gobe in sha Allah zanje Na samu mijin ta da wani Mai fada a ji a anguwan su".

"Gaskiya hakan shine daidai Allah Kai mu goben". Ameen yace..

Laylerh Na can dakin ta tana kwance rungume da hoton Naseer a kirjin ta tuni ta tafi duniyar tunani tsam ba son auren Umar Farouq take ba, ba shi din ne kadai bata so ba a'a auren ne gaba daya yanzu bata sa mishi Rana ba Gashi ita sharudan da Alhaji M wakili ya shimfida tsam bai Mata ba sai dai can kasan zuciyar ta take jin gwara tayi auren don shine gatar ta.juyawa daya bangaren hannun ta ta kwanta tare da Jan dogon rigar jikin ta ya sauka kasa ta rufe kafar ta da shi tana kuma tunanin sai yaushe zasu koma ga ahalin su Na asali da wannan tunanin bacci ya dauke ta hoton Naseer Na kirjin ta..

Washe gari da safe kan Malam ya nufi gidan Hauwa sai ga Mai gidan ta yazo yana sallama

" malam Ana sallama a kofar gida".

"Je Ki Kice gani nan zuwa" to tace sannan ta nufi gate din tana budewa taga Alhaji ne sunkuyawa tayi ta gaishe shi nan ya amsa cikin Fara'a ita ko ciki ta koma ba jimawa sai ga Malam ya fito,hannu ya bashi suka gaisa "Amma ban shaida Ka ba".

" ni Mai gidan Hauwa ce wacce ta Baku rikon Laylerh ".

" Allah sarki to shigo daga ciki mana"tare suka shiga inda malam ya shimfida musu darduma a tsakar gidan"Alhaji ya gida da iyalai dai".

"Duk suna lafiya dama nazo kan batun Laylerh ne,malam Ka San girman amana ko to ita din amana ce ga Hauwa sannan ta arawa mai dakin Ka ita saboda jinyar da take, to yanzu kuma tace tana da bukatar yarinya Mai dakin Ka tace bata San da zancen ba".

" Malam kasan sha'anin mata sai a hankali Na yarda matar kace ta Ara Mata Laylerh Amma kuma ina son Na sanar da Kai abunda baka sani ba,Laylerh ta hadu da mahaifiyar ta kuma ita ce ta bani rikon ta har ma an Mata miji yanzu zata yi karatu Na shekara biyu daga nan sai a Mata Aure"shiru mijin Hauwa yayi don shi tsam bata fada mishi wannan batun ba"to duk da haka dai ya kamata yarinya ta koma wajen ta in ba dai ita ce tace tafi son zaman nan ba".

"To Shikenan Bari a Kira maka yarinyar sai kaji ta bakin ta Na kuma maka alkawarin in har tace zata tafi tare da Kai ba Zan hanata ba" kiran Laylerh ya Fara saboda ya San irin wannan lokacin tana kitchen kuma dole zata ji shi wanke hannun ta tayi sanin yana tare da bako sai ta Kunce Vail Na kanta ta yafa ta nufi inda suke tare da durkusawa tace"malam gani".

"Laylerh nasan kin shaida shi to yace yazo ne domin Ku tafi tare yanzu zabi ya rage naki shin zaki zauna tare da mu ne ko zaki bi shi?" Shiru tayi tana nazari don a gaskiyar zance bata fiya son zaman gidan Baaba ba don in Auta Na nan bata jin dadin halin da take nuna Mata, gidan Ummi kuma ga Zainab sannan kowa Na kaunar ta aiki ne dai take cin uban ta da shi kuma Ai tana samun lokacin hutu to in ta koma gidan kishiyar Ummi ta kashe ta ko ta illata ta ya zata yi,sannan kuma Ai barin gidan Baaba Na nufin barin karatun ta tunda a nan aka ce ta zauna "Zan zauna a nan" tace ba don tana so ba sai don karatun ta don ta San yanzu dai duk tsiya Auta ta kusa dawa hutu Gashi dole zata Dade."Alhamdulillah to Alhaji Ka dai ji me tace ko,Laylerh tashi Kije Allah miki albarka"Ameen tace sannan ta mike ta koma ciki,hannu Alhaji ya Mikawa malam yace"tunda ita yarinyar ce ta zaba Mun hakura Zan yiwa Mai daki Na bayani Allah sa hakan shine mafi alkhairi ".Ameen malam yace nan ya raka shi har kofar gida..

Koda ya koma gida sai yace" Kinga yarinyar ce bata son zama da mu Ki hakura kawai kuma fa mahaifiyar ta ce ta basu ita"da yake duk kwadayin ta da gulman ta tana son mijin ta bata taba mishi musu shiyasa tace ta hakura Amma a karkashin zuciyar ta cewa tayi dole suci arziki tare koda Laylerh bata gidan ta..

Baaba ko taso ya bar Laylerh ta koma can ko zata huta Amma sai wani jin yarinyar yake kamar Yar shi Gashi ba hali tayi magana sai ya nuna bacin rai shiyasa tsakanin ta da Laylerh gaisuwa ce Wata Rana kuma sai suyi hira har Laylerh Na mamakin ta don yanzu fuska biyu Gare ta,ta rasa shin son ta take yi ko tsanar ta tayi..

Yanzu ta idar da sallah i'sha tana zaune akan sallaya ta gama addu'ar ta Amma bata mike ba idanun ta Na kan hoton Naseer haka kawai bata gajiya da kallon hoton, duk da kya'n shi ba har can bane ita ji take duk duniya ba Na mijin da ya Kai shi kyau saboda kyan zuciya ita ce kyau..wayar dake kan katifar ta taji ya Fara ringing kamar zata share nan taja dogon tsaki tana mika hannu tunda ta San dai ba Aunty'n ta bane sannan ba ya Muhammad bane don su ringing tune Na Musamman ta sa musu Allah ya sani bata fiya son Call ba a rayuwar ta wanda hakan kuma halittar tace shiyasa ma bata da lambobin mutani dayawa, mika hannu tayi ta dauka da yake wayar a kife take sai ta juya tana kallon fuskar wayar,kwabe fuska tayi ganin bakuwar lamba ce ke kira shiyasa da farko kamar ba zata daga ba sai kuma tayi receiving tare da Sawa a kunnen ta tayi shiru bata yi magana ba idanun ta kuma Na kan hoton Naseer, daga daya bangaren ma shiru aka yi jin haka sai tayi tsaki tana kokarin cire wayar a kunnen ta

"kada Ki kuskura koda wasa Ki sake mini tsaki saboda ni ba sa'an Ki bane"muryar da taji ne yasa jikin ta duk ya Fara kyarma wayar Na kokarin fadiwa da kyar ta fisge wayar ta mayar kunnen ta idon ta Na kawo ruwa kamar a gaban shi take don bata manta yadda ya kusa hallaka ta kuma ba zata taba manta wannan muryar ba Wanda ta San Na mahaukacin nan ne ba baki Na rawa tace"Ka..Ka..Kayi...hak'uri.... Ban San Kai bane".shirun da yayi Na dogon lokaci yasa ta tunanin ko ya katse kirar sai ta cire ta duba screen din wayar taga yana reading sai ta mayar kunnen ta

"an kawo miki takardun ne?"yayi tambayar cikin ko in kula da kuma nuna jin Kai

"A'a" ta fada da sauri nan ma shiru yayi ita ko ya gama kawo ta har wuya ji yadda yake kona Kati Wai shi a lallai miskili a ranta taja tsaki tana murkuda baki tunda ta San ba ganin ta yake ba

"Ki tabbatar an kawo kan karshen wannan satin".in sha....."bata Kai karshen zancen ta ba taji ya katse kirar"yafi nono fari"ta fada a fili ita wallahi har yau ganin

mahaukaci take mishi tana kuma tsoron ya illata ta numfashi taja tana mamakin zallar jin Kai irin nashi to shi a jin shi waya fi?kudi kuma Ai Allah ke bayarwa kuma dayawa sun fi shi,tsaki taja ita daya kuma tace in kyau ne Ai ba'a sa fararen maza a jerin kyawawa namji fari Ai Dan daudu ne,murmushi tayi ita daya nan ta maida hankalin ta kan wayar dake hannun ta sannan tayi searching number'n Aunty Nah nan ta Fara dialing ringing biyu yayi Aunty ta dauka "Assalamu Alaikum".

" Wa'alaikisalam Laylerh dazun muka gama waya lafiya Kika sake Kira?"

"Aunty yanzu ya Kira ni yana tambayar an turo mini takardun ne to ni kuma a ina Na San Zan samu tunda yana can garin mu kuma wallahi Aunty ya fiya jin kanshi sai kace wani mace".murmushi Aunty tayi tana jinjina yadda komai yayi baya burge Yar tata nan tace

" wallahi dama ina tunanin tura miki kada Ki damu gobe in sha Allah za'a kawo miki batun shi kuma in yaja miki Aji ke ma Ki rama".wauta yasa ta fadin

"Aunty a ina aka samu kuma Wa zai kawo?"kin San me da yayi magana sai ya jima yake sakewa Allah ganin Dan daudu nake mishi har da wani fadin" Ki tabbatar an kawo kafun karshen satin nan".ta kare zancen da kwaikwayon muryar shi Mai Amo da kuma nitsuwa, a tare kuma suka fashe da dariya ita da Aunty'n ta zaka ce ba uwa da diyar ta bace,tsam bata so Yar ta tayi Wata Kawa sama da ita shiyasa ta bude Mata kofar fada Mata duk wani damuwa nata,ba laifi ta kan biye Mata suyi ta shirme don tafi jin laylerh fiye da Muhammad Allah ya sani ita Kawa ta haifawa kanta ba diya ba shiyasa tace

"Masu Kawa suna dayawa Ai batun ina aka samu kuma rubuta Miki aka yi Amma wannan Yaron ya fiya rigima".

" mahaukaci dai".jin Baaba Na kirar ta ne

suka yi sallama Aunty ko kallon Muhammad tayi tace" Dan Allah kada Ka sa diya ta ta haukace in ta Gan Ka tunda Ka hanani fada Mata".

"Aunty so nake Na shammace ta Kinga dama Na gama shiri gobe da safe in sha Allah Zan tafi kwana daya kuma zanyi don makaranta".

" to Allah kaimu".

A can bangaren Umar Farouq ko Tun jiya Abba ya sa shi a gaba da maganar ya tambaye ta ko an turo takardun ta shiyasa koda yace baida number'n ta yace Nana ta tura mishi a take ko ta tura don duk so suke ya samu lokacin ta ko zai rage maida hankali akan aiki su kuma fahimci juna kan Aure Amma sai yaki,shi ba bai son ake cusa mishi wannan yarinyar Mai shegen rawan Kai da sa ido da kukan banza yanzu ma yana zaune akan bed nashi daga shi sai three quarter da vest laptop Na cinyar shi yaga wayar shi ya Fara ringing yana leka screen din yaga Abba ne shiyasa ya bar wayar ta katse sai ya Kira ta..

Suna gama call din cikin hanzari ya Kira Abba yana picking yace"Abba tace ba'a turo ba".

"Ohk sai da safe" daga nan suka yi sallama Abban shi Na addu'ar Allah sa mace ta samu gurbi a zuciyar shi..

Washe gari karfe takwas motar su Muhammad ya nufi jalingo sai farin ciki yake zai ga Yar kanwar shi number'n malam ya Karba yana isa tashar jalingo ya Kira sa.. rufe shago malam yayi yaje har Tasha ya dauko sa koda suka isa gida Baaba ce kadai don Laylerh ta fita shago sayan abu..

Zama yayi aka bashi ruwa suka gaisa da Baaba cikin sakin fuska da yake tana da zolaya har da mishi wasa shi ko so yake ya tambayi inda Laylerh take Amma bai son suce ya fiya hanzari..sallama tayi a kofar falon tana shiga kan ta a kasa saboda taga takalmi kuma ta tabbata bako Na miji aka yi zama tayi a can gefe tace"ina wuni"daidai nan ta dago fuska tana kallon shi sosai zuciyar ta ya buga tana ganin kamar idon ta ne, shi ko murmushi ya Mata yana fad'in "lafiya qalau Laylerh" mikewa tayi da gudu ta fada jikin shi tana sakin kuka Mai cin rai malam dai murmushi yayi Baaba ko fuska ta tabe"meyasa baka ce mini zaka zo ba kuma waya nuna maka nan yaushe aka gane Ka,kaje wajen Aunty ne?"ta jera mishi tambaya tana Kai mishi duka a kirjin shi

"Haba Aunty Laylerh duk wannan tambayar ni daya Kinga sauka a jiki Na sai Na amsa miki" da sauri ta sauka a jikin shi tare da rike hannun shi gam kamar wani zai

kwace Mata shi nan yace"Bayan tafiyar Ku da kwana biyu Na koma wajen Aunty har naje Maiduguri Na dauko takardu yanzu ma shi Na kawo miki".

"Shine Wato kuka boye mini kai da Aunty ko to nayi fushi?" Ta fada cikin shagwaba "yi hak'uri ba Gashi yanzu kinyi murnar gani Na ba". Kasuwa malam ya koma Baaba ko waje ta basu nan tayi ta zuba mishi shagwaba tana tambayar shi abubuwa iri iri har wayar ta ta kawo mishi" iyehh su Aunty Laylerh an girma za'a yi aure"cikin yin kasa kasa da murya tana tabe baki da harara tace"Nifa ba so nake ba kawai Na amsa ne kaga in suka biya mini kudin makaranta kafun shekara biyun Na samu wani sai nayi Aure Na kawai"Kai ya gyada cikin biye Mata ya bata hannu nan suka tafa suna dariya kasa-kasa yace "kuma shawarar kin tayi Kinga munyi musu wayo kenan "

"Ai dama Na San in kana nan ba zaka Bari Na auri wancan mahaukacin da ko dariya baya yi ba wallahi mugu ne kaga yadda ya kusa kashe ni ranar". Ta kare zancen tana sauke ajiyar zuciya saboda tuno ranar da abun ya faru tayi

" to mu dai Allah ya Isar mana".

"Ameen fa Aunty kam da ba sanin shi tayi ba Wai ya Mata Allah ko ita ya samu zai duka".

haka suka wuni hira har dare nan yaci tuwon dare sannan ya ajiye musu tsarabar da Aunty ta tura musu Laylerh ko takardun ta ya bata nan ya sallame su gaba daya don gobe da safe zai wuce ba yadda malam da Laylerh basu yi da shi ya kwana a gidan ba don cewa tayi a dakin ta zasu kwana yace yana da aboki a gidan su zai kwana..

Zuwan yayan ta sosai yasa Mata farin ciki shiyasa ta kwana cikin nishadi Washe gari Bayan malam ya dawo da yamma sai ya mika Mata form tana budewa taga an rubuta Muwanshat college of health science and technology a saman da manyan bakake kenan health tech zata yi Amma bayin Allah'n nan sun raina Mata wayo sarai ta gane zata amfani yan gidan ne da wani abu in tayi makarantar"Ki cika gobe in sha Allah zamu je tare sai kiyi submitting "to tace nan ta koma daki ta cika dadi kamar zai kashe ta nan ta cika form din..Washe gari ta shirya tare suka nufi makarantar a gate keke napep ya sauke su a ido dai ta raina fasalin makarantar sannan students da take kallo da uniform kusan duk Mata ne kuma gani tayi kamar matan Aure sun fi yawa ba maza dayawa shagon photo copy dake cikin makarantar suka je nan suka yi photocopying duk abunda ya dace sannan suka nufi office Na

bursary.. malam ne ya gaisa da shi da alama kuma sun San juna nan ta gaishe shi sai suka yi submitting ya kuma tabbatar musu in sha Allah nan da sati biyu za'a sake admission.. Koda suka fito students sai kallon ta suke yi ita ko mita take a zuciyar ta mutum yasa uniform a secondary sannan a nan din ma yasa wallahi gwara Mata polytechnic ko college of education abu ga makarantu dayawa a rasa inda za'a kawo ta sai nan kenan kullum Gata cikin wanke uniform a haka suka nufi gida..

Bayan sati biyu tana kallo taji text a wayar ta tana dubawa taga Muwanshat ne suke congratulating nata Na cewa ta samu admission saura tazo Karba.. Ai a Washe garin ta shirya cikin abaya black ta sallami Baaba ta nufi makarantar.. Yadda take kallon students daga gate ya tabbatar Mata wadanda suka samu admission din suna dayawa hakan sai ya bata mamaki wannan kam duk wadanda suka nema ne suka samu..

Tasha wahala sosai kan aka zo kan ta da yake bata da saurin sabo kuma bata shaku da kowa ba nan ta nufi gida Bayan ta huta sai ta Fara karanta admission din nan ne ta fahimci zasu yi karatun Wata uku sai ayi wedding exams kuma cikin su Dari shida mutum hamsin kawai ake so nan ne fa hankalin ta ya tashi ta kuma jinjina kyan zuciya irin Na Alhaji M wakili lokacin da taga kudin makarantar.. Cikin sati daya aka gama Mata komai Na makaranta ba abunda ba a Mata ba,school bag duk ta saya don nan kam kudi aka tura Mata da Na handout din ta asusun bankin malam don bata bude account ba.. ta Fara zuwa makaranta sai dai waec awaiting ta sa saboda da can bata yi ba sai next year zata kawo musu karatu kam Alhamdulillah suna samu yadda ya kamata ta kuma yiwa kanta alkawarin in sha Allah ba zata yi Kawa ba har sai ta zama daya daga cikin mutani hamsin da za'a dauka don ta fahimci mutani dayawa a department din brain nasu naja..

Dole Baaba ta koma girki tunda yanzu Laylerh ba zama take yi ba Gashi Sunday da take free ma wankin Kayan ta take yi..

Bayan Wata uku suka yi exams cikin amincin Allah tana daya daga cikin wadanda aka dauka murna kamar ta hade rai nan aka Mata registration suka gama komai ta dinka uniform har Kala hudu duk da mitar wanke uniform da take saboda an tura Mata kudi enough.. da yake wando Ash Riga white sai half sunnah hijab ne ta kan daura after dress akai in zata tafi sai ta shiga school take cirewa nan ta Fara zuwa makaranta.. Har ila yau kuma bata sake ganin kiran Umar Farouq ba kuma hakan dadi ma ya Mata..

Horn motocin shi ke yi a kofar gidan su nan security ya bude kofar driver ya Danna hancin motar ciki Na securities nashi ma Na biye da shi parking suka yi nan daya daga cikin securities din ya fito ya bude mishi Amma sai bai sauko ba illa Bluetooth dake makale a kunnen shi yana magana a tsanake da alama kuma yana girmama Wanda yake magana da shi,lumshe idanun shi yayi Wanda ke dauke da dogayen lashes sannan ya bude su yana shafa sajen fuskar sa lokacin da ya Dan taba Bluetooth d'in alamar katse kirar.. a hankali ya sauko sai kuma yaja dogon numfashi da alama kuma a gajiye yake,as Usual sanye yake cikin suit sai dai ta yau black ce hakan ya Dada fito da Hasken fatar shi sosai yayi kyau hannun shi rike da Goran ruwa cike da jin Kai ya Fara taku sai suka ga cikin gidan su ya nufa tsabanin bangaren shi kamar yadda yake yi kullum.. da sallama ciki ciki wanda ba kowa ne zai jiyo shi ba ya shiga falon sai dai a take ya hada rai kamar zai yi aman bala'e sakamakon tozali da Sadiya da yayi ta fito daga kitchen rike da tray ga Kannen shi wadanda basu yi Aure ba duk suna falo har Aunty Hauwa "shigo mana Umar Farouq"Aunty Hauwa ta fada a hankali ya cigaba da shiga falon cikin takun kasaita yana kuma yiwa Sadiya kallon kaskanci,duk da ta Lura da kallon da yake Mata can kasan zuciyar ta ta tsorata sai ta basar ta karasa cikin falon tana fad'in "Aunty Kinga Na gama taba Ki ji".

" Masha Allah Yar albarkar"Aunty ta fada tana testing abincin da Sadiya din tayi sisters nashi kuma ko wacce Na harkar gaban ta don Sadiya Ai ba sa'ar su bane sai dai yayan su"kaga Tun dazun bakuwar Ka tazo wallahi yarinyar kirki da kyar securities suka bar ta ta shigo kaga har girki tayi taba kaji"ni ban cin abunda ta dafa"ya fada lokacin da ya juya ya nufi barin falon, tsam Aunty Hauwa bata jin dadin furucin nashi ba duk da ta san halin shi ta kuma kasa sabawa da hakan ta sani da wata ce ba ita ba tayi mishi magana banza zai yi shiyasa ta bi shi waje Sadiya ko ta rasa dalilin da Hana shi kyautata Mata zato Allah ya gani tsakani da Allah kawai take son shi ta kuma San hakan da yake yi kuskure ne don Wata Rana Ana zaton wuta a makera sai a same ta a masaka har yaushe zai gane shi din kadai take so Bayan shi bata da wani buri so take ya zama uba ga marainiyar Yar ta sannan ya zama miji Gare ta,hawaye ta share tana jin zuciyar ta Na Zafi duk da tasan dama shi a rayuwar shi baida yarda gani yake kamar kowa Na son ganin Bayan shi...

"Farouq yanzu abunda Kayi Ka kyauta?" Kin tsayawa yayi cigaba da tafiyar shi yayi tana biye da shi a baya"Wato don bani Na haife Ka ba shiyasa ina maka magana Kayi banza da ni"cak ya tsaya tare da Juyowa yana kallon ta Allah ya sani tayi kokari da shi da kannen sa ko mahaifiyar su iyakacin son da zata musu shiyasa ya juyo Gare ta tare da lumshe ido sannan ya rike hannun ta da dukka hannun shi da kyar yace"Sadiya ba yadda kike tunani bace wallahi mace ce Mai hatsarin gaske Wanda ni kadai na sani yanzu ma so take ta shiga jikin Ku ne don ta cutar da Ku Wanda ba

Zan taba barin hakan ta faru ba,har ila yau ban daina zargin da hannun ta a kisan Hashim ba don ba yadda za'a yi ta gano su in ba tare suke ba"ya kare zancen cikin sanyin da kuma soyayyar ahalin shi shiru tayi tana kallon kyakyawar fuskar shi yanayin shi Na rashin son magana da hayaniya sai ya koma abun tausayi a idon su suna ganin kamar akwai abunda ya rasa a rayuwa shiyasa suke son mishi Aure, wajen aikin shi yana da masu burin ganin Bayan shi Wata Rana suyi nasara Wata Rana kuma shi yayi nasara akan su duk da bai tabbatar da su wanene bane "Shikenan in sha Allah Zan kula kuma daga yau ba Zan Bari a sake barin ta ta shigo ba". Murmushin gefen baki yayi yace" dama shiga nayi don Na sallame Ki saboda Zan tafi Cameron wani aiki ".

" Allah ya bada sa'a Kai kullum ba zama Abban Ka har yayi Dana sanin nema maka aikin yanzu ya zaka yi da Yar mutani "ido ya lumshe kamar ba zai yi magana ba sai kuma yace"Allah na nan".yana gama fadin haka ya wuce Aunty Hauwa ko baki a bude ya bar ta sai Salman ne da yanzu shigowar shi ya rufe Mata baki yana fadin" yau kuma ya Farouq din ne ya zama sabon mutum? "

"Salman ban sani ba ko kunne nane bai ji da kyau ba,in ko naji da kyau kamar fa baida matsala da auren kila sun dadidai da yarinyar" kafadar ta ya dafa yace "Kai Masha Allah kila muma zamu Fara samun lokacin shi" daga nan suka juya bangaren su,duk yadda Aunty taso Sadiya ta tafi abun yaki don Allah ya sani tana matukar girmama zancen Umar Farouq.. Karfe biyar nayi tace akwai series da take kallo a star times broken heart nan sister's nashi suka tambaye ta sai ta labarta musu nan suka Fara kallo tare sun kuma ce in sha Allah kullum zasu ke kallo..sai gab da magrib ta tafi tsam a fuska Aunty bata nuna Mata sauyi ba..

Bayan magrib ko jirgin su Umar Farouq ya tashi..

**

Kasancewar yau bata da makaranta kwance take a three seater tana kallo Baaba suna da Aure kuma daurin auren da safe ne ta tafi malam ma ya tafi kasuwa sai ya rage ita daya a gida kamar daga sama Auta ta diro tana"Salamu Alaikum Na dawo "ba yabo ba fallasa Laylerh ta dube ta tace" Ai basu nan sannu da dawa"daga sama har kasa take kallon Laylerh ganin ta sanye cikin abaya wacce ake yayi sannan tayi asetta da Dan kwalin,tsaki taja Amma har kasan zuciyar ta tana jin zafin Laylerh nan ta nufi corridor dakin Umar Farouq ta bude sai taga alamar an Dade ba'a yi amfani da shi ba kenan da gaske ya tafi kamar yadda malam ya fada Mata Bayan sun dawo lokacin da ya Kai Mata visit, Jan kofar tayi ta rufe tana jin kewar shi sai ta

nufi nata dakin ta shaba wanka da kwalliya ganin Laylerh tayi sai ta dauki Kayan sallar ta Tasa tare da fece turare nan ne ta fito falon.. hararar Laylerh tayi tace"Wai ba zaki bani abinci bane?"hankalin ta naga TV tace"ke da gidan Ku har sai wani ya baki abinci ga kitchen Kije Ki dafa".

"Kan uba ina magana kina mayar mini a matsayin Ki Na Yar aiki tukunna ma Wa ya baki Kayan jikin Ki?"

"Ki jira in masu gidan sun dawo Ki tambaye su". Kan tace wani abu Baaba ta shigo da gudu ta fada jikin Baaba tare da fashewa da kuka tace"Baaba Ki duba Yar aiki da Rainin wayo ina Mata magana tana fada mini bakar magana". Ga mamakin ta sai gani tayi Baaba ta dubi inda Laylerh take tana fad'in" abinci je Ki kitchen Ki duba cikin wani blue cooler zaki samu".to yau kuma me yake damun mahaifiyar tata da bata yiwa Laylerh holo kamar yadda ta Saba ba.. kitchen ta nufa Bayan ta d'ebi abincin sai suka nufi dakin Baaba a can ne tana cin abinci Baaba Na bata labarin abunda ya faru a Bayan ta sai dai ta boye Mata batun Laylerh ce ta dauko evidence sannan zasu yi Aure saboda wani dalilin nata"to Baaba ina kuma Laylerh ta samu Kayan jikin ta su fa ake yayi wayar ta ma tsada Gare shi".

"Ba Na fada miki ta hadu da mahaifiyar ta ba Ai dangin tane suka saya Mata".

" to meyasa Baku bar ta a wajen su ba".

"Malam mana da karambani" da yake bata son laifin uban ta kuma ta San in suka cigaba da hira Baaba ta Riga daura mishi laifi kenan shiyasa tayi shiru..

Sai gab da magrib suka fito falo kallon Laylerh dake zaune akan kujera Auta tayi tace "Baaba kin fa Hana mu hawa sama kalli Laylerh a sama take zaune".

" nace Ki cire ido akan ta".zuwa yanzu kanta ya daure ganin Baaba ta daina yiwa Laylerh fada ita ko yi tayi kamar bata ji su ba..

Malam Na dawa ta mishi oyoyo cike da farin cikin ganin ta yace"Masha Allah an karbi hutu kenan ina fatan sakamakon yayi kyau".

"Ai bamu Karba ba Baba form master'n an samu matsala da shi sai aka Kore shi to yanzu an bawa wani bai gama ba sai Mun koma zamu Karba".

" Masha Allah "a hankali Laylerh ta sauka kasa ta mannu da jikin kujera tare da yafa Dan kwalin ta a Kai ya rufe Harda Rabin fuskar ta tace"sannu da dawa malam".

" Yauwa Ai ko kamar kin San ina Neman Ki".

"Ni kuma?" Ta tambaya zuciyar ta Na tsinkewa"matsoraciya kawai ba wani abu bane batun angon Ki ne kunyi waya tunda ya tafi kuwa saboda a ranar ya Kira ni muna meeting Na yan kasuwa nace Zan Kira shi daga baya Ashe sallama zai mini sannan ya Kira Baabar Ku wayar ta a kashe ".

" a'a tunda ya tafi bamu yi waya ba".

" kullum da dare ina ji kuna waya Kice baya kiran Ki Ince ranar har nace Ki bani mu gaisa Kika Ki don Kinga banda number'n kasar da yaje" fadin Baaba kenan malam ko yi yayi kamar bai ji me tace ba"to meyasa baki Kira shi ba".

"Malam Nima banda number'n shi ta wancan kasar kila aiki ne ya mishi yawa" ta fadi haka don kada su fahimci ba wani shakuwa tsakanin su Auta ko sun bar ta a duhu ance angon Laylerh sannan an ambaci wani kasa bugu da Kari kuma kamar iyayen ta Nada kusanci da shi angon ko dai yayan ta ne da sauri ta girgiza Kai don Laylerh bata Kai ajin matar da zai nema ba"Baba Wai akan Wa kuke zance ne?"mikewa yayi yana zungure kanta yace "ban son gulma" daga nan ya wuce masallaci Laylerh ma mikewa tayi ta nufi daki nan Tasa Baaba a gaba da tambayar wanene angon Laylerh "Umar Farouq ne fa kuma su malam ne suka cusa mishi ita ba don yana so ba". Mikewa tayi ta nufi daki yanayin ta kuma ba zaka iya fahimta ba..

Bayan sun idar an dawo falo Auta sai wani mannewa Laylerh take don son gani ko zai Kira sai tayi snatching number'n shi a ganin ta cikin dabara zata ce Laylerh ta bata su gaisa sai tayi snatching number Laylerh ko ta ma manta da shi tunda sau daya ya taba kiran ta kusan Wata hudu kenan yanzu akan me zata sa ran zai Kira..

Ba karamin mamaki taji ba ganin number'n da ba Na Nigeria ba ya bayyana a fuskar wayar ta kuma ta San dole shine tunda ba Wanda ta sani a kasar waje kurawa wayar ido tayi kamar sokuwa zuciyar ta Na bugawa, haka Auta ma fuskar wayar take kallo Laylerh ta Kai hannu zata daga sai Auta ta Riga ta cikin rawar Kai da nuna tafi kusanci da shi tayi receiving tana fad'in

" hello yaya Na ya kake ya gida kwana dayawa Auta ke magana ".A bangaren shi ko cire wayar yayi a kunne ya kurawa fuskar wayar ido sai ya katse kirar..

Da wuri ta cire a kunnen ta tana yiwa Laylerh kallon tuhuma ba dadewa kuma wayar ta Fara ringing number'n dazun ne sanin halin shi da shegen masifa da kuma iko yasa Laylerh fisge wayar ta zata yi receiving Auta tace" banda munafurci asa a hands free mana".sanin ba zancen arziki suke yi ba bai wuci ya Kira don ya tambayi wani abu bane yasa ta receiving tare da Sawa a hands free "Assalamu.....".

"Kifa shiga hankalin ki dani don kin gama raina ni shine Zan Kira wayar Ki Ki bawa Wata ta amsa tana mini ihu a kunne? "Murya Na rawa tace" ita ce fa ta fisge ".

" cire mini waya a hands free "ya fadi cikin tsawa da yasa hanjin cikin ta kadawa da wuri ta cire wayar a kunnen ta tare da cirewa a hands free don in an sa maka waya a hand's free zaka ji maganar da kake yi yana dawo maka, Auta ko iya takaici tayi Wai ita yake cewa tana mishi ihu har yaushe ya San Laylerh..

Ita ko Laylerh jin yayi shiru sai ta mike tare da nufar dakin ta cikin tsoro tace

" ina wuni".

har ta fidda ran zai amsa sai yace"malam Na gida ne?"a zuciyar ta tace Ai dama Na sani ba amsawa zai yi ba

"Ehh yana nan".

"Kai mishi wayar"a gadarance ya fada to tace a zaton ta ko zai kashe wayar in ta Kai sai ya Kira sai taga wayar Na reading shiyasa bata yi magana ba tana isa tsakar gida ta Mikawa malam waya nan suka gaisa sai ta basu waje sun jima suna waya sannan malam ya Kira ta yace"Ki kaiwa baabar Ku waya su gaisa".ya ilahee shi ba zai Kira ta line nasu bane nan ta nufi dakin Baaba ta bata cikin zancen da suke da Baaba ne ta fahimci ya manta wayar shi da line nasu ke ciki a kuma karshen zancen

ne taji Baaba Na cewa "to in sha Allah zata tura maka" nan ta Mikawa Laylerh wayar tana fad'in Ki tura mishi layin Auta ".

" ni banda layin ta"Zan baki"to tace ta fice a dakin ba tare da sanin bai kashe wayar ba tace"Ai ko zai ga number wallahi sai Randa Nasa kati Zan tura mishi in gaskiya ne ita Baabar ta tura mishi ta wayar ta mana Wato nice Mai katin banza".a bangaren shi ko Kai ya girgiza a fili yace"yarinya karama da rawar Ka". Allah ya sani bai son macen da bata da nitsuwa sai ya katse kirar

Can Bayan ta koma daki ba jimawa sosai sai taji rashin dacewar abunda tayi daga nan ta wuce dakin Baaba ta kwashi number'n Auta a wayar ta ta tura mishi..

A bangaren Auta ko Baaba ta sanar Mata ya karbi number'n ta zai Kira ta a take farin ciki ya lullube ta shiyasa ta nufi dakin ta wayar ta Na Fara ringing ta leka taga ba number'n kasar nan bane sai taki dagawa Wai a lallai zata nuna tayi fushi ta san zai yi ta Kira,Amma me zai faru daga Kira dayan bai sake ba abunda bata sani ba shine ya Kira ta ne saboda karancin da ta mishi lokacin da yake gidan su..

Wayar ta ta dauka nan ta Fara dialing number'n shi Kira ya Kai sau biyar ba'a daga ba nan tayi ihu tare da yin jefi da wayar...

Comment

Share

©Hafciey Musa

[1/25, 5:41 AM] Hafciey Musa😘: *□LAYLERH□*

(The prettiest emerald)

Washe gari tana tashi kasancewar ta makara a gurguje tayi breakfast sannan ta share iya falon daga nan ta Fara shiri cikin hanzari ganin lokaci ya kusa kurewa,Bayan tayi wanka sai ta fito falon daure da towel da yake ta San malam baya nan,uniform nata da ta goge ta dauka bata bi ta kan Auta da ke Mata tsaki ba a gurguje ta sa sannan ta dauka turare ta fesa sai ta dauki school back nata hannu daya ta makala a falo ta tarar da Baaba"Na tafi"tace lokacin da take fita bata jira amsar Baaba ba tayi gaba don taji alamar Mai keke a kofar gidan nasu Gashi in ya wuce kan ta samu wani zai dau lokaci kasancewar anguwar a lungu take"ina kuma zaki je ga can kaya Na fitar ki wanke mini"tabbas taji me Baaba tace har taso manna Mata hauka sai taga bai dace ba cikin daga murya tace"Ki ajiye in Na dawo Zan wanke yanzu sauri nake yi"ta Kai karshen zancen tana bude karamin gate Na gidan tana jin Baaba Na fad'in "da yake bani Na haife Ki ba Ai kya ce haka in Amina ce ta saki tuni zaki yi""Shiga keken tayi tana duba agogon dake daure a tsintsiyar hannun ta sai addu'a take Allah sa kada ta makara sanin lecturer psychology din in ya shiga ko da minti daya Ka Kara to baza Ka shiga ba..keke Na ajiye ta da wuri ta biya shi ta shige cikin school din tana tafiya cikin sauri saboda taga motar shi..da yake class nasu a upstairs yake Tun a downstairs din take jin hayaniya Wanda ta tabbatar daga department nasu ne don tana ji cikin zancen Ana kiran sunan wasu course mate nata hakan ya sata sauke dogon ajiyar zuciya tana murmushi ita daya sai taci gaba da haurawa a hankali don bata fatan Allah ya kawo ranar da zata yi missing class nashi Gashi katon Arne ne sai shegen ra'ayi kuma course nashi two credit unit ne..

Tana shiga hall din ta tarar kowa Na harkan gaban su iya wadanda take sannu da su ta Mikawa hannu suka gaisa daga nan ta zauna tana Dan duba handout nata.. Bayan Isar ta da kamar minti talatin aka ce duk yan department nata su tafi office Na provost akwai receipt da zasu Karba dayawa hamdala suka yi jin an kashe lecture Na Mr chufo..layi suka yi Ana shiga daya Bayan daya sai ranar da ke cin kaniyar su shiyasa ma Tasa handout ta tare fuskar ta..

A daidai lokacin ne kuma security dake sanye da uniform nashi an rubuta sunan makarantar ya wangale gate motoci uku suka shigo duk students dake waje da ido suke bin motar tsabanin ita da kallo daya tayiwa motocin ta cire Kai don in bata yi karya ba motocin boss nata Na company ne..

Bude mishi kofar aka yi nan ya fito sai wani jin kan shi yake yi daga jikin motar ya dakatar da guards nashi ta hanyar daga musu hannu sannan cikin isa da nuna mahaifiyar shi Wata ce ya Fara dumfaro su,kallon students din ya ke yi idon shi bai

fada ko ina ba sai kanta,glasses Na idon shi ya gyara yana fad'in "ina ne office Na provost". Tsarai ta San da ita yake magana don tana jin yadda idon shi ke yawo a kan ta sai tayi kamar bata San da mutum ba sanda ya maimaita tambayar shi a Karo Na biyu don a tunanin shi bata ji bane" ban San office din ba"ta bashi amsa ba tare da ta dubi bangaren da yake ba"Ince a makarantar nan kike?"ya tambaya ran shi Na sosuwa ga dai uniform a jikin ta sannan tace bata San office Na provost ba"na dai ce da Kai ban sani ba Ka tambayi sauran ".cikin tafasar zuciya ya daga hannu zai mare ta wani lecturer ya rike shi" sannu da zuwa sir"lecturer ya fada yana wage hakora kamar gonar auduga jin bai amsa ba sai ya sake fad'in "ke me ya hada Ki da shi?"

"Ai wallahi Sir da Ka bar shi ya mare ni sai Na Rama jiya fa ba yau bane a tunanin Ka kullum ne zaka mini cin Kashi Na bar Ka to nan dai ba company'n da kake gadara da shi bane inda Ka Kore ni Na zama jobless" zuwa yanzu ji yake kamar ya shake wuyar ta sai yaga ta daina numfashi ba abunda yafi tsana a rayuwar shi fiye da ayi disgracing nashi a bainin jama'a shiyasa cikin tafasar zuciya ya juya ya nufi mota daidai nan kuma provost ya fito daga office nashi saboda an Kai mishi gulman yazo.. ganin Sulaiman ya juya da gudu ya Fara bin shi nan wasu lecturers suka rufa ma provost baya, yana isa mota ya shiga nan driver yaja..

Akwai alfarmar da provost din ya jima yana nema a wajen Sulaiman Allah bai yi zai samu damar ko haduwa da shi ba sai yau to Gashi yau din ma da alama an bata mishi rai.. security aka Hana bude gate din college din inda student ke bin provost da lecturers da suke bin shi da kallo suna mamakin to shi din wane ne..ganin an Ki bude mishi gate sai ya fita a motar da kafa ya fice cikin makarantar sai a wajen ne suka cim mishi"Dan Allah ranka shi Dade Ka dawo muyi maganar da Allah fa Na hada Ka"

"Maganar nan ba zata yuwu yanzu ba zamu sake sa time". Yana gama fadin haka motocin shi suka karaso inda yake nan ya shiga suka tafi..

Provost ko yana Komawa cikin makarantar direct office nashi ya wuce inda yasa aka watsar da students dake gaban office din yace yana son kasancewa shi daya jin haka fa sai hankalin Laylerh ya tashi tana Mai fargaban hukuncin da zasu dauka a kanta shiyasa cikin mutuwar jiki ta Fara nufar class sai academic sectary da yake son maganar ta yayi kiran ta zuwa office nashi..

Waje ta samu ta zauna zuciyar ta sai bugawa yake yanzu in suka Kore ta me zata ce a gida" me ya hada Ki da shi?"tambayar shi ya katse Mata tunani shiru tayi tana

wasa da zoben dake hannun ta can cikin jikin ta kuma har ya so ma rawa"Laylerh nace me ya hada Ki da Babban mutum kamar shi?"

"Banda abun Ka in kaga budurwa kamar ta tayiwa Na miji kamar sa rashin kunya Ai kasan akwai alakar soyayya a tsakanin su kila Bayan ya gama da ita sai ya yaudare ta shiyasa ita ma ta Rama". Rintse idanu tayi jin Kalmar da lecturer din ya tofa akan ta Amma kuma bata da bakin magana shima acadamic sectary bai so Kalmar da Abokin aikin nashi ya fada ba shiyasa yace" tashi Kije".koda ta fita a hankali take tafiya baran ma da taga yadda sauran yan uwan ta students ke bin ta da ido sai duk ta tsargu tana Mai da na sanin abunda ta aikata direct class ta nufa nan ta zauna class din sai kallon ta suke kamar bakuwa ita ko wasa take da pen a hannun ta kuma a jikin window take zaune,a zahiri wasa da pen din take Amma a badini ta rasa me ke Mata dadi har bata San pen din ya fadi ta waje ba nan ta fita domin daukowa"ni wallahi dama haka kawai nake jin zafin ta shiyasa Na kosa naji hukuncin da provost zai dauka a kan ta".

"Ai Ki Bari ni nasan duk yadda aka yi saurayin ta ne Bayan ya gama abunda zai yi da ita ya bar ta".

" Nifa ba abunda yafi bani haushi kamar yadda bata shiga harkar kowa a department nan bare ta kaiga yin Kawa".yan department nasu ke tattaunawa Bayan fitar ta ba tare da sanin tana jin su ba,koda ta shigo shiru suka yi tare da Kama wani babin hira..wani lecturer ne yazo yayi kiran ta Wai provost Na Neman ta mikewa tayi kamar wacce kwai ya fashewa a ciki ta nufi office din..

A can bangaren provost kuma Bayan ya rufe kan shi a office sai ya Fara tunanin irin danyan hukunci da zai yanke Mata,in ya Kore ta a makarantar ma ba zai ji sanyi ba don Ai batafi Wata hudu a makarantar ba in kuma yace suspension zai bata nan ma duk ba zai huce takaicin da Tasa mishi ba shiyasa ya hada board meeting a nan ne yake Neman a bashi shawarar hukuncin da zai yi Mata sai wasu suka ce a Fara kiran ta Aji ta bakin ta tukun shiyasa ya aika a Kira ta..

Koda tayi knocking ta shigo sosai gaban ta ya fadi ganin duk lecturer school din Na wajen sai wani lecturer ne yace"dube ta fa yarinya da ita sai son bin maza banda haka me zai hada ta da shi ".

" sir ina ji ance zato zunubi koda ya kasance gaskiya kamata yayi kaji daga baki Na kan Ka yanke mini hukunci "duk sunyi mamakin karfin halin ta ita kan ta bata San tana da wannan jarumtar ba Amma koma yaya ne tayi alkawarin kare kan ta a gaban su gudun kada a Kore ta don Auta kadai ta ishe ta,nan wasu malamai masu basira suka ce bata dama..

Tiryan-tiryan ta Fara basu labarin rayuwar ta da kuma haduwa da shi sannan ta gyara labarin yadda za'a yi reasoning nata" ba abunda yafi mini ciwo fiye da yadda suka daura mini sata a company'n sannan ya Kore ni kuma ko Bayan ya gane gaskiya bai bani hak'uri ba,ni abunda Na fahimta a nan shi din ya mini farin sani don ba yadda za'a yi ya Kira suna Na ba tare da Na fada mishi ba sannan har ya fadi shekarar da Na gama makaranta,nayi imani yana amfani da rashin Gata nane yake mini duk abunda yaga dama Wanda bai kamata ace ya mini shi ba kasancewa ta mace wannan dalilin yasa Na mishi abunda Na mishi yau dugun kada gaba yayi mini a inda bai dace ba"duk shiru suka yi suna daura zancen ta a mizani da kuma jin tausayin ta don bata ce da su ta gane iyayen ta ba,ita ko addu'a take Allah sa zancen da tayi ya shige su"in ko haka ne kinyi daidai don kamata yayi a koda yaushe mace ta kwaci yancin ta Amma kuma Ki kiyaye don in kin yiwa wani ya bar Ki ba lallai wani ya bar Ki ba".Cewar provost ita ko Kai ta sadda kasa kamar mutumiyar arziki tana godiya ga Allah da yasa ta wanke kanta a gaban su har ma da masu zargin akwai wani alaqa tsakanin ta da head boy Wanda har zuwa wannan lokacin kuma bata gane shi ba sallamar ta suka yi nan ta koma class.

**

Gaba daya ahalin Alhaji M wakili zaune suke a third floor Na gidan suna breakfast saboda wannan ita ce al'adar gidan kullum a third floor suke breakfast gaba dayan su Wato a sashin Abba, Umar Farouq ne basu fiya samun lokacin shi ba don sai a Irga sau nawa yayi breakfast a gida tunda ya Fara aikin NIA,kuloli Dan daidai ne jire a dining din Aunty Hauwa Na serving nasu duk yaran sauri suke don suna da lectures da safe"Aunty zuba mini Ki fita harkan yaran nan".

"Amma Salman Rainin Ka yayi yawa Ince duk gidan nan ba wacce Ka girma" shi dai Abba glass nashi ya gyara yana breakfast can kasan zuciyar shi ko kewan Dan shi ne..Bayan ta gama serving nasu sai ta zauna don tsam yan aiki basu hawa bangaren shi nan ta Fara breakfast ba Mai magana cikin su,Fara breakfast nata ba jimawa wayar ta ya Fara ringing nan ta duba sai taga daga gate Na gidan ne ake kiran ta"Assalamu Alaikum Hajiya fatan an tashi lafiya"bai jira amsar ta ba yaci gaba "dama wannan abokiyar aikin Umar Farouq ne tazo Wai sai an bude Mata gate ta shiga to ni kuma jin kin Hana mu budewa ne yasa nace Bari Na sanar da ke".

" kace da ita ba kowa a gidan"da sauri ya rinsina Kai kamar yana gaban ta yace"an gama Hajiya ".daga nan ya katse kirar.

" wacece tazo? "Abba ya tambaye ta ba tare da ya dube ta ba yana Mai cigaba da cin abincin shi yaran ne suka zuba Mata ido suna jiran amsar ta" Sadiya ce abokiyar aikin Umar Farouq to kuma yace a Mata iyaka da gidan"ta bashi amsa hankalin ta duk Na kan shi tana jiran amsar da zai bayar don tasan shi da ra'ayi"Kice ya bude Mata ta shigo "taso mishi musu Amma ganin ba fuska sai ta Kira ta sanar da security ya bar ta ta shigo sannan ta katse kirar.

"yanzu don Umar Farouq bai son maganar ta Shikenan sai Ki Hana ta shiga gidan,to fada mini wace macece Umar Farouq ke son maganar ta Bayan yan uwan shi da ya zame mishi dole kin sani yarda ce tsam baida ita a rayuwa don yanayin aikin shi ba Wai yarinyar ce baya so ba,taya za'a ce wacce ta wanke shi daga zargin da ake mishi Ki saka Mata da haka".

A can waje kuma security Na budewa Sadiya Tasa hancin motar ta cikin gidan yau dai ita kadai ke yawo kuma daga makarantar Yar ta take saboda ta sauke ta ne tayi hanyar gidan su Umar Farouq duk da tasan baya kasan,Bayan tayi parking motar wayar ta kadai sai key ta dauka nan ta nufi cikin gidan,sadiya kyakyawa ce sosai wacce ko Yar uwar ta mace ce tasan tana da kyau ta kuma yi gaskiya da tace tafi Laylerh kyau..a falon ta zauna nan yan aiki masu gaishe ta suka ce" ance Ki hau lifter Ki same su a third floor ".ba tare da ta amsa musu ba ta mike direct lifter ta hau sai third floor tana isa ko murmushi ta shimfida a fuskar ta ganin breakfast suke sai ta zauna a falon" bismillah karaso mana muyi breakfast ".

" a'a Hajiya Na gode kuci kawai".murmushin dole Aunty Hauwa tayi don tsam bata son yarinyar kusa da su tunda Umar Farouq ya gargade ta Gashi yanzu baya kasar.."ina kwana Abba"Sadiya ta fadi lokacin da take Zamewa daga kujerar da ta zauna tare da rusunar da Kai kasa" lafiya ya wajen aikin?"alhamdulillah tace nan ta gaishe da Aunty Hauwa ba yabo ba fallasa ta amsa daga nan sai ta koma kujerar ta zauna tana latsa wayar ta nan kannen shi suka gaishe ta can ta maida hankali kan TV dake falon tana sauraron news "gaskiya kasar nan ba tsaro ko kadan". Da yake shi Abba Babban mutum ne ya San rashin tsaron kasar fiye da ita sai yace" Ai Ki Bari wallahi jiya mutani uku aka yi kidnapping a jalingo kuma duk cikin anguwa daya koda dayan yaso musu gardama sai suka kashe shi can you imagine ace har gidan mutum za'a shiga a dauke shi Allah dai ya kawo mana sauki a kasar nan".

"Hmm Abba Ai Nima jiya security Na ya tsinci wasika da aka ajiye a kofar gida Na cewa nice next target". Duk dakatawa suka yi da breakfast din suka maida hankalin su kan ta" Target Na me kuma?"Aunty ta tambaya "wace target kuma ya wuce Na kashe ni".

" subhanallah shine kike yawo a gari ba tare da saro ba yanzu wani mataki Kika dauka "Abba ya tambaya

" Ai nayi reporting a agency namu kuma an Kara mini securities ba komai gida Na a tsare yake".

"Alhamdulillah kinyi daidai Wai ace duniyar yanzu in Kai talaka ne Ka wahala in Mai kudi ne kuma baka tsira ba".

" Allah dai ya kyauta ita kuma taci gaba da addu'a ".Cewar Aunty nan Abba ya mike zuwa Asalin falon sa don ya gama breakfast Aunty Hauwa ko cewa tayi" muje second floor ko don so nake Na shirya Zan fita anguwa ".to tace inda ta mike suka koma bangaren ta..Sadiya ko Na yaba tsaruwar gidan da kuma rashin nuna su d'in wasu ne da masu gidan ke yi sai Umar Farouq ne ke bawa rayuwar ta wahala..duk yadda taso suyi hira da Aunty Hauwa ta kuma jima a gidan bata samu fuska ba don Aunty Hauwa nuna Mata tayi tana busy da shirin fita dole ta mike ta sallami Aunty Hauwa.. Ajiyar zuciya Aunty Hauwa ta sauke ganin ta tafi don ta San haka kawai Umar Farouq ba zai ce kada su ja ta jiki ba da yake shi mutum ne Mai sirri duk lalacewar Ka ba zai taba fadawa duniya ba sai in Ka shiga gonar shi nan ne zai maka iyaka Amma banda wannan bai damu ba kaje can Kayi rayuwar Ka don bai taba daurawa kan shi damuwar wani ba cuxx yasan in har Kayi dipping into somebody's life dole zaka samu abunda ranka baya so wannan yasa tsakanin shi da kannen shi ma sai dai ya musu ihsani in kuma batun tarbiya ce ya yarda da mahaifin shi da kuma yadikkon shi..

A gajiye ta dawo gida direct dakin ta ta wuce sai dai kallo daya zaka Mata Ka San jikin ta yayi sanyi don abunda ya faru a makaranta,jifa tayi da school back nata sannan ta Fara kokarin cire uniform din wandon ta, ta zauna a bakin katifa ta karasa cire kafar wandon don yana Mata wuyar fita daga nan ta cire rigar ya rage daga ita sai inner wears ta shige toilet wanka tayi ta fito cuxx azahar kam tayi shi a makaranta gown Mara nauyi ta saka sai hula nan ta fito falo don Allah ya sani yunwa take ji"sannu da dawa malam"ta fadi tana durkusawa "Laylerh an dawo ya makarantar da fatan Ana karatu" da murmushi a fuskar ta tace"Ehhh malam gobe da safe ma muna da test ".Masha Allah nan ta mike zata tafi" baki ji ba"Komawa tayi ta durkusa "nace me ya hadaki da baabar Ku da safe har Kika tafi baki yi girka ba". Da fuskar confusion ta kalle shi" girki kuma wallahi nayi wanki ne tace Na Mata sai nace lokaci ya kure in Na dawo zan mata".

"To aikin cikin gida kuma me ya Hana Ki yi?"

"Malam falon da kake zaune a ciki ma ni Na share sannan batun sauran aikin naga Na makara ne kuma Ai kamata yayi a mini uziri tunda ga Auta sai tayi ba sai komai ne zanyi ni daya ba". Ta Kai karshen zancen tana jin zafin sharri da su Baaba suka Mata so take ta fito fili ta nuna musu cewa yanzu fa su ke cin arzikin ta ba ita ke cin nasu ba Amma nauyin malam ba zai bar ta ba" to da Kika ce kinyi abinci meyasa baki ajiye musu ba Kika yi naki ke daya?".

"Malam taso muje kitchen din Ka gani da kan Ka". Mikewa yayi suka nufi kitchen tana addu'ar Allah sa ta gani koda suka shiga kitchen din sai ta duba kusa da sink Na wanke wanke inda ta rufe musu doya da kwai da ta soya sai bata gani ba daga idon ta tayi sama nan taga kulan cikin drower sai ta Ciro shi tana hamdala a ran ta" ka gan shi nan".

"Banda abun Ki ina zasu gani tunda kin boye a sama".

" wallahi wallahi a nan Na ajiye "ta fada tana nuna inda ta ajiye sannan taci gaba da fad'in" kuma mu dauka a sama Na ajiye Ai sun San a kulan nan ake zuba breakfast sannan Ka taba flaks sanda Na sa tea, Na rasa meyasa Baaba take biyewa Auta don kawai ba gidan mu bane sai suke mini abunda ran su ke so..lokacin da nazo gidan nan nazo ne a matsayin Yar aiki shiyasa duk wani rashin kunyar da Auta ke mini nake hak'uri duk da Na girme ta Amma yanzu ba daya yake da lokacin da nazo ba don sai nake ganin kamar mu duk daya ne tunda har mahaifiya ta ta bar muku ni me zai Hana ita ma Auta take wani aikin a cikin gidan nan".numfashi yaja don bai son nuna Mata ya fahimci laifin Baaba ne gudun kada yaja Mata raini sai yace"Laylerh duk lokacin da Ka kasance a karkashin wani to fa dole sai Kayi hak'uri bare ke da duka duka bai fi shekara daya da rabi bane ya rage miki Ki gama makaranta Ki bar gidan nan Ki tafi inda girka mika za'a yi ba kece zaki girkawa wasu ba don haka Ki Kara hak'uri ".yana Kai karshen zancen shi ya fita a kitchen din ita ko Kai ta girgiza ta rasa meyasa Baaba bata ji bare gani akan Auta ko don ita ce kadai Yar su sai Allah..

A bangaren su kuma sun San malam ba shiga kitchen yake yi ba shiyasa basu boye kulan da nisa ba..

Ganin ba'a taba abincin ba sai ta nemo plate ta diba sannan ta koma daki school bag nata ta bude ta Ciro lacasera da ta saya Tun a school ta sha da doyan sannan ta maida plate din kitchen ta dawo ta kwanta, har bacci ya Fara fisgar ta taji an banko kofar da karfi bude idanun ta da suka yi nauyi sannan suka koma kalar ja tayi Tun tana kallon wacce ta bude kofar dishi dishi har ta kalli Auta tsab nan taja dogon tsaki sannan ta juya daya bangaren zata cigaba da bacci" Amina Kika yiwa tsaki ba ni ba".da sauri ta tashi jin muryar Baaba sai tace"kiyi hak'uri wallahi ban zata ke ce ba Auta Na gani".

"Don Auta ce sai Ki Mata tsaki Ince gidan uban ta ne ba uban Ki ba". Kadan ya hanata bude baki tace taga dai don ita ake tallafa musu sai kuma ta fasa don zasu ce fallin makaranta ce" Baaba wallahi wannan yarinyar asiri ta yiwa yaya Na har ya amince zai Aure ta".

"Dama mutum da dangin sa suka watsar da su me kike tunanin suka yi banda asirin" ta inda suke shiga bata nan suke fita ba ita dai shiru tayi Amma duk kalaman cin zarafin da suke Mata suna kona zuciyar ta"uban Wa yace Ki dauki abinci a kitchen Ki ci?"

"Baaba gani nayi ba a mini iyaka da abinci a gidan nan kuma fa Tun Na safe ne ba'a ci ba shiyasa naci gudun kada ya baci a zubar".

" in an zubar din nace tsohon Ki ke shefene?"ido ta rintse tana jin zafin yadda suke zagan mata uba da ya rasu hakan yasa ta kwanciya tare da basu baya sai Auta ce ta Fara danna wayar ta tana fad'in "tunda kin raina Baaba Bari Na Kira shi yaya nasan Ai baki isa Ki raina shi ba". Tana kaiwa karshen zancen ta ta Fara dialing number'n shi Laylerh ko a zahiri sai ta nuna ko a jikin ta a badini kuma addu'a take Allah sa kada number'n ya shiga in kuma ya dakatar da ita daga zuwa makaranta fa..aiko tayi sa'a wayar Na ringing yadda yake ringing haka zuciyar Laylerh ke bugawa ba jimawa ya amsa wani mashahurin farin ciki ne ya lullube Auta ganin Tun yaushe take kiran shi baya dagawa kuma bata minti talatin bata Kira shi ba Amma sai Gashi ya daga tana hararar Laylerh tace" Assalamu Alaikum "bata jira amsar shi ba taci gaba da fad'in" yaya karar Laylerh Na kawo maka duk gidan nan yanzu ba wacce take tsoro sai ma rashin kunyar da take yiwa su Baaba tana ji da kanta ita a dole Kai zaka Aure ta".tana kaiwa karshen zancen ta ta jira amsar da zai bayar sai taji shiru nan ta Fara fadin "hello,hello kana ji Na?" Shiru fahimtar ita daya take

magana sai ta katse kirar Haba me Laylerh zata yi banda wasewa da dariya Harda shewa tana daga daga kafa da kuma tafi tana nuna Auta da hannu..

A can bangaren Umar Farouq ko ya dawo gida don ya huta kwance yake daga shi sai vest da three quarter ya dauki wayar zai yi Kira sai kirar Auta ya shigo mistakenly yayi receiving jin abunda ta Fara fadi sai ya jefar da wayar yana dogon tsaki a zuciyar shi yake fad'in "wasu mutani basu da tunani ina ruwa Na da family affairs nasu yaushe ma suka San ni da zasu fada mini damuwar su" mita ya Riga yi shi daya kan cewa basu da sirri kuma tunda basu daura auren ba me nashi da ita shiyasa fa lokacin da yake gidan su don rashin son manna mutum a jiki in sun shiga dakin shi yake tada hauka Autar ma yana daga Mata kafa ne kawai don ita yarinya ce..

In ran Baaba dubu to duk ya baci da dariyar da Laylerh ke yi bata taba kawo muguntar yarinyar ya Kai haka ba shiyasa cikin bacin rai ta dubi Laylerh tace"in nice Na haifi Auta sannan Na amsa suna Na sai Na wargaza auren Ki da Umar Farouq Na aura mishi Auta".

Comment

Share

©Hafciey Musa[1/25, 5:41 AM] Hafciey Musa😘: *□LAYLERH□*

(The prettiest emerald)

31

Bayan shekara daya da rabi

Abubuwa dayawa sun faru cikin shekara daya da rabi da suka gabata,akwai Na farin ciki da kuma kishiyar haka..cikin abubuwan bakin cikin da suka faru Harda

mutuwar tsohuwa Dadda Wanda ya jijjiga ahalin ta sosai har Dada tazo sanda aka yi arba'in ta koma kuma kan ta koma taje har gidan Baaba wajen Laylerh..

Kwance take a dakin ta ta kifa book a kirjin ta don karatu take yi saboda yau ne last pepper'n su tunanin abubuwan da suka faru cikin shekara daya da Rabin nan take yi inda gaba daya zaman gidan Neman fin karfin ta yake Musamman yanzu da Auta ta gama makaranta, har ila yau kuma Umar Farouq bai sake Kiran ta ba shiyasa ma suka koma Mata gori kan cewa ya guje ta dama ina zai kaita wannan dalilin yasa ta koma zaman daki.. takan fahimci yana Raye ne ta hanyar malam in sun yi waya da Abban shi Wanda shima sai ya dauki lokaci yake kira hakan ya sata fahimtar ahalin basu son takura, taje yola har sau biyu sannan Aunty'n ta ma tazo jalingo lokacin rasuwar Dadda tazo ta'aziyya daga nan kuma sanda tayi sati biyu kan ta koma..ganin lokaci Na kurewa sai ta mike ta nufi toilet wanka tayi sosai cikin shekara daya da Rabin nan ba karamin sauyawa tayi ba don yanzu ta cika cikekkiyar budurwa kallo daya zaka Mata ta burge Ka.. tana fitowa Tasa rigar sign out nata Wanda yake fari sai skirt baki da kuma half sunnah nan ta daura after dress akai, don saurin da take har ta manta wayar ta sai da taji yana ringing sannan taja tsaki ta koma dakin nan ta dauka sai taga foreign number ne

"Assalamu Alaikum ".

" Wa'alaikisalam "ya amsa Mata nan ne ta shaida Mai kiran nata" ina kwana "tace da shi karkashin zuciyar ta ko tana mamakin kiran ta da yayi don cikin shekara daya da Rabin bai taba kiran ta ba sai dai ya Mata transfer'n kudi har sau biyu.." Yau zaku yi last pepper ko?"ya tambaya ba tare da ya amsa gaisuwar da take mishi ba"in sha Allah ".daga nan shiru ne ya biyo baya a bazata taji yace" congratulations".kamar yadda ya Mata tambayar a bazata haka ita ma tayi murmushi a bazata Wanda bata San dalilin yin shi ta ba tana mamakin yau kuma lafiyar shi yake wani kula ta "thank you" tace sai shiru ya sake bin baya hakan ne ya tabbatar Mata shi din ba gwanin surutu bane shiyasa sai ya dau lokaci yake iya tuna abunda zai fada, "my regards to malam"katse kirar yayi ba tare da ya sake cewa komai ba ita ko bin wayar da kallo tayi tana tabe baki tace duk Kai daya mutum ne Wai baka isa fahimtar halin shi ba nan ta mike ta fito zuwa falon tace"malam yace Na gaishe Ka"

"Shi Wanda ke gaishe shin bai da suna ne?" Baaba ta tambaya. Baya ta juya musu tana wani shu'umin murmushi tace

" Umar Farouq ".sannan ta nufi daki don ta tabbatar duk kallon ta suke yi har shi malam da Kwanaki ya shiga damuwa don rashin kiran ta da Umar Farouq din ke yi

" kaji yarinyar da rashin kunya Ai ni tunda naga uwar ta tazo nasan ruwa bata tsami banza wani asirin ta kawo Mata shiyasa Yaron nan hankalin shi ya sake dawa Gare ta".Baaba ta fadi"yanzu don Allah me amfanin abunda Kika yi? yarinyar nan fa ta Fara gano akwai abu a zuciyar Ki fa".yace yana girgiza Kai don shi tsam bai San gaba da gaba ta fadawa Laylerh cewa zata aura mishi Auta ba kuma shima kullum bin shi take kan ya bata batun auren su ya hada da Auta "yo in Kai baka son yarinyar nan ni ina son ta,duk Wata wahalar Umar Farouq mu muka yi in sakayya ce mu ya kamata ya sakawa Amma haka kurum yarinyar da bata San hawa ba bata San sauka ba za'a aura mishi".

"Dama ita din matar sa ce sannan batun auren Auta sai naga yadda zai Aure ta tunda uba ke bada Aure ha uwa ba,ke ko kunya baki ji yadda kuka sa yarinyar nan a gaba cikin gidan nan Ko tari bata isa tayi ba Bayan Ku ke cin arzikin ta a yanzu".

" to wallahi in dai kan auren Auta da Umar Farouq ne sai dai mu rabu don in ina Raye ba zai auri yarinyar can ba"ta fadi tana hararar shi"tunda haka Kika ce to ina Mai tabbatar miki zaman Ki ya kusa zuwa Karshe a gidan nan".yana Kai Aya ya mike ya fita Auta da ke zaune tana jin zancen iyayen nata ko sabuwar tsanar Laylerh taji ganin iyayen ta Na shirin rabuwa a silar ta.

Laylerh dake labe tana jin su hawaye ta share da Bayan hannun ta tana Jan hanci lallai lokaci yayi da zata bar gidan nan kada bayin Allah su rabu a dalilin ta,sannan Umar Farouq da suke tada jijiyoyin wuya a kan shi Allah ya sani ba ko digon son shi a zuciyar ta kawai don ba yadda ta iya ne tunda ta tabbatar shi zata aura dole wani abun ta rungumi kaddara Bayan wannan ita har yau Naseer take so duk da yanzu bata jin son shi kamar da..daki ta shiga nan ta karasa shirin ta sannan ta fito ta wuce su, sanin ko tayiwa Baaba sallama bata amsa Mata...

Bayan sun gama pepper karfe uku sun hada dinner a school din nan ta Kira malam ta shaida mishi cewa ba yanzu zata dawo ba zata Kai karfe biyar nan yace Mata ba matsala.. Party yayi party maza da Mata sai rawa ake ga Kayan ciye-ciye iri iri tana can zaune a gefe sai murmushi da kuma vedio take musu har bata San magrib yayi ba don sun sha'afa..da sauri ta dauki back nata sannan ta fice tana yiwa course mate nata sai da safe,sanda ta fito titi ne ta fahimci har an idar da sallah a masallacai nan zuciyar ta ya Fara bugawa tana fargaban abunda zata tarar a gida..

Da kyar ta samu keken kasuwan yelwa nan ta shiga sai addu'a take, a junction aka sauke ta nan ta Fara jiran keken da zai shiga ciki..

A can gida ko ba Wanda ya damu da rashin dawar ta don malam baya nan wayar Baaba ce tayi ringing "Auta Kinga wannan number'n kamar ba ta kasar nan bane".

" to Ki daga mana kiji ko wane ne".Auta ta fada cikin daga murya da yake tana kitchen ne Baaba ko Na falo"Assalamu Alaikum "amsa sallamar Umar Farouq yayi jin shine sai tayi wani shu'umin murmushi sannan suka gaisa,sanin halin shi Na rashin son dogon magana sai tace" Yauwa nikam Laylerh ta sanar da Kai inda taje ne?"

"Laylerh kuma?" Ya tambaya yana kwabe fuska kamar a gaban ta yake"Ehh Tun safe da ta fita har yanzu bata dawo ba da yake ba Wanda take tsoro duk gidan nan shiyasa Wata Rana sai Bayan i'sha take dawa".shiru yayi bai ce komai ba sai suka yi sallama..

Wani keke napep ne yazo zai shige sai kokarin tarewa take yaki tsayawa har sun Dan gangara sai taga ya tsaya da wuri ta bi shi sai ganin malam tayi da fuskar confusion ya kalle ta"Laylerh daga ina kike?"shiga keken tayi Bayan Mai keken ya Fara tafiya sai tace"wallahi malam ban San cewa magrib tayi ba sai da Na fita a makaranta kuma Tun dazun nake tsaye a nan ban samu keke ba".ya sani gaskiya ta fada don ta k'ofar makarantar su yabi kuma yaga wasu daliban a lokacin suke fitowa shiyasa bai ce komai ba har suka isa..ita ce ta Fara shiga Baaba Na ganin ta tace"to Hala Umar Farouq kam bazawara zai dauka don Na fahimci yawon karuwanci Kika Fara".banza tayi da Baaba ta nufi daki..

A bangaren Umar farouq Yana katse kirar ya Kira malam Bayan sun gaisa sai yace"ance yarinyar nan zasu gama jarabawa yau?"

"Kwarai haka ne Bayan sun gama paper ma suka hada bikin su Na dalibai har Laylerh bata samu dawowa da wuri ba saboda yamma in yayi Ana wuyan machine Na anguwan mu,daga karshe dak sai mashin da na dauko ne yazo sannan ta samu ta shiga muka karasa gida... Shiru Umar Farouq yayi can sai yace" sai da safe".da wuri malam yace "Mai daki nace ta sanar da Kai cewa bata dawo ba ko,Umar Farouq kada Ka kasance cikin mutanin da suke saurin karban zance akan Laylerh ba tare da sanin Mai fada din bai son Ku tare ba,shekara biyu da rabi da Laylerh tayi a gida Na wallahi Na fahimci tana da tarbiya don haka in har kana son ta Ka daina karban jita jita sannan Mai daki Na tayi haka ne don wani son zuciya nata kuma

koda a gaba ita ko Auta zasu fadi maka zance akan Laylerh kada Ka dauka". Shiru yayi sai can suka yi sallama..

Washe gari ko shiri tayi don tafiya makaranta karban clearance nata sai Auta ta sha gaban ta Baaba ko cewa tayi

" Wato duk iskancin da Kika yi jiya bai ishe Ki ba yau ma fita zaki yi?".bata tanka ba sai Auta ce tace"kin San Ai ta raina Ki Bari Na Kira Wanda ya isa da ita".nan ta Fara dialing number'n Umar Farouq Amma har missed call shida bai dauka ba nan ta fice zuwa makaranta abun ta..

Abuja

Bude gate Na gidan security yayi nan Sadiya ta jefa hancin motar ta cikin gidan don Alhaji M wakili yace kada a sake Mata iyaka da gidan kuma Tun zuwan ta wancan lokacin bata sake zuwa ba sai yau..Bayan ta gama parking sai ta shiga a falon kasa ta tarar da Aunty Hauwa "manyan baki Sadiya idon Ki kenan sai kace Mun miki laifi". Zama tayi tana sake fuska tace" Ai ko kun mini laifi Hajiya don zuwa Na karshe nace muku an mini barazana Amma ba Wanda ya sake Kira Na ya tambayi ya Na kare shiyasa sai naja jiki Na daina zuwa".ta fadi Amma can karkashin zuciyar ta a headquarter din su taji Ana cewa saura sati biyu Umar Farouq ya dawo don ma har ya wuce lokacin da aka dibar mishi shiyasa tazo taji Dahir.

"Kwanaki Sadiya kina raina naso kiran Ki to sai Na samu labarin zaki tafi Cameron kuma aikin naku gani nayi kuna dadewa kan Ku dawo".Hajiya ta fada tana addu'ar Allah sa hakan ce

"Ayya Ai ban dad'e a Cameron ba Wata Na shida ne kawai".hamdala Hajiya tayi a zuciyar ta jin zancen ya zauna sai tace"Allah sarki ya yarinyar Ki?"lafiyar ta kalau Umar Farouq kam har yanzu shiru".

"Kin San Umar Farouq din ne ba Wanda ya isa sanin ina yake don yanayin aikin Ku to mu dai yace mana daga Singapore sai ya shige Switzerland to yana gama aikin shi sai ya wuce Saudi domin yin umra Amma in sha Allah nan da sati biyu zai dawo".

Yalwataccen murmushi tayi tace" Allah dawo da shi lafiya".Ameen..bata wani jima ba tunda taji abunda take so nan ta Mata sallama sannan ta koma gidan ta..

11pm

Kwance take kan Italian bed nata tana rungume da Yar ta,taji alaman an kawo Mata hari..a can wajen gate kuma wasu ne suka kawo Mata hari nan aka yi ma security duka tare da daure shi sai suka shiga gidan,guards nata ko musayar wuta suka Fara da su Amma Allah bai samu nasara ba saboda wadanda suka kawo harin sun fi karfin su shiyasa suka ji musu ciwo wasu ko an harbe su nan suka nufi cikin gidan..

Sosai jikin ta ke rawa nan ta dauki Yar ta Tasa a kafada ta rasa ina daya zata shiga don ba karamin tashi hankalin ta yayi ba..a can falon ko dakunan yan aiki suka shige rufe su da duka suka yi sannan suka daure su Amma basu musu wani abun cin mutunci ba tunda dama ba wurin su suka zo ba..ta fito falon kenan suka harbe ta da bindiga inda Allah yaso ta a hannu ne da wuri ta koma daki tare da rufo kofar nan ne ta tuna da underground building dake gidan ta sai ta shige ciki Yar ta sai kuka take yi..ta Bayan gidan ta fice nan ta Fara tare keke da kyar ta samu Kai tsaye gidan oga'n su ta nufa Amma sai securities suka Hana ta shiga kasancewar shi Babban mutum ba Kai tsaye zaka shiga gidan shi ba sai ya San da zuwan Ka bare yanzu da yake dare..wayar shi tayi Kira har sau uku bai dauka ba nan securities din suka Mata korar kare duk da tace da su tana aiki a karkashin shi..hawaye take yi tana jinjina rashin imanin wasu yanzu ko don Yar ta ba za'a taimaka Mata ba Gashi bata da kowa a garin, ta kuma rasa ina zata ga hannun ta sai bleeding yake yi nan take gidan su Umar Farouq ya fado Mata sai ta nufi can..

Nan ma security yaki bude Mata sanda Wanda yake duty da safe ya Gan ta to shi ya Santa cux duk zuwan ta shine a gate ganin yadda take Zubda jini sai ya Fara dialing number'n Alhaji.. "Hello Sir wannan abokiyar aikin oga Umar Farouq ne tazo da alama hari aka Kai Mata don hannun ta Na bleeding".

" let her in".ya fadi yana kunna hasken dakin tare da Daukan glass nashi a bedside ya zura takalmin shi dake bakin gado "Alhaji lafiya kuwa?" Aunty Hauwa wacce hasken da ya kunna ne ya tashe ta tayi tambayar"wallahi ban sani ba ance Sadiya ce a gate?".ya bata amsa lokacin da yake fita a dakin ita ko agogo ta duba"to me tazo yi a wannan lokacin sha biyu fa ya wuce ".mikewa ita ma tayi ta dauki hijab cikin wardrobe ta daura kan sleeping dress nata tabi Bayan shi da sauri..

Har bakin gate ya nufa tana biye da shi a wajen ne yaga Sadiya tsaye Yar ta ko Na rike da kafafun ta kallo daya zaka musu su baka tausayi" subhanallah Sadiya me ya faru?"ya tambaya lokacin da yaga hannun ta ita ko kokarin bashi amsa take sai ta yanke jiki ta fadi don ta Zubda jini sosai"Kinga Hajiya daga ta Bari driver yazo sai mu tafi asibiti ".a take aka tada driver dake bacci nan aka sa Sadiya a mota da Yar ta suka nufi asibiti da yake yana da immunity..taimakon gaggawa aka Fara bata inda suka yi nasarar cire bullet din tare da Mata allurar bacci yarinyar ta ma hawa gadon tayi ta rungume mamar ta don irin yara marasa son mutanin nan ne..ganin asibitin akwai tsaro sai Alhaji da Hajiya suka nufi gida Bayan sun tabbatar ba abunda zata bukata..

A Washe gari Abba yasa Aunty Hauwa Kai Mata breakfast ba don ran ta yaso ba ta nufi hospital din tako yi sa'a Sadiya bata bacci sai bandage da aka daura Mata a hannu tana rungume da Yar ta kamar za'a kwace Mata ita" sannu Sadiya ya jiki?"

"Da sauki sosai Hajiya Na gode da dawainiya". Zama Aunty Hauwa tayi a bakin gadon tana taba temperature'n Sadiya jin jikin ba wani Zafi sai tace" Alhamdulillah kin Fara samun sauki".

"Eh wallahi".

" to garin yaya ne hakan ya faru?"

"Wallahi Aunty ji kawai nayi an kawo mini hari da kyar Na tsira Amma kuma sun harbe ni a hannu".ta karisa zancen tana kallon hannun ta" Allah kiyaye gaba"Aunty Hauwa ta fada nan ta gabatar musu da breakfast a zuciyar ta ko cewa take suna gama ci zata tattara tayi gaba ba zata sake dawa asibitin ba..

Saudi

Shiru yayi yana sauraron jawabin da ake koro mishi na harin da aka kaiwa Sadiya sai da azo gaban da aka ce Ai gidan su ta nufa nan take ya katse kirar ya Kira Abba bugu biyu ya dauka Bayan sun gaisa sai yace" meyasa zaku karbeta Abba Bayan duk lokacin da abu makamancin wannan ya faru ko by what time ne yaje agency Ana bashi maximum protection, me yasa bata je can ba ".

" Umar Farouq Wai yaushe zaka Fara yarda da mutani Ka kyautata musu zato ne yarinyar nan dai kasan bata da kowa a garin nan".

" Abba Ai zaman kanta take yi taje ta nemi taimako wajen wasu mana".

"Look ba Kai zaka fada mini abunda ya dace da Wanda bai dace ba fa Ince taimakon Ka tayi".ya fadi cikin bacin rai

" Amma...".

"In Wannan maganar ce ta saka Kira sai Anjima" Abba ya fadi tare da katse kiran shi ko iska ya nausha ya rasa dalilin da yasa dangin shi ke kyautatawa kowa zato daga nan Aunty ya Kira..

Abuja

To da taga kiran shi sai ta daga Kai ta kalli Sadiya ganin hankalin ta duk Na kan Yar ta sai tayi receiving "Hello Umar zamu yi magana Anjima yanzu akwai abunda nake yi ne". Jin ta ambaci Umar sai Sadiya ta dago Kai tana kallon ta

" A'a yanzu nake son muyi magana Wai akan me zaku taimaki Sadiya wannan fa duk shiri ne".

Kai Aunty ta daga ganin yadda Sadiya ta kura Mata ido sai tace"ba nace maka zamu yi magana Anjima ba yanzu ina asibiti ".

" Alhamdulillah bata waya"

Ita ko Sadiya jikin ta ya bata ance Aunty ta bata waya shiyasa tace

"Aunty bani wayar".Kai Aunty ta girgiza Mata alamar a'a don ta San Umar Farouq da Dan banzan zuciya yanzu ya Mata wankin Babban bargo

"Allah Ki bani"

ta fadi tana mika hannu cikin sanyin jiki Aunty ta mika Mata wayar

"hello".

"Sadiya Ardo ban gargade Ki da shiga lamarin gidan mu ba,ina ruwan su da harin da aka Kai miki in anso a kashe Ki sakayya ce Allah ke nuna miki banda munafurci me ya hanaki zuwa gidan oga ko kuma gidan kawayen Ki sai Ki nufi gidan mu da can uban Wa ya saki Neman aikin inda baki da yan uwa". Shiru tayi tana sauraron shi sanda ya Kai Aya tace" Ka gama? Umar Farouq Ka bincika naje gidan oga securities suka Hana ni shiga sannan Ka tambaye shi ko bai samu missed call Na har uku ba a Daren jiya,sannan batun kawaye ban San wane ne ya turo mutanin nan ba taya zanje Gare su sannan wadanda Na yarda da su gidan su ba tsaro,ganin gidan Ku akwai tsaro sannan ga karamar yarinya a hannu Na shiyasa Na nufi can Amma ba komai Kayi hak'uri in sha Allah gaba ba Zan sake ba,ban taba jin zafin rashin iyaye ba sai yau Ashe har zaka iya mini gorin iyaye kasancewa ta marainiya Na gode fa".tana gama fadin hakan ta katse kirar tare da fashewa da kuka Mai cin rai ta rasa dalilin da yasa baya taba kyautata Mata zato cikin kuka take fad'in "Aunty me laifin marainiya don ta nemi taimako cikin dare so yake da mutunci Na naje hotel Na kwana ne ko me gaskiya Umar Farouq zuciyar shi Na dutse ne,ni Tun jiya nake kukan rashin yan uwa yanzu dubi gani kwance a asibiti ba Mai taimaka mini sannan ga 'ya ta ina Na San Zan Kai ta a kula da ita taci gaba da zuwa makaranta har Na warke". Sosai kalaman ta suka shiga Aunty Hauwa tana kuma tausaya Mata a matsayin ta Na ya mace shiyasa ta kira Abba ta tambaye shi ko ta tafi da Yar ta har sai ta warke nan ya amince Mata sai ta dauki yarinyar suka dawo gida tare duk da da kyar ta yarda..

Najeeha ta bawa yarinyar,najeeha Yar tace kuma ta San tafi sauran iya kula da yara shiyasa ta bata ita hannun yarinyar Najeeha ta Kama suka nufi bedroom nata nan ta Mata wanka sai Tasa Mata Kayan yaran Aunty Nana..

Dialing number'n Umar Farouq take yi don auren ta ya kusa kuma tace ya sayo Mata gold a Saudi don sun fi kyau da quality ganin yarinyar zata taba sucket ma wuta sai tace" kul beta zai kona Ki".haka Maman ta ke kiran ta Amma ba Asalin sunan ta bane, a bangaren Umar Farouq ko yayi receiving jin sunan da ta ambata sai yace"wace ce ita?"don in ba karya yayi ba haka Sadiya ke kiran ta"Yar aunty Sadiya ce dazun Mommy ta dawo tare da ita daga asibiti ".hmm kawai yace sannan ya katse kirar yana tunanin dole ya dawo Nigeria kafun Sadiya tayi something stupid..

Bayan kwana biyu

Yau ake shirin sallamar Sadiya don taji sauki sosai yanzu haka ta biya kudin magunguna ne haka kawai take tausayin kan ta da kan ta..

Tun Bayan da suka kaita asibiti Abba bai sake zuwa ba sai yanzu da ya fito anguwa sai kawai ya yanke shawarar ya leka ta..tana zaune a bakin gado ya same ta nan ta durkusa tana gaishe shi" lafiya ya jiki"

"Da sauki sosai".

" Masha Allah sai gida ko?"

"Eh ga takardar sallamar ma an bani". Ta fadi tana kallon takardar hannun ta shi ko kallo daya ya Mata sai ya juya ga doctor da ke tsaye" doctor naga gaba daya fuskar ta a kumbure yake kuma ace an sallame ta?"gyaran murya doctor yayi yana murmushi yace"Alhaji Ai kwana kuka take wannan kumburar da kaga fuskar ta yayi don kuka ne sai dai Ka tambaye ta dalili".ya Kai karshen zancen shi yana juyawa ya fice Abba ko waje ya samu yana duban ta don yana sane yayi tambayar kallo daya ya Mata ya fahimci kuka ne ya kumbura fuskar Amma sai ya tambayi doctor da yake he is a straight forward person sai yace"Sadiya kukan me kike yi".

"Babu tace tana murmushi" look Ki dauke ni kamar uba fada mini mene ne"wallahi Abba tsoron Komawa gida Na nake yi".murmushin su Na manya yayi yace"banda abun Ki ba sai Ki saya wani gidan tunda Allah ya Hore miki ko Ki Kama haya ba".

"Abba ba sayan gidan ne bana so ba rashin tsaro din nake gudu don wancan Karon ko da nayi reporting a agency mu aka bani securities to fa ranar da suka shiga duka suka musu wasu ma an karbe su ni zaman abujan ne ma ya fita a raina da ace ina da iyaye a Raye da Na koma wajen su Na hakura da wannan aikin".

" Allah sarki ke marainiya ce?"

"Ehh iyaye Na dukkan su biyu sun rasu a hatsarin mota kuma ba yadda za'a yi Na iya rayuwa da hannu daya tunda ba haka Allah ya halicce ni ba sannan ga yarinya a gaba Na ba Zan iya daukar dawainiyar Kai Na ba ma bare nata".

" yanzu ke matsalar Ki waje Mai tsaro ne?sai Na nema miki".

"Abba duk yadda kake tunanin aikin mu yafi haka ni bukata ta Na koma gaban iyaye Na ne ko Na sati daya don nan da sati biyu Zan tafi aiki London Gashi banda iyayen".numfashi yaja sannan yace" tunda kin kusa tafiya aiki kizo Ki zauna da mu Na sati biyu kafun hannun Ki ya warke sai Ki Kai complain agency'n Ku".

"Abba kana ganin Umar Farouq zai amince?"

"Kada kiji komai ni nace kizo yanzu Zan bar miki mota daya da driver". Har kasa ta durkusa tana godiya shi ko fita yayi yana sanar da Aunty Hauwa zuwan Sadiya a waya...

masu comment ina ganin comment naku ina kuma godiya sosai da sosai,wallahi lokaci ne ban fiya samu ba shiyasa bana replying comment naku da godiya ayi mini uziri

Comment

Share

©Hafciey Musa

[1/25, 5:41 AM] Hafciey Musa😘: *LAYLERH*

(The prettiest emerald)

Jin abunda Abba yace da baya baya Aunty Hauwa ta koma har kafar ta Na Neman kasa daukar ta,dafe gado tayi tare da zama a Kai"Sadiya a gidan nan Wai me Alhaji ke nufi ne?".share gumin jikin ta tayi sai Umar Farouq ya fado Mata a rai hannun ta har rawa yake wajen Neman number'n shi,tana dialing tana addu'ar Allah sa ba abunda yake yi Ai ko tayi sa'a don shi da wuya yan gidan su su Kira shi bai daga Na"Assalamu alaikum Umar kana jin danyen hukuncin da Abban Ka ya yanke Sadiya fa yace ta dawo gidan nan".shiru tayi tana sauraron abunda yake fadi can suka yi sallama tana Mai jin sauki a ran ta..

A can asibiti kuma Sadiya ta gama hada komai nata inda driver ya dauka ya Kai mota don yanzu ta zama abun tausayi kuma kallo daya zaka Mata Ka fahimci tayi Dana sanin abubuwan da ta aika ta a baya,ko da suka iso gidan bude musu gate security yayi nan ne driver yasa hancin motar cikin gidan yana gama parking ta shege ciki.ba kowa a falon sai yan aiki nan ta zauna tana jiran saukowan yan gidan Amma shiru har ta Kai minti goma wanda ta tabbatar yan aikin su sanar da su shiyasa tayi tagumi da hannun ta Mara ciwon tana hawaye Wai yau ita Sadiya ce ta zama abun tausayi har zata zo gidan wasu ayi banza da ita...can Najeeha ta sauko sai ganin ta tayi tana hawaye"Aunty Sadiya sannu da zuwa ya jiki".

"Da sauki". Ta amsa Mata tana goge hawayen idon ta" kizo Na Kai Ki dakin Ki".mikewa tayi don zaman falon ya gundure ta Gashi ko wace Mai aiki in ta fito sai su zuba Mata ido kamar kauyawa,a second floor ta bude wani daki ta shige"bismillah shigo".Kai Tasa a dakin tana Dan dube dube daki daya ne Amma babba sosai ne don Bayan gado a can gefe an sa set Na kujeru har ma da dinning sannan akwai karamin kitchen komai dai Masha Allah Yadda ba zata takuru ba"yanzu Ki zauna Ki huta Anjima Zan kawo miki beta".da Kai ta amsa nan najeeha ta rufo Mata kofa direct dakin Hajara ta nufa a can ko ta tarar da Yasmeen don dama su uku suka rage basu yi Aure ba kasancewar mahaifin su Na aurar da su da wuri.."lafiya Ki Najiha zaki fada mana a daki ba ko sallama". Fadin hajara,da sauri ta haye gadon tace"wallahi Hajara Baku ga abunda Na gani ba Aunty Sadiya fa kuka take yi".zaro ido Hajara tayi"Najiha kiji tsoron Allah".

"Har wallahi fa tagumi tayi tana ta hawaye".

" lallai duniya ta karantar da ita".Cewar Yasmeen da bata fiya magana ba"wallahi ni abun dariya ma ya bani".Najiha ta fada tana dariya tare da rufe bakin ta kada Sadiya ta jiyo ta"Kun ga Ku tashi muje mu gani".Cewar Hajara"Ashe zamu sha dariya"..duk mikewa suka yi a bakin kofar dakin suka ci Karo da Aunty Hauwa"Sadiya sa'ar Ku ce Ince sa'ar yayan Ku ne in shine a matsayin ta kun Isa Ku Fara tunanin yi mishi haka ne, sannan ke Yasmeen da akewa ganin kin fi su nitsuwa Harda ke a cikin ayarin zuwa".duk sadda Kai kasa suka yi ba Wanda yace da ita komai"to wallahi Ku kula in Abban Ku yaji sai ya bata muku rai".tana gama fad'in

haka ta fice a dakin duk sai taji ba dadi a ranta don taji duk zancen su"ni wallahi yarinyar ce ba son maganar ta nake yi ba to Amma ya Na iya ta bani tausayi dole naje Na dubo ta".tana tafe take wannan tunanin tare da wasa da yatsun hannun ta har kadan ya rage suyi Karo da Yar aiki"yi hak'uri Hajiya ".

" ba komai laifi nane".wannan saukin kan nata da kuma yadda ta rungumi yaran Hajiya maryam Mai rasuwa yasa har gobe yaran basu taba kukan rashin uwa ba sannan son da take yiwa Umar Farouq ko Salman da ta Haifa bata mishi ko don Umar Farouq din ya kasance Mai biyayya a Gare ta ne sai Allah, knocking kofar tayi jin shiru sai ta tura kofar ta shiga kwabe fuska tayi ganin har yanzu Sadiya kuka take yi"Assalamu alaikum".

"Wa'alaikisalam sannu da shigowa Aunty Hauwa".

" Yauwa ya jiki".ta tambaya lokacin da take zama a kujera"jiki alhamdulillah ya dawainiyar Beta".

"Masha Allah waje ya miki ko duk da kin San gidan Ka gidan Ka ne dole zaki ji kina takure".

" Laaa ba komai wallahi waje yayi".daga nan shiru ne ya biyo baya sai Sadiya da ko wani Bayan seconds sai tace hmmm Tun Aunty Hauwa bata damu ba har tace"lafiya kuwa".ajiyar Zuciya tayi tace"kawai dai naso da iyaye Na suna Raye".

"Nikam Sadiya baki taba ciwo bane sai wannan Karon?"

"Ina yi mana akwai lokacin da ulcer ya Sani a gaba har wasiyya Na bayar".

" to duk wancan lokacin baki taba tunanin ina ma ace iyayen Ki Na Raye ba sai yanzu".shiru tayi har kamar ba zata amsa ba sai kuma tace"saboda wannan Karon abun yayi tsanani,Kinga ba hali naje gida Na har sai an gama binciken da ake yi sannan ga beta Wa zai ke Mata shirin makaranta duk ma ba wannan ba ko ATM banda shi Wa zai je makarantar su ya sayo Mata wani uniform da books sannan dubi fa Na zama Mai hannu daya ".numfashi Aunty Hauwa taja sai tace" yanzu mu bar zancen nan Ki dauka kaddara ne Bari a kawo miki abinci ".

" wallahi da an bar abincin nan baki Na ba dadi".

"Ohk to Zan sa a hada miki coffee".

" wallahi da yafi kam don nayi warming ciki Na".

"Ki dauki dakin nan matsayin gidan Ki duk abunda kike so zaki yi sannan in naje kitchen Zan sa a kawo Miki Kayan abinci in case in kina da bukatar fast food sai Ki dafa a nan in kuma Mai nauyi kike bukata zaki iya shiga kitchen dake nan second floor kan yan aiki su fita,batun beta kuma kin fi son privacy ne ko Na turo miki Mai aiki?"

"Ina privacy ga mutumin da komai sai an taimaka mishi a turo mini da ita kawai sannan ina godiya sosai da karancin Ku a Gare ni Amma kuma tsoro Na daya kada Umar Farouq ya dawo ina gidan nan".

" banda abun Ki Sadiya mutumin da ba tabbacin abunda ya fada gaskiya ne me zaki ji tsoro sannan Ai kince nan da sati biyu zaki tafi aiki Singapore ".

" to Ai Aunty sai hannun ya warke".

"In sha Allah zuwa lokacin zai warke"

"Allah yasa don ba Zan so Umar Farouq ya tarar da ni a gidan nan ba". Ameen kawai Aunty tace don ranta Na soyuwa in Sadiya ta nuna kamar Umar Farouq din baida imani kenan ta Gaza wajen mishi tarbiya..

Husna Yar aikin ta ta Kira kuma duk cikin yan aikin ba wacce ta Kai ta iya gulma ta San komai ta gani zata zo ta shafa Mata kuma ita tsam bata yarda da Sadiya ba shiyasa zata tura Mata Husnah nan tace taje dakin Najeeha yarinyar Na bacci ta dauke ta tace to...

**

Zaune take a falon ta Ana Mata tausa yanzu da zuwan ta Taraba sati biyu kenan, gefen ta amincecciyar Yar aikin ta ce sai Ummi,Tun da tazo take Neman Mai kitso Amma bata samu ba kuma ita bata fiya zuwa saloon ba sai a can abuja wancan satin an kawo Mata Mai kitso to hannun Mai kitson bai karbe ta ba gaban gashin ta ya yanke.. Rabi Yar aikin ta Kawar Ummi ce kun San ta da kwashe-kwashe Ai to dama Mommy Sulaiman din tana da bukatar kubewa da kuka bushesshe masu kyau sai tace Mata Ai akwai Kawar ta da ta taba bata Amma bata San a ina ta saya ba zata tambaye ta,ko da aka Kira Ummi a waya jin babbar mace ce kuma Mai kudi ke so sai tace zata kawo musu har gida Ai jiki Na zikiri ta sayo musu shine yanzu ta kawo Bayan Hajiyar ta duba sai tace" gaskiya suna da kyau".tabe baki Ummi tayi a tunanin ta matar zata yi ta yabon ta ne sai taga ba haka ba duk da ta fahimci matar Na ji da kan ta"Rabi dauka Ki Kai mini kitchen kuma Ki Adana".to tace sannan ta mike Bayan ta dawo ta zauna ne sai tace"Wai nikam ba wacce Kika Sani Wanda ta iya kitso sai matar wukarin da ta mini ranar?"

"Ehhh Hajiya Ai ta iya kitso".

" Na San ta iya hannun ta ne bai karbe ni ba Wata nake so".

"Hajiya wallahi akwai yarinyar da Na Sani ta iya kitso sosai sunan ta laylerh in kina so Zan kawo miki ita har gida". Laylerh ta iya kitso sosai Tun farkon zuwan ta jalingo sai dai bata nunawa ne iyakaci ta kamawa Baaba Ummi kuma ta gane hakan ne don a ranar da taje wuni gidan Dadda tayiwa Nabeela kitso Mai kyau

 "Shikenan a turo mini da ita".jikin Ummi har rawa yake tace"daga nan ma gidan su zani in shaida Mata".da ido Momy Sulaiman tayiwa Rabi magana nan ta cire dubu biyar ta bawa Ummi sai Washe baki take don abun dubu biyu ta saya Gashi har ribar dubu uku tayi..keke ta tare sai kasuwan yelwa drop ma ta dauka har ciki ji take yi ba zata bar wannan Hajiyar ba Gashi matar komai nata Na zamani..

"Assalamu Alaikum".tayi sallamar cikin daga murya don kowa ya shaida ita ce tazo" wa'alaikisalam muryar Wa nake ji kamar Ummi ".tana sa Kai a falon tace" Ai ko nice Baaba ".murmushi Baaba tayi don Ummi tayi Wata uku bata leko su ba tace" sannu da zuwa fa".

"Yauwa Baaba Na same Ku lafiya".

" lafiya kalau".wannan halin ta ne rashin rike mutum a Zuciya don Baaba tayi tunanin tunda ta hanata laylerh zumunci ya kare sai taga tsabanin haka don da bai fi sati uku da rikicin su ba tazo shiyasa suka je Mata rasuwar Dadda "ina Auta ne ta kare makaranta ko?"

"Duk suna daki makaranta kuma ta kare tana shirin jona diploma ne".

" diploma kuma Ince tayi Jamb Ai laylerh ma rashin jamb ne ya sata yin diploma".shiru Baaba tayi a zuciyar ta tana tunanin Ai Mai biyawa Auta kudin makarantar ne baya son mace tayi zurfi a karatu su kuma ba zasu iya Daukan nauyin ta har ta kare digree ba"ya Kika yi shiru?"

"Kin San Ai bata ci jamb bane shiyasa zatai diploma".

" Allah sarki".Auta ce ta Fara fitowa tana latse latsen wayar ta ta gaida Ummi sannan ta samu waje ta zauna ba jimawa laylerh ma ta fito kunnen ta sanye da earpiece don kitchen zata"laylerh zo mana ai wajen Ki nazo ".da yake bata kure volume Na wakar da take ji bane shiyasa ta nufi Ummi tana cire earpiece din a kunne ta" sannu da zuwa Ummi ".

" Yauwa laylerh ya gida an kare makaranta sai kuma zaman gida".

"Eh wallahi".

" hmm laylerh am Wata Mata Mai kudi ce take Neman Mai kitso nace Mata kin iya sai tace Na Kai Ki".ta fada cikin sauri sauri da yake haka maganar ta yake "Ayya to Bari Na watsa Ruwa sai mu tafi". Ta fadi tana mikewa" Kinga dawo Ki zauna abun Ki Ai ba yau bane".Komawa tayi ta zauna a center carpet din tana murmushi sai Ummi tace"Baaba kin amince taje".

"Me zai Hana?" Ita Baaba fa bata Ki Ummi ta dauki laylerh su koma gidan ta ba sai tace"Yaron da baya ganin girman Na gaba da shi sannan baka Isa fada mishi abu yayi ba sai yadda ran shi yaso me za'a yi da shi?"Kai laylerh ta sadda kasa don tasan Ummi kuma ta samu abun magana kenan shiyasa taji takaicin sharri da Baaba da Auta ke bin ta da shi"wallahi Baaba in kaga yaro ya raina Ka to baka rike shi tsakani da Allah bane Amma har yaushe kamar laylerh zata raina Ki Ki bar ta".ta fadi hakan ne don laylerh ta fahimci ita tafi son ta tunda ta Lura yarinyar akwai kashin arziki gwara kawai ta dauke ta Baaba ko shiru tayi sai Ummi ta dubi laylerh "Haba laylerh ko Ruwa ba zaki bani bane?" Nan laylerh ta nufi kitchen sai ta kawo Mata Harda abinci tana Fara ci tace"wallahi wannan abincin laylerh ce ta dafa haka take dafa shinkafar ta baya gama nuna lokacin da take gida Na ma Alhaji gagara ci yake har yayi complain ".

" in gaskiya ne Ki daina ci mana".laylerh ta fada a zuciyar ta sanda ta cinye abincin tas ta sha Ruwa tare da yin gyatsa sai ta mike tace"to ni Zan tafi gobe Ki shirya da wuri Zan biya Na dauke Ki kuma Ki kwana Neman irin style da zaki Mata don babbar Mata ce".tana gama fadin haka ta juya ga Baaba"to Baaba sai nazo gobe".su mamakin ta suke yadda in tana magana ko numfashi bata ja Gashi maganar sauri sauri "Allah ya kaimu". Baaba ta amsa Mata nan ta fice laylerh ko daki ta koma don bata Isa zaman falo ba...

Washe gari karfe goma Bayan ta gama breakfast sai ta fito daga ita sai breziya da zani a kirji ta Kai kwano kitchen sai ta zauna a kan kujera tare da daura duk kafafun ta akai ta dauki remote ta Kai Zee world tana kallon maimaicin wani series da bata kalla jiya ba..fitar ta ba jimawa Auta ta fito nan ta dauki remote din ta sauya Tasha zuwa wani Nigeria film.. ci kan Ki laylerh bata ce da ita ba sai wayar ta da ta dauka ganin tana da data sai ta shiga IG..

" Assalamu Alaikum ".suka tsinkayo muryar Ummi daga waje,duk da basu shiri ko Na miskala zarratin sai suka kalli juna tare da fashewa da dariya a daidai lokacin kuma Ummi Tasa Kai a falon" me haka daga gani Na Ku Kama dariya".da sauri laylerh ta girgiza Kai tana hadiye dariyar da yake cin ta sai Auta ce ta hade rai tace"sannu da zuwa mu fa hira muke".Baaba ma jin muryar Ummi sai ta fito Bayan sun gaisa sai ta dubi laylerh "Haba Baaba ya zaki bar ta tana zama da zani a kirji budurwa da ita haka zata je tayi a gidan miji kwana biyu ya koro mana ita Shikenan kuma ta mana asaran hujerar Makka da Jan miyan da muke ci". Zuwa yanzu Baaba ta Fara fahimtar habaici Ummi ke yi Amma in ta tanka ta kuma Ai ba hujjar cewa da ita take shiyasa Auta taja dogon tsaki tana hararar Ummi tayi ciki Baaba ma Bayan ta tabi" Baaba ni a Hana matan nan zuwa gidan nan ta fiya shisshigi".

"Ai in Kinga ta bar zuwa to laylerh ce ta bar gidan nan".

A can falo kuma Ummi matsowa kusa da laylerh tayi cikin son jin gulma tace" ya naga ta miki tsaki Bayan kuma kin girme ta ko dai Baku shiri ne?"

"A'a fa muna shiri mana kawai dai Sim biyu Gare ta" ta fadi tana nunawa Ummi yatsa biyu Wato Auta Nada tabon hankali "to ya naga baki shirya ba".

" nayi wanka fa kaya kawai Zan sa".

"To Ki zabo masu kyau da tsada gidan manya ne baki ga Nima Na sallar da ya wuce Na sa ba".to tace sai ta wuce daki tana gab da bacewa ganin Ummi ta tsinkayo muryar ta tana fad'in" kuma Na tuba a shafa powder da Jan baki kada a fito kamar kullum matar bata son Dotti".naga ta kaina da Ummi ta fada a hankali sannan ta shige daki nan ne Tasa abayar ta baka Mai kyau tare da fesa turare sai Tasa powder kadan sai lipstick don ita ba gwanar kwalliya bace.."Masha Allah kinyi kyau muje ko".fita suka yi Amma basu samu keke ba sanda suka sha tafiya Ummi sai mita take da kyar suka samu tace"presidential lodge zaka Kai mu".Ku shiga yace nan suka shige sai anguwar, duk zaman laylerh a Jalingo bata taba zuwa anguwar ba tunda suka shigo anguwar kuma ta fahimci ta manya ne haka kawai gaban ta ke mugun fadiwa naman saman idon ta rawa yake ga zuciyar ta dake baranazar fashewe ji take kamar Tasa ihu don gaba daya tsikar jikin ta ma tashi yake abunda bata taba ji ba a rayuwar ta..

A kofar wani gida Mai kyau keke yayi parking nan Ummi ta biya shi ita ko laylerh ji take kafar ta ba zata iya tafiya ba ganin tana tsaye sai Ummi taja hannun ta knocking Na gate din suka yi nan Mai gadi ya bude karamin waje a gate din sai ya Gan su"ya dai".

"Me haka malam Ka bude mana kofa Ka tsaya cewa ya dai to ni da kake gani jiya ma nazo kuma Mai kitso Na Kawa Hajiya". Ta fada cikin masifa don a ganin ta Ai ita ma yanzu Yar gida ce ya tsaya Mata rashin mutunci..tsaki yaja sannan ya rufe Dan karamin kofar da ya bude nan ta Fara bubbuga kofar tana fad'in" matsalar Ku kenan talakawa Baku iya samun waje ba".laylerh kam fa ta rasa a duniya take ko lahira

don ji take kamar an cire Mata rai gangan jiki ne ya rage..a bangaren Mai gadi kuma cikin gidan ya Kira yace Mai kitso tazo aka ce ya bude sai ya bude kofar Ummi ko Jan hannun laylerh tayi don bata fahimci ta shiga wani hali ba har kamar zata bankade Mai gadi da duwawun ta don jiki take da shi kuma akwai duwawun nan suka shiga, sa kafar ta cikin gidan sanda taji numfashin ta ya dauke Na wasu seconds sannan ya dawo.. bangaren Sulaiman idon ta ya fara sauka tana yaba kyan gidan nan suka shige falo ba kowa sai Ac dake aiki da kuma TV zama suka yi tana karewa falon kallo"laylerh am ke ma Wata Rana kina irin falon nan ko Wanda ya fi shi ni dai addu'a Na kada Ki manta da ni".

"In sha Allah hakan ba zai faru ba". Ta fada ba tare da sanin abunda take yi ba sai kallon tafin hannun ta da yayi sanyi take yi wannan wani irin feeling ne da bata taba jin irin shi ba..

Ummi ce ta Kira Rabi a waya nan ta fito Bayan sun gaisa sai ta kawo musu refreshments sannan ta nufi dakin mommy Sulaiman ta sanar da ita Mai kitson ta zo..

Sun yi zama kusan Na minti Ashirin har laylerh ta Fara jin takaici sannan aka budo wani kofa inda can Asalin falon ta yake ta fito da sallama" Assalamu Alaikum ".daga ido laylerh tayi don ganin matar daidai lokacin kuma mommy Sulaiman Tasa idon ta cikin Na laylerh a take tace" innalillah".don ji tayi kamar wani abu ya fita a jikin ta.. laylerh ko tana sa ido cikin Na mommy Sulaiman ta mike tsaye tana kallon ta..gaba dayan su ji suke yi a jikin su su din jini daya ne Amma ta ya ya?"

Mommy Sulaiman ba kowa bace face Hadeexa Yaya ga mahaifiyar laylerh sannan ita ce ta saci gold a shagon Abbu Wanda ita ya kamata ya aura Amma ya butulce Mata ya auri kanwar ta Yar yaddikon ta Amina kenan ita da boss nata da basu shiri Tun tana primary school yaran Pendo ne ba tare da sanin su ba..

A take kuma sai nitsuwa yazo musu dukkan su sanin ba Yadda za'a yi laylerh ta kasance jinin ta Amma bata San ta ba duk da rabon ta da gidan su zai yi shekara Ashirin.. Zama laylerh ma tayi sai suka gaisa Amma sai kallon junan su suke "ita ce Mai kitson?" Ta tambaya "Ehhh Ai ta iya sosai" Ummi ta bata amsa don ita tsam bata fahimci halin da suke ciki ba da tayi gulma lokacin hankalin ta Na kan abun ciye-ciye da suka ajiye musu.."Rabi dauko mini cump da kifiya sai man kitso a cikin drower".ta fada cikin Dan daga murya don Rabi Na kitchen "to Hajiya". Rabi ta fada

sannan ta nufi daki ta kawo" Ki zo nan muyi".ta fadi tana kallon laylerh sannan tana jin son yarinyar har cikin ran ta.cikin sanyin jiki laylerh ta mike ta zauna a kujera ita mommy Sulaiman ko filon kujerar ta ajiye akan tiles din,bismillah laylerh tayi lokacin da ta rike kan mommy Sulaiman ita ko sanyi ta ji a ran ta,tsagu tayi Ummi da bakin ta ke cike da abu tace"Ki Mata Mai kyau fa".Kai laylerh ta girgiza tana mamakin halin Ummi sai kace wacce bata samu mijin ta fa yana da Na rufin asiri..

Kitso kanana take watsawa mommy Sulaiman kuma sosai yake kyau ganin sunyi rabi sai Ummi tace"laylerh ni Zan wuce Alhaji zai dawo daga tafiya abincin shi Na ajiye zamu yi waya".

"To Shikenan Allah kawo shi lafiya". Laylerh ta fada tare suka amsa da momy Sulaiman wajen fad'in" Ameen".daga nan momy Sulaiman ta bata dubu uku tayi Na machine nan tayi ta godiya ta tafi..shiru suka yi ba Mai ce komai sai mommy Sulaiman dake Danna waya laylerh so take tace Mata ta ajiye Kai Amma nauyin matar ya Hana ta..

Sun kusa gamawa ne wayar ta ya Fara ringing sai taga kirar daga company ne nan ta daga lissafi suka Fara ganin sun kasa fidda lissafin Mai kyau sai tace ya Mata text in ta gama kitso zata yi calculating nashi haka ko Ka yi..

Suna gama kitso Tasa aka kawo Mata pen da jotter zata copa laylerh tace ta kawo ta Mata nan ne ta cope Mata sai ta Fara lissafi Amma ta gagara ganin haka sai laylerh tace"kawo Bari Na gwada".

"Haba Nima fa Na gagara". Murmushi laylerh tayi tace" Ai jarrabawa zanyi ".

" to Gashi Ki yi in kin gagara zan jira Sulaiman ya dawo".nan ta Karba ta Fara ta dau lokaci kan ta fidda shi daidai sosai momy Sulaiman taji dadi Harda Mata godiya.."Wani school kike?"

"Na gama diploma Na".

" to meyasa baki ci gaba ba?"bata so tace Mata surkin ta baya so don ita ma ba budewa mutani cikin ta take yi ba sai tace"Aure zanyi ".

" Masha Allah yaushe auren?"

"Ba'a sa Rana ba tukun".

" yanzu in kin samu aiki kan auren zaki yi?"

"Ehhh".

Abinci aka kawo Mata sannan aka kawowa mommy Sulaiman sanan ga mamakin kowa sai tace laylerh tazo su ci tare abunda bata taba ba kenan Bayan Sulaiman bata cin abinci da kowa..duk da nauyin ta da laylerh ke ji haka ta daure suka ci tare daga nan ta shige ciki domin gabatar da sallar azahar laylerh ko aka ce ta shiga toilet dake falon tayi alwala haka ko aka yi..

Bayan sun idar da sallama sai taga Ana ta shirye-shiryen a gidan kamar dai za'a yi liyafa don taga sai fitar da Kayan decorations daga store'n gidan ake yi Bayan mommy Sulaiman ta fito ne ta dube ta tace"zo muje Ki ga yadda nake decorating waje".murmushi tayi sannan tabi Bayan ta can backyard Na gidan fili ne Babban ga mutani sai dafa abinci suke nan ta Fara decorating din ganin colors da take hadawa baya matching sai laylerh tace da dai da Kala kaza za'a hada sai naga zai fi aiko da aka yi hakan sosai yayi kyau nan dai tayi ta tayasu aiki momy Sulaiman ko abun ta kadan sai tace laylerh haka yayi in yayi tace Ehhh in bai yi ba tace bai yi ba a haka har aka gama waje ya zama gwanin ban sha'awa masu girki ma sun gama komai ready ganin yamma yayi sai tace" Hajiya ni Zan koma gida kada a mini fada".

"Yanzu ba zaki tsaya ba birthday'n son nane fa kuma suprise nake son mishi".

" Ayya yamma yayi ne Ai".

"To Shikenan Victoria karbi number'n ta". Victoria secetariyar tace nan suka yi exchanging numbers sannan mommy Sulaiman ta bata dubu biyu.

.

Tana tafe tana mita ita shiyasa bata son nunawa ta iya kitso don Rainin wayon mutani yayi yawa abu home service Amma a cire dubu biyu Ana bata Ai a gida in sun ji Auta kadai ta ishe ta tana mita ta hau keke ta nufi gida a falo ta tarar da su koda aka tambaye ta sai ta tsinci kan ta da cewa zasu Mata transfer ta nufi daki ranta duk a jagule..

Washe gari da safe tana kwance taga Victoria Na kiran ta kamar ba zata daga ba don abunda suka Mata jiya sai wani Zuciya yace ta daga nan ta daga Bayan sun gaisa sai tace ta turo account number'n ta tana turawa da minti uku taji alert Na dubu asirin tana cikin murna kenan Victoria ta Kira ta" madam tace Ki tambayi iyayen Ki in sun amince zata baki aiki a company'n ta Amma fa Ku yanke hukunci da sauri don wani sati zata koma abuja".Na gode tace tare da shilla wayar kan katifa bata damu da an katse kirar ko ba'a katse ba tayi sujudu shukur tana godiya ga Allah da yasa zata huta zaman gida...

**

Kwance take a kan three seater taji an banko kofar dakin ta da karfi, da sauri ta mike sai ganin Umar Farouq tayi tsaye ya Nade hannu a kirji fuskar nan a nurtuke cike ta izza ya Fara taku har ya iso cikin dakin..

Tun Randa Aunty Hauwa ta sanar da shi Sadiya ta dawo gidan da zama yace dama ya gama umra abunda ba'a rasa bane ya ajiye shi Amma in sha Allah gobe yana tafe..

Yadda ya hada fuska haka ita ma ta hada"me haka zama shigo mini daki ba sallama in Ka same ni nicked fa".tsaki yaja sannan yace"har akwai wani abunda za'a gani a jikin Ki ne Bayan kowa ya gama kwasar rabon shi".murmushin Rainin wayo tayi tace

"In fitsari banza ne kazama tayi mana Kai ma Ka kwasa din". Tofa yawu yayi yana nuna tsantsar kyamar ta yace" Allah sauwaka me zanyi da ke Nida nake da fresh tomatoes ".ji tayi da shake ta yayi da mutu da wannan furucin da yayi akan laylerh" Ai wallahi in sura ce kasan karya ne ta nuna mini yarinyar da kirjin ta Na manne da Fata sannan how sure are you ita din virgin ce waya San me take aikatawa a Bayan Ka

ko dai Na maka zigidir Ka gani ne Yadda zaka tabbatar da cewa Ruwa ba sa'an kwando bace".

"Kin ga Tun a nan kin fadi,inda tafi Ki kenan ko kudi Na biya in har ba sadaki bane ba zata tube zigidir a gaba Na ba and nazo ne Na miki warning Ki nemi wajen zama don you are not welcome a nan sannan nazo miki da albishir yarinyar da kike rainawan Na tsaida ranar Aure Na da ita nan da Wata daya so in mutuwa zaki yi Ki mutu ban damu ba". Yana Kai karshen zancen shi ya fice a dakin...ita ko ihu ta saka tare da daura hannu a Kai..

Comment

Share

©Hafciey Musa

[1/25, 5:42 AM] Hafciey Musa😘: *□LAYLERH□*

(The prettiest emerald)

Alhamdulillah naji sauki sosai ina kuma godiya a Gare Ku da kauna da kuka nuna mini ta hanyar yi mini addu'a ina kaunar Ku sosai da Sosa

33

Wangale musu gate din aka yi nan driver da guards nashi suka sa hancin mota cikin gidan..yau ya dawo daga tafiya..parking suka yi da sauri guard nashi ya fito ya bude mishi k'ofa cikin gidan ya nufa sanin Mom nashi Na gari sai dai bata falo, turawa yayi a Kira ta sai aka ce da shi tana backyard nan ya nufi wajen "happy birthday swthrt". Ta fadi fuskar ta dauke ta murmushi sannan ta bude mishi hannayen ta,shima murmushi yayi yana karewa wajen kallo don ba karamin kyau yayi ba nan ya nufe ta hugging Na juna suka yi..duk duniya ji yake ba wacce ta Kai shi dacen uwa a kullum bata da wani buri da ya wuce ta faranta mishi shiyasa bai son bacin ran ta ko kadan

" I love you mom".ya fadi Lokacin da suka yi breaking hug din"so how do you like it?".

"Mom am so so happy you are the best". Ya fadi yana sake hugging nata,ba Wai suprise birthday bane ya mishi dadi har haka ba,a'a kaunar ta da kuma yadda kullum take maida shi yaro ne ke sa shi cikin farin ciki..

Hannun shi ta Kama har inda aka ajiye mishi cake din.. shine farin cikin ta kuma zata iya yin komai domin shi,yanka cake din yayi ya Kai Mata baki gusura kadan tayi tana yake don hawayen da ya cika Mata ido,Baban shi Nada yara dayawa Amma ita kuma shi kadai Allah ya mallaka Mata nan ta bashi cake din shima, sanin tunanin da take yi yasa shi girgiza Mata kai

" enough mom in sha Allah muna tare har karshen rayuwa ".murmushi tayi saboda shi kan shi bata taba sanar da shi dalilin rabuwa da mahaifin shi ba sannan ta haramta mishi zuwa gidan shiyasa wasu kannen shi ma bai Sani ba Amma duk da haka bai taba tambayar ta dalili ba hakan yasa take jin shi tamkar shi kadai ne rayuwar ta" Mom Bari Na shiga Na watsa Ruwa".

"Alright ga wannan". Ta fadi tana mika mishi wani kwali da aka yi rapping nashi Wato gift" I love you form moon and back mom you are the best ".dafa kafadar shi tayi sannan ta mishi alama da Kai kan cewa ya tafi haka kawai take ji a jikin ta abunda ta dade tana boyewa ya kusa bayyana sirrin da ko Bayan ba ranta bata so wani yaji in ko haka ne ta San rayuwar ta ce tazo karshe..

Adamawa

Cikin shekara daya da Rabin da suka gabata Aunty taje har can Maiduguri inda ta sayar da daya daga cikin filayen da Muhammad ya kawo takardun su..koda bappan su Laylerh yaji ta sayar da fili nan ya Fara Neman ta Amma babu ita babu labarin ta saboda ko gidan Baban ta bata Isa ba mahaifiyar ta ce dai suka hadu da daddare nan take tambayar labarin Hadeeza aka ce har yau shiru bata dawo ba a Washe garin ta bar Maiduguri gudun abunda zai biyo baya in sunyi ido hudu ba bappan yaran ta...

Zaune take ita da Muhammad wanda yau bai je makaranta ba sai zulai wacce ke cin abinci a gefen su kuma Sirajo ne Wanda yanzu gidan ya dawo wajen wunin su in basu da makaranta

" Muhammad ni fa Zan sa ranar Komawa gida Na saida dayan fili da kuma gida da ya rage saboda kaga auren Laylerh ya gabato tunda har ta gama makaranta yanzu zancen auren za'a Fara kuma ba zai yuwu mu zuba ido sai abunda malam da gidan su Yaron suka Mata ba".numfashi yaja sannan yace

"Aunty maganar Ki gaskiya ce Amma Tun wancan dawar Ki aka sanar da ni Bappa yace duk Randa aka sake ganin Ki a garin a sanar da shi hukuncin da zai dauka

wannan Karon sai yafi Na farko Kuma filin da Kika sayar baki sha da haka ba kotu zai shigar da ke ".

" to in ya shigar da ni me a wajen Ai Shari'a ce tsakanin karya da gaskiya ".

" Anty kamar fa kin manta wane ne shi".

"To yanzu ya kake so muyi ita kadai ce ya mace gare ni fa sai Na zuba ido ayi auren ta ba abunda nayi".

" yanzu mu bar zancen sai munyi tunani a Kai".Cewar Sirajo.

"Aunty wallahi Na kosa auren nan yazo muje jala gaskiya zamu shashe a auren Laylerh".Cewar zulai, Kanta Aunty ta zungure tare da fad'in

" to sannu Hana biki maraici".nan suka kwashe da dariya Sirajo da Muhammad ko shagon Aunty dake kofar gida suka nufa..

A kullum in ta zauna bata da wani tunani da ya wuce Na aurar da Laylerh tana so Yar ta ta rayu tamkar sarauniya duba da wahalar da yarinyar ta sha a rayuwa Wanda ko ita kanta bata sha irin shi ba wani lokacin kuma sai zuciyar ta ya raya Mata Aure tsakanin Laylerh da Umar Farouq ba abu bane Mai yuwu Wa don Ruwa ba sa'ar kwando bane,ta sani suna da kudi kuma masu kudi kan aurar da yaran su ga yan uwan su masu kudi ne sai dai kaji suna cewa tuwon girma miyan nama da wuya kaga Yar talakawa ta auri Mai kudi sai in rabo ya rantse...ta sani Laylerh'n ta Nada kyau daidai gwargwado sannan kuma tana da farin jini Amma hakan ba yana nufin zata hada matsayin Yar ta da Na Umar Farouq bane wani lokacin ta kan yi Dana sanin amincewa da auren don bata San mijin wane ne ba sannan daga ina yake ya halin shi yake wadan nan tunanin sukan jefa ta cikin wani hali Gashi ko ganin shi bata taba yi ba kuma ko irin kiran nan da samarin yanzu ke yi su gaida surkuwar su ko don su samu gindin zama shi bayayi to wani irin mutum ne shi Babban damuwar ta shine yawan fadiwa da gaban ta ke yi in ta tuna Laylerh Wanda hakan ke tabbatar Mata akwai abunda yake tunkaro rayuwar Yar ta Wanda kuma ta sani ba Alkhairi bane don takan ji hakan a duk lokacin da mummunan abu zai faru

da ita..sai dai duk da fargaban da take yi wani zuciya Na raya Mata duk munin abunda zai faru Alkhairi ne ga rayuwar Laylerh din..

"Aunty tunanin me kike yi?"

zulai ta tambaye ta lokacin da ta dafa ta nan tayi murmushin yake tace

"babu Kinga Ki zauna a gida Na San Ki da shegen son yawo Bari naje wajen malam Na amshi magani nazo".

" Amma kada Ki Dade Dan Allah wallahi kullum in Kika bar ni a gidan nan tsoro nake ji".

"Ke da Laylerh kam ban San Wa ya fi wani tsoro ba Ince sakata zaki sa a gate kuma fa su Muhammad suna kofar gida". To tace kamar zata yi kuka ganin haka sai Aunty tace" dauko hijab naki mu tafi".da wuri ta mike don dama yawon take so ba wani tsoro nan suka fice..

**

"Malam ina kwana?"

"Lafiya Laylerh ya gida". Da murmushi dauke a fuskar ta tace" alhamdulillah daga nan shiru ne ya biyo baya sai wasa da zoben hannun ta da take yi ta rasa ta inda zata Fara zancen "Laylerh akwai abunda kike da bukata ne?" Da sauri ta gyada Kai alamar Ehhh"uhum ina sauraron Ki".

"Malam dama... Dama...".

" Kinga fadi abunda ke ran Ki".

"Malam dama wacce nayima kitso rancan ne tace zata bani aiki in iyaye Na sun amince".

" aiki kuma wace iri?"

"Babbar Mata ce to tana da company shine tace in za'a bar ni a gida zata bani aiki to shine nayi magana da Aunty Na sai tace Na tambaye Ka in Ka amince bata da matsala".

" wani company ne haka?"

"Wallahi ban tambaya ba saboda banyi shawara ba Amma in sha Allah yanzu Zan Kira Na tambaya". Numfashi yaja sai yace

" Laylerh Zan fi kowa farin cikin in kina aiki don zaki huta zaman kadaici sai dai ba a nan matsalar yake ba saboda kin San gidan da zaki je basu son mace tayi aiki kuma dole in zaki yi aiki su sani ".

"Ayya malam tunda basu yi maganar auren ba Zan Fara Na gaji da zaman gida wallahi".ta kare zancen kamar zata yi kuka don wallahi ba kaunar auren take ba tafi kaunar aikin da da wannan mahaukacin da za'a aura mata

" to ba komai Zan Kira shi Umar Farouq din Na sanar da shi in ya amince to Shikenan ".

tunda taji yace Umar Farouq to tasan ba samun aikin nan zata yi ba don ba yarda zai yi ba shiyasa cikin mutuwar jiki tayi godiya gami da mikewa ita gwara a Kira kowa a tambaya ta San kila su ji tausayin ta Amma shi kam ba yarda zai yi ba Harda da guntun hawayen ta nan ta fara dialing number'n Victoria lokacin da take shiga dakin ta" hello ina kwana ".daga daya bangaren Victoria ta amsa" am Dan Allah nace ya sunan company'n? "

"Nature's pride farm". Tsoro ne ya bayyana a fuskar ta da kyar ta iya katse kiran tana godiya ga Allah da yasa Umar Farouq ba zai amince da aikin nan ba,cab inda aka Kore ta sannan taci zarafin CEO company'n gaskiya tana tsoron Komawa to kuma zaman gidan ya gundure ta.mikewa tayi ta koma falo kan ta sanar da malam

sai cewa yayi" munyi magana da shi ".sannan ya mike ya fita Bayan shi tabi da kallo" sun yi magana to me yace kila rashin mutunci yayiwa malam dama nasan ba yarda zai yi ba".

a falo ta zauna ba jimawa Auta ta fito can gefe ta zauna tana satar kallon Laylerh.. sarai Laylerh ta Lura da ita kuma ta San abu take so a wajen ta sai tayi banza da ita taci gaba da kallo a karkashin zuciyar ta kuma tana addu'ar Allah kawo ranar da ita da Auta zasu yi zaman jin dadi

"Laylerh Dan min wayar Ki Na tura labari ki Na wannan satin".Auta ta fada tana kallon gefe a dole ba zata kalli bangaren da Laylerh take ba..ita ma laylerh girgiza Kai tayi sannan tace

"Hmm labari Na fa Kika ce,Ai ita Sumayya dadi ne ya ishe ta ni kuma da kike gani har yau ba'a gama nawa labarin ba kuma baida ranar karewa sai Na mutu"..ta kare zancen da mika Mata wayar nan ta mike tazo ta Karba" Sorry ina nufin labari Na"...ita Laylerh ta fahimci rashin shirin ta da Auta ya kan yi tsamari ne in an tada batun Umar Farouq,ganin sha daya saura sai ta mike ta nufi kitchen don daura abincin Rana blending Kayan miya tayi sannan ta daura a wuta..

A can falo kuma duk vedio da yayi ma Auta turawa take yi tana cikin haka sai taga suna yayi appearing a screen din wayar "Ya Umar" sannan wayar ya Fara ringing da wuri Tasa wayar a silent zuciyar ta Na harbawa da karfi

"Auta naji kamar waya Na ke ringing ".Laylerh ta fada lokacin da ta fidda Kai a kitchen din don a zaton ta Aunty'n tace

" Ehhh mtn beep ne kuma fa number ne".ta fadi tana kallon screen din wayar da har yanzu yake ruri"me karshen number'n? "Laylerh ta tambaye ta" zero zero".ta fadi tana addu'ar Allah sa Laylerh ba number'n da ta Sani Wanda ya kare da wannan number'n " ban San me number'n ba". Ta fadi tare da Komawa kitchen Auta ko takaici take ji meyasa baya tashi Kira sai wayar Na hannun ta ringing wayar ya sake yi kamar zata katse irin Na dazun tace beep ne sai kuma ta tuna Ai Laylerh zata ga missed call Gashi call log nata akwai password bare tayi deleting call din sai tace

" ga wayar Ki Ana Kira".

"Waye ne?"

"Oho ban Sani ba". Jin yadda ta amsa Mata sai ta kwabe fuska tare da tabe baki ta fito ba tare da tace komai ba don ta San in ta biye Mata fada zasu yi hannu Tasa ta karbi wayar ganin sunan da ya bayyana a fuskar wayar sai dai gabanta ya fadi a zuciyar ta tace" Ai Ruwa baya tsami banza".

"Assalamu Alaikum".

" wa'alaikisalam ".ya amsa can ciki ciki kamar dole aka sa shi

" ina kwana? "

"Lafiya". Sosai taji mamakin yadda ya amsa da wuri kuma a nitse yake wayar kamar kullum da wuri ta nufi kitchen jin abun ya Fara konewa tana shiga ta sauke so take Tasa wayar a hands free don ta fahimci sai ya dau lokaci yake magana Amma kuma zai gane shiyasa ta makala wayar tsakanin kafadar ta sai da ya hau lokaci ita a zaton ta ma ko ya katse kiran ne taji yana fad'in

" am running late malam told me kina son Fara aiki ina ruwa Na da rayuwar Ki da sai an tambaye ni kiyi duk abunda Kika ga dama I have nothing to do with you".da sauri ta girgiza Kai kamar yana ganin ta don tasan inda kwanan zancen yake "Ehhh". Tace don duk ta rude da fadar da ya rufe ta da shi har bata San amsar me zata bashi ba shiyasa tace Ehhh tana tausayin kanta da kanta..shiru ne ya biyo baya inda take shesshekan kuka a hankali yadda ta tabbatar ba zai ji ta ba,shi ko wallahi mamakin wasu yake yanzu fisabillah Tun ba'a lika mishi yarinyar ba an Fara tambayar shi izini in zata yi wani abu wannan wani irin rashin sirri ne..sun dau lokaci a haka a bazata kuma taji yace

"And what's the name of the company?"

"Nature's pride farm".ta fadi tana mamakin irin halin shi da yake canzawa cikin ko wani dakika yanzu fa ya gama cewa ina ruwan shi da ita

" alright Zan sa a bincika ".yanzu kam har ido ta zaro don ba karamin bata mamaki yayi ba

" Allah fa company'n Nada kyau Na taba aiki a wajen ".ta kare zancen cikin rawar murya

" and me yasa Kika Bari?"ya tambaye ta Kai tsaye ba tare da bata lokaci ba

"Saboda time I am not qualified". Ta tsinci kan ta da fadi don tasan in tace korar ta aka yi akan sata Ai abun kunya ne

" Alright ba komai kina iya zuwa".kamar tayi tsalle haka take ji don ta manta zancen Boss din nata

"thank you so much ".

Ba tare da yace komai ba ya katse kirar....

Murmushin gefen baki yayi yana kallon madubin motar yana kuma girgiza kai,ba kowa yake kallo ba face Sadiya wacce Tun fitar shi ta biyo Bayan shi a lokacin yake waya da malam koda ya fada mishi bukatar Laylerh shiyasa yace zai Kirata sai yace da guards nashi su bashi waje sai ya Kira ta da farko bai San tana wajen ba shiyasa ya fitowa laylerh a Umar Farouq nashi da ya fahimci tana wajen kuma sai ya sassauta kalaman shi suka dauki lokaci suna wayar da ya tabbata Sadiya naji kuma daga cikin motar ya hango yadda mood nata ya canza da hannu ya Kira guards nashi nan suka fice a gidan ita ko a wajen ta zauna tare da rushewa da kuka Allah ya gani son shi take tsakani da Allah kuma irin blind love nan take mishi ita ba Laylerh kadai ba in yaso ya kawo irin Laylerh har uku ita ta zama Na hudu ba zata damu ba don shi take so kishiya bai dame ta ba don shi ta gyara halin ta Amma ya Gaza fahimtar irin son da take mishi ta kuma rasa da me wancan Laylerh ta fita da har ya bata tsahon lokaci suna waya abunda bata taba gani yana yi ba har da wani biyewa karamar yarinya..kuka take har da shesheka..

"Fine ba dai Dani kake zance ba mu zuba mu gani". Ta kare zancen tana share hawaye sannan tace

" Nature's Pride farm daga Randa tayi stepping legs nata a company'n Zanga yadda za'a yi Ka Aure ta".tana kaiwa nan ta sake rushewa da kuka don tana ji a jikin ta ko ya rasa Laylerh ba zai Aure ta ba..

Abba da Aunty Hauwa ne suka fito zasu anguwa sai yace "Hauwa kamar fa mutum ce a Bayan motar can".

" Ai kuwa dai Bari Na duba Na gani".nan ta nufi wajen shi ko motar da zasu fita da ita ya nufa,dafa kafadar Sadiya Aunty Hauwa tayi don sarai ta gane Sadiya bata son fadawa Alhaji ne,kin dagowa Sadiya tayi Alhaji kuma Bayan ya shiga mota sai yace da driver suje wajen da su Aunty suke haka ko aka yi suna Isa yace"Sadiya sana'ar taki kike yi ne?sanin shi kam bata Isa ta mishi iskanci ba ya sata dago Kai tana sauke Kai kasa"Nifa a sanin da Na miki you are a strong woman Amma yanzu duk kin lalace".

"Abba ba komai zaka iya daurewa ba wani abun fin karfin mutum yake".

" Allah kyauta Hajiya Kira yaran nan su shigar da ita ciki".

"Ohk Yasmeen ce kadai a gida don hajara da Najeeha sun tafi makaranta". Tana zancen ne lokacin da take kiran layin Yasmeen ba jimawa kuma ta daga sai tace tazo ta shigar da Sadiya ciki Ai ko da wuri ta fito nan sadiya ta mike" Yasmeen Ki zauna da ita Kinji maybe zaman kadaici ke sata kuka".da Kai Yasmeen ta amsa nan suka nufi cikin gida har dakin Sadiya sai dai ita Yasmeen jugum tayi don bata fiya magana ba Sadiya ko sai sharban kuka take kamar ranta zai fita ita Yasmeen mamaki ma ta bata ace mutum da girman shi ya tsaya yana wannan kukan kuma ba mutuwa aka mishi ba a zahiri kuma ko inda Sadiya take bata kallo ta San da Najiha ce a matsayin da take yanzu ba taga abunda zai Hana ta viewing kukan da Sadiya ke yi ba..

Ita Sadiya bata Yasmeen take ba zuwa yanzu har ta Fara ramewa don gwara a kashe ta da ace Umar Farouq baya son ta Wai watan ta yake so, watan ma Laylerh yarinya karama kalen ya jawa kan shi raini tana kuka take wannan tunanin..

A bangaren Laylerh ma taga lokacin da Auta ta labe tana jin hirar su a karkashin zuciyar ta take mamakin yau kuma da wani salo yazo ko dai don yaga ta gama makaranta ne dama daga Mata kafa yake..

Jin sun gama waya da gudu Auta ta nufi falo tana ihu kamar wacce uwar ta ta rasu..

Niko nace Umar Farouq Allah ya maka farin jinin Mata kam..

Da sauri Baaba ta mike tana fadin "ya dai me kuma ya faru?"

"Baaba Tun farko sanda nace Ki dau mataki Amma Kika ce ba abunda suka Isa suyi to Gashi yanzu ya Kira ta kuma hirar soyayya suka yi".

" Kai Auta kila wani saurayin ta ne fa".

"Yaseen Baaba shine wayar fa a hannu Na yake". Shiru Baaba tayi can tace" Ai dama zuwa Adamawa da tayi nasan wani asirin aka mishi shiyasa ya dawo Amma ba komai Allah ba azzalumin bawan shi bane kuma ya Hana zalunci tsakanin bayin shi akwai kawata da aljanu suka budewa makociyar su ido tana bada magani yanzu Zan Kira ta Na sanar da ita matsalar mu ".

" Yauwa Baaba kiyi sauri kada su tada zancen auren don Allah in ba haka ba mutuwa Zan yi".

"Kada Na Kara jin zancen nan a bakin Ki in har ina Raye bazan bar Umar Farouq ya auri Laylerh ba". Daga nan ta shiga dialing number'n Kawar ta ta sanar da ita matsalar ta ta kuma ce in sha Allah zata fadawa makociyar tasu..

Jin haka sai tace Baaba ni bara naje gidan su Kawa ta". A dawo lafiya Baaba ta Mata nan ta fice..

Tafe take tana Danna wayar ta har ta kusa gidan su Kawar tata sai taji ance" na san kina cikin damuwa, saboda tsananin son wani da kike yi Amma shi tsam bai son Ki,kada Kiga laifin shi an hada tauraron shi ne da Na yarinyar dake gidan Ku".da farko har tayi banza da shi jin abunda ya fada sai ta tsaya tare da kura mishi ido irin buzaye masu bada maganin nan ne sai dai shi Dan yaudara ne"ya aka yi Ka Sani".

"Hmm ba abunda ban Sani akan Ki ba ni magani nake bayarwa kuma kuna Karba shi da yarinyar can har Abada ke ko sunan ta ba zai iya tunawa ba". Cikin zakuwa tace" da gaske? "

"Ce miki aka yi ina wasa dake bare Na miki karya".

" to kaga sa mini number'n Ka a nan Zan sanar da Baaba ta duk yadda ake ciki zaka ji".Kira Mata number'n yayi Tasa da sauri ta juya gida,gidan Kawar tata da bata je ba kenan..

Koda ta sanar da Baaba yadda suka yi sai hamdala Baaba tayi tare da fad'in Allah ne ya turo musu shi Ai dole ma su Kira shi..

Laylerh ko Na gama abinci ta shirya gidan Mommy Sulaiman ta nufa da documents nata da kyar Mai gadi ya bar ta ta shiga Bayan ta Kira Victoria nan ne ta fahimci mai gadin masifeffe ne gwara da Ummi ta mishi rashin mutunci ranar..

Rabi ce kadai a falon ita ma Bayan sun gaisa sai ta nufi kitchen domin karasa girki Victoria ce ta fito ta duba takardun tace sun yi har ta mike zata tafi sai ga Mommy Sulaiman ta fito"congratulations Laylerh zaki iya Fara aiki daga gobe a financial department under accounting yake Victoria ta sanar da ni takardun Ki Nada kyau dama mu bamu duba qualifications kwarewar da kwazo muke dubawa".

"Na gode sosai Aunty Allah saka da alkhairi".

" Ameen shawarar da Zan baki shine Ki maida hankali akan aikin don zaki iya samun cigaba".godiya ta sake yi sannan ta tafi tana farin ciki da kuma mamakin saukin Kai irin Na Mommy Sulaiman..

Koda malam ya dawo gida sai ta sanar mishi gobe zata Fara zuwa aiki nan yasa Mata albarka...

A Daren kuma ya sanarwa Baaba sai dai bata ce komai ba ita Allah Allah take gari ya Waye Laylerh tayi masar da malamin su yace ayi kuma a tabbata ita ce ta raba sadakar...

Washe gari ko da ta tashi sai ta kwaba masar nan ta Fara shiri kan ya tashi kasko uku ta tuya ganin zata makara ta kuma san ko mutuwa zata yi Baaba ba barin ta zata yi ba sai ta sulale ta gudu ba Wanda ta sallama tunda sun ce sadaka zasu yi in sun fito su karasa samun ladan..

Keke Na sauke ta a kofar company'n zuciyar ta ya Fara bugawa don tsoron haduwar ta da boss ta rasa cikin shi da Umar Farouq wa tafi tsoro.. Shiga tayi sosai company'n ya sauya Mata cikin shekarun da suka wuce kamar ba'a nan ta taba aiki ba an samu cigaba sosai nan ta gaida security shi kuma yana Mata kallon Sani Amma bata ce da shi komai ba ta zauna jiran mota tana addu'ar Allah sa yau kada boss ya shigo.. Bayan sun Kai su biyar sai aka shigar da su kamar before a admin department aka ajiye ta nan ta shige ciki duk Wanda ta gani sai ta gaishe shi yan department din ma duk sabbin fuskoki ne coppers duk sun tafi haka kawai sai ta tsinci kan ta a takure Gashi maza sun fi yawa a department din kuma wannan Karon da Na miji aka hada ta ya koya Mata aiki jatutu nw kadai ta shaida fuskar shi a department din..

Haka ta wuni bata sake da kowa ba sai da aka tashi suka hadu da Nabeela nan suka Fara hira sai kusan magrib suka rabu..

Zata shiga gida malam kuma zai fita"Laylerh an dawo".

"Ehhh malam Mun same Ku lafiya".

" shiga ciki Baabar Ku Na jiran Ki da katon sanda".

"Me kuma nayi?" Ta tambaya tana murmushi tuno laifin da tayi"Ai kin fi ni Sani".shima ya fada yana murmushi "malam sauri nake yi fa shiyasa ban karasa tuyar ba".

" Au Ashe kin San me Kika yi Kika ce baki Sani ba Ki shiga ni masallaci zani in ta gama dukan Ki nazo Na Debi sauran Na Kai asibiti".yana gama fadin haka yayi gaba ita ko jin haka cikin sanda ta shiga gidan har ta shiga corridor sai Auta tace"Laaa Baaba Gata ta dawo".me zata yi banda sa kafa tana shiga dakin ta Tasa key ita abun ma har dariya ya bata nan tayi murmushi tare da shiga toilet tayi alwala tayi sallah..don tsoro haka ta kwana da yunwa Washe gari ta tashi da wuri zata yi girki sai taga kitchen din a rufe kuma ta San don ita aka rufe a tunanin su zata fito Neman abinci da dare..shiri tayi karfe bakwai ta bar gidan,gidan Dadda ta nufa..

Tunda Dadda ta rasu sai maryam ta koma dakin yanzu tare suke kwana da Nabeela shashin ta nufa da yake ta fita da kudi sai tace yunwa take ji nan maryam ta karbi kudin ta sayo musu indomie da koyi suka girka da yake akwai karamin stoof a dakin lokuta da dama su kan saya abu su girka cikin Daren in anyi bacci in ko yan gidan suka ji to dole haka zasu kasa sai kowa ya samu..

Yan din ma suna gamawa zasu Fara ci kenan Wata bazawara ta shigo ta inda take shiga ba ta nan take fita ba suna deba Mata tayi shiru..suna gama ci Nabeela ta shirya suka nufi company a hanya take sanar Mata tana fargaban haduwa da boss sai Nabeela tace Ai yanzu bai fiya zuwa ba..

Tun a gate security ya sanar da Nabeela zuwan madam din don sun Saba sosai yanzu nan suka shiga mota command madam din ta bayar kan cewa motar staff dake Bayan ta su bita don sunyi late nan ko suka bita zuwa inda ake processing sugarcane..

Sulaiman Na Danna wayar shi sai ya daga ido har ya cigaba da dannawa sai brain nashi ya dawo mishi da hoton ta da sauri ya sake kallon illa kuwa ita din

ce"what?"ya furta da sauri..Mom nashi kuma Na ganin ta tace"ohh it's you Laylerh meet my son Sulaiman ".sannan ta juya ga Sulaiman tace" son meet Laylerh ".

Jikin ta Na rawa har fitsari take ji don bata taba tunanin Sulaiman Yaron madam bane Shikenan kuma tata ta kare a hannun shi..

manage this wallahi ina Fara typing sai Na Fara jin jiri□dama ciwo ke shiga lkc guda,lafiya kuma a hankali ake samu

Comment

Share

©Hafciey Musa

[1/25, 5:42 AM] Hafciey Musa😘: *□LAYLERH□*

(The prettiest emerald)

34

Murmushin yake yayi gami da waving nata ya nuna kamar this is the first time da ya Fara ganin ta yace"Hy it's Nyc meeting you".amma deep inside his heart kuma yaji dadin ganin ta dawo aiki a karkashin shi zai kuma gwada mata kuskuren ta..ita ma yi tayi kamar bata San shi ba"tnx"tace ba tare da ta dubi bangaren shi ba don sosai zuciyar ta ke bugawa..

"Son muje ko tunda Na gama abunda ya kawo ni kada nayi missing flight Na".

" ohk Mom "ya amsa idon shi akan Laylerh ji yake kamar ya shake ta har sai ta daina numfashi, juyawa Mom nashi tayi nan yabi Bayan ta yana gab da shiga motar yayiwa Laylerh alamar zai dawo da hannu carab akan idon mommy Sulaiman" wait Sulaiman Ka San ta ne?"sanin ko da zai yiwa duk duniya karya ita ba zai taba Mata ba sai yace"yeah ta taba aiki a company'n nan".

"Really" ta tambaya tana kallon Laylerh kan ta amsa sai taci gaba da fad'in "but meyasa baki fada mini ba?"

"Saboda sai daga baya Na San sunan company'n". Ta amsa idon ta a kasa don tana jin yadda idon Sulaiman ke yawo a kan ta kuma tasan kallon tsana yake Mata,shiga motar suka yi nan suka tafi ita ko hamdala tayi sannan ko wacce ta nufi department nata..

Direct airport suka wuce don dama da shiri suka fito ba shi ya bar airport din ba sanda yaga Tashin jirgin su yana jin zai yi kewar ta..

Duk zaune suke a second floor cikin main falo da yake falo hudu ne a second floor din,daya Na Aunty Hauwa sai daya Na yara daya kuma Na kawaye wadanda Baku shaku ba sai general falo wacce suke zaune a cikin ta yanzu kowa da abunda yake yi..

Kamar ko da yaushe Sadiya ce zaune a one seater ta sha tagumi Yar ta sai magana take Mata

" Mammi jiya nace Ki mini assignment Kika ce Na ajiye zaki mini kuma baki yi ba Gashi naje school an buge ni class mates Na sai dariya suke mini kuma an bamu notice Na meeting shima baki je ba".duk zancen da yarinyar ke yi ba wacce Sadiya taji don gaba daya hankalin ta ba'a nan yake ba

"Haba Sadiya yarinya Na miki magana kin yi banza da ita akan me zaki saka yarinyar da bata San komai ba cikin damuwar Ki baki San zai shafi karatun ta bane".kamar yadda Beta ta gama zancen ta Sadiya bata ji ba haka ma Aunty Hauwa "Mom". Beta ta Kira ta tana jijjiga ta a take ta firgita

" yes beta me kike so?"ta tambaya tana shafa fuskar yarinyar Aunty Hauwa ko Kai ta girgiza tana Allah kyauta a zuciyar ta. su Najeeha kuma suna abunda ya dame su don inda sabo sun Saba,fahimtar duk zancen da tayi mammin ta bata ji ba yasa ta fita a falon ita sadiyar ko ji tayi gaba daya duniyar ta fita a ran ta kuma ko kadan bata yi Dana sanin abunda ta aikatawa Yar ta ba..

A stairs beta ta zauna tare da yin tagumi Aunty Hauwa wacce ke saukowa ce ta Gan ta,zama tayi kusa da ita tana shafa kan ta tace"Beta me kike yi a nan?"

"Ba Mammi Na bane ta daina so Na ko ina magana bata ji".

" shussh"Aunty Hauwa ta fadi tana daura yatsar ta manuniya akan lips Na beta

"kul kada Ki Kara fadin haka Mammi Na son Ki sosai Aiki ne ya Mata yawa".

"Da gaske?" Ta tambaya tana murmushi "Ehh mana" Aunty Hauwa ta fadi cikin muryar gaskiya da gaskiya don tasan kan yara sosai"ni kadai Mammi nake so ko?"

"Ehhh mammi's pet Kinga yanzu zo muje mu huta a waje". Da sauri ta mike tana rike yatsar Aunty Hauwa suka nufi swimming pool da gudu ta sake hannun Aunty Hauwa ta Fara wasa ita ko Kai ta girgiza tana tausayin yarinyar don halin da uwar ta ke kokarin jefa ta a ciki..zaman su ba jimawa su Hajara suka fito duk joining nasu suka yi sai hajara ce dake kallon beta Na wasa tace" Aunty wallahi abunda Aunty Sadiya ke yi ya Fara affecting yarinyar nan ita wace irin matsala ce Gare ta da ta kasa fadawa mutani a bata shawara ".

" Sadiya fa soyayyar Umar Farouq ke dawainiya da ita ".Aunty Hauwa ta fadi ita ma idon ta akan beta wacce take wasa ita daya tana dariya" Soyayya kuma shi da yake da wacce zai aura".Cewar Hajara"to banda abun Ku Ai shi ya San halin Sadiya sarai shiyasa ba zai taba son ta ba duk wannan abunda take yi tana yi ne don Aji tausayin ta".

"Haba Yasmeen Ki tatausa kalaman Ki mana ke da kullum ake cewa kin fi mu nitsuwa Nida Hajara shine kike fadin haka,in har soyayyar ya Farouq ke dawainiya da ita to son gaskiya take mishi, kin taba ganin inda mutum yayi pretending akan soyayya har ya daina cin abinci sannan abun ya Fara affecting karatun yarinyar ta,kun Sani shi din irin Na mijin da ko wace mace zata so ne to me laifin ta don ta so shi,Na yarda halayen ta basu da kyau to Ai tayi nadama ko Dan Allah kuke kyautata Mata zato ni wallahi gaba daya tausayi take bani sai kace ba Aunty Sadiya ba". Cewar Najeeha kuma sun gamsu da zancen ta don tabbas son gaskiya take mishi sai dai kuma Bayan ta bai da kyau Ai

" kun ga Ku bar wannan zancen don ba maganar Ku bace Allah ne kadai masanin abunda ke zuciyar ta".Aunty ta fadi tana mikewa don ita ma abun sadiyar ya Fara bata tsoro..

**

Daga airport direct gida ya wuce don dama bacci yake Mom nashi Tasa aka tashe shi ya rakata company daga nan su wuce airport, wanka ya shiga Bayan ya fito kuma breakfast nashi is ready sai ya zauna yayi breakfast gaba daya he is bored ya rasa ina zai je"company "wani bangaren Na zuciyar shi ta raya mishi a take kuma ya sake wani killer smile yana shafa sajen shi" ta ya Zan manta ya kamata Na koma can ko don Na banbancewa Laylerh tsakanin Aya da tsakuwa".driver ya Kira yace "get the car ready". Nan take kuma duk suka shirya direct company suka nufa..

A bangaren Laylerh ko Bayan ta shiga office nasu da yanzu yake su uku ne kadai a ciki kuma kowa da desk nashi sannan dukkan su biyun maza ne sai ta zauna tare da Fara aikin ta Amma gaba daya bata sakewa ji take a takure take,jifa aka yi da system nata Wanda har yaje karshen desk din kadan ya rage ya fadi ta tare da hannun ta cikin hanzari a zuciyar ta ko tana mamakin wane ne da wannan karfin,cike da son ganin Mai shi ta dago Kai ta zuba idanu cikin nashi da sauri ta sauke kanta kasa jikin ta Na Daukan rawa a lokaci daya kuma ta mike tsaye

" ke har kin Isa kina Yar matsiya ta wacce bata da asali Kice za Ki yi disgracing Na a bainin jama'a har kina da karfin gwiwar dawa company'n mahaifiya ta kiyi aiki,tunda company'n ba Na uwar Ki bane Zan gwada miki abunda Zan iya".ya Kai karshen zancen shi yana nufo ta sauran abokanayen aikin ta ma duk mikewa suka yi suna mamakin halin shi Ashe dai shi ma Dan Iskan kan shi ne..

Yadda yake matso ta haka take Komawa baya tana hawaye don kalaman shi sun kona Mata zuciya sosai Ai dama ita bata ce mishi company'n Na uwar ta bane da zai tsaya cewa bana uwar ta bace sannan tsam bata son kusancin da suke kokarin samu a tsakanin su yanzu don zuciyar ta bugawa yake jinin ta kuma Na gudu da sauri jikin ta Na bata shi din kamar jinin ta ne..a bazata taji ta junguna da gini Wanda tsam bata yi tunanin ta iso wajen ba shiyasa ta zare ido tare da juyawa tana kallon ginin da wuri kuma ta dawo da duban ta Gare shi tana karanta duk addu'ar da yazo bakin ta ganin ya iso inda take da wuri ta rufe ido ji take kamar zuciyar ta zai fashe don yadda yake bugawa.. shi ko hannu yasa ya shake wuyar ta a take

kuma ta bude idanun ta da suke jawur hawaye Na bin fuskar ta so take ta tantance kwayar idanun shi irin Na wane ne don yana Mata Kama da Na wani Amma bata San Waye ba,ganin haka da sauri daya daga cikin abokanayen aikin ta yazo ya cire hannun Sulaiman da duk wani karfin shi sannan ya shiga tsakanin su"Sir...".bai Kai karshen zancen shi ba yaji saukar Mari a fuskar sa ido ya kurawa Sulaiman yana dafe da kuncin shi Wai masu kudin nan me suka dauki kan su ne,don kawai yana aiki a karkashin sa shine zai daga hannu ya mare shi, ko ba komai shi yasan darajar mace ba zai Bari a tazorta ta ba don haka a shirye yake ya karbi duk wani hukuncin da Sulaiman zai mishi..Laylerh Na ganin haka tasa kafa hannu ya mika zai rike ta Amma ya makara don tuni ta fice a office din da gudu tana share hawaye ganin haka sai ya rufa Mata baya tana gab da sauka ya cimmata ya daga hannu zai mare ta yaji an rike hannun shi ta baya

"kada Ka kuskura Sulaiman Ashe Kai din ba yadda nake tunani bane namijin kwarai baya taba daga hannu ya daki mace sannan waya baka damar dukan staffs Na company'n nan?"wani dottijo kuma professor Wanda shi ma Mai kudi ne yana tsaye da kafafun shi ba Wai ya dogara da company'n bane kawai yana taimakawa mommy Sulaiman ne sannan Sulaiman Na ganin girman shi bai Isa ya tanka ba,ganin duk staffs din sun kura musu ido sai yaji a jikin shi wannan ma Ai disgrace ne a gaban staffs nashi ake fada mishi haka shiyasa ya shige office Na professor nan professor ya biyo shi a baya

"Sulaiman na san kana da personal issue da yarinyar Amma hakan ba yana nufin zaka Mata duk abunda ran Ka ke so ba,Kayi amfani da brain naka tunda yanzu yarinyar ta shigo hannun Ka sai Kayi dealing nata yadda ranka ke so ba tare da kowa ya fahimci akwai wani abu tsakanin Ku ba".shiru yayi yana daura maganar uncle a mizani tabbas ko yayi gaskiya don yanzu in ya hukunta ta sannan ya Kore ta ba zai ji saukin abunda ta mishi ba zai barta kamar yadda uncle ya bada shawara sannan yake dealing nata yadda ran shi ke so tunda a karkashin shi take aiki shiyasa yana murmushi yace"Na gode uncle ".sannan ya mike ya fita ran shi fal farin ciki yana tuna irin muguntar da zai ke Mata..

A bangaren Laylerh ko ta juya zata koma office ta dauki bag nata sai taji jatutu yace" dama Na San ba zai taba barin Ki ba shiyasa da naga kin dawo aiki a company'n nan nayi mamaki".ita dai hanci taja tare da share hawaye da Bayan hannun ta ta nufi upstairs domin daukar bag nata ta bar company'n don ta hakura da aikin..durkusawa tayi tana cire wayar ta da Tasa a chaji taji Ana kwankwasa saman desk nata nan ta mike sai ganin wannan professor tayi

"Na zo ne Na baki hak'uri game da abunda Sulaiman ya miki".

"Ba komai uncle kasan aiki a karkashin wani sai Kayi hak'uri sannan a gaskiya ni Na hakura da wannan aikin". Ta Kai karshen zancen ta tana rufe zip Na bag nata Bayan Tasa wayar ta a ciki" no kada muyi haka dake duka duka yaushe Hajiya ta dauke Ki aiki da har zaki ce kin hakura in taji haka ba dadi zata ji ba in akan abunda Sulaiman ya miki ne to Ki kwantar da hankalin Ki Na mishi fada kuma ba zai sake ba".

"Mai hali fa baya fasawa".

" yanzu so kike Kice ban Isa Na fada miki abu Ki ji ba Ince ni nace miki ba zai sake ba".ya fada cikin Dan holo sai ta sunkuyar da Kai kasa"to Shikenan Zan zauna ".murmushi yayi gami da cewa" Allah miki albarka"sannan ya fice ita ko da ido ta bi shi don Bayan malam shine mutum Na biyu da ya sa Mata albarka.. Haka ta wuni a office din rai duk a jagule har aka tashi yau kam tsam basu tsaya hira a gate ba fahimtar bata jin dadi yasa Nabeela ma bata dauko wani zancen ba nan suka rabu..

Tana shiga falo Auta ta sha gaban ta,tsaki tayi gami da canza hanya nan ma ta sake tare Mata hanya,a Karo Na uku ta sake matsawa sai Auta ta sha gaban ta Kai ta girgiza don a yanzu bata da burin da ya wuce ta ganta ita daya ko don abunda ya faru a company raba gefen Auta tayi ta nufi dakin ta kan katifa ta fada tana sauke ajiyar zuciya..

A falo kuma Auta fashewa da kuka tayi duk da ba abunda Laylerh din ta mata nan Baaba ta janyo ta jikin ta tace

"Ki kwantar da hankalin Ki Na lokaci kankani ne zaki daina jin zafin ta...

Ko da ta idar da sallah bata cire hijab din ba ta fito falo direct tsakar gida ta nufa inda malam ke cin abinci da kuma sauraron radio durkusawa tayi tace"sannu da hutawa malam".

"Yauwa Laylerh an dawo ko?"

"Ehhh wallahi". Ta amsa fuskar ta ba walwala kamar kullum gyaran murya tayi sannan tace

" malam dama zuwa nayi Na sanar maka gobe in sha Allah Zan bar gidan nan".da wuri ya rage volume Na radio da yake sauraro yace "ban... Fahimce Ki ba".ajiyar zuciya tayi sannan tace

" malam a gaskiya Na gaji da abunda Auta ke mini a gidan nan,da ace lokacin da ban gano asali Na bane Zan cigaba da zama a nan Amma tunda yanzu ina da uwa da kuma yaya ni kawai Zan koma Adamawa ".shiru yayi sai kuma taga ya mike yace" biyo ni".ba musu tabi Bayan shi nan suka shige falon sun ko yi sa'a Baaba da Auta duk suna falon"zauna ".yace ba tare da ya kalle ta ba nan ta zauna shima zama yayi tare da gyaran murya" me ya hada Ku da Laylerh? "Ya tambaya yana kurawa Baaba da Auta ido" Au zuwa Kayi Ka Rama Mata abunda aka Mata ne,munafuka Wato Kara ta Kika Kai wajen shi".cikin bacin rai da takaicin halin matar ta shi muryar shi har yana rawa yace"tambayar Ki nake fa".

"In naki amsa maka duka Na zaka yi ne abunda aka yi kuma anyi kuma ba abunda Ka Isa Kayi malam Nifa Na Dade da fahimtar kwadayin abun duniya yasa kake nuna kana son ta don in taje can kada ta manta da Kai banda haka yaushe zaka tsaya Mara Mata baya ga Yar cikin Ka wacce ta dace da shi". Hannun shi Na rawa ya nuna kan shi yace" ni kike fadawa haka a gaban yara?"

"To karya aka maka?" Muryar shi kamar Wanda zai yi kuka yace"Shikenan Ki tattara naki ya naki Ki bar mini gida Na".yana Kai karshen zancen ya fice yana jin ta tana fad'in "yafi nono fari dama wani abun arziki ake samu a gidan naka". Auta ce ta fashe da kuka cikin kukan take fad'in" Laylerh kin kyauta burin Ki ya cika kin raba kan iyaye Na mutanin da suka saka miki da alkhairi ke kuma da sharri Kika saka musu to Allah ya Isa tsakani Na da ke". Mikewa Laylerh tayi cikin sanyin jiki ta nufi dakin ta

"Baaba don Allah kada Ki tafi Na San Zuciya ne yasa Baba fadin haka in ya dawo Ki bashi hak'uri nasan bai da riko zai hakura in Kika tafi fa da Laylerh fa za'a bar ni Kinga ba abunda ba zata mini ba". Komawa tayi ta zauna tana huci tace" wallahi

Auta Nima ban son tafiya ina kaunar malam Amma Na rasa dalilin da yasa Tun shigowar yarinyar nan gidan nan nake mishi abunda rai Na ke so ba".

"Baaba dama zuwa tayi don ta raba tsakanin Ku don haka kada Ki Bari hakan ta kasance".

" in shine burin ta ba zai taba cika ba kuma in sha Allah in malam ya dawo Zan bashi hak'uri "..

°°°°°

Sanye yake cikin plan trouser Ash color dogo har kasa sai boot da ya sanya a kafar shi da Riga Mara nauyi exercise yake yi Wanda a kullum sai yayi don yanayin aikin shi shiyasa ko da yake jalingo malam kan fitar da shi ya motsa jiki..ginenne jiki ne da shi sai zufa yake hadawa gefe kuma PA'n shi ke goge mishi zufa ya kuma mika mishi Ruwa in ya sha sai ya cigaba, a kullum ya kan ware hour daya yayi exercise.. Daga can saman upstairs kuma Sadiya ce ta kura mishi ido tana kallon ko wani motsin shi har murmushi take yi ita daya" Umar Farouq Allah ya baka komai tamkar Kai Kayi kan Ka ina matukar son Ka".ta fadi tana murmushi lokaci daya kuma annurin fuskar ta ya bace bisa karasa exercise da yayi ya shige ciki,a irin wannan yanayin ne kadai take farin ciki banda haka ba abunda ke sa ta farin ciki kuma alhamdulillah hannun ta Na warkewa..

Har kofar dakin Laylerh Baaba da Auta suka je ba irin bugawar da basu yi ba taki ta bude kofar

Ganin haka sai suka juya Laylerh ko tana jin su har yanzu kuma kuka take yi..

Malam ko yana fita waje ya samu ya zauna tare da Ciro wayar shi a aljihu ya lalabuba number'n M Wakili tare da Fara dialing sai dai har ta tsinke ba'a daga ba,yana shirin sake kira wayar sa ya hau ruri yana dubawa ko yaga Alhaji M wakili ne nan ya amsa da sauri,Bayan sun gaisa sai ya Dan yi Jim kadan"malam ina jin Ka lafiya Ka Kira da wannan lokacin ".

" Alhaji dama batun yarinyar nan ne".

"Wacce yarinya kenan?"

"Laylerh ta gama makaranta kuma naji shiru har yanzu baka tada maganar auren su ba".

" to ni in ba yanzu ba ban San ta gama makaranta ba".

"Amma Ai shi Umar Farouq din yana sane".

" to yanzu Ka Bari zuwa gobe Bayan nayi shawara sai muyi maganar".daga nan suka yi sallama gida ya koma ran shi duk ba dadi yana shiga daki Baaba ta fashe da kukan munafurci"Dan Allah malam Kayi hak'uri wallahi sharrin shaidan ne kuma in sha Allah ba Zan sake ba,sannan in dai batun Laylerh ne daga yanzu Na maka alkawari ba Zan sake shiga tsabgar ta ba".banza yayi da ita yayi kwanciyar sa..

A Washe gari ma Laylerh bata fito ba sai yayi tunanin kila don abunda suka Mata jiya ne yana tsaka da karyawa Kira ya shigo wayar shi Na Alhaji M wakili sai dai network ya Hana shi ji da kyau shiyasa ya sa wayar a hands free"Malam a jiya Mun yanke shawarar auren nan da Wata daya tunda ba abunda za'a jira,sannan ban son yawan zirga zirga shiyasa in sha Allah wani sati zamu zo kawo goro da Kayan lefe dukka sannan mu Zan ta sosai akan batun".

"Masha Allah alhamdulillah Allah kawo Ku lafiya".

" Ameen Ameen".Baaba dake rike da abinci a hannu sai ta sake shi a kasa jin Wai an tsaida auren Laylerh da Umar Farouq nan da Wata daya kenan duk maganin da suke yi a banza ne dole ma ta tashi tsaye...

Comment

Share

©Hafciey Musa

[1/25, 5:42 AM] Hafciey Musa😘: *LAYLERH*

(The prettiest emerald)

35

Duk da yana sane da furucin auren Laylerh da Umar Farouq ne ya sata Zubda abun hannun ta Amma ko kallon inda take malam bai yi ba nan ta tattare wajen ta nufi ciki..

A bangaren Laylerh ko sosai jikin ta yayi sanyi da abunda ke faruwa a gidan shiyasa da kyar ta iya shirya kan ta ta fito falon ba kowa don haka sai ta wuce company. Tun a keke napep take jin gaban ta Na fadiwa a ranta take tuna yau kuma Mai zai faru da ita,Bayan an sauke ta sai ta tsaya jiran mota Bayan sun Kai adadin da ake dauka sai suka shiga ciki..office nasu kamar ciki da falo ne ita da abokanayen aikin ta suna falo yayin da sabon Accounter da aka dauka yana daga ciki,ajiye bag nata tayi akan desk nata tana mamakin rashin ganin sauran abokanayen aikin ta shiyasa ta duba agagon hannun ta sai taga Ai ba sammako tayi ba ya kamata ace sun iso.zama tayi gami da rufe fuskar ta da hannu biyu tana tunanin rayuwar ta sai ji tayi an bude kofa ko da ta daga Kai don ganin wane ne sai taga Accounter ne da kuma budurwar shi don mutumin akwai shegen Neman Mata"morning Sir ".ta fada tana sauke Kai kasa tare da jin zafin shi don Wata Rana ma musulmai yake Kawa office din". Waving nata da hannu yayi nan suka shige ciki da bakuwar ta shi ita ko ajiyar Zuciya ta sauke tare da Ciro waya a bag domin kiran Auntyn ta don Tun safe basu yi magana ba kuma ta San ita ce kawai zata iya sama Mata nitsuwa a irin wannan lokacin. Tana kokarin dialing number'n Accounter ya fito sai ta ajiye wayar tare da mikewa da sauri don ganin ya nufo ta" ga wannan Kije shagon madam mery Ki karbo mini chi exotic guda biyu sai rice and stew sannan a sa koyi da cabbage pure water kam akwai a fridge Na office Na".ya Kai karshen zancen sa yana ajiye Mata kudin a desk tare da juyawa ya koma office ita ko dauka tayi ta fice domin zuwa aikan shi,da yake shagon a cikin company'n yake ba tare da bacin lokaci ba taje nan dai aka sa Mata a Leda tare da chanji sai ta juyo zuwa office din..

Knocking tayi"come in".taji muryar mace ta amsa Mata nan ta shiga tana kalle kalle kamar Mai Neman wani abu"kina duba oga'n Ki ne ya fita Ai kuma yace in kinzo Ki ajiye ".jin haka sai ta ajiye a gaban bakuwar ta shi tare da juyawa" ke zo Ki bani cup a fridge ". dauko Mata tayi ta ajiye a gaban ta bakuwar ta tsiyaya ganin ta Fara sha sai ta fice tare da rofo Mata kofa..

Har bacci ya Fara fisgar ta don jiya tsam bata yi bacci ba don damuwa kuma yau ba'a kawo Mata aiki ba taji an bude kofa tana daga Kai taga Accounter ne" ina aikan?"

"Yana ciki". Ta bashi amsa daga nan bai sake cewa komai ba ya nufi office din,shigar shi da sake wani rikitaccen da kuma gigitaccen Kara lokaci guda ne Wanda hakan ya tsoratata a take ta mike sai ganin shi tayi ya fito yana kuka kamar yaro ihu yake tsakanin shi da Allah hakan yasa har yan downstairs suna Jin shi da sauri aka Fara taruwa a office din Ana tambayar shi ko lafiya har da zama yayi a kasa yana kuka Mai ban tausayi Wanda tuni bugun zuciyar Laylerh ya tsanan ta" yanzu kuma me ya faru Na shiga uku Na ni Laylerh ".ko an tambaye shi baya iya magana sai dai ya nuna office nashi da hannu tuni aka nufa ciki har da Laylerh me zasu gani banda wannan bakuwar tashi kwance ba rai a jikin ta ga kumfa a bakin ta Wanda ko ba'a fada maka ba kasan poison ta sha,a take ji da ganin Laylerh yaso daukewa da kyar take iya karanto addu'ar da yazo bakin ta karshe ma zama dirshan tayi a office din

" Accounter me ke faruwa ne Wa yayi kisan Kai a company'n nan".uncle professor yayi tambayar cikin yanayin tashin hankali kowa ido ya zuba mishi yana jiran ta bakin shi sai gani suka yi ya nuna Laylerh da yatsa daga falon office din ita ko tana ciki

"you mean Laylerh ce tayi kisan Kai?"professor ya tambaye shi cikin kaduwa, da Kai ya amsa yayin da ita Laylerh ko ta gagara furta komai

"No hakan ba zai taba faruwa ba Laylerh tayi yarinya da kisa sannan me tsakanin ta da bakuwar Ka da zata kashe ta".sai a yanzu ya bude baki har a lokacin kuma yana hawaye "Nima abunda nake tunani kenan,ga ta Ka tambaye ta ko da Na shigo da bakuwar ita ce kadai a office Bayan wani lokaci kuma Na aike ta shago kan Na dawo kuma sai gawa Na tarar".

" don Ka tarar da gawa baya nufin ita ce tayi kisa kila a Bayan Ka wani ya shigo sannan da alama poison yarinyar ta sha kila wani ne a Bayan Ka ya shigo ya bata ko ita da kan ta zata iya kashe kan ta".jatutu ya fadi

"believe me gaskiya nake fadi".

"Taya zamu yarda da zancen Ka without prove in kana da shaida Ka nuna mana". Uncle Professor ya fada har zuwa yanzu kuma Laylerh da suke rikici a kan ta bata iya furta komai ba

" Sir a duba CCTV".Abokin aikin Laylerh ya fada don ba wanda ya yarda cewa zata iya aikata hakan nan ko aka duba tabbas daga Laylerh ba Wanda ya sake shiga office din sannan yarinyar ba abunda Tasa cikin drink din kenan hakan Na nufin Laylerh ce tayi poisoning abun sha din,unbelievable ba don sun gani da kan su ba ba Wanda zai yarda cewa Laylerh zata yi kisan Kai..

Kan kace wani abu company ya rude labari ya shiga ko wani lungu da sako Na company'n cewa Laylerh tayi kisan Kai ko da Nabeela taji wannan mummunan labarin sai ta fashe da kuka tace tsam Laylerh ba zata iya kisan Kai ba da gudu ta nufi department nasu Laylerh.. Police aka sanar nan suka zo da doctor aka yi duk wani binciken da ya kamata tare da Daukan hoton gawar an kuma tabbatar musu da cewa poison aka sa cikin abinda ta sha,Nabeela Na shigowa duk tarin mutanin nan haka ta nemi hanya da gudu ta fada jikin Laylerh ta fashe da kuka Amma ita Laylerh tamkar gunki don shocked haka ta koma girgiza ta take yi da iya karfin ta"don Allah Laylerh Ki bude baki Kice musu ba ke ce Kika yi kisa ba".ina ba bakin magana sai gawar da ta kurawa ido tamkar tana son gano wani abu nan police suka sa Mata ankwa tare da Daukan ta"Laylerh kiyi magana mana".

"Nabeela ban Sani ba,ban San nice ko bani bace". Wannan furucin da tayi ya Kara tabbatarwa kowa tana da hannu a kisan nan aka dauke ta zuwa jalingo division..

Ganin duk hankalin su yayi nisa kowa Na jimami yasa Nabeela daukar bag Na Laylerh da waya ta fice da gudu tana kuka a lokaci guda kuma take dialing number'n malam don tasan password Na Laylerh

" Assalamu Alaikum Laylerh ".fashewa tayi da kuka" malam Nabeela ce Laylerh an tafi da ita police station Ana zargin ta da kashe Wata".ta Kai karshen zancen tana

sake fashewa da kuka nan take hankalin shi ya tashi jikin shi duk rawa yake yi ya rufe shagon ya nufi police station..

A lokacin har an sata a cell kuka take tsakanin ta da Allah, yana shiga ya tsaya wajen constable "Dan Allah malam wajen yarinyar da aka kawo ba jimawa nazo". Ba tare da ya bar rubutun da yake yi ba yace" kace wacce tayi kisa".cikin rudewa da rashin sanin abunda ya fada yace"Ehhh ita".da hannu ya nuna mishi cell da take da wuri ya karasa wajen tana kallon malam ta mike da sauri "wallahi malam ba nice Na kashe ta ba".

" Na Sani laylerh ba zaki iya kisan Kai ba Amma Ki tsaya nan Bari Na nemi bail naki".cikin kuka ta gyada mishi Kai nan ya nemi ganin D.P.O yin duniyar Allah ba yadda bai yi ba an Hana shi bail laylerh karshe har kuka yayi nan ya nufi gida kallo daya zaka mishi Ka San yana cikin Tashin hankali,mutum daya ne zai iya fidda laylerh a wannan halin kuma ba kowa bane face Umar Farouq Amma kuma ba zai iya fada mishi ba tunda ita din gidan shi zata bai da tabbacin Bayan sun fitar da ita zasu yarda da auren shiyasa ba zai fada musu ba.."Sannu da dawa Baba".tsam hankalin shi baya tare da shi shiyasa bai San da zaman Auta da Baaba a falon ba"malam lafiya me kuma ya faru?"

"Laylerh ce ake zargi da kisan Kai yanzu haka tana hannun yan sanda". Alhamdulillah yanzu kam zata fita a rayuwar mu Baaba ta fadi a zuciyar ta a zahiri kuma sai ta nuna jimami" innalillah to Ai malam can ya kamata kaje a nemi bail nata".

"Naje ba yadda ban yi ba sun Ki,yarinyar nan abun tausayi wallahi". Ya fadi yana share hawaye da Babban yatsar hannun shi,Auta dai gaba daya falon ba Wanda zai ce ya fahimci halin da take ciki mikewa malam yayi don yabi kafan manyan da ya Sani kila a sake ta..

Ganin ya fita sai Baaba ta fashe da dariya" Auta Kinga Umar Farouq ba zai Aure ta ba Shikenan ya zama naki".

"Laylerh ba zata taba kashe mutum ba". A bazata Baaba taji furucin Auta shiyasa ta juya Gare ta da sauri tace

" maimaita abunda Kika fada kin San me kike cewa kuwa hankalin Ki Na jikin Ki kuwa?"ido ta zubawa Baaba cikin gaskiya da gaskiya tace

"Baaba laylerh ba zata yi kisan Kai ba,kiyi tunani me zai sa laylerh kisan Kai in don kudi ne ba Wanda ya Umar baya tura Mata sannan da ace kudi take da bukata da tuni ta kashe shi Ya Umar din in kuma don tsana ne ni nafi kowa cancanta da ta kashe in kuma don yin kan ta ne tsam ba zata iya ba,wani irin cin mutunci ne ban Mata ba Amma tayi hak'uri tabbas wani ko Wata Wanda basu son ta ne suka Mata sharri".ta karashe zancen muryar ta Na rawa kamar zata yi kuka.. Tabbas Baaba ta yarda da batun Auta laylerh ba zata iya kisan Kai ba Amma koma mene ne ita dai hakan ya Mata dadi tunda ta bar rayuwar su,Auta ko har cikin ranta take tausayin laylerh don kisa Babban abu ne shiyasa yadda malam ya kwana bai rintsa ba haka ma Auta gaba daya hankalin ta a tashe yake Baaba ce kawai ta rintsa..

A Washe gari Tun Asuban fari malam ya wuce jalingo division haka Auta ma Tasa Baaba a gaba da suje su duba laylerh don lokaci daya tausayin laylerh ya shige ta da kyar Baaba ta amince nan suka shirya zuwa division din..

Fiddo da laylerh aka yi tana ganin Baaba da gudu ta fada jikin ta tana kuka Mai ban tausayi

" wallahi Baaba ba nice Na kashe ta ba me riba Na in nayi hakan,Wai sai yaushe masifa zai daina bibiyar rayuwa ta Na samu sauki wallahi ban kashe ta ba don Allah Ku fada musu ban kashe ta ba".sosai ta bawa Baaba tausayi nan ta shiga shafa Bayan ta Auta kuma dafa ta tayi sai ta fada jikin Auta suka rungume juna suna kuka,cikin kuka Auta take fadin"Na Sani laylerh bake ce Kika yi kisan nan ba sharri ne ".kukan da Auta take yi ko Na laylerh albarka Wanda hakan yasa laylerh tausayin kanta da kan ta tunda yau Auta ke Mata kuka don halin da take ciki lallai ta cika abar tausayi

" Kai ya ishe Ku haka in kuka kuke so Ku tafi can gidan mutuwa kunzo kun cika mana kunne mtsww ".fadin wani Dan sanda banza suka yi da shi nan Wata mace tazo ta Kama hannunta ta maida ta cell Auta kuka take yi da iya karfin ta suna gab da fita motocin sojoji ya Riga sa Kai cikin division din a take kuwa sojojin suka shiga fitowa inda aka bude kofa sai ga Wata Mata Mai tsananin Kama da wacce aka kashe ta fito,ita din general ce Na sojoji..

General Rebecca 'ya ga professor Emanuel Dalong kamshakin Mai kudi ne shi kuma ita kadai ce Yar shi duk wani dukiyar da ya Tara nata ne a lokacin da tazo service jalingo ne suka hadu da Baban Gloria (wacce ta rasu)soyayya sosai suke yi Amma lokacin da ta gabatar da shi ga Baban ta sai cewa yayi ba zata Aure shi ba Ai tuwon girma miyan nama haka suka cigaba da soyayya har ta samu cikin Gloria sai suka je court suka yi Aure Bayan gama service nata da wasu watanni ta haifi Gloria nan ne ya shiga Neman mata wulakanci iri iri yake Mata ganin haka sai ta nufi gidan su Baban ta kuma yace in har tana so ya amince da ita sai dai ta mayar mishi da Yar shi ta dawo Gare shi ita daya,don tsanar da tayiwa Baban har ya shafi Gloria shiyasa ta maida mishi Yar shi ta Fara rayuwa ita daya sai da labarin mutuwar shi ta riske ta sai ta Fara shirin zuwa Nigeria daukar Yar ta a jiya kuma ta samu labarin anyi poisoning Na Gloria shiyasa ta iso a yau..

Division din tamkar zai Kama da wuta don sojoji cewa suka yi sai dai a basu Laylerh su tafi da ita custody su jin haka yasa Auta fashewa da kuka da yaja hankalin mutani sai ake tambaya su Waye ne nan ne aka ce sune yan ruwan yarinyar da aka kashe,cikin izza madam Rebecca ke taku gashin dokin ta Na zube a gadon Bayan ta kallo daya zaka Mata Ka fahimci halittar ta Na maza ne shake wuyar Auta tayi

"tunda har daya daga cikin Ku ta kashe mini 'ya duk kashe Ku Zan yi".da kyar aka samu ta sake Auta wacce sanda aka yi da gaske numfashin ta ya dawo nan take tayi dialing number'n malam Wanda yaje gidan sarki ko zai sa baki a maganar Ai ko bai samu Samar shiga ba nan ta sanar da shi komai..

Dama har yanzu ba'a mishi iso ba ficewa yayi a ran shi yake raya lokaci yayi da zai sanar da Alhaji M wakili in ba haka ba komai zai iya faruwa.. Dialing number'n yayi Bayan sun gaisa sai yace

"Alhaji don Allah alfarma nake nema a wajen Ka wannan yarinya laylerh ce ake zargi da kisan Kai yanzu haka tana police station komai Na iya faruwa ".mikewa yayi daga kujerar office nashi da yake zaune yace" innalillah garin yaya?"

"Wallahi a wajen aikin ta ne hakan ya faru?"

"Aiki?dama tana aiki ne? ba Na sanar da Ku cewa ban son mace tayi aiki ba".

" Kayi hakuri Alhaji da izinin Umar Farouq ta Fara aiki".katse kirar yayi yana duba time sannan yayi dialing number'n Umar Farouq

"Umar nan da minti talatin Na same Ka a gida".

" Abba kasan duk yan headquarters namu a Villa muke sallar juma'a tare da General Buhari kuma Ka San kan Na fita a wajen zai dau lokaci and ina da aikin yi a cikin gari da zaran Na bar villa".

"Nace nan da minti talatin Na same Ka a gida umarni ne ba shawara ba cikin ni da aikin Ka sai Ka zabi daya". Dib ya katse kirar,shiru Umar Farouq yayi yana tunanin to me kuma ya faru..

Ko da suka idar da sallar juma'a gida ya nufa sanye yake cikin jumper fari sal da hula Fara sosai yayi kyau,Bayan driver yayi parking sai ya fito da alama Abba ma ya dawo shiyasa ya nufi cikin gidan Kai tsaye

" Assalamu Alaikum ".mikewa Abba da Aunty Hauwa suka yi cikin tafasan Zuciya Abba ya dube shi

" yanzu har Ka Kai Ka fini iko a cikin gida Na yaushe Ka girma Umar, Ince yarinyar nan nice Na zaba maka ita Na kuma Hana ta aiki Kai da yake Ka fi ni sanin me kake yi sai Ka bata izinin yin aiki".

"Abba in hakan da nayi ya bata maka rai Ka gafarce ni". Ya fadi kan shi a kasa

" hmm to Ai ga abunda Ka jawo yanzu haka tana police station Ana tuhumar ta da kisan Kai kuma komai zai iya faruwa ".da sauri ya dago yana kallon Abba a saman labban shi ya maimaita" kisan Kai"don ya San ya mutum yake ji in aka daura mishi wannan laifin tunda shima ya taba shiga wannan hali..Sadiya da Tun shigowar Umar Farouq gidan ta sauko falon kasa ce tace

"Abba ba lallai zargin ta ake ba ita ma zata iya aikatawa Ai".wani kallon tuhuma Umar Farouq ya Mata da Abban kan shi don sai yanzu yayi da Na sanin ajiye Sadiya a gidan shi shiyasa cikin tafasar Zuciya ya hau sama Aunty Hauwa ma bin shi tayi don bata da ta cewa..hannu Umar Farouq ya hada inda yayi tafi daya zuwa biyu sannan yace

"weldone Sadiya aikin Ki yana kyau,Ai dama nasan Sadiya ba zata taba zama shiru ba". Yana zancen ne lokacin da yake nufar ta hannu yasa ya shake wuyar ta tare da manna ta da gini sannan ya zuba idanun shi cikin nata

" na rantse miki da sunan Allah ko da cizon sauro ne Na samu a jikin ta wallahi wallahi sai kin yi Dana sanin zuwa duniya don wannan Karon kin debo ruwan dafa kan Ki da kan Ki".yana gama fadin haka ya hankade ta ta fadi kasa sannan ya haura sama zuwa third floor, zaune ya same su duk sun yi jugum waje ya nema tare da zama sai ya dubi Aunty Hauwa ita ko cire Kai tayi alamar tana fushi da shi saboda duk shi ya ja musu sai kuma ya maida duban shi ga Abban shi da yayi shiru cikin sanyi yace

"Abba Dan Allah Kayi hak'uri ban taba tunanin haka abun zai zama ba".

"Ehhh Alhaji gaskiya ya fada kamata yayi a nemi hanyar da za'a fitar da ita kan maganar yaje court".ya sani a duk lokacin da yayi laifi ta kan kare shi shiyasa yake jin ta a ran shi.. Jin ya musu shiru dukkan su sai Umar Farouq ya fita direct bangaren shi ya nufa a bakin gado ya zauna yana tunanin me abun yi,waya ya dauka ya Kira

" a mini booking jet nan da hour biyu zuwa Taraba".shirye-shiryen tafiya ya Fara nan ya Kira abokanayen shi biyu ya sanar da su da kuma securities Na jalingo kowa ya San da zuwan shi shiyasa suka zauna cikin shiri, Abba ma ya Kira mutanin shi ya sanar da su don tare zasu cikin abunda bai fi hour daya ba sun kammala shiri nan motoci uku suka musu rakiya zuwa airport su goma zasu don akwai abokanayen shi biyu da kuma securities sai mutanin Abban shi da Abban kan shi..

Ko da suka yi landing motoci goma suka zo Daukan su don Umar Farouq ba karamin mutum bane securities ne ta ko ina nan suka hada convoy tare da sake jiniya motocin gudu suke kamar zasu tashi sama ba abunda zaka gani sai dai gilmawar motocin ga jiniya dole ake hauce musu a hanya a haka suka iso cikin division din har zuwa lokacin kuma madam Rebecca Na nan don Tun dazun take fama da D.P.O ya bata laylerh yaki..

Duk motocin aka zubawa ido Ana mamakin su wane ne nan take securities suka fito aka budewa Umar Farouq d'in kofar..da yake already madam Rebecca ta dauko commissioner of police zuwa division din nan take aka shiga meeting inda Abba da Umar Farouq din ne sai abokanayen shi biyu da kuma madam Rebecca.. Duk yadda zasu yi sun bi Amma da yake ba'a bada bail din irin wannan case sai aka Hana su bail Na laylerh shi dai Umar Farouq shiru yayi yana nazarin commissioner of police..

ko da commissioner of police zai fita sai Umar Farouq ya bishi"so nake naji ya nauyin asusun bankin Ka yake".ya tambayi commissioner of police likacin da suka jera suna tafiya commissioner of police ya tsinkayi muryar Umar Farouq "A cike take dam".

" in ko ta samu Karin da jin su zai iya dakatar da kunnuwan Ka daga aiki Na wasu mintuna fa".da sauri commissioner of police ya juyo yana kallon Umar Farouq Wanda ya tamke fuska kamar bashi yayi maganar ba"me kake so ayi maka Sir".

"Ni din security ne Na Sani bai dace a same ni da cin hanci ba to Amma wannan yarinyar tabbas ba ita tayi wannan kisan ba,Zan baka kudi masu yawa sannan Ka toshe bakin mahaifiyar yarinyar da ta mutu da fadin za'a dauki mataki ita kuma wacce ake tuhuma Ka bani bail nata Zan cigaba da bincike ba tare da ita kan ta ta Sani ba".

" ohk sir".juyawa yayi ya koma inda suka yi meeting din yace da Abban shi zasu iya Komawa masaukin su Na hotel don dare ya Fara yi,Abban shi yasan wanene Umar Farouq da kuma abunda zai iya yi shiyasa ba musu duk suka wuce hotel din..

A bangaren commissioner kuma da yake kowa ya San yadda kasar tamu Nigeria take komai sai da cin hanci shiyasa ya yaudari madam Rebecca da fadin tayi hak'uri taje gida za'a shigar da case din court ta kuma yarda da abunda ya fada sai ta

tafi..tafiyar ta ba jimawa aka fiddo da laylerh da gudu ta fada jikin Baaba, Baaba ko ikon Allah take gani dubi yadda Umar Farouq ya canza cikin shekara biyu mutumin da ya zauna a gidan su na kusan shekara Amma dubi yadda ya koma tayi imani yanzu in tace ta San shi za'a ce karya ne ba abunda ya bata mamaki kamar yadda ya gaishe ta sama-sama ya tafi..

Mota daya aka bar musu ya maida su gida duk shiru suka yi a motar kowa da abunda yake damun shi,koda suka Isa gida har daki Auta ta daka laylerh sai bata baki take Amma a banza don laylerh a kwance take bata da aikin yi sai kuka Gashi har yanzu iyayen ta basu San da batun ba..

A can hotel kuma Bash ne Abokin aikin Umar Farouq kuma aminin shi yace

"Farouq ina ji ya kamata Kayi magana da ita don jin ta bakin ta kasan dai mahaifiyar yarinyar ba zata bar maganar nan ba in taji an sake ta".shiru yayi kamar ba zai ce komai ba sai kuma ya janyo waya ya Fara dialing number'n Baaba tana picking yace

"an wuni lafiya ".cikin tabe baki da jin haushin abunda ya Mata dazun tace" lafiya ".

" dama so nake Na sanar da ke ina tafe Anjima in Allah ya yarda".da sauri tace"to to Allah kawo Ku lafiya ".nan ya katse kirar ita ko jiki Na rawa ta nufi dakin Auta

" ke tashi kiyi wanka Ki shafa powder sannan kisa wancan atampar taki da take matse Ki Umar Farouq Na tafe".

"A Daren nan?"

"Eh yi maza Ki shirya kafun su iso".

" Haba Baaba a irin wannan halin da muke ciki yaushe Zan tsaya gyara Ai sai ya tsane ni yace banda imani".

"Dallah rufewa mutani baki dama ce fa Kika samu gwara kiyi amfani da shi Ai bance kiyi kwalliyar yadda zasu gane ba". Shiru tayi don har karkashin zuciyar ta bata jin zata yi wanka don ta burge Umar Farouq duk da tana son shi" to Baaba zanyi".

"Yauwa Yar albarka". Tana ganin Baaba ta fice ita ko dakin laylerh ta nufa yadda ta bar ta haka ta tarar da ita" Kinga laylerh Dan Allah kukan ya Isa haka tashi Ki yi wanka sai kici wani abu".

"Auta ban jin Zan yi wankan nan".

"Jiya fa haka Kika wuni sannan yanzu Kice a haka zaki kwana Ai jikin Ki zai Hana Ki bacci Dan Allah Ki daure Ki watsa Ruwa sai kizo kici abinci". Ganin yadda Auta ta damu da ita take kuma nuna tausayin ta yasa ta mike ta shiga toilet nan Auta ta fice ita ma dakin ta ta shiga wanka ta fesa tare da sa powder kadan yadda ba zai fita ba sai atampa da ta sa Wanda ya matse Boob's da hips nata dankalin daurin tsoffi ta mishi sai ta nufi dakin Baaba, hayaki Baaba ta Mata

" maza je Ki karkabe falon Ki fesa turare yanzu dai sun kusa tunda Kinga dare nayi".falo ta wuce ta gyara kamar yadda Baaba ta umarce ta Bayan ta gama sai ta zauna nan ne kuma laylerh ta fito tayi wanka sanye take cikin gown atampa da yake kanta ba'a raba shi da acuci sai hula da Tasa,gown din yabi shape Na jikin ta ya zauna..Auta Na ganin ta ta nufi dining tea ta hada Mata ta kawo"Nifa gaskiya ban fiya son tea da madara ba don ina jin Tashin Zuciya in Na sha".

"Ke fa Kika ce baki jin cin abinci shiyasa Na miki tea Ki daure Ki sha ba don ran Ki Na so ba". Karba tayi ta Kai baki sai taji sugar bai ji ba nan ta mike sugar ta Kara tana gauraya tea din Baaba ta fito" Yauwa....."sai kuma ta hadiye sauran maganar ta don tozali da laylerh da tayi"Ashe dai anyi wanka ".ta fada tana hararar laylerh sannan ta mayar da akalar zancen nata ga Auta" Yauwa kin gama kimsa ko ina ko yanzu zasu shigo ".haka kawai sai taji gaban ta ya fadi sannan koma wanene zasu shigo din jikin ta ya bata ba Mata bane maza ne shiyasa ta mike domin dauko hijab a daki,tana Isa tsakiyar falon taji muryar da ta shaida Na wanene a take kuma ta Kara saurin tafiyar tata sai dai ta makara don yana shiga falon idon shi bai fada ko ina ba sai kanta duk da bai San wacece bane tsakanin su biyu din tunda baya ta basu..Bash ne ya matso kusa da shi cikin dabara ya juya kamar Mai duba wani abu

a baya sai ya rada ma Umar Farouq" Farouq kana ganin yarinyar can,dubi yadda Bayan ta yake cike ni dai in ba ita ce madam taka ba wallahi nayi kamu don hips kam Masha Allah ".cike sa takaici da kuma haushi Umar Farouq ya buge shi yadda ba wanda ya Lura sannan suka shiga falon Bayan Auta ta amsa musu sallama..

Koda ya sauke idon shi akan Auta ya shaida ta don haka kenan wacce ta shige ciki laylerh ce,murmushin gefen baki yayiwa Auta lokacin da yake zama don yarinyar ta mishi halacci duk da a mahaukaci yazo gidan su bata taba kyamatar shi ba

" Yaya sannu da zuwa ".ta fadi cikin tsananin farin ciki,fuskar shi a hade kamar yadda yake kullum tsabanin yadda ya Mata da farko yace" uhum".Haba zo kuga dadi wajen Baaba da Auta don a ganin su hayaki ne yake aiki,juyawa yayi ga Baaba suka gaisa haka ma Bash,duk zancen da suke laylerh Na jin su haka kawai sai taji hawaye Na zubo Mata Bayan duk abunda ya faru da ita su har suna iya dariya da yan uwan ta ne ta tabbatar jimami zasu taya ta shiyasa ta fasa fita falon ta koma dakin ta..

A falon kuma Auta ce ta mike drinks da malam ya sayo da faro ta kawo musu tare da fad'in "bismillah". Gyaran murya yayi sannan ya kalli Baaba" Ashe ga abunda ya faru".cike da jimami kamar da gaske tace"Ehhh wallahi Allah dai ya kiyaye gaba".

"Ameen". Bash ya amsa.

" ina ita yarinyar take?"ya tambaya yana Danna wayar shi kamar bashi ne yayi tambayar ba"tana ciki Bari Na dubo ta".Auta ta fada duk da ranta ya tsoyu da ya ambaci laylerh, kwance ta tarar da ita"laylerh kizo ya Farouq Na Kira".

"Kice da su nayi bacci".

" sun fa ga shigowar Ki daki".mikewa tayi tana tsaki tabi Bayan Auta suna shiga falon kuma Tasa Kai a kasa can gefe ta zauna, "sannun Ku da zuwa". Ta fadi cikin muryar ta da ta dishe da kuka har baya fita sosai". Bash ne ya amsa Mata yana duban ta sai dai yadda ta sauke Kai baya iya kallon fuskar ta Umar Farouq ko tamkar baya falon hakan ya Dada sa Baaba farin ciki,mikewa Baaba tayi ta basu

waje shiru ne ya biyo baya Auta sai mamakin sauyawar Umar Farouq take dama haka yake da kyau" garin yaya hakan ya faru?"ya tambaya har yanzu kuma baya kallon ta,ita ko takaicin shi take ji shiyasa taji kuka yazo har wuyar ta ko da tayi kokarin magana sai taga kuka zata yi shiyasa tayi shiru daga shi har Bash kuma sun fahimci haka shiyasa Bash ya dafa shi yana daga Kai kuma sai ya mishi alama da ido kan cewa su je waje..kamar ba zai je ba sai ya mike ya fice "Kinga tashi Ki bi shi zaku yi magana a waje". Bash ya fada yana maida hankalin shi dukka a kan ta cikin sanyi ta mike tabi Bayan shi..

.ko da ta fita a falon sai taga tafiya kawai yake sai bata ce da shi komai ba taci gaba da bin shi har ya Isa inda yake bi ya fita lokacin da yake gidan sannan ya tsaya, kujeru biyu ta dauko tare da ajiye nata nesa da nashi zama yayi lokacin da yake fadin

" so nake Ki mini magana cikin nitsuwa ba tare da daga murya ba me ya faru?"kanta a kasa tana wasa da bakin hijab nata tace

"ba nice Na kashe ta ba".

" Mai ya faru?"ya kuma maimaita Mata tambayar yana Danna wayar hannun shi yanzu ne kuma ta fahimce shi Wato so yake ta fada mishi komai da komai Amma ya kasa bude baki ya tambaya

"shekaran jiya ko da naje office ba kowa a department namu sai daga baya ne Accounter yazo da budurwar shi shigar su ba dadewa ya fito ya aike ni Na sayo musu abinci koda Na kawo baya nan sai Na ajiye Mata Na fice".

" me dalilin Ki Na kashe ta".ya jefa Mata tambayar idanun shi a screen Na wayar shi

"Wallahi ban kashe ta ba".

" kina da personal issue da Accounter din ne?"

"Ban gane ba".

" I mean saurayin Ki ne ko kuma kina crushing nashi Kinga wannan dalilin zai sa Ki kashe ta".

"Accounter Babban mutum ne don zai yi hamsin me zai hada ni da shi sannan kowa ya San shi da Neman Mata".

" wacce Kika saya abinci a wajen ta sun San juna ne?"

"Duk company'n ba Wanda bai San ta ba don a wajen ta ake sayan abinci". Shiru yayi yana nazarin maganar ta can yace

" kuma ba Wanda kuke sa'in sa da shi a company'n? ".Kai ta girgiza

" think carefully cux sau daya Zan tambaye shi tunda ba zaman Ki nake yi ba ".

Ikon Allah wato shi tsam ba'a zaman lafiya da shi ta fadi a zuciyar ta sai kuma ta fara tunani da sauri tace

"Sulaiman ".

" wane ne shi?"

"Boss nane Ka tuna nace maka Na taba aiki a company'n aka Kore ni to shi ne". Nan ta zayyano mishi daga farkon haduwar ta da Sulaiman har korar ta da aka yi don tuhumar ta da sata".cikin tsawa yace

" me yasa tsam ba hankali da nitsuwa a jikin Ki?har ni zaki yiwa karya don rashin kunya".take idanun ta ya kawo kwalla don dama ba daina kukan tayi ba,cike da takaicin ta ji yake kamar ya make ta yarinya da girman ta sai shegen kukan banza da a can cell din ma aka barta yaga ta tsiya sai yace

" shine number one suspect Na".daga nan shiru ne ya biyo baya sai Bash ne ya fito "wow wallahi Farouq baka ga yadda kuka dace ba".

Sai a lokacin kuma ya iya daga fuska ya kalle ta Tun farkon zaman su,cire Kai yayi daga duban ta nan bash ya Karo su" kaga dare yayi gyara Na muku Hoto ".Kai ta girgiza cike da tsoron shi da kuma kunya har zata Mike sai kuma ta saci kallon Umar Farouq da ba ita yake kallo ba..idon ta a kan shi yake amma tunanin ta ya tafi ga Naseer tsab Naseer ya dawo Mata ran ta suka yi Hoto shiyasa ta mike a guje ta shiga falo ta kofar kitchen tana danne kukan da yake son kufce Mata..

"Dude wallahi Kayi dace Gata yarinya sannan dubi yadda take da kunya wallahi yaran Ku zasu yi kyau Musamman in suka dauko idon ta". Ji yayi kamar ya cize Bash din sai ya danne bacin ran shi nan suka fice don Bash ya sallami cikin gida..

A bangaren Sulaiman ko ya tafi wani aiki a sardauna akwai abunda suke son suyi establishing nashi shiyasa ko da aka yi kisan Kai din an yi ta trying numbern shi ba'a same shi ba don can ba network Na MTN sai kawai professor ya sanar da Mommy Sulaiman, sosai tayi mamaki duk da Dan Adam baka Isa yanke mishi hukunci ba Amma haka kawai take ji a jikin ta laylerh ba zata yi kisan ba..sai a yau ya dawo kuma da labarin ya Fara cin Karo shiyasa yayi murmushi a fili yace" in har Na amsa suna Na Sulaiman sai Na ingiza case nan an tafi court in ba haka ba kuma ni ba Dan Hadeeza bace...

Comment

Share

©Hafciey Musa[1/25, 5:42 AM] Hafciey Musa😘: *□LAYLERH□*

(The prettiest emerald)

36

Phone nashi ya Ciro a aljihu sannan yayi dialing number'n uncle professor bugu biyu ya daga"Hello Sulaiman yaushe Ka dawo".

"Ban jima da shigowa jalingo ba sai kuma naji labarin abunda ya faru a company". Cikin jimami uncle professor yace" Ehhh wallahi dukkan mu ba Wanda ya taba tunanin Laylerh zata aikata haka".

"But uncle garin yaya hakan ta faru?". Nan ya labarta mishi duk yadda aka yi,duba agagon hannun shi yayi ganin da sauran time sai yace" Alright gani nan shigowa company'n yanzu ".sallama suka yi nan yayi wanka yasa suit nashi sai ya nufi company wannan Karon shi daya yake driving don zai yi zirga-zirga dayawa ya San driver ba zai mishi yadda yake so ba..ko da security ya Gan shi shi daya sosai yayi mamaki nan ya wangale mishi gate direct admin block ya nufa" welcome Sir ".ake ta fada mishi daga downstairs din bai kula ko wanne daga cikin su ba ya wuce upstairs har office Na Accountant, jikin Accountant Na rawa ya mike yana Mai nuna mishi kujera" welcome Sir ga waje zauna".zama yayi yana karewa office din kallo

"a Kira mini duk wadanda suke aiki a karkashin Ka".landline ya dauka ya Kira wadanda suke falo Wato abokanayen aikin Laylerh ba jimawa kuwa dukkan su suka shigo a kasa suka zauna

"ina kuke lokacin da Laylerh tayi kisa?" Shine tambayar da ya jefa musu

"Sir gaba daya bamu department nan a ranar don ni ina livestock department ganin ba aiki shi kuma wannan bai zo ba".kallon cikin idon su yake yi don son gane gaskiyar abunda suke fada sai uncle professor ne da suke tare yace

"gaskiya suka fada Sulaiman ranar basu nan abun ya faru".shiru yayi Na wani lokaci sannan yace "zaku iya tafiya". Da wuri suka mike ko wannen su ya fice..

Juyowa yayi ga Accounter

" and you me alakar Ka da wacce aka kashe da kuma Laylerh ".Kai yake sosawa don kowa ya San shi da Neman Mata sanda Sulaiman ya buga desk din cikin bacin rai ya kuma maimaita tambayar shi

" Sir girlfriend Na ce".

"Girlfriend sannan Ka rasa inda zaka kawo ta sai company ita Laylerh kuma fa?"

"I got nothing to do with that girl ban San reason nata Na kashe Gloria ba".cikin kallon tuhuma Sulaiman yace" Accounter Na San zaka Kai shekara hamsin,sannan Gloria ba zata wuce Ashirin ba mom nata Nada arziki sosai me zai hada ta da mutum irin Ka?"

"Sir ina son ta ne kuma ita ma haka".

" what ever yanzu so nake a Kai ni gidan mom nata".ya karashe zancen yana mikewa tsaye Accountant kuma ido ya zaro yana fad'in "Sir wallahi ina tsoro in har ta San nine Na kawo Yar ta company'n nan aka kashe ta she won't spare me". Ba tare da ya kalli Accountant ba yace

" Ai Kai ma akwai ayar tambaya a kan Ka so just get Ready kuma yanzu nake so mu tafi".sosai cikin Accountant ya dau ruwa tsam bai yi tunanin Sulaiman zai yi haka ba tunda Ai ba shi yayi kisan ba kamata yayi a nemi Wanda yayi kisa Amma kuma sai ace yayi rakiya zuwa gidan matar da bata da imani ta kuma rantse duk Mai hannu a kisan Yar ta sai taga Bayan shi..

Ba don ran shi yaso ba yabi Bayan Sulaiman uncle professor zai bi su sai Sulaiman yace "No uncle Ka tsaya a nan ni zanje Na jajanta Mata abunda ya faru don nasan har yau ba Wanda ya jajanta Mata on behalf of this company".

" Alright Allah ya tsare".Ameen yace nan ya shiga mazaunin driver Accounter kuma ya zauna a gefen shi gaba daya gumin yake hadawa Amma sai Sulaiman yayi banza da shi kamar bai San da zaman mutum a motar ba illa sauraron shi da yake yi in ya fadi direction da zasu bi..

A haka har suka iso kofar gidan ta parking Sulaiman yayi daga gate din kuma yake hango sojoji kuma ya tabbata sai yayi da gaske zai samu shiga,zuwa lokacin kuma Accountant ya gama fidda rai ga rayuwa nan Sulaiman ya bude murfin kofar ya fita a gate wajen sojojin ya tsaya"weldone Sir ".yace da sojan dake kare mishi kallo" yes how may I help you".shiru yayi yana tsara zancen da zai fada a zuciyar shi sai can yace

"Suna Na Sulaiman Kuma nine CEO Na company'n da aka kashe Yar madam Rebecca nazo ne don mu tattauna kan batun ko zaka mini alfarmar ganawa da ita".

" no Ka koma wani lokaci kana iya dawa yanzu madam bata da lokacin kowa".hannu biyu ya hada alamar pleading yace"pls Sir ganawa da ita yana da amfani sosai".waya Sojan ya cire yayi kiran ta basu jima suna magana ba ya katse kirar"tace I should let you in".

"Na gode sosai". Ya fada yana Mikawa sojan hannu suka gaisa mota ya koma inda Accountant ke zaune sai addu'a yake Allah sa kada a Bari su shiga" zaka iya Komawa office ".daga nan ya juya da wuri Accountant ya fice shi ko har zai shiga gidan ya Danna key'n motar nan motar ta kawo wuta tare da yin Kara alamar an rufe ta..

A dakin baki ya zauna ya Kai minti goma kan madam Rebecca ta fito yana ganin ta ya mike tsaye" sannu madam".fuskar ba annuri da gani kuma tana jimamin mutuwar Gloria tace"have a seat".zama yayi tare da yin gyaran murya

" Suna na sulaiman nine CEO na natures pride farm,da farko dai madam Zan Fara da baki hak'uri Na rashin zuwa gaisuwa akan lokaci hakan ya faru ne bisa bana gari but....".bata Bari ya Kai karshen zancen nashi ba cikin daga murya tace "but me wannan wani irin company ne da zaku Tara ma'aikata Amma tsam ba security ace har za'a iya kashe mutum a ciki sannan Wai ace kuna can Kai da Mom naka ba abunda ya dame ku a tunani Na zaku daga hankalin Ku sosai Amma da yake ba Yar Ku aka kashe ba sai yanzu zaka debo jiki kazo mini jaje".ido Sulaiman ya zuba Mata

yau dai yaga wacce tafi shi bala'i,ita ko cigaba tayi" Ku saurare ni Bayan Na gama da ita yarinyar company'n Ku Zan Rusa".tana kaiwa nan ta dauki Ruwa dake gefen ta ta sha

"madam pls abi abun nan a hankali company'n mu bata da hannu a ciki".

"Ba dole kace haka ba tunda kasan Zan iya aikata hakan Ai ita Mom naka ma bata ga ta zama ba kamata yayi ta tashi tazo har jalingo Amma tana can tana business nata". Hak'uri ya cigaba da bata Amma tsam taki sauraron shi ya kuma Lura tana da kafiya,mikewa tayi zata tafi nan shima ya mike yana fad'in" what in nace miki an bada bail Na yarinyar da ta kashe miki daughter ".

cak ta tsaya da tafiyar tare da Juyowa murya Na rawa tace" maimaita abunda Ka fada".

Murmushi yayi ganin anzo gabar da yake so yace "Ehhh an bada bail nata Tun a ranar da Kika bar police station din".

" Jesus da ni madam Rebecca suke zance ".ta fada tana buga kirjin ta sannan ta cigaba" tunda har haka suka yi I promise case nan ba zai tsaya a Taraba ba Lagos Zan Kai karar su har ni zasu nunawa court sun San case nawa nake da shi a court ".Kai ya girgiza Mata" case uku nake da shi a court daya Na dukiyar mahaifi Na daya Na sarautar garin mu daya kuma sirri ne sai an yiwa Gloria justice in ba haka ba suna Na ba Rebecca ba".

"Ma'am kada kiyi haka naga alamar yarinyar tana da influence Amma ban San ta ina ba so nake mu hada hannu da hannu don Nima ina da personal issue da ita kuma so nake a daukarwa Yar Ki fansa".

" what's that your name? "Da wuri yace" Sulaiman ".

" Sulaiman ba Zan bar case nan a Taraba ba".

"Ma'am trust me nasan judiciary a nan sosai I promise you za'a yiwa Yar Ki justice".

" fine Zan baka wannan damar in Kayi failing kuma gaba Zan Kai".rusunar da Kai yayi yace"Na gode sosai ma'am".daga nan ya fita yana wani mugun smile direct high Court ya wuce a take kuma ya shigar da karar ta hanyar Barrister Ali waru.

Bayan ya kammala komai Na court din ya kuma tabbatar a ranar za'a turawa Laylerh sammaci sai yake jin nishadi yana shiga mota yasa music yana bin music din tsintar kan shi yayi cikin wani nishadi da ya Dade bai ji irin shi ba ko ba komai lokaci yayi da zai batar da ita a Daron kasa da yardar Allah, wayar shi ne yaji ya Fara ringing hannu yasa ya daga*my Dad*ne yayi appearing a fuskar wayar,katse music din yayi yana karewa wayar kallo fiye da shekara biyu wannan number'n bata bayyana a fuskar wayar shi ba sai yau shi yayi tunanin an daina amfani da layin ma..har kirar ta katse bai samu damar dagawa ba sai ga wani kiran ya shigo parking yayi a gefen titi sannan ya daga"Sulaiman ".shine abunda ya Fara ji an Kira cikin kakkausar murya akan ayi sallama" Na'am sir".

"Sulaiman". Ya kuma Kira a Karo Na biyu" Yes Ranka shi dad'e ".

" Sulaiman sau nawa Na Kira sunan Ka?"

"Sau uku".

" yaushe rabon Ka da gida Na,naji ance ya Kai shekara ".

" shekara uku ne".

"Ashe ma yadda naji zancen ba haka bane to in har Kai din Dan halal ne ba zina Hadeeza tayi ta haifo Ka ba Na baka nan da kwana biyu Ka dawo gida,Wai har Hadeeza ta Isa ta raba ni da Kai".

" Baba bana Maiduguri fa ina Taraba ".

" koma yaya ne Na fada maka in kuma Kai din Dan shege ne ba ta hanyar Aure aka samo Ka ba kada Kayi yadda nace ".katse kirar mahaifin shi yayi shi ko Kai ya kifa a steering motar yana Mai jin takaici akan me za'a ce ya koma gida shi da yanzu zasu Fara case da Laylerh da wuri ya Ciro wayar shi yayi dialing number'n Mom nashi

" Hello mom akwai matsala ".

" wace irin matsala kuma Sulaiman me ya faru akan case din?"

"Mom ba akan case din bane Baba ya Kira ni yace ya bani nan da kwana biyu Na koma gida". Shiru tayi har yayi zaton ko network ne shiyasa yace

" Mom kina ji Na?"

"Sulaiman lokaci yayi da zaka zabi tsakanin ni da mahaifin Ka,in har Ka koma Maiduguri wajen sa to Ka Sani ni Hadeeza Na yafe Ka har Abada in kuma zaka zauna da ni bismillah". Daga haka bata Kara cewa komai ba sai wayar da ta katse

" Hello Mom!Mom!"

Jin shiru sai ya Ciro wayar a kunnen shi ganin ta katse sai ya naushi iska Allah ma ya Sani ba zai iya Komawa wancan bahagon gidan inda aka musgunawa mahaifiyar shi ba..

Zakari Kurnari Asalin Dan Biu ne kuma ya kasance Babur ne shi, shine mahaifi ga Sulaiman matar shi ta farko sunan ta lauratu wacce sun shafe shekaru tare kan ya auro Hadeeza zaman amana suka yi da Lauratu ba Wanda yake jin kan su sai dai hausawa sunce zo mu zauna zo mu Saba wannan yasa wani lokacin suke samun

tsabani,Allah yayiwa Lauratu rasuwa sosai Hadeeza tayi kuka don tayi rashi Bayan wasu shekaru kuma ya auro Wata Mata Mai suna Ladidi,tunda ladidi ta shigo gidan sai Hadeeza ta koma wahala a gidan..

Ba wani Mai kudi bane amma dan siyasa ne ya dai taba rike makamin commissioner yana kuma karkashin wani minister ne..

Ladidi tazo da agola har biyu gidan haka ma Hadeeza lokacin yaran ta biyu kuma suna zaune ne da Wata kanwar mahaifin shi..gaba daya gidan sai abunda ladidi tace ake yi don gaba daya ta mallake shi har kanwar shi da mijin ta ya rasu zaman hak'uri take da Ladidi,agolan da tazo da su kuma duk sun fi su Sulaiman iko da gidan don ko rashin lafiya Sulaiman yayi yi da an tambaye shi kudin magani sai yace Allah kawo, in kuma agolan Ladidi ne har asibiti zai Kai su bama chemist ba..

Duk da wadannan Abubuwan da Ladidi ke yi haka Hadeeza ta cire ido don Wata Rana ko Ladidi ce da girki sai taki fitowa dole Hadeeza ce zata yi girkin ta Sawa kanwar mahaifin nasu su Ladidi kuma a inda ta Bari a nan zata zo ta samu don take away Zakari yake Mata ita da agolan ta..

Ana haka har Ladidi ta samu ciki iya shege iri iri take yi Hadeeza ce ke girki kullum Amma miji baya kwana a dakin ta sai dai a dakin Ladidi daga karshe kam sauke Mata girki yayi tsam mu'amalar Aure baya shiga tsakanin su ko omo'n wanki baya bata kudi ta saya a sallah kuma in anyi yanka sai ya haramta Mata nama ita da dan ta,a duk lokacin da tace ta gaji da gidan zata tafi sai kanwar shi tayi ta bata hak'uri da nuna Mata in ta tafi ta bar yaron ta fa wahala zai sha..

Ladidi ko lokacin da cikin ta ya Kai haihuwa sai ta haifi Yar ta mace..

A Washe garin suna aka nemi Yar Hadeeza aka rasa a karshe sai gawar ta aka kawo Wanda ta tabbata Ladidi Nada hannu a ciki shiyasa ta tashi tsaye ta Kai karar Ladidi gaban manya Amma da Zakari yaji sai ya Mata duka a Daren kuma ya sake ta saki uku Ladidi da yaranta kuma suka yi watsi da Kayan Hadeeza da farko taso barin Sulaiman a gidan Amma ganin yadda yake kuka kamar ranshi zai fita yana fad'in "momy Zan biki ba Zan zauna da su ba". Sai tausayin Yaron ya kamata nan kanwar mahaifin shi tace" Hadeeza Ki tafi da Sulaiman in ba dai so kike shima Ki rasa shi kamar yadda Kika rasa Yar Ki ba Ladidi bata da imani Gashi makaho zai wahala

Kinga Nima ban Isa Na tanka a gidan nan ba ".nan Sulaiman ya cigaba da kuka yana rike kafar ta Zakari Na ganin haka ya kwace Dan shi don shi ne kadai da namji Gare shi,ganin sai tirjewa Sulaiman yake yi sai yace" in har Ka bi momyn Ka kada Ka sake dawa gida Na Na yafe Ka".da gudu ya nufi Hadeeza don yana jin inda kamshin ta ke fitowa nan suka bar gidan daga wannan lokacin kuma mahaifin shi bai sake sanin ci da shan shi ba har ya mallaki hankalin shi,a ranar da Hadeeza ta bashi dama yaje gidan mahaifin shi sai aka yi rashin sa'a lokacin mahaifin ya tafi kasar waje tare da minister kuma dama ya Kira shi ne don ya kula mishi da shagon shi don zannuwa yake saidawa sai kuma Sulaiman din yazo a makare,daya daga cikin agolan ne ta mishi rashin kunya don yanzu sun girma sosai nan ya Mata duka daga wannan ranar kuma bai sake zuwa gidan ba don yasan karamin aikin Baban shi ne ya Rama Mata tunda an mallake shi..

"Ba Zan taba Komawa gidan can ba". Ya fada a zahiri sannan ya tada motar shi ya nufi gida..

**

Koda sammaci ya Isa ga su Laylerh sosai malam yayi mamakin ganin ba police station bane ta shigar da case din company'n ne don sun San dole dama za'a je court..

Laylerh da yanzu gaba daya ta koma kalar tausayi shiru tayi tana sauraron malam

" Gashi su Umar a Washe garin ranar da suka zo suka koma don ba Wanda yayi tunanin da wuri haka za'a shigar da case din,ni abunda yafi bani mamaki ma Wai company'n ne suka shigar da case din dole Na Kira Alhaji M wakili Na sanar da shi don naga date da aka sa shida ga watan nan ne Gashi yau muke biyu ga Wata kenan kwana hudu ya rage".

"Baba ina ga fa masu son ganin Bayan Laylerh dayawa suke don Na tabbatar ba madam Rebecca bace ta shigar".

Cewar Auta kenan wacce ta maida hankalin ta gaba daya kan Malam

" Laylerh akwai Wanda kuke sa'in sa da shi a company'n ne?"

"Ehhh malam bamu shiri da CEO din".

" kaji Dan shegiya to shi kuma wani kanzagi ne ya shigo da shi wannan case".Cewar Auta cikin subutar baki Laylerh ko nuna Mata malam tayi da ido da wuri ta rufe bakin ta

"nafa hane ki da ashar yanzu dai Bari Na Kira Alhaji M wakili din".ya fadi yana dialing number'n duk shiru suka yi tare da maida hankali kan shi don Baaba kam ta fita"Assalamu Alaikum ".jin muryar da ya amsa din ne ya tabbatar mishi da ba M wakili bane don yanzu bai fiya samun shi direct ba sai da P.A'n shi

" wa'alaikisalam wake magana? "

"Dan Allah ko Zan iya magana da Alhaji?"

"Yanzu ya shiga meeting Wa za'a ce ya Kira?"

"Don Allah in ya fito ace da shi malam ne ya Kira daga taraba an shigar da zancen Laylerh kotu kuma shida ga watan nan za'a yi zaman".

" in sha Allah ".nan malam ya mishi godiya sannan suka yi sallama..

" Kinga Laylerh kila sakon ba zai Isa wajen Alhaji da wuri ba Kira Umar Farouq din Ki sanar da shi".

"Wallahi Tun ranar da abun ya faru waya ta Na rasa inda ya shiga sai dazun ne Na Kira Nabeela ta daga ta kuma ce in sha Allah in ta tashi aiki yau zata kawo mini".

" to Shikenan Allah kaimu".Ameen duk suka amsa ita ta kosa Nabeela ta kawo Mata waya ta sanar da Aunty'n ta don bata ga dalilin da zai sa a boye musu wannan Tashin hankalin ba..

Kamar yadda Nabeela tayi alkawari sai Gashi ta kawowa Laylerh waya sai dai lokacin da tazo Laylerh Na wanka ta kuma ce ba zata iya jira ta fito ba don Mai keke Na jiran ta Gashi magrib ya kawo Kai ba zata samu abun hawa ba in tayi dare a anguwar sai ta ijiye Mata wayar ta tafi..

Tana fitowa wanka kuma taga wayar ta taji haushin tafiyar Nabeela don basu gana ba...

Abuja

Fitowar Alhaji M wakili kenan daga meeting gefen shi Abokin shi ne"Sir anyi Kira daga taraba Wai sunan shi malam yace a sanar da Kai an shigar da case Na Laylerh kotu kuma shida ga watan nan za'a yi zama".da Kai ya amsa nan P.A'n shi ya juya ya tafi su kuma suka cigaba da tafiya sai dai yanzu duk zancen da Abokin nashi ke yi baya cewa komai "Alhaji Wakili lafiya kuwa?" Karamin tsaki yaja sannan yace

"Ina ko kaga lafiya yarinyar da Umar Farouq zai Aura ce ake zargin ta da kisan Kai kaga yanzu an shigar da case din kotu".

" Yar wace ce a garin nan?"

"Ba Yar kowa bace". Da sauri Alhaji Dan Lami yace" baga irin ta ba ance Ka fita harkar talakawa kaki yanzu Umar Farouq da kyan shi da ilimin shi da ajin shi ace Ka nema mishi Mata wacce ba Yar kowa ba Ka tsallake yaran mu da suke da kyau da wayewa da Kayi magana Ai da Na bashi Zaitun don ta gama masters nata a Dubai ".numfashi Alhaji M wakili ya sauke sannan yace

" Ai yanzu kam aikin gama ya gama".

"Yanzu kana nufin zaka shiga case din".

" dole Na Ai duk taurin kan Umar Farouq ne kuma yaja mini".

"Kaga Ka manta da su suje can su karata shi kuma Umar Farouq Zan bashi Mata talaka tsam bai yi ba". Hannu Alhaji M wakili ya mika masa suka gaisa yana fad'in

" to ni Zan wuce akwai inda zanje kada Na makara sai Mun sake haduwa"yana Kai karshen zancen shi ya fice Alhaji Dan Lami kuma da ido ya raka shi nan shima ya shiga motar shi direct gidan M wakili ya nufa..

Koda aka sanar da Aunty Hauwa zuwan shi sosai tayi mamaki sai tace ya shiga,a falon kasa ya zauna cikin lullubi ta sauko

"Alhaji yau kuma Kaine a gidan namu".ta fada cikin sake fuska

"To ya za'a yi tunda mijin Ki Nada taurin Kai Ai gwara nazo Gare Ki kila Ki iya fahimtar da shi".

" to Ince lafiya dai ko".ta fada zuciyar ta Na tsinkewa don a tunanin ta wani abu ne ma,Sadiya ko zazzabi take yi shiyasa bata samu daman fitowa taji gulma ba

"Batun yarinyar da yake son aurawa Umar Farouq ne,a gaskiya zai aikata kuskure da zai zo yayi Dana Sani yarinya karama ace tayi kisan Kai Ai komai ma zata iya aikatawa bare in idon ta ya bude". Shiru tayi tana nazarin maganar shi ganin haka sai ya cigaba" waya Sani ko hada baki tayi da magautan shi domin ta cutar da shi shiyasa ta yarje ma auren shi duk da ta San akwai tazara tsakanin su kuma M wakili so yake ya bata sunan shi a gari don haka ya rage naki Ki ankarar da shi ni Na barki lafiya".

mikewa yayi ya tafi bai ko sha ruwan da aka kawo mishi ba..

Da daddare duk zaune suke a falon har Umar Farouq don Abba yayi kiran shi Sadiya ma ta lallaba ta fito jin muryar Umar Farouq din da yake a second floor suke

"Umar Farouq Ka shirya gobe a Taraba zaka kwana don an shigar da case Na Laylerh kotu sai kaje Ka tsaya akai tunda Tun farko taurin kan Ka yasa Ka bata umarnin aiki".

"Alhaji gaskiya ba zai yuwu ba yaushe Umar Farouq ya gama da case nashi irin wannan sannan yanzu ace ya shiga Na Laylerh, Nifa gani nake ya hakura da ita kawai tunda ba ita ce autar Mata ba banda haka yarinya budurwa ace ta bar gaban iyayen ta sannan daga baya koda ta gane su sai bata zauna a gaban su ba yanzu kuma ace tayi kisan Kai gaskiya ya nemi Wata kawai tunda dama ita din zabin Ka ce" Cewar Aunty Hauwa Sadiya ko can kasa kasa yadda ba Wanda zai jita tace

"Ba dai mu ake Kira yan iska ba to karuwa za'a aura". Daga shi har Alhaji M wakili sun ta shiyasa cikin bacin rai Abba yace

" dadin abun ni nake fada Aji a gidan nan ba ke ba don haka Umar Farouq Ka Fara shiri".

yana Kai Aya ya wuce third floor Umar Farouq din kuma banzan kallo ya wasawa Sadiya duk da yaga ta lalace sannan ya fita yana dialing number'n malam"wa'alaikisalam malam a duba mini gida mai kyau a presidential lodge so nake Zan saya don gobe zuwa jibi Zan shigo Taraba".

sanda malam ya gama jawabin shi sannan suka yi sallama..

A Washe garin ranar aka sama mishi gida Mai kyau nan yayi transfer kudi daga bisani kuma aka kawo furniture's aka jera gida ya fito tas kamar Na amarya..

Bai samu isowa a ranar ba sai Washe gari Wanda ya Kama saura kwana biyu a shiga court, tunda yace ya tashi Baaba da Auta da Malam har Laylerh suka je gidan da safe aka share inda bai zauna ba aka gyara gida kam ko Na amarya albarka nan suka koma gida aka Fara mishi girke-girke..

Ita dai Laylerh tana yi ne kawai ba don tana so ba don komai ya fita a ranta Gashi ta gagara fadawa Aunty'n ta kamar yadda tayi niya..

Karfe Shifa Na yamma ya Isa gidan da wasu securities nashi da suka mishi rakiya kusan a tare suka Isa da ahalin gidan malam don shatan keke napep suka dauka da abincin da aka girka mishi..

Lokacin da suka shiga falon ba kowa nan aka jera mishi a dining ita dai Laylerh gefe ta samu ta takure,can ya fito sanye cikin jallabiya da alama wanka yayi gaisawa suka yi da su Baaba Auta ma cikin zumudi ta gaishe shi sai dai ita Laylerh ta gagara cewa da shi ko sannu.. Ganin an Fara kiraye kirayen sallah sai yace suyi alwala malam yaja su sallah nan securities nashi suka yi dakin da aka mallaka musu su Baaba kuma a waje suka yi shima ciki ya shige Laylerh ko Na can gefe don bata sallah..

sun daidaita Sahu har malam yayi kabbara sai ya fito hannun shi duk danshi ruwa yana sauke hannun rigar kamar wani abu ne yace ya juya yana kallon gefen da take kallo daya ya Mata ya cire Kai nan suka yi sallah Bayan sun idar kuma suka ci abinci shi da securities nashi ita dai tana falo.

"Umar Farouq dare ya Fara mu zanu wuce sai gobe Zan shigo in sha Allah".

" Ehhh Nima nayima Doctor Jibril magana yace zasu shigo da lawyer Anjima don haka ita yarinyar ta tsaya don ya dauki statement nata in zai wuce sai ya sauke ta a gida".tsam wannan tsarin bai yiwa malam ba taya zai bar laylerh budurwa da ita a gidan in Auta ce Ai ba zai yi haka ba shiyasa ya wayance

"to Shikenan Bari dukka mu zauna in sun gama sai mu tafi". Daga yadda ya kalli malam,malam ya tabbatar da ya gane tuhumar shi yake yi shiyasa sai jikin shi ya mutu

" to ba komai zamu wuce sai ya dawo da ita".nan duk suka mike Auta ko ji tayi ina ma ita ce aka ce ta tsaya. Laylerh ma bin su ta Fara sai malam yace

"a'a ki zauna a nan sai Anjima zasu maida ke ".

Haka tana ji tana gani suka tafi cikin falon ya rage su biyu don securities nashi Na waje..

Comment

Share

©Hafciey Musa

[1/25, 5:42 AM] Hafciey Musa😘: *Laylerh*

(The prettiest emerald)

Thank you for contacting Sdeendtm! *BUY DATA FROM THE AFFORDABLE PRICE*

I selling MTN data with this cheap price

MTN DATA PACKAGE

500MB@===200

1GB@=====300

2GB@=====600

3GB@====900

5GB@====1,500

Dial *131*4# or *460*260# to check Data balance.

Validity 1 month

Airtel,9mobile and Glo *also available.*

Subscription for DStv gotv star time electric pay bills *Whatsapp OR

Call 08066268951*

Tsintar kanta tayi cikin masanancin tsoron shi shiyasa ta gagara ko motsi Mai kyau tattare jikin ta waje daya tayi kamar Mai jin sanyi sannan ta hada Kai da gwiwa zuciyar ta Na bugawa da sauri sauri tana kuma satar kallon shi ta kasa don tsoron shi da take ji,mikewa yayi ya shige inda take da tabbacin bedroom nashi ne nan taja dogon ajiyar zuciya tare da maida duban ta ga TV dake aiki a channel na cartoon shi daya..ya dau lokaci kan ya fito kamshin turaren shi ta shaka tana lumshe idanun ta rike da wayar shi sanye yake cikin plan trouser fari sal sai top Mai karamar hannun dantsen shi duk a waje kallo daya ta mishi ta cire Kai duk da iya son kallon ta..ba tare da ya dubi bangaren da take ba ya Fara making calls ita dai jin shi kawai take don yawanci da turanci yake maganar,Bayan ya gama sai ya sauke ajiyar zuciya nan taga ya mike inda take ya nufo nan ta zare ido duk taku daya da yayi bugun zuciyar ta tsananta yake kan ta a kasa ta zubawa kafar shi da ya zura Slipper's Mai kyau ido..ganin da kusa karosa ta da sauri ta mike tare da dafa bangon ta rufe idanun ta tuni jikin ta ya dau rawa..

"Hmmm"

Shine abunda taji ya furta haka kawai kuma abun ya tsaya Mata a rai to me kuma yake nufi da hmm kujerar da take zaune a kasan shi yasa hannu ya dauki remote sannan ya juya yana gyara zaman rigar shi ta baya da sauri kuma ta cire ido saboda

hango boxers nashi da tayi hakan kuma ya faru ne saboda wandon da ya Dan sauka shiyasa ma yake gyara rigar adaidai lokacin kuma ta sauke ajiyar zuciya..

Zama yayi kan one seater inda ya Fara scrolling channels har sanda ya Isa news sannan ya Bari..gefen da yake ta saci kallon shi cikin rashin sa'a kuma sai suka hada ido da wuri ta sauke nata kasa cikin kuma rashin sanin abunda zata yi ta hau juya wayar ta dake hannun ta baki Na rawa t

"Sannu da hanya ".

tace da shi tana cigaba da wasa da wayar hannun ta shi ko banza yayi da ita har ta cire ran zai amsa saboda maida hankalin shi da yayi kan TV ya kuma kishingida kadan

" dama wani salon iskanci ne ya Hana Ki magana Tun dazun?"jin tambayar da ya jefo Mata yasa ta daga ido da dube shi sai gani tayi hankalin shi tsam baya kanta rasa amsar da zata bashi tayi shiyasa suka cigaba da zama shiru har kusan Na minti biyar,knocking kofar falon aka yi nan yace

"yes come in".daya daga cikin securities nashi ne ya shigo

"Sir Doctor Jibril yazo da Lawyer".

" shigo da su".nan security ya fice ita ko mamakin izza irin nashi take..ba jimawa kuwa sai ga Doctor Jibril Wanda shi kam ta shaida shi lawyer din ne dai bata San shi ba

"Sir Ashe Ka iso".Doctor Jibril ya fada

"Yeah ban jima da sauka ba kuna iya zama".ya fadi yana nuna musu kujera Nan duk suka zauna Bayan sun yi musabaha

" Sir wannan sunan shi Barrister Usman Ale ya iya aiki sosai shine Wanda nace da Kai Na mishi magana".Kai Umar Farouq ya daga yana karewa Wanda aka Kira da barrister Usman kallo da kuma nazartar shi

"Sir kamar yadda Doctor Jibril ya fada maka ni dai barrister ne kuma ba yau Na Fara solving irin wadan nan cases ba don haka Zan so ganawa da ita yarinyar da ake zargi".da ido Umar Farouq ya nuna ta "kece?" Barrister ya tambaya Bakin ta har rawa yake tace

"Ehhh suna Na Laylerh Musa".gyara zaman shi yayi da kyau inda ya juyo yana fuskantar ta tare da maida hankalin shi dukka Gare ta yace

" malama Laylerh shin da gaske kin aikata laifin da ake tuhumar Ki akai ne?"da sauri ta girgiza Kai sai kuma ta kalli Umar Farouq Wanda tsam hankalin shi baya kan su yana ga TV don a zaton ta zai ce da Barrister bata aikata ba

"wallahi bani bace ban kashe kowa ba".

" duk da shi Accounter din ya Kai shekara hamsin ba Zan cire ran cewa akwai alakar soyayya a tsakanin Ku ba don naga matan yanzu kun fi son sugar daddy's Wanda Na tabbata dumping naki yayi shiyasa Kika dauki mataki akan budurwar shi".wannan wani irin kazafi ne lawyer yake Mata to a haka ne zai kare ta tunanin da take yi kenan

"ina jin Ki".

Ya kuma fada shiyasa ta dawo hayyacin ta inda Doctor Jibril kuma ke sauraron su

"Tsam ba wannan alakar tsakanin mu sannan nasan tambayar Ka ta gaba zaka ce me alaka ta da yarinyar ko ita ma ba komai tsakanin mu in takaice maka ban fi sati biyu da Fara aiki a company'n ba". Ta bashi amsa cike da kwarin gwiwa don ta fahimci so yake ya sata kuka a banza

" gwara Ki daure Ki fadi gaskiya in nauyin su kike ji sai mu kebance in har ke Kika yi kisan ya kamata Na Sani kada sai case yayi nisa a gano ke ce".

"Nafa ce maka bani nayi ba me kuma kake so Na fada Bayan wannan". Ta kare zancen cin jin zafi sau nawa zata shaidawa duniya ba ita tayi kisan ba amma sun gaza fahimta kowa tambaya daya yake maimaita mata..Har Umar Farouq da bata yi tunanin yana jin su ba sanda ya daga Kai ya dube ta ganin rashin kunya taki son yi bai kuma sauke idon shi a kanta ba sanda ya tabbatar idon ta ya shiga cikin nashi, tabbas ta San me hakan yake nufi Wato gargadi ya Mata da ido shiyasa ta sassauta kalaman ta

" Sir wallahi yarinyar da aka kashe ba don gawar ta da Na kura Wa ido ba da ba Zan iya gane ta ba don kallo daya Na Mata Na cire ido sannan naji ance shi Accounter din yana da Neman Mata".

"Listen Ki nitsu Ki bani labarin abunda ya faru cikin sati biyu don Zan dauki statement naki".

Tiryan-tiryan ta Fara bashi labarin Tun ranar da Mommy Sulaiman ta dauke ta aiki har zuwa ranar da aka yi kisan".

" duk Wanda yayi wannan kisan yana da wayo sosai shiyasa bai bar abunda zai yi implicating nashi ba sai abu daya Wanda Na tabbata shima kuskure ne ko mantuwa yayi".duk ido suka zurawa Umar Farouq lokacin da yake magana Amma kuma hankalin shi Na kan TV cigaba yayi

" makashin yana da basira sosai sai dai ya mance abu daya wannan abun sha da aka sa poison a ciki shine kuskuren da ya aikata dole akwai sa hannun Mata Mai shagon don Na tabbata akwai boyeyyiyar alaka a tsakanin su Wanda ba Wanda ya Sani".Barrister baki ya wangale ganin shi ne barrister Amma ga Wanda yafi shi sanin kan aikin shi

"Dole an sa poison din ne a shagon ko kuma an shigo da drink din cikin shagon Bayan an sa poison, to a nan Mata Mai shagon dole akwai ayar tambaya akan ta sannan ya zama wajibi a tura wani Wanda basu San shi ba company'n don yasa ido akan shagon".

" Sir akwai Wanda Na Sani kuma Babban mutum ne yana aiki a company'n ".

" Ai zancen da nake yi Doctor Jibril ba zai yuwu ba don A yanzu company'n bata cikin nitsuwa don haka ba zasu dauki ma'aikaci sabo ba sannan batun Wanda Ka Sani har yanzu bamu tabbatar da ba hannun company'n a kisan,staff Wanda bai da matsayi ba'a kuma San da zaman shi ba za'a nema".

cikin sauri Laylerh ta katse Umar Farouq da fadin

"Akwai Kawa ta Nabeela".kallon tuhuma Barrister ya Mata yace

" Kawar Ki?Ince a nan Kika ce baki fi two weeks da Fara aiki ba,Nifa wallahi ban wani yarda da abunda Kika fada ba".

"To Ai Na taba aiki a company'n shekaru biyu da suka wuce". Ta fada tana kwabe fuska don jinin su bai zo daya ba

" Sir kana ji fa nace da ita ta fada mini komai Amma sai ta fadi son ran ta Anya". Barrister ya kare zancen cikin tsigar kai karan Laylerh wajen umar Farouq, Kai kawai Umar Farouq ya girgiza ganin ido hudu Laylerh ke son sawa Barrister ciwon kai

"Kinga Laylerh Ki fada mishi Tun farkon zuwan Ki company'n". Doctor Jibril ya fada cikin lallashi nan ta zayyane musu komai, murmushi Mai sauti Umar Farouq yayi sannan yace

" Tabbas cikin biyu anyi daya ko Sulaiman ne yayi kisan da yake yana son ganin Bayan ta sai ya lakaya mata ko kuma ita ce ta yi kisan don ta rugusa company'n kan shi ya ruguza ta,sannan barrister Ka karbi number'n ita Kawar ta ta sai kuyi magana zaku iya tafiya ".

Mikewa suka yi inda suka je har inda yake suka yi musabaha sannan suka fice ita dai Laylerh duk haushin su take ji ganin kamar kowa zargin ta yake Gashi bai ce su sauke ta a gida ba Amma daga yadda yake magana tasan dole ya karanta low..

Bayan fitar su sai wajen yayi shiru ba Mai cewa komai sai dai lokaci zuwa lokaci tana duba wayar ta don ganin time ya kuma Lura da abunda take yi..mikewa yayi yana Hamma ya nufi bedroom nashi ba shiri ta mike da sauri tana fad'in

" Ayya Ka manta da nine?"

Tuni har ya shige bedroom ya maida kofar ya rufe kuka ta Fara

."Shikenan kuma kazafin da Baaba take mini zai tabbata da wani idon Zan kalli malam Na mishi bayani".tsam ta gagara zama sai safa da marwa da take yi a falon tana hawaye can driver ya shigo

"Oga yace kizo Na maida Ki gida".dama jira take da wuri tabi Bayan shi suka fice a gidan..

A can gida kuma sosai hankalin malam ya tashi ganin har karfe Tara da rabi Laylerh bata dawo ba sai yanzu yake nadamar barin ta a can haka ma Auta don tsam ta rasa sukuni,Baaba ma bata yi bacci ba don ita nata manufar daban ne bata son Laylerh da Umar Farouq din su samu kusanci ne ko kadan

"Baba Ka Kira laylerh a waya mana zuwa yanzu Na tabbatar lawyer ya tafi".Cewar Auta kenan nan ya fiddo waya zai yi kiran Laylerh sai suka ji tsayuwar mota a kofar gidan cikin subutan baki Baaba tace

"Na tabbata shi ya dawo da ita".

" to sai me in shi ya dawo da ita Ince shi zai Aure ta".malam ya fada yana fita waje nan suka hadu da Laylerh da kuma driver Bayan sun gaisa sai driver ya tafi su kuma suka shiga ciki..

Tambayar ta yadda aka yi malam yayi daga nan ta zayyana musu komai

"In sha Allah zamu yi nasara don yau saura kwana biyu a shiga kotu". Daga haka ko wannen su ya shiga makwancin shi.

Washe gari!!

Abuja

Aunty Hauwa ce zaune a falo an daura Mata lallen gargajiya a kafa dinning table ta kalla sai tace" yau kuma lafiya abinci ya rage dayawa haka kun San fa Alhaji bai fiya son Ana zubar da abinci ba".

"Hajiya wallahi Aunty Sadiya ce bata fito taci abincin ta ba". Daga Kai tayi ta duba agogo sai ganin karfe sha daya ma yayi" kila tayi a can dakin ta".daga nan bata sake cewa komai ba ta cigaba da jiran lallen ta ya Kama.. shiru shiru har sha biyu ba alamar Sadiya, Bayan ta cire lallen sai ta nufi dakin Sadiya kwance ta Gan ta akan gado karasawa cikin dakin tayi inda ta zauna a bakin gado tana yaye blanket da sadiyar ta rufu da shi

"Sadiya lafiyar Ki kuwa Kika kashe Ac da fankan dakin sannan Kika shiga bargo a zafin nan ko dai baki jin dadi ne". Da kyar ta lallaba ta mike zaune hawaye Na bin gefen fuskar ta ta gyada Kai alamar eh

" Subhanallah me ke damun Ki? "Aunty Hauwa ta tambaya tana taba wuyar ta don jin yanayin zafin jikin ta Ai ko Zafi jau taji shi

" wallahi kwananan ban jin dadi ne".

"Allah dai ya sauwaka Amma Sadiya ke ma kin daura ma kan Ki damuwa dayawa ciwo ace daga Na hannu yanzu kuma yana son wuce gona da iri,rayuwar da Kika gani kowa da irin tashi kaddarar don haka Ki cire abunda yake ran Ki don Allah". Kai ta iya gyadawa don Aunty Hauwa bata San me take ji game da Umar Farouq bane shiyasa tace haka Gashi yanzu yayi tattake har taraba duk akan wannan banzar Wai ita Laylerh..

Waya Aunty Hauwa ta Kira tace a kawo ma Sadiya abinci ba bata lokaci kuma aka kawo Mata

" Kinga Sadiya Ki daure kici zama da yunwa shima Wata cuta ne dubi yadda gaba daya Kika lalace".

"Wallahi Aunty ba Zan iya ba baki Na daci".

" to Ai Mara lafiya kam kowa ya San haka ne Ki dai daure kici ko kadan ne".in kaga yadda Sadiya ta koma ko baka da imani dole kaji tausayin ta don yadda soyayyar Umar Farouq ke dawainiya da ita"Aunty a bani tea".

Aunty da kanta ta hada Mata tea Mai Zafi ta bata,karban cup din tayi Amma kuma duk hannun ta rawa yake alamar tana jin zazzabin sosai seeping biyu tayi ta cire a baki tare da ajiyewa kan bedside drawer

"Ya dai Sadiya sha mana". Kai ta girgiza

" amai nake ji..".kan ta Kai karshen zancen ta tayi toilet da gudu daga bedroom din Aunty ke jin yadda take amai sosai taji tausayin ta nan ta mike ta wuce toilet din,sannu take jero Mata ganin gaba daya ta fita hayyacin ta nan ta taimaka Mata suka fito falo ta ajiye ta a gado,bargo take ja don gaba daya jikin ta ya dau rawan sanyi har hakoran ta Na gogan juna da wuri Aunty Hauwa ta lullube ta sannan tayi dialing number'n family doctor'n su tana Mai tsananin tausayin Sadiya..

Bai dau dogon lokaci ba yazo nan ya Mata duk wani gwaje gwajen da ya kamata sannan ya rubuta Mata magani

"Hajiya ace ta rage yawan tunani in ba haka ba zata hallaka kan ta".Doctor yace lokacin da yake rufe zip Na brief case nashi Bayan ya gama duba ta"Shikenan doctor zamu kiyaye Mun gode".daga nan ya tafi Aunty Hauwa kuma driver ta tura ya sayowa Sadiya magani nan ta zauna a bakin gadon ta kurawa Sadiya ido..

Bayan irin minti Ashirin driver ya kawo magani da kan ta ta bawa Sadiya ganin ta Fara bacci don dama ya Mata allurar bacci yasa Aunty Hauwa fita a dakin ta rufo Mata kofa..

Sadiya ko bacci take Amma hawaye Na bin gefen fuskar ta..koda Aunty Hauwa ta fita a falo ta tarar da Najeeha da kuma Yasmeen sun dawo skull"Najiha in driver ya dauko beta daga skull Ki kawo ta daki Na kada taje wajen Maman ta".

"Ohk". Tace sannan suka cigaba da cin abincin su..

**

A kofar company'n Mai keke yayi parking nan Wata Mata ta fito sanye cikin doguwar Riga brown kafar ta sanye da safa haka zalika hannun ta ma Tasa safa fuskar ta kuma rufe da nikab wannan yasa Kai tsaye ba zaka iya ce da kalar fatar ta ba..koda ta shiga cikin company'n a gate ta tsaya har mota yazo Daukan su Bayan sun taru direct admin department ta wuce.. Office Na manager ta shiga gaba daya sai yaji bai yarda da ita ba Bayan ya bata wajen zama sai tace", Nazo wajen CEO company'n ne".

" Ayya Gashi baya nan".Jim kadan tayi can sai ta mike tace"in yazo Ka sanar da shi Wata tazo Neman sa wacce take dauke da duk Wata hujja Na kisan da yake bukata in har yana da bukatar su anjima karfe hudu ya same ni a sebos wajen saida waya".tana gama fad'in haka ta fice a office din shi ko Wajen Accounter ya nufa ya sanar da shi"Haba manager me yasa kake haka bai kamata a bar ta ba Ai ko da

duka ne da sai ta bamu hujjar".a tare suka fice don dakatar da ita daga fita a company'n sun kuma Kira security kan cewa ya hanata fita..

Tabbas ta shiga company'n ta kuma fito daga admin department Amma daga nan ba Wanda ya sake ganin inda tayi security ma ya tabbatar da bata fita daga company'n ba duk girman company'n kuma anyi Neman duniyar Allah babu ita babu alamar ta da wuri uncle professor yayi dialing number'n Sulaiman..

A bangaren Sulaiman kuma kwance yake yana bacci yaji wayar shi ta dau ringing ba tare da ya duba Mai kiran ba yaja dogon tsaki lokacin da yayi receiving wayar yasa a kunne "uhum". shine abunda ya fada

" Sulaiman akwai Wata mace tazo Neman Ka ta kuma tabbatar mana da tana da hujjar kisan da aka yi in kana da bukata Ka same ta a sebos da Anjima sai dai kuma abun tsoron shine ba Wanda ya San ta ina ta bar company'n Amma ba Wanda yaga fitar ta daga gate kenan aljana ce".da wuri ya tashi daga kwancen da yake yace"uncle kenan so kuke naje wajen ta ta karasa ni".

"Listen Sulaiman kazo company yanzu sai muyi magana don ko wace ce tana da wayo tunda kaga bata ajiye number'n waya ba don ta San za'a iya tracing".

" OK uncle gani nan zuwa ".daga haka ya mike ya shiga bandaki Amma har kasan zuciyar shi a tsorace yake nan ya shirya sannan ya nufi company.. A take aka shiga meeting ba yadda ba'a yi da Sulaiman yaje ba yace ba inda za shi

" kenan so kake mutani su cigaba da zargin cewa da hannun wannan company'n a kashe Gloria ko so kake a rufe company'n Mom naka tayi asara".jin sunan mom nashi da aka Kira ya sa shi cewa zai je tunda ya San kwana biyu ya rage musu su shiga cotu..

A ranar kuma ya shirya inda ya dauki securities nashi guda uku aka Kara mishi da Na company gudun ko kidnapping nashi za'a yi duk da kowa ya San sebos wajen saya da sayarwa waya ce akwai dubbanin mutani ba yadda za'a yi a dauke shi ba tare da an Lura ba..Don su badda Sahu sai shi ya Riga securities nashi tafiya Bayan

Isar shi da minti biyar motar dayan securities din ya iso Bayan minti biyar kuma dayan ya sake zuwa..

Wajen tsam ba alamar kowa sai mutani dake safa da marwa Ana saya da sayarwar waya mutani a kalla zasu yi dubu uku a cikin wajen, daga mirror'n motar shi Na dama yana hangan motar securities nashi daya,daga Na hagu ma yana hangan dayan motar duk da akwai Dan tazara a tsakanin su hakan ya sa shi jin he is safe..sun tsaya da irin minti talatin securities din shi suka ga motar shi ya Fara tafiya direct barde way yayi da wuri suka tada motar suka bi Bayan shi don basu yarda shi ke driving ba sosai suka ba motar su wuta Ai ko shi din ne hakan yasa su jin relief Amma kuma suna mamakin meyasa shi juyawa Bayan wacce suke jira bata zo ba direct company ya nufa..

Cikin company'n kuma gaba daya departments din an hadu a admin department Ana jiran feed back wannan dalilin yasa Nabeela kiran Barrister ta sanar da shi,shi kuma ya Kira Umar Farouq ya sanar da shi kan su ya kulle sosai yo ita kuma wace ce dole su Fara haduwa da ita kan ta Isa ga Sulaiman..

Bayan ya shiga admin department din sai manyan company'n suka Fara tambaya anyi nasara

"Sir fa bai jira zuwan ta ba kawai ya dawo ".daya daga cikin securities da yaje da su ya fada

" but why Sulaiman ".

" uncle tazo fa".what duk suka ce suna jiran ya fadi abunda tace ko ya bada hujjar sai yace"karya kawai take yi".daga haka ya juya ya fita..

A zahirin gaskiya kuma lokacin da suke jiran ta daga cikin motar shi a seat Na baya yaji muryar mace wacce bai San yaushe kuma ta yaya ta shigo motar ba"Sannu Sulaiman ".shine abunda ta fada shi ko bai juya ya kalle ta ba ta mirror motar yake kallon ta yau ma sanye take cikin nikab"Na San kazo nan ne don kaji wake da hannu a kisan da aka yi a company'n Ku don haka kaje Ka bincika Accounter Ka

kuma tilasta mishi ya fada maka Asalin alakar shi da yarinyar sannan Ka fita harkar Laylerh don bata San komai ba". Tana kaiwa nan bata Bari yayi magana ba ta fice daga nan ya tashi motar sa,koda yaje company'n kuma sai ya musu karya don shi har ga Allah ya yarda Laylerh ce tayi kisan kuma yana son a koya Mata hankali shiyasa bai dauki zancen matar ba don baya son a samu second suspect tunda gobe ne za'a yi zama...

A bangaren su Laylerh kuma tayi nisa a tunanin rayuwar ta da irin jarrabawa da take fuskan ta ta rasa me yasa ita kadai Allah ke jarabta da musiba iri iri,da farko an kashe Mata uba sannan an raba ta da mahaifiyar ta da d'an uwan ta,an Mata kazafin maita Bayan ta gano iyayen ta tayi karatu tana tunanin wahala ya kare kuma yanzu ga Wata musibar hawaye ta share daidai lokacin kuma wayar ta ya Fara ringing ganin Aunty'n tane sai tayi receiving ko da suka gaisa sai tace

" Laylerh haka kawai gaba Na ke yawan fadiwa ina ji a jiki Na wani abu Na shirin faruwa dake Gashi yanzu duk bana gane miki".

Jin haka sai ta fashe da kuka ba yadda Aunty bata yi da Laylerh ta fada Mata me ya faru ba sai tace ba komai, katse kirar tayi ta Kira malam sai yace inda hali tazo taraba yau..

Jin haka fa sai hankalin ta ya tashi tace in sha Allah tana hanya duk nacin Muhammad Na ta Bari sai gobe taki yaso suje tare nan ma tace ya jira shago sai ya rakata Tasha..

Da yake bata tashi da wuri ba karfe hudu ta shigo jalingo nan ta Kira malam ta shaida mishi yace Gashi nan zuwa..

Tun a safen ya sanar da Baaba sai dai Laylerh bata da labarin zuwan Aunty'n ta..koda ya dauko ta daga tasha har kofar gida Mai keke ya kawo su nan ya Kira Auta ta fito kofar gidan,akwatin Aunty'n Laylerh ya mika Mata yace"wannan mahaifiyar Laylerh ce Ki Kai ta ciki sai Ki sanar da Baabar Ku".da to ta amsa taja akwatin suka nufi falo"bismillah zauna".

Zama tayi sai ta kawo Mata ruwan sha sannan ta wuce dakin Baaba ta sanar da ita tana fita kuma dakin ta ta koma ta kwanta...

Ruwa Aunty'n Laylerh ta sha nan ta zauna a falon tana jiran taga ta ina Baaba ko Laylerh zasu fito Amma shiru babu su babu labarin su Tun zaman Na Mata dadi har ya dundure ta..

Baaba ko Na can dakin ta da yake akwai TV tana kallo hankali kwance ba kuma ta manta da Aunty'n Laylerh din bane a'a salon wulakanci ne kawai,Laylerh kuma bata San da zuwan ta ba..

Tayi zama har Na hour daya Auta ta fito zata shiga kitchen domin deban ruwan tea Aunty'n Laylerh tace

"Baiwar Allah taimaka mini da sallaya da buta nayi sallah".ita Auta duk zaton ta Baaba ta fito sun magantu sai ta koma shiyasa cikin sakin fuska ta nufi dakin Baaba ta dau sallaya

"Aunty'n Laylerh tace Na Kai Mata".

" to kai mata mana".yadda Baaba bata nuna komai ba ya tabbatar Mata da sun gaisa sallaya ta Kai Mata sai tace"Ai da kin shigo ciki kinyi alwala".

"A'a nan din ma yayi ke dai bani buta".Bayan ta bata buta sai ta wuce dakin Laylerh tayi knocking

" Ki fito Maman Ki tazo"sosai Laylerh tayi mamaki Auta ko juyawa tayi ta koma kitchen.. Da gudu Laylerh ta haye jikin Aunty'n ta tana fad'in

"shine ko Kice mini zaki zo". Zama tayi tace

" Kinga Bayan Mun gama waya ne naji hankali Na bai kwanta ba sai Na Kira malam shine yace nazo kawai to Amma ya banga Baabar taku bace ko ta fita ne?"cak Auta ta tsaya don ta gama abunda zata yi kenan zata koma daki

"Bata fito bane?" Auta ta tambaya

"Ni nayi zaton baki sanar da ita bane Ai".

" Na sanar da ita har sau biyu".tana gama fadin haka ta nufi dakin Baaba

"Ayya Baaba Tun dazun fa nace miki Maman Laylerh tazo Amma baki je ba".

" to uban Mi kike so naje Na Mata ne eh shegiyar yarinya kawai".daga falon suke jin yadda Baaba ke yiwa Auta holo Amma basu jin me take cewa.. A can dakin kuma Auta fita tayi ta Kira malam ta sanar mishi sai ya Kira Baaba cikin lafazi da rarrashi irin Na maza yace" Haba ya kike abu kamar yarinya Nifa ban San Ki da wannan halin ba bakon Ka fa annabin Ka ko so kike Ki nuna Mata ba kaunar Yar ta kike yi ba shiyasa baki shiga wajen ta ba".

"Ince don taji Umar Farouq yazo gari ne yasa tazo don su Kara dafa ta shi kuma ko kisa aka ce yayi akan ta zai iya to akan me zanje wajen ta". Duk da kalaman da tayi amfani da su sai bai damu ba yace

" zato fa zunubi ne tsam ita bata San da zuwan shi ba yanzu ma tazo ne don ni Na Kira ta bata ma San case Na Laylerh ba".

"Oho dai zaku Ji da shi". Ta fada sannan ta katse kiran shi kuma gida ya nufo a falo ya tarar da Laylerh da Aunty'n ta sai hira suke Laylerh Na makale a jikin ta ta manta damuwan ta ma..gaisuwa suka yi sai ya nuna bai San abunda Baaba ta Mata ba kallon Laylerh yayi yace

" kin bata abinci kam".

"A'a yanzu ta idar da sallah".

" haka ake yiwa bako maza dauko Mata abinci ".

" a'a malam ta Bari kawai a koshe nake ".bata rai yayi yace" Laylerh ba nace Ki dauko Mata ba".

Kitchen Laylerh ta nufa sai dai bata ga abinci ba sai Na malam nan ta fito ta rasa ta inda zata Fara ce mishi ba abinci "ya Kika fito hannu banza".

" dama yanzu Zan daura".jinjina halin Baaba yayi a zuciyar shi don ya sanar da ita zuwan mahaifiyar Laylerh Amma bata ce ayi abinci da ita ba shiyasa ya nufi kitchen din nashi ya dauko Mata da kyar ta yarda taci kadan don abunda aka Mata a gidan ya Mata Zafi sosai..

Bayan taci ne ta huta malam ya sanar da ita ya kuma tabbatar Mata da gobe zasu koma kotu shiyasa yace Laylerh ta dauki akwatin ta ta Kai daki don ta San suna da Abubuwan da zasu tattauna sosai..koda suka je dakin sai ta tambayi Laylerh meyasa Baaba ta Mata haka nan ta sanar da ita komai daga nan suka kwanta..

Washe gari Laylerh ce tayi breakfast ko da tana rabawa Baaba Na tsaye akan ta sai ta dauko wani kula a tunanin ta Baaba zata ce Na Waye sai bata yi magana ba nan tasawa Aunty malam kuma ya sayo Mata pick milk Na gwangwani don dama na Leda yake saya..

Already tayi wanka nan suka yi breakfast tare Auta ma ta shigo ta gaishe ta ko me Baaba ta tuna ne sai Allah ko malam ne ya Mata holo oho har dakin tazo ta bawa Aunty'n Laylerh hak'uri ta kuma mayar Mata da abunda ya faru Ana cikin haka ne kuma malam ya shigo yace su zo su tafi ga keke a kofar gidan..

Rufe ko ina suka yi suka nufi high Court dake cike da mutani sun tarar Ana wani case dole suka jira..

Dama Sulaiman da madam Rebecca normal lawyer suka nema ganin lawyer'n Laylerh senior advocate of Nigeria (SAN)sai suka rude nan suka sa lawyer'n ya samo musu (SAN)a safiyar..

Koda aka shiga case kowa ya gabatar da kan shi sai lawyer'n Sulaiman da madam Rebecca ya nemi da a daga shari'ar don da safe yaji zuwa wani lokacin..

Alkali ya daga shari'ar zuwa wani sati...

wallahi Na Lura ynx aikin banza da kuma zaman kashe wandon nake yi sbd Baku son comment kalilian ke yi kuma ni wlh ba kaunar sticker's nake yi ba ta ya Zan San kuna krntw,Amma ba komai lokaci ne in kk shiga da haka ba jimawa Zan ajiye rubutun tunda Allah yy an kusa bude schools

Comment

Share

©Hafciey Musa

[1/25, 5:43 AM] Hafciey Musa😘: *□LAYLERH□*

(The prettiest emerald)

Thank you for contacting Sdeendtm! *BUY DATA FROM THE AFFORDABLE PRICE*

I selling MTN data with this cheap price

MTN DATA PACKAGE

500MB@===200

1GB@=====300

2GB@=====600

3GB@====900

5GB@====1,500

Dial *131*4# or *460*260# to check Data balance.

Validity 1 month

Airtel,9mobile and Glo *also available.*

Subscription for DStv gotv star time electric pay bills *Whatsapp OR

Call 08066268951*

Duk fita suka yi a court din inda kowa ya Kama gaban shi wasu ko gefe suka koma suna tattaunawa,ciki kuma Harda Umar Farouq Wanda suke cikin mota tare da Barrister yana sanar da shi ganin lawyer'n Laylerh Senior advocate ne yasa suka daga hankalin su..Bayan sun gama har zai wuce sai malam yayi knocking window motar nan ya sauke,hannu malam ya mika mishi suka yi musabaha sai yace

"mu zamu wuce gida sai kuma wani satin in Allah ya yarda sannan Kayi kokari Ka shigo Anjima saboda mahaifiyar Laylerh tazo sai Ku gaisa" Dan Jim yayi kamar Mai tunani Shifa bai San taya zai fara wannan kunyar dake tsakanin surkunaye ba

"yanzu ina da aiki in sha Allah Zan shigo Anjima ".

" Yauwa da Ka kyauta ".daga nan malam ya juya keke napep suka tare inda Sulaiman ko kallo Laylerh bata ishe shi ba kuma hankalin Umar Farouq duk a kan shi yake har zuwa irin kallon da yake Wa Laylerh yana ankare, sai madam Rebecca ce ke watsa musu kallon tsana..

Har kofar gida keke ya Kai su Bayan sun shiga gida sai Laylerh ta kawo ma Aunty Ruwa duk da ba wani jimawa suka yi a can din ba Amma suna jin gajiya a tare da su..duk hutawa suka yi

" To Aunty'n Laylerh Kinga dai yadda case din ya tafi yanzu sai wani sati kuma".

"Khairan in sha Allah Amma ni yau Zan wuce sai wani satin Zan shigo in Allah ya yarda".da sauri malam yace,

" ah Haba wucewa kuma sati daya fa kamar yau ne Ki jira mana".Laylerh ta daura da fadin

"Eh Aunty Dan Allah Ki jira".

" a'a Laylerh ina da abun yi dayawa a can kuma Ai dama zancen naki ya kawo ni tunda an daga dole Na koma in ko zaki bi ni sai mu tafi tare".ta fada don tsam ba zata iya zaman gidan ba ko don bakin hali da Baaba ke nuna Mata kuma so take ta tafi da Yar ta gaba daya

"Aunty Ai ba zai yuwu Na tafi dake ba Kinga lawyer Na yawan zuwa waje Na".

"Gaskiya Laylerh ta fada da dai kin zauna din kawai". Malam ya fadi

" in Na zauna a nan Wa zai lura mini da ayyukana Na can Kinga Laylerh muje Ki tayani hada kaya".mikewa Laylerh tayi tabi Bayan ta Baaba da Auta kam dama basu tsaya a falon ba ko wacce daga cikin su dakinta ta wuce..

"Aunty in dai batun Baaba ne kiyi hak'uri Ai waje Na Kika zo ba wajen ta ba".

"Ke da zuciyar Ki ya mutu sai Ki cigaba da zama har a gama case nan kuma da an gama tare zamu wuce don ba ce musu aka yi bana kaunar Ki bane Na bar musu ke". Shiru tayi tana jin yadda Aunty'n ta ke ta mita a lokaci guda kuma tana hada Kayan ta,suna gama hada Kayan ta mike rarrashin duniyar Allah tayi kan cewa ta tsaya taci abincin Rana taki haka suka fito falon

" Kinga Kira Baabar Ku Kice da ita mahaifiyar Laylerh zata wuce ".malam ya fada yana kallon Auta da bata jima da fitowa ba mikewa tayi ta shiga ciki sannan ya maida akalar zancen shi kan Aunty

" to Gashi kuma sirkin naki yace zai shigo Ku gaisa tunda Baku San juna ba sai kuma Kika ce zaki tafi".

"Gaba yafi baya yawa Ai malam in sha Allah zamu hadu Na barku lafiya Na kuma gode da karrama ni da kuka yi". Haka kawai sai malam yaga kamar Hausa ta mishi ita ko har karkashin zuciyar ta ba komai face alkhairi daidai nan kuma Baaba ta fito

" Haba ba dai tafiya ba sai kace wacce ake kori".murmushi tayi tace

"Ina da abun yi ne ni Na bar Ku lafiya".

" To Allah kiyaye hanya ".da Ameen duk suka amsa nan Laylerh ta dauki akwatin ta suka fita malam da Auta Na Mata rakiya..suna Isa tsakar gidan suka ga wani security ya wangale kofar gidan nan motoci uku suka sa Kai

" Aunty shine fa".Laylerh ta fada Mata cikin rada nan Aunty'n ta sauke Kai kasa bata yarda ta sake duban inda motar tasu ke parking ba..

Bayan sun gama parking sai malam ya nufi motar ta shi

"kaga kazo a daidai don yanzu ma tafiya zata yi".

"Tafiya kuma". Ya fada yana fitowa a mota Bayan security ya bude mishi kofa sanye yake cikin jumper black yasa space a fuskar shi sosai ya mishi kyau,ido Auta ta kura mishi tana Mai rainawa kan ta daga ita har Laylerh don shi ba sa'an su bane,shi ko cikin nitsuwa ya nufi inda yaga su Laylerh suna tsaye da babbar Mata wacce ta bashi baya don kunya ya kuma tabbatar da ita ce mahaifiyar Laylerh.. Tazara Mai Dan yawa ya Bari tsakanin su sannan ya cire glass Na idon shi a hankali ya durkusa kan shi a kasa yace

" sannu da hanya Umma ".

ita gaba daya sai ta rude don bata taba fuskantar haka ba Wai yau har Laylerh ce ta girma da wani Mai sunan Wanda zai Aure ta yake girmama ta haka

" Yauwa sannu ya Ka baro iyayen naka".

"Suna lafiya". Ya amsa yana kallon wrist watch d'in hannun shi yana kokarin dauke kanshi idon shi ya sauka akan well arranged toe nails Na Laylerh Wanda suka sha pedicture sai dauke ido suke yi saurin kau da kan shi yayi saboda jin wani erotic tingle da ya taso mishi game da ita

" mu zamu wuce ".Aunty tace tana tafiya

" Allah kiyaye hanya".sosai Laylerh da malam suka ji dadin yadda ya mutunta mahaifiyar ta haka ita ma Aunty sai taji ya burge ta don bata yi tunanin yana da wannan tarbiyan ba kasancewar shi d'an masu kudi..

Wuce shi Laylerh tayi suka cigaba da tafiya murya kasa kasa kamar Mai rada yace"Laylerh ".Cak ta tsaya don zata iya ransuwa da sunan Allah cewa wannan ne Karon shi Na farko da taji sunan ta a bakin shi,malam tsam bai ji shi ba haka ma

Auta Amma ita Aunty taji don kunnen ta diyar tata ta gado, cigaba da nufar gate suka yi..

Laylerh ko juyawa Gare shi tayi sai taga ya nufi mota kallon su Aunty tayi ganin ba Wanda ya Lura da ita securities nashi kuma Na harkar gaban su sai tabi Bayan shi har ta Isa jikin motar da ya bude ya shiga..sauke glass din yayi sannan yasa hannu a inda ake ajiyar kudi a mota ya Ciro kudi masu yawa ya mika Mata

" ga wannan Ki bata".da sauri ta zaro ido ganin yawan kudin sai kuma ta girgiza Kai

"A'a Ka Bari ta gode".bai ce komai ba ya kuma mika Mata kudin a Karo Na biyu

" Allah ta gode".idon shi dake kalar Na bacci da ke rikitar da ita ya jefa cikin nata

"ba ke Na bawa ba Ai".ya fada cikin kakkausar murya ba kuma alamar wasa a fuskar shi Kai ta sauke kasa a bazata taji ya damko hannun ta yasa kudin a ciki da wuri ta daga Kai ta kalle shi sai dai tsam ba ita yake kallo ba

"Jazakallahu khairan Allah Kara budi". Ta fada tana juyawa shi ko ciki ciki ya amsa da Ameen..

Tana fita ta nunawa malam kudin sannan ta Mikawa Aunty Amma sai taki Karba har malam yasa baki da kyar ta Karba,motar shi daya ce ta fita nan driver yace

" Ranki shi Dade shigo a Kai Ki Tasha".

Ko ba'a fada ba sun San umarnin Umar Farouq din ne nan Aunty da Laylerh suka shiga, da farko Auta tayi niyar zuwa Tasha Amma ganin Umar Farouq sai ta fasa ko ba komai zata samu lokaci tare da shi tunda laylerh ta tafi..

Bayan tafiyar su sai malam ya mishi iso zuwa falo don zasu tattauna batun case Na laylerh din..

Bayan zaman su da wasu mintuna Auta ta kawo musu Ruwa sai dai tsam daga shi har barrister ba Wanda ya nuna alamar yana da bukatar ruwan,proper gaisuwa suka yi sai malam yace

"Barrister yanzu kana ganin case nan zamu yi nasara naga fa mahaifiyar yarinyar a tsaye take".

"A koda yaushe gaskiya Na take karya,Amma Allah ne masani shin zamu yi nasara ko a'a,tsam Laylerh ba ita tayi wannan kisan ba kuma ba zata taba iyawa ba sannan zancen gaskiya akwai wacce ta San da zaman kisan har take kokarin bada hujja sai dai bata bayyana kan ta ba wannan dalilin yasa dole shi barrister yasa ido a kan shiga da fitar Sulaiman". Umar Farouq ya fadi sai kuma ya cigaba da latsa wayar shi

" Sir case nan is very complicated wallahi sai Ka rasa ta ina aka yi kisan da har ba'a bar evidence komin kankantar shi ba".

dama duk cikin su ba Wanda yayi tunanin zai amsa don ya kan yi magana a lokacin da ran shi yake so ne ya kuma bada amsa duk sanda yaji kamar zai iya shiyasa yayi shiru bai ce komai ba..

Baaba dake zaune a can gefe ita da Auta ganin duk sunyi shiru sai tace"Auta ba nace Ki daina sa wadan nan Kayan ba dubi fa yadda suka matse Ki".ta karashe zancen ta tana kallon Umar Farouq da kuma ddu'ar Allah sa ya dubi Auta din,Ai ko kallo daya ya Mata ya cire Kai tsam shi bai ga wani rough dressing da tayi ba compared to shi da yake zaune a Abuja Mata iri iri yake gani

"Wai ba magana nake miki bane".Baaba ta kuma fada nan Auta ta mike sai wani kwarkwasa take a tunanin ta idon Umar Farouq Na kan ta sai dai tsam shi Yama manta da ita corridor ta shige su ko cigaba da tattaunawa suka yi can ta sauyo kayan ta fito sai dai shima ba maraba da Na farkon..

Tattaunawa suke Wanda malam da Barrister ke zancen shi dai baya cewa komai can ya dago zai yiwa Barrister magana sai yaga duk hankalin shi Na kan Auta kallon ta yayi sai yace

"Ince yanzu aka miki holo akan irin Kayan akan kisa hijab sai Kika fito a haka".ya fada don bai ji dadin yadda barrister ke kallon ta ba ita ma Ai kamar kanwa take a Gare shi abunda ba zai so ayiwa su Najeeha ba ita ma hakan ce.

"Kin wuce ko sai Na Saba miki kuma ko kin sauya Ki tsaya a can dakin don ba sa'ar Ki a nan". Malam ya fada cikin tsananin bacin rai don ya fahimci hakan shiri ne don a Dana Wa Umar Farouq tarko..

" to Ai malam kasan ba laifin ta bane shi Umar Farouq din shaida ne lokacin da yake gidan nan bata sa irin Kayan Laylerh ce ta bata ta da sa kananan kaya".rasa abun fada malam yayi don ba zai iya karyata ta a gaban Umar Farouq da barrister ba shiyasa yayi shiru Umar Farouq ko mikewa yayi don su tafi haka kawai sai yaji ran shi ya baci da furucin Baaba Na karshe...

A can Tasha kuma Aunty tayi sa'a ko da suka Isa mutum daya ce ta rage a wani motar yola nan ta shiga motar su ya tashi..Wani a wajen Wanda shima da alama rakiya tashar yayi yace

"Dan Allah malama baki ji ba".ta tabbatar da ita yake shiyasa ta tsaya sai dai bata juya ba"Kayi hak'uri ni matar Aure ce".ta fadi da shi tana kokarin shiga mota don driver kam dama yana ciki

"to Ai Nima mijin Aure ne".yace da ita nan ta dakata daga shiga motar ta juya ta kalle shi

"Dan Allah malam Kayi hak'uri gaskiya Na fada maka kasan dai haramun ne magana da ni a musulunce ko tunda Kai din so Na keke ba wani abu ba".

" Shikenan yi hak'uri ban yi tunanin da gaske bane don haka yan matan yanzu suke yi in saurayi bai musu ba".

"To ni dai matar Aure ce ba yan Mata ba". Daga nan ta shiga mota driver ya tayar yana jinjina tarbiyar ta wani bangare Na zuciyar shi kuma ya raya mishi kila ganin idon shi ne tana tsoron ya sanarwa uban gidan shi shiyasa tayi haka..motocin su Umar Farouq Na tafiya suka iso a gate ta tsaya tare da mishi godiya ta shige ciki..

" wallahi Kinji kunya da girman Ki da martarbar Ki ace kike wannan halin Wai me zaki samu in kin aibata Laylerh ne shin me burin Ki,to abunda ke baki Sani ba shi Umar Farouq din ya fara gano manufar Ki tunda kullum baki da abun yi sai aibata ta batun kananan kaya kuma yarinyar nan Dan banza karamin gyale ma bata Sawa sai in da doguwar rigar shi ne Amma ko kunya Mata sharri baki ji ba".wannan holon ta shigo ta tarar da malam yana yi ta inda yake shiga ba ta nan yake fita ba karshe ma gidan gaba daya ya Bari..

***

Tun da ya dawo daga court sai ya Watsa Ruwa nan ya fito tsakar gidan ya zauna kasan wani bishiya yana shan iska daga inda yake kuma yana hango gate man dake zaune da radio a kofar..knocking Na gate din aka yi sai gate man ya leka ta inda yake lekawa ko da yaushe Amma bai ga mutum ba mita ya Fara

" wallahi anguwar nan yaran makotan akwai su da iskanci sun San dai gidan ba mace bare akai ga yara yan uwan su har suzo wasa da yake sun raina ni sai su buga kofa su buya".yana cikin mita aka sake bugawa nan ne Sulaiman ya daga murya yana fad'in

"Wai wane ne a kofar".

" ranka shi dad'e ina ji almajirai ne".ya fada yana nufar gate din ya bude sai ganin wannan matar dake zuwa kullum cikin nikab yayi,letter ta mika mishi tace

"ga wannan Ka bawa Sulaiman ".daga nan ta juya shi ko gidan ya koma sannan ya rufe wajen Sulaiman din ya nufa

" Ranka shi Dade ga wannan ".

" waya kawo?"

"Wata Mata ce tana sanye da nikab". Karba yayi yana warware latter din

" Ka same ni a sebos nan da hour daya".sake karantawa yayi a can karkashin zuciyar shi ko ya Fara zargin Anya ba Laylerh ce ke turo ta ba..

After 1 hour!!

Yau shi daya yaje sebos din tunda yaga zuwa da securities ba amfani don tafi shi wayo,sanin yau bai zo da securities ba sai ta bude gidan gaba ta shiga,tabbas yau yaga lokacin da take nufo shi har ta shiga motar ba kamar wancan Karon ba kenan ita din idon ta a kanshi yake tunda har ta San bai zo da securities ba..

"Wace ce ke?" Shine tambayar da ya jefa Mata

"Na fahimci kana da taurin Kai fa sosai,yau kun shiga court anyi zama sai dai ba abunda aka gudanar,Sulaiman Tun wuri gwara Ka hada hannu da ni in ba haka ba company'n Ku Na gab da rushewa nace Ka binciki Accountant kaki,batun wace ce ni kuma in lokaci yayi zaka Sani but ina kara gargadin ka da ka fita harkar laylerh saboda in suka yi wining wannan case zaka ci wuya a hannun Umar Farouq Na bar Ka lafiya tunda Na fahimci baka son hujjar Zan kaiwa Laylerh nasan zai Mata amfani ita da Umar Farouq kuma duk Randa yasa aka rufe company'n Ku Kaine sanadi". Tana kaiwa Aya ta fice a motar nan ta bace mishi cikin dubanin mutanin da suke wajen..buga steering motar yayi yana jin takaicin rashin tambayar ta mene hujjar Gashi yanzu zata kaiwa Laylerh dole yayi wani abu...

Tada motar yayi gudu yake kamar baya kaunar ran shi nan ya nufi gidan madam Rebecca da yake yanzu sojojin sun shaida shi sai ba Wanda ya Hana shi shiga..a falo ya same ta bai jima ba ta fito

" madam ya kamata Ki dau mataki don bai dace ace yarinyar nan an bar ta free tana yadda take so a cikin gari ba kisa fa tayi".shiru tayi tana nazarin maganar shi sai ya kuma fad'in

"wannan fa alama ce Na nasara a Gare su take".

" ba zai yuwu ba kaga zo mu tafi police station wajen commissioner of police zamu".motar shi ya shiga ita ma ta fita da soldiers nata direct jalingo division suka nufa..

Ba yadda ba'a yi da commissioner of police ba kan ya Kama Laylerh yaki sai Sulaiman yace zasu rubuta petition against commissioner of police Amma duk da haka yaki abun fa karshe sai ya zama ba dadi sanda aka Kore su da tiyagas..

Bayan barin su police station din sai huci take

"relax madam yanzu muje gidan su yarinyar Ki dauke ta kawai sai mu ga ta siyar"..

Wayar malam dake kwance a masallacin anguwar ce ke ringing yana dubawa yaga sunan Alhaji M wakili ne

" to yau kuma Kai tsaye yake Kira Allah sa dai lafiya ".receiving yayi da sallama.

" malam yanzu commissioner of police na jalingo ya Kira ni Wai baya samun layin Umar Farouq maza Ka fitar da Laylerh a gidan Ka a kaita wani wajen don yanzu

madam Rebecca da sojojin ta suna hanyar gidan Ka".katse kirar yayi malam ko da wuri ya shiga gida a falo ya tarar da ita hannun ta ya fisge yana fadin

"Kinga zo mu tafi".nan ya cigaba da Jan ta bai bi ta kan Baaba da ke tambayar shi ko lafiya ba suka fice..fitar su yayi daidai da tsayuwar Wata bakar mota a kofar gidan cikin gudu don kura motar ta tayar bai Ankara ba aka ja hannun Laylerh aka jefa ta a motar nan motar ta bar kofar gidan at 360..

Sosai hankalin shi ya tashi nan ya Kira number'n M wakili bai samu ba haka ma Na Umar Farouq sai kawai ya zauna a kasa dirsham don ya tabbatar sune suka dauke Laylerh..

Jiniya ya Fara ji nan take sojoji suka cika kofar gidan shi Ana tambayar Laylerh yace an dauke ta sun bincika gidan gaba daya babu ita babu alamar ta...

Abuja

Yau dai Sadiya taji sauki kadan shi yasa ta lallaba ta sauko falon kasa Amma kallo daya zaka Mata kasan tana jin jiki"Sannu Sadiya "Aunty Hauwa ta fada

" ya jikin dai".Abba dake shirin fita ya tambaya "da sauki sosai". Tana magana tana cije labbe alamar jin jiki kujera ta samu ta zauna da kyar sauran yaran ma duk sannu suke jero Mata ganin yadda tayani munin ta ya fito..bata jima a zaune ba taji gwara ta koma daki kawai don hayaniyar Na affecting nata ta tashi kenan ta Fara jin jiri basu Ankara ba suka Fara ganin idon ta Na yawo a sama ita ko hannu take kokarin Mikawa Yar aiki da ta gani a dining don sun fi kusa ko zata taimaka Mata Amma kan a Kai Mata agajin ta yanke jiki ta fadi...

Da wuri Abba ya Ciro wayar shi cikin Gare yace driver should get the car ready Aunty ko tallafa ta tayi ita da Najeeha da kuma Yar aiki daya suka kaita mota nan Yasmeen ta kawo ma Aunty hijab suka nufi asibiti..emergency aka nufa da ita inda Aunty da Najeeha ke safa da marwa suna jiran fitowar Doctor Yasmeen ko tana zaune ta sha tagumi..Bayan wasu lokuta Doctor ya fito da wuri Aunty da Najeeha suka nufe shi" Doctor ya jikin nata?"

"Da sauki ina iyayen ta?"

"Iyayen ta basu kusa Ka fada mana ko mene ne".

" Ku su Waye nata ne?"

"Guidance". Aunty ta fada cikin gajiya da zancen nashi shi da kamata yayi ya fada musu halin da ake ciki Amma ya tsaya jero musu tambayoyi sai kace Dan jarida

" ohk Ki same ni a office ".daga haka ya wuce office da sauri ta bi shi

" have a seat".zama tayi sai yace"a gaskiya patient naku Na fama da rashin lafiya Wanda ga dukkan alamu ta taba samun heart break don yanzu maganar da nake miki heart attack Na Neman wajen zama a rayuwar ta".ido Aunty ta zare tace"Heart attack kuma subhanallah".

"Ni dai shawaran da Zan Baku shine a kula da ita sosai in ba haka ba za'a iya samun matsala".

" in sha Allah Doctor ".ta fada daga nan ta fice tana Mai tsananin tausayin Sadiya wannan wani irin so ne take Wa Umar Farouq da har take kokarin nakasa rayuwar ta..

Ta jima a asibitin Sadiya bata tashi ba da yake an Mata allurar bacci don ta samu hutu sai tace

" Najeeha ni zanje gida Ki zauna ke da Yasmeen a kan ta".

"A'a Ki tafi da Yasmeen kin San ba son jama'a take yi ba kamar ya Umar Farouq in mugun halin ta ya motsa akan Aunty Sadiya zata sauke don ba kaunar ta Yasmeen

take ba".ta San maganar Najeeha gaskiya ne yadda Umar Farouq baya kaunar Sadiya haka ma Yasmeen sai tace

" Shikenan Zan turo Hajara Ku kwana tare don ita zata kawo muku abincin dare".to tace nan Aunty da Yasmeen suka tafi ya rage ita kadai a asibiti..

An kusa magrib Hajara ta kawo abinci ita da Salman sun Dade suna hira zuwa lokacin Sadiya ma ta farka Amma sai hawaye take ganin dare yayi sai Salman ya tafi..

Sunyi iya kokarin su wajen ganin taci abinci Amma taki nan suka kyale ta suka kwanta..cikin dare Sadiya ta farka tana kuka

"Wayyo kirji Na Zan mutu don Allah Ku Kira mini Umar Farouq ".Najeeha ce ta tashi don Hajara akwai nauyin bacci sosai abunda Sadiya ke yi ya bata dariya shiyasa ta Fara recording ganin da gaske ne sai tayi dialing number'n Umar Farouq Amma bata same shi ba daga nan ta maida kiran kan Aunty Hauwa sosai hankalin su ya tashi a gida sai Abba yace ta Kira Doctor a Mata allurar bacci haka ko aka yi sai a lokacin ta samu bacci..

**

Ganin Dad nashi ke Kira sanda gaban shi ya fadi don yasan bai wuce zancen zuwan shi gida Bauchi bane da kyar ya iya receiving

" wallahi Sulaiman in har gobe baka zo Bauchi ba Zan tsine maka".kit aka kashe kirar dole ya Fara shiri ba tare da ya sanar da mom nashi ba don zuwa kawai zai yi ya dawo bai son yake haddasa matsala tsakanin iyayen nashi..

A Washe garin ya Kama hanyar Bauchi..

A bangaren Laylerh ko Ana jefa ta a motar ta Fara musu musu tana hawaye lokaci guda kuma ta kaiwa hannun dake rike da ita duka tana fadin

"ni Dan Allah Ku sake ni kuma sai Na hada Ku da ya uma.....".dakatawa da zancen nata tayi don kamar kamshin turaren shi take ji da sauri ta dago Kai ta dube shi yana zaune a seat Na baya gaba kuma driver ne da sauri ta matsa nesa da shi sai kuma ta nitsu ba abunda ke tashi a motar sai ajiyar zuciya da take ta saukewa akai akai shiyasa ya mika hannun shi ya dauko faro tare da mika Mata ba musu ta Karba sanda ta kusa shanyewa sannan ta cire a bakin ta tare da sauke doguwar ajiyar zuciya daga nan motar ya dau shiru kamar ba mutani

Shi ko ya Riga Abban shi jin labarin madam Rebecca zata zo daukar ta don idon shi akan Sulaiman yake duk inda Sulaiman yayi yana ankare da shi wannan dalilin ne ma ya sa shi sanya gida a anguwar da shi Sulaiman din yake da ya samu labarin kuma sai yazo ya dauke ta..

Direct gidan shi ya wuce da ita driver Na parking ya fice ya nufi ciki a hankali ita ma ta fito tana gyara zaman hijab nata tamkar wacce kwai ya fashewa a ciki haka take tafiya don gaba daya ta tsargu da kallon da wasu securities nashi ke Mata shiyasa da sauri ta shige falon dake kamshi ta zauna a kasa.. Shi ko bedroom ya wuce nan ya cigaba da aikin shi ya dau lokaci kan ya fito daga shi sai dogon wando da kuma vest kitchen dake falon ya nufa ita ko mamakin rashin son zama da rigar shi take tunda ko a gidan malam ma da riga armless yake zama ko kunya baya ji..can ya fito hannun shi dauke da cup da tururi ke fitowa coffee ya hadawa kan shi kujera daya yaja cikin na dining din ya zauna sai dai ita ta Gaza nitsuwa murya Na rawa tace

"to Ayya Ka Bari Na tafi wajen Nabeela ba Wanda ya San gidan".kallon ta yayi Na wasu mintuna har ta cire ran zai amsa sannan yace

"Kice driver ya Kai Ki".da sauri ta fita nan driver ya kaita gidan Dadda sosai tayi murnar ganin Nabeela nan ne take tambayar ta labarin Ummi kwana biyu bata je wajen su ba sai take cewa sun tafi Aure Amma ta San tana dawa zata ce zato jaje nan suka sa dariya..

Kullum sai driver'n shi ya Kai Mata breakfast lunch da kuma dinner hakan kuma ya Mata dadi don ta tabbatar yan gidan zasu ce ciyar da ita aiki ne ba kuma ranar da za'a kawo abinci ba'a hado da abun sanyi da kuma kaza ba sai dai in dare bai yi ba shiyasa wani lokacin in Nabeela ta dawo daga company Allah Allah take dare yayi

don su uku kawai suke ci sannan Nabeela ko Maryam ke fita su karbo ita dai tana cikin gidan I'm ko tayi wanka Kayan Nabeela take Sawa..

Tuni kuma su Sulaiman suka neme ta suka rasa..

A kofar wani gida Mai kyau daidai misali Sulaiman yayi parking bai duma kan shi wajen yin horn Mai gadi ya bude mishi ba,gidan ya canza mishi sosai cikin shekaru ukun an samu cigaba dayawa duk da can baya gidan ba lalacecce bane..gaisawa da Mai gadi suka yi sai ya shige ciki yayi knocking kofar falon..

Ana budewa yaga wannan agolar da ya buga ce shiyasa yaja tsaki"yau kuma Kaine a gidan nan?"ta tambaya ba tare da sanin lokacin da zancen ya fito ba..raba ta gefen ta yayi yana shiga yace"kin San Dan halak duk inda yake kuma komin jimawa dole ya waiwayo gida sai dai in shige ne ko shegiya wacce bata da uba zata zauna gidan uban wani".ba ita ba har Ladidi dake zaune a falo sun San da su yake yi shiyasa cikin daga murya yadda Abban shi dake daki zai ji Ladidi tace

"Ai dama Kai sai Ka jima baka zo ba kuma duk Randa Ka tashi zuwa da buhun rashin mutunci kake zuwa".

"To ya son ran mutum?" Ya tambaya yana nufar fridge nasu dake kusa da dining ya dauki pure water yana sha,jin alamar bude kofa sai Ladidi ta fashe da kuka tana fad'in "yanzu Sulaiman ni kake nufin nayi cikin shege Na haifo su ko". Dariya Sulaiman ya kece da shi yana fad'in

" to Hajiya Ladidi sai Ki jira in Mai gidan ya fito Ki mishi kukan wannan Yar Ki ce ta fito ".kanwar shi ce Wanda uban su daya ta fito daga daki jin muryar Dan uwan ta..

" sannu da zuwa ya Sulaiman ".

" Yauwa ya gida".

"Lafiya" tace da shi don ita bata dauki halin uwar ta da yan uwan ta ba

Baba ne ya fito yana fad'in

" ya ishe Ka haka Sulaiman maza tashi Ka bar mini gida Na tunda kace baka gaji mutunci ba".Allah ba don mahaifin shi bane da ya San me zai ce mishi,mutum ya tashi Tun daga taraba har Bauchi sannan yanzu yace ya koma "Shikenan Baba Zan koma in sha Allah ba Zan sake zuwa ba".

Tafiya ya Fara sai Baban nashi duk yaji ba dadi" tsaya Sulaiman Zan zo muyi magana ".kallon agolan yayi yace" kin dai ji Ai Dan gida dai ba Wanda ya Isa ya Kore shi".

"Kaga ban son matsala maza je waje Ka jira ni". Baban shi ya fada nan ya nufi waje..

" yanzu fisabilillah Sulaiman rayuwar da Ka daukarwa kan Ka yayi maka?"

"Baba bana shaye shaye bana bin Mata sannan ban sata da shan giya kowa ya Gan ni yaga mutumin arziki to me nayi".

" yanzu ace Kai ne babba a gidan nan Amma baka damu da sana'a ta ba Kai dai kullum aka Gan Ka a company'n mahaifiyar Ka".

"Baba gidan nan fa ba zai zaunu ba kuma alhamdulillah ina da aikin yi". Da yake Baban shi bai son laifin gidan shi sai ya canza magana" kaga akwai maganar sirri da nake so mu tattauna Wanda ko mahaifiyar Ka ban yarda Ka fada Mata ba".nan suka cigaba da tattaunawa cikin sirri..

Bayan sati daya!!

Duk sun gama shirin tafiya court Laylerh ma a safiyar ranar ta dawo gidan sai ga kiran Aunty'n ta ya shigo wayar ta

"Laylerh kuna ina ne yanzu Na iso tashar jalingo ".don cin fuskar da Baaba ta Mata yasa bata tashi zuwa ba sai a yau da za'a yi zama dama tayi booking mota tana idar da sallah suka Kama hanya da yake tsakanin yola da Taraba awa biyu ne kuma karfe Tara za'a shiga court sai ta iso kan lokaci

" Aunty yanzu Mun fita Ki wuce Court din Kai tsaye kawai".Haka ko aka yi..

Duk sun zo madam Rebecca da Sulaiman Na tsaye a gefe Umar Farouq ko Na mota sanda aka tashi shiga court din yace

"Barrister wancan matar sun kawo ta a matsayin shaida ce sannan mu ma zamu yi amfani da ita cuxx ita ce Mai shagon da Laylerh ta saya abu a wajen ta sunan ta Mery,Zan fada maka tambayoyin da zaka Mata sannan Ka tabbatar duk amsar da zata bayar ya zama Ehhh ko A'a".

"Ohk Sir". Nan ya fada mishi duk tambayoyin da zai yi sai suka shiga..

Prosciutto ne ya karanta case din sai lawyer'n Sulaiman ya Mike yace

" Suna Na Barrister yahuza nine lawyer'n Wanda suke Kara".sai ya yayi bowing kan shi alamar girmamawa ga alkali sannan ya zauna nan barrister Usman ya mike

 "suna Na Barrister Usman nine lawyer'n dake kare wacce ake Kara". Nan alkali ya bawa Barrister yahuza damar Fara gabatar da shaidu tunda suke Kara..

Mai shagon ya gurfanar a gaban kowa sannan yace" madam mery ko zaki iya fadawa kotu me alakar Ki da wacce ake Kara?"

"Ni dai muna aiki waje daya ne da ita kuma Mun San Juna Amma ba sosai ba,a ranar Wata laraba accountant ya shigo da budurwa company'n da yake ina facing Na admin block ne shiyasa Na Gan su,ba jimawa ya turo Laylerh ta saya mishi abinci da

Kayan sanyi sai dai koda tazo mita take kan Neman matan da yake har cewa tayi Wata Rana zai kwasowa kan shi bala'i wannan shine abunda Na Sani".

" Na gode".Barrister yahuza ya fada sai alkali yace ko barrister Usman Nada tambayar da zai Mata,mikewa yayi yana gyara rigar shi ta lawyoyi a lokaci guda kuma yana kallon Umar Farouq nan ya lumshe ido ya sake bude su akan Barrister Usman sai ya juya ga Mai shagon"kamar yadda Kika fada a gaban kowa alakar dake tsakanin Ki da Laylerh nidai tambaya daya zuwa biyu Zan miki".

"Ina sauraron ka".ta fada cike da kwarin gwiwa

" Na San Dole shagon Ki Babba ne tunda a cikin company yake,ya mu'amalar Ki da customers naki yake abunda nake nufi a nan shine shin in sunje sayan abu kece kike basu ko da kan su suke dauka?"

"Suke dauka da kan su".

" Good Amma taya Kika tabbatar da abun sha din asali ba da poison din yazo ba ita ce Tasa".

"Saboda a ranar mutani dayawa sun saya kuma ba'a samun irin wannan matsalar ba".

" Zan so malama Laylerh ta fito gaban court ".mikewa tayi ta fita

" Shin malam Laylerh zaki iya tuna ranar da Kika je sayan abu a shagon ta kece Kika dauka da kan Ki ko baki da hannun ta tayi".

"Tabbas a ranar bani Na dauka da Kai Na ba itace ta bani".

" madam ko zamu iya jin dalilin da yasa Kika bata baki Bari ta dauka kamar yadda kike ba".

"Objection my lord...." Barrister yahuza ya fada sai alkali ya daga masa hannu yace"bar shi ya karasa aikin shi".zama Barrister yahuza yayi barrister Usman kuma godiya yayi

"ina jin Ki madam mery Kinga kenan Ku biyu ke da hannu a kisan don already dama kin ajiye Wanda zaki bata a gefe shiyasa baki Bari ta dauka da kanta ba".da sauri ta girgiza Kai tace

"a'a saboda a lokacin Zan fito waje ne ina da bako shiyasa Na fito Mata da shi".

"Malama Laylerh shin Kinga bakon nata?"

"Tsam ba wani bako don bata fita daga shagon bama".

" zaku iya zama".yace sannan ya maida zancen ga alkali

"Ya Mai girma Mai Shari'a bisa amsa da mai shago ta bayar hakan Na nufin tana da hannu a kisan".

" ko barrister Wanda suke Kara yana da Wata shaida ".

" Ehhh ".daga nan Mai goge goge a company'n ne ya gabatar da kan shi ya kuma tabbatarwa kowa cewa daga Laylerh ba Wanda ya sake shiga office din accountant din ma daga baya ne ya shiga..

" ina bukatar ganin Accountant din a gaban kotu".nan aka ce baya jin dadi sai alkali yace ya daga zaman kuma a zama Na gaba a tabbatar an kawo accountant..

Suna fita a court d'in Kira Na shiga wayar madam Rebecca a wajen aiki Ana Neman ta shiyasa tana komawa gida ta Fara shiri tana gamawa kuma ta bar taraba...

to Wai ya kuke son ni Yar Musa nayi da rayuwa nane?Dan Adam fa komai Kayi ba zaka burge shi ba Kunce Sulaiman Na Baku haushi yanzu kuma Kunce kun tsani Umar Farouq a nemawa Laylerh wani□

Comment

Share

©Hafciey

[1/25, 5:43 AM] Hafciey Musa😘: *□LAYLERH□*

(The prettiest emerald)

Page 39

Koda ahalin gidan malam suka fito a court din zasu shiga keke Aunty ce tayi gyaran murya

"Malam Nifa daga nan gida Zan koma". Zare ido yayi yana duban ta cike da dottaku murmushi dauke akan fuskar shi yace" Haba gida yanzu fa azahar ta kusa muje gida Ki huta in yaso gobe sai Ki koma".

"Batun azahar yayi duk ba matsala bace don ina yola ina Taraba zuwa magrib Zan Isa".

" Ki dai yi hak'uri muje gida".Cewar Baaba

"A'a Na bar Muhammad a gida bai jin dadi shiyasa". Shiru duk suka yi don malam ya fahimci matar Nada kafiya shiyasa yace" to Allah tsare Gashi shi Umar Farouq din Tun kan a gama case din naga kamar an Kira shi a waya ya fita".

"Ba komai ni Na tafi". Laylerh ce ta Kama hannun Aunty'n nata nan suka tare keke sai Tasha..

" wallahi kin ji kunya baiwar Allah nan ba don komai taki zuwa gidan mu ba sai don bakin halin da Kika nuna Mata da yake ita din ba Mai son wulakanci bane shiyasa ta gwammaci ta koma a yau din".Cewar malam

"Yanzu har kana da bakin fadin haka shekara nawa ina rike Mata da yarinyar ta?ita yarinyar me ya hanata tafiya in har ina da mugun hali".

" ke dai Kika sani wallahi gwara Tun wuri Ki canza ".

" ba abunda Zan chanza Ehem Ince har da baki nasa kan cewa kada ta tafi Amma taki".ganin mutani sun Fara taruwa suna sauraron maganar tasu ne yasa shi tare keke ya nufi gida shi daya,Auta ko Tare musu keke tayi tare da rike hannun Baaba tana fad'in "Kinga muje kawai". Nan suka shiga keke suka nufi gida...

Sulaiman

Zai iya rantsuwa cewa ya Dade bai ji yalwataccen farin cikin da yake ji a yau ba don tsam bai ganin alamar su Laylerh zasu yi nasara a wannan case shiyasa lokaci zuwa lokaci ya kan yi murmushi daga Bayan seat Na mota inda driver ke Jan shi don daga court din suka fito zasu koma gida..

Tunda suka shigo cikin presidential lodge junction Na shiga gidan shi yaga Wata mota a fake Ana kuma mishi alama da hannu kan cewa ya tsaya

" oga hannu fa ake sa mana Na cewa Na tsaya, Ka yarda Na tsaya?"driver ya tambaya hankalin shi duk Na kan hanya,yayi nisa a tunanin makomar Laylerh wacce zai iya rantsuwa da sunan Allah kan cewa bai San dalilin da yasa shi tsanar ta har haka ba sannan kuma wani bangare Na zuciyar shi Na fada mishi abunda

yake aikatawa ba daidai bane zai zo yayi Dana sani a lokacin da bai zai mishi amfani ba..sanda driver ya sake maimaita tambayar nan yaja dogon numfashi sannan yace

"Muje kawai ba zai wuce mabarata bane".

" Kai da gani wannan ba maroka bane".

"Nace kada Ka tsaya". Ya fadi hakan cikin tsawa don haka kawai yaji ran shi ya baci ba kuma don maganar da driver din yayi bane a'a saboda zuciyar shi da take raya mishi abunda yake aikatawa ga Laylerh ba daidai bane,shi din ya kasance ba mugu bane sannan uwar shi bata mishi tarbiya a haka ba asalima ba Wanda ya Isa ya kuce tarbiyar shi to me dalilin da yasa yake wasu banzan hali..

A daidai lokacin da driver ya Fara horn kan gate man ya bude gate kamar daga sama aka bude murfin motar gidan baya inda Sulaiman ke zaune aka finciko shi take aka jefa shi cikin motar su hakan ya tabbatarwa da driver kidnapping Na Sulaiman aka yi inda daga shi har gate Man sun gani..

Bawa motar su wuta suka yi nan take securities nashi suka shiga mota aka rufa musu baya,shin in an tafi da Sulaiman wace amsa suke da shi da zasu bawa Hajiya cewa Dan ta daya tilo Wanda ta kawo su don tsaron lafiyar shi an dauke shi hakan yasa su bawa tasu motar wuta da yake anguwar shiru ce ababen hawa ma basu fiya yawa a titi ba shiyasa suke iya hango motar..

Lokacin da suka fita a anguwar sai ababen hawa suka yawaita nan dai suka cigaba da bin su tunda suna iya hango motar daga nesa,dai dai round about Na barde way motar ta wuce kenan sun sa Kai sai ga Wata babbar mota duk yadda suke Wa driver babbar motar alama ya tsaya bai Lura ba kuma sun San in suka ce zasu wuce accident za'a yi dole suka hakura motar ta wuce sannan suka gangara hanyar anguwan gadi inda motar tayi..

Tabbas motar tabi hanyar sai dai ta bace musu don a karshe hanyar ya rabi Kashi uku,basu San shin kofar sarki ko karofi ko kuma hanyar kasuwa motar tayi ba dole

suka hakura hankalin su a matukar tashe da tunanin yadda hankalin Hajiya zai tashi...

A hanyar Laylerh Na raka Aunty'n ta Tasha ta dube ta tace

"Aunty me ya samu ya Muhammad din jiya munyi waya Amma bai ce mini baya jin dadi ba".ajiyar Zuciya tayi tana fadin

" Laylerh lafiyar shi kalau kawai zaman gidan ne bana so kuma ke ma Randa aka gama case nan dauke Ki zanyi".

"Amma shine Kika ce baida lafiya in ko suka ce zasu je duba shi fa". Ta kare zancen murya na rawa don so take ta nunawa Aunty'n bata yi daidai ba Amma da yake uwa ba wasa bane shiyasa ba zata iya fada Kai tsaye ba

" Na sani Laylerh ban kyauta ba Amma ba yadda Na iya".shiru tayi daga nan bata sake cewa komai ba har saida motar su Aunty ya cika sannan ta Mata Allah kiyaye hanya sannan ta nufi gida...

Koda ta Isa a falo duk ta tarar da su zaune da alama kuma dawar ta ake jira don ta daura abinci, ita wallahi mamakin halin su take yi Wai mutum Na jin yunwa Amma don son jiki sai ya jira anzo an dafa an bashi abunda ba zata taba iyawa ba kenan..

"Sun tashi ne?"malam ya tambaye ta

" Ehhh sun tashi".nan ta zauna a falon don yunwa take ji"me za'a daura?"

"Kunga ba sai kunyi girki ba nayima fullo magana zata kawo mini Nono kuma kun San dayawa take Kawa in an dafa abinci zai zama asara". Duk sunyi Na'am da maganar shi ba jimawa kuma fullo ta kawo Nono Mai sanyi don Harda kankara a ciki don ba'a son yayi tsami,tabbas ta yarda Taraba akwai nono saboda yana nan fresh sai kamshi yake Gashi da shegen araha ba kamar kano ba don wasu lokuta madam Na saya..

Nonon ya Mata dadi da yake yaji sugar shiyasa ta sha sosai don bata San yaushe rabon da ta sha ba..Bayan sunyi azahar ne kuma kowa ya nufi daki don bacci..

Umar Farouq

Tun a court din ya samu Kira daga Agency kan cewa Ana bukatar shi da gaggawa a wajen aiki dole ya mike nan securities din shi suka rufa mishi baya..

Anguwar da yake daya ne da Sulaiman Wanda shi Sulaiman bai sani ba don suna da tazara kadan Amma shi Umar Farouq idon shi akan Sulaiman yake shiyasa koda yazo junction Na gidan Sulaiman din ya fahimci ba lafiya..

Har cikin gida driver yayi parking security ya fito ya bude mishi kofa..taku yake cikin jin Kai hannun sa biyu dukka Na cikin wandon sa direct bedroom nashi ya nufa tare da Daukan Abubuwan shi masu amfani ya bar sauran don yasan dole zai dawo..

Airport ya wuce securities din kuma mota zasu bi nan jirgin su ya tashi..

Tunda aka jefa shi a motar aka Danna mishi handkerchief a hanci yana Shaka kuma duk jikin shi ya mutu nan bacci ya dauke shi siyasa bai San hanyar da suka bi ba inda CBN suka nufa sai nausawa cikin daji suke inda ba mutani sosai..

A hankali ya Fara bude idanun shi har ya bude su tas sai kuma yaji hannun shi a daure ta baya nan ya Fara moving kujerar da yake Kai Amma ba alamar zai Kunce sai ma in yayi garaje ya fadi kasa...jin alamar ya tashi yasa ta fitowa kamar koda yaushe sanye take da nikab ga kuma maza majiya karfi tsaye a kan shi..

Yau dai ba safar hannu a hannun nata shiyasa ya gane launin jikin ta cewa ita din Fara ce,a hankali Tasa hannun ta kan nikab Na fuskar ta, ta yaye nan fuskar ta ya bayyana

"Kece?" Ya tambaya fuskar shi cike da mamaki don bai taba zaton ita ce ke wannan danyen aikin ba don ya Mata farin sani,lumshe idanun ta tayi tace

"To ya zan yi don Na fahimci kana da taurin Kai sosai my dear"girgiza kujerar yayi da niyar ko zai Kunce kanshi don har yanzu a daure yake

"Relax Zan Kunce Ka za kuma Ka tafi but before then akwai abunda nake son sanar maka,Tun ba yau ba Sulaiman Na fada maka Laylerh ba ita ce tayi kisan nan ba Amma kaki yarda". Cike da masifa yace

" karya kike ita ce ta turo Ki,ba yadda za'a yi Kice ba ita ce tayi kisan nan ba".

"Sulaiman kasan wacece Laylerh?"

"Niko Na Santa tunda munyi makaranta daya da ita". Ya kare zancen nashi ya kuma juya kujerar

" uhum ba wannan sanin nake nufi, Laylerh maraniya ce wacce aka yiwa mahaifin ta yankan rago sannan Bappan ta ya tauye musu hakkin su suka shiga duniya.. Wannan Laylerh da kake gani abar tausayi ce wacce tayi yawo akan titi Na sati biyu kan ta samu makafaka,yarinyar da ta jure duk wani wahala a wajen larai sannan a karshe aka saida ta ga wacce bata da imani inda har sharrin maita aka Mata..wannan yarinyar a karshe Allah ya hada ta da wani bawan Allah Wanda shine ya ceci rayuwar ta da yanzu an mance da shafin ta..

Tayi rayuwa cikin mutanin da bata sani ba, ba kuma tasan yan uwanta da iyayen ta ba a karshe ta shigo wannan garin Wato taraba inda Bayan tafiyar ta ne kuma Allah yayiwa jigon nata rasuwa..

Shin Ka taba tambayar kan Ka wace kaddara ce ta kawo ta Taraba har ta lalace haka Tun da lokacin da take Maiduguri makaranta daya kuka yi wannan zai tabbatar maka gidan su a wadace yake".shiru tayi ta kura mishi idanun ta inda shima sauraron ta yake a hankali kuma yake jin rauni a zuciyar shi wacce bai San Na

mene ne ba Amma ya tabbata bana tausayin Laylerh bace,ita ko cigaba da magana tayi

"Akan wani dalili kake tunanin zata aikata kisa,in har akwai Wanda laylerh zata kashe to Kai ne". Ta karashe zancen tana nuna shi da yatsa shi ko idanu ya zaro

" but why me?"ya Mata tambayar cikin gaggawa

"Saboda Ka zalunce ta dayawa,da farko a makaranta sannan Na biyu Ka Mata Kora mafi kaskanci a company'n Ku ta hanyar tuhumar ta da sata,Na uku kuma Kaine nan Ka zuga madam Rebecca aka shigar da case nan court". A wannan gaba shiru yayi don baida abun fadi

" Why?har sai yaushe zaka fita a rayuwar ta,in har laylerh bata kashe Ka ba to Wanda zata iya kashewa Na biyu Umar Farouq ne".

"Wane ne kuma Umar Farouq?"

"Shine Wanda ya tsaya akan case nata sannan shi din NIA ne". Murmushin raini wayo yayi sannan yace

" you most be kidding ina wani NIA zai saurare ta".

"Wannan kuma a tunanin Ka ne don ba kowa ne baida imani irin Ka ba,shi in ta kashe shi zata samu kudi sosai Amma taki,Tun Randa muka Fara haduwa da Kai nace Ka binciki Accountant naka Amma kaki,shin Ka San me ya Hana shi zuwa court a zama biyu da aka yi?"Kai ya girgiza

" saboda yana tsoron haduwa da Madam Rebecca don ya Mata farin Sani ".shiru yayi yana nazarin zancen ta don da farko yayi tunanin tsoron madam Rebecca ce ya Hana shi zuwa yanzu da tace haka kuma yaji kamshin gaskiya

" kana da hoton shi ne?"

"A'a". Sai kuma yace

" Ehhh akwai soft copy nasu Na company Bari Na duba ".nan aka Kunce hannun shi ya Ciro wayar shi a aljihu sannan ya duba tare da yin screenshot

" yanzu Kayi cutting Na hoton sai Ka turawa madam Rebecca Ka tambaye shin ta San shi ne,zata tambaye Ka a ina Ka samu hoton kace da ita baka sani ba".

Haka ko aka yi luckily for him tana online nan ya tura Mata ko da ta gani kuma kamar yadda matar ta fadi hakan ce tambayar shi tayi a ina Ka San shi nan ta karbi wayar shi ta Fara typing

"Bayan tafiyar Ki yazo court yana kuka Wai yasan Yar Ki Gloria kuma dole abi Mata hakkin ta". Tana gama typing tayi sending a take kuma madam Rebecca ta karanta don har Allah Allah take yayi replying hakan ya tabbatar mishi da cewa ta mishi farin sani

" hmm wannan da kake gani baida mutunci da imani yaso kudi fiye da komai a rayuwar sa kuma zai iya aikata komai akan kudi,bai taba son mutum don Allah ba sai don abunda kake da shi tsam bai da gaskiya ".a tare suka karanta nan ta sake typing

" ya aka yi Kika San shi haka?"

"Sulaiman duk time da ya sake zuwa Ka Kama shi don Na tabbatar shi ke da hannu a wannan kisan kila shi ya biya yarinyar ta kashe Gloria Zan kuma yi maganin shi". Sanin ba zata fada musu inda ta San shi bane yasa shi cewa" ohk duk sanda Na ganshi I will let you know ".daga nan ya kashe datan shi

" wannan shine prove Na farko da Zan gabatar maka kuma nasan Ka Fara gamsuwa,daga yanzu zamu ke haduwa ba a sirri ba Amma Ka sani Laylerh ba tayi kisan Kai ba".kan shi ya daure tabbas ya gamsu da hujjojin ta sannan yana ji a jikin shi cewa ba ita ta aikata ba amma zuciyar shi ta kasa yarda da hakan

"Tashi a maida Ka gida but on one condition".

" me kenan?"

"Zan daure maka ido". Murmushi yayi sannan yace

" ni dai a sani Na ke mutumiyar kirki ce to ina Kika samo wadan nan majiya karfi da suke kewaye dake".ya fadi yana juya baya don ta daura mishi ido

"Kada Ka damu da su".

" to ke a tunanin Ki in aka barni ido a bude Zan kawo polisawa ne?"murmushi tayi sai tace

"Kai dai Allah ya tsare hanya".

" Ameen Ameen"nan aka sa shi a mota suka bar gidan..

A daidai round about da suka bacewa securities nashi nan suka Kunce mishi ido tare da ajiye shi suka juya shi ko keke ya tare ya nufi anguwar su sai maganganun matar ke mishi yawo a kwanya yana juya su da kuma jin haushin kan shi a haka har suka iso nan ya sauka gaba daya securities din ba Wanda yayi tunanin shine a keken sanda ya fito nan ya biya Mai keke suko da gudu suka nufe shi

"Ranka shi dade sannu da dawa". Ganin yadda duk suke rawan jikin akan shi ya sa shi daka musu tsawa don yana da bukatar ya huta ko don yayi tunani akan Laylerh.

" Sir sannu da dawa wallahi kar kaso kaga yadda Hajiya ta daga hankalin ta".zare ido yayi cikin takaici da kuma tsawa yace

"Kuma yanzu Shikenan sai kuka sanar Mata". Da wuri kuma ya Ciro waya a aljihu don yasan yanzu tana can hankalin baya jikin ta ringing daya ta daura

" Mom".jin muryar shi ya sata tsaya daga tafiyar da take don yanzu haka airport take Gashi sai kuka take kamar wacce aka ce da ita ya mutu,cikin kuka tace

"Sulaiman nawa suke so wallahi Zan basu".cikin sigar lallashi da son kwantar Mata da hankali yace

" relax Mom yanzu haka ina gida ba abunda ya same ni".da sauri cikin kuma girgiza Kai tace

"A'a Sulaiman ban yarda ba yanzu haka gani a airport Zan zo taraba".

" mom kin San fa bana miki karya wallahi ina gida Ki koma kawai".

"No ina zuwa". Ta fadi tana share hawayen ta tare da katse kirar..tabbas ya sani yau din nan ba abunda zai hanata zuwa in ba mutuwa ba ya kuma San hankalin ta dukka a tashe yake saboda shi kadai Gare ta dole ya hakura

" tunda kun sa ta taso sai Ku shirya zuwa tarban ta".ya fadi yana hararar su sai daya ne can kasa kasa yace

"Yazo yana wani fadin rai Bayan gudowa yayi". Kallon security din yayi yace

" kana magana ne?"Kai ya girgiza nan duk suka juya sai security din yace

"Da yanzu yaji maza Ai". Gyaran murya yaji ta Bayan shi sai ya juya nan yaga Sulaiman ne da wuri suka nufi gate..

Tsam bai jin kamar zai shiga ciki shiyasa ya zauna a waje yana Mai tunani iri-iri..

Abuja

Tsam jikin Sadiya yaki yin sauki don yanzu in Ka ganta ba zaka ce ita ce Yar kwalisa ba Gashi zuwa yanzu magana ma da kyar take iya fisgo shi,in tana magana zaka ce Mai kogin magana ce..

Kwance take a gado Aunty Hauwa ce zaune a gefen ta hannun ta dauke da fruits

" Sadiya Ki daina wahalar da ni mana Tun dazun fa nake cewa Ki tashi Ki sha Amma Kika Ki yaushe rabon da kici wani abu".murya can kasan makoshi maganar bata fita da kyau tace

"Zan tashi Na sha,but ni sai nake ganin kamar wahalar da kan Ki kike don wannan ciwon nawa nasan ba Zan tashi ba". Ta karishe zancen tana hawaye kuma ita kadai ta San me take ji

" kada Kice haka Sadiya yanzu kin gwammace Ki mutu akan d'a Na miji Wanda bai San kina yi ba?"

"Aunty da in ina da yadda zanyi Na cire son Umar Farouq a zuciya Na da Na cire jarrabawa ce kadai".

" Sadiya ba yadda banyi dake kan cewa Ki fadi inda yan uwan Ki suke a sanar da su halin da kike ciki Amma Kika Ki".shiru tayi sai hawayen da ke bin fuskar ta don bata son tuna Bayan ta ko kadan

A daidai lokacin ne kuma Najeeha tayi sallama a dakin da sallama

"Aunty kin aiki Salman ne?"

"A'a Ki dube shi a bangaren shi Amma me yasa kike Neman shi ke da nasa aiki".

" Yaya Umar ne yayo waya Wai ya share mishi daki yana dawa".from no where sai ga Sadiya tsaye akan kafafun ta Wanda an Nance rabon da ta tsaya ita kan ta tayi mamakin yadda ta mike sai dai jikin ta duk rawa yake alamar zata iya fadiwa a ko wani lokaci shiyasa Aunty Hauwa mikewa ta ajiye ta a bakin gado..

Hannun ta har rawa yake ta dauki fruits din tana ci da wuri

"Aunty Na rame sosai ko,nayi muni ko kada ya Gan ni hankalin shi ya tashi don yadda Na sauya kin San bai son yaga Na sauya".

Tabbas Sadiya ta kusa zaucewa don Umar Farouq kam ba magana zai Mata ba,a take ta shanye fruits din tas ta mike tana bin jikin bango ta nufi toilet Wai zata yi wanka kan ya dawo..

Sosai Aunty Hauwa da Najeeha suka tausaya Mata nan Najiha ta fice domin zuwa dakin Salman..

Karfe uku duk suka tashe bacci yanzu haka Baaba ke complain

" ni dai gaskiya a samu abunda za'a dafa mana Mai Zafi don yunwa nake ji".

"Yanzu nonon bai ishe Ki ba?" Malam ya tambaya

"Ko kadan ni kwadayin gwaten shuwaka nake ji Laylerh taje kasuwan yelwa ta sayo sai muyi".

" wallahi Nima shi nake so".Cewar Auta nan malam ya bata kudi ta nufi daki ta dau Babban hijab sannan ta fice a gidan..

Tun fitar ta sai jikin ta yake bata kamar Ana kallon ta nan Tasa hannu tana kokarin tare keke yayinda hannun nata ke dauke da waya..

A bazata aka fusge wayar Wanda kuma timing nata ake yi Tun lokacin da ta dawo Tasha kuma sa su aikin aka yi nan suka shiga keken suka gudu..

So take tayi ihu sai kuma ta gagara gida ta koma cikin Tashin hankali tace an kwace wayar ta

"Kai Allah raba mu da yan kwace mutum abu ba naka ba Ka kwace".

" to ita in ba iskanci irin Na yan matan yanzu ba yaushe zaka tsaya rike waya a hannu don Ka nunawa duniya kana da shi ba dole a kwace ba".Cewar Baaba,ita Laylerh ko gaba daya ranta ya jagule ta rasa meke Mata dadi...

Tana fitowa wanka ta sane jikin ta da kyar gashin nan dai yau kam a kitse yake wani gown ta dauka Tasa sai kuma ya Mata Ruwa,duk Kayan da Tasa Ruwa yake Mata karshe dai ta maida Na farkon ta nufi waje tana rike da gefe da gefen rigar..

A Babban falon ta tarar da Aunty Hauwa

"Aunty nayi kyau ko ina fatan Umar Farouq zai so launin Kayan nan sai dai ya mini yawa Gashi gidan nan Baku da keke da Na rage, Aunty a Kai ni boutique don ba Zan iya zuwa ni daya ba,Aunty yanzu wani kalan abinci Zan girkawa Umar Farouq, Aunty a bani abinci Na sake ci don nayi jiki kan ya iso don taraba da Abuja awa nawa ne?"

Haka ta Riga kiran sunan Aunty Hauwa tana sambatu,Har hawaye Aunty Hauwa ke yi ganin yadda kan Sadiya yake kamar Na mahaukaciya ga rigar da ya Mata yawa..

Da yake tana jin jiki ta kwana biyu bata yi dogon magana ba nan take jiri ya Fara deban ta sai jikin ta ya sake ta kuma gama sadaukarwa cewa kasa zata haka ma Aunty Hauwa sai ji tayi an rike ta,tana daga ido taga Umar Farouq ne....!

Comment

Share

©Hafciey Musa

[1/25, 5:43 AM] Hafciey Musa😘: *□LAYLERH□*

(The prettiest emerald)

Thank you for contacting Sdeendtm! *BUY DATA FROM THE AFFORDABLE PRICE*

I selling MTN data with this cheap price

MTN DATA PACKAGE

500MB@===200

1GB@=====300

2GB@=====600

3GB@====900

5GB@====1,500

Dial *131*4# or *460*260# to check Data balance.

Validity 1 month

Airtel,9mobile and Glo *also available.*

Subscription for DStv gotv star time electric pay bills *Whatsapp OR

Call 08066268951*

Bashi ya tashi a inda yake zaune ba har aka dauko Mom nashi daga airport da yake tsakanin Abuja da Taraba minutes ne kawai..

Daidai lokacin da aka bude Mata kofa ya mike ya nufe ta yana kallon yadda ta kura mishi ido tamkar zata hadiye shi,ya sani ba sai wani ya fada mishi ba cewa tana tsananin son shi kuma zata iya yin komai domin farin cikin shi,a kullum yana Kara godewa Allah da ya mallaka mishi ita a matsayin mahaifiyar shi

"Mom" ya fada cike da rauni,ganin hawaye a fuskar ta

"Sulaiman". Ta Kira sunan shi lokacin da ta ida karasawa wajen shi tare da rungume shi tana shesheka

" enough Mom ba abunda ya same ni".tsam bata yarda ba shiyasa ta Fara duba jikin shi,rike hannun ta yayi fuskar shi dauke da murmushi

"Relax Mom Wata friend nata ce fa kuma ba kidnapping bane".

" Friend ".ta tambaya tana kwabe fuska

" Ehh Mom so take ta gwada mini influence da take da shi cux nace bata Isa dauka Na ba".on a serious note tace

"Call her right now".

" but why?"cikin tsawa tace

"Just do as I said". Dole ya Ciro waya a aljihu da yake sunyi exchanging contacts ya Fara Neman number'n tare da yin dialing, ya gama tsara yadda zai yi cux da ta dauka zai Mata magana a baibai yadda zata fahimta but sai jin wayar ta Fara ringing yasa mom nashi sa hannu ta fusge Ana receiving tace

" Assalamu Alaikum ".daga dayan bangaren taji sallamar sai dai bata yi tsammanin ba Sulaiman bane jin muryar mace ya sata yin shiru

" nasan kina jina I called to warn you,ko da wasa bana so Ki sake dauka mini yaro warning naki nake yi ban so".shiru tayi don tasan Mom naji da shi tana da Zafi shiyasa ta sauke Kai

"Hajiya kiyi hak'uri in sha Allah ba Zan sake ba". Jin hakan yasa ta hakura tare da katse kiran shi ko ajiyar zuciya ya sauke..

" Sulaiman ya case din ke tafiya ".

" mom kamar kin sani ina son miki magana akan yarinyar can Laylerh but Ki huta tukun".so take taji me ya faru don ta rasa dalilin da yasa bata son laifin Laylerh case din ma don tausayin Laylerh da take ji ne yasa ta kin zuwa court

"No ban gaji ba kuma naci abinci so Ka fada mini kawai". Sanin tana da kafiya kamar Aunty'n Laylerh yasa shi bada umarnin a kawo Mata kujera hakan ce ta kasance don a waje suka zauna..

Tiryan-Tiryan ya bata labarin duk abunda yake faruwa,ajiyar zuciya ta sauke tare da fad'in

" wallahi Na sani Laylerh ba zata aikata ba sai dai banda hujjar kare ta but Kai ya aka yi Ka sani?"

"Mom investigation nake yi har yanzu kuma ban Kai ga Wanda yayi kisan ba sai dai Na San ba ita bace".

" Ayya marainiya taga rayuwa kyan ta ta auri Mai wadata ko don ya kula da ita".ta karashe maganar tana kallon shi kasa kasa kamar Mai kokarin cusa mishi son Laylerh din don so take taga reaction nashi

"Allah ba maraniya bace baki ga wani garan da zai Aure ta yadda yake zuwa da convoy ba Wai a lallai shi NIA".ya karishe zancen nashi da tsaki da kuma jin zafin Umar Farouq din Wanda bai San dalilin ba..

A matsayin ta Na uwa wacce d'an ta baya boye Mata komai ta kuma San shi ciki da waje sai tayi murmushi tace

" me yasa Ka fadi zancen cikin kishi?kana son ta ne?"mikewa yayi yana borin kunya

"Allah sauwaka me zanyi da ita tunda tana da wani gara". Wannan Karon murmushi Mai sauti tayi jin sau biyu yana kiran Umar Farouq da gara Wanda hakan Na nufin kishi yake yi da shi

" look in kana son ta Ka fada mini Zan shige maka gaba".

"Pls Mom mu bar maganar nan".

" fine but mind you duk lokacin da kace mu daga zancen ba Zan yarda ba".

"Na yarda now pls Ki fada mini yadda zanyi Na taimake ta".

" in har kasan gidan su kaje sai Ku tattauna zaka sake samun bayanai a wajen ta".haka kawai sai bai yi musu ba nan ya Mata godiya sannan suka shige ciki shi ya nufi apartment nashi..

Ya sani ba wannan bane Karon shi Na farko da yake zuwa wajen mace Amma ya rasa dalilin da ya sa shi wargaza wordrobe nashi gaba daya Yane Neman Kayan Sawa da kyar ya cire wani jumper black yasa,fece jikin shi yayi da turare sai ya dauki key'n mota don shi daya yake son zuwa..

Apartment na mom nashi ya shiga luckily for him tana falo

"Wow Kayi kyau ina zuwa haka?" Kai tsaye ya amsa Mata

"Zanje wajen Laylerh". Danne dariyar da ya taso Mata take yi don ta tabbata in ya gani zai yi fushi sai tace

" Allah tsare a gaida mini ita ace ba zata zo bane".

"In sha Allah". Yace lokacin da ya juya yake gyara zaman hular kan shi..mota ya shiga inda ya nufi anguwar su Laylerh..

Abuja

Da wuri ya sake ta ta fadi kasa don tsam bai so tare ta ba bai kuma San wace ce bane kasancewar baya ta bashi duk da kuma suna magana da Aunty Hauwa bai dago muryar ta ba don can ciki ciki muryar ke fita kamar Na jajirai..da sauri Aunty Hauwa ta mike ta nufe su tare da Kama hannun Sadiya tana jera Mata sannu

" wannan covid 19 ne ya Kama ta ko Bari Na Kira securities su Kai ta isolation room ".ya fadi on a serious note don ya tabbata in ba covid 19 bane Sadiya ba zata lalace haka ba..ganin fa da gaske zai Kira su yasa cikin takaicin shi da bacin rai Aunty Hauwa tace

" Umar Farouq tafi apartment naka".da yake a gajiye ya dawo kuma ya shigo ne don daukar key'n bangaren shi shiyasa ya haura third floor Bayan ya dauka kuma ya sauko ba tare da ya sake bin ta kan su ba..

Daki Aunty Hauwa ta kaita aka kwantar da ita sai kuka take tana kiran sunan shi karshe maganin bacci Aunty Hauwa ta bata..

A hankali yasa Kai cikin falon shi inda daddadan hamshi ke tashi ga ko ina tsab kamar kullum da mutum a ciki,lumshe idanun sa yayi ya sake bude su inda ya ware su akan enlargement dake falon Wanda hoton Hajiya Maryam ce Wato mahaifiyar shi,a hankali yake taku hannun sa dukka a cikin aljihu har ya Isa gaban hoton,cire hannun sa daya yayi daga aljihun tare da shafa fuskar ta dake jikin hoton

"Allah Kai haske kabarin Ki Ammi nah". Duk da yasan ita din ta bar shi Tun yana yaro Amma ba zai ce yayi maraici ba don Aunty Hauwa ta cike mishi duk wani gurbi Na uwa dama yan uwan shi..

Yafi minti biyar tsaye a wajen karshe dai ya karisa cikin bedroom din a hankali kuma ya sauke ajiyar zuciya tare da Fara rage Kayan jikin shi..

Boxers kawai ya rage a jikin shi don ko vest din ya cire nan murdaden kirar shi Na cikekken da Na miji ya bayyana,gaban wordrobe yaje nan ya Ciro bath rub fari sal

sai towel dake hannun shi a hankali kuma ya ajiye bath rub din sannan ya daura towel din a kugun shi ya nufi toilet..

Yakan jima a bandaki wannan Karon ma hakan ce ta kasance yana fitowa kuma gaban dressing mirror ya tsaya yayi drying kan shi da kuma shafa Mai Kala Kala don bai fiya aski ba sai dai ya rage kadan..

Jallabiya ya jura Bayan ya gama fece jikin shi da turare nan ya shimfida sallaya ya Rama Azahar da ke kan shi sai kuma ya hau Italian bed nashi sanin baccin tsakanin azahar da la'asar Nada kyau..

Da yake dama bai fiya samun hutu ba,ba jimawa kuma bacci ya dauke shi...

A kofar gidan su Laylerh yayi parking motar shi ya fito tare da jingunuwa a jikin motar ya rungume hannun shi a kirji,wani yaro ne yazo wucewa hannun shi rike da markadadden geda da gani kuma aikan shi aka yi, da hannu yayiwa Yaron alama yazo nan ya nufe shi..

Dafa kafadar Yaron yayi cikin sakin fuska yace

"Ka shiga gidan nan kace Ana kiran Laylerh".da gudu Yaron ya nufi gidan a falo ya tarar da su

" Wai ance Laylerh taje Ana sallama da ita a waje".dakuwa Auta ta mishi tana fadin

"Kaci gidan Ku haka kawai zaka fado mana gida ba ko sallama". Murkuda Mata baki yayi sai Baaba ce tace

" kila an gane wayar Ki ne tashi Kije".jin haka sai Yaron ya fice ita ko daki ta wuce ta dauko hijab ta nufi waje..

Tana bude kofar kuma tayi ido hudu da Sulaiman da wuri ta juya zata koma don yadda zuciyar ta ke bugawa ga wani matsanancin tsoron shi da take ji

"Tsaya". Cak ta tsaya

" so nake Ki mini iso Na shiga gidan don zamu yi magana".

Murya Na rawa ta nufi cikin gidan nan ta sanar da Baaba oga'n ta Na wajen aiki ne sai Baaba tace ya shigo nan ta ajiye stool biyu sannan tace mishi bismillah don bata son ya fahimci tsoron shi take ji..

Da sallama ya shiga gidan,zama yayi lokacin da yake karewa gidan kallo..gyaran murya yayi

"Na San zaki ji mamakin gani Na a gidan Ku".duk da taji mamakin sai bata nuna mishi ba

" ko kadan banji mamaki ba".tabe baki yayi cikin ko in kula yace

"Alright this time around zuwa nayi don Na taimake Ki kuma Ki nitsu Ki fada mini abunda ya faru". Ta sani shi din ba Mai kaunar ta bane ta kuma tabbatar yazo ne don ya samu wani information akan ta don da an shiga court suyi winning shiyasa tayi murmushi

" iya gaskiya ta Na fada a court kuma yanzu ma shi Zan maimaita maka".nan ta bashi labarin duk abunda ya faru kamar yadda ta fada a court

"Ohk yanzu Zan sa ido akan shiga da fitar Mai shagon sannan Zan sa a bincika mini ko za'a samu wani prove". Shiru kawai tayi don tsam bata ji haka kawai zata iya yarda da kalaman bakin shi sai dai kuma tana kyautata mishi zato,jin tayi shiru ya kuma San yarda da shi ba abu bane Mai sauki a wajen ta sai yace,

" Na sani ba zaki taba yarda da ni ba but pls nazo nan ne ba a matsayin boss naki ba,Ki dauki duk abunda ya faru tsakanin mu a baya Ki ajiye a gefe,Laylerh ni ba azzalumi bane kuma ba Zan ga Ana zalunci Na hakura ba shiyasa da Na tabbatar baki da hannu a wannan kisan nazo don Na taimake Ki".ajiyar zuciya ta sauke tana kuma rokon Allah yasa maganar bakin shi har zuciyar shi ne shiyasa tace

"Ya aka yi Ka gane bani ce nayi kisan ba".

" tabbas bake ce Kika yi wannan kisan ba ke dai kin taka sawun barawo ne don da hannun Accountant a kisan".

"Kenan baka San waya yi kisan ba?" Kai ya gyada Mata sai tayi wani murmushin da bai taba tunanin ta iya ba yace

"Kaje wajen wacce ta fada maka cewa bani ce nayi kisan ba zata fada maka Wanda yayi". Karon farko da taga dumbin mamaki a fuskar sa taya aka yi ta San mace ce sannan Ai wacce ta fada mishi ya San ba zata taba iya kisa ba,to ko dai bakin su daya da Laylerh ne da wuri kuma ya girgiza Kai don yasan wancan tafi karfin Laylerh..ita Laylerh ma canka kawai tayi don bata San mace ce ko Na miji ba..

" Kayi shiru ".ido ya kura Mata yana mamakin yadda tsam bata jin tsoron shi kamar a baya,rasa abun fadi sai yace

" daga gobe Zan sa a Fara bincika mini shagon don haka ina son muyi exchanging number".ba tare da bata lokaci ba tace mishi bata da waya an fisge nan ya Mata jaje sannan ya fice..

Koda ta koma gida ba Wanda yace da ita komai.

**

Tsaye take a bakin titi kulan soft drinks nata Na gaban ta da alama abun hawa take jira,Wata bakar mota ce tazo tayi parking kusa da ita shiru ba'a bude kofan ba can aka bude sai tace

"Mtsww ni Ku matsa mini a gaba Na ina jiran abun hawa ne". Daga cikin motar aka nuna Mata bindiga

" maza shigo ".gefe da gefe ta kalla ganin kowa Na harkan gaban shi sai ta shiga a hankali don ta tsorata da su,kulan ta aka shigar nan suka Fara tafiya..

Tafiya Mai saho suka yi karshe har Wuro sembe karshen kwalta suka tsaya daidai wani gida nan aka bude gate..ta sani wannan ba kidnapper's bane duba da yadda suka dauke ta a titi kuma da sanyin safiya sannan basu rufe Mata idanu ba..

Bayan an gama parking sai aka Ciro ta nan suka shiga cikin wani kango gidan dai irin abundant home nan ne irin an Dade ba'a yi amfani da shi ba..koda suka shigar da ita ciki daure ta suka yi hannun ta a baya,Mari aka Kai Mata har sanda ta fadi kasa nan ta Fara bin yan kangon da kallo,maza ne marasa imani kuma majiya karfi nan aka dago ta

" waya yi kisan".cike da karfin hali tace ban sani ba".Mari aka kuma Kai Mata a Karo Na biyu nan ma cewa tayi bata sani ba har da magiyar ta..

Wani wire wuta daya daga cikin su Wanda ba digon imani a fuskar sa ya dauko a kafar ta yasa nan take jikin ta ya hau shocking sai ta Fara kuka

"Ki sauwaka mana aikin mu Ki fadi wane ne yayi wannan kisan ko mu kashe Ki". Kuka ta Fara tana rokon su da su barta zata fadi,cire wayar yayi yace ina jin ki..

Ta sani anyi warning nata sannan kuma ance a bakin ran ta ne,to sanin mutuwa daya ce saboda yanzu din ma mutuwa ce a gaban ta shiyasa cikin azaba da suka jiyar da ita tace

Waiwaye

Wata Rana ina zaune a shago Na cikin Nature's pride farm abun duniya sun ishe ni saboda yanayi Na rashin kudi da nake ciki,tagumi nayi hankali Na yayi nisa har ban San da zuwan accountant ba sanda ya dafa kafada ta Na firgita

" madam ya dai?"ajiyar zuciya Na sauke sannan nace mishi

"Ba zaka gane bane,wallahi tsam yanzu ba cinki Gashi Christmas ya kusa ban sayawa yara Na komai ba,a kauyen mu kuma ance akai contribution Na dubu Dari biyu saboda duk karshen shekara muna Kai Wa".

" hmm Ai garin ba yadda yake kowa fama yake".duba Na Na Kai Gare shi sannan nace

"Nifa Allah yanzu Zan iya yin komai a kan kudi". Yadda naga ya juyo Gare ni gaba daya sanda naji mamaki don kamar abun nema ne ya samu a Gare shi nan yace

" really zaki iya yin komai".

"Ehhh".

" weldone akwai aiki da Na jima ina Neman Mai mini kuma wancan zaki samu kudi sosai kusan million biyu ".jin adadin kudin da wuri Na mike ina gyara zaman zani Na nace

" am ready Ka fada mini ko me ne".cikin yin kasa da murya kamar Mai tsoron Aji mu yace

"Kisa zamu yi". Da wuri Na dafe kirji Na da hannu biyu nace

" Jesus ba Zan yi ba".alama ya mini da hannun shi cewa nayi shiru yace

"Zan baki million biyu da rabi". Jin ya Kara Gashi a bukace nake sai nace

" Ka fada mini me zanyi".da murmushi dauke a fuskar shi yace

"Weldone yanzu dai ba wani aiki Mai wuya zaki yi ba,akwai yarinyar da gobe Zan shigo da ita to ita ce nake son kashewa da Mun shigo in ita ce Zan baki sign ta hanyar daga miki hannu".

" but a cikin company taya zaka kashe ta?"

"It's simple Zan saya drink ne a waje sai nayi injecting nashi da poison sannan yanzu zanje Na kawo miki sai Ki ajiye shi separately Zan tura azo a Karba mini".

" No Sir kasan duk Wanda zai zo ya Karba zaka yi implicating nashi".

"Yeah Nima ban son implicating kowa saboda muna good terms da kowa Na rasa Wanda Zan tura".shiru duk muka yi alamar tunani sai can nace

" ina wannan sabuwar zuwa Laylerh naga tsam basu shiri da boss kaga in ita ce za'a ce tana son durkusa company'n ne".

"Wow what a brilliant idea superb haka za'a yi". Murmushi nayi nan ne ya fita ya sayo injection da drink d'in yayi injecting a gaba Na sannan ya bani na ajiye yadda Zan gane..

.

A Washe gari da yazo da yarinyar ya mini sign shiyasa yana turo Laylerh Na bata wannan dalilin yasa bai zauna a office din ba don kada kowa ya zarge shi Bayan Gloria ta sha sai ta mutu,a Washe garin ranar ya biya ni kudi Na yanzu haka Na taba dubu Dari biyar don Na bata contribution sannan Na Fara sayayya". Tana zuwa gabar nan ta sadda kanta kasa tana cigaba da kuka,tafi take ji a kunnuwan ta sai dai ta sani ba'a gaban ta ake yi ba kamar daga cikin waya yake fitowa nan ta daga ido tana kallon inda take juyo sautin.

Zare ido tayi lokacin da idon ta ya sauka kan fuskar laylerh ta cikin labtob dake gaban ta

" Na jinjina muku kunyi kokari sosai".daga haka bata sake cewa komai ba ta katse vedio call din sai wannan Mara imanin yace

"Kin dai ga camera munyi recording komai don haka zamu sake Ki kiyi tafiyar Ki Amma kada Ki kuskura Ki fada Wa kowa komai inko Kika ce da wani kin fadi wanda yayi kisan a bakin ranki,sannan abu Na biyu Ki sani idon accountant akan Ki yake in ya San Ki fadawa wani kashe Ki zai yi". Da wuri ta amince nan aka dauke ta aka ajiye ta a titi..

A bangaren Sulaiman ko Tun safe yazo Company'n nan ya samu Wata wacce ya San ta Dade tana crushing nashi ya bata task Na buga mishi cikin Mai shagon ko ta duba shagon ko zasu samu wani abu..

Koda ta iso company aka tambaye ta dalilin rashin zuwan ta kan lokaci sai tace d'an ta ne bai ji dadi ba nan dai yarinyar da Sulaiman yasa aiki ta Fara buga cikin ta Amma shiru nan ta duba shagon ba abunda ta samu da yake accountant Nada wayo bai bar evidence ba..

Koda ta sanar da Sulaiman sosai ran shi ya baci har zai Fara halin shi Na masifa sai kuma ya saukar da Kai don kada ta fahimta..

So yake ya sanar da Laylerh Gashi ba hali shiyasa ya nufi gidan su Bayan an bashi izinin shiga..

Kamar jiya a farfajiyar gidan suka zauna..shiru duk suka yi sai shi ke kare Mata kallo sanye take cikin farin hijab har kasa ganin bata da niyar magana sai yace

"Jiya nayi duk wani kokari na don ganin Na Kama Mata Mai shagon nan kuma ban son yin something stupid kin San ni da zuciya sai dai tsam yadda Na fahimta bata da hannu a cikin wannan kisan". Ba tare da ta kalle shi ba tace

" waya fada maka?ita ko ke da hannu a wannan kisan,in Ka koma Ka tambaye ta jiya da ta fito zata company tana tsaye a bakin titi wace mota ce ta dauke ta sannan ina ta Kai ta?kuma so kake ta gaya maka abunda ta fadawa wadanda suka dauke ta".on a serious note yace

"See Laylerh ni ban son irin haka Ki fito fili kawai Ki fada mini abunda ke faruwa". Ajiyar zuciya ta sauke nan ta fada mishi yadda aka yi,poster yayi yana kallon ta da tarin mamaki ina ta samu influence Na yin haka

" but Laylerh..... ".

" abunda ya wuce ya wuce Ai".shiru ne ya sake biyowa sai kuma yace

"Ni kuma Na miki alkawarin kawo madam Rebecca a zama Na gaba saboda a tunanin accountant ba zata zo ba kuma Na San ba Mai iya miki wannan sai ni". Ya kare zancen yana murmushi

" uhum uhum fa in Ka San disappointing Na zaka yi gwara Ka bar ni nayi abu Na".ido cikin ido yake kallon ta yace

"Alkawari Na daukar miki kuma in sha Allah Zan cika,Kinga Na manta Hajiya tace ba zaki je Ku gaisa Ki Mata kitso bane?". Jin ya ambaci kitso sai taji tana son zuwa ganin matar Amma kuma me zata ce a gida tunda case suke yi

" heyy".ya katse Mata tunani nan tace

"In sha Allah gobe Zan zo".

" ohk in kin shirya Ki jira ni Zan so Na dauke Ki".nodding head nata tayi nan suka cigaba da hira tana kuma mamakin yadda take sakewa da shi ba kamar before da take tsoron shi ba tana dai jin kamar Dan uwan ta ne shi din..

Mikewa yayi zai tafi nan ya Ciro waya Abba gida gida sabuwa a aljihun shi ya mika Mata sai ta girgiza Kai

"Kinga Karba ina da abun yi kuma ba don wani abu Na saya miki ba sai don muke communicating Kinga yanzu ma abunda ya kawo ni gidan ku kenan da ace akwai waya Ai ba sai nazo ba". Karba tayi gami da mishi godiya nan ya fice ita ko cikin gida ta nufa,Baaba dake labe Tun dazun da gudu ta koma falon ta zauna Laylerh Na shigowa ta Washe baki

" Kinga saurayin Ki kam kyakyawa yafi Umar Farouq ma".koda bata son shi ta San wannan kam zance ne Baaba ta fadi son ranta ne Amma Ai Umar Farouq yafi Sulaiman kyau

"Dama yace gobe naje nayima Mom nashi kitso".

" ba komai Kije kawai ni Zan San Karyan sa Zan yiwa malam Ehem Kinga da kina waje Umar Farouq ya Kira ta waya ta yana Neman Ki".ta kare zancen tana Mikawa Laylerh waya nan ta Karba ta nufi dakin ta,hada sabuwar wayar ta tayi sannan ta kwashe number'n Umar Farouq din daga wayar Baaba Tasa a nata ta Fara dialing har ta katse bai dauka ba nan ne kuma ta tuna tabbas saboda yanayin aikin shi ba lallai ya dauka ba sai ta Kira da layin Baaba nan ma har kiran ta katse ba'a daga ba..

Tabe baki tayi har ta mike zata mayarwa Baaba wayar ta sai ga kiran shi ya shigo da kakkausan murya yace

"Bakon naki kuma wane ne shi". A take cikin ta ya dau Ruwa don bata yin tunanin an fada mishi ba murya Na rawa tace

" Boss nane".

"Wanne daga ciki Ai boss naki a wajen aikin dayawa Allah yayi su".cike da tsoron abunda zai biyo baya tace

" Sulaiman ".

" hmm that's good for you but this time around Ki sani duk maganar da Kika debo wallahi wallahi ba hannu Na a ciki tunda kince ke kwakwalwar Ki ta kifi ce,how on earth za'a ce kuna good times da mutumin dake Neman ganin Bayan Ki mtsww".shiru tayi sai can kuma yace

"And ina Kika bar wayar Ki da take kashe?"

"Shekaran jiya aka mini kwace to shine yanzu Sulaiman ya kawo mini waya Na Kira Ka da line din ma Baja yi picking ba". Sanda ta gama zancen sai kuma ta tsorata akan me ma zata ce mishi Sulaiman ya sai Mata waya

" Alright yanzu lokaci yayi da Zan bar shi yayi handling case naki Nima Na huta".yana gama fadin haka ya katse kirar ita ko hawaye take matsewa to shi wani irin mutum ne ita bata ga abun fushi a nan ba..

A bangaren shi kuma zaune yake a office ya kura waje daya ido Bayan sun gama waya a ran shi yake jin dole ya fasa auren Laylerh tunda dama Abban shi ne ya mishi zabi, tsam ita ba kalar matar da zai Aura bane duba da yanayin aikin shi Na

sirri ita sai saurin yarda da mutani kamar bata San zafin kan ta ba,tsaki ya kuma ja a Karo da ba adadi ya rasa me ma ya sa shi wannan tunanin nata..

Ganin ba inda tunani zai Kai shi sai ya cigaba da aiki...

A Washe gari kuma sai ga Sulaiman yazo daukar Laylerh nan suka fice zuwa gidan su a hanya sai hira suke kamar sun Saba har suka iso gate man ya wangale musu kofa,da kan shi ya bude Mata kofa Bayan ta fita sai ya rufe suka nufi cikin gidan tare gwanin ban sha'awa..

Suna shiga ta zauna a falo shi ko kitchen ya nufa domin tabbatar da an gama girke-girken da ya sasu ko da ya fito da kan shi ya bata Ruwa sannan ya nufi dakin Mom nashi yace tazo ga Laylerh..

Tana fitowa Laylerh ta durkusa kasa zata gaishe ta sai ta girgiza Mata Kai tare da bude Mata hannaye nan taje suka rungumi juna..

Yalwataccen farin ciki ne dauke a fuskar Sulaiman har ji yake ina ma su kasance a haka su ukun har Abada,ko da Laylerh tayi zancen kitso sai Mom nashi tace a'a a bar kitson nan dai suka cigaba da hira ba tare da sanin su din abu daya bane..

Ganin yamma ta Fara sai tace zata tafi nan ne Sulaiman yaje sauke ta a gida..

Suna fita Mom nashi tayi murmushi tare da sauke ajiyar zuciya tace

"Tunda har Laylerh ke sa Sulaiman farin ciki ni kuma Na mishi alkawarin ko me zai faru sai Na aura mishi ita..

*wallahi ina ganin comment naku ina kuma jin dadi sosai da sosai but time na reply ne bana samu,masu cewa a yi pages biyu a Rana ko a Kara yawan typing wallahi

kuma ina gani but lokaci ne babu da zanyi haka kuyi hak'uri da wannan din kun San typing ba wasa bane*

Comment

Share

©Hafciey Musa[1/25, 5:43 AM] Hafciey Musa😘: *□LAYLERH□*

(The prettiest emerald)

Thank you for contacting Sdeendtm! *BUY DATA FROM THE AFFORDABLE PRICE*

I selling MTN data with this cheap price

MTN DATA PACKAGE

500MB@===200

1GB@=====300

2GB@=====600

3GB@====900

5GB@====1,500

Dial *131*4# or *460*260# to check Data balance.

Validity 1 month

Airtel,9mobile and Glo *also available.*

Subscription for DStv gotv star time electric pay bills *Whatsapp OR

Call 08066268951*

Bangaren Sadiya kuma Tun ranar da Umar Farouq ya dawo ya wulakanta ta sai situation nata yayi worst don yanzu haka a asibiti take Gashi dai kallo daya zaka Mata Ka San ta zauce

"Wallahi ga Umar Farouq kam Ku kalle shi". Tana gama fadin haka ta Fara fisge fisge dole aka danne ta su Najeeha sai hawaye suke Ashe da gaske mutum Na iya zaucewa akan soyayya, bata taba kiran komai sai Umar Farouq ko Doctor ne ya shigo haka zata fada jikin shi ta rike shi gam tace Umar Farouq ne she won't let go of him wannan abu ya tayarwa Aunty Hauwa hankali don yanzu kam an rasa yadda za'a yi da ita..

Duk abunda ake Umar Farouq bai sani ba don a Washe garin ranar da ya dawo ya koma bakin aikin shi,Alhaji ma koda yaga yadda take kiran sunan Umar Farouq din tana Kama mutani da kuma kuka sanda ta bashi tausayi a Daren ranar kuma ba tare da ya sanar da Umar Farouq wane ne a asibiti ba yace ya shirya ya raka shi..

Duk da yana da aiki sosai sai dai baya taba bata ran Abban shi shiyasa ya Fara shiri..

Bayan ya fito daga wanka hannun shi rike da towel jikin shi kuma duk danshi Ruwa ga sabulun da yayi wanka da shi sai kamshi yake,cike da izza ya karasa gaban dressing mirror yana kallon kan shi ta cikin mirror da kuma murdadden halittan jikin shi Wanda shi kan shi ya San yana da lafiya, a hankali ya cigaba da tsane ruwan yana gamawa kuma ya murza Mai a jikin shi sai ya gyara gashin kan shi daga nan ya nufi wajen Kayan shi..

Jumper ya cire baka Mai kyau tare da hula tunda asibiti zaka je cikin mutani kamata yayi Kayi shigen mutunci.. Yana gama sa Kayan shi ya daura agogon shi da ya zama tamkar ta gado Wato Na agency su a tsintsiyar hannun shi sannan ya kafa hula akan shi sosai yayi kyau..

Takalmi ya dauko sannan ya zauna a bakin gado yana Sawa daidai lokacin wayar shi ta shiga ringing yana dubawa yaga Abban shi ne shiyasa ya kwashi wayoyin shi ya fito..

Tabbas shi din ba'a son a San shi shiyasa ko tafiya yayi in zai dawo mota daya zuwa biyu ne suke zuwa Daukan shi,to sanin haka ne yasa Abban shi bai Tara convoy kamar yadda yake yi in zai fita shi daya ba,a baya suka zauna Bayan ya Mikawa Abban shi hannun shi sun gaisa basu sake magana ba har suka Isa farfajiyar asibiti..

Sosai yayi mamakin ganin Najeeha nan suka shiga ciki daidai lokacin aka danne Sadiya dake fisge-fisge tana kiran sunan shi..

Duk da ita din abar tausayi ce Amma shi a ran shi ji yake karya take, ko da aka ce Mata ga Umar Farouq sai tace Tun dazun haka kuke fada mini kuma ba shi bane..

Sun d'an jima kadan kan su tafi..

**

A yau aka koma court inda kowa ya halarta sai dai Aunty'n Laylerh bata samu damar zuwa ba,Umar Farouq ma bai zo ba sai dai wannan Karon Mommy Sulaiman taje..Accountant ne tsaye a gaban court inda barrister ke tambayar shi alakar shi da Gloria da kuma abunda ya faru a ranar da ta mutu

"She was my girl friend sannan ranar da naje da ita company a ranar Laylerh ta kashe ta Wanda kuma ban San dalilin ta Na yin haka ba". Kallon shi Barrister Usman ke yi Wato barrister'n Laylerh can yace

" for how long Ka Santa?"

"Gaskiya Mun jima sosai tare da ita kuma muna matukar son juna".

" but me yasa tunda aka Fara wannan case baka taba zuwa court ba sai yau da ake zama Na uku".da yake dama ya gama tsara abunda zai fada a gaban court Kai tsaye ba tare da jin wani dar dar ko tsoro ba yace

"Saboda a lokacin ban gama dawa normal ba ma'ana ban fita daga shocked Na mutuwar ba". Murmushi Mai cike da ma'anoni Barrister Usman yayiwa Accountant Wanda ya sa shi tsorata nan yace

" ohk zaka iya tafiya ".boyeyyiyar ajiyar zuciya ya sauke sannan ya nufi fita a court din gaba daya ba tare da an kammala case din ba a daidai lokacin ne kuma Madam Rebecca ta samu Isa cikin court din,yana ganin ta ya Fara kokarin buya don kada ta ganshi sai dai abunda bai sani ba shine ta Riga da ta Gan shi

" what the hail are you doing here wallahi yau Zanga Mai raba ni da Kai dama Na sani dole kana da hannu a wannan kisan".

Cikin Dan daga murya alkali yace

"Behave nan court ne ba zaki zo kina mana abunda ran Ki ke so ba". Sassauta muryar ta tayi inda wutar bala'i ke ruruwa a gaba daya ilahirin naman jikin ta so take a bar ta da accountant yau din nan ba sai gobe ba zata aika shi lahira murya Na rawa tace

" Sir wannan mutumin shi ya kashe mini daughter Na".

"Kina da prove". Alkali ya tambaya Kai tsaye nan ta girgiza Kai sai yace an gama da batun accountant kam..roko da magiya ta Fara cikin rashin sanin abun yi ta Fara fad'in

" wannan da kake gani ba kowa bane face uncle din ta Wato kanin mahaifin ta,Tun lokacin da mahaifi Na yace ba zai rike Gloria ba na maida ta wajen mahaifin ta don tsanar sa ya Fara shafan ta,to daga wannan lokacin suke tare da shi wannan

mutumin suna zaune a gida daya har ta Fara girma,lokacin da mahaifin ta ya Fara samun kudi sai yake kashe Mata har zuwa lokacin da ya mutu..

Daga wannan lokacin suka koma zama tare da shi wani lokacin har kokarin keta Mata haddi yake Amma taki bashi fuska, ganin tafiyar su ba zai zama daya ba sai ya Fara Neman hanyar da zai yi ya mallaki dukiyar ta tunda ita ce kadai magajiya, so dama yana kokarin kashe ta sai dai Na kan kare ta sai a wannan gaban ne ya cimma hakar sa".duk da kasancewar ta soja sanda ta kare zancen da rauni tuna yadda tayi banza da Yar ta a matsayin ta Na uwa,shiru court din yayi accountant ko cewa yayi

"Karya take yi ban San ta ba". Da yake lawyer da ya kamata ya kare shi from the start Sulaiman ne ya nemo shi to yanzu kuma Sulaiman ya gano gaskiya ya kuma ce da lawyer'n kada ya yawaita magana yayi shiru kawai ya nuna an kure shi shiyasa baya cewa komai sai lawyer'n laylerh ne ya mike yace

" duba da yadda wannan Shari'a ke tafiya inda a farko accountant yace shi saurayin ta ne sannan yanzu kuma ya tabbata uncle nata ne hakan Na nufin bai da gaskiya sannan shi yayi kisan,ina rokon wannan court Mai daraja da ta yanke mishi hukuncin da ya dace da shi".yana kaiwa nan madam Rebecca ta Karba

"Karya yake shi ba saurayin ta bane uncle nata ne". Don ita bata court din lokacin da yace haka

" kuna da shaida ".tabbas dole sai suna da shaida Gashi basu da shi shiyasa suka Fara kallon kallo

" Ee muna da shaida a gafarce ni kuma Na shigo court din a makare".duk juyawa suka yi suna kallon Umar Farouq Wanda Laylerh kam ta kasa cire ido a kan shi don bata yi tunanin zai zo ba saboda last word da yayi altering Mata,sanye yake cikin red suit ya matukar yi kyau gashin kan shi sai sheki yake a haka ya cigaba da shiga court din har ya Isa gaban alkali..

Tunda Sulaiman ya Gan shi sai ya nemi nitsuwar sa ya rasa haka kawai yake jin zafin Umar Farouq din shiyasa ya daga Kai ya Kai duban sa ga Laylerh daidai lokacin ita ko bin Umar Farouq take da idanu kamar zata hadiye shi don mamakin ganin

shi,ji yayi tamkar ya tashi ya shake Umar Farouq sai dai ya San hakan ba mafuta bane shiyasa ya Fara kokarin danne bacin ran shi..

Koda Umar Farouq Isa gaban alkali labtop da ke hannun shi ya bude yana fadin

"A gafarce ni nabi ta legal way nayi sourcing information". Nan yayi playing vedio inda Mata Mai shagon ke cewa accountant ne yayi kisan,Bayan alkali ya gama kallo nan ne ya juyar da fuskar system din ga yan court din kowa ya kalla,a take accountant ya Fara hada gumi nan alkali ya gyara zaman glass Na idon shi yace

" yanzu dai ya tabbata Kai ne Kayi kisan don haka kada Ka wahalar da shari'a wajen amsa laifin Ka..

A ranar da aka sace Mata Mai shago Umar Farouq ne yasa aka Mata duk wani abunda aka yi Mata sannan ya Kira line Na Laylerh a kashe sai ya Kira Auta ko da ta hada su sai yace taje dakin shi ta bude inda aka yi drower ta dauko system sai ya fadi Mata duk yadda zata yi.

"Sharrin shaidan ne". Cewar Accountant nan dai aka yanke mishi hukuncin kisa ta hanyar rataya sannan aka yankewa Mata Mai shago shekara uku a gidan yari,court ta wanke zargin da akewa Laylerh Na kisan Kai..

Wannan abun ba karamin faranta ran Laylerh yayi ba shiyasa a wajen tayi sujudu-shukur,yadda take farin ciki haka ma Sulaiman zaka ce tare aka musu sharri kallon ta yake yana murmushi a ran shi yake tuna yanzu zata zo mishi godiya saboda kawo madam Rebecca da yayi Gashi yanzu an gama wannan case,lumshe idanun shi yayi ya sake bude su a kan ta sai yaga ta nufi inda Umar Farouq yake.

Fuskar ta dauke ta murmushi har ta karisa inda yake Wanda shi tsam bai San da Isar ta wajen ba saboda waya yake yi,farin cikin da take ji a yau Wanda shine sanadiyar shi ta rasa taya zata Fara gode mishi,a sanadiyar shi ta hadu da mahaifiyar ta da kuma Dan uwan ta sannan tunanin ta ya dawo, a sanadiyar shi kuma ta samu ta kammala secondary school nata har tayi diploma..

Ta sani baya son ta saboda yana jin ya fita nesa ba kusa ba haka ita ma ba son shi take yi ba sai dai kuma a yanzu ganin Naseer take mishi Wanda ya inganta rayuwar ta ta kuma yi alkawarin ba zata sake son wani don yana taimakon ta kamar yadda tayi misunderstanding Naseer ba,shi din zai zama kamar yaya ne a Gare ta kuma zata cigaba da girmama shi shiyasa ta lumshe idanun ta ta sake bude su akan shi,a hankali ta Ciro hannun ta dake cikin hijab nata ta Kai ga hannun shi..

Tabbas taji sauyi sai dai ta danne don bata son katse mishi kirar,sanyin tafin hannun nashi take ji har jikin ta..

Shi ko jin yadda aka rike hannun shi ya tabbatar ba Na miji bane don jikin shi ya bashi shiyasa ya rintse idanun shi da wuri, a hankali ya bude idanun ba tare da ya kalle ta ba ya cire hannun shi cikin nata sannan ya juyo Gare ta

"Na gode sosai Allah saka da Alkhairi". A saman labban shi ya amsa da Ameen ita ko sai godiya take jero mishi..

Duk abunda suke yi idon Sulaiman Na kan su Wanda ya cika saura ya fashe,Mommy Sulaiman ma ta gani saboda yadda d'an ta ya kura musu ido yasa ta kallon su..

Dafa kafadar shi tayi ko da ya dago sai taga Ashe kuka yake yi,da wuri yasa handkerchief ya goge da wuri kuma ya fice a harabar court din ya nufi gida yana kuka kamar karamin yaro..

Baaba da malam ne suka mishi godiya on behalf of Aunty'n Laylerh da bata zo ba daga nan yace zai koma hakan ce ta kasance..

A bangaren Sulaiman kuma baya mom nashi ta rufa mishi tana Isa gida direct apartment nashi ta wuce, a parlor ta tarar da shi sai kuka yake kamar karamin yaro Wanda shi kan shi bai San dalilin kukan ba

" kana son ta ne?"a sama ya jiyo muryar ta da wuri ya share hawayen sa sannan ya dube ta ba tare da yace komai ba

"From the start sanda nace maka in kana son ta Ka fada mini but Kayi denying Gashi yadda abun ya zama yanzu". Sai a yanzu ya mike inda take ya nufa idanun shi jazir hannun ta ya kamo da dukka hannun shi cikin disheshiyar murya yace

" mom kin Sani ba Zan iya boye miki komai ba ban taba jin ina son laylerh ba sai a yau da Na ganta da wani,Mom ji nake kamar zuciya ta zata fashe Na tsani wancan garan mom,pls Mom I need her in my life wallahi Mom ina son ta".ido ta zuba mishi tana kallon shi for the first time taga ya karaya har yana hawaye a kan mace yana kuma cewa yana son ta..

"Fine Na maka alkawarin nema maka auren ta in no time ko da anyi baikon ta".

" Mom sun jima da shi fa kuma shi ya biya Mata kudi tayi karatu".

"Don't you trust me ko Ka manta wace ce Mom naka tunda ni nace maka Zan aura maka ita to Ka Fara shirin Aure kwananan". Ya sani zata iya mishi komai a duniya tunda makaho aka haife shi Amma bata karaya ba haka ta Riga nema mishi magani har ya warke sannan daidai da Rana daya taba taba barin shi yayi rashin uba ba..

Ficewa tayi tana tuna yadda zata Isa ga iyayen Laylerh..

Koda Umar Farouq ya Isa gida sosai yayi mamakin ganin motocin Abban shi a gida Wanda ya tabbatar kila akan rashin lafiyar Sadiya ce shiyasa ya yanke hukuncin sanar da agency su sai su San yadda zasu yi da Sadiya don ya gaji da ganin ta a gidan su Kai tsaye cikin gidan ya nufa..

A falon kasa ya tarar da Abban shi da Aunty Hauwa sai kuma oga'n shi Na wajen aiki

" to kaga ga nan Umar Farouq kam".Cewar Aunty Hauwa duk juyawa suka yi suna kallon shi

"Umar ina kaje baka gida kuma baka office?"

"Sorry Abba naje taraba ne kuma da private jet naje kasan yau aka koma court". Ya fada lokacin da yake Mikawa oga'n shi hannu suka gaisa sannan ya nemi waje ya zauna yana Mai yiwa Aunty Hauwa tambaya da ido ko lafiya ita ko Abban shi ta nuna mishi da ido sai ya maida hankalin shi kan Abban nashi

" ni kwata kwata Na manta yau zaku koma court din so ya case din?".ajiyar zuciya ya sauke sannan yace

"Alhamdulillah an gama case din kuma ba ita ce tayi kisan ba". Daga nan sai ya basu labarin yadda abun yake

" Masha Allah Alhamdulillah ".shine abunda suke nanatawa nan ne Abban shi yayi gyaran murya yace

" Umar Farouq jikin Sadiya yaki sauki a halin yanzu Mun dawo da ita gida sannan Na gama yanke hukuncin zaka auri Sadiya to save her life".da sauri ya mike yana kallon Aunty Hauwa domin tabbatar da abunda Abban ke fadi haka ne duk da ya San magana daya Abban ke yi ita ko da ido ta mishi alamar ya zauna shiyasa ya koma ya zauna murya cike da rauni yace

"Abba Ka gafarce ni in abunda Zan fada yanzu zai bata maka rai,da farko Ka mini zabi wacce tsam ba son ta nake yi ba Amma Na karbe ta hannu biyu har ya Kai ga Na tsaya Mata sannan Na iya zuwa domin kare ta ba tare da Na sanar da kowa ba duk don Na faranta maka ne ba don yin Kai Na ba,sannan yanzu kuma a sake dauko mini wani Abba sai nake ganin kamar ba'a mini adalci ba a bar ni Nima Nayi zabi na". Tunda ya Fara magana duk suke kallon shi har zuwa yanzu da ya Kai Aya

" cikin ni da Kai wane ne ya haifi wani?"can kasa kasa yace

"Kai ne".

" to a matsayi Na Na uba a Gare Ka umarni nake baka ba shawara ba Zan jinkirta batun Laylerh Ka Fara da Sadiya ".

" Alhaji ni sai nake ganin tunda abun haka ne duk a rabu da su ya nemi Wata wacce yake so".

"Ai Na sani ba sai kin fadi haka ba,tuni Na gane kece Mai hure mishi kunne Wato Na raini Dan maciji ya girma,sanin kanki ne bana karya alkawari dole sai ya Aure su.. In har Ka Ki bin doka ta to da Kai da ita duk zaku bar mini gida Na". Fuuu ya fice kamar kububuwa wannan wace iriyar rayuwa ce shi ina zai Kai Sadiya mutum sai kace Mai HIV sannan wancan karamar su Babbar su sai uban rawan kai..

Spot car ya dauka cikin bacin rai ya jefa a titi nan ya Fara zagaye titin kamar yadda Sadiya ke yi,yafi awa biyu yana zagayen kan ya nufi guest house nashi a can yayi wanka Bayan yayi ordern abinci yaci sai ya kwanta bacci..

A can cikin gida kuma jin da spot car ya fita sai hankalin Aunty Hauwa tashi don akwai time da yake irin wannan yanayin yana fita kuma yayi accident..

M Wakili kuma number'n Malam yayi dialing Bayan sunyi sallama da oga'n Umar Farouq Wanda shi zai zama waliyin Sadiya ya tafi..

A can bangaren malam kuma yana zaune a falo don basu jima da dawa daga court ba..

Ummi ce tayi sallama a kofar dakin ita da Wata budurwa kyakyawa nan malam ya amsa Bayan sun gaisa sai tace

" wallahi zuwa nayi Na muku Barka game da abunda ya faru".yau dai daga malam har Laylerh Kai har su Baaba ma suna farin ciki nan aka zauna Ana ta hira da ita Laylerh.. bakuwar da Ummi tazo da ita kuma sai karewa gidan kallo take don ya Mata kyau tana kuma mamakin yadda Laylerh ta canza kamar ba ita ce yarinyar da shekaru biyu da suka wuce ta zauna a gidan Ummi ba..

Basu wani jima ba don Kira da Ummi ta samu wajen mijin ta nan suka koma Bakuwar kuwa Ai anguwar su Ummi gaba daya ta shela yadda Laylerh tayi kyau da kuma haduwar mijin da zata aura don taga hoton shi a wayar Auta..

Bayan tafiyar su kokarin mikewa yake sai ga kiran M wakili Bayan sun gaisa sai yace

"Na San abunda Zan fada zaka ji shi wani iri, batun auren Umar Farouq da Laylerh nake son a daga zuwa wani lokaci saboda wani dalili dan zai yi Aure". Dama Laylerh Na jera abinci a dining da hannu ya Mata alama tazo Baaba kuma Na falo,Auta ko ganin an Kira Laylerh ita ma sai ta nufi falon,a hands free yasa wayar sannan yace

" Alhaji network Na ba kyau Dan maimaita maganar da Ka fada".

"Dama batun auren Laylerh da Umar Farouq ne nake son a Dan daga zuwa wani lokaci yanzu zai auri Wata,ba kuma nayi hakan don cin zarafi ko wani abu bane Ka sani ni din mutum ne Mai rike alkawari Zan kuma aurawa Laylerh Umar Farouq". Gaba daya sun nitsu suna jin abunda yake fadi sai malam ne yace

" Alhaji ni ko sai nake ganin in har dalilin ba wani Babba bane me zai Hana a hada auren su kawai".tabbas shawarar ta mishi don bai kawo haka a ran shi ba nan dai yace zai yi tunani sannan suka yi sallama..

A hankali Laylerh ta mike ta nufi daki tana Mai jin tsanar Umar Farouq fiye da kullum, ta sani Tun ba yau ba baya son ta biyayya kawai zai yi ga mahaifin shi Wanda yanzu kam ya fito fili ya nuna ma duniya bai da bukatar ta wacce yake so zai Aura shiyasa cikin jin takaici ta Kira Aunty'n ta ta sanar Mata komai

"Kina nufin dama baya son Ki?"

"Eh Aunty".

" Kin sha wahala dayawa a rayuwa diya ta ba yadda za'a yi ki auri Wanda bai ganin mutuncin ki sannan ya hada ki kishi da Wata, jarrabawa iri iri Kika gani yanzu lokaci yayi da zaki Fara jin dadi don Zan bayyana sirrin boye da ya Dade a rufe Wanda sai ya jijjiga kowa ".tana gama fad'in haka ta katse kirar Laylerh tayi ta kiran ta taki dagawa

" mene ne wannan sirrin da Aunty ke cewa sai ya jijjiga kowa?"

Koda ya dawo gida ganin shi cikin koshin lafiya sosai ya faranta ran Aunty Hauwa nan ta rufa mishi baya,sanin tana biye da shi a falo ya tsaya

" Umar Farouq Na sani hukuncin da Abban Ka ya yanke maka bai yi daidai ba sai dai biyayya zaka yi kamar yadda kake yi koda yaushe sannan Ka sani wannan Karon Sadiya ta shiryu da gaske take son Ka Ka Aure ta don Allah ".

" Aunty Baku San wacece Sadiya ba".

"Umar mutum kan canza Dan Allah Kayi tunani a Kai in ba dai so kake ni da Kai mu bar gidan nan ba". Daga haka ta fice..

A Washe gari Ana breakfast har da shi Umar Farouq din sai Abba yace

" jiya Na maka magana baka bani amsa ba duk da zaman Ka a gida Na yana nufin Ka amince ".dakatawa yayi daga cin abincin sannan yayi gyaran murya Bayan ya goge bakin shi da tissue

" duk abunda Ka zaba mini Na tabbatar Mai kyau ne don ba zaka cutar da ni ba,Na amince Zan Aure ta in har yin hakan zai faranta maka".ya gama fahimtar Abban shi nasa sunan Aunty Hauwa ne a cikin zancen don ya San ba zai taba Mata butulci ba ko don yadda tayi fama da su

"Allah maka albarka sai dai a halin yanzu Na canza shawara nan da sati biyu Zan aura maka Sadiya da Laylerh".

Comment

Share

©Hafciey Musa

[1/25, 5:43 AM] Hafciey Musa😘: *□LAYLERH□*

(The prettiest emerald)

Thank you for contacting Sdeendtm! *BUY DATA FROM THE AFFORDABLE PRICE*

I selling MTN data with this cheap price

MTN DATA PACKAGE

500MB@===200

1GB@=====300

2GB@=====600

3GB@====900

5GB@====1,500

Dial *131*4# or *460*260# to check Data balance.

Validity 1 month

Airtel,9mobile and Glo *also available.*

Subscription for DStv gotv star time electric pay bills *Whatsapp OR

Call 08066268951*

Tabbas wannan labarin ya faranta ran sadiya shiyasa ma taji sauki yanzu haka zaune suke a dining har shi Umar Farouq din Ana breakfast sai dai tsam ta gagara nunawa saboda ta San dole aka mishi kuma taga yadda yake cin abincin kamar dole...

Wayar tace ya Fara ringing ganin sabon number sai tayi picking sai hello Hello take cewa

"This days network Na gidan nan Nada matsala Nima jiya haka ya mini kisa a hands free" Abba ya fada ba tare da ya kalle ta ba,Satan kallon Umar Farouq tayi sai ganin shi tayi yana ta wasa da cokalin hannun shi ya kasa cin abincin, sanin in bata sa a hands free kamar yadda Abba ya Fada ba zasu ga kamar bata da gaskiya shiyasa Tasa..

"Salamu Alaikum Haleema ina ta kokarin kiran Ki bana samun Ki". Ba yan cikin falon kadai ba Harda Umar Farouq da yake cikin yanayin damuwa sanda ya daga Kai ya dube ta saboda muryar ba abunda ya banbanta shi da Na Sadiya, da ace Sadiya bata wajen sai suce ita ce..katse kirar tayi tana fad'in

" Zan Kira Ki".duk da ido take bin su daya Bayan daya ta kuma tabbatar kowa da alamun tambaya a fuskar sa,tana son kallon Umar Farouq Amma tana tsoro..

"Kince baki da Yar uwa wannan da ta Kira Ki muryar Ku iri daya kuma wace ce?" Abba ya gefa Mata tambayar yana kallon ta

"Kawa ta ce kuma haka kowa ke fadi Wai muryar mu daya sai dai tsam bamu Kama ko kadan". Ba Wanda ya sake cewa da ita komai sai Beta dake gefe ne tace

" Mammi time Na tafiya kuma kinyi alkawarin yau zaki je PTA meeting Na school namu".shafa kan Beta tayi sannan ta dubi Najeeha tace

"Pls Najeeha Ki Kai mini ita". Daidai lokacin Abba ya mike Bayan ya goge bakin shi da tissue ya nufi ciki, a hankali Aunty Hauwa ma ta mike domin bin Bayan mijinta ta taya shi shiryawa tana fad'in

" a'a Sadiya Kije da kanki Ai kin warke ko ba komai yarinyar zata ji dadi".ta karashe zancen ta tana shigewa ciki ba tare da ta jira amsar Sadiya ba Wanda hakan Na nufin umarni take bata..

Kallon juna Najeeha da Hajara suka yi ganin har yanzu Umar Farouq bai mike ba sannan su biyu suka rage don Salman da Yasmeen tuni suka tafi makaranta..

Da ido Hajara ta nunawa Najiha daki,ta kuma fahimci Yar uwarta ta Na nufin su basu waje shiyasa ta dauki cup of tea sai wayar ta a tare suka mike,beta kuma ganin Najiha ta mike don duk gidan sun fi shakuwa sai tabi Bayan su..

Shiru dining area yayi inda baka jin komai sai karar Ac da kuma cokalin da Umar Farouq ke wasa da shi akan plate, ido Sadiya ta daga ta dube shi ta kuma tabbatar wutar bala'e zai Mata sai dai ga mamakin ta sai taga ya lumshe ido ya kuma bude su a hankali ya mike yana tura kujerar da ya zauna baya kadan sannan yasa hannu a aljihun wandon shi ya juya ya nufi downstairs, da ido ta bi shi wanda ta tabbatar shirun shi ba Alkhairi bane a Gare ta tunda an tsaida batun auren su Amma bai ce da ita komai ba ita wallahi gwara yayi magana ko da zagin ta ne yayi..

Cikin mutuwar jiki ta nufi dakin ta nan tayi Dan danne danne a wayar ta kamar dai abu take turawa sannan ta fada toilet tayi wanka tare da shiryawa..

Koda beta ta shigo Najiha ta shirya ta tsab shiyasa suka fice a gidan..tunda suka yi nisa a tafiya ta fahimci wani mota Na bin su duk da ba ita ke driving ba,fahimtar haka yasa ta cewa driver ya tsaya daidai wani shago nan ta fice zuwa shagon tana kallon motar dake bin ta da gefen ido yayin da Mai shi ke waya,don kwarewar ta a aikin ta da kuma bincike ta fahimci yana sanar da wani inda ta tsaya ne..abunda ba'a rasa ba ta saya duk da bada niyar sayan ta sauka ba nan suka cigaba da tafiya ta sake ce da driver ya tsaya nan motar ta tsaya sai ta fice tare da cewa driver ya jira ta a wani wajen..koda driver ya tafi sai ta fahimci ita din ake bi ba driver ba shiyasa tayi yadda zata yi ta bacewa motar nan ta samu driver suka nufi makarantar..

Da yake hijab Mai face mask Tasa sai ba zaka ga ramar da tayi ba a haka har aka kammala suka nufo gida..

Shi ko Mai bi Mata ganin ta bace mishi sai yayi waya bayan nan juya ya koma inda ya fito..

Adamawa

Shirun Aunty tayi inda ta kurawa waje daya ido, tunda Laylerh ta sanar da ita batun jinkirta auren ta da kuma cewa Umar Farouq ba son ta yake yi ba daga wannan ranar ta daina bacci don yar tata ta wahala sosai a tunanin ta lokacin jin dadin tane yayi Ashe da saura..

Muhammad ne a gefen ta yana goge Kayan shi kallo daya ya Mata sai yace

"Aunty Nifa banga abun tunani a nan ba,naga Laylerh da gatan ta tunda muma son ta suke walakanta ta kuma Ai ba shine autar maza ba a fasa auren Allah zai kawo Mata wani Wanda yafi shi Tun yaushe nake fadin haka kin Ki yarda da shawara ta". Ba tare da ta kalle shi ba har yanzu waje daya take kallo tace

" Muhammad ina so in inganta rayuwar Laylerh, ina son Laylerh taji dadi kamar yadda ko wacce ya mace ke ji in tayi aure, ina so Laylerh tayi alfahari da ni ko Bayan raina sai dai Na Gaza don ban Isa canza kaddarar ta ba,Muhammad zanfi kowa murna idan aka fasa wannan auren don nasan ko anyi ba zata ji dadi ba tunda baya son ta sai dai baki Na yayi nauyi ba Zan iya ba,wadannan mutanin sune suka inganta rayuwar Laylerh Na sannan suka inganta tawa rayuwar bugu da Kari sune suka nemo mini Kai sannan gidan da muke ciki sune suka bani Harda jari...

Na sani zamu iya fasawa bisa wasu dalilai Amma kuma Ai Ana barin halaq don kunya, tsam ba Zan iya hada ido da su Bayan Na Hana su Laylerh ba".tabbas tayi gaskiya kuma shima jikin shi ya mutu shiyasa ya kashe dutsen gugan,Yar uwar shi Nada bukatar farin ciki a rayuwa sai dai har yanzu lokacin bai yi ba..

Mikewa tayi ta nufi daki wardrobe ta bude ta zabi Kayan ta Kala biyar tazo ta zuba mishi

"Ka goge mini su gobe Zan tafi Bauchi".

" Bauchi kuma?"

"Eh Ka goge Bari Na shiga gidan su zulai Na sallame su daga nan gidan ta nufa shi ko Kayan ya goge Mata..

Zuwa dare ta gama shiri tsab nan ta Fara dialing numbern Laylerh tana dagawa tace

" Laylerh ya wajen Ku?"

"Lafiya Aunty Kika Kira dazun muka gama waya?"

"Laylerh gobe zani Bauchi". Tashi daga kwancen da take tayi tace

" Bauchi kuma lafiya ".

" lafiya kalau zanje ne domin goben Ki yayi kyau".

"Gobe Na kuma?Aunty me zai Kai Ki Bauchi".

" sirri ne in Na dawo zaki Sani ".duk yadda Laylerh tayi da ita taki fadi Mata gaskiya dole suka yi sallama..

A Washe garin kuma Muhammad ya raka ta Tasha nan ta nufi Bauchi..

Isar dare tayi Amma da yake an San da zuwan ta nan aka zo aka dauke ta,sosai suka yi murnar ganin juna da matar da ta sauka a gidan ta..hirar yaushe gamo suka Fara daga baya ko suka koma hirar su ta sirri Wanda a karshe har kuka suka yi..

A Washe gari kuma suka shirya tsab domin zuwa gidan yayar ta Hadeeza don taji labarin tayi kudi kila zata iya taimakawa rayuwar Laylerh,da kyar Mai gadi ya barsu suka shiga nan agolan gidan ta fito tana Tauna chewing gum

" uhum Wa kuke son gani?"

"Alhaji Zakari".

" baya nan.

Kishiyar Hadeeza ce ta fito kallon Tara saura kwata ta musu don taga Kama tsakanin Aunty da Hadeeza

"Me ya kawo Ku gidan nan?" Ta tambaya duk da bata San su ba

"Wajen Mai gidan muka zo".

"Kunga Tun muna shaida juna Ku bar mini gida Na kuma ba zaku Gan shi ba".

" to ita Hadeeza fa?"dariya ta fashe da shi tace

"Tunda suka rabu ban San inda tayi ba". Ganin korar kare take son musu yasa Aunty cewa su tafi sai dai ya zama dole ta nemo yayarta don ta tabbata zata inganta rayuwar Laylerh..

Kwana biyu tayi ta koma saboda ta fahimci ganin Zakari abu ne Mai wuya don so take ta tambaye shi ko ya San inda Yar uwar ta take..

Niko nace tana can jalingo tare da Yar Ki Laylerh kina nan kina wahalar Neman ta..

Taraba

Gaba daya zuwa yanzu bai ji zai iya rayuwa babu Laylerh shiyasa lokacin da ya Kira ta yaji line busy sosai ran shi ke tafasa don gani yake kamar da Umar Farouq take waya,Allah ya sani ya tsani Umar Farouq..

Safa da marwa yake yi a bedroom din yana sake dialing number'n ta nan ta daga da sallama, boyeyyiyar ajiyar zuciya ya sauke sai kuma yace

" Na Kira Ki kina waya da Wa kike waya?"ita yadda yake nuna gadara akan ta ma abun har dariya yake bata

"Da Aunty Na".

" ya kamata Wata Rana Ki hada mu".

"In sha Allah". Tace da shi don ta fahimci son ta yake shiyasa wani zuciya ke cewa ta yarda da shi kawai ta fita harkan Umar Farouq, hira suka cigaba da yi kan su yi sallama ta kwanta..

Washe gari da yamma sai Gashi a kofar gidan Wai don ya Kira ta sau biyu bata yi picking ba shine gaba daya ya tada hankalin shi ya nufo gidan su..kirar ta yake a zuciyar shi yana cewa in bata dauka ba shi zai shiga gidan kawai sai ko ta daga

" Ki fito gani a kofar gidan Ku".yana gama fad'in haka ya katse kirar ita ko kallon wayar tayi tana mamakin shi..hijab ta dauka nan ta nufi fita a tsakar gidan suka hadu da malam

"Ina zuwa da yamman nan?"

"Dama Boss nane yazo karban wani sako". Ya gane hanyar Zamewa take nema shiyasa yace

" LAYLERH kada fa Ki manta har yanzu akwai maganar Aure tsakanin Ki da Umar Farouq don haka kibi a hankali ".to kawai tace ganin ya cigaba da tafiya sai ta fice..

Shigar shi gida yayi daidai da shigowar kirar M wakili wayar shi nan yayi picking lokacin da yake zama a kujera yana kuma cire hular shi

" wa'alaikisalam ".

" malam Ku shirya an tsaida bikin Laylerh nan da sati biyu sai a sanar da yan uwa da mahaifiyar ta".wani bangaren zuciyar shi yayi farin ciki wani ko kishiyar haka ne don hankalin shi ya Fara karkata ga Sulaiman don yaga kamar zata fi samun

kwanciyar hankali ba kamar can da zata zauna da kishiya ba shiyasa da to kawai ya amsa..

Auta taji zancen Harda Baaba sai dai fa Auta kanta ta tsorata don ba zata iya zaman kishi da Wata ba tunda ita ce zabin Umar Farouq karshe wahala kawai zata sha gwara dai Laylerh din taje ta wahala tunda ta Saba..

Ita Baaba ma abunda ke ranta kenan..

A can waje kuma kamar zai Mata kuka yace

"Wai ina kike ajiye waya ne?"

"Ina aiki ne fa".

" gaskiya ni bana son wannan aikin Zan nema muku Yar aiki nake biyan ta".kallon shi tayi tana fad'in

"Ni dai gaskiya Ka rufa mini asiri, ba gwara Na koya ba".

" tunda haka Kika ce Shikenan Mommy ma tace Na gaishe Ki".

"Ina amsawa". Daga nan samples Na akwatuna ya Fara nuna Mata yana kuma tambayar ta Wanda take ganin yafi kyau,a haka suka dau lokaci ganin magrib ya kusa sai ta sallame shi..

Yanzu ma a tsakiyar gidan ta hadu da malam za shi masallaci

" Abban Umar Farouq ya Kira ya kuma ce a sanar dake auren Ki saura sati biyu".tsam ba haka ta so ba shiyasa ran ta ya baci nan ta nufi cikin gida ji take kamar ta rusa kuka..

Gaba daya birkewa tayi shiyasa ta Kira Aunty cikin kuka tace

"Aunty wallahi bana son shi Kice a fasa kuma fa da Wata zai hadani Allah in basu fasa ba Zan shiga duniya". Sosai zancen ta ya tada hankalin Aunty Amma sai bata nuna Mata ba cikin fada tace

" duniya kuma sai dai Ki kara tunda kin taba shiga,wallahi in baki da hankali Ki sake wannan maganar addu'a zaki yi sannan Nima Zan ga abunda zanyi".daga nan ta katse kirar..

Sulaiman ya Kira ya Kai sau biyar bata daga ba sanin zai iya dawa sai ta daga

"Me ya samu muryar Ki me aka miki?"

"Wai fa tsaida Aure Na aka yi nan da sati biyu ba tare da an shawarce ni ba".jin shi da Gan shi daukewa yayi Na wasu dakiku da kyar ya iya cewa

" da wancan garar?"sanin Umar Farouq yake Kira da gara shiyasa tace Ehhh daga nan ta katse kirar..

Ance in Ana sallah ba'a magana don birkicewan Sulaiman yafi Na Laylerh hauka tukuru da kuka yakewa Mom nashi da kyar ta lallashe shi ta hanyar cewa gobe za'a je nema mishi auren ta Amma duk da haka bai yi bacci ba..

Washe gari tsab Mom nashi ta shirya da kanshi ya Kai ta gidan,sai ta tsaya a waje..

Auta ce a falo lokacin da tayi sallama, fahimtar babbar Mata ce naira ya zauna sai ta durkusa a gaban ta

"Sannu da zuwa Hajiya ina kwana".

" lafiya kalau ko mamar Ku tana ciki?"

"Eh bara Na Kira miki ita". Nan ta mike ta nufi daki sai Gata sun fito tare da Baaba

" Hajiya sannu da zuwa".Baaba ta fadi tana zama".

"Yauwa Mun same Ku lafiya".

" lafiya kalau".daga nan duk shiru suka yi nan Auta ta kawo Mata ruwa

"Malam yana nan ne?"

"A'a yana kasuwa Amma ya kusa dawa tunda yau juma'a ce zai dawo wanka Allah dai yasa lafiya".

" lafiya kalau Laylerh fa?"

"Ina ga tana bacci". Daga wayar ta tayi nan taga missed call Na Sulaiman har biyu sai ta mishi text Na abunda aka ce..

Shiko yana can waje yau fa ko kwana ta Kama zasu yi don sai sun gana da malam..

Karfe sha biyu ya wuce Sulaiman cikin mota a kofar gidan don bai Lura da shi ba,text ya turawa Mom nashi kan cewa ga malam din yana shigowa gida,shi fa ya San dole shi zai Aure ta tunda ba son Umar Farouq take yi ba..

Malam Na shiga yaga bakuwar fuska nan suka gaisa har zai shige ciki sai Baaba tace

" Ai bakuwar kace Tun dazun take jiran Ka".Komawa yayi ya zauna ita ko cikin muryar gaskiya da gaskiya tace

"Suna Na Hadeeza nice mahaifiyar Sulaiman Wanda Na tabbata Ka San shi ko don zuwa wajen Yar Ka dayake yi". Kai ya gyada sai ta cigaba

" Sulaiman yana son Laylerh da Aure ne kuma alhamdulillah yana da aikin yi,a jiya yake sanar da ni an tsaida auren ta dawani Wanda Na tabbata Laylerh ba son shi taje yi ba,a zamanin yanzu an daina auren dole Na kuma zo ne don Na nema mishi auren Laylerh ".ajiyar zuciya ya sauke don zancen ya mishi dadi sai yace

" gaskiya nema cikin nema bai kamata ba sai dai kuma kamar yadda Kika fada bai dace a Mata dole ba,ni banda hurumin da Zan bada Laylerh ko Na Hana saboda wacce take da wannan hurumin tana Raye Na kuma miki alkawarin Zan sanar da ita sakon Ki duk yadda ake ciki zaki ji daga Laylerh ".godiya tayi nan ta fice koda ta sanar da Sulaiman sai yace in zuwa gobe ba'a basu amsa ba har Adamawa zasu je ta kuma amince don farin cikin shi..

Sai Sulaiman din ne ya sanar da Laylerh yadda aka yi ita dai bata ce komai ba don shi Sulaiman din ma bata tabbatar tana son shi ba..

Bayan kwana biyu!!

Ayyuka ne suka sha kan Sulaiman da kuma nuna mishi illar gaggawa da Mom nashi ke yi shiyasa ya hakura har aka Kai kwana biyu..

A bangaren malam kuma sanda yayi dogon nazari sannan a yau ya Kira Aunty'n Laylerh picking tayi Bayan sun gaisa sai yace

" Aunty'n Laylerh akwai wani yaro da yake zuwa wajen Laylerh Sulaiman Wanda suka yi case da shi,to a kwana biyu da suka wuce mahaifiyar shi tazo nema mishi auren Laylerh Niko sanda nayi dogon nazari Na sanar dake..

Gaskiya dai in har Laylerh bata son Umar Farouq kamar yadda shima baya son ta ina ga a hakura da wannan auren don nace Mata sai Na sanar dake".shiru tayi sai can tace

"Wannan ba maganar waya bace Ka sanar da ita gobe Zan zo mu hadu". Daga nan suka yi sallama..

Sosai Laylerh taji dadi jin gobe Aunty'n ta Na hanya har ta sanar da Sulaiman nan shima ya sanar da Mom nashi sai suka Fara shirin haduwa da ita..

A Washe garin ta Kira ta sanar da malam cewa ta kusa Isa Gata a Zing nan Laylerh ta sanar da Sulaiman shi kuma ya sanar da Mom nashi suka shirya tsab..

Abinci zai Fara ci sai ga kiran M wakili yana dagawa yace

" gamu a cikin jalingo da lefe da kuma komai da komai Na auren nan da minti talatin zamu iso".sosai hankalin malam ya tashi saboda ya ce da mommy Sulaiman tazo suyi maganar auren Laylerh da Mommy Sulaiman yanzu kuma Gashi an kawo lefe,tsam bai zai Bari su hadu ba,mikewa yake yi nan miya ya zube mishi a jiki don rudewa nan ya nufi Randa dake kitchen don ya wanke sai wayar shi ta fada a ciki..

Wannan ita ce Tashin hankalin da ba'a sa Mata Rana in Allah ya kaddara abu dole zai faru..

Gare Ku reader's shin ya zata kaya idan Aunty'n Laylerh ta hadu da yayar ta da take nema?

M wakili zai hadu da mommy Sulaiman da tazo Neman auren Laylerh ne kuma ya zai dauki malam?

In suka gane Laylerh da Sulaiman cousin ne ya zancen auren ta da Umar Farouq?

wallahi da ciwon Kai Na tashi niya Na nayi Mai yawa Amma na gagara manage this pls

Comment

Share

©Hafciey Musa

[1/25, 5:43 AM] Hafciey Musa😘: *□LAYLERH□*

(The prettiest emerald)

Kwance take kan katifa waya makale a kunnen ta don tsam bata San wainar da malam ke tuyawa ba

"Yanzu kam ta wuce zing mana". Daga can daya bangaren Sulaiman yace

" wallahi gaba daya Na kosa ta iso kin ga yanzu haka wanka Na fito tana zuwa kuma za'a tsaida auren mu nan da kwana uku".baki ta bude tamkar a gaban shi take tace

"Kwana uku kuma? Ina laifin Wata uku". Zama yayi a gaban dressing mirror inda ya makala wayar tsakanin kunnen shi da kafadar shi sannan ya dauki lotion ya Fara shafawa a lokaci guda kuma ya amsa Mata

" Ashe so kike Na haukace yanzu tsakanin Ki da Allah zaki iya Kai Wata uku ba tare da an aura mini ke ba". Can ciki ciki tayi dariyar mugunta sannan tace

"To me ne kamar yau ne Ai".

" rufe idon Ki".ya fadi yana mikewa tsaye saboda ya gama shafa Mai,cumb ya dauka yana Mai kallon kan shi cikin madubin

"In rufe ido Na kuma?"

"Yeah just do as I said". Yace da ita tare da ajiye cumb din ya nufi wajen Kayan shi,wardrobe ya bude inda ya ciro wani gezna blue a daidai lokacin ne kuma tace

" Na rufe".

"Ki rantse". A bangaren ta ko sai yanzu ta rufe idon ta tana fadin "wallahi Na rufe".

" ohk yanzu kiyi imaging ace har sahon Wata uku bamu yi Aure ba".ba tare da sanin zancen zuciyar ta ya fito ba tace

"Wallahi ba Zan iya ba". Wani mashahurin farin ciki ne ya lullube shi har bai San sanda ya naushi gado ba yana sakin murmushi

" sound Na me naji?"ta tambaya cikin jin kunyar cewa ba zata iya ba

"Abu ne ya fadi". Jikin ta ya bata karya yake yi shiyasa tace

" ko kuma farin ciki ya saka buga wani abu ba".keyar shi ya tsotsa yana mamakin yadda aka yi ta gane a lokacin ne kuma ya zare boxers ya sanya tare da murza towel dake kugun shi yayi kasa,vest ya dauka ya sanya sannan ya zauna a bakin gado yace

"I knew it kina so Na kawai baki son fada ne don taurin Kai irin naki Wanda Tun yaranta har yanzu yana nan".

" yaranta kuma a ina Ka San yaranta Na".murmushi yayi yana Kira Mata sunan makarantar da suka yi tare sannan yace

"Kin tuna wani head boy naku Sulaiman". Take zuciyar ta ya buga

" Ehhh Na tuna shi but me hadin Ka da shi".tsam ta mance shima sunan shi Sulaiman shiyasa yace

"Wancan Wanda yaci zalin Ki shine nan Wanda kike magana da shi". Ai ba shiri ta mike tana fad'in

" ban yarda ba ya akayi ban gane Ka ba".

"Wallahi nine kawai dai lokacin kina yarinya ne shiyasa". Nan yaci gaba da fada Mata Abubuwan da ya faru a wancan lokacin sosai tayi mamaki, gaskiya Sulaiman ya zalunce ni dayawa a rayuwar sa but with time Zan Rama".

" a ina zaki Rama".bata San yaji zancen ba sai ta murkuda baki don abun ya bata haushi Musamman yadda shi ya gane ta Amma ita bata gane shi ba sai tace

"Nikam Ai Na sani".

" Kinji haushi ne gaskiya ni bana son Mata Mai mantuwa kada yara Na su dauke ta,beside yara nawa zaki Haifa mini ".kunyar zancen sa ya sata katse kiran ba tare da ta bashi amsa ba koda ya sake kira sai bata dauka ba..

Murmushi yayi sannan yasa Kayan shi tare da daura agogo a hannun shi,gaban mirror ya tsaya yana fesa turare da kuma yaba yadda yayi kyau dole ma ya mallaki Laylerh don ita kadai ce ta dace da shi..

Bayan ya kammala shirin sa sai ya dauki wayar sa ya nufi apartment Na Mom nashi,a falo suka ci Karo ta shirya cikin lace nata Mai matukar kyau da Ka ganta kaga Babbar mace

"Masha Allah angon Laylerh yayi kyau". Murmushi yayi yana jin dadin sunan da ta Kira shi da shi nan suka fice zuwa wajen motocin su..

A bangaren Laylerh kuma tana katse kiran Auta ta shigo tace malam Na kiran ta nan ta mike ta nufi falo..

Dukkan su uku ido suka zuba mishi ganin yadda yake safa da marwa a falon bai kuma ce komai da su ba hakan yasa Baaba cewa

" lafiya kuwa Tun dazun hankalin Ka ke a tashe kaki cewa komai ".zama yayi yana kallon Laylerh yace

" akwai matsala ".gaban ta ne ya fadi don ba Wanda ta fado Mata face Aunty'n ta shiyasa idanun ta ya Fara Tara ruwa tace

" me kuma ya samu Aunty Na?"

"Kwantar da hankalin Ki lafiyar ta kalau,dama M wakili ne ya Kira ni yace suna jalingo Anjima kadan zasu kawo kaya sannan Gashi munce Sulaiman su zo".duk sun rikice Musamman ita Laylerh don ita fa Umar Farouq baya gaban ta sannan akan me zasu ke gadara da ita haka ake kawo kaya ne

" Ai kuwa don zuwa yanzu Na San dole sun fito gida".

"Wallahi ban son zama mutumin banza a idon su kuma Na rasa yadda Zan bullowa lamarin".

" Mallam a Kira gidan su Sulaiman din ace su jinkirta zuwa saboda motar Aunty'n Laylerh ta baci a zing kuma suna da yan uwa a wajen sai zuwa gobe su zo,kaga kafun nan su M wakili sun gama har sun tafi".Cewar Baaba

"Allah Sulaiman zai ce zai dauko ta".

" ba sai Ki Hana shi ba Ki nuna mishi ita Aunty'n Ki bata son haka".Cewar Auta..

Duk sun yarda da zancen nan ta Fara dialing number'n Sulaiman sai dai is not reachable

"Ki sake gwadawa". Duk ido suka zurawa wayar hannun ta jira kawai suke Sulaiman ya dau wayar sai dai bata shiga nan hankalin su ya sake tashi..

Suna cikin haka suka ji horn Ai ko sun San su Sulaiman ne

" kunga kuje Ku bude musu gate".Laylerh kam saban rudewa ita ce ta nufi gate din har ta Isa sai kuma ta juyo

"Ya baki bude ba?"

"Ba ni ya kamata Na bude musu ba". Auta ce ta nufi gate din Bayan ta bude musu sai ta musu sannu da zuwa ta juya zuwa falon

" wallahi su ne".Laylerh Na jin haka ta nufi daki malam ko waje yaje ya musu iso..

Koda suka shigo sai baza kamshi suke duk a sama suka zauna sai Auta ce ta kawo musu Kayan sanyi

"Sannun Ku da zuwa". Malam yace fuskar sa dauke da damuwa

" Yauwa Mun same Ku lafiya ".Mommy Sulaiman ta fada nan Sulaiman ya gaishe su sai dai sun Lura kamar mutanin suna cikin damuwa,da yake mommy Sulaiman she is straight forward person sai tace

" lafiya kuwa naga kamar Baku farin cikin zuwan mu".

"Ai kuwa ba lafi.....".malam ne ya katsewa Baaba zancen ta da fadin lafiya kalau..tsam bata yarda ba don kamar hankalin su Na wani waje sai Sulaiman dake baza idanu a falon yana Neman inda zai ga Laylerh..

Shiru falon yayi Na wasu mintuwa malam sai ajiyar zuciya yake akai akai,ganin kallon da mommy Sulaiman ke mishi Wanda yana da tabbacin Na tuhuma ne yasa shi yanke hukuncin fada Mata gaskiya kawai,gyaran murya yayi sannan yace

" a gaskiya akwai matsala, kamar yadda kuka sani ita Laylerh an Riga da an bada ita to fahimtar shi Wanda aka bata ba son ta yake yi ba ko taje can wahala kawai zata sha shiyasa muka yanke hukuncin bada ita ga Sulaiman in mahaifiyar ta tazo,to a halin yanzu kuma gidan su Yaron sun Kira ni sunce gasu a jalingo kuma da Kayan Aure suka zo shine fa duk hankalin mu ya tashi muna tunanin yadda zamu yi da Ku".ajiyar zuciya ta sauke sannan tace

"Alhamdulillah naji dadi da Ka fada mini gaskiya ko ba komai zamu San yadda zamu bullowa lamarin,gaskiya dai daya ce kuma ita ce sun Riga mu Neman auren Laylerh don haka mu zamu zauna a matsayin baki masu tarbar su Bayan sun tafi sai muyi zancen Sulaiman da Laylerh". Sosai wannan abun ya faranta musu nan aka cigaba da hira banda Sulaiman da ya nemi duk wani farin cikin shi ya rasa jin Wai zasu kawo kaya..

Cikin abunda bai fi awa daya ba motoci suka Fara horn,malam ne ya mike inda ya wangale musu gate motoci biyu kadai suka zo da shi don ba nuna Kai suka zo yi ba..

Abba da Amintaccen Aminin sa ne suka fito a motar farko duk sanye suke cikin Gare sun sha kyau kace daurin Aure suka zo yi,hannu malam ya mika musu suka yi musaba fuskar shi a sake don yanzu bai da sauran damuwa..

Dayan motar kuma Aunty Hauwa ce sai kanwar shi Mai bi mishi Nana da kuma Dan ta da take shayarwa..gidan suka zubawa ido suna kare mishi kallo,kallo daya zaka musu su hudun Ka San kudi ya zauna musu.

" Bismillah Ku shigo ciki".a tare suka jera zuwa ciki inda Baaba da Mommy Sulaiman suka basu wajen zama,matan ne suka Fara shiga kan mazan falon sai ya zama yana cike da mutani nan aka Fara gaishe gaishe, koda Aunty Hauwa da Mommy Sulaiman suka zo gaisawa sai suka gane juna don suna yawan haduwa gidan bikin manya a Abuja

"Masha Allah Hajiya Hadeeza ya amaryar tamu take a wajen Ki?" Dukkan su ba Wanda yayi tunanin za'a musu wannan tambayar ita ko cewa tayi

"Ai ni din uwa ce a Gare ta". A nufin ta uwar miji sosai suka yi murna nan Auta da malam suka fitar da darduma aka shimfida kasan bishiyar gwaiva inda aka fitar musu da abincin su..ganin haka yasa Sulaiman ficewa Kai tsaye motar shi ya shige tare da rufewa ran shi duk a jagule yana Danna wayar da bai San me yake dannawa ba..

Falon ya rage matan ne kadai,Auta ce ta mika hannu zata karbi Yaron Aunty Nana domin su samu suci abinci Amma sai yaki

" Kinga kyale shi yan Mata kiwuya Gare shi".Cewar Aunty Hauwa.. Abincin kadan suka ci sai Aunty Nana tace

"Yan Mata rowar amaryar tamu kuke mana ne". Duk murmushi suka yi sai Mommy Sulaiman ne tace

" Kinga je Ki Kira ta su gaisa".ciki ta wuce kwance ta samu Laylerh tana waya da alama kuma duk abunda ya faru take sanarwa Aunty'n ta da kuma yadda suka shawo matsalar

"Laylerh ance kizo".

" Aunty Bari naje Ana nema Na ke ma Na San nan da minti talatin zaki iso Allah kiyaye hanya".Ameen tace sannan ta katse kirar,kallon Auta tayi tace

"Suna dayawa ko?"

"A'a Mata biyu ne kawai sai mommy Sulaiman".

" ni wallahi zuciya ta sai bugawa yake yi ".

" Kinga kizo muje kan ace wani abu".hijab babba ta dauka nan suka fito falon kan ta a kasa,sosai mommy Sulaiman ta zuba Mata ido tana kuma ji a jikin ta Sulaiman ne yafi dacewa da Laylerh ba wani can daban ba,kallon kulilla Nana ke Mata ta kuma gano yarinyar kyakyawa ce hancin da babu kuma ba matsala bane sai dai Sadiya tafi ta kyau,Aunty Hauwa ma ta kalle ta ta kuma yaba da kyanta sai dai kuma gani take kamar tayiwa Umar Farouq kankanta...gaishe su tayi duk suka amsa cike da sakin fuska

Kanta a kasa har Mommy Sulaiman tace ta koma ciki da wuri ta mike don duk a takure take..

Driver's ne suka Fara shigo da Kayan akwati Masha Allah,daga cikin mota Sulaiman ya tabe baki yana fad'in

"Yanzu duk kudin su iya abunda zasu yi kenan,Bari a tsaida batun Aure Na da Laylerh sai sun sha mamakin Kayan da Zan Mata..

Akwati set uku ne,biyu nata sai daya Na iyaye..

" wallahi kun shammace mu da Mun yi gayya don aga kaya".Cewar Baaba

"Kada kuji komai baga Hajiya Hadeeza ba ita kadai ta Isa Ai".

Daga nan hira ake ba Wanda ya bude Kayan duk da Auta ta kosa a bude ta gani...

A can waje kam tsam su Abba basu ci abincin ba sai ruwa da suka sha cikin aro jarumta malam ya fuskanci Abba yace

" Alhaji akwai maganar da nake so muyi ne?"

"Feel free ina sauraro".

" Dama batun hadin wannan auren ne sai nake ganin kamar ya kamata muyi maganar fahimta, kada ka damu wallahi in Umar Farouq ya fasa auren Laylerh ba zamu dauke Ka mutumin banza ba sannan zamu ci gaba sa zumunci..

Abunda Na fahimta shine shi Umar Farouq baya ra'ayin ita Laylerh to duba da yadda ta wahala a rayuwa sai nake ganin kamar lokacin jin dadin ta yazo bai kamata ace ta auri Wanda baya son ta ba don kada ta kare rayuwar ta a wahala Harda kishiya ".tunda ya Fara zancen shi suke sauraro har zuwa yanzu da ya Kai Aya

" Amma Kai me yasa kace haka?"Amintaccen M wakili ya tambaya

"Saboda da farko an tsaida auren shi da ita daga baya kuma yace a jinkirta karshe kuma zai hada su dukka, a gani Na Umar Farouq bai Kai munzalin da za'a hada mishi Mata biyu a lokaci guda ba tunda daya yake so kaga ita Laylerh wuya zata ci ga yanayin aikin shi ba zama yake ba". Sai yanzu Abba yayi magana

" Ka cire wannan tunanin a ranka duk wani hukunci nine nake yankewa Umar Farouq ba shi ba,sannan batun wacce yake so kuma duk cikin su bai bude baki yace ga wacce yake so ba a matsayin su Na matan shi zasu San yadda zasu ja ra'ayin shi sannan Na San wanene Umar Farouq ko yana son abu ba zai taba fada ba wallahi Laylerh ta mishi jin Kai ne kadai yasa yake share ta ".

"Amma baka ganin yin hakan ba daidai bane, a barshi ya zabi mata wacce yake so don ita Laylerh ma bata ra'ayin shi saboda akwai wani dake zuwa wajen ta".

" malam wacce Na zaba mishi Na biyu nema take ta zauce a kan shi Amma saboda rashin imani irin nashi bai damu ba,kuma yaran yanzu Ai in mutum yace zai biye musu sai a hankali mu dai roki Allah ya tabbatar da Alkhairi ".Ameen Ameen duk suka ce..

A can cikin mota kuma dialing wani number Sulaiman ya Fara yi Ana picking yace

" Haba Hajiyar nikab kwana biyu shiru ina Kika shige ne tunda aka gama case Na Laylerh baki zo kinyi congratulating nata ba Gashi yanzu har Ana shirin tsaida ranar auren mu".daga daya bangaren tace

"Kai alhamdulillah Amma naji dadi wallahi congratulations saboda Kayi dashen Mata,kada Ka damu in sha Allah zuwa jibi Zan shigo sai Ka Kai ni har gidan su Laylerh din mu gaisa,Amma fa sai Kayi alkawarin ba zaka fada Mata nice nan nace maka bata da hannu a kisan ba".

" nayi Amma saboda meyasa baki son Na fada Mata,wait are you related to her?"

"Ko kadan asalima Laylerh bata San ni ba haka Nima ban taba ganin ta ba,batun fada Mata kuma ban son lada Na ya zube don saboda Allah Na taimake ta ba don wani abu ba".

" kin kyauta Amma ni har yau ban daina mamakin yadda aka yi Kika fita a company'n mu ranar da Kika Fara zuwa aka neme Ki aka rasa ba".murmushi Mai sauti tayi sannan tace

"Wallahi buya nayi sanda aka gama nema Na security ya zaga sannan Na bude kofa Na fice abu na".

"To influence da connections nan fa daga ina Kika samu?"

"Ba ni kadai nake aiki ba akwai Yar uwa ta tare muke yi".

" ina ita Yar uwar taki".

"Kaga mu bar wannan zancen sai Na shigo jibi".

" Shikenan Allah ya kaimu".daga haka suka yi sallama..

Abuja

Shiru gidan yayi kasancewar su Aunty Hauwa Na Taraba yan matan gidan kuma sun tafi school, beta ma bata nan..

Sosai tayi kyau cikin shirin ta Na fita da tayi sanye take cikin doguwar Riga don bata son sa wasu kaya gudun kada ramar ta ya fito

Yau dai har powder ta saka purse ta dauka da car key ta fito harabar gidan inda ake ajiye motoci..

Umar Farouq Na can dakin shi tsaye yake a jikin window daga shi sai three quarter jikin shi babu Riga hannun shi rike da cup of tea yana sipping a hankali.

Sosai fatar jikin shi ta murje ya koma Umar Farouq nashi ba kamar lokacin da yake gidan malam ba..lumshe idanun shi yayi ya sake bude su yana Mai shakan iskan dake shiga jini da bargon jikin shi,juyawa yayi zai koma cikin dakin sai kuma yaga Sadiya Na kokarin shiga mota..hannu yasa cikin aljihun wandon shi nan ya Ciro karamin waya tare da Fara dialing wani number

"Yanzu zata fita a gida Ka tabbatar duk inda ta shiga kana biye da ita". Daga can bangaren yace

" ohk sir ".nan ya katse kiran ya koma bakin aikin shi..

Sadiya ko ficewa tayi a gidan Bayan an wangale Mata kofa, a lokacin kuma Wanda Umar Farouq yasa aiki ya Fara bin ta..sun yi tafiya Mai Dan nisa sannan Wanda ke binta yace driver ya sauke shi haka ko aka yi tari taxi tare da cewa yabi mishi motar Sadiya Wanda hakan umarnin Umar Farouq ne don ya Santa tsarai da Basira..

Gidan oga'n su ta nufa nan ya sanar da Umar Farouq ya kuma tambaye shi ko ya juya tunda yaga inda tazo kila tayi kwalliyar ne don kada a fahimci tayi rashin lafiya Amma sai yace ya dai cigaba da bin ta..

Kamar zata tsaya kofar gidan sai kuma tayi corner can nesa da gidan kadan tayi parking motar,daga can nesa da motar ta kadan keke napep din ya tsaya..

Wata Mata ce ta fito ta shiga motar sun jima a ciki ya kuma sanar da Umar Farouq din can sai ga Sadiya ta fito sai dai ta canza kaya nan ya sanar da Umar Farouq din..

Taxi ta shiga ta bar motar ta a wajen cigaba da bin taxi din yayi sai yaga Tasha suka nufa..

Koda ya sanar da Umar Farouq sai yace ko wani mota ta shiga ya bita nan ta shiga motar makodi haka Dan leken asirin Umar Farouq ma,mota daya suka shiga..

After one hour!!

Cikin shirin fita ya fito sanye yake cikin maroon suit Wanda ya matukar amshe shi sai shining yake sauri yake da alama wani waje Mai mahimmanci zai je..

Motar da Sadiya ta fita a cikin ta ne ya shigo gidan daidai inda ya tsaya aka yi parking nan Sadiya ta fito..

Ya sani tana da matukar wayo kenan ta fahimci bin ta ake yi shiyasa ta canza salo,wayar tace tayi ringing har a lokacin kuma yana tsaye don jiran driver ya Ciro mota yake,a hands free Tasa wayar

"Sadiya ance mini kinzo gida Na fita but gani Na dawo" da matar oga'n su take waya nan tace

"Alright yanzu Na shigo gida but gani nan zuwa". Ko kallon inda take bai yi ba sai shigewa motar da aka bude mishi yayi nan yayi dialing number'n Dan leken asirin shi

" ina take? "

"Gata nan next to me".

" rubbish ba zaka taba yin aiki da kyau ba Gashi Ka Bari ta tsere maka".daga haka ya katse kiran..

Sadiya ko fita tayi da motar nan ta koma gidan saboda a can aka Kai Kayan auren ta so take taje ta gani..

Sosai ta raina Kayan da aka Mata don komai daidai da Na Laylerh ne sai dai ba Na iyaye tunda ita marainiya ce

"Duk kudin da suke da shi iya abunda zasu yi kenan". Transfer 5 million tayiwa matar oga'n su tace a Kara Mata kaya don abun kunya ne kawayen ta su gani daga nan tayi tafiyar ta...

**

Tun Bayan da ta biya Mai keke kudin shi ta nufi cikin gidan zuciyar ta ke bugawa sosai da sosai ga kanta dake sarawa,a hankali ta tura karamin gate Na gidan ta shiga bakin ta dauke da sallama daga can nesa kuma take hangan su Alhaji M wakili..

Sulaiman dake cikin mota kuma ta mirror ya kalle ta ya kuma tabbatar ita ce mahaifiyar Laylerh tunda dama ita daya ake jira nan ya bude kofar motar ya fito yana Mai tsananin jin farin ciki tunda a wajen ta za'a nema mishi auren Laylerh..

Yana Isa inda take yasa hannun shi dukka biyu ya karbi jakar yana Mata sannu da zuwa sannan ya nufi ciki da jakar don dama hanyar shiga ciki yake nema don yace

da mahaifiyar shi ta fito su tafi tunda Maman Laylerh bata karaso ba don in ya cigaba da zama zuciyar shi zata iya bugawa..

A bangaren ta kuma wajen mazan taje cikin mutunta juna suka gaisa nan ta mike ta shiga ciki..

Mutum uku ne kadai a falon daga Auta,Aunty Hauwa sai Nana don mommy Sulaiman taje sallah a dakin Baaba,Baaba kuma tana kitchen tana Dan girka abun tabawa..

"Oyoyo Aunty sannu da zuwa".Auta ta fadi cikin sakin fuska don tuni Sulaiman ya shigo da jakan ta sai dai ganin mommyn shi bata falo yasa shi ficewa da wuri..

" Yauwa Auta ya gida".Aunty ta tambaya cikin sake fuska ita ma

"Lafiya". Auta ta amsa tana Mai mikewa domin zuwa kawo Mata abun sha..

Su Aunty Hauwa sun San ita ce mahaifiyar Laylerh tunda an sanar da su zuwan ta shiyasa suka gaisa cikin mutuntawa can kasa kasa kuma take kallon akwatunan dake zube a falon..ruwa Auta ta kawo Mata nan ta sha sai tace zata yi sallah a lokacin ne kuma Baaba ta fito nan suka gaisa cikin aminci ita har mamaki taji ganin yadda Baaba ta nuna kula a kan ta..mikewa tayi tana fad'in

" ina so Zan Rama sallah da ban yi ba".

"Bismillah muje ciki". Baaba ta fadi tana shigewa nan Aunty'n Laylerh ta biyo ta zuwa dakin Baaba inda Mommy Sulaiman ke sallah..

Taga Mata Na sallah ta kuma tabbatar ita ce suka zo Neman auren Laylerh a wajen ta tunda Laylerh ta sanar da ita komai a waya

" bismillah ga toilet Ki shiga sai kiyi alwala ".toilet ta shige nan Baaba ta fice a dakin..

Fitowar ta yayi daidai da idar da sallah mommy Sulaiman har ta cire hijab nata tana Nade sallayar da tayi sallah a kai,bakin ta har rawa yake saboda ita ce ta Fara ganin ta tace

" yaya Hadeeza ".tabbas mutum daya ke kiran ta da wannan sunan kuma ta jima ba'a Kira ta da sunan ba tunda bata gida da wuri ta daga Kai illa kuwa Amina kanwarta ta gani,da gudu kamar yarinya ta fada jikin mommy Sulaiman a tare kuma suka fashe da kuka Mai cin rai don sun fahimci illar sakaci da ziyara..

Sosai suke kuka sai dai ba Mai sauti ba don Ai su manya ne cikin kuka. Aunty tace

" yaya Hadeeza ina Kika shiga tsahon wannan shekarun wancan satin naje har Bauchi gidan mijin ki neman Ki".rungume Yar kanwar ta tayi tace

"Amina ban San yaushe rabo na da Bauchi ba,gidan mu ma tunda Na rabu da Zakari ban sake Komawa ba sai dai Na Kira Ummi Na a waya".

Sunyi kuka Mai Isar su don kan su suka yi shiru a nan ne kuma Aunty ta labarta Mata mutuwar mijin ta Musa sosai taji abun tunda ita ya Fara nema..

" akwai maganar da nake son muyi Amma kan nan Bari nayi sallah Kije waje Zan fito".

"Yaran ki nawa Anina?"

"Yara na biyu ke fa".

" Nima biyu ne Amma macen ta rasu yanzu saura Sulaiman ".

" Allah sarki yanzu dai Bari nayi sallah sai mu sha hirar yaushe gamo". mikewa mommy Sulaiman tayi toilet ta shiga ta wanko fuskar ta tana jin farin ciki Ai abun yazo da sauki Na gida za'a yi tsakanin Laylerh da Sulaiman ba wani batun Umar Farouq, to ta ya Na gida bai koshi ba za'a bawa Na waje da wannan tunanin ta fice..

Bangaren Laylerh ko Tun dazun Auta ta sanar da ita zuwan Aunty'n ta jira kawai take mommy Sulaiman ta fita a dakin taje wajen ta Ai ko tana fita da wuri ta shige sai dai ta tarar tana sallah dole ta jira..

Tana idarwa Laylerh ta fada jikin ta tare da fashewa da dariya

"Aunty nayi kewar Ki wannan Karon kam tare zamu tafi".

" to amarya Ai dole Na".cike da shagwaba tace

"Nidai ban son wannan sunan,suna Na Laylerhr Aunty'n ta Amma ya naga idon Ki ja me ya faru?gajeren tsaki taja sannan tace

" babu Kinga Bari naje waje ke kuma Ki cigaba da zaman daki".tura baki tayi lokacin da Aunty'n ta ke fita zata iya rantsuwa da sunan Allah bata taba ganin Aunty'n ta cikin farin ciki irin Na yau ba kila ba zai rasa nasaba da auren ta ba..

Dakinta ta koma ta cigaba da zama kamar sabuwar amarya..

A can falo kuma kusa da mommy Sulaiman Aunty ta zauna nan aka kawo Mata abinci sai tace

"Ni gaskiya in nayi tafiya bana iya cin abinci sai dai ko ruwan Lipton". Take aka kawo Mata Bayan ta sha ne kuma aka taba hira sannan Nana ta janyo akwatin tana fad'in

" tunda dama ita ake jira gwara mu bude".Kaya kam fa Masha Allah super wax ne exclusive sai manyan laces mommy Sulaiman sai kallo take ta daga ta nunawa Yar uwar ta don ita pendon amarya ce..

Koda suka zo kan Dan kunne an zuba gold har da irin Wanda mommy Sulaiman ta sata a shagon malam Musa Allah jikan rai nan ta daga tace

"Amina kin tuna wannan gold?" Kai ta girgiza

"Dadi Na dake mantuwa Ki tuna da kyau". Shiru tayi kamar Mai nazari can tace

" Ehhh Na tuna".

"Duniya kenan Gashi an Sawa 'ya ta irin shi a lefen ta". Kan Baaba fa ya daure ta rasa meke faruwa tsakanin mommy Sulaiman da Aunty'n Laylerh jin yadda take kiran ta da sunan ta da kuma yadda suke abu kamar sun San juna Amma ba bakin tambaya..

A haka suka cigaba da kallon Kayan har suka gama nan Auta ta fice ta tattaro kwanukan su malam nan ne aka ce tace da su su Alhaji M wakili zasu shigo suyi Sallam don zasu tafi..

Koda ta fada sai suka ture Kayan gefe,a can waje kuma mikewa duk suka yi suka nufo ciki aminin Alhaji M wakili ne ya dubi Sulaiman dake zaune cikin mota yace

" Dan samari zo mu shiga mana".don a tunanin shi Dan gida ne,duk da ran shi a jagule dole ya fito ya bi su cuxx ya San Dole Mom nashi zata yi wani abu..

Bayan sun zauna sai aka bude taro da addu'a Sulaiman dai sai tabe baki yake nan Alhaji M wakili yayi gyaran murya yace

"To alhamdulillah Na San duk kun San dalilin taruwan mu a nan an tsaida auren Laylerh da Umar Farouq Wanda yanzu saura kwana goma, to batun dawainiyar biki duk Mun sauke muku ban sani ba ko ita amaryar zata yi wani program Amma ni dai ban son bidi'a,walima kuma zata iya yi a nan Amma in taje can za'a sake Mata ita da mijin in akwai Mai magana kuma sai ya fadi". Duk Masha Allah suka ce tare da fatan Allah Kai su lokacin..

Sulaiman ko ya cika saura ya fashe ganin Ana kokarin kare zance kowa ya watse sai yace

" Assalamu Alaikum ".da wuri mom nashi ta dago ta dube shi don ta San dole zai yi something stupid shiyasa take girgiza mishi Kai Amma yaki sauraro

" ni dai zuwa muka yi tare da mahaifiya ta don a nema mini auren Laylerh amma ba Wanda naji yayi zancen ".shiru duk suka yi sai Aunty ce ta juya tana kallon yayar ta tace

" yaya Hadeeza kune kuka zo Neman auren Laylerh ".cikin jin kunyar abunda Sulaiman ya aikata ta gyada Kai

" kenan shi wannan din Yaron Ki ne?"Aunty ta tambaya tana nuna Sulaiman da yatsa nan ma da Kai ta amsa

"A'a yaya Hadeeza kada Ki mini karya Dan Allah gaskiya nake son ni,Na sani shi ba Yaron Ki bane saboda Na Riga Ki Aure ba yadda za'a yi ace kin haifi saurayi kamar wannan ba".

" Amina Ki bar maganar nan zamu yi shi Anjima ".

" a'a a Bari ya huce shi ke bada rabo ga wani Na roke Ki Dan girman Allah Ki fada mini me alakar Ki da shi?"jin ta hada ta da Allah sai tace

"Yaron miji nane?"

"Wani mijin Ki daya?"

"Alhaji Zakari mana". Da wuri Aunty ta Fara girgiza Kai tace

" to Ai ba Aure tsakanin su".

"Yanzu don abunda ya wuce a baya shine zaki Hana da Na auren Yar Ki?"

"Ko kadan Ai Mun Riga da Mun yafi juna a ciki".

" to meyasa Aure ya haramta a tsakanin su?"

"Saboda Sulaiman da Laylerh uban su daya ne".

Tirkashi!!!

Ehem a nan Zan Dan tuna muku wani abu don Na Lura kusan duk masu karanta Laylerh basu fahimta ba,Tun farko kamata yayi Ku gane Sulaiman ba biology Dan ta bane tunda dama malam Musa zata aura Amma Allah bai yi ba sai Amina ta Aure shi..kunga kenan Amina ta Riga ta Aure ba yadda za'a yi ace tana da saurayi kamar Sulaiman

We no dey carry last Ai yau kuma update a makare yazo Ku gafarce ni banda chargi ne

Comment

Share

©Hafciey Musa

[1/25, 5:44 AM] Hafciey Musa😘: *LAYLERH*

(The prettiest emerald)

masu tunanin Nima team Na Umar Farouq ne ya sauya lbrn kuyi hak'uri wallahi haka lbrn yake team Sulaiman ayi mini afuwa

Cikin tsananin bacin rai gami da tafasar zuciya Mommy Sulaiman ta dubi Yar uwar tata tace

"Amina don kawai baki son Sulaiman ya auri Yar Ki sai Kice uban su daya,me naci miki Mai Zafi haka? "Cikin girgiza Kai tace

"Yaya Hadeeza da gaske nake Zakari kurnari shine Baban Laylerh". Duk yan falon ido suka zuba musu Musamman Alhaji M wakili da kan shi ya daure,taya za'a ce Adda da kanwa suna kirarin sun auri miji daya dole akwai lauje cikin nadi ko cikin yaran akwai shege ko shegiya

" shekarun Laylerh nawa?"Mommy Sulaiman ta jefa Mata tambaya

"Ashirin tana Neman da daya".

" Masha Allah yanzu da Bari Na gidan Zakari shekara sha Tara ne kina nufin a baya nane ya Aure Ki Kika haifi Laylerh ko a waje aka samu cikin ta".da sauri Laylerh ta rintse idanun ta zuciyar ta Na bugawa da sauri sauri don tunda aka ce uban su daya da Sulaiman ta rasa me ke Mata dadi,addu'a take kada zancen pendon ta ya tabbata don zata iya haukacewa..

Fargaba gami da tsoro ne ya rufe Sulaiman kamar Laylerh bai son kunnen sa su jiye masa zancen da brain nasa ba zai iya dauka ba Na cewa mommy Sulaiman ba ita ce ta haife shi ba shiyasa cikin zafin nama ya mike tare da rike hannun Mom nashi yace

"Enough is enough Mom just because ina Neman auren Yar su hakan ba yana nufin Zan Bari a tozarta Ki ba tashi mu tafi". Ita ma ranta ya baci da zancen Yar uwar tata Amma tafi ganin kamar Yar uwar lafiya bai ishe ta ba shiyasa ta Fara kokarin mikewa

" Dani dake duk Mun San Sulaiman ba Dan Ki bane,saboda Na Riga Ki Aure ba yadda za'a yi ace kin haifi saurayi kamar Sulaiman shin ina taki jaririyar da Kika Haifa".cak ta tsaya kafafun ta suka gagara daukar ta dole ta fadi kasa cikin Tashin hankali, shi kuma Sulaiman kamar kububuwa ya fice duk don kada kunnen sa su jiye masa wannan batun...

Amintaccen Dan gidan Alhaji M wakili ne ya rufa mishi baya daidai lokacin da yake kokarin shiga mota

"Gaskiya ce kake gudu ko kuma zallar taurin Kai ne,Wa Ka fi a cikin mu?Ka dai San ko bamu muka haife Ka ba muna da kamar Ka ko wadanda suka fika". Idanun shi sun rufe bai San me yake yi ba shiyasa yace

" Kai kuma a Wa da zaka fadi mini abunda ya dace,stay out of this".ganin Yaron akwai rashin kunya sai ya dubi securities da suka zo da su guda biyu da suke gate yace

"In ya kuskura ya fita Ku banbance mishi between blue and black". Ido ya daga ya kalli securities din sanin shi girman falo ne ba wani karfi ne da shi ba sai yace" kaci darajar mahaifiya ta Na ciki if not ba Zan shiga ba".

A can falon kuma duk suna sauraron yadda suke musayar yawu shiyasa falon yayi shiru can sai gasu sun shigo a tare kowa ya nemi wajen zama..

"Amina ina jin Ki". Mommy Sulaiman ta fada..

" Nida Mommy Sulaiman yaya da kanwa ce"ta fadi tana duban Laylerh da Sulaiman nan taci gaba

"Yaya Hadeeza daga ranar da Na auri malam Musa Wanda yake saurayin Ki har kun tsaida ranar kawo kaya sai zuciya ya debe Ki Kika bar gida zuwa gidan kawun Ki..a lokacin ni kuma muna Maiduguri da malam Musa..

A can gidan kawun naki Allah ya hadaki da Zakari Wanda yake da Mata daya,duk da tsam Mai Mata baya tsarin Ki sai Kika gwammace kiyi auren huce takaici tunda Nima nayi wannan dalilin yasa kawun Ki aura miki Zakari ba tare da kin bawa mahaifin mu wannan hakkin Na aurar da ke ba..

A lokacin da Kika shiga gidan shi kin tarar uwar gidan shi ba lafiya sannan ga jariri hakan yasa Ki fahimtar don Ki taimaka Mata ya auro Ki,nan Kika dauke Yaron kina kula da shi da kuma mahaifiyar shi wacce bata da matsala ko kadan..

Dole aka yaye Sulaiman Tun bai Kai yaye ba don ciwon mahaifiyar shi ana haka ne kuma Allah ya dauki ran ta...sosai kike tausayin Sulaiman shiyasa Kika fi maida hankali akan shi fiye da mahaifin shi..

Shiru shiru kun shafe shekara biyar da Aure ko Bari baki taba ba hakan yasa dangin sa tilasta mishi Kara Aure,da yake shi din ma akwai son Aure Aure sai ya amince ya auro Ladidi..

Tun shigowar ta sai Kika zama banza a gidan don duk wani sarauta ya koma Gare ta Gashi kullum cikin miki gori ake don iyayen Ki da yan uwa ba Wanda ya taba zuwa wajen Ki..

Saukin Ki daya a gidan gwaggon Sulaiman, don rashin mutuncin kishiyar Ki shiyasa ko yan uwan Maman Sulaiman basu zuwa dubo sa..

Shigar ladidi da shekara sai ga ciki ya bayyana a Gare ta tsam baki tada hankalin Ki ba don kina jin Sulaiman tamkar Dan ta Kika Haifa ga alkawarin da Kika yiwa kan ki Na zama uwar shi har karshen rayuwar ki, kin fi maida hankali kan sama mishi magani idon shi ya budu..

Ladidi ta haifi Yar ta mace tana yaye ta kuma ta sake samun ciki a lokacin ke da Mai aiki Baku da maraba saboda ko ranar girkin Ki ne a dakin ta Zakari ke kwana.. Bauta kina sha don Ladidi sai taga dama take girki ga agolan da tazo da ita bata da kunya ko kadan..

Allah maji rokon bawan sa a lokacin da Ladidi ke da ciki Kika fahimci shigar ciki jikin Ki har Na Wata hudu Wanda hakan ba karamin tada hankalin Ladidi yayi ba har take tambayar Ki inda Kika samu ciki tunda miji ba kwana yake a dakin Ki ba da kyar dai ta hakura tunda tasan cikin nashi ne..

Saboda yadda Kika bar gida baki taba waiwayar su ba sai dai kina kiran Innar Ki a waya wacce ita ma bata San a wani gari kike ba saboda kin Ki fada Mata sai dai ta kan tura miki kudi in Kika Kai kukan Ki Gare ta ba tare da mahaifin mu ya sani ba..

Wata Rana ina zaune da malam Musa aka sanar da ni haihuwar Ki cewa kin haifi ya mace..duk wannan bayanan ina samu ne a bakin Wata makobciyar Ku wacce ta kasance Kawa ta..

"Malam Hadeeza Allah ya sauke ta lafiya ta haifi ya mace".

" Masha Allah Alhamdulillah ita ma yau Allah ya azurta ta".cike da farin ciki nace

"Wallahi Ai ta Kai kusan shekara bakwai da Aure fa". Saboda yadda yaga ina farin ciki yasa yace Mai zai Hana naje gida ganin Ki nan nace ba zaki taba yafe mini ba..a nan ya Riga mini wa'azi da nuna mini illar rike abu a zuciya sai Na fahimtar da shi kece Kika dauki abun da Zafi nan yace tunda shine silar Na shirya jibi zamu gida Bauchi..

Sosai nayi murna lokacin Muhammad Nada shekara uku..

Kamar yadda ya fada haka muka nufi gida sosai Inna ta tayi murnar gani Na haka ma innar Ki duk da tana danne damuwar ta..a ranar muka basu hak'uri da kuma cewa gobe in sha Allah zamu je miki Barka mu kuma nemi yafiyar Ki don ranar suna mu nuna musu kina da Gata..

A can gidan kuma duk da haihuwa Kika yi ba Wanda yake kan Ki sai gwaggon Sulaiman inda ita ke kula da shi yanzu kasancewar shi makaho tunda kin haihu sannan take yiwa jaririya wanka Ladidi dai wahala take jiyar da ke..

Da taimakon Kawa ta muka nufi gidan Ki lokacin malam Musa ya saya mota,gidan ta da naki ba nisa sosai shiyasa muka Fara biyawa muka dauke ta don ta nuna mana gidan sai dai Mun kusa Isa kofar gidan muka ga Ladidi ta fito rungume da jaririya Gashi duk a birki ce take hankalin ta a matukar tashe shiyasa muka yi tunanin yarinyar ba lafiya nan ta shiga taxi suka tada motar..

Cikin Zubda hawaye nace jaririyar ba lafiya don Allah mu bisu kila yaya Hadeeza ma Na cikin motar asibiti zasu..

Da wannan tunanin muka Fara bin bayar motar sai dai me fitar gari motar ta nufa kamar zamu juya nace sai dai muje..

Can wani kauye me taxi d'in yayi parking a lokacin ne kuma muka fahimci mutum biyu ne kadai a motar..

Ladidi rungume da jaririya ta fito nan ne muka Fara bin ta ba tare da ta San muna biye da ita ba..

Karamar kasuwar kauyen ta nufa cike da taka tsantsan kamar Mai Irga wani abu,daidai wani gida Mai dakin bukka anyi ginin da Jan block an kuma penta gidan kofar gidan cike da yashin kogi kallo daya zaka yiwa gidan Ka tabbatar ta amarya ce..

Zuwa yanzu Mun fahimci hallaka jaririyar ake son yi shiyasa suna barin kofar gidan muka karasa da gudu nan ne malam Musa yace Na tsaya su kuma Bari su bi Bayan Ladidi..

Daukar jaririyar nayi gami da rungume ta su kuma suka bi ta..

"Kin tabbatar yan kauyen ba zasu kaita police station ba".Mai taxi ya tambaya

" Na fa San me nake yi,Ai Boka Na ya fada mini taku nawa zanyi sannan ya kwatanta mini gidan,Na San gidan amarya ce nan kuma dole ta rike ta kasan kauye da tausayi sannan wannan yarinyar da kake gani cikin wahala Mara misaltuwa zata tashi don ban bar ta banza ba,duk wani farin ciki ba zata taba haduwa da shi ba".tana gama fadin haka suka tafi nan su malam Musa suka dawo Gare ni tare da fada mini abunda ya faru

"In sha Allah Zan maidawa yaya Hadeeza Yar ta wannan ita ce halaccin da Zan Mata".

" Amina ba za'a yi haka ba,ba kiji me tace game da yarinyar ba kila in an maida ta kashe ta zata yi".Cewar malam Musa,share hawaye nayi ina fadin

"To ya kake son nayi da wannan jaririyar gaskiya ba Zan bar ta a nan ba sannan wani Tashin hankali kake tunanin yaya Hadeeza zata shiga".

" zaki zame Mata uwa ni kuma Zan zame Mata uba".sosai naji dadi nan muka dauke ta muka dawo cikin gari Kai tsaye gidan Kawa ta muka nufa tare da ajiye ta sannan muka bar Mata jaririyar tunda a gida an San banda 'ya..

Koda muka koma gida sai muka ce ba muje wajen Ki ba sakamakon layin kawata da baya shiga an kuma yarda da mu saboda in munce Munje yaya Hadeeza zata iya tunanin ko mune muka sace Yar ta ..

Kawata ta Kira ni ta sanar da ni cewa lokacin da Ladidi ta dauke jaririyar kina bacci don ansa miki maganin bacci Sulaiman ko sun fita da gwaggon shi lokacin da Kika farka ba yarinya hauka ne kadai baki yi ba sai hak'uri ake baki..

A ranar Zakari ya miki duka don cewa yayi kin batar mishi da 'ya ya kuma tsine miki in har Kika fita ba tare da izinin shi ba,tsinuwa ya Riga jera miki dole Kika zauna gwara da cewa yayi in kin fita a bakin auren Ki ne,to Amma cewa yayi Allah tsine miki..

Mu kuma a Washe gari muka juya Maiduguri don munce Ana Neman malam Musa..

Daga nan muka yi yadda addini da al'ada ya tanadar Na sa Mata suna Laylerh.. Ban taba barin ta taji a jikin ta cewa bani ce Na haife ta ba..

A haka Kika rungumi Sulaiman kuka cigaba da rayuwa saboda Ladidi ta cire hankalin Ki akan Yar Ki da Kika tabbatar kashe ta tayi,har Bayan wasu lokuta..

A hankali kuma Kika Fara dawa hayyacin Ki nan Kika ce Ladidi ce ta kashe miki 'ya Zakari ko duka ya miki tare da sake Ki,kin so tafiya Ki bar Sulaiman tunda gidan uban shine sai dai makahon sai kuka yake don kece ya sani matsayin uwa nan gwaggon shi Tasa baki da kuma tunatar dake amanar da uwar shi ta bar miki..

Zakari ya bashi zabi tsakanin ke da shi nan ya zabe Ki sai Kika dauke shi kuka tafi tare..

Ana haka Allah yayiwa innar Ki rasuwa dole muka zo da Laylerh Bayan an gama zama ne muka sanar dasu Bappa abunda ya faru sun kuma yi alkawarin ba Wanda zai ji..

Bappa yaso share Ki sai ya kasa saboda yadda muka ce kike wahala nan ya nufi gidan Ki sai ce mishi aka yi kun rabu kin shiga duniya ba kuma Wanda ya sake ji daga Gare Ki..

Cigaba da rike Laylerh muka yi tare da bata sunan malam Musa duk da Mun San haka ba kyau sai dai jin kin shiga duniya Na tabbatar da ba ita ba gidan uban ta kuma bamu so ta San cewa bamu muka haife ta ba...

Kamar yadda Ladidi ta fadi hakan ce ta kasance Laylerh kullum cikin jarabawar rayuwa take shiyasa Bayan Mun sake haduwa da aka tsaida batun auren ta da Umar Farouq sannan aka ce da Wata daban yasa nace wahalar ta Isa haka dole Na nemo Ki don zaki iya saya Mata shiyasa naje Bauchi a gidan kawata Na kwana muka yi kuka Mai Isar mu Na tausayin Laylerh sai kuma Na nufi gidan Baban ta duk da Na San baki nan sai nace da Ladidi wajen Ki nazo koda tace baki nan sai nace ina son ganin Zakari ta hanani..

So nake Na sanar da shi batun Yar shi da kuke tunanin ta mutu tana Raye don ban San wane ne gawan fari ba..

Sannan Sulaiman ma Ladidi ce ta cire hankalin shi a gidan shiyasa baya zuwa".ta kare zancen tana Mai tsananin tausayawa Sulaiman da Laylerh... Shiru falon yayi kamar ruwa ya cinye su sai Laylerh dake kuka kasa kasa

"Tsam ban shiga duniya ba sai dai ina jin zafin Bappa Na aura miki malam Musa da yayi shiyasa ko da aka sake ni kauyen su Inna ta Na nufa da Sulaiman.ina can Allah ya Mata ratusuwa nan naji ba abunda Zan dawo nayi a gida dama akwai dukiyar ta

a can Wanda ko Bappa bai San da shi ba nan naci gadon gona biyu da kuma lambu sai gida daya..

Bayan Na sayar dukka sai Na samu miliyan biyu nan ne Na dauko Sulaiman muka dawo cikin gari Na Kama mana gidan haya daga baya kuma Na Fara business..

A hankali abu ya Fara tafiya sai Na Fara sarin kaya ina kuma nemawa Sulaiman magani da Allah yasawa abun albarka sai Na Fara zuwa wasu gari sari inda Na bude Babban shago sai ya zama kaya Na sari ake..daga baya har kasashen waje nake zuwa har can kuma ina nema mishi magani..da farko da company'n pure water Na Fara har abu ya zauna..

Duk da nasan Na taba haifar ya mace sai dai Na Bari a mutuwa tayi shiyasa ban maida Sulaiman ga yan uwan Maman shi ba ina fargabar kada su raba ni da shi shiyasa da kudi ya zauna mini Na bar garin..

Da taimakon wani malami Wanda muka shiga mota daya idon Sulaiman ya budu daga nan ban barshi yaji a jikin shi cewa ba nice Na haife shi ba".ta kare zancen cike da rauni don bata San ya Sulaiman din zai ji ba sai kuma ta juya ga Laylerh tausayin yaran duk suke ji...

Sulaiman ko kan shi da brain nashi sun Gaza yarda ji yake kamar mafarki ne ba gaskiya ba sai dai abu daya da ya tabbatar shine yana jin son Laylerh har cikin jinin shi sai dai bai taba jin feeling nata ba shi a ganin shi kila don bai Saba zama da Mata bane sai yanzu ya fahimci saboda ita kanwar shi ne..

Gyaran murya Alhaji M wakili yayi sannan yace"Alhamdulillah sai mu Kara godewa Allah, ni da farko ban so zama naji ba saboda mu ba family members bane Amma jin maganar sai nayi tunanin ko bata da uba shiyasa Na zauna,Mun makara zamu koma masaukin mu gobe da safe in sha Allah zamu koma saboda Fara shirye-shiryen biki..kowa jikin shi a mace Aunty Hauwa kam bata Ki a daura a wajen su tafi da Laylerh ba don su gwada Mata zallar kauna da soyayya, ta kuma godewa Allah da bata kasance yadikko irin Ladidi ba nan suka tafi...

Baaba ko da Auta falon juya musu yake malam ko yayi farin ciki sosai da hakan,mikewa mommy Sulaiman tayi tace

"Malam mu zamu wuce gida Na a can zamu kwana magrib ta kawo Kai".ya sani suna da bukatar kasantuwa tare shiyasa bai Hana su ba,hannun Sulaiman da ta tabbatar ba zai iya tashi ba ta kama nan suka nufi mota Aunty Na rike da hannun Laylerh mommy Sulaiman ce tayi driving...

Suna fita Baaba ta fashe da kuka Wanda ita kan ta bata San Na menene ba haka ma Auta sai dai ita Auta cikin kuka take fad'in

"Shikenan mu gidan mu sai dai yaran masu kudi su zo su zauna a karshe mu tashi a tutar babu Ashe Laylerh ma Yar Gata ce". Malam dai baki ya tabe yana tura akwatunan Bayan kujerun falon sannan ya nufi masallaci..

Tana parking Sulaiman ya wuce dakin shi da ido ta bishi tana jin yadda ya rufo kofa tasan dole zai ji Zafi..

Ciki suka shige yan aikin ta sai gaishe ta suke direct bedroom suka wuce abinci aka kawo musu sai dai ba Wanda yake jin zai iya ci sai Laylerh ce ta mirgina ta kwanta kan tattausan bed din mahaifiyar ta ji take kamar ba a kanta ake magana ba Wata Laylerh ce can daban,taya za'a ce Aunty da Abbu basu suka haife ta ba sannan Muhammad ba ciki daya suka fita ba,bangaren daya kuma Sulaiman da Tun tana primary suke tare Amma bata taba ji a jikin ta cewa Dan uwan ta bane duk da in tana tare da shi ta kan ji she is safe..duk da ido suke kallon ta Bayan Aunty ta sake Neman gafarar mommy Sulaiman a Karo da ba adadi sai mommy Sulaiman tace

" Dan Allah mu manta da baya Ki dauka kamar ba abunda ya faru,ni Tun bayar rasuwar Bappa sai naji ban son kowa don ke kam ban taba Neman Ki ba a karshe naji rasuwar innar Ki,to duk sun mutu me kuma zai Kai ni gida gobe ma Zan sa aje a dauko mini Muhammad mu rayu cikin salama".daga nan hirar yarinta suka Kama a karshe Aunty tace

"Shin ya kike ganin batun auren Laylerh da Umar Farouq tunda su biyu ne".

" gaskiya upon all wahalar da ta sha a rayuwa ba Zan Bari ta kare cikin kunci ba,in har Na tabbatar su biyu zai aura Zan San abun yi".

"Ya kamata kam".duk hirar da suke tana jin su a karshe dai suka kwanta...

A bangaren Sulaiman ko sai safa da marwa yake so yake ya farga daga mummunan mafarkin da yake sai dai kuma ya fahimci kamar ba mafarki bane,zama yayi a bakin gadon yana fashewa da kuka Mai ban tausayi da haka bacci ya sace shi...

**

Cikin gidam malam kamar mutuwa aka musu shiru yayi sai shi da ya fice zuwa kasuwa don ko a jikin shi..sallama aka yi a kofar falon Bayan an amsa ne Dada,Ummi da Nabeela suka shigo ciki..

Kokarin danne rai Baaba ke yi nan suka gaisa a mutunce sannan suka ce sunzo kallon kaya ne don Laylerh ta sanar da Nabeela jiya kan su shiga wani yanayi..

Auta ce ta Fara Jan akwatunan ganin bata yi da jiki sai Ummi ta mike tana fadin

"Kinga in baki yi bani waje nan ta janyo akwatunan suka Fara kallo

" wannan super wax ba bai kyau bane zai yi zuba ".abunka da Mai baki ta fadi lokacin da ta daga atampar sai Dada ce ta kalli atampar tace

" wannan kam Mai kyau ne".a haka suka cigaba da kallon kaya Nabeela sai dadi take ji a karshe jin shiru sai Dada ta tambayi Laylerh nan kuma aka sanar da ita gaskiya sai Ummi tace su tashi suje gidan

"A'a basu tare da nitsuwar su bai kamata kuje ba".

" ya haka ko dai bakin ciki kike yi ne,to wallahi sai Munje ".Cewar Ummi kenan tana mikewa sai kuma ta daura da fadin

" Ai Tun Randa Na kaita tayiwa mahaifiyar tata kitso Na fahimci jini daya ne don kamar asiri ne ya fita a jikin ita Hajiyar sai dai Na rike abu Na a ciki Na ban fada bane kawai".ta idda maganar tana fita waje Nabeela ko akwatin take rufewa nan suka fice..

Ummi uwar karambani da kakkamba Ai ko keke ta tare musu tare da fadin anguwar a haka suka nufa..har ila yau dai wannan Mai gadin da tayi fada da shi zuwar su da Laylerh ne koda ya ganta murmushi kawai yayi ya bude Mata don ya San ta da masifa..

A falo suka zube suna jiran fitowar yan gidan,Laylerh ce ta Fara fitowa tana ganin Dada da gudu ta fada jikin ta Allah ya sani tayi kewar Dada sosai Musamman yadda suke kwana bisa katifa daya..murmushi Dada tayi zuciyar ta Na raunana tuna Naseer da ya bata Laylerh sai Gashi yau Bayan ba ran shi ta hadu da iyayen ta

"Allah ya jikan Ka". Ta fadi a zuciyar ta Laylerh Na sake ta Ummi Harda bude hannu sai taga jikin Nabeela ta fada cikin rashin iya danne bacin ranta da son nunawa Laylerh Ai ita ma ta Santa tace

" Wato ni kuma ba mutum bace ko".sake Nabeela tayi nan ta nufi Ummi daga karshe suka gaisa sai suka ce ta Kira musu mahaifiyar ta..

A take suka fito jin Dada ce tazo sosai suka hadu suka Mata godiya Ummi ko sai son cusa kanta take don ita ma a gode Mata..sun jima sosai duk da Laylerh bata yanayin jin dadi Amma tayi farin cikin zuwan su,koda suka tashi tafiye kudi masu yawa Mommy Sulaiman ta bawa Dada tace taja jari kasa ta zube tana godiya sai cewa suka yi Ai sune da godiya..

Ummi ma an bata da yake ba Mai raina abu bace sai taji dadi sosai..

Nabeela ce dai aka barta da Laylerh don tace ita zata Mata kyauta ta Musamman Wanda yafi abunda Mommy Sulaiman ta bawa su Dada ita Nabeela dai murmushi kawai tayi...

Bayan sun tafi ne kuma Mommy Sulaiman ta nufi bangaren shi kwance ta tarar da shi bisa gado"Na sani ni din Mai laifi ce a Gare Ka Sulaiman, Ka gafarta mini Na rashin fada maka bani ce Na haife Ka ba sannan ban hada Ka da dangin mahaifiyar Ka ba..Ka sani nayi hakan ne ba don komai ba sai don kaunar da nake maka da gudun a kwace mini Kai,kada kaji komai a ranka wallahi har gobe Kai d'a nane baka ga ita Laylerh ta Aunty'n ta take yi ba".juyawo yayi yana fuskantar ta tare da rike hannun ta dukka biyu yace "mom ban San da wani baki Zan miki godiya ba,ba abunda baki yi akai Na ba Wanda ko uwa ta iya abunda zata mini..Ki daina bani hak'uri har yanzu ina jin Ki a raina kuma ko kadan son Ki bai ragu ba,Na godewa Allah da yasa muka gane ba don haka ba da Mun aikata haram kuma jinjina ga Laylerh ba don Na hadu da ita ba a kan case nan har nayi insisting aka shiga court sannan daga baya Na fahimci Na Fara sonta har ya Kai mu ga batun aure da duk wannan bai faru ba da baki hadu da Yar uwar ki da kuma Yar ki Laylerh ba".

" to masu kanwa kaga tashi muje Kayi breakfast ".mikewa yayi suka fito falon don already an kawo mishi abincin..

**

Abuja

Su Aunty sun Isa lafiya kowa Na hutawa..

Sadiya ce zaune a falo ita daya sai system da ta ajiye kan center table da kuma popcorn da alama aiki take yi tana kuma ci..kunnen ta manne da Bluetooth Wanda tantama babu waya take tana kuma sauraron abunda ake fadi ne daga daya bangaren sai kuma cikin fusata tace

" a kullum in mutum ya baka aiki sai Kayi failing nashi tsam baka taba yin abun arziki ba,haka lokacin da nasa Ku kwace wayar Laylerh sanda aka bi diddgin wayar Wanda ba don ina da wayo ba da an Kama ni".shiru ta sake yi tana sauraron yadda yake bata hak'uri sai kuma tace

"Nace ban bukatar aikin Ka daga yanzu kada Ka sake Kira Na". Ta kare zancenTare da Dan Danna Bluetooth din alamar ta katse kiran,daga Kai tayi tana kallon gefen ta ila kuwa Umar Farouq ta gane tsaye ya rungume hannayen shi a kirji Wanda tantama bata yi yaji duk abunda tace!

Comment

Share

©Hafciey Musa

[1/25, 5:44 AM] Hafciey Musa😘: *□LAYLERH□*

(The prettiest emerald)

Sosai ta tsorata nan take jikin ta ya hau kyarma jira kawai take taji yace wani abu,sanin halin shi Na rashin magana da kuma jin Kai ya sata Fara fad'in

"Umar....". Sai kuma ta dakata bisa jin yana magana ga dukkan alamu kuma waya yake yi da can yayi shiru ne domin yana sauraron abunda ake fada daga daya bangaren, doguwar ajiyar zuciya ta sauke lokacin da taga ya juya ya bar falon ya nufi third floor hakan ya tabbatar Mata da cewa Aunty Hauwa yake nema..

Tattara abubuwan ta tayi ta koma ciki can kasan zuciyar ta tsarai ta San yaji Amma sai ya manna Mata hauka dole sai yi abunda bata taba tunani ba..

A can gidan Mommy Sulaiman kuma a Washe garin aka Mata confirming cewa Umar Farouq su biyu zai aura kuma dayan abokiyar aikin sa ne,zaune suke a falo har Sulaiman Laylerh ce kadai bata nan kuma taki fitowa ne saboda muryar Sulaiman da ta jiyo a falo,tsam ba zata iya ido hudu da shi ba ace yayan ta uban su daya don rashin sani suka fada soyayya..

" yaya Hadeeza yanzu me abun yi kenan?"

"Gaskiya ba Zan bari ta Aure shi ba,Zan tura ta abroad taje can tayi degree in ta tafi ina zasu ganta har ayi auren".

" gaskiya hakan yayi".duk zancen da suke yi Sulaiman Na jin su Amma bai ce komai ba saboda shima kunyar kanwar shi yake ji..

A ranar Muhammad yazo taraba murna sosai suka yi nan ne Laylerh ke fitowa su taba hira Amma da taji muryar Sulaiman zata koma ciki..

Kayan Aure kuma an bar shi a gidan su Baaba a Cewar su in Laylerh ta tafi sai a maida musu abun su..

Bayan kwana biyar!!

Sosai ahalin gidan Alhaji M wakili ke shiri Musamman yanzu da Aure ya saura kwana uku,sun canza duk wani furniture's Na gidan an sake painting gidan ya zama sabuwa dal..zuwa wannan ranar baki yan nesa duk sun zo yaran shi da suka yi Aure ma sun dawo gida har sai an gama biki..

Tuni Sadiya ta koma gidan ta inda tayi dilka tayi kyau ba zaka ce ita ce Mara lafiya a kwanaki da suka wuce ba don yadda ta cika tayi kyau ga kawayen ta cike a gidan..

Can gidan su Laylerh ko ba abunda aka Mata saboda mommy Sulaiman tashi tsaye tayi tana nema Mata makaranta inda nan da kwana biyu zata bar Nigeria..

Koda Alhaji M wakili ya Kira malam ya tambaye shi batun shirye-shiryen biki sai yace tana wajen mahaifiyar ta Ana Mata shiri Na Musamman duk da ya fahimci kamar ba zasu Bari ayi auren ba Amma kuma ba zai iya fadawa Alhaji M wakili din ba...

**

Rayuwa gaba daya ta juya mishi, Tun Bayan da ya take dukiyar su Laylerh ya bar Maiduguri zuwa jigawa a can ya Fara business kuma Alhamdulillah komai Na tafiya yadda yake so,arziki ya zauna mishi ta inda in Ana Neman masu rufin asiri sosai za'a sa shi,ya Kara Aure inda ya auro gogeggiyar Yar barki,yaran shi duk sun girma su Sadiya ma an Kai Aure a irin haka saboda rashin tsaro kidnapper's suka dauke shi,duka duka riban da ya samu cikin kasuwanci bai fi miliyan 10 ba sai access da ya saya saboda kudin ba Na halal bane ba yadda za'a yi yayi albarka.. Koda suka dauke shi sai suka nemi miliyan 20 Wanda dole yasa aka Riga sayar da abubuwan da ya Tara aka karbo shi..

Tun da ya fahimci reshe ta juya da mujiya sai ya shiga tsananin damuwa Wata Rana yana tsaye kawai sai ya fadi daga nan gefen shi daya ya shanye dama Tun lokacin da aka ce a kawo kudi ba dukka yaran shi suka bayar ba sun rage wani abu don ba yadda za'a yi ace su basu da komai cikin dukiyar uban su..

Daga wannan lokacin sai ya dawo musu liability tsam bai da amfani komai sai an mishi karshe amaryar ta bar mishi gidan shi da yaran ta..yaran uwar gidan kuma duk da kasancewar shi uban su tsam basu tausaya mishi shefene ma basu yi zuwa yanzu kuma abunda zai sa a cikin shi ma yafi karfin shi..ga shi ya zame musu jidali don a jikin sa yake fitsari da kashi dukka don ba halin magana bakin shi ya karkace kamar Wanda garsa ya buge..

Wannan kenan!

Tun safe Alhaji M wakili ya shirya cikin gezna Mai tsadar gaske sai baza kamshi yake,Aunty Hauwa ko ido ta zuba mishi tana tsaye a Bayan shi ganin yadda yake komai da kan shi sai kure adaka yake

"Alhaji wankan ya Isa haka mana".turare ya dauka yana fesawa yace

" ba zaki gane bane auren aboki Na fa zani kuma Mun Dade bamu hadu ba".murmushi tayi tare da sanya mishi hula nan ya Mata sallama ya kuma tabbatar Mata a ranar zai dawo tunda auren Umar Farouq saura kwana biyu dole yazo a

gama shirye-shirye da shi..private jet yayi booking zuwa Bauchi shi da amintaccen sa..

A can cikin gidan shi kuma baki sun gama cika duk da ba bidi'a za'a yi ba gida ya zama ba abunda ke tashi sai hayaniya a daura wannan a sauke wancan yara gasu ko ta ina..

A bangaren Umar Farouq ko tsam ba zaka yi tunanin shi za'a yiwa Aure ba don ba wani shiri da yake har ila yau kuma yaki daukar hutu a wajen aiki kullum yana zuwa sai su Bash ne ke shirya abunda ba'a rasa ba su kan je su zanta da kawayen Sadiya yayinda Laylerh ma Na cikin Abuja a gidan Mommy Sulaiman Amma ba Wanda ya sani..

Tun azahar ake kiran number'n Abba sai amintaccen shi ya daga yace yana cikin jama'a hakan ya Fara tada hankalin iyalan shi suka Fara tunanin ko ba lafiya ba...

Ana gama daurin Aure suka juyo zuwa Abuja tare da bako..

Already ya sanar da Aunty Hauwa cewa duk iyalan shi su jira shi a bangaren Umar Farouq sanin gidan akwai baki hakan ko aka yi..

Umar Farouq Na can cikin bedroom ya jiyo hayaniyar su a falo nan ya zura jallabiya ya fito..

Da addu'a aka bude taron nan Abba yayi gyaran murya sannan yace

"Dukkan godiya ta tabbata ga Allah ubangijin talikai na San duk zaku yi mamakin jin Na tafi daurin Aure har Bauchi ba tare da shiri ba Wanda ya taso mini a gaggawa sannan da Na tashi dawa kuma sai Na dawo tare da bako". Shiru suka yi suna sauraron shi yayinda Umar Farouq ko maida hankalin shi ga bakon kallo daya ya mishi ya gano akwai kamar jini tsakanin bakon da Laylerh

" to Alhamdulillah shi wannan bakon ba kowa bane face surkin Umar Farouq ".

" yau kuma Wata matar Abba ya sake samowa ya Umar kenan".Cewar Najiha nan Abba yaci gaba

" shi din mahaifi ne ga Laylerh kuma munyi university tare,a Daren shekaran jiya Na samu labarin cewa an gamawa Laylerh komai Na tafiya makaranta kuma gobe in sha Allah zata wuce abroad wannan dalilin yasa ni Neman mahaifin ta tunda shi ke da hakkin bada ita ba wani ba, tun a washe garin aka hada mini komai akan shi to Alhamdulillah koda naje Bauchi sai muka shaida juna duk da shekaru sun ja a nan ne Na sanar da shi bukata ta ba tare da bata lokaci ba kuma ya amince da batun auren har yace in ba laifi za'a iya daurawa..a halin yanzu Laylerh matar Umar Farouq ne saboda an daura musu Aure kamar yadda addini ya shardanta".da sauri Umar Farouq ya dago yana kallon Abba duk da yasan da batun daurin auren nasu jibi ne Amma Abba ya shammace shi,Shikenan shi kullum bai da freedom of life sai abunda Abban shi yayi,mikewa yayi ba tare da yace da su komai ba daga falon suka ji yadda ya rufo kofar dakin,Sosai Aunty Hauwa taji tausayin shi yanzu kuma jibi a sake lika mishi Sadiya gaskiya Abba baya mishi adalci..

Shi ko Zakari Wato mahaifin Laylerh lokacin da Alhaji M wakili yaje da batun nemawa Umar Farouq auren Laylerh yana ganin kudi sai duk ya rude nan matar shi ta Riga zuga shi kan ya amince saboda tasan in ba hakan aka yi ba ba zata samu shiga jikin Laylerh da mahaifiyar ta a Karo Na biyu ba wannan dalilin yasa shi amincewa ba tare da bata lokaci ba Bayan an idar da sallah azahar a masallacin dake kusa da su aka daura kuma dole ya biyo su saboda Alhaji M wakili ya San mommy Sulaiman da kafiya cewa zata yi bata San da batun ba Amma in taga uban Laylerh dole ta yarda da cewa an daura auren..

Jiki a sanyaye duk suka Fara mikewa kowa Na fita a bangaren Salman ko hotel da aka kamawa Baban Laylerh ya nufa da shi wanda yake jin kan shi kamar zai fashe tunda zai hada zuri'a da su..

A Washe garin kuma Abba ya dauke shi tare da Aunty Hauwa suka nufi gidan Mommy Sulaiman wacce ke shiri zata Kai Laylerh airport tana ganin Aunty Hauwa kuma sosai tayi mamaki

"Kaga uwar Ango ba Hajiya Hauwa Ashe kuna fita a irin kwanakin nan".

" to ya zamu yi".Aunty Hauwa ta fadi lokacin da take zama bisa kujera nan Aunty'n Laylerh ta fito cikin sakin fuska suka gaisa basu nuna Mata komai ba..

"Tare muke da Alhaji fa". Kallon kallo suka yiwa juna sannan Aunty tace

" bismillah su shigo mana".mikewa tayi nan tace su shigo Ai ko da Zakari ta Fara arba da sauri ta mike tana fadin

"Abban Sulaiman a gida Na". Aunty'n Laylerh ce tayi karfin halin ce musu su zauna Harda kawo musu ruwa ita dai mommy Sulaiman kicin-kicin tayi da fuskar ta don tsam bata da bukatar Kara ganin shi a rayuwar ta duk da kasancewar shi uba ga Yar ta,gaisuwa ta mutunci suka yi sannan Abba yayi gyaran murya

" da farko Zan Fara da baki hak'uri ".tunda taji wannan Kalmar ta hak'uri ta San fa dole an cuce ta ne shiyasa zuciyar ta ya Fara bugawa saboda ta sani Zakari ba zai taba yin abun arziki ba

" Na San abunda nayi bai dace ba Amma kuma da zuciya daya Na aikata hakan saboda ina yiwa Umar Farouq sha'awar auren Laylerh don Na fahimci yarinyar tana da tarbiya sannan kuma zai sata farin ciki, a shekaran jiya Na samu labarin kina shirin tura ta wata kasa karatu shiyasa Na tashi tsaye nan nasa aka binciko mini mahaifin ta inda a jiya naje Bauchi Na same sa a halin yanzu kuma an daura auren Laylerh da Umar Farouq sai dai muyi musu fatan alkhairi".

"Tsam ba zai taba yuwuwa ba in ina raye auren Laylerh da Umar Farouq mutumin da ba son ta yake yi ba,so nake Na inganta rayuwar 'ya ta sannan Na aurar da ita ga Wanda nake so..Kai kuma Zakari ko kunyar abunda Ka aikata baka ji ba,Na yarda Kai uban ta ne Amma daidai da Rana daya Ka taba sanin tana Raye ne ko ta mutu,shin a hannun Wa take baka San cin ta da shan ta ba koda nayi korafi akan batar ta sai Ka mini duka a karshe Ka sake ni sannan yanzu kace Ka aurar da ita wannen ne kuma ba Zan yarda ba Ka tauye mini hakki Na dayawa". Shiru falon yayi kamar ruwa ya cinye su sai Mommy Sulaiman da ke bala'e

" Kinga Hadeeza abunda ya faru ya Riga ya faru Aure kuma Allah ya kaddara matar sa ce,matsalar dake tsakanin mu kuma ina ga mu cire yara a cikin ta".Cewar mahaifin Laylerh

"Haka zaka ce ko to Zan nuna maka nafi Ka iko da ita Kai Ka daura Mata Aure Niko Zan Hana ta tarewa don makaranta Zan tura ta". Duk hak'uri suka shiga bata tsam taki karshe ma mikewa tayi ta nufi ciki Laylerh dake jiyo su kuma fashewa tayi da kuka Mai cin rai Shikenan kuma da wannan mahaukacin aka daura Mata Aure..

Aunty'n Laylerh ce ta basu hak'uri tare da musu alkawarin zata shawo kan ta tunda an Riga da an daura auren nan suka fice shiko Zakari sai cewa yake ko yau Umar Farouq ke da bukatar matar shi ya sanar mishi da kan shi zai Kai ta har dakin ta....

A can bangaren Umar Farouq kuma toilet ya shige inda ya sakarwa kan shi shower shiru yayi yana jin yadda ruwan ke zuba a kan shi,kallo daya zaka mishi Ka iya karanta damuwar dake shimfide a fuskar shi saboda nan da sati biyu zai tafi US wani aiki Gashi yanzu Abba yayi gaggawar daura mishi Aure da Laylerh.. Towel ya janyo inda ya daura a kugun shi sannan ya rike daya yana goge jikin sa da yake dauke da danshin ruwa a haka ya fito a gaban dressing mirror ya tsaya yana karewa halittar jikin sa kallo Wanda ya tabbata karyar Laylerh ta iya Daukan shi,shi dai an kawo mishi yarinya ya raina ne kawai..da wannan tunanin ya gama goge jikin shi inda yaja stool din ya zauna tare da Fara murza Mai a jikin shi yau komai cikin sanyi yake yi Wanda shi kan shi bai San dalilin hakan ba..Bayan ya gama sai ya gyara suman kanshi da ke cike kullum Ana kan gyara ta sai dai baya aski ya kan je saloon a rage mishi kadan,mikewa yayi ya nufi wardrobe Bayan ya zabi Kayan da zai sa nan ya shirya kan shi cikin farar jumper da ta matukar amshe shi ya fito Ango sak sai ya fece turare tare da duba takalmi,ajiyar zuciya ya sauke nan ya dauki waya da key'n mota ko da ya fito harabar gidan sosai yaga mutani sai ya fuske kawai Aunty Hauwa wacce ke dakon shi kuma da sauri ta nufe shi tana murmushi don a tunanin ta yana can cikin bakin ciki ne

"Masha Allah kaga angon Laylerh ba". Lumshe ido yayi ya kuma bude su a kanta inda ya rike hannun ta dukka biyu ya zuba Mata manyan idanun shi yana iya karanto farin cikin dake shimfide a fuskar ta game da wannan auren

" ina tayaka murna daga yau zaka Fara sabuwar rayuwa ubangijin Allah ya baka ikon rike musu 'ya tsakani da Allah da kuma zuri'a dayyiba".a saman labban shi ya amsa da Ameen saboda Mai faruwa ta Riga da ta faru,suna a haka Nana ta fito rike da d'an ta

"Congratulations ya Umar Dan Allah Ka tura aje a dauko ta tunda an daura" ta karishe zancen tana mika mishi Yaron ta da yaketa wasil wasil zai je wajen uncle nashi,jefa Yaron sama yayi ya cabke instead of Yaron ya tsorata sai Gashi ya Washe baki yana dariya sosai abun ke basu mamaki saboda ya Riga da ya cirewa Yaron tsoro, mika Wa Nana yayi sai ga Yaron ya fashe da kuka kan shi ya shafa sannan ya Fara tafiya

"Ayya dai ango baka ce komai ba". Nana ta fada kamar zata yi kuka ba tare da ya dagata daga tafiyar da yake ba kuma bai juya ba yace

" Ai bani Na daura ba Kije wajen Wanda ya daura Kice ya dauko ta".yana gama fadin haka ya bude motar shi ya shige yau da kan shi yake driving sannan shi daya ya fito direct gidan Bash ya wuce da yake shima Bash din tuzuru ne baida Mata..

A falon ya zauna yana sauke ajiyar zuciya Bash da yanzu fitowar shi daga bedroom ne yaja birki ya tsaya tare da zubawa Umar Farouq idanu

"Ya haka malam zaka shigo mini gida ba sallama ko ce maka aka yi gidan naka ne". Banza ya mishi nan Bash din ma ya fita harkar shi tare da cigaba da aikin da yake yi

" ya shirye-shiryen tafiya da kuma biki Na tabbata da guda daya zaka tafi".sai a yanzu ya dago kai yana fad'in

"Aure Ai an Riga da an daura kuma guda dayan ce ba wacce za'a sake lika mini".

" ban gane an daura ba Ince sai gobe".

"Tun jiya Abba ya daura mini da yarinyar can". Ihun dadi Bash yayi inda ya taso yayi hugging nashi yace

" Amma naji dadi da aka Fara daura maka da Laylerh gobe kuma za'a daura da Sadiya kenan".mikewa yayi ya nufi fita yana fad'in

"Har Abada ba za'a daura da Sadiya ba".

" Amma Umar Farouq.....".kan ya ida zancen tuni Umar Farouq din ya fice dama zuwa yayi don ya Dan rage abunda yake ji a zuciyar shi to kuma wannan Mai Dan banzan surutu ba zai bar shi ba kuma dama shi ba Mai abokanaye bane duba da irin aikin shi..

A bangaren Zakari Baban su Laylerh kuma komai aka kawo mishi ci yake tsakanin shi da Allah ba kunya bare tsoron Allah wani lokacin kam ma har ya Kira Ladidi yana fada Mata kalar dadin da yake ci ita ko Harda cewa Ai zata zo ita ce zata Kai Laylerh dakin mijin ta..

Bayan fitar su Alhaji M wakili sai Mommy Sulaiman ta fashe da kuka Shikenan kuma sun gama da rayuwar Yar ta gaskiya Zakari baya tsoron Allah

"Yaya Hadeeza kiyi hak'uri mu rungumi kaddara Umar Farouq nan dai shine mijin ta ba yadda muka iya,Nima da farko ban so auren ba shiyasa ma Na Fara Neman ki Amma Kinga Allah ya nuna mana ba dabara ko wayon mu ne zai sa a fasa auren ba sannan in kina kuka ita Laylerh ya zamu yi mu rarrashe ta". Tana rufe bakin ta Sulaiman ya shigo zama yayi ya kura musu ido yana jin zafin kukan da mommy'n shi ke yi,cikin kuka take fad'in

" Amina dole nayi kuka upon duk wahalar da ta sha yanzu kuma ace za'a hada ta kishi da wacce ta girme ta gaskiya ba Zan iya bashi ita ba".gyaran murya Sulaiman yayi sannan yace

"Duk wani bincike da yaya kan yi kafun a aurar da kanwar shi nayi Na kuma gano Umar Farouq din baida Wata matsala sai ta jin kan shi kamar yafi kowa sannan batun kishiyar ta in har ya kuskura ya daura Aure da Sadiya a gobe to wallahi haka zata tsallake auren nashi ta tafi kasar waje karatu ko Baba kuma ba abunda ya Isa ya yi tunda shi yace son duniya ya daurawa kan shi".

" Sulaiman Na sani tsam Sadiya bata da mutunci a binciken da nayi zata cutar da Laylerh ce kawai".Mommy Sulaiman ta fadi

"Kada Ki damu Allah kaimu gobe daura auren shi daidai yake da bawa Laylerh ticket Na tafiya abroad karatu kuma dole ya rubuta saki ya ajiye". Mikewa Aunty tayi ta nufi daki inda ta tarar da Laylerh sai kuka take da gudu ta fada jikin Aunty tana fad'in

" wallahi Aunty ni bana son shi kawai mutuncin shi nake gani kuma ni ba Zan iya zaman Aure da shi ba yafi karfi Na".sosai maganar Laylerh ta bata dariya saboda takaicin auren ya sata fadin haka duk da cewa kuma har yau har gobe bata boyewa Aunty komai saboda haka ta Mata tarbiya shiyasa a kullum take fada Mata duk abunda yake ran ta..petting Bayan ta tayi tace

"Ke baki ji dadi ba ma kin samu miji Na nunawa duniya kuma Allah yana son Ki jin Kai ne kawai yasa yake batsarwa".

" ni koma yaya ne bana so".,

"A'a tunda an Riga da an daura hak'uri zaki yi Ki daina tadawa Mommy'n Ku hankali har kuka fa take yi akan Ki kuma kin San ba kyau".

" to Shikenan Aunty Na daina".ta fada tana share hawayen ta da kyar ta lallaba ta taci abinci..

Bangaren Sadiya ko da wasa bata ji labarin auren ba sai ma shirye-shiryen da take Na daurin Aure gobe sosai gidan ta ya cika makil da mutani gobe kawai take jira ta mallake Umar Farouq..

A Washe garin mutani suka cika makil a masallacin da za'a yi daurin auren bisa gayyatar su da aka yi..

A can cikin gidan kuwa hoyo-hoyo ta ko ina sai dafa abinci ake Ana saukewa uwar Ango taci adon ta cikin wani lace Mai tsada ta zuba sarkoki masu tsada duk inda ta wuce sai an bita da ido Gashi ta rasa zama don hidima haka shima Abba gaba daya baida natsuwa zaka ce shine angon..

Bangaren Umar Farouq ko ya Kai minti arba'in a toilet inda Bash ke zaune a bedroom din ya fito mishi da Kayan shi white jumper da ya sha aikin wuta ga wrist watch Na shi da hula sai kuma takalmi da turare duk ya ajiye mishi a kan gadon

"Umar Farouq sai kace mace wacce za'a yiwa auren dole kaga Ka fito Abba ya Fara kiraye-kirayen waya". Bude kofar toilet din yayi ya fito daure da towel a jikin sa kare masa kallo Bash ke yi don bai taba ganin sa a haka ba sai yau

" Anya wannan karamar zata iya maka kuwa".tsaki yaja gami da manna mishi hauka nan ya Fara shiri a tsanake har ya gama nan ya fito ango Tun yana daura agogon a tsintsiyar hannun shi Bash ke kashe shi da Hoto nan suka jero motoci hudu suka mishi rakiya zuwa wajen daurin auren inda Sulaiman ma ya kasance cikin ayarin shaida daurin auren..

A can bangaren Sadiya ma taci kyau an Mata make up ga Jan lallen ta sosai yayi kyau jira kawai take taji an daura..

Laylerh ko baccin ta take yi sai dai haka kawai zuciyar ta ke tsinkewa tana kuma fargabar kada ya daura wani auren ta zama karamar bazawara...

Kowa ya halarci bikin inda Ango kadai ake jira a daidai lokacin da suka iso an Fara gaishe-gaishe sai kawai wasu yan ta'adda suka zo cikin mota uku duk sauka suka yi kallo daya zaka musu Ka fahimci yan kwaya ne

"Kowa ya wase ba auren da za'a daura don ba haka muka yi da Sadiya ba".

" Haba samari Dan Allah kuyi hak'uri bamu Neman Tashin hankali da kowa yanzu za'a daura auren nan a gama".Cewar amintaccen Abba

"Tsoho wallahi ko Ku watse ko muyi muku jina jina". Tsam yaki Bari su karasa cikin masallacin bare su Abba da shi Umar Farouq din su San me ke faruwa su dai sai cewa suke Sadiya ta yaudare su ba haka suka yi da ita ba ganin fa ya Kira musu securities Na Abba da kuma na Umar Farouq sai kawai suka Fara fesa musu tiyagas nan take kowa ya Fara Neman inda zai sa kan shi sai ihu ake da kyar aka kare Umar Farouq da Abba aka nufi gida da su..

Tun a hanya Abba ke trying number'n Sadiya baya shiga shiyasa direct gidan ta suka nufa yan Aure kawai suka tarar nan ne suke shaida mishi Sadiya ta fita hankali a tashe ta gudu da yar ta hakan ya tabbatar mishi Sadiya Na boye wani abu don haka suka nufi gida cike da Tashin hankali..

Koda ya Isa gida jama'a Na cike shiyasa ya wuce bangaren Umar Farouq din Baban Laylerh kuma Na bin shi a baya kamar jela..

Yana shiga yaja birki ya tsaya saboda ganin Sadiya zaune a dakin kan ta a kasa,bakin shi Na rawa yace

" Umar Farouq a ina Ka samo ta".

"Abba wannan ba Sadiya bace Sumayya ce". Kallon Sadiya ya kuma yi sannan ya kalli Umar Farouq irin kallon Rainin wayon nan yace

" ya zaka ce mini ba Sadiya bace ko dai idon Ka ya samu matsala ne".Bash ne ya zaunar da Abba sannan ya nunawa Baban Laylerh wajen zama da kuma Amintaccen M wakili din nan shi ma ya zauna

"Abba lokacin da muka fita zamu je wajen daurin Aure munyi nisa a tafiya sanda muka zo hanyar da ba mutani sai wasu suka kawo mana attack,duk yadda securities suka so Kama su abun yaci tura nan ne suka shake Umar Farouq suna fadin su dai sai sun kashe shi saboda abunda aka turo su suyi kenan,da yake ya San aikin kudi suke yi sai ya tambaya nawa aka basu nan ne suka fada sai ya ninka musu kudin biyu don yana son sanin Wanda ya turo su..

Daga nan ne securities suka yi nasarar Kama su dukka sai muka nufi gidan Ka da su aka Fara jona musu shocking Ana tambayar su wane ne ya turo su a nan ne suka ce wani Babban politician ne Wanda ba irin harkar da baya yi Kama daga safarar mutani,kwaya yankan Kai da dai sauran su..a iya bincike an bincika an kuma tabbatar da Umar Farouq ke aiki a Kan shi yana kuma hada evidence da zai gabatar ga federal government Na Nigeria Wanda a halin yanzu yayi nisa sosai kuma dama shi da Abokin aikin shi Hashim suke yi, lokacin da suka farga sai suka sa aka kashe shi Hashim din tare da daurawa Umar Farouq kisan.. time da aka ajiye shi a underground building nan ma an so kashe shi sai kuma ya sira inda ya dugu taraba..

Ganin in aka kashe shi gaba da gaba za'a iya samo evidence din sannan dole za'a fahimci wane ne ya kashe shi sai suka canza salo inda aka nemo Na kusa da shi..ba kowa aka nemo ba face Sadiya ".Bash Na kaiwa nan yaja dogon ajiyar zuciya yana kallon Abba sannan ya cigaba

" lokacin da aka yiwa Sadiya tayin aikin da wuri ta Karba don tana da bukatar mukamin shi wannan dalilin yasa ta Fara shige mishi har aka sa muka Kai Mata attack duk don ta koma gidan su,Sadiya first plan nata ya tafi yadda ake so sai kuma tayi moving zuwa plan nata Na gaba inda a nan ne ta Fara ciwon karya duk don ya tausaya Mata su sami kusanci sosai ta Yadda zata yi poising nashi ko kuma ta dauke shi ta Kai shi wani wajen sai a kashe shi ba tare da ta bar prove ba sai dai tsam yaki bata fuska don bai taba yarda da ita ba a irin haka ne kuma ta kamu da son shi so na asali ba tare da ta shirya ba har take jin zata Aure shi

.koda kace ya Aure ta sosai taji dadi sai ta manta da mutanin can da kuma kudaden da suka bata har a yau ake daurin Aure aka farga shine aka turo su su kashe shi kawai,to nan ne yace suje wajen taron su wargaza mutani ".duk salati suka Fara tare da jinjina lamarin sai Abba yace

" ita kuma wannan fa".dogon ajiyar zuciya Umar Farouq ya sauke sannan yace

"Sunan ta Sumayya Mahmud Ardo Yar uwa ce ga Sadiya uwar su daya uban su daya in fact yan biyu ne wadanda suka kasance identical twins sai Ka Lura da kyau zaka ga banbanci inda Sadiya ta fita wayewa da kuma haske".ya kare zancen yana kallon ta sai dai har yanzu Abba bai gamsu ba Sadiya bace

" ni ba Sadiya bace kuma Na San ko Zan kwana fada ba yarda zaku yi ba Amma Bari Na Kira ta a waya don bata San an Kama ni ba".dialing number'n Sadiya ta Fara tana dagawa tace

"Hello Halima ina kike ne?"

"Sumayya kiyi maza Ki bar Abuja saboda Ana nema Na kuma Na gudu da beta in an Gan Ki Kama Ki za'a yi saboda a tunanin su ni ce ko kuma Ki koma yawo da nikab". Tana gama fadin haka ta katse kirar sun kuma gamsu saboda muryar Sadiya suka ji..

" da ni da Sadiya yan biyu ne sai dai Tun Tashin mu ta fini son duniya da kuma wayewa,daga lokacin da ta zama budurwa ta Fara iskanci hankalin ta kwance sai dai duk iya shegen ta a gida take kwana don tana tsoron Baban mu a irin haka ne Allah ya mishi rasuwa daga nan sai ta bar gida don ta fahimci mahaifiyar mu ba yadda ta iya da ita..da farko ta kan je wajen yan uwan mu masu kudi a irin Abuja Kaduna da dai sauran garuruwa sai tayi ta iya shege In taga sun dago ta sai ta canza wani gidan sai dai ta kan zo gida..

A hankali ta Fara harka da manyan mutani Kama daga ministers da kuma governor's saboda Allah ya Mata kyau,sosai ta Fara Tara kudi sai ta cigaba da degree din ta har ta gama a nan ne kuma ta hadu da wani minister ya nema Mata aiki da NIA sai daga baya kuma ya Aure ta sai dai bai son nunawa duniya karuwa ya aura sannan iyayen matan shi ne suka nema mishi mukami da yake Kai duk Randa suka fahimci yaci amanar matar shi sauke shi za'a yi shiyasa ya ajiye ta a hotel tana kuma zuwa wajen aikin ta..

A hankali har ta samu cikin beta lokacin ne kuma aka farga da yayi Aure gudun abunda zai je ya dawo sai ya sake ta daga nan ta cigaba da aikin ta da kuma rainon cikin ta har Allah ya sauke ta lafiya taje gida inda ta gyara mana gida tare da Alkhairi dayawa don tunda ta haihu ta daina iskanci..

Kwanaki ta Kira ni inda take sanar da ni anyi kisan Kai a wani company sannan ba yarinyar bace tayi sharri ne kawai accountant din ne yayi don Allah Na taimake yarinyar Zan samu lada nace ta yaya,nan ne ta fada mini yadda Zan yi har muka Fara haduwa da Sulaiman Wanda lokuta da dama yana tambaya Na ina Na samu influence saboda sunyi degree da Sadiya kuma ganin mutumiyar kirki yake Mata,ganin kamar ba zai yarda ba sai tace Na taimaki marainiya Na sa mishi son ta a zuciyar shi ni ban kawo komai rai Na ba haka ko aka yi..akwai ranar da muka hadu da ita a kofan gidan oga'n ta inda shi Umar Farouq din yasa anbi Bayan ta nan ne Na shiga taxi Na tafi haka Wanda ke bin mu ma sai dai koda Umar Farouq din ya koma gida sai yaga Sadiya nan ya Kira a waya sai Wanda yasa aiki yace Gashi tare da ni Amma tsam bai yarda ba don bai San mu biyu bane ba mutum daya ba..haka ranar da Na Kira ta a gaban Ku Tasa wayar a hands free tsam ban taba tunanin amfani take da ni ba sai a yau da Umar Farouq ya tsince ni a titi lokacin da suke dawa daga daurin Aure kallo daya kuma ya mini ya tabbatar ba Sadiya bace in ba don shi ba nasan DQ yanzu an kamani kuma so nake Na koma gida don mahaifiyar mu ita daya Na bari".tana kaiwa nan falon yayi shiru kamar ruwa ya cinye su sai dai sunyi farin ciki sosai da Umar Farouq bai Aure ta ba nan dai Abba ya Kira Aunty Hauwa ta shiga da ita ciki wajen biki da kyar ita ma ta yarda ba Sadiya bane haka ma kannen shi nan dai aka cigaba da shagalin biki..

Sanda ta huta sannan aka hada ta da securities suka Kai ta Tasha ta nufi garin su..

Comment

Share

©Hafciey Musa[1/25, 5:44 AM] Hafciey Musa😘: *□LAYLERH□*

(The prettiest emerald)

Cike da farin ciki ya shigo gida fuskar shi dauke da murmushi direct main falon su ya shiga inda a can ya tarar da Mommy Sulaiman tayi jugum duk ta koma kalar tausayi jira kawai take ace Mata ya daura da Sadiya, zama yayi Bayan ya gaishe da Aunty'n Laylerh sai ya Kai duban sa ga Mom nashi

"Mom". Ya Kira ta cikin sanyi

" Na sani Sulaiman ba sai Ka fada mini ba sun Riga da sun daura Shikenan kuma rayuwar 'ya ta ya ruguje but ba komai wallahi da auren nasa a kan ta Zan tura ta wani wajen karatu".mikewa yayi inda ya Isa Gare ta durkusawa yayi a gaban ta tare da daura kan shi a cinyar ta sannan ya daura hannun ta daya a kan shi inda yake fad'in

"Mom Laylerh Yar uwa ta ce ba Zan taba son abunda zai cutar da ita ba duk da ni din ma Na zalunce ta a baya Wanda ba Wanda ya Mata irin shi,for now I want to repaint so nake tayi alfahari da ni a matsayin yaya shiyasa Na gaza samun nitsuwa da naji su biyu zai aura sai dai bana nunawa..a dazun da Na sallame Ki Na tafi wajen daurin auren Tun a hanya zuciya ta ke bugawa ko da Na Isa naga taron jama'ar gurin sosai hankali Na ya tashi don Na tabbatar sai an daura wannan auren,sai dai ance kaddara ta Riga Fata cikin ikon Allah auren Umar Farouq da Sadiya ba'a daura ba kuma Na gano da hannun shi a hakan". Wani dogon ajiyar zuciya ta sauke tare da dago kan shi tana duban fuskar shi Kai ya gyada Mata alamar tabbatar Mata da zancen shi nan take kuma ta shiga shafa kan shi

" Allah maka albarka wannan labarin ya faranta mini sosai saboda ina fargaban shigar Laylerh gidan can don wahala zata sake ci".murmushi yayi sai Aunty'n Laylerh dake zaune daga gefe ne tace

"Kai Alhamdulillah Allah Mun gode maka". Duk duban ta suka yi shi ko sosai yake farin ciki ganin yasa su farin ciki,gyaran murya tayi sannan tace

" rashin daura auren ba shi ke nufin zan sakarwa Umar Farouq ragamar rayuwar Laylerh yayi yadda yake so da shi ba,Na fahimci ba son ta yake yi ba don haka

Laylerh ba zata tare ba har sai yazo gaba na da bakin shi yace yana da bukatar ta yana kuma son ta sannan Zan bashi".

"Mom wallahi ya fiya jin Kai sai kace yafi kowa".

" A'a yaya Hadeeza kada kiyi haka Yaron nan fa suna magana da ita a waya".ba tare da ta bata amsa ba ta kwala kiran Laylerh nan take ta fito daga daki duk tayi sanyi Wai yau ita ke daure da igiyan auren wani har uku,gefe ta zauna

"Ya Sulaiman ina kwana?"

"Laylerh kin tashi lafiya".

" lafiya kalau mom gani".

"Laylerh when last kuka yi waya da Umar Farouq?" Kan ta a kasa murya Na rawa tace

"Tun da aka gama case bamu sake waya ba".

" kin dai ji da kunnen Ki".ta fada tana kallon Aunty'n Laylerh nan ta cigaba

"Na Lura komai mahaifin shi ke mishi shi dai yana zaune Nade da hannu yana jiran a Kai mishi mata to a yanzu anzo gabar da sai yayi abu da kan shi yazo har nan ya roki Na bashi Laylerh in ba haka ba tana nan wallahi kuma bai Isa datse igiyar auren nan ba haka ko Zan tura ta karatu duk wannan jin Kai sai ya sauke, Zan ja shi a kasa ne yadda bai taba tunani ba don yasan ita din Mai daraja ce ba sadaka aka bashi ba". Sosai wannan zancen yayiwa Laylerh dadi don ta fahimci tsam he don't value her nan ta mike ta koma ciki su ko suka cigaba da tattaunawa ita dai Aunty'n Laylerh gani take tunda an Riga da an daura a bashi kawai su musu fatan Alkhairi

sai dai tsarin yayar tata ya burge ta don bai nuna ya damu da Laylerh din ba ko kadan..

****

Kura Mata ido yayi a Karo Na biyu yace

"Ki Kira ta mana Hauwa kin fa San lokaci Na kurewa". Ajiyar zuciya ta sauke sannan tace

" ba kiran ta ne bana son yi ba wallahi matar tana da Zafi sosai bana jin zata amince ".

" Ki dai Ki gwada ".daga nan tayi searching Na number'n Mommy Sulaiman nan ta Fara dialing zuciyar ta sai bugawa yake,sanda wayar ta kusa tsinkewa sannan Laylerh ta daga

" Assalamu Alaikum Hajiya Hadeeza ".da yake ta San Mai number'n sai bata wani sake fuska ba tace" wa'alaikisalam ya hidimar biki?"don duk tayi niyar basu wahala

"Alhamdulillah muna fama". Daga haka sai tayi shiru Abba ko sai Mata alama da tayi magana yake yi murya Na rawa tace

" ya Laylerh amarya? ".

" lafiyar ta kalau".ta fadi cikin gajiya da zancen don ta San haka kawai ba zasu Kira ta ba

"Masha Allah wallahi Wata alfarma ce yasa Na Kira Ki".

" feel free ina jin Ki".

"Hajiya kin San yadda aka yi auren Laylerh da Umar Farouq sannan an tsara auren da Na Sadiya sai Allah bai kaddara tana cikin matan shi ba don haka jama'a duk sun gama taruwa sai dai ba amarya ko daya". Tana kaiwa nan tayi shiru tana sauke ajiyar zuciya Mommy Sulaiman ko murmushin Rainin wayo tayi sannan tace

" uhum ina jin Ki".

"To Hajiya Mun gama gayyatan mutani walima inda manyan mutani zasu halarci wajen shine muke so Ki bamu Aron Laylerh Na Rana daya Na miki alkawarin Ana gamawa Zan dawo miki da ita".

" Hajiya Hauwa kenan Wato shi Dan naku har yau ba zai ajiye girman Kai din ba ko to Laylerh dai ba Zan bayar ta".ta fada Kai tsaye don ba shakkar su take yi ba

"Don Allah Hajiya Hadeeza". Shi dai Abba ido ya zuba yana sauraron su don a hands Free wayar take

" kin San Tun yaushe rabon da ya Kira ita Laylerh? Shin ji yake cewa sadaqa za'a bashi ne ko mene ne?kin fa San in za'a yi Aure zaki ga tare ango da amarya zasu tsara biki Amma shi kamar yafi karfin ta yake ji a haka kike so Na Baku ya ta don Ku fita kunyar duniya tsam ba Zan bada ta ba ".

" Na sani tsam bai kyauta ba ya kuma cancanci hukunci Amma yanzu da Allah nake hadaki Ki taimaka Ki bamu Laylerh Na yau daga baya sai a mishi duk hukuncin da aka ga ya dace Dan Allah dai ke ma uwa ce kin San mutani zasu ga gazawa ta a matsayin yadikko sannan zasu fahimci akwai matsala ".ajiyar zuciya ta sauke don ita din ma yadikko ce Ai kuma komin daren dadewa dole zata aurar da Sulaiman nan tace

" Zan Baku ita iya lokacin walima daga wajen walima kuma gida za'a dawo mini da ita don ba Zan Bari ta kwana a gidan Ku ba".so take tace a basu ita Na complete day sai Abba ya girgiza Mata Kai kan cewa hakan ma yayi shiyasa tace

"Shikenan Mun yarda Allah saka da Alkhairi waliman karfe biyu ne".

" Shikenan Allah kaimu".daga nan sallama suka yi cike da farin ciki Abba yace

"Ni nan ma kadai Na ishe shi zanyi maganin shi don Ana gama biki Zan manta da Na daura mishi Aure Inga ta siyar shi yanzu Kira mini shi da line naki".kiran shi ta Fara sai da ya katse sannan ya Kira ta nan ta Mikawa Abba wayar

" wa'alaikasalam Ka Kira laylerh yanzu ta tura maka account number'n ta Ka tura maka kudin Kayan biki".jin muryar Abba ba wasa sai yace to tare da katse kirar da kyar ya lalubo number'n ta ya Fara dialing sai dai har ta katse ba'a daga ba,Kira ya sake a Karo Na biyu nan ma ba'a yi picking ba

"A lallai raini ya tabbata Tun yanzu". Ya fadi a zahiri sannan ya Kira Abba yana picking yace

" Na Kira ta bata dagawa".

"Alright". Kawai Abba yace nan yace Aunty Hauwa ta sake kiran Mommy Sulaiman haka ko aka yi tana picking tace

" fatan ban takura miki ba dama so muke Laylerh ta turo account number'n ta a sa Mata kudin Kayan biki".

"Laaa Kinga kada Ki damu da wannan".

" a'a Hajiya Ai nauyin a kan mu yake".duk yadda Aunty Hauwa tayi Mommy Sulaiman kin yarda tayi a Cewar ta Yar ta daya tilo zata saya Mata dole suka hakura..

Sallamar su yayi daidai da shigowar makobciyar Mommy Sulaiman nan suka gaisa

"Aiko kamar kin shiga raina hajja kande nikam Hanan da sabriyat sun dawo hutu ne?"

"Sun dawo yanzu haka Na barsu a gida kin San sun dawo da Yar bappan su Na Maiduguri".

" to Alhamdulillah dama yau ne waliman Laylerh so nake su Mata kawance don bata da kawaye a nan".

"Hajiya Wai baki nawa zaki yi ne Ince kince ba yanzu zata tare ba"..

" Ehhh ba tarewa bane yanzu gidan mijin suka nemi alfarmar a basu ita Na lokacin walima kawai".

"Ohk kawaye kam Ai su Hanan suna da su dayawa in yaso sai a Kara ko biyu".

" a'a ukun ma yayi yanzu dai Ki roka mini Baban su zamu tafi boutique da ita Laylerh din da su".to tace nan ta wuce gida Mommy Sulaiman ko sai kiran frnds nata a waya take tana sanar da su batun waliman duk da sun San da daurin auren nan ko suke cewa in sha Allah zasu zo da yake bata taba aurarwa ba ita kuma kullum tana zuwa musu..

Aunty'n Laylerh ko kitchen ta nufa inda take sanar da yan aiki kalar abincin da za'a daura kan wadanda aka gayyata su karaso..

Wacce aka Kira da hajja Kande ne ta dawo tare da wasu yan Mata yan gayu sai dai wacce ta fi su kyau da rigima mita take yi

"Haka kawai za'a ce muyi Mata kawance Nifa abu da disgrace ne bana so especially in abokanayen ango suka Gan amaryar bata Waye ba raina mu zasu yi in tayi low class dayawa sa Kayan ta zanyi naje a matsayin ta". Duk sauran ba Wanda yace da ita Kala har suka shigo gidan,ganin yadda gidan yake da kyau da kuma tsari ne yasa ta nitsuwa kadan har suka karasa falon inda suka gaisa da ma'aikatan gidan da kuma Aunty'n Laylerh dake ta safa da marwa a dakin,zama suka yi nan Mommy Sulaiman ta fito gaishe ta bakuwar su hajja kande tayi don ita ce bata San ta ba su hanan kam sun Santa nan su ma suka gaisa sai ta shige daki domin kiran Laylerh..

A can ne kuma ta tarar ta gama shiri suna waya da Muhammad dake sanar da ita cewa yana da exams da yazo

" muje ko?"sallama tayi da Muhammad nan ne suka fito falo birki taja tana kallon bakuwar su hajja kande baki Na rawa tace

"Fateema". Da wuri wacce aka Kira da Fateema ta daga Kai tana kallon Laylerh duk ta tsarai ta gane ta sai ta basar don yanzu halin da ta daukowa kanta kenan Na jiji da kai

" Fateema kin San ta ne ita ce amaryar fa".jin Laylerh ce amaryar sai ta sake fuska nan suka rungumi juna..Fateema ba kowa bace face Kawar Laylerh Na makaranta wacce suke cin abinci tare lokacin da head boy ke cin uban ta..sosai suka yi murnar ganin juna nan Mommy Sulaiman tace su tafi..

Fitar su ke da wuya wayar Aunty'n Laylerh ya Fara ringing tana dagawa taga Aunty Hauwa ce Bayan sun gaisa sai tace

"Na sani a yau Na takura muku dayawa Amma Dan Allah so nake Ki rokar mini yayar Ki don naga tana jin maganar Ki tayi hak'uri ta bamu Laylerh Na complete day don ayi budan Kai kada kuma mutani su fahimci bamu tare da amaryar". Sosai taga hakan ya dace nan ta Mata alkawarin Mata magana..

A bangaren gidan Ango ko komai Na tafiya yadda ya dace jira kawai suke lokacin walima tayi..

Su Laylerh koda suka fita wani Babban boutique suka nufa Wanda ita Laylerh sai da ta raina kanta tana kuma jin cewa ita din Yar Gata ce, Kayan amare ba irin Wanda babu gasu ready made nan aka Fara dubawa Laylerh suna cikin dubawa Fateema da ake Kira da teema tace

" Aunty shi angon wani color'n kaya zai sa?"duk ba Wanda ya San irin Kayan da zai sa Gashi ita ba zata ce Laylerh ta Kira shi ba saboda ita ta hanata daga call nashi ko dazun da yake Kira tana gani

"I really don't know but zamu dauka Mata fari tunda zai je da ko wani color". Nan ko aka dauka Mata wani farin gown da kudin sa ya jijjiga Laylerh ita ko Mommy Sulaiman so take kallo daya in aka yiwa laylerh a tabbatar Ehhh Yar ta ce,nan suka koma wajen takalmi da purse subhanallah Ai Mommy Sulaiman ta kashe Wa Laylerh kudi sosai,neck lace nata kadai abun kallo ne daga nan kawaye kuma maroon Na lafaya ta saya musu da takalmi sai aka koma bangaren Kayan maza su dai ta bar su suna zabawa Laylerh net da zata daura akan gown din shiyasa basu San me take yi ba sai da aka zo fitar musu da kaya ne suka ga katon akwati irin Na kasa aka sa cikin motar Bayan nasu sayayya..

Daga boutique din saloon din Wata Mata professional suka wuce cikin gaggawa aka wanke Mata Kai sannan suka dauki matar domin Mata make up..

Lokacin da suka iso gida sosai mutani suka taru sai hira ake abun Ka da manya nan ne su Laylerh suka gaishe su tare da wucewa ciki wannan matar ta Fara zama Mata Jan lalle a hannu,Aunty'n Laylerh ko abinci ta gabatar musu inda take bawa Laylerh a baki tunda Ana Mata lalle..

Suna sallar azahar lokacin tuni lallen Laylerh ya bushe don a hannu kadai aka yi ta shiga wanka haka sauran kawayen ma tana fitowa kuma suka Fara make up..

Da yake professional ce matar basu dauki lokaci sosai ba nan ta dauki inner wears nata sabo masu tsada ta nufi toilet Tasa tana fitowa kuma aka Fara kokarin tayata sa rigar tana gamawa suka Fara dauri kawaye ma sun shirya..

Aunty'n Laylerh ce tabi Bayan Mommy Sulaiman ganin ta shiga daki don tuni mutani suka cika

" Amina har yanzu baki shirya ba".Kama hannun Mommy Sulaiman tayi tace

"Yaya Dan Allah alfarma nake nema a wajen Ki duk da Na San ban Isa da Laylerh ba".

" Haba Amina wannan wace irin magana ce".

"Yaya don girman Allah Ki Bari Laylerh ta kwana a gidan can su samu suyi budan Kai ko don wannan Mata Mai kirki ta fita bakin duniya,sannan ita Laylerh in aka ce daga wajen walima za'a dawo da ita nan Ai kawayen Ki sai su zargi wani abu Ki dai bar su suje suga gidan mahaifin Yaron ni nan Na miki alkhairin kula da komai in muka je can". Ajiyar zuciya ta sauke don wannan shine Karo Na farko da Amina ta roke ta shiyasa ta rungumi Yar uwar ta daya da ta rage Mata tace" Shikenan Ai kece uwar Laylerh bani ba yanzu dai Kije Ki shirya".sosai taji dadi sai tace

"To yaya ya batun motoci kunyi magana da su ne".

" Amina bamu yi magana ba kuma ba Zan tambaye su ba in basu tura ba Shikenan sai mu rike ta Kinga je Ki shirya".ficewa tayi nan Mommy Sulaiman ta hau shiri cikin wani tsaddaen lace da ta saya musu iri daya da Aunty'n Laylerh kallo daya zaka Mata kaga babbar Mata daga nan bangaren Sulaiman ta wuce kwance ta same shi

"Laa yanzu Sulaiman har lokaci yayi baka shirya ba".

" no mom ni kuma me zanje nayi a cikin Mata".

"See you waliman Ai Na maza da Mata ne hurry up Ka shirya".

" Mom bana jin Zan iya zuwa Nifa yaya ne kin taba ganin inda yaya ke rawan jiki a auren kanwar shi gwara da ni mace ce".gaskiya ya fada yawanci yayyu zaka ga sun kame a auren kannen su a lallai basu son raini basu kuma fiya shiga tsabgar auren ba sai in Ana bukatar taimakon su,wayar tace ta hau ringing tana picking Aunty Hauwa tace

"Allah sa kun gama shiri don motoci Na hanya".

" kada Ki damu duk Mun gama".

"Masha Allah mu ma yanzu muna hanya ne". Daga nan suka yi sallama buga shoulder'n Sulaiman tayi tace

" ohk you take care".

"To Mom". Nan ta fice zuwa dakin da ake shirya Laylerh Tun a hanya take jin kamshin turare tana bude kofar kuma idon ta ya sauka kan Laylerh da aka ajiye ring light a gaban ta Ana watsa Mata hotuna da video

" Masha Allah ".ta furta ganin kyan da Laylerh tayi,a hankali Laylerh ta Isa Gare ta tare da yin hugging nata tace

" Mom kinyi kyau".breaking hug din ta yi tana bin lungu da sako Na jikin Laylerh da kallo tace

"Tsarki ya tabbata ga ubangijin da ya hallice Ki gaskiya kin yi kyau". Daga nan aka shiga watsa musu Hotona a haka Aunty'n Laylerh tazo ta tarar da su in ba Ka sani ba sai Ka rasa wace ce mahaifiyar Laylerh a cikin Su..sa ta a tsakiya suka yi aka yi ta hotuna a haka suka fito falo sai yaba kyan Laylerh ake yi a lokacin ne kuma motocin suka iso Amma ba Wanda ya fita don Mommy Sulaiman cewa tayi kawayen ta su zo su dauki Hoto da amarya haka ko suka yi ta yi..

Da yake kawayen ta manyan mutani ne su shida suka zo da motocin su inda motocin da aka tura musu ma guda takwas ne sai dai gaba daya masu tsada sosai ne..sai yanzu Sulaiman ya fito aka Fara jera mutani da shi inda motoci biyu cikin takwas din ya kasance Na abokanaye daya kuma Na kawaye saura biyar kuma Na yan rakiya..Sulaiman yayi mamakin ganin motoci masu tsada haka gasu a Jere nan kawaye suka shiga nasu su biyu a baya Teema a gaba sai wani aboki inda su kuma brown jumper suka sa..sauran manyan matan duk fito da motocin su suka yi nan motoci sha hudun suka jeru kuma ba Na karamin kudi..

Sulaiman da kan shi ya fiddo Laylerh hannun shi daya rike da ita daya kuma rike da purse nata tana tafiya a hankali don bata Saba tafiya da takalmi hill ba,motar da tafi ko wacce kyau Gata Fara sabuwa fal da tinted glass kallo daya zaka mata ka san ita ce na amarya yayi knocking tare da bude Mata inda ya taimaka Mata ta shiga sannan ya tattare kasan rigar ya shigar

" Allah kiyaye hanya ".yace lokacin da ya rufo kofar daga ciki kuma taga yana waving nata murmushi tayi tana jin shi a ran ta..a hankali motocin suka Fara tafiya ita ko hankali kwance take gyara abun hannun ta inda ta ajiye purse din a cinyar ta sai driver dake driving Wanda bata kallon shi sosai tana jin kamshin turaren maza Mai sanyaya zuciya da kuma ji kamar akwai mutum a gefen ta Amma sai tayi tunanin kila kamshin driver ne,karar waya taji a gefen ta hakan ya sata Kai duban ta inda taji ringing din..Umar Farouq ne sanye cikin sky blue jumper Harda Gare da ya sha aikin wuta ga hula da yasa a kanshi ba karamin kyau yayi ba da wuri ta cire ido a kan shi jin yana amsa wayar

" uhum in sha Allah ".sannan ya cire wayar a kunnen shi..ba karamin baci ranta yayi ba ganin bai nuna ya San da mutum a motar ba shiyasa ita ma tayi banza da shi sannan ta juya ga window tana kallon inda suke wucewa, sunyi tafiya sosai sannan taga motocin gaban su sun tsaya a gaban wani Hall Mai shegen kyau sai a yanzu ne driver din ya juyo yana kallon su fuskar shi dauke da murmushi yace

" sannu amaryar mu".ta shaida shi Bash ne shiyasa tace"Yauwa ".daga nan kuma duban shi ya Kai ga Umar Farouq

" Ku jira kadan Bari mu kimsa mutani ".yana gama fadin haka bai jira amsa ba ya fice..

Shiru motar ta dauka ba abunda ke tashi sai sanyin AC da kuma kamshin turaren su sai music dake tashi a hankali,ganin Bash Na knocking Na kofar ta juya zata bude sai taji ya rike hannun ta dake tsakanin su jiki Na rawa ta zuba idanun ta kan hannun shi dake sanye da wrist watch yana murza yatsun ta a hankali wadanda suka sha Jan lalle da wuri kuma ta Kai duban ta ga fuskar shi dake shimfide da saje sai taga duk hankalin shi Na kan yatsar jikin ta Na cigaba da rawa taja hannun ta sai taji yana rike da shi take idanun ta ya Fara Tara ruwa murya Na rawa tace

" k..a..sake....n...i".jin yadda maganar ke fita daya daya ya sa shi kallon fuskar ta a take kuma ya lumshe ido ya sake bude su a kanta yana sauke ajiyar zuciya tare da matsawa kusa da ita nan take zuciyar ta ya Fara bugawa ganin yana kusanto fuskar shi da nata,Iskan bakin shi Mai dumi ya hura Mata a ido sai ga hawayen ya zuba tissue ya dauka yana goge Mata yadda ba zai bata kwalliyar ba,jin ringing na wayar ta ya sa shi matsawa baya hannun ta Na rawa ta gagara fiddo wayar ganin haka ne ya sa shi bude purse din tare da Ciro wayar ya sata a hands free ganin Mom ke Kira

"Dan uban Ki me kike yi da shi a cikin mota Tun dazun kin fito ne ko sai nazo wajen, Ai Na San zai yi tsaurin ido shiyasa ban shiga ba Tun dazun ina mota maza Ki fito Na fahimci tsam baida ta ido". Hannun ta har rawa yake ta Fara kokarin bude kofar nan ya maida Mata wayar ta sannan ya Dan kwanto a cinyar ta ya mika hannu yana kokarin bude Mata kofa da sauri ta rintse idanun ta jin zuciyar ta Na barazanar fita yana gama budewa ya tashi da sauri ta Fara kokarin fita a saman labban shi ya furta

" kinyi kyau".Ai duk bata wannan take ba tsoron amsar da zata bawa Mommy Sulaiman take shiyasa ta fice.. a hankali ya bude kofar bangaren shi cike da jin Kai din ya fito nan masu vedio coverage suka Fara aikin su da masu Daukan Hoto a haka suka jera tare zuwa Hall d'in kawaye da abokanaye Na baya kace reception ne..

Masha Allah kowa ke furtawa lokacin da suka shiga hall d'in duk da ido ake bin su Ana ganin dacewar su inda aka tanada domin su suka zauna Allah ya sani wajen ya Mata kyau yadda aka yi decorating nashi..

An Fara gabatar da walima ba jimawa Mommy Sulaiman ta shigo sosai Laylerh ta tsorata da kallon da take Mata don kallon zamu gamu ne,walima yayi walima nan aka Fara serving mutani abinci kam Masha Allah sai kalar da Ka zaba nan aka Fara ci ango da amarya kam shiru suka yi kaman gumaka..

Jin an kusa tashi yasa Mommy Sulaiman nufar wajen Aunty Hauwa wacce ke fama da jama'a taja ta gefe

"Kin San dai da kyar Na yarda Na bada Laylerh to so nake in zaku tafi can gidan Ku kada a hada ta mota daya da Umar Farouq don ni tsam ban yarda da shi ba so nake a hada ta mota da uwar goyon ta ko Na koma da ita". Zancen ta dariya ya bawa Aunty Hauwa Wai bata yarda da Umar Farouq ba to me zai Mata

" Shikenan in sha Allah haka za'a yi".a haka har taro ya watse nan aka sa Laylerh da Aunty'n ta cikin wani mota ango ko da abokanayen shi suka tafi..

Direct gidan Alhaji M wakili aka nufa da ita da kawayen mommy Sulaiman sosai suka yi mamakin ganin girman gidan da tsaruwar shi Wanda ko ba'a fada ba kasan Babban gida ne..

Bangaren su Fateema kam tunda suka ga Umar Farouq wajen walima suka tabbatar da Laylerh tayi dace..tarba Mai kyau aka musu daga nan aka wuce da ita third floor can bangaren Abba aka basu daki ciki da falo da toilet Harda kitchen da dinning ga dakin Babba..

Nan take Aunty Hauwa tazo hannun ta dauke da karamin akwati cikin shi kuma wani shegen super wax an kashe mishi dinki da Vail gami da takalmi da jaka da kuma sarka da Dan kunne,nan Mata Mai make up din da yake sun zo tare da ita ta gyara Mata make up din suka sake shirya ta sosai tayi kyau,su Nana da su Najeeha ne suka shigo sosai suka yaba da kyan Laylerh nan aka fidda ta wajen budan kai

inda a can ta tarar da Umar Farouq sanye cikin gezna Fara ta sha aikin wuta ya baza Gare fuskar shi sai walkiya yake kan shi a kasa don bai son taron jama'a ba dai yadda ya iya ne sosai yayi kyau gefen shi aka zaunar da ita nan masu algaita da maroka suka Fara aikin su masu Hoto ma nayi..

Bangaren Zakari Baban Laylerh ko tuni aka Kama mishi hotel a yau din ne kuma Ladidi ta iso da yayar Laylerh wacce suke uba daya ba laifi suma sun sa kaya Mai tsada tunda ance tuwon girma miyan nama nan ne ya Kira M wakili sai aka tura Hajara ta dauko su yanzu shigowar su kenan an Fara budan Kai..

"Nawa kuka sai bakin amarya?" Kawar Mommy Sulaiman ta tambaya

"Million uku".zuciyar Laylerh sosai ya buga a hankali ta daga ido domin ganin wacce ta fada saboda kamar ta San muryar Ai ko ba kowa bace face Hajiya kaltume mahaifiyar Naseer da sauri ta sauke Kai kasa tana gyara Vail nata yadda ba za'a Gan ta da kyau ba..

Hajiya kaltume da Hajiya Maryam Wato mahaifiyar Umar Farouq kawaye ne sosai shiyasa ta halarci bikin..Tun Bayan da suka gama da Sani a court Baban Naseer ya buda Mata wuta kan cewa in ta sake ko batun Laylerh ne a bakin auren ta wannan dalilin yasa ta shiru lokacin da Dada tazo kuma sai ta fahimtar da ita komai cewa Laylerh ba mayya bace kuma Tun a wajen walima ta gane Laylerh..

Karasawa su Ladidi suka yi tare da samun waje suka zauna yayar Laylerh kuma sai kallon Laylerh take yi tana jin son ta..

Akwati set Aunty Hauwa ta gabatar musu Na amarya inda ba abunda babu a ciki nan ne kuma Aunty'n Laylerh tayiwa Umar Farouq budan kan million biyu sai Babban akwati Wanda mommy Sulaiman ta saya lokacin da suka je boutique, yadin gezna masu tsada guda goma sai water proof shima goma kuma ko wanne da takalmin shi sai agogo biyar da sallaya daya da Qur'an..wannan shine al'adar su a haka masu liki suka yi ita dai Laylerh kanta a kasa sai in camera man yace ta dago sai hajara ko Najiha su daga fuskar Ladidi ko Na daga can ta kurawa laylerh ido tana tunanin ta inda zata bullo Mata..

A haka aka gama budan Kai nan aka maida ta dakin sai a lokacin Aunty'n Laylerh ta farga da Ladidi bata nuna Mata komai ba suka gaisa nan ta gabatar da su ga Laylerh sosai laylerh taji zafin matar tunda ita ce sanadin duk wahalar da uwar ta ta sha a gidan Zakari Yar uwar ta kuma hannu biyu ta amshe ta nan ne Aunty'n Laylerh ta zame ta sanar da mommy Sulaiman zuwan Ladidi Ai a take ta birkice ta Kira Aunty Hauwa ita a lallai su maido Mata Yar ta

"Haba Hajiya kece fa Kika ce kin bamu ita".

" to Na fasa ko Ana dole ne wallahi ko Ku maida mini 'ya ta ko Na muku rashin mutunci "..abu kamar wasa sai ga magana ya dau Zafi har yan biki sun Fara ji nan Hajiya kaltume tace

"Ai wannan duk don uwar shi bata Raye ne har yaushe za'a ce an daura Aure Amma uwar ta ke da iko da ita tana cewa a maida Mata Yar ta". Nan fa yan uwan mahaifiyar Umar Farouq da wasu daga cikin dangin Abban shi suka Fara zagin Aunty Hauwa karshe daki taje ta rufe kanta ta sha kuka sosai haka yaci ma su Nana da Yasmeen rai matar tsam bata taba nuna su ba nata bane don haka Nana ta sanar da Umar Farouq cewa mahaifiyar Laylerh tace a maida Mata Yar ta kawayen Ammi da wasu yan uwan Abba kuma sun Ki Gashi sai zagin Aunty Hauwa ake tana kuka..

Gurmi ba sai ya zama babba ba dama gidan biki ba'a taba watsewa lafiya ganin abun da gaske ne har Mommy Sulaiman Na cewa zata zo da kanta yasa Umar Farouq kiran malam kan cewa ya Mata magana..

Sosai malam yaji mamaki don shi bai San an daura auren ba tunda dama yau ne auren Amma Gashi har cewa yake anyi budan Kai shiyasa yace tunda ba'a fada mishi ba ba hannun shi..

Karshe har Abba sanda yaji Amma Mommy Sulaiman taki hakura kuma taki fadan dalilin ta Na rashin son Laylerh ta kwana Wanda a zahirin gaskiya gani take kamar Ladidi zata sake cutar da ita a Karo Na biyu..

Da kyar Sulaiman ya nuna Mata illar abunda take yi zai haifarwa Laylerh bakin jini Tun yanzu a dangi miji tayi hak'uri batun Ladidi kuma Allah Na nan zai kare ta sannan ga Aunty'n ta wacce ta kasance jigo a rayuwar ta..

Wannan dalilin ya sata hakura tare da cewa kafar Laylerh kafar Aunty'n ta kuma kada su kwana daki daya da Ladidi don kada ta tsafe Mata 'ya cikin dare sannan shi uban gayyan ma bata yarda da shi ba..

Haka Aunty'n Laylerh ta kwana gadin Laylerh ba tare da ta rintsa ba Washe gari kuma Tun bakwai da rabi ta tura musu breakfast lokacin da aka kawo Abba zai fita sosai yayi mamakin ganin abinci daga waje ko da ya tambaya sai aka ce daga gidan uwar amarya aka kawo nan yaje ya rufe Aunty Hauwa da holo Wai ba'a Kai musu abinci ba nan take ta nuna mishi abincin tana hawaye..

Karfe sha daya aka Fara cewa za'a je gidan amarya nan ne aka sanar da su ba'a kimsa ba daga haka mutani suka Fara watsewa zuwa dare saura bakin nesa..

A Daren kuma aka hada musu goma Na arziki sannan aka sa amarya a mota aka maida ta gida Ladidi da Yar ta kuma hotel suka koma..

Koda suka koma duk a gajiye suke shiyasa suka kwanta Washe gari kuma mommy Sulaiman ta Kira ta bawa malam hak'uri tare da sanar da shi ita ma sanda aka daura ta sani..Abba ma ya Kira shi ya bashi hak'uri nan Baaba ta rikice sai tazo aka ce Ai bata tare ba..

Auta kam Tun ranar da aka ce an daura auren Laylerh da Umar Farouq take kuka har yanzu..

Tun tana fargabar a tambaye ta me ya faru har ta cire abun a ranta..

Bayan kwana biyu

Yanzu duk hankalin su ya dawo jikin su bangaren Alhaji M wakili ma tuni baki sun tafi gida ya rage shi da yaran shi ango dai duk a takure yake..

"Yaya yanzu sai yaushe zata tare?"

"Sai Bayan azumi in shi Yaron yazo".

" Wata biyu kenan fa".

"Ehhh".

Comment

Share

©Hafciey Musa

[1/25, 5:44 AM] Hafciey Musa😘: *□LAYLERH□*

(The prettiest emerald)

Page 47

Bangaren Sadiya kuma yanzu ta rayuwar ta take duk da sai a yau ta samu labarin auren Umar Farouq din sosai ranta ya tafasa ta kuma yi alkawarin dawa Gare su Amma sai in ta daidaita komai..

Bangaren Ladidi ma a Washe garin suka koma Bayan Alhaji M wakili ya Musu goma Na arziki don ta tabbatar tana da bukatar sake shiri don taga yanzu Hadeeza a tsaye take kan Laylerh da Sulaiman..

Isar su gida sai agolan ta tafahimci mahaifiyar Na cikin damuwa.. Tsaye take da saurayin ta a kofar gidan sai dai tsam hankalin ta baya kan shi gaba daya tana tunanin mahaifiyar ta ne don ta San tabbas da matsala wannan dalilin yasa ta

sallamar shi sannan ta nufi cikin gida nan ta wuce Zakari da wani bakon shi ganin duk hankalin ta baya jikin ta tana tafiya tana tada kura ya sa shi bin Bayan ta Bayan ya sallami bakon shi kitchen yaga ta nufa nan shima ya rufa Mata baya..

Ladidi tsaye take a kitchen din tayi nisa a tunani har bata San da shigowar agolan ba sanda ta dafa kafadar ta nan ta firgita

"Mama me ne naga tunda kuka dawo daga auren Laylerh hankalin Ki baya jikin ki". Ajiyar zuciya ta sauke sannan tace

" ina fa hankali ya zai zama a jiki Na Bayan duk kulla kullar da nayi Na dauke Laylerh Na Kai ta kauye Na Yar sannan Na toshe bakin uban ta da uwar daga baya uwar ta ta so dagowa sai kawai Na cire hankalin Zakari a kanta yadda ko ta fadi zance ba zai yarda ba karshe duka ya Mata sannan ya Kore ta".

"Mama Ai Na San da wannan me yasa kike maimaita mini?"

"Ai matsalar shine yanzu Laylerh Na cikin jin dadi Wanda ban taba kawo a raina zata ji dadi ba saboda duk Wata wahala da ta sha sa hannu Na ne,tsam ba Zan juri ganin tsatson Hadeeza cikin farin ciki ba shiyasa Na Kira malami Na Na fada mishi sai yace kada Na damu komai zai daidaita Amma Na tabbatar ba Wanda yaji wannan zancen nace mishi ke ce kadai Kika sani yace ke ma kina da baki Na kiyaye fada miki yanzu dai kin San ba Wanda ya San da zancen nan ki tafi wajen shi ki karbo mini magani dole naci arzikin nan sai Na raba Laylerh da uwar ta ya zama sai abunda Na fada Laylerh zata yi". Haka ta cigaba da tonawa kanta asiri da kuma jaddawa agolan kada ta bar kowa yaji,ta bude kofar zata fita kenan suka ga Zakari tsaye ya Nade hannu a kirji da alama kuma ya gama jin komai..hannu Ladidi ta daura a Kai tana kuka don ita ba hukuncin da zai dauka bane damuwar ta a'a tunda yaji Shikenan kuma ta kade har Ganye saboda abun ba zai yi aiki ba..

Ba tare da tunanin a gaban Yar ta suke ba ya debe ta da Mari har sanda ta fadi kasa tana cigaba da kuka

" kin kyautawa kan ki kin sa Na Gaza yiwa yaya Na abunda ya dace nayi sai bauta da nake yi miki ke da agolan ki da yan gidan Ku tsam ban taba tunanin cutar da ni kike yi ba Amma ba komai Kije Na sake ki saki uku ki jira sakayyar abunda Kika aikatawa Hadeeza da Yar ta kuma".kare fashewa da kuka tayi tare da rike kafar shi tana rokon shi

"Dan Allah Zakari Ka rufa mini asiri yanzu in Na tafi ina zanje". Kwace kafar shi yayi sannan ya dube ta cikin tsananin bacin rai yace

" kaico Na da Na auri Mata irin ki wacce ta raba ni da Yar uwa ta kwaya daya tilo nayi banza da lamuran ta,wallahi Ladidi hakkin mutani ba zai bar ki ba son Aure Aure Na ya ja mini..kin fi kowa sanin Na iya dukan Mata tunda ba sau daya nake dukan Hadeeza a gaban idon ki ba don haka Tun wuri ki fice mini a gida ko nabi lafiyar jikin ki".da sauri ta mike sanin halin shi sarai zai aikata abunda ya fada shiyasa ta nufi shiga ciki

"Kada ki kuskura ki shiga don baki zo da komai ba hatta da sutura Nike saya miki". Yana gama fadin haka ya Kira kanwar Laylerh yace ta dauko Mata hijab yarinyar Na tambaya ko lafiya sai ya daka Mata tsawa da wuri ta wuce ta kawo tana kuka

" Shikenan kun ga Baban Ku ya tona mini asiri ya sake ni".haka take fada take yaran ta uku Wanda duk Mata ne suka Fara kuka agolan kuma fisge hannun Ladidi tayi tace

."Kinga Mama zo mu tafi daina kuka akan wannan shashasha Ai ba shine autar maza ba malamai Na nan kwananan wani Alhaji zai fito ki Aure shi banda kaddara me zaki yi da shi".Ai ko mopper ya dauka yayi kan su da gudu ya raka su har gate Bayan Mai gadi ya rufe sai ya juyo gida yana sauke ajiyar zuciya tare da tsanar kan shi yanzu Ashe duk abunda yayiwa Hadeeza Ladidi ke Sawa,zama yayi a falon tare da fashewa da kuka nan yaran suka Fara taya shi,su din yaran ta ne Amma basu yo halin ta ba nan gwaggon su ta shigo

"Ka godewa Allah Zakari mutuwa bata riske Ka a haka ba Kayi nadamar abunda Ka aikata tsam Ladidi ba mace ta gari bace hakika ta cutar da mutani dayawa". Kuka yake yi haka ma yayar Laylerh don tafi sauran takaicin halin uwar su all she needs was a shoulder to cry shiyasa gwaggon su kwantar da kanta a kafadar ta nan tayi kuka Mai Isar ta don kanta ta hakura..

Daga wannan ranar suka koma rayuwa su biyar a gidan inda gwaggon su ke kula da su ta kuma yi musu girki kan su dawo daga makaranta ta kuma cewa Zakari ya dace yan uwan Laylerh gaba dayan su suje Gare ta ko don ta san su yace in lokacin tarewar ta yayi dukkan su zasu je don kunyar abunda ya aikata yasa tsam ba zai iya sa baki a zancen tarewar Laylerh ba gwara dai Mommy Sulaiman tayi duk yadda take so..

**

Duk kowa ya fita harkar Umar Farouq ba Wanda ya sake mishi maganar Laylerh sai dai ido aka zuba mishi aga gudun ruwan shi,sai dai a jiya ba karamin mamakin Umar Farouq din suka sha ba don ba Wanda ya taba tunanin zai yi abunda yayi..

Da dare Abba Na third floor sanye da glass yana karanta magazine Aunty ko coffee ta hada mishi tana mika mishi sai suka ji anyi knocking Na kofar falon tare da sallama a lokaci guda,duk da ciki ciki yayi sallamar sun shaida muryar shi shiyasa Abba hade rai sannan yace

"Shigo". A hankali ya shigo sanye yake cikin plan trouser black sai rigar shi da take armless as usual Fara da slippers Mai kyau dake kafar shi,a hankali yake shigowa cikin falon inda Aunty Hauwa ta zuba mishi ido tana kuma kare mishi kallo tsam bai da hayaniya,yana karasa shiga ya zauna kan kujera daya dake cikin falon kan shi a kasa yace

" Barka da dare Abba".

"Uhum". Kawai yace sai yayi sipping Na coffee din shi

" Barka da dare Aunty Hauwa ".

" Ka fito lafiya ".a saman labban shi ya amsa da lafiya daga nan shiru ne ya biyo baya sai ya maida hankalin shi kan TV, tsarai Abba ya fahimci da magana a bakin

shi ya rasa ta yadda zai Fara ne Amma sai yayi kamar bai gane ba,Aunty Hauwa ce tace

" Umar Farouq takardar me ne Ka kawo".dama abun nema ne ya samu a wajen shi nan ya mika Mata takardar dake cikin envelop nan ta fiddo su tare da Mikawa Abba suna kallo a tare,a tare kuma suka daga ido suna kallon shi cike da mamaki Abba yace

"Million Hamsin da bakwai fa Umar Farouq".kan shi a kasa yace

" Abba takardar Na gida ne kuma jiya Na saya duba da dawainiyar da Kayi shiyasa Na saya gidan da Kai Na".duk basu taba tunanin zai saya gida ba, ba Wai kuma don baida kudin bane a'a saboda basu ga alamar yana son auren ba bare har yayi sha'awar zama da ita.. so yake ya tafi Amma kuma bai gama zancen shi ba shiyasa ya dubi Aunty yace

"Aunty Hauwa a sanar da mom gidan is set zasu iya zuwa Jere". Yana gama fadin haka bai jira amsar kowa daga cikin su ba ya mike tare da nufar kofa yana fad'in

" sai da safe".sannan ya rufo musu kofa yayi gaba,Aunty Hauwa ko dariya tayi sannan tace

"Kaga Alhaji Ka bamu matar mu tunda Mun Fara nuna interest a kan ta". Shima murmushi yayi yace

" Wai ni Umar Farouq zai maida yaro,to Wa ya fi wayo ya saya gida Harda cewa aje ayi Jere Wato don a bashi Mata Ai ko yanzu aka soma wasar sai ya bude baki yace a bashi ita tukun".

"A'a in dai adalci za'a yi wallahi daga abunda muka yi ma an San muna son matar mu gida Na million hamsin da bakwai fa muka saya". Ajiye magazine din hannun shi yayi inda ya mike ya nufi bedroom yana fadin

" in dai kudi ne yanzu kuka Fara kashewa don yarinya da gatan ta sai ki dauki takardun gidan ki Adana muku in kun samu lokaci sai kuje kuga gida ke da su Nana kan su koma ".yana gama fadin haka ya shige ciki ita ko abubuwan da yayi amfani da su ta dauka ta Kai kitchen tana dariyar Umar Farouq ita daya don bai San yadda suka yi niyar bashi wahala ba..

Koda ya fita a bangaren Abba a hankali yake saukowa downstairs din yana kuma juya wayar shi a hannun shi,ji yake kamar akwai abu Mai amfani da ya manta bai sanar musu ba ba iya zancen gidan bane Amma ya rasa mene ne Gashi kirjin shi ya mishi nauyi alamar akwai abunda ke damun shi Amma ya Gaza gane mene ne,a haka har ya karasa sauka ya nufi kofa gaba daya hankalin shi yayi nisa a tunani Wai ko zai iya tuno abunda zuciyar tashi ke so

" Ya Farouq ".Nana dake sanye cikin sleeping dress Mai nauyi ta Kira sunan shi,tsayawa yayi ba tare da ya juyo ba nan ta karasa wajen shi tare da dafa dantsen hannun shi

" kallo daya Na maka Na San kana cikin damuwa,akwai abunda kake son kasance da shi wanda kake jin kamar shine barin jikin Ka Amma baka San mene ne bane,Ka nitsu Kayi tunani zaka fahimci abunda kake so Ka daina wahalar da kan Ka".tana gama fadin haka ta wuce shi tare da nufar upstairs tana murmushi ita daya,shi ko ya Kai minti biyu tsaye a wajen sannan ya nufi fita,Nana Yar uwar shi ce kuma kanwar shi ce a lokaci daya kuma abokiyar shi don Tun suna yara ta kan fahimci abunda yake so kan bakin shi ya furta shiyasa ko kadan bai yi mamakin yadda aka yi ta gane me yake ji ba,yana gab da shiga bangaren shi ya hadu da Salman

"Ya Farouq,ya Bash yazo yana bangaren Ka". Da Kai ya amsa sannan ya zura hannu a aljihu ya cigaba da shiga Bangaren a falo ya tarar da Bash kwance, kafar shi ya buge sannan ya nemi waje ya zauna da sauri Bash ya tashi

" wani salon wulakanci ne wannan daga yin Aure sai Ka Fara mana iskanci ".Kala bai ce da shi ba nan Bash ya gyara zaman shi yace

" batun office ne Ka San an baka hutun sati daya kuma kana Komawa maybe da two weeks zaka tafi Dubai in ba'a yi sa'a ba sai cikin azumi zaka dawo don haka nazo Na baka shawarar Tun wuri kace musu kana son matar Ka a baka Ka more sadakin Ka ko Na sati biyu ne kan Ka tafi".wallahi bai taba jin haushin aikin shi ba sai wannan Karon ya kuma rasa dalilin da yasa shi jin haushin tafiyar da zai yi ba jimawa

"Kayi shiru Ince Ka saya gida me ya rage".

" babu".sosai Bash yayi mamakin furucin nashi don a zaton shi zai yi banza da shine yadda yayi da farko,wayar Bash ne ya Fara ringing nan ya amsa call din Bayan ya gama sai ya ajiyewa Umar Farouq din wani envelope Wanda Na aikin su ne sannan ya bashi hannu suka gaisa

"Ni Na wuce Hajiya ta Na nema Na". Daga nan ya fice ajiyar zuciya Umar Farouq ya sauke sannan ya Dan kwanta jikin kujerar tare da rungume filo gaba daya ji yake kamar bashi bane wani ne daban,wayar shi ya Ciro a aljihu yana son bin umarnin zuciyar shi shiyasa ya lalabu number'n Laylerh ya Fara Kira sai dai har ta katse ba'a daga ba take kuma ran shi ya sake baci nan ya nufi bedroom tare da dauro alwala ya kwanta sai dai me zai faru tsam bacci yaki daukar shi sai uban tsaki da yake ja karshe mikewa yayi ya Kama nafila tunda bacci ya gagara..

A bangaren Laylerh ko suna rayuwa cikin farin ciki duk da Muhammad har yanzu bai zo ba Sulaiman ko bai koma taraba ba yanzu ta sake da Sulaiman su kan zauna su sha hirar su yanzu ma duk zaune suke a falon mommy Sulaiman ita ko tana kitchen abinci ta kawowa Sulaiman nan ta ajiye mishi

" thank you amarya ". Kwabe fuska tayi tace

" Nifa nace bana son sunan nan".murmushi yayi sannan yace

"To a mini afuwa zo muci". Daga nan zama tayi suka Fara cin abincin tare Aunty'n Laylerh TV take kallo sai Mommy Sulaiman ne ke ta buga lissafi su ukun suna taba hira a haka wayar Laylerh dake ajiye a kasa ya Fara ringing tana ganin sunan ta cire Kai

" Laylerh kiran ki fa ake yi".Cewar Sulaiman

"Shine fa". Daga nan shiru suka yi sai mommy Sulaiman ne ke kallon wayar kamar Umar Farouq din take kallo har kirar ta katse akai akai take Satan kallon Laylerh don a tunanin ta zata ga sauyi a fuskar ta sai taga ko a jikin ta sai ma hira kasa-kasa da take yi da Sulaiman

" Allah yaya zaku dace bata da matsala fa kuma ni Tun ranar da Na San Kai yaya nane Na maka sha'awar Nabeela ".

" Nifa bata mini ba".baya ta bashi tana fadin

"Shikenan tunda har Kawa ta kake cewa bata maka ba kuma daga yau ba ruwa Na da Kai".

" Kinga to zo muyi magana dama Aji nake ja muku".da wuri ta juyo tana murmushi

"Kai mace ce da zaka ja mana Aji, Yauwa nikam ina Neerat ne Mommy Na Na school budurwa Ka?"

"Ni Tun a lokacin Na manta da ita". Daga haka wayar shi ta dauka tare da sa number'n Nabeela sannan ta mishi saving da final choice haka suka yi ta hira har suka shiga..kwanciya mommy Sulaiman ke kokarin yi sai Aunty'n Laylerh tace

" yaya Niko sai nake ga kamar gwara a Fara shirya laylerh Tun yanzu tunda ta kusa tarewa bamu San yadda Allah zai yi ba kila ta tare kafun lokacin da muka tsara".fasa kwanciyar tayi Tasa glass a idon ta tace

"Wannan gaskiya ne Bari zanyiwa matar malam magana kila ta iya sai mu bata wannan damar kada tace ba'a Mata adalci ba". Kiran sunan Baaba da tayi sai ya tuna Mata irin wulakanci da ta Mata lokacin da tazo gidan su shiyasa tace " hmm".

"Ya dai".nan ta labartawa Yar uwar ta abunda ya faru sai tace

" bar su Ai duk Zan gayyace su in laylerh zata tare kuma sai nayi maganin su".

"A'a yaya abunda ya wuce ya wuce bakon Ka fa annabin Ka ne".

" Kinga kwanta kiyi bacci gobe Zan yiwa hajja kande magana sai a samo mini Mai gyara ta sai su Fara da dilka".

Kamar yadda ta fada Washe gari aka samo Mata Wata Yar Maiduguri nan aka Fara shirya Laylerh sosai kuma ta Fara canzawa inda Sulaiman ke sata a gaba yana tambayar ta shima in aka yiwa matar shi zata yi kyau haka ta kan ce mishi Ehhh..

Abu wasa gaske sai ga Umar Farouq ya rasa sukuni duk ya dawo wani Kala da Ka mishi magana kuma sai ya fusata a take yanzu ma Yaron Nana ne ya sa shi a gaba duk da kaunar Yaron da yake yi sai ya buga mishi tsawa

"Ba nace Ka Bari bane". Tunda Yaron yake da kawun sa bai taba mishi tsawa ba shiyasa ya fashe da kuka gaba daya jikin sa Na rawa da wuri Nana Tasa hannun ta dauki Dan ta tare da sa shi a kafada tana jijjiga shi ji take ita ma kamar tayi kuka don sosai take son Yaron

" ya Farouq yaro ne fa ba abunda ya sani"..cikin tsawar da yasa falon amsawa sannan duk sanda hanjin su ya kada Salman kam fitsari ne kawai bai yi ba inda Aunty Hauwa ta zuba mishi ido yace

"Ki rufe mini baki ko jikin ki ya gaya miki bar ganin kina da Aure wallahi ba ruwa Na duka Zan miki kuma maza ki shirya ki koma tunda an gama bikin". Yana gama fadin haka ya fice a falon duk da ido suka bi shi Anya ba'a canza musu yayan su ba kuwa don yayan su ba haka yake ba,Aunty Hauwa ce ta karaso inda Nana ke tsaye ta karbi Yaron sannan ta dafa kafadar Nana tace

" nashi ba irin naku bane,kada kiji komai".hawaye Na zuba a idon ta tace

"Na sani wallahi Aunty Na sani matar shi yake da bukata Amma jin Kai ya Hana shi bude baki ya fada wannan dalilin yasa nake tausayin shi".

" Nana kada ki damu a hankali sirrin zuciyar shi zai fito sai dai in bai dame shi bane".

"Kinga Bari naje Na karasa shiri tunda dama da yamma miji Na zai zo ya dauke ni kada ya mini duka kamar yadda ya fada". Duk murmushi suka yi su Yasmeen dake zaune a dining kuma har yanzu jikin su bai daina rawa ba saboda ko su bai taba musu wannan tsawar ba sai yaro karami da ba abunda ya sani..

Yana fita sai huci yake kamar mayunwacin Zaki direct toilet ya fada tare da sakarwa kan shi ruwa nan ne yaji dama dama,yana fitowa ya dauki jumper'n shi sky blue yasa Amma bai sa hula ba sosai yayi kyau sai takalmin shi irin Na sarauta nan ya fece jikin shi da turare masu dadi sannan ya dauki key'n mota ya fito shi kan shi bai San ina za shi ba..

Ya jima a cikin motar kan ya tayar Ai ko bai tsaya ko ina ba sai kofar gidan su Laylerh nan yayi horn Mai gadi ya leka,hannu ya mika mishi

" samari ban shaida Ka ba".Kai tsaye yace

"Nine mijin Laylerh". Washe baki Mai gadi yayi tare da bude mishi gate din ya shiga Bayan yayi parking gate man ya rufe gate sai ya dawo Gare shi

" ko zaka mini iso?"yana Washe baki yace

"To To" sannan ya nufi ciki a hanya suka hadu da Sulaiman

"Yauwa kaga mijin laylerh ne yazo Wai Na mishi iso". Ba karamin mamaki Sulaiman yayi ba nan ya leka sai yaga bakuwar mota

" kaje Bari Na mishi iso".daga nan Sulaiman yayi ciki Mai gadi kuma ya fito yana Washe baki yace

"Yayan ta yaje maka iso". Hannu yasa a inda yake ajiye kudi nan ya Ciro masu yawa ya Mikawa Mai gadi take kuma ya Fara godiya kamar ba gobe sannan ya koma bakin aikin shi..

Sulaiman ne ya fito nan ya nufi motar Umar Farouq,glass Umar Farouq ya sauke nan ya mika mishi hannu fuskar Sulaiman a sake yace

" bismillah ".daga nan ya fito a motar Sulaiman Na jinjina haduwar shi suka nufi ciki..

A falo suka tarar da Mommy Sulaiman nan ya zauna a kasa kan shi a kasa yace

" sannu da hutawa Mom ".kallon tsab ta mishi kamar ba Yar ta yake Aure ba sannan tace

" Yauwa ".Sulaiman ko yana zaune a sama yana kuma tausayawa Umar Farouq don bai San wace ce Mom ba

" Mun wuni lafiya ".

" lafiya kalau ya gidan naku?"

"Duk suna lafiya". Daga haka shiru ne ya biyo baya Mommy Sulaiman ta cigaba da aikin ta a laptop shi ko sai raba ido yake kamar Mai Neman wani abu,can Aunty'n Laylerh ta fito ita ma cike da girmamawa ya gaishe ta sai ta koma ciki..

Dama duk suna falo tunda Sulaiman ya shigo yace Umar Farouq yazo Mommy Sulaiman tace

" Ai Na San za'a yi haka laylerh wuce daki kada ki kuskura ki fito sai ya tafi".mikewa tayi ta nufi daki inda a can suke zaune da Aunty'n ta yanzu da ta gaishe shi ta koma sai suka cigaba da hirar su ita Laylerh ko a jikin ta..

A can falo kuma duk shiru suka yi bai sake cewa komai ba ganin haka ne sai Mommy Sulaiman tace

"Umar Farouq wani abu kake so ne?" Wannan tambayar sanda yaji kamar yayi ihu shiyasa ya girgiza Kai yana fad'in

"A'a nazo ne mu gaisa ni Na wuce". Daga haka ya mike ran shi a matukar bace ya kuma rasa dalili a haka Sulaiman ya raka shi mota Allah ne kadai ya Kai shi gida lafiya..

Ai fadawa yayi a gado yana jin gaba daya duniyar ta fita a ran shi ya kuma rasa dalili tabbas zuciyar shi Na son wani abu Amma mene ne wannan abun..

A can bangaren su Mommy Sulaiman ko yana fita tayi murmushi Bayan Aunty'n Laylerh ta fito

" Amina wallahi har yanzu Yaron nan bai San ni bane sai ya dubi ido Na yace Na bashi Laylerh tukun Zan ba shi".murmushi kawai ita ma Aunty'n Laylerh tayi..

Duk da an bashi hutu sai Gashi ya koma zuwa wajen aiki ko zai samu nitsuwa Ai ko kowa yayi mamakin ganin shi nan Bash yayi ta mishi tsiya Wai ango ba amarya wannan abun ya Kara harzuka shi sai Gashi Wai yau shine bai iya aikata komai ba koda aka tashi sai suka hadu da Bash a wajen daukar mota nan ya shiga motar Bash sai kuma yayi shiru ido Bash ya zuba mishi ya kuma yi alkawarin sai dai su kwana a haka in har Umar din bai yi magana ba shima ba zai yi ba can yaja tsaki yace

"Bash wallahi ina cikin damuwa kirji Na Zafi yake Gashi ya mini nauyi ina ji a jiki Na akwai abunda nake so Wanda in ban samu ba Zan iya hauka Tun Randa aka daura mini Aure da Laylerh ban sake bacci ba har Rana Mai Kama ta yau,ta farko nayi tunanin abun zai zo da sauki Ashe tsam ba haka bane Mom nata akwai kafiya Gashi Abba kam nunawa yake kamar ya manta da zance Na wallahi damuwa ta mini yawa".yana kaiwa nan yayi ajiyar zuciya don zai iya rantsuwa wannan shine Karo Na farko da ya sanar da wani damuwar shi..

Kallon shi Bash yayi fuskar shi dauke da murmushi yace

" ko ba komai zaka ji sauki tunda Ka fitar da abunda ke ranka Umar Farouq wannan abunda kake so ba komai bane face matar Ka Laylerh wacce a tunanin Ka damuwa biyu ne a zuciyar Ka tsam guda daya ne,Kai din ne da ban haushi kake Ka fiya kyaliya da nuna abu bai dame ka ba waya ce maka Ana yiwa mace haka? Wannan kyaliyar taka ita taja maka don yana Mata Zafi har iyayen ta Kai harma naka iyayen shiyasa suka cire ido a kan Ka".kallon Bash yake kamar Wanda ya samu TV Anya kuwa Laylerh ce. Kadai zuciyar shi ke so da har ya mishi nauyi

"Ka ajiye jin Kai kaje kace da su kana son ta a baka zai fi maka". Tsam zuciyar shi taki yarda da cewa Laylerh kadai yake so duk da wani bangare ta aminta da haka shiyasa ya fita a motar ba tare da yace da shi komai ba ya koma nashi motar nan ya nufi gida..

Koda yazo kwanciya kalaman Bash sai dawo mishi suke a hankali kuma ya Fara samun nitsuwa tare da sakin murmushi

" fine tunda ita zuciya ta ke so Na San abunda Zan yi".haka kawai yaji nishadi nan ya fita ya nufi cikin gida a second floor ya tsaya inda ya nufi bangaren Aunty Hauwa luckily for him tana ciki don Abba bai dawo ba..

"Sannu da aiki Aunty Hauwa". Sosai take kare mishi kallo duk da ba murmushi yake a lokacin ba Amma annurin fuskar shi ta yau daban ce

" Kai ma sannu da shigowa ".shiru yayi can kuma sai yace

" Aunty Na San kin sani tunatarwa kawai Zan miki kan cewa bai dace Bayan an daurawa budurwa Aure a maida ta gidan su ba gidan miji ya kamata a Kai ta ko a addinan ce Amma taya za'a ce fiye da sati da yin Aure yarinya Na gidan su".ido ta zuba mishi kamar yau ta Fara ganin shi..

Niko nace yau Umar Farouq ya zama sheikh Harda wa'azi😂..

Sanda ta gama mishi kallon mamaki sannan tayi murmushi tace

"Ina Umar Farouq".da sauri yace

" gani a nan"sosai ya bata dariya Amma sai ta danne sanin suna good times da shi

"To Ka saurare ni da kyau wannan wa'azin surkuwar taka ya kamata kaje Ka Mata saboda ita ce tace sai Bayan azumi Laylerh zata tare". A bazata taji yace

" Bayan azumi Na shiga uku Na lalace ni Umar Farouq ".

Team Umar Farouq kunga so ake a zautar muku da shi😂😂😂

Comment

Share

©Hafciey Musa

[1/25, 5:44 AM] Hafciey Musa😘: *□LAYLERH□*

(The prettiest emerald)

Page 48

Jikin Bappa Dalha fa tsam yaki don abun sai gaba yake yi bakin baya rufuwa sai dai kaga yawu na bin jikin shi sai kaga ya jika Riga da yawu a inda yake din kuma zai kwanta yayi fitsari da Kashi Tun uwar gidan shi mahaifiyar Sadiya Na hak'uri har abun yafi karfin ta tunda daidai da ruwa sai an bashi a baki Gashi yana sha yana zuba, zuwa yanzu ko yayi Kashi bata fiya kula shi ba sai dai tayi ta aikin gaban ta shiko Kuda yayi ta bin shi yanzu ma Kashi yayi so yake ya toshe hancin shi don wari Amma ba dama jiki duk ya shanye ga idanun shi da a ko yaushe ke Zubda ruwa..sanda ta gama wanke-wanke sannan ta nufe shi

"Amma Dalha wallahi kaci duka yanzu Kashi Kayi, Na rantse da Allah in baka maida hankali a jikin Ka bain Ka cigaba duka Zan ke maka don ni ba jakar Ka bace". Haka taci gaba da mishi holo kamar Yaron ta shi ko da ido kawai yake bin ta Wai yau shi Dalha ne ya zama haka har take fada mishi abunda ranta yake so Gashi duk yaran shi sun guje shi..a haka har ta cire mishi kaya a wajen sannan ta wanke shi nan Tasa mishi wani Kayan sannan ta dube shi tace

" Ka saurare ni da kyau Zan daina baka abinci tunda shi ke saka Kashi don ba Zan iya ba nayi Na yaran Ka nayi naka".Wayyo rayuwar shi haka ta karashe mitar ta tayi ciki ta bar shi a wajen..

**

Kallon shi Aunty Hauwa ke yi tana kuma murmushi can kasa-kasa Wai ya shiga uku ya lalace to Ai kadan ma ya gani..jin taki cewa komai a hankali ya mike yana jin zuciyar shi Na tafasa Gashi duk hucin da yake fitarwa da Zafi yake fita da kyar ya samu ya nufi bangaren shi nan ya fada kan gado tare da kiran layin Laylerh sai dai as usual bata dagawa..

Washe gari sai da kyar ya iya tashi yayi sallar Asuba saboda zazzabi da ya buge shi,a dafe ya idar da sauri ya koma kan gadon gaba daya jikin shi ya dau Zafi Gashi rawan sanyi yake yi so yake ya kashe Ac Amma baya jin hannun shi zai iya motsi,wannan zazzabin da ya sauka mishi ba karamin daga mishi hankali yayi ba don ya mance rabon da yayi ciwo sai Gashi zazzabin Na Neman maida shi nakashesshe tunda baya iya motsa hannun shi..

A can cikin gida kuma yanzu Abba ke shirin fita hular shi Aunty Hauwa ta mika mishi tana fadin

"Jiya da dare mutumin Ka ya shigo Harda wa'azi ya mini". Nan ta fada mishi yadda suka yi da Umar Farouq din fuskar ta dauke da murmushi ta kare zancen

" da nace mishi ance sai Bayan azumi zata tare Ka San me yace?"Kai ya girgiza Mata shima murmushin yake yi sai ta cigaba da dariyar ta harda dafa kafadar shi

"Cewa yayi ya shiga uku ya lalace". Haba me Abba zai yi banda dariya Mai sauti haka suka yi ta dariyar shi sosai kalman ke basu dariya karshe dakatawa da dariyar yayi yana kallon ta..ta gama mishi komai Na rayuwa tunda ta kula da yaran shi da uwar su ta Bari kuma duk da zagin ta da aka yi a auren Umar Farouq d'in Wanda shima yayi nashi tsam bata rike abun a ran ta ba,gaskiya samun yadikko irin ta Na wuya sai dai halin ta baya rasa nasaba da sunan ta saboda masu suna Hauwa suna da hak'uri sosai..sanda tayi Mai Isar ta sannan ta dube shi ganin yadda ya zuba Mata ido ya sata cewa

" Alhaji lafiya kuwa?"Kai ya girgiza Mata sannan yace

"Ni Zan wuce kuma ba Zan nuna mishi Na San da ya same ki ba". Daga nan ta mishi rakiya ko da suka fita sunga duk motocin Na nan alamar bai fita ba Amma basu kawo komai a ran su ba nan ya tafi ita ko ciki ta koma..

A falon ta tarar da Hajara,Najeeha, Yasmeen sun zuba hotunan Aure da aka dawar yanzu a falon suna kallo nan ta zauna cikin su suna kallo tare

" Aunty wallahi Laylerh fa musulmin kyau Gare ta sai Ka nitsu zaka gane ba irin Aunty Sadiya ba kallo daya zaka Mata Ka fahimci tana da kyau".Cewar Najeeha lokacin da ta dauko wani hoton Laylerh ita daya a filin budan Kai kan ta a kasa,dakuwa Aunty Hauwa ta Mata tace

"Ai Shikenan kuma kun samu fuskar raina ta tunda ya auro sa'ar Ku ko ma wacce kuka fi kadan zancen, ce Mata Aunty ma bai taso ba ko?" Ta kare zancen da alamar tambaya duk shiru suka yi

"Batun Sadiya kuma Ai kyan Dan maciji ne da ita". Yasmeen ta fadi

" daga Rana Mai Kama ta yau kada Na sake jin Kunce Mata Laylerh, Kai in kunga dama Ku fada shi yayan naku Ai yana nan daidai da ku".daga nan hotuna suka cigaba da kallo..

Bangaren su Laylerh kuma sosai tayi kyau duba da dilka da ake Mata a yau ne kuma Mommy Sulaiman ke sa ran Kayan daki da tayiwa Laylerh order zasu iso,falon yau a cike yake don su Teema sun shigo sai hira ake Harda Sulaiman da Laylerh ke kokarin maida shi yaro sa'an ta karfi da yaji,Teema ce ta dubi Laylerh on a serious note tace

"Laylerh har Na tuna primary school namu,kin tuna wannan mugun head boy da ya more ki Kai Allah ya Isa miki". Duk yadda Laylerh ke girgizawa Teema Kai tsam bata dago ba nan ta cigaba

" shege Gashi kato a cikin mu sai cin Zali da shegiyar budurwar shin can gaskiya ni duk inda yake ba Zan daina ja mishi Allah ya Isa ba,kila yanzu yayi Aure Allah sa Mata Mai dukan shi ya aura".ganin bata da niyar dainawa yasa Laylerh rufe Mata baki ita ko sai ido take zarewa so take Laylerh ta sake ta ta cigaba da maganar ta shi ko Sulaiman kallon su yake yaso a barta yaji karshen zagin da zata mishi

"Ke ki nitsu wancan headboy d'in ba kowa bane face yaya Na Sulaiman". Da sauri ta daga ido tana kallon shi shima ita yake kallo yayi kicin-kicin da fuska ji yake kamar ya rufe ta da duka

" wallahi shine".nan ta shafa Mata komai Ai Tun Laylerh bata Kai Aya ba ta fice a falon da gudu don kunyar ahalin Laylerh din da ya kamata su Hanan kuma dariya suka sa shi ko sai hararar Laylerh yake yi kamar ita ce tayi zancen

"Kaga Sulaiman ina ga Kayan ya iso kazo kaje Ka dauko su". Mikewa yayi yana cigaba da hararar Laylerh nan Mommy Sulaiman ta bashi number'n su ya fice cike da takaici..

" Amma Teema in ta shiga hannun shi zata ji jiki".Cewar Laylerh

"To uwar surutu Kinga zo ki dauki maganin ki ki sha". Mommy Sulaiman ta fadi lokacin da ta mike ta shige bedroom Laylerh ko da sauri ta taso ta Isa gabab Aunty'n ta dake zaune a kujera kamar zata yi kuka tace

" Aunty kicewa Mommy maganin ya Isa haka ba dadi ne da su ba".

"A'a gwara dai mu gyara ki kada ya jiki ba test". Tana jin Aunty'n ta har ranta don har yau kallon uwar da ta haife ta take Mata shiyasa ta rike hannun Aunty tana girgiza Kai tace

" ba wani gyara ni ya ishe ni haka tunda ni din ba bazawara bace kuma ma ni ko naje ba abunda zai mini".ta karashe zancen ko a jikin ta tunda dama ba boyewa juna abunda ke ran su suke yi ba

"To naji ba abunda zai miki karbi ki sha". Ta kare zancen da murmushi

" Allah ko Aunty in yace zai gwada mini karfi ihu Zan mishi Na Tara mishi jama'a tunda ba'a dole".ganin in ta biyewa zancen Laylerh sai tayi abun kunya tunda ita babba ce shiyasa tace

"Haba laylerh'n Aunty'n ta ki sha ni nan zanji da komai Ai tare zamu tare ta ina zai miki komai". Haba ba sai dadi ya rufe ta ba tunda da Aunty'n ta zasu je nan take ta sha Aunty Na sa Mata albarka nan taje tayi na wanka wayar ta kam ko inda yake ma bata sani ba..

Babu jimawa sosai Sulaiman ya dawo tare da Kayan,Masha Allah kaya kam ko ba'a fada ba Ka San an kashe kudi Laylerh fa Yar Gata ce a gidan aka ajiye kan a karbi key a hannun uban gayyan..

" Kinga taso muje muyiwa Mom godiyar Kayan daki da ta saya mana".

"A'a Aunty Kije ke daya in ba haka ba cewa zata yi ina son tafiya ne". Ta gamsu da zancen Laylerh hakan ce ta kasance ita Mommy Sulaiman ko har mamakin yadda take gode Mata tayi kace alfarma aka Mata lallai duk da Laylerh bata sha nonon Amina ba ta tabbatar kaunar da sukewa junan su Na gaskiya ne ta kuma yi alkawarin a koda yaushe zata bar Amina a matsayin mahaifiyar Laylerh tunda ita ma bata da 'ya mace

" Kinga bar godiyar nan haka yanzu ma Na Fara shirye-shiryen tafiyar mu can Bauchi mu nemo Dalha wallahi duk kudin da yaci sai ya dawo muku da hakkin Ku ke da Muhammad bai San dawa yake zance bane".

"A'a yaya Hadeeza abar wannan maganar sai Laylerh ta tare". Duk yadda Mommy Sulaiman tayi da ita kin yarda tayi a Cewar ta sai Laylerh ta tare don shine Babban burin ta yanzu dole ta hakura..

Bangaren Umar Farouq ko har yanzu zazzabin ba ko alamar zai sauka, cikin gida ko jin shiru ko breakfast bai nema ba Gashi har azahar tayi yasa Aunty Hauwa tunanin ko fushi yake shiyasa tace Bari taje ta rarrashi Dan ta nan ta nufi bangaren shi..

Da yake jiya a fusace ya shigo shiyasa tura kofar dakin kawai yayi bai rufe ba hakan ya sata shiga tana karewa falon kallo da alama yau mutum bai fito cikin sa ba..kofar bedroom d'in ta nufa tayi sallama Amma shiru sau uku tana sallama taji shiru sai dai bata jin zata iya shigewa bedroom nasa Kai tsaye shiyasa ta Kira Salman a waya ba jimawa kuma sai Gashi yazo

" kaga Salman shiga Ka dubo mini ko Umar Farouq Na ciki".to yace sannan ya nufi bedroom din bakin sa dauke ta sallama,sosai ya tsorata ganin yayan nasu kwance sai rawan sanyi yake da alamu ko wanka yau bai yi ba Tun Kayan shi Na jiya ne a jikin shi,cikin daga murya yace

"Aunty ki shigo Gashi nan ba lafiya". Ba tare da bata lokaci ba ta nufi dakin Ai ko sosai tausayin shi ya kamata nan ta taba jikin shi taji da Zafi

" kaga Kira Abban Ku Ka fada mishi".ita gaba daya ta rasa abunda zata yi sai jikin ta da ya hau rawa Abba Na picking yace

"Abba Ka dawo ga ya Umar ba lafiya". Duk da yana da meeting nan da minti goma sai ya bar abun saboda rayuwar Dan shi ya fiye mishi nan ya nufi gida hankalin shi a tashe..

Koda ya iso Aunty Hauwa ta rufe shi da bargo Amma duk da haka bai daina rawan sanyi ba,sanin bashi da yarda shiyasa bai barin family Doctor ya mishi wani abu yasa Abba kiran Bash yace ya samo musu doctor yanzu ga Umar ba lafiya..

Sosai shima Bash hankalin shi ya tashi jin Umar Farouq ba lafiya nan ya nemo mishi Likita don shi Umar Farouq ya yarda sai da Dan gari ake cin gari da yaki shiyasa gwara a nema mishi Wanda bai San shi ba ya duba shi tunda in ya tafi ba dawa zai yi ba..

A tare Doctor da Bash suka shigo nan aka tarar da iyalan gidan hankalin su a tashe duba shi yayi inda yace ba wani matsala zazzabi ne kawai nan ya mishi allura ba jimawa kuma sai Gashi yayi bacci...

Bash ne ya sallami Doctor inda ya dawo bedroom din yace" ba komai Abba zaku iya tafiya Zan Lura da shi".jikin su a sanyaye suka fice shima falon ya dawo ya zauna..

After 3 hours!!

Wani gumi ne ya keto mishi Wanda hakan Na nufin zazzabin ya sauka shiyasa ya tashi duk da jikin shi ba kwari sai ya nufi toilet jin shi yake kamar ya kwana biyu bai yi wanka ba,jin motsin shi yasa Bash lekowa sai ya tarar ya shige toilet don haka Salman ya Kira a waya yace a kawo mishi abinci ya tashi..

Daga Abba har Aunty Hauwa dawa dakin suka yi don dama hankalin su ba a kwance yake ba sun tarar da shi yana sallah dole suka jira ya idar,a bakin gado ya zauna nan suka shiga jero mishi ya jiki ya amsa sannan aka bashi abinci.. Gaba daya yayi loosing appetite nashi shiyasa kadan yaci duk da yana jin yunwa daga nan kuma ya kwanta su ko suka fita ya rage daga shi sai Bash..

"Dude ya jiki?" A saman labban shi ya amsa

"Da sauki". Shiru ne ya biyo baya sai can Bash yace

" Ka sha wani abu ne da aka Daura maka Aure har ya saka zazzabi don an Hana Ka matar Ka?"ya kare zancen cikin gaskiya da gaskiya baya kuma kallon Umar Farouq din,da farko yaso yayi banza da shi sai kuma ya tuna kila kowa kallon da yake mishi kenan shiyasa can kasa-kasa cikin muryar marasa lafiya yace

"Tsam ni ba sha'awar Laylerh nake ji ba kawai ina son kasancewa da ita ne a gida daya matsayin Mata da miji".

" to me zai Hana Ka ajiye shi jin Kai din Ka fada musu kana son ta".

"Ba zaka gane bane Bash sun dau abun da Zafi". Ya kare zancen yana gyara kwanciyar shi

" to ba dole ba Ka nuna tsana ga Yar su".

"Allah shaida ne kuma ita ma Laylerh shaida ce ban taba nuna Na tsane ta ko Na Mata wani abun muzgunawa ba,sau biyu Na taba Marin ta Wanda shima banda option da ya wuce hakan ne lokacin da take mini bincike Amma ban mare ta don tsana ba,Na yarda in ance bana kula ta Amma Ai Mai hankali zai fahimci ina son ta". Da wuri Bash ya juyo Gare shi jin ya kare zancen da cewa yana son ta

" to meyasa ba zaka fada Mata cewa kana son ta ba?"

"Sun toshe duk Wata kofa sannan ita ma sun hure Mata kunne bata picking call Na,wallahi wallahi ko su bani ita ko nayi abunda basu so don sai Na dirka Mata ciki a waje naga ta tsiyar su". Sosai ya bawa Bash dariya shiyasa ya Fara dariya yana kallon shi Harda tafi yace

" Ince yanzu Ka gama cewa ba sha'awar ta kake ji ba".cikin kufula bai San lokacin da zancen ya fito ba yace

"To don uban Ka naga ba haramun bane in naji sha'awar ta din?ta ina ma aka taba so ba sha'awa ni fa tunda Na fito a matsayin mutum suna son walakanta ni shiyasa zanyi abun kunya, ni son ta nake Amma sun gagara fahimta Ai ko har gidan zanje nayi abun kunya inyi tafiya ta".

" kaga Ka rufa Mata asiri naga mahaifiyar ta akwai Zafi mu bi komai a hankali yanzu in Ka warke sai mu samu Abba ".

" kaga in zaka raka ni Anjima sai muje don Na warke"..

A can cikin gida kuma sun gagara gane dalilin zazzabin nashi duk da suna zargin kila don ance sai Bayan azumi ne shiyasa ma suka gagara nitsuwa kada fa su rasa shi tunda akwai alamar ba zai bude baki yayi magana ba jin Kai ya Hana shi..

Suna a haka ne Mommy Sulaiman ta Kira su kan cewa Sulaiman Na hanya zai zo ya karbi key'n gida don ayi Jere da to Aunty Hauwa ta amsa tunda key din a wajen ta yake sai dai bata ce musu baya jin dadi ba..

Hakan ce ta kasance a gate Sulaiman ya tsaya aka Kai mishi key nan ya juya ya nufi gida..

Koda dare yayi Bayan Abba ya shigo duba shi har zai fita sai Bash yace

"Dan Allah Abba in ba zaka damu ba akwai maganar da zamu yi". Komawa yayi ya zauna tare da fadin

" ina sauraron Ku".

"Yauwa Abba dama alfarma muke so a mana ta hanyar bamu Laylerh". Kai Abba ya daga yana kallon Umar Farouq sai kuma yayi tsaki yace

" in dai wannan maganar ce kaga tafiya ta tunda shi baida bakin magana ".har yasa Kai ya tsinkayo muryar Umar Farouq

" to Ai Abba ya Ari baki nane yaci mini albasa Dan Allah a bani ita".ya kare zance murya Na rawa cike da kunya kuma,ba tare da Abba ya juyo ba yayi murmushi sannan ya fice yana jin Umar Farouq Na fadin

"Don Allah ba don hali Na ba Abba". Ya kare zancen kamar zai yi kuka Bash ma jikin shi yayi sanyi..

Bayan kwana biyu!!

A yau za'a je yiwa Laylerh Jere ba wani gayya da suka yi tunda masu aiki a company'n da aka yi Kayan ne zasu hada komai daga Aunty'n Laylerh sai Hajja kande da kuma Sulaiman suka nufi gidan Ai ko sun yaba da tsarin gidan sosai nan suka Fara abunda ya Kai su..

A bangaren Umar Farouq ko jin Abban shi yayi shiru Gashi ya warke sai ya nemi number'n Mommy Sulaiman sai juya wayar yake a hannun shi yana son kiranta karshe dai ya Fara dialing ya jima yana ringing kan ta dauka ganin sabuwar number

" Assalamu Alaikum Mom ina yini".Mom ta maimaita a ranta to wane ne shi

"Lafiya". Shiru ne ya biyo baya can tace

" Ka Kira kuma Kayi shiru wake kan layi".murmushi yayi a bangaren shi tare da gyara rikon da yayiwa wayar yace

"Ayya dama Na San ba zaki gane ba mijin Laylerh ke kan layi".ya kare zancen yana shafa sajen shi

" Na shiga uku ni Hadeeza kaga yaro da fitsara ".ta fadi a zuciyar ta a zahiri kuma sai tace

" eyya ya gida?"

"Lafiya kalau". Shiru ya sake biyo baya ya kuma fahimci in ba nuna musu yayi baida kunya ba haka zasu rike ta har sai Bayan azumi shiyasa yace

" Mom nikam baki so nane?Shikenan kuma an bawa Laylerh daki ni ba'a bani ba don Allah a nema mini daki a gidan Nima Zan dawo".abun nashi tsoro ya bata shiyasa ta katse Kira ba tare da tace komai ba Aunty'n Laylerh ko murmushi tayi a zuciyar ta tace Ai gwara da Kayi haka.. Ta Dade tana tunani kan batun karshe dai ta mike ta nufi daki bata bi ta kan Aunty'n Laylerh da ke fada Mata tsaruwar gidan da yadda komai ya kasance ba..

A bangaren shi ko cewa yayi yanzu aka Fara..

A Washe gari sai ga Umar Farouq ya hada kaya a akwati bai fadawa kowa ba ya nufi gidan Mommy Sulaiman da yake gate man ya San shi sai ya bude mishi kofa nan suka gaisa sai ya nufi ciki da sallama ya ko yi sa'a Laylerh ce kadai a gidan don Aunty'n ta ta shiga gidan hajja kande mommy Sulaiman kuma sun fita tare da shi sulaiman din..

Can ciki ciki yace

"Assalamu Alaikum". Shiru ba'a amsa ba nan ya sake daga murya kadan nan ma shiru sai ya zauna a daya daga cikin kujerun falon yana bin ko ina da kallo..

Wanka take ta kuma ji muryar mutum Na sallama a falo shiyasa ta karasa da wuri ta fito daure da towel nan ta janyo Babban hijab ta fito falon Ai tana ganin shi da sauri ta nufi ciki Kai ya girgiza kamar ba zai yi magana ba sai kuma yace

" babe Kinga gwara kizo mu zauna a nan ko Na biki ciki azo a same mu".ba shiri ta dawo falon kafar ta duk rawa yake yi can nesa da shi ta zauna

"Ina wuni". Kallon tsab yake Mata sai kuma taji yace

" hmm".hakan yasa ta dago Kai ta dube shi

"Ayya kaga ba kowa kaje sai sun dawo kazo". Murmushin ne ya bayyana kan fuskar shi wanda ta kwana biyu bata ga yayi irin shi ba

" Kice ango nake gidan ba kowa".sosai ta tsorata sai Gata ta Fara hawaye cire Kai yayi

"Zo"yace da ita yana kafe ta da ido kafada ta makale mikewa yayi yana gyara rigan shi ya nufe ta bata yi auni ba taji ya daga ta in a bridal way suka nufi dakunan sai dukan kirjin shi take tana

" Dan Allah Ka Bari wallahi Zan bika".dariya ma ta bashi sai cewa yayi

"Sai yanzu Kika San zaki Bini Ince in Na Kira wayar ki baki dagawa".

" Allah daga yau zanke dagawa ni Ka sauke ni".

"Yanzu nuna mini ina ne dakin ki kada ayi abun kunya a dakin Mom". Kuka ne yaci karfin ta ganin iya shege da kuma rashin kunyar da yake son mata, ya San ba zata fada ba shiyasa ya Riga bude bedrooms din yana lekawa har ya iso inda yake da tabbacin a nan take kwana da kafa ya turewa bedroom din suna shiga ya rufe da Bayan shi yana karewa dakin kallo,a hankali kuma ya dire ta har ta nufi kofa ya sa hannu ya riko ta in a surrender way ya daga hannun shi dukka biyu sama yace

" heyss bana cin mutani ".fuskar tausayi ta mishi

" to Ayya Ka bar ni Na tafi".da baya ya fada kan gadon tare da yin filo da hannun shi yana dariyar shakiyanci yace

"Kinga cire wannan lodin da Kika yiwa jikin ki Na kare miki kallo in ba haka ba tafiya sai ya gagare ki". Da sauri ta girgiza mishi Kai tana hawaye a hankali kuma Tasa hannu ta Fara zare hijab din nan wayar ta ya hau ringing sai ta dakata Tasa hannu

zata daga ya Riga ta ganin sunan Mom ne sai yayi receiving tare da ajiye wayar a gefe cike da salon iya shege yace

" Kinga yi sauri kan Mom ta dawo ".sosai zuciyar Mommy Sulaiman ya buga Umar Farouq da wayar Laylerh gaskiya wannan Yaron bai da kunya, Kai take girgiza mishi jin zai sake wani Maganan da sauri ta karaso tare da rufe mishi baki da tafin hannun ta tana girgiza mishi Kai a lokaci guda kuma take hawaye, hannu ya Kai ya katse kirar tare da Jan ta jikin shi ya rungume yana ajiyar zuciya

" Dan Allah Ka tafi da Allah Na hada Ka Na San duk inda Mom take dole ta dawo gida yanzu ".Kara manne kirjin ta yayi da nashi yace

"Ke kin zabi ki zauna a gidan Ku da Aure Na". Ya kare zancen yana tura hannun shi cikin hijab nata da sauri ta rintse idanun ta tare da rike hannun shi..

Shiru dakin ya dauka can taji numfashin shi gab da nata Wanda hakan Na nufin fuskar su ta kusa mannewa da sauri ta bude idon ta lokacin da yake kokarin sa bakin shi cikin nata ne kuma aka Fara horn a gate ba kakkautawa,kuka ta fashe da shi tace

" Mom ta dawo Dan Allah Ka koma falo".sake ta yayi ya fito falo ya zauna zaman shi ke da wuya Mommy Sulaiman ta shigo kallon tuhuma take mishi sannan ta zauna suka gaisa ba jimawa Aunty'n Laylerh ma ta shigo nan suka gaisa cikin mutunci da yake kuma shi ba ma'abocin magana bane sai shiru ya biyo baya.. abinci aka gabatar mishi nan yaci abun shi magrib nayi suka fita masallaci da Sulaiman suka dawo su dai ikon Allah suke gani tunda yaki tafiya gida..kan shi a kasa yace

"Mom ina ne daki Na nazo da kaya Na yana mota tunda an Hana ni Mata ta". To fa abunda da gaske ne Cewar Mommy Sulaiman a zuciyar ta sai tayi banza da shi har Tara yana gidan ganin fa da gaske yake a gidan zai kwana sai tace

" kaga jeka gida in sha Allah gobe zamu yi magana da Abban Ka".yaji dadi Amma bai tashi ba ita tsoro ma ya Fara bata shiyasa cikin lallashi tace

"Kaje abun Ka zamu yi magana da shi ne kan tarewar Laylerh". Ba kunya ya shiga godiya ya kare zancen da

" wallahi da an kyauta mini Amma an bar ni ba mata".daga nan ya tafi ita ko sai tagumi ta zuba

"Yaya ba sai kinyi wani tunani ba Ai kun bashi wahala ace Aure Na Neman sati biyu kun Hana shi Mata don Allah ya Isa haka yanzu kam Ai kun gamsu cewa yana son ta".

" Ai dole Na bashi don Na fahimci baida kunya gobe zanyi magana da Abban shi tunda an Mata Jere kuma an gyara ta nan da sati daya zata tare".sosai zancen yayiwa Aunty'n Laylerh dadi a Washe gari aka sanar da Abban shi ko da Umar Farouq yaji rawan Kai ya Fara..

Nan take Mommy Sulaiman ta sanar da yan Taraba tuni Auta da Baaba suka shirya tsab malam dai yace sai daga baya zai je..

Bangaren Ummi kam Harda dinki tayi tare da gayyatar mabociyar su Wai dole suje Abuja gidan Laylerh, Dada ma tana nan kuma gidan Dadda su uku zasu je Dada, Nabeela sai innar maryam duka duka su bakwai kenan..

Ana saura kwana uku ta tare suka Kama hanyar Abuja inda mommy Sulaiman ta tura musu kudin mota da Na abinci..

A ranar da suka Isa guest house nata dake kusa da gidan ta aka sauke su ba abunda babu abinci lafiyeyye aka Kai musu..

A Washe garin kuma mommy Sulaiman ta hada karamar walima inda ta gayyaci mutani Harda yan gidan M wakili Aunty Hauwa da su Najeeha ne suka je don basu yi gayya ba tunda bangaren su an gama biki..

Laylerh taci kyau wajen walima kaza daga half sai full abinci ba Wanda babu Ummi Leda ta samu ta saka a ciki makobciyar ta da suka je tare kuma lokacin da taci wani alele sai tace

"Dole in Na koma jala nayi irin shi".

" ke rufewa mutani baki wannan Na masu kudi ne in Na tuna Zan tafi Na bar jin dadin nan sai hankali Na ya tashi ".fadin Ummi..

Bangaren su Baaba fa sun raina kan su ganin gatar da Laylerh ke sha Gashi sai kunya ya Kama Baaba in suka hada ido da Aunty'n Laylerh tunawa da wulakanci da suka Mata..

Sosai Laylerh taji dadin ganin Nabeela har ta gabatar da ita wajen Mommy Sulaiman Wai matar da ta zabawa yayan ta ta kuma yaba da hankalin Nabeela shi ko Sulaiman ya Fara kyasawa..

Ana saura kwana daya ta tare a ranar gwaggon ta da yan uwan ta suka zo sosai Mommy Sulaiman tayi murnar ganin gwaggon su tunda sunyi zaman dadi yaran kuma yayar Laylerh kadai ta sani don Ana goyon sa'ar Laylerh ta bar gidan sai kuma Autar su..

Ranar juma'a da dare an gama kimsa ta motoci goma suka zo daukar ta sosai tayi kuka lokacin da ake Mata wa'azi sanda Sulaiman ne ya daga ta yasa a mota suka tafi har aka Isa kuka take yi Wai ba zata je ba..

Gida fa sanda Baaba da Auta suka gani sai suka sa kuka Nabeela kam da su Teema dadi suka ji Ummi kuma ta taba nan ta leka can sun yaba da tsaruwa da kuma Kayan da aka sa a gidan..

Ba bata lokaci kuma suka juya don ba kwana zasu yi ba da kyar aka raba Laylerh da Aunty'n ta duk kuka suke yi tana ji tana gani suka tafi gidan ya rage ita daya..

Comment

Share

©Hafciey Musa

[1/25, 5:44 AM] Hafciey Musa😘: □ LAYLERH □

(The prettiest emerald)

page 49

Dukunkunewa tayi wuri guda tana ta kuka harda shidewa.Ta dauki tsawon lokaci tana zabgawa hardai muryarta ya dashe dan kanta ta hakura da kukan sai ajjiyar zuciya kamar wata yarinya ita wallahi tsoron kwana gida daya da Umar Farouq take yi..

Da dai daya maganganun da su Auntyn ta sukai mata ke dawowa kwanyarta na daga nasihohi dasukai mata

Qwafa tayi tana girgiza kai a fili tace

" wllhi mutum yayi kokarin takura mini Mana groins nashi zan kaiwa naushi,ko na sace mai gwuiwowi da naushi,ko na gantsara mai babban cizo I got the tactics duka ai"..ta fadi tana murmushi kamar ba ita ce ta gama kuka ba

A bangaren ango Umar Farouq kuwa ba karamin shirye-shirye yake ba ya gagara natsuwa Bash tun abun na bashi dariya hardai yafara bashi haushi.In ba dan Bash ma dake daddanne Shi ba da saisun kusan riga amaren isowa gidan ma.Shi ke hana duk yunkurin da Umar farouk din yayi na son tafiya

"Haba Mana Umar Farouq be a man Mana,naga dai matar nan for the whole remaining of the night zata kasance in ur possession why the haste?"dalla kar ka bada maza at least a dan ja Mana ajinnan da aka saba ja".

Idanunsa da tun dazun suke kulle yadan bude ya kalli Bash sanan yamayar ya rufe kaman Wanda bayason maganar yace..

"Bash...bash baraka fahimta bane".

wani kallon bnxa Bash ya aika mishi Yana mere baki dan wallahi Umar Farouq yau ya kawoshi har makoshi.

Karfe 10 da minti 7 dot ta sauke kafafunta daga kan gadon tawuce toilet direct ta wanke fuskarta tas,tsayawa kallon yadda fuskarta ya cicciko tayi a mirror sanan daga bisani tadauro alwala tagabatar da sallanta ta biyo bayan da shaf'i da wutr idonta har mannewa suke saboda bacci datake ji.Hijab kawai ta iya zarewa tafada kan gadon in some seconds ma bacci yatafi da ita..

Umar Farouq

zabura yayi kamar Wanda aka tsikara Yana gyara hular kanshi baqa da ke tsabanin qyalli Wanda haske keta reflecting ya dubi Bash Yana cewa

" Ina!Ina this is enough Bash u can't hold me no more,babu yadda za ai nabar amanata har past 10 ita daya kan wani banxan reason waishi aji,as for laylerh I don't have any aji towards her yes nayarda ta kalleni with zero class,I love her!"

tuntsirewa Bash yayi da dariya shima ya miqe Yana duban Umar farouk din yace

"What's all this harzuqa for? kaga muje na rakaka har gate daga nan na juya dannaga wannan zafin ran innace zan karasa ciki you can bang the door to my face".

tun kafin ya karasa maganarshi ma Umar farouk yanufi hanyar waje haka akayi kuwa har gate Bash ya kai shi bayan sun tsaya sun sai grilled fish manya sai Kuma cranberry juice haka kawai yaji she may like flavor din dukda be San preference nata ba.

Bash na riqeda steering yace

"toh ango nidai iya nan zan tsaya saidiga baya zn zo ganin amarya,have a good night sleep". Ba kunya yace

"Thanks bash"

yafada cikin daddadan muryarshi Yana tattare ledojin dasuka taho dashi Allah yasa dai be tattara harda ledan bash ba😁.

Da sallama ya shiga falon shiru ba abunda kaki ji sai karan Ac a hankali ya maida kofar ya rufe sannan ya hau upstairs direct dakin shi ya nufa..rike kugu yayi kamar wani mace yana lumshe idanun sa Allah ne kadai ya San irin farin cikin da yake ji Ashe dai haka Aure ke da dadi,murmushi Mai sauti yayi shi daya tare da ajiye ledan sannan ya Fara rage Kayan jikin shi, sanda ya cire tsab sannan ya nufi toilet wanka yayi ya fito..Duk necessities da ya kamata yayi kafin shigowa dakinta saida yayi Yana sanye da jallabiyarshi me guntun hannu ash color me Zane Zane ya nufo dakinta although be manta da ledojinshi ba saida ya nufi dakin gadan gadan yaji pace na heartbeat nashi yayi tripling kan wani stool dake dap kofan dakinta ya ajjiye leathers din Yana monitoring zuciyanshi a fili da huskily yace.

"come on man u are still that Umar...yes Umar

Team Umar kunga tsoron shiga ma yake😂

saikuma yaji karfin gwuiwa yazo mai nan take ya seizing leathers din yayi tapping faintly without waiting for permission yaturo kofa bakinshi daukeda sallama.

Daga bakin qofar ya tsaya wata slight murmushi akan face nashi ganin yadda ta kudundune jikinta alamar sanyi na damunta Amma bata Samu damar lullubuwa

ba.Kamar me Wanda ya karasa kan reading table da ke dakin ya ajjiye nauyin hannunsa sanan yayi tiptoeing zuwa bakin gadon,kaman wani me Shirin aikata criminal act.

Durkusawa yayi daidai inda face nata yake ya daga hannu zaikai kan face din kamar Wanda ya tuna cewa zai taba naked wire Kuma sai yayi saurin janye hannun ya tsaya admiring face din dake ta glowing saboda hasken wutan dakin.

Miqa hannu yayi ya dau remote kan bedside ya kashe Ac din completely tunda bawai zafi ake ba and besides,ga wata jibgegiyar ox standing fan a can karshen dakin sai bada iska take ta kowani angle.

Hannu yakai ya kamo soft hands nata ai a take ya lumshe idanuwa daidai lokacin da palms nashi suka Samu contact da nata...ware idanun yayi tarr a kanta a hankali Kuma ya Fara caressing hand din ta Dan motsi tayi ta gyara kwanciyar ta alamar dai kaman Ana takura Mata.. Murmushi yayi in his heart yace

"She's a kitty,a sweet like kitty". Face nashi ya Kai daidai nata ya hada hannun su wuri daya yana shakan numfashi da take fitarwa..

Ya Kai 5mns da Dori a haka sannan ya bude idanun shi ya Kai bakin shi saitin eyelids nata ya Fara hura Mata Iskan bakin shi me dumi a hankali.. Mar mar mar ta Fara yi da idanunta ta Kara motsowa garin gyara kwanciyarta ta sake sakalo hannun shi da already ke cikin nata,har ta wuraren cikin ta..

Cigaba yayi da hura Mata Iskan sannan kaman me magana da babu cikin muryar da ke fitowa makogwaro yace

" Lay...l-a-y-l-e-r-h".

Bata motsa ba saida ya maimaita sau uku sannan cikin yanayi Na nuna bata son disturbance da ake Mata tace

"Uhmmm".

Wannan amsawar da tayi tare da duk wani bangare Na jikin shi suka amsa domin wani deep fragrance breath ta fesar mishi Wanda ya wuce direct har bronchi nashi sannan ne kuma ta Fara bude idanun ta a hankali har dai ta sauke su akan shi Ai wuf ta mike zaune har tana gwara goshinta da nashi...dafe goshin yayi cikin yanayin shi Na jin Kai da yanga yace

" Awwch easy girl ".

Ya wani karairaya girl din,da Wata manufa nashi da ya barwa kan shi sani..

Yana rike da goshin shi take satar kallon yadda yake ta caressing Na goshin Kai kace da icce aka buga Mai..

Satar shi tayi ta dirko akan gadon ta nufi kofa da gudu..da sauri ya rufa Mata baya kafun ta Isa kofar ya sha gaban ta yana daga hannu dukka biyu sama in a surrender yace

"Heyss miss bana cinye mutani". Ya fada yana wani bin duk duk angle Na jikin ta da sassanyar kallo ita ko mamaki da tsoro sun rufe ta,she was like

" what is this man after?"

kamo hannun ta yayi steadily yana duban yatsun ta kamar bada ita yake maganar ba hankalin shi kan yatsun yace

"You don't bath in zaki kwanta kazamiya?" Bata San meyasa ba,sai taji tambayar don't sound offensive, da yake be yi da sigar cin fuska ba. ita ma ido ta sauke kan hands nasu tana kokarin janyewa ya hanata hakan yasa ta hakura sai samun kanta tayi da me bashi amsar

"To nayi kuka ne shine Na gaji nayi bacci". Matse hannun ta dake cikin nashi yayi hakan ya sata rintse ido..yana kallon yadda take rumtse idon ya Kai face nashi kusa da nata sannan yace

" huhn cry cry little baby,ke baby ce?".da sauri ta girgiza Mai Kai tana ta Allah'n ya sake ta bata bude idanu ba cikin rawar murya tace

"To ni kanata matse mini hannu". Kara matse hannun yayi sannan commandingly yace

" now Zan sake ki kiyi wanka and wear on something light I got something for you".

Ai bata tsaya digesting abunda yace ba yana sanar Mata hannu ta nufi toilet har ta rike handle ta tsinkayo muryar shi yana cewa

"Don't try zama a toilet Zan biyo ki and will play you dirty". Ita dai karasa shiga toilet dinta tayi tana mamakin yadda yake ta wasu maganganun da ita bama ta fahimta,yo wannan turancin da yake tayi Ai sai shi ya San ma'anar su..

Bakin gadon ya koma ya zauna a hankali yake karanta mails da ake turo mishi Na bada amsa ya bada sauran kuma ya barsu Dan sai yayi bincike.. A haka ya duba yaga lokaci ya tafi sosai hakan yasa ya kashe wayar ya nufi kofan toilet din yayi tapping yace

" remember I said Zan shigo in baki fito ba".a firgice Laylerh cikin daga murya tace

"A'a fa yanzu Na gama Zan fito ne". Bai ce Kala ba ya koma ya zauna ita ko sai taraddadi take Na yadda zata fito yana dakin ta samu komai da take bukata cikin toilet din har sleeping robe duk da maras adone haka ta zumbura wani peach color ta wrapping kanta cikin wani soft towel peach tana ta zuba kamshi..

Ganin fa ko yaya tayi sai ta fito ne ya sata shahada ta fito..yana jin motsin kofa ya mike zaune yana kare Mata kallo cikin ran shi yace

"Damn...everything suits her har da boubou PJs "..

Tana rirrike jikin ta ta nufi gadon zata zauna kasa ya Mata nuni da bakin gado dole ta zauna nesa da shi briefly ya kalle ta yace

" alwala?"

Fahimtar me yake nufi ya sata gyada Mai kai,because Ai tana alwala kafun ta kwanta..bai Kara cewa komai ba ya wuce wardrobe ya dauko Mata abaya,hijab sai kuma sallaya da ya shimfida babu bata lokaci suka tayar da sallah Bayan tsattsareta da yayi da ido while tana daura abayar kan PJ din,yayi ta cire taki dole haka suka gabatar da sallah yayi musu necessary addu'a sannan cikin natsuwa ya kamo goshinta ya manna Mata wani everlasting kiss..lumshe idanun ta tayi tana sauraron yadda numfashin shi ke sauka kan goshinta bata iya Wata kwakwaran motsi ba har sai da ya saki kanta yana duban yadda ta lumshe idanuwa...

Murmushi yayi me Dan sauti sannan yace

"Are you waiting for more?" Cikin tsananin jin kunya ta ware idanun ta kam shi ganin ita yake kallo kuma sai ta zumbura baki ta kau da Kai gefe..ganin ya Fara Nade sallayar da yayi sallah a Kai ne ya sata mikewa zata Nade Wanda take Kai ya Kama hannun ta cikin whisper yace

"This one is on me,kiyi reserving energy din ki zai miki amfani Anjima". Dif dif dif zuciyar ta ya Fara bugawa yes wallahi yanzu kam ta fahimci kudirin sa so yake ya bubbuda ta daga zuwan ta gidan shi ko kwana bata yi ba to wallahi bare yiwu ba Ai tactics nata Na nan tayi mastering nasu..

In ba rashin kunya da rashin tausayi ba Ai zai bar gajiya ya fita a jikin ta ba sai ya nuna zamalamar shi a fili ba..shi ya katse Mata tunani da fad'in

"Ai dai kya cire wannan Lodi da kikaiwa jikin ki". Cikin sanyi ta karasa bakin wardrobe ta zare hijab din Bayan ta linke ta maida su tana da confidence Na cewa PJs din ya rufe Mata ko ina shiyasa bata damu don ta cire abayar yana nan ba..

Ledojin shi ya Fara budewa da yake shi sabon shiga ne ko irin tunanin dauko plate and fork bai yi ba..dagowa yayi ya dube ta yace

" bismillah join me".sai kuma yayi murmushi yace

"Or I better say kizo ki zauna nayi joining naki after all it's yours gwara muyiwa junan mu adalci Nima Anjima nayi gadara da abunda yake nawa". Jin furucin ya sata fashewa da kuka shi ko ciza Lower lip nashi yayi cikin ran shi yace

" Ai ko ba kiyi kuka bama tukun".mikewa yayi yaje ya kamo hannun ta Haba a nan ta hau tirjewa hawaye sharkab kan fuskar ta sai cewa take

"Ni dai wallahi baran ci ba ni bana ci". Dakatawa yayi daga Jan ta da yake yi ya leka face nata kaman a shaqiyance yace

" are you sure?baki jin yunwa?what you are about to face ba'a daukar shi da yunwa".Ai Haba fashewa tayi da mashahurin kuka tana toshe kunnen ta idon ta a rufe tana cewa

"Ni dai wallahi bana so".

...saida yabarta tasha kukan yadda yakamata sanan yace

"waike ba'a Miki wasa?I was just kidding zo yanzu kici wani abun saiki Samu ki kwanta dawuri saboda ur eyes shows kina jn bacci".

Jin haka yasa ta yarda cikin yanga takarasa tazauna kan lallausan rug din ta takure tareda cusa kanta cikin cinyoyinta

Zama yayi facing her sanan ya dauko plastic fork dake cikin package na kifin yayi bismillah tareda tsakalan kifin da yaji tomato and garlic sauce yakai baki,lumshe idanuwa yayi can qasan maqoshi yanda shikadai yaji yace...

"yumm" saida ya gama taunewa sanan ya fiddo plastic cocktail cups din ya tsiyaya musu cranberry juice din ya dubi yadda take yai shaking kai sannan cikin tattausar murya me cikeda umarni yace...

"ki dago kisamu kici wani abun,all is set"

Samun kanta tayi da kasawa wurin musa mishi sai ta dago din a hankali kuwa ya miqa mata fork din bayan ya tsakalo mata.Miqa hannu tayi garin karba hannunsu ya Samu contact da gudu ta janye nata tana Kara ja baya kamar wacce ta taba wuta,tabe baki yayi shidai be ce komi ba yasake Mika mata with care ta karba yadda hannunsu bare hadu ba takai baki a hankali take taunewa tana lullumshe ido Dan dadi kallonta kawai yake baya ko kyafta ido tana gama taunawa ta dago tana kallonshi da ido ya nuna fish din sai Kuma ya kalli fork din hannunta cikin sanyin murya yace..

"add"

Kai ya girgiza kamar me tsoron magana tace..

"na koshi".

Be ce komi ba yadau cup dake dauke da juice ya Mika mata girgixa kai ta sake tareda ajjiye fork shima ya ajjiye cup din Yana kallonta ta Mike zata haura gado harta daga qafa zata hau ya kamo hannunta still Yana zaune yanai mata wata shuumar kallo

A hargitse ta juyo tana kokarin kwace hannunta ya Kara damkewa sannan a nitse ya miqe tsaye still idonshi kan glowing face nata

Fara murza hannun yayi kaman baya son magana yace,

"bacci zakiyi?

Dasauri tahau gyada kai tana sa ran in yaji hakan ya sakar mata hannu.

Hannu ya daga,a hankali ya kamo waist nata carelessly unexpectedly Kuma ya matsota jikinshi sosai harsaida tafara sharing dumi da kamshin jikinshi....idanu ya lumshe ya bude a take saboda wani niimtaccen kamshinta da ya shaqa, still looking at how ta rumtse ido yakai hancinshi gefen wuyanta Yana sakan numfashi cikeda gayya yace...

"nikuma banajin bacci,ya zamuyi?

Samun kanta tayi da kasa ko motsi,because ya toshe duk wani hanya dazata bi dan kubucewa sai numfashi take fitarwa da sauri da sauri.

Kwantar da kanshi yayi kan kafadarta Yana moving hannunshi da ke waist nata yace,

"uhmmm Laylerh ya zamuyi?

Dakyar ta iya samo muryarta cikin karkarwa tace.

"Maybe kaje ka gwada kwanciya ka kulle ido?

Dawo da fuskanshi yayi saitin nata yace..

"no,I got a better plan, what if I....yafada Yana kai babbar yatsarshi yashafo lower lip nata yacigaba bayan ya mayarda muyarshi rada yace...

"kiss yhuu?

Ware ido tayi ta zuba cikin nashi ganin haka ya kashe mata ido daya Yana sauke idonshi kan lips nata,nan take wani karfi yazo mata ta turashi baya ta tsinka dagudu tanufi kofa takama doorknob cikin tsinkewan zuciya zata fice a dakin

Kafin ta kai ga budewa taji an danne kofa tana dubawa taga fair good looking hands nashi ne yasa ya danne kofar

Ware idanu tayi ta juyo a firgice zatabi ta dayan gefenshi zata gudu yayi saurin saka dayan hannun ya danne ta kasance in his custody,zazzare ido tahau yi saikuma tayi kokarin sunkuyawa tabi ta kasa kai ya girgiza ya matsota sosai yakai tip na harshenshi Yana playing kan wuyanta yace...

"Be calm,no way to escape".

Idanu ta rufe,tana fidda numfashi sama sama sabda abunda Umar Farouq ke mata yafi karfin kanta besides,wait,is this really the farouk she knows?

A hankali yake wasa da harshenshi kan wuyanta har yakai kan chin nata ganin ya gama batar da ita hakan yasashi kai lips nashi kan nata Yana jiran reaction dinta ganin tafara saddaqar mai ragamarta yasashi kokarin kai harshenshi cikin bakinta,bata hanashi ba kuwa hakan yabashi damar twisting tongue nashi da nata yafara tsotsa like madly...tsoro yake sosai karta hanashi shiyasa yake kissing dinta hastily cikin barin jiki...

Laylerh sosai take karbar sakonshi tana taimaka mai saboda unknowingly to her har wani kamo qeyarshi tayi tana yamutsa mai gashin wurin a hankali, just like urging him to do more,to go beyond abunda yake bata yanzu..

Laylerh kin bada mu□□□

Sakamakon yadda yaketa jujjuya harshenta dafarkone yasa taji wani zogi na ziyartar harshen nata,Umar Farouq beyi tsammani ba kawai sai ji yayi ta janye harshenta cikin nashi da dukkan sauran energy daya bar mata a jiki ta tureshi dukkansu biyu sai numfashi suke loudly

Kafin yayi attempting yin wani abu tayi wup ta fice daga dakin tana zaz zare ido ganin key ta waje kawai saita murza ta rufe kofan but still tana rike da knob dan gani take kmr ze iya budowa.Takai 5mns tana tsaye sannan nitsuwa yafara dawo mata da gudu ta nufi stairs tasauqa ta burma dakin baqi Allah yasa nan ma akwai key ta murza sannan a hankali ta sulale ta zauna kasa nan jikin kofar idanun ta na tsiyayo da ruwa...

"Me hakan kenan me Na aikata?" Ta tambayi kanta tana fashewa da kuka nan take taji ta tsani kan ta..

Zamewa shima yayi idanun Shi a lumshe yazauna dabas a kasa saboda ji da yayi ta yiwa dakin key,he won't bother following her,he won't call her,he won't force

her,he's not a monster,bare tabata ba harsai da izininta tunda ya fahimci ita ma irin sa ce...a haka yadau lokaci me tsawo sannan yamiqe yayi toilet yadafa sink yabata shiruuu cikin tunani.Ya dade a nan ma sannan yayo wanka sharp sharp yafito daure da towel yazauna bakin gado ya riqe kanshi da dukkan hannayenshi idonshi a lumshe,Yana tuna what just happened,some moments ago ya riqe Laylerh,like intimate riqo...he kissed laylerh,he sucked laylerh's saliva,he just swallowed laylerh's saliva....lives full of sweetness....yafada Yana fadawa kan gadon yayi pillow da hannunshi be San tsawon lokacin da yadauka kafin bacci ya sace Shi ba..

Manage this da babu ance gwara ba dadi

Comment

Share

©Hafciey Musa

[1/25, 5:44 AM] Hafciey Musa😘: *□LAYLERH□*

(The prettiest emerald)

Washe gari da safe ko ita ce farkon tashiwa saboda Tun hudu da rabi ta tashi,mikewa tayi tana karewa dakin da yaji komai Na more rayuwa kallo sannan a hankali kuma ta zura takalmi a kafar ta tana bin jikin ta da kallo don Tun Kayan da aka kawo ta da shi ta kwana..

Har zata shige toilet sai kuma ta fasa kofar dakin ta bude tare da ficewa zuciyar ta Na bugawa ta Fara hawa stairs din,ta Dade tsaye a kofar dakin ta kafun a hankali ta bude kofar tana gama cire key din ta sauka da sauri tare da Komawa dakin baki tayi masa key..

Bai jima da tashi ba bai kuma manta cewa jiya Laylerh ta rufe shi ta waje ba shiyasa Bayan yayi addu'ar tashi daga bacci sai ya nufi toilet domin alwala ya kuma sa a ran

shi da ya fito zai Kira ta a waya yace ta bude shi ya tafi masallaci ba tare da sanin a dakin ta bar wayar ta ba..yana fitowa yaji alamar tana bude kofar sai bai motsa ba don ya San tsoron shi take ji shiyasa sanda yaji saukan ta kasa sannan ya fito direct dakin shi ya wuce..

Ba abun fadi game da dakin sai Masha Allah wardrobe ya bude inda ya fiddo jallabiya maroon ya zura tare da sa takalmi ya sauko kasa..kallo daya yayiwa dakin bakin ya cire ido don wutar dakin a kunne take nan ya fice zuwa masallaci.

A bangaren Laylerh ko taji fitar shi shiyasa ta fice a hankali zuwa dakin ta tana shiga kuma tayiwa kofar key tare da zama a bakin gado

"Wai yau ni Laylerh ce matar Aure ikon Allah". Ta fadi abun a fili don abun mamaki yake bata,bata tashi mamakin hakan ba kuma sanda aka kawo ta gidan Umar Farouq ta kwana.. Mikewa tayi ta nufi toilet nan ta cire komai nata sannan tayi wanka tana fitowa kuma ta sa dogon Riga tare da Fara nafila nan ta zauna a sallayar har aka Fara sallah sannan tayi..ta Dade zaune a sallayar har sai da gari ya Fara haske sannan ta rufe Qur'an da take karantawa gami da hawa gado ta janyo wayar ta tana Neman number'n Aunty'n ta bugu biyu kuma ta dauka..

A can gidan mommy Sulaiman kuma tunda aka tafi Kai Laylerh sai Mommy Sulaiman taji kewar yarinyar sosai duk da ba wani jimawa suka yi tare ba,ita da Sulaiman kadai suka rage duk jugum suka yi har su Aunty suka dawo gidan..

Ai a ranar Aunty'n Laylerh kasa bacci tayi sai juyi take yi a gado sai can kaji tace hmm in ya sake dadewa ta sake fada Mommy Sulaiman duk tana jin ta can tace

" Amina lafiyar ki kuwa naga ba'a kan Laylerh aka Fara Aure ba".ta fada cikin dauriya don ita ma kewar Laylerh take yi da kuma tuna Mata sabuwar rayuwar da zata Fara take yi..

"Ba zaki gane bane wallahi tausayin Laylerh nake ji don yadda Umar Farouq ya Riga rawan kafa ni dai Allah sa kada yaji ma 'ya ta ciwo". Ta fadi hakan cikin zuciyar ta a

zahiri ko cewa tayi babu da haka har bacci ya dauki mommy Sulaiman ita ko kasa bacci tayi hankalin ta Na can ga tunanin Laylerh..

Washe gari ma da tunanin ta ta tashi so take ta Kira ta Amma kuma ta San kila suna tare da Umar Farouq shiyasa bata Kira ba ta kuma tabbatar in har ita ce ta raini Laylerh dole zata Kira ta sai Gashi ko kiran ya shigo shiyasa ta dauka da wuri..

" Aunty ina kwana".jin muryar Laylerh normal sai ta sauke ajiyar zuciyar da har sanda Laylerh din taji sannan tace

"Lafiya Laylerh ya bakunta".

" Lafiya Kika sauke ajiyar zuciya?"murmushi tayi kamar a gaban Laylerh take sannan tace

"Ba komai". Kamar Laylerh ta San abunda yake ran Aunty'n nata shiyasa cikin yin kasa kasa da murya tace

" kwantar da hankalin ki Aunty ba abunda ya faru wallahi rufe shi nayi a daki".a tare suka sa dariya kamar masu tabin hankali sai kuma ga hawaye a fuskar Aunty'n ta, tsam bata son abunda zai raba ta da Laylerh domin Laylerh Kawa ce a Gare ta ba 'ya ba ji take ba zata iya rayuwa ba tare da wannan yarinyar ba share hawayen tayi sannan taja hanci tace

"Kin kyauta Ai da Kika rufe shi Amma kada ki Kara babu kyau".

" to Shikenan sai Na bar shi yayi yadda yake so da ni?"ta kare zancen cikin tsigan tambaya

"To ba mijin ki bane Ince farko matsalar don baya son ki ne yanzu kuma yana son ki ko so kike mala'ikun Allah su Riga tsine miki ne?ko a kauye fa Mata sun daina

gudun maza wallahi in kin Kai shi bango raping naki zai yi haka kike so ko"cikin sanyi tace

" a'a".

"To Kinga yanzu ki tashi ki gyara gidan sai kiyi wanka ki sha kyau kada fa ki nuna mishi kina tsoron shi". To tace nan dai ta tambayi kowa da kowa aka ce lafiya sannan suka yi sallama..

" Amma Amina Allah shirye ki ke da Laylerh, yanzu da girman ki kike biyewa Laylerh kuke irin maganar nan?Allah sa shi Umar din ya jita ya buga bakin nata".ido kawai ta zurawa yayarta ta sai kuma murmushi da take yi akai akai..

"Kinga Na manta ban fada Mata Anjima kawayen ta zasu Kai Mata Kayan gara ba".

" in sun je ta Gan su Ai".

A can bangaren Laylerh ma sosai taji sanyi a ranta da kalaman Aunty'n ta, ita fa wallahi ba komai ya sata rufe daki ba sai don tsoron abunda zai Mata.. so take ta Kira Mom nata Amma kunya take ji don gani take zata yi tunanin yanzu ita ma ta San komai da kyar dai ta Kira ta jin ba'a daga ba sai ta sauke ajiyar zuciya don ta San komai lafiya tunda sunyi waya da Aunty'n ta..

So take sai taji motsin shigan shi daki sannan ta fita ta gyara gidan don bata son suyi ido hudu shiyasa ta zauna shiru a dakin Harda kashe Ac..

Can taji motsin shi kofar ta kurawa ido tana jin kamar zai shigo ta kuma ga lokacin da ya murda handle Na kofar jin ta a rufe sai ya wuce dakin shi..

Yana shiga ya zare jallabiyar tare da fadawa gado nan ya janyo filo daya ya rungume shi don so yake a tsakanin nan ya huta kan ya koma bakin aikin shi

shiyasa ya Fara bacci.. Kamar Wata munafuka haka ta Riga leke jin ba alamar shi sai tabi corridor da kallo kafun ta sauka downstairs duk da gidan ba wani Dotti nan ta gyara ko ina tana kuma yaba kyau da tsaruwar gidan ta kuma gode Allah da ya mallaka Mata Mommy Sulaiman matsayin uwa wacce ta kashe ta da Kayan daki masu tsada.. Bayan ta gama gyara falon sai ta wuce can dining din nan ta gyara sannan ta shige kitchen..

Sosai tayi mamakin ganin irin Kayan da aka Mata nan ta shiga bude ko ina ba abunda babu Na bukata, kallon cikin ta tayi jin bata jin yunwa sai ta haura sama ta kwanta tunda Ai amare basu girki a Washe garin da aka Kai su a fadin ta..

Baccin hour daya kawai tayi don duk ji take tana takure nan ta bude wardrobe nata ta Ciro super wax nata don daga zannuwan da Umar Farouq da Mommy Sulaiman suka Mata duk ba kananan zannuwa..dinkin gown ne nan ta Ciro shi tare da fidda inner wears nata sabbi Tasa tunda tayi wanka da asuba sannan ta kashe daurin ta..takalmin zaman gida da aka saya Mata ciki ta dauki daya ta zura tare da fesa turare sannan ta sauko kasa don yanzu kam ta Fara jin yunwa dole ta nemi abunda zata ci ko ba Mai nauyi bane tunda shi bai iya kawo Wa amarya breakfast da safe ba..

Irish ta deba daidai cikin ta zata Fara ferewa kenan taji an rungume ta ta baya sannan hannun shi ya rike ta gam kamar za'a kwace mishi ita,ko ba'a fada Mata ba ta sani don jikin ta ya bata Umar Farouq ne sannan turaren shi ya tabbatar Mata da hakan shiyasa ta Kai hannun ta kan nashi tana turewa jikin ta ya hau rawa, jin ba rikon wasa ya Mata ba sai tace

"Dan Allah Ka sake ni bana so". Ta kare zancen murya Na rawa jin yasa fuskar shi a kafadar ta tana jin yadda numfashin shi Mai dumi ke sauka a wuyan ta,can kasa kasa yadda ita daya zata ji shi yace

" meyasa Kika rufe ni a daki jiya Allah Tarawa kan ki kike yi if to say jiya kin tsaya da an wuce wurgin yanzu "".yanzu kam hawaye ta Fara don Allah ya sani bata son wannan kusancin da suke samu sannan maganganun shi tsoro suke bata,ta yarda zata zauna da shi tunda shi Allah ya zaba Mata matsayin miji Amma tsam bata son suke samun body contact don wallahi kunyar shi take ji gani take tayi yarinya da wasu Abubuwan shi ko kunya ma baya ji..firgita tayi lokacin da taji ya manna Mata kiss a gefen kumatu sai kawai ta fashe da kuka Anya Umar Farouq da ta sani ne

"Calm down girl Na sake ki". Ya fadi lokacin da ya sake ta tare da juyo ta gaba daya tana fuskantar shi daga kafar ta yake bi da sassanyan kallo a hankali har ya iso fuskar ta,hannun ta dukka biyu ya Kama idanun shi a kan ta yace

" Shikenan daina kukan ya Isa haka in dai wannan ne ba Zan sake ba".jin haka sai tayi shiru kanta a kasa tace

"Ina kwana?" Sai da ya kare Mata kallo kamar ba zai amsa ba sai kuma yace

"Lafiya ya bakunta". Tsintar kan ta tayi da bashi amsa

" alhamdulillah ".daga haka ta juya

" heyss me zaki yi?"let it be Zan yi order see ke fa amarya ce".ba tare da ta juyo ba har yanzu kuma bata koma daidai ba don gani take kamar zai Mata abunda yayi jiya sai tace

"Ni dai yunwa nake ji kuma bana son abincin waje". Ta kare zancen tana turo baki..

" baki son abincin waje ".ya fadi yana leken fuskar ta don ya San in yace zai taba ta kuka zata sa mishi shiyasa Tun farko yace akwai ta da kukan banza tausayin kan shi ne ya Kama shi don duk Randa yace wani abu zai shiga tsakanin shi da ita sai ta Tara mishi yan anguwan gaba daya,katse mishi tunani tayi da fadin

" in dafa da Kai zaka ci".tambayar tata dariya ma ta bashi duk da cewa bai jin cin abincin sai yace eh lokacin da ya kurawa breast nata dake cikin kaya ido ganin zata dago sai ya tsotsa keyar shi tare da Komawa gefe ya tsaya duk inda tayi ya bita da kallo so yake ya taya ta Amma taki bashi fuska

.

Wayar shi ce ta Fara ringing ganin kiran Mai amfani ne sai ya fice a kitchen din nan tabi shi da kallo har ya bacewa ganin ta sannan tacigaba da aikin ta,ita dai Allah ma ya sani tayi amfani da sanin yadda yake ci lokacin da suke gidan malam ne ta dafa daidai su tana gamawa kuma ta daura tea inda yaji Kayan kamshi sannan ta juye mishi a flaks nan ta Kai dining ta ajiye mishi ita ko daukar nata tayi ta nufi stairs..

Sosai yayi mamakin ganin ta ajiye mishi a dinning sannan ita kuma bata nan shiyasa ya haura sama tare da tapping kofar ta sau biyu

"Laylerh".

" Na'am".tace Bayan tayi sipping Na tea'n ta Mai Zafi

"Ki fito muyi breakfast tare".Kai tsaye tace

" wallahi ni kunyar Ka nake ji ba zan iya ci a gaban Ka ba".murmushi yayi still yana tsaye a kofar yace

"To zo ki dauki abunki Nima ba Zan ci ba".shiru tayi taci gaba da cin Irish nata nan ya sauka kasa tea din ya hada da yake safe da dare baya shan tea Mai madara yafi son Lipton sai Irish din ne yaci kadan yana kuma tunanin sai yayi da gaske Laylerh zata Sake da shi..koda ya gama breakfast din bai tashi a wajen ba nan ya Riga receiving calls sai can ya nufi bedroom nashi..

Tsaki yake ta ja can ya janyo wayar shi tare da Fara dialing number'n Laylerh..

A bangaren ta ko ta gama cin abinci kokarin fidda kwanukan take yi taji wayar Na ringing ko da ta leka fuskar sai taga sunan shi

" yanzu kuma me zanyi ".ta fada tana murkuda baki kamar yana gaban ta sannan ta sa hannu ta dauko wayar lokacin har ta kusa katsewa

" ki kawo mini fruits ".yana gama fadin haka ya katse kiran,ita ko kafa ta buga a kasa kamar karamar yarinya wallahi ita nan da can ne bata son yi wucewa kitchen din tayi da kwanukan hannun ta nan ta ajiye sannan ta wuce dinning ta tattaro nashi da kadan taga yaci ta rufe,fridge ta bude Bayan ta fiddo fruits din sai ta yanka tare da rufewa da plate ta nufi hanyar dakin zuciyar ta Na bugawa kila ma wayo yake son matw..ta Dade kafun a hankali ta tura tare da yin sallama tana shakan kamshin dake fita a dakin take ta lumshe idanun ta har cikin ranta take jin wani sanyi,karewa dakin kallo take sosai ya Mata kyau ganin baya falon sai ta Fara leke leke tana kuma tabe baki so take ta kalli ko wani lungu da sako Na dakin Amma bata son ya Gan ta yace kauyanci..gyaran murya tayi sannan ta Dan daga murya

" Assalamu Alaikum ".

" yes shigo ciki".taji muryar shi daga bedroom din Wai yes sai kace ba musulmi ba a hankali ta cigaba da takawa har ta Isa kofar bedroom din kanta a kasa ta shige sai dai nan yafi falon sanyi ma,idon ta a kasa take takawa har ta Isa inda taga center table nan ta ajiye ta juya zata tafi ta tsinkayo muryar shi a zama yana fadin

"Ai ban sallame ki ba". Juyowa tayi da niyar sa mishi kuka ko zai ji tausayin ta as usual sai kuma ta rintse idanun ta da sauri ta rasa me yasa tsam baya cikin maza masu kunya..kwance yake a kan gadon daga shi sai three quarter ko vest bai sa ba bare Riga irin kwanciyar rub da cikin nan yayi inda ya daga kafan shi sama yana kuma aiki a system..

A hankali ya juya Gare ta ganin yadda ta rintse ido sai ya cize lower lips nashi tare da rufe system din ya ajiye a bed side drower ya mike tsaye ji kawai tayi ya kamo hannun ta

" nikam bana so Ka sake ni".

"Calm down massage kawai zaki mini kiyi tafiyar ki". Kamar zata yi kuka tace

" wallahi ban iya ba".yana jinta Amma bai ce komai ba nan ya jata suka zauna bakin gadon yana kallon ta har cikin ido inda ita ko ta sauke nata kasa

"Kinga ba abunda Zan miki massage kawai zaki mini Kinji ko". Ya fadi cikin tsigar rarrashi don Allah ya sani so yake su ke spending quality time tare ko zata saki jiki da shi kan ya koma bakin aikin shi ya rasa lokacin ta..

Kifuwa yayi akan gadon ya bata baya ita fa ba zata iya kallon shi ba da kyar ta saci kallon shi taga yadda roban wandon ya matse shi sosai ga fair skin nashi da sai dauke ido take yi da sauri ta cire idon ta..ya sani ko ba'a fada ba bata taba ba tunda ba Aure ta taba ba shiyasa ya mike tare da Daukan filo ya Fara nuna Mata yadda zata yi da kyar ta iya gyada mishi Kai idon ta a rufe Tasa hannun ta a nicked skin nashi..ajiyar zuciya ya sauke lokacin da yaji palm nata masu sanyi a nicked skin nashi a hankali take massaging yana kuma lumshe idanun shi har wani bacci bacci yake ji..hannun shi yasa kan nata inda ya Kai hannun kan kugun shi gane abunda yake nufi ya sata Fara massaging wajen cike da tsoro.. Sun dau lokaci a haka sannan intercom Na gidan ya Fara Kara alamar Kira ne daga gate nuna Mata yayi da ido yana fad'in

" get the call".a hankali ta mike ta nufi inda taga intercom din,idanu ya zuba Mata kamar zai hadiye ta

"Assalamu Alaikum". Ajiyar zuciya ya sauke don dama so yake yaji sallama zata yi ki akasin haka..ganin ta kura mishi ido sai ya daga Mata gira alamar mene can kasa kasa tace

"Wai baki aka yi".

" Kice su Waye ne sannan duk a lissafo sunan su".maida wayar kunnen ta tayi tare da fadin yadda yace sai ta dube shi tace

"Yan gidan mu ne".ba tare da ya kalle ta ba yace

" suna".haushin shi taji tunda yan gidan su ne me Na tambayar suna shi da zai basu umarni

"Nabeela,Auta,Teema,Yaya ta da kanne Na biyu".ta kare kamar zata yi kuka

" su shigo ".haka ko ta sanar da security dake gate din sannan ta dawo bakin gadon ta tsaya

" Na tafi?"ba shiri taji ya janyo hannun ta ta fada kan shi nan ta fara fadin ya daina bata so

"Kinga Nima massage Zan miki".

" a'a wallahi Na yaf..."kasa karasa zancen tayi jin ya Fara massaging dantsen hannun ta ya kuma matse ta a jikin shi dole tayi shiru har ya Fara massaging kafar ta da Bayan ta duk idon ta a rufe,tana ji ya cire Dan kwalin kanta yana karewa kitson kan ta kallo sai kuma taji numfashin shi kusa da fuskar ta hakan ya tabbatar Mata da kissing nata yake son yi shiyasa ta bude ido da sauri Ai ko fuskar shi dab nata ture shi tayi tare da mikewa ta dauki Dan kwalin ta ta fice a bedroom din ya nufi downstairs tana jin shi yana fadin

"Allah kina Tarawa kan ki ne"..

Da yake shi yake controlling remote Na main kofar shiga falon tana ficewa ya Danna pin din turawa kawai za'a yi ya budu suna turawa suka ci Karo da ita a tsakiyar falon tana daura Dan kwali a kanta..

Hugging Na junan su suka Fara cike da farin ciki

"Sannun Ku da zuwa bismillah Ku zauna"gaba daya zama suka yi suna bin ta da ido Musamman Auta wacce gani take kamar daga jiya zuwa yau Laylerh ta canza

" Amarya kin sha kamshi ".ita dai murnar ganin su take nan ta shiga tambayar su mutanin gida daya Bayan daya daga bisani ta mike domin kawo musu abun sha inda duk da ido suka raka ta lokacin da ta nufi fridge ta dauko musu Kayan sanyi sannan ta dawo

" Auta ya Baaba".zuwa yanzu dole tayi giving up don Umar Farouq ya Mata nisa shiyasa tace

"Tana lafiya tace a gaishe ki".

" Masha Allah Nabeela Dada da Ummi fa ya Baku zo tare ba?"

"Ai da an dauko ta korin mu ango zai yi". Cewar Auta nan suka sa dariya don tsam basu yi tunanin Umar Farouq din Na gida ba

" yaya sannun Ku da zuwa".tace da Yayar ta da kuma kanwar ta

"Aunty Laylerh ki kunna mana TV". Cewar kanwar ta kuma Autar gidan su nan ta mike ta kunna TV gaba daya hankalin yarinyar ya koma kan TV shiyasa Teema tayi gyaran murya tana kuma kallon gefen da kanwar Laylerh take wacce tayi nisa a scrolling channels a haka ta iso kan cartoon

" Amarya ya muka ga baki dingishi".tsam ita bata son irin wannan wasar da kawaye ke yi shiyasa ita ma ta kalli gefen da kanwarta take sannan tace

"Kinga Teema ki bar irin zancen nan baki ganin yarinya ne". Dariya suka Mata a lokacin ne kuma kanwarta ta dago ta dube su

" ni dai a iya sani Na kina sallah ba za kuma ace an daga miki kafa bane to ko dai daurewa kike don kada mu gani".ta bude baki zata yi magana sai ta kalli Umar

Farouq Na saukowa daga upstairs cikin shirin fita kunnen shi makale da Bluetooth duk kallo daya suka mishi suka cire ido a haka ya karaso

"Sannu ina kwana". Suka hada baki wajen fada nan ya amsa ba yabo ba fallasa sannan ya dubi bangaren da kanwar Laylerh take yace

" Ai ke kam za'a bar mana ke ko?"ganin ita yake kallo shiyasa ta fahimci da ita yake yi nan ta gyada mishi Kai sai kuma ya Kai duban shi ga Laylerh

"Laylerh". Ya Kira sunan ta Bayan ya Fara tafiya kallon su tayi ganin duk ita suke kallo sai tabi Bayan shi suna fita waje ya dube ta fuskar shi dauke da murmushi yace

" Zan Dan fita but ba Zan jima ba abokanayen aiki Na sunce Anjima zasu zo ganin amarya Zan yi take away sai frnds naki suyi serving nasu".

"Nope ba sai Ka saya abinci ba since muna da yawa zamu dafa kawai". Ta tsinci kan ta da fada

" no ban son ki wahala ".shiru tayi tana wasa da yatsun hannun ta don irin kallon da yake Mata..everlasting kiss ya Mata a forehead sannan yace

" fine tunda kince zaku yi ni Na wuce ".

" Allah tsare".

"Ameen yace yana murmushi sannan ya shiga motar shi ita ko ciki ta koma nan suka cigaba da hira daga bisani suka haura sama zuwa bedroom nata nan suka tayata gyara suka sake sauko downstairs din indomie da egg suka dafa sai a sannan ne ta sanar da su zuwan frnds nashi aiko aiki suka Kama abinci iri iri suke dafawa gida tuni ya haure da kamshi don yadda suke barna ta tabbatar wasu abun kam ba

cinyewa za'a yi ba shiyasa tace wallahi ko a Leda sai ta zuba musu sun tafi da shi tunda su suka yi barnar..

Basu suka gama ba sai Asr nan dai ya Kira ta a waya yana tambayar ko sun gama tace Ehhh..

" Kinga maybe suna hanya Kije kiyi wanka ".ciki ta shige su ko falon suka sake kimsawa tunda sunci abinci a ciki..

Motoci uku suka shigo gidan inda cikin wadanda suka zo Harda Bash su bakwai ne da shi Umar Farouq din takwas...

Knocking suke Amma duk sauran nauyin su suke ji shiyasa aka rasa me zuwa ya bude cikin su Auta ce dai tayi maturity ta mike inda ta bude kofar fuskar ta dauke da murmushi tace

" bismillah ".tana basu hanya nan suka Fara shiga suna karewa gidan da falon kallo,zama suka yi har shi Umar Farouq d'in nan ne suka gabatar musu da ruwa da kuma drinks shiru ba alamar Laylerh kuma bai jin zai tambayi ko daya a cikin su don gudun raini

" excuse me".yace da su inda ya haura sama yayi tapping Na kofar dakin ta,ta San shine shiyasa ta bada izinin shiga nan yasa Kai a dakin yana Binta da kallo sanye take cikin material Mai kyau fuskar ta ba wani ado kuma Kayan bai matse ta ba,kanta a kasa tace

"Sannu da dawa". Karasa shiga yayi tare da hugging nata yana fad'in

" kinyi kyau".bata ce komai ba ganin ta gama sai ya janyo ta suka fito falo nan ta shiga gaishe da bakin nasu sun Dan taba hira sannan Auta tace dinning is ready nan suka nufa ita tayi serving nasu inda Bash ke yawan satar kallon ta a karshe dai ya tambayi sunan ta

"Safiyya". Tace da shi daga nan duk sama suka koma dakin Laylerh suka bar su suci abinci shi dai Umar Farouq ba abunda yaci suna Dan taba hira irin nasu Na maza..

Sun jima a gidan sai kusan magrib sannan ya Kira Laylerh a waya yace su fito zasu tafi aiko tukuicin dubu Dari suka bata nan tayi godiya su kuma suka fice..

Sai Bayan i'sha ya shigo har lokacin kuma su Auta Na nan sai yasa driver ya mayar da su daga nan ya wuce dakin shi don gobe zai yi resuming yana da abubuwan yi dayawa..

Laylerh ma gaba daya a gajiye take shiyasa tayi wanka sannan ta kwanta bacci..

Sai karfe daya ya gama nan ne ya nufi dakin ta ya tarar tayi bacci sai ya rufa Mata blanket tare da shafa kanta yayi kissing nata ya fice zuwa nashi dakin don sai gajiya ya fita a jikin ta before ya Mata abunda take gudun tunda yanzu ba da bane da zaka ga a ranar da aka Kai amarya ango zai abka mata nan shima ya kwanta bacci..

Comment

Share

©Hafciey Musa